NAZARIN AYYUKAN MAKAXA SA'IDU MAIDAJI SABON BIRNI (1938-2000)

(JUZU'I NA DAYA)

Na

ANAS SA'IDU MUHAMMAD

M. A. AFRICAN LITERATURE (HAUSA)
DEPARTMENT OF AFRICAN LANGUAGES AND CULTURES,
FACULTY OF ARTS,
AHMADU BELLO UNIVERSITY, ZARIYA
NIGERIA

2012

Nazarin Ayyukan Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni
(1938-2000)

Na

Anas Sa'idu Muhammad
M.A. ARTS/ 10670/ 2008-2009

A Dissertation Submitted to the Postgraduate School,
Ahmadu Bello University, Zaria
Nigeria

In Partial fulfilment for the Award of
Master of Arts
African Literature (Hausa)

Department African Languages and Cultures
Ahmadu Bello University, Zaria
Nigeria

2012

DECLARATION

I Declare that the work in the thesis entitled "Nazarin Ayyukan Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni" has been performed by me in the Department of African Languages and Cultures under the supervision of Dr. Muhammad Lawal Amin and Dr. Magaji Tsoho Yakawada. The Information derived from the literature has been duly acknowledged in the text and a list of references provided. No part of this thesis was previously presented for another degree or diploma at any university.

_____	_____	_____
Anas Sa'idu Muhammad	*Signature*	*Date*

CERTIFICATION

This thesis entitled "NAZARIN AYYUKAN MAKAXA SA'IDU MAIDAJI SABON BIRNI" by Anas Sa'idu Muhammad meets the regulations governing the award of the degree of M. A. African Literature (Hausa) of Ahmadu Bello University, and is approved for its contribution to knowledge and literary presentation.

Dr. Muhammad Lawal Amin
Department of African Languages and Cultures
Major Supervisor
(Jagoran Duba Bincike na Xaya)

Dr. Magaji Tsoho Yakawada
Department of African Languages and Cultures
Minor Supervisor
(Jagoran Duba Bincike na Biyu)

Professor A. A. Joshua
Dean School of Postgraduate Studies
Ahmadu Bello University, Zaria

ABUBUWAN DA KE CIKI

		Shafi
Godiya	: : : : : : :	***xi***
Sadaukarwa	: : : : : : :	***xvi***
Gabatarwa	: : : : : : :	***xvii***
Abstract	: : : : : : :	***xxi***
Tsakure	: : : : : : :	***xxii***

BABI NA XAYA : SHIMFIXA

1.0 Gabatarwa	: : : : : : :	1
1.1 Hasashen Bincike	: : : : : :	3
1.2 Manufar Bincike	: : : : : :	4
1.3 Farfajiyar Bincike	: : : : : :	6
1.4 Iyakancewar Bincike	: : : : : :	7
1.5 Hanyoyin Gudanar da Binciken	: : : :	8
1.6 Naxewa	: : : : : : :	11

BABI NA BIYU : BITAR AYYUKAN DA SUKA GABATA

2.0 Gabatarwa	: : : : : : :	12
2.1 Tarken Ayyukan da Suka Kawo Tarihin Rayuwar Makaxa Maidaji	: : : :	13
2.2 Kundayen Bincike	: : : : : :	34

2.3 Bugaggun Littattafai : : : : : : 43

2.4 Maqalu da Takardu : : : : : : 55

2.5 Naxewa : : : : : : : 63

BABI NA UKU : JIGOGIN WAQOQIN MAKAXA MAIDAJI SABON BIRNI

3.0 Gabatarwa : : : : : : : 65

3.1 Jigo da Ma'anarsa : : : : : : 65

3.2 Ire-Iren Jigo : : : : : : 66

3.3 Nau'in Waqoqin Makaxa Maidaji : : : : 67

3.3.1 Waqoqin Fada : : : : : : 76

3.3.1.1 Waqoqin Fada na Lokacin Yaqi : : : 78

3.3.1.2 Waqoqin Fada na Yammaci : : : : 80

3.3.1.3 Waqoqin Fada na Lokacin Kewaya ko Rangadi : 82

3.3.1.4 Waqoqin Fada na Lokacin Taro : : : 84

3.3.1.5 Waqoqin Fada na Lokacin Naxin Sarauta : : 87

3.3.2 Waqoqin Noma : : : : : 89

3.3.3 Waqoqin Jama'a : : : : : 94

3.3.4 Waqoqin Siyasa : : : : : 98

3.3.4.1 Waqoqin Siyasa na Gaba Xaya : : : 98

3.3.4.2 Waqoqin Siyasa na Jam'iyya : : : 101

3.4 Jigo a Waqoqin Makaxa Maidaji : : : 104

3.4.1 Jigon Yabo : : : : : : 104

3.4.2 Jigon Zuga : : : : : : 110

3.4.3 Jigon Faxakarwa : : : : : : 113

3.4.4 Jigon Siyasa : : : : : : 120

3.5 Tubalan Ginin Jigo a Waqoqin Maidaji : : : 122

3.5.1 Nasaba : : : : : : : 123

3.5.2 Addini : : : : : : : 128

3.5.3 Ta'aziyya : : : : : : : 132

3.5.4 Koxa Kai ko Wasa Kai : : : : : 134

3.5.5 Habaici : : : : : : : 136

3.5.6 Kyauta da Karimci : : : : : : 141

3.6 Naxewa : : : : : : : 146

BABI NA HUXU : TSARI DA SALO A WAQOQIN MAKAXA MAIDAJI SABON BIRNI

4.0 Gabatarwa : : : : : : 147

4.1 Me ake Nufi da Tsari a Waqar Baka? : : : 147

4.2 Me da me Tsarin xa ya Qunsa? : : : 148

4.2.1 Ma'ana : : : : : : : 152

4.2.2 Qirga : : : : : : : 153

4.3 Tsarin Xiya a Waqoqin Makaxa Maidaji : : 153

4.3.1 Tsarin xa Mai Sauqi: : : : : 154

4.3.2 Tsarin xa Mai Tsauri : : : : : 159

4.4 Tsarin Rerawa a Waqoqin Makaxa Maidaji : : 163

4.4.1 Qulli : : : : : : : 164

4.4.2 Qari : : : : : : : 168

4.4.3 Tarbe : : : : : : : 169

4.4.4 Rakiya/ Karvevveniya : : : : : 171

4.4.5 Takidi a Waqoqin Makaxa Maidaji : : : 183

4.5 Matsayin Salo a Waqar Baka : : : : 188

4.6 Me ake Nufi da Salo? : : : : : 189

4.7 Adon Harshe a Waqoqin Makaxa Maidaji : : 190

4.7.1 Tamka : : : : : : 191

4.7.2 Kwalliya : : : : : : 194

4.7.3 Alamtarwa : : : : : : 197

4.7.4 Jinsintarwa : : : : : : 200

4.7.5 Kinaya : : : : : : 203

4.8 Salon Sarrafa Harshe : : : : : 205

4.8.1 Qarangiya : : : : : : 206

4.8.2 Karin Magana : : : : : :

4.8.3 Savi Zarce : : : : : :

4.8.4 Karin Harshen Waqa : : : : :

4.9 Naxewa : : : : : : :

BABI NA BIYAR: KAMMALAWA : : :

5.0 Gabatarwa : : : : : : :

5.1 Abubuwan da Bincike ya Gano : : : :

5.2 Wanda ya Gadi Makaxa Maidaji : : : :

5.3 Naxewa : : : : : : :

Manazarta : : : : : : :

JUZU'I NA BIYU
RATAYE NA XAYA

- *Matanin Wasu Daga Cikin Waqoqin Makaxa Maidaji Sabon Birni : : : : :*

RATAYE NA BIYU

- *Hirar Makaxa Maidaji Tare da Malam B. S. Y. Alhassan, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya :*

- *Hirar Makaxa Maidaji Tare da Alhaji Ibrahim Xiso, Rediyon Rima, Jihar Sakkwato :*

SADAUKARWA

Da yardar Allah, tabaraka wa ta'ala, na sadaukar da wannan aiki zuwa ga mahaifana, Farfesa Sa'idu Muhammad Gusau da Hajiya Lubabatu Abubakar Buba Maigoro. Allah ya saka musu da alherinsa, amin.

NAZARIN AYYUKAN MAKAXA SA'IDU MAIDAJI SABON BIRNI (1938-2000)

(JUZU'I NA BIYU)

Na

ANAS SA'IDU MUHAMMAD

M. A. AFRICAN LITERATURE (HAUSA)
DEPARTMENT OF AFRICAN LANGUAGES AND CULTURES,
FACULTY OF ARTS,
AHMADU BELLO UNIVERSITY, ZARIYA
NIGERIA

2011

RATAYE NA XAYA
KANUN WAQOQIN MAKAXA MAIDAJI DA KE CIKIN WANNAN KUNDI

Waqa	Shafi
1. Sarki yai abin daka ya huta : : : :	
2. Binu xan Baraz Zaki Xanbawa : : : :	
3. Qi garaje uban Bebi bai xauki wargi ba : :	
4. Balaraben Sarki : : : : : :	
5. Na Ali xan bajini : : : : : :	
6. Kai ab bahagon gulbi : : : : :	
7. Na yi hamdala nai shukura da godewa : : :	
8. Na shira kaya za ni garai : : : : :	
9. Gagari gaba na Salihu : : : : :	
10. Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa : :	
11. Sarki Muhamman xan Kilo : : : :	
12. Gagara badau ‘yak Kaso : : : : :	
13. Uban Na-Allah uban Madauci : : : :	
14. Ya wuce tantama : : : : : :	
15. Da shiri yat tasa : : : : : :	
16. Kak ka yarda da raini uban Baraya : : :	

17. Xansidi amshi sandar mulki qasatai : : :

18. Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi : :

19. Mata in ba ku ba gida : : : : :

20. A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo : : :

21. Madogara Alhaji Mamman : : : :

22. Na yi mamakin harka tai : : : : :

23. Allah za ni roqonka : : : : :

24. Dogo xan Abubakar na Malumfashi : : :

25. Jikan Kunda ai ina kan zuwa gaisai : : :

26. Malam Alo na baraz zaki : : : :

27. Jikan Jari ginshiqi : : : : :

28. Ka buwayi maza sai na zo : : : : :

29. Mainsara na Isa na Musa : : : :

30. Namijin daga uban Gardaye : : : :

31. Uban Makama uban Gardaye : : : :

32. Ginshimin Zakari Baqadire na Audu qasaitacce:

33. Harka da ilmi mu kai : : : : :

34. Ya kwan yana aikin mota : : : :

35. Alhaji xan Sarkin Hillani : : : :

36. Xangara jikan xan layayya : : : :

37. Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi : :

38. Uban Zagi na Muhamman mai Sabon Birni : :

39. Gwarzon Galadima ya ci arna : : : :

40. Ummaru ginshimin Ali ci hwansa : : :

41. Ya gade gidan gardaye : : : : :

42. Kak ka xau reni : : : : : :

43. Sarkin Gandu ubangijin gutsun gawo : : :

44. Hali nai girma : : : : : :

45. Ina anniyan ishe mai : : : : :

46. Na taho gaida babba gardaye : : : :

47. Iro na Bawa baqon dole : : : : :

48. Da yaqi ya ci maza : : : : :

49. Xangara Dabo xan Kasau : : : :

50. Toya matsahwa baqon dole : : : :

51. Bawa na Jekadiya : : : : : :

52. Inzo kixi inda Sani na Ummu : : : :

53. Ginshimin yari magajin Magaji : : : :

54. Dogo na Jekadiya : : : : : :

55. Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa : : :

56. Barka da shirin zamani : : : : :

57. Na biyo jikan Nana Sarkin Hillani : : :

58. Ya hana aikin yini : : : : :

59. Wuce maza xan kurma : : : : :

60. Gagara gasa na Alhaji Gardaye : : : :

61. Na zaka barka da azzukka : : : :

62. Sadauki Bala gagon Salihu : : : :

63. Na zo ganin bajinin qani : : : : :

64. Ga ni na zaka murna garai ka sarki gwarzo : :

65. Madogara na Alhaji Isa : : : : :

66. Uban Jekadiya : : : : : :

67. Baban Yari baban Makama : : : :

68. Ya tara dame mai dama : : : : :

69. Abarshi xan mai damma xan Shibo : : :

70. Niqatau na Jekada bajimin magajin gari : :

71. Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala : :

72. Ibrahim xan Makoxa rai nai yai haske : : :

73. A gaishe ka na Amadu : : : : :

74. Lahiya na Muhamman : : : : :

75. Jikan Kaso xan Kaso : : : : :

76. Sai mu taru mu yi roqon Allah : : : :

77. Ya kwan cikin shiri ya tashi tsaye : : :

78. Yai halin mazan jiya Isa maqi garaje : : :

RATAYE NA BIYU

- *Hirar Makaxa Maidaji Tare da Malam B. S. Y. Alhassan, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya :*

- *Hirar Makaxa Maidaji Tare da Alhaji Ibrahim Xiso, Rediyon Rima, Jihar Sakkwato :*

- *Jerin Wasu Daga Cikin Mutanen da Makaxa Maidaji ya yi wa Waqa : : :*

RATAYE NA BIYU
MATANIN WASU WAQOQIN MAKAXA
SA'IDU MAIDAJI SABON BIRNI

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Waqar Noma ta Arzika[1]*,*
***01.** Gindin Waqa : Sarki yai abin daka ya huta,*
: Zaki xan Abubakar xan Buda.

Jagora : Baba mijin Shibo mijin Maryama,
'Y/Amshi : Giwa maganin itacen daji,
: Sarki yai abin daka ya huta,
: Zaki xan Abubakar xan Buda.

Jagora : Ah Baba mijin Shibo mijin Maryama,
'Y/Amshi : Giwa maganin itacen daji.

Jagora : Arzika jikan Salau magajin Sanda, x^2
: Zaki mai kasam ma kai nainama, x^2
'Y/Amshi : Sarki yai abin daka ya huta,
: Zaki xan Abubakar xan Buda.

Jagora : Ina Arzika xan Imamu bawan Alllah, x^2
: Bai ci amanar gida ba balle daji, x^2
'Y/Amshi : Sarki yai abin daka ya huta,
: Zaki xan Abubakar xan Buda.

Jagora : Kullum fata nikai wurin Jabbaru,
: Don albarkacin Sabilillahi,
: Kuma albarkacin mutanen Makka,
: Ka sallace dubu kahin jinmu,
'Y/Amshi : Sarki yai abin daka ya huta,
: Zaki xan Abubakar xan Buda.
Jagora : Arzika tun zamanin kana xan yaro, x^2

---

[1] An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{50}$ $^1/_2$.

: Hak kak kai kana cikin qarninka,
: To hay yau ba ka raina matar wani ba,
‘Y/Amshi : Sarki yai abin daka ya huta,
: Zaki xan Abubakar xan Buda. x^2

Jagora : Hwaxa ma samarin ga masu son matanmu,
: Hwaxa musu Alhaji mai kixi ya gane,
‘Y/Amshi : Sarki yai abin daka ya huta,
: Zaki xan Abubakar xan Buda.

Jagora : Arzika jikan Salau magajin Sanda,
: Zaki mai kasam ma kainai nama.
‘Y/Amshi : Sarki yai abin daka ya huta,
: Zaki xan Abubakar xan Buda.

Jagora : To ku yi min godiya ga horon Buda,
: Buda rigar da ni hwaxi ya ba ni,
‘Y/Amshi : Sarki yai abin daka ya huta,
: Zaki xan Abubakar xan Buda.

Jagora : To, kai Ali kai da Salisu Mamman,
: To, ni ga ni na yi baqon doki,
: Amma ba ku ba ni abin da zan ci sai ba,
‘Y/Amshi : Sarki yai abin daka ya huta,
: Zaki xan Abubakar xan Buda.

Jagora : Ina Arzika xan Imamu bawan Alllah,
‘Y/Amshi : Bai ci amanar gida ba balle daji.

Jagora : To, na gode ma Argiji, na gode, x^2
‘Y/Amshi : Don ga binjimin zane ta ba da. x^2
Jagora : Godiya mai yi Rabbana yab ban ‘yan Makka,
: Ga kuxxin sayen zane yab ban.
Jagora : Godiya mai yi Rabbana yab ban ‘yan Makka,
: Ga kuxxin sayen zane yab ban.
‘Y/Amshi : Sarki yai abin daka ya huta,
: Zaki xan Abubakar xan Buda.
Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,

Alhaji UmmaruNa-Allah (1957-1966),

02. *Gindin Waqa : Binu xan baraz Zaki Xanbawa*[2]*,*
: Jikan Kilo gwamron giwa.

Jagora : Binu xan baraz zaki Xanbawa,
'Y/Amshi : Jikan Kilo gwamron giwa,
: Na Malam gwanin daga,
: Na-Allah jikan hillani xan Musa na Malam.

Jagora : Shin Ummaru ne ko Yakubu Daudu, x^2
'Y/Amshi : Ko ko Kada ne yad dawo. x^2

Jagora : Shin Ummaru ne ko Yakubu Daudu,
'Y/Amshi : Ko ko Kada ne yad dawo,
: Na Malam gwanin daga,
: Na-Allah jikan hillani xan Musa na Malam.

Jagora : Kakanka ya mulki Gobir, x^2
'Y/Amshi : Sai ya mulke mulkin,
: Da kakanai yay yi. x^2

Jagora : Dur ran da na Yakuba yai sarki,
'Y/Amshi : Da mu za a shan kalwa birni,
: Na Malam gwanin daga,
: Na-Allah jikan hillani xan Musa na Malam.

Jagora : Dur ran da na Yakubu yay sarki,
'Y/Amshi : Da mu za a shan kalwa birni.
Jagora : Da mu za a shan kalwa,
'Y/Amshi : Ran nan da mu za a tarboso ne birni.
Jagora : To! Da mu za a shan kalwa,
'Y/Amshi : Ran nan da mu za a tarboso ne birni.
Jagora : Mu mulke waxan birni, x^2
'Y/Amshi : Mu biya mu mulke mutanen Kurawa. x^2
Jagora : Mu mulke waxan Tara, x^2

---

[2] Wannan rerawa an same ta a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsunan Nijeriya da Al'adu, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. A Faifai mai lamba AL $^1/_{147}$ $^1/_6$.

‘Y/Amshi : Mu biya mu mulke mutanen Gatawa. x^2
Jagora : Gangara da xam Maliki, x^2
‘Y/Amshi : Kai ad da mulkinsu,
: Ba wani bayan kai,
: Na Malam gwanin daga,
: Na-Allah jikan hillani xan Musa na Malam. x^2

Jagora : To, ina masu son sarki, x^2
‘Y/Amshi : In anka shaqa mijina as sarki. x^2

Jagora : Ga wani na jiran sarki,
‘Y/Amshi : Daxa sai shi koma jiran Sarkin Karma,
: Na Malam gwanin daga,
: Na-Allah jikan hillani xan Musa na Malam.

Jagora : Mu sai ma takobi da hamilo,
‘Y/Amshi : Da taggo da wandon dirbanci,
: Na Malam gwanin daga,
: Na-Allah jikan hillani xan Musa na Malam.

Jagora : Ya muradi kake Musa,
‘Y/Amshi : Allah ya yi ma xaukakar Sarki Shawai,
Jagora : Ya muradi kake Musa,
‘Y/Amshi : Allah ya yi ma xaukakar Sarki Shawai,
: Na Malam gwanin daga,
: Na-Allah jikan hillani xan Musa na Malam.

Jagora : Shin Ummaru ne ko Yakubu Daudu,
‘Y/Amshi : Ko ko Kada ne yad dawo,
Jagora : Shin Ummaru ne ko Yakubu Daudu,
‘Y/Amshi : Ko ko Kada ne yad dawo,
: Na Malam gwanin daga,
: Na Allah jikan hillani xan Musa na Malam.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa,
Mai Waqa : Malam Hassan Xansanda,

03. *Gindin Waqa : Qi garaje uban Meli bai xauki wargi ba*[3]*,*
: Dole in yaba Malam Hassan mai halin girma.

Jagora : A gai da Sale Xansanda gasurgumin icce, x[2]
'Y/ Amshi : Wanda ya hana shegantaka nan qasar Tara,
: Qi garaje uban Meli bai xauki wargi ba,
: Dole in yaba Malam Hassan mai halin girma. x[2]

Jagora : Ga shi giwa na saraki ya dankwashe gaba,
: Na Umma ruwan wanke dartsa Uban Makau,
'Y/ Amshi : Ga Uban Sule ya mai da kora na xan mantai,
: Qi garaje uban Meli bai xauki wargi ba,
: Dole in yaba Malam Hassan mai halin girma.

Jagora : Lalle ashe harkar malami na da ban da tsoro,
: Ce ma 'yan makaranta su bar ja da Xansanda,
'Y/ Amshi : Yanzu ya wuce harkarsu ba za su immai ba,
: Qi garaje uban Meli bai xauki wargi ba,
: Dole in yaba Malam Hassan mai halin girma.

Jagora : Malami mai kyauta kama tai Uban Makau,
: Sai Malam Sidi sai malamin Tsadau,
: Sai Malam Habaru wancan na Samaru,
'Y/ Amshi : Yaushe niz zaka ni ma yana ba ni in na zo,
: Qi garaje uban Meli bai xauki wargi ba,
: Dole in yaba Malam Hassan mai halin girma.

Jagora : Ka gani ba kukan Uba nai ma Allah ba,
: Ni ba kukan Uwa nai ma Allah ba,
Jagora : Don mutuwa ba ni tsoran ta sha raina,

[3] An sami wannan rerawa ne a Kundin Fasahar Baka. Gusau, S. M. (ed), 2004.

: Kwancin qabari shi xai ka ban tsoro,
: Kana kwance cikin duhu ba ka motsawa,
: In ka yi gaba bango ya tarbe ka,
: In ka yi yamma bango ya tarbe ka,
: Ba ka tashi tsaye sai itace shi kwabre ka,
: Kuma kana so ka ga naka ba a ba ka hanya ba,
‘Y/ Amshi : Allah ka yo mana halin zuwa mui zaman kewa,
: Qi garaje uban Meli bai xauki wargi ba,
: Dole in yaba Malam Hassan mai halin girma.

Jagora : Marafa na gane duniya zamanin yanzu,
: In zama yai daxi mutane ka vata shi,
: Tun da ban cuci mutun ba kar ya cuta ni,
‘Y/ Amshi : In mutum ya cuce ni Allah ya rama min,
: Tun da na tsare Allah yana yo min komi,
: Qi garaje uban Meli bai xauki wargi ba,
: Dole in yaba Malam Hassan mai halin girma.

Jagora : A gai da Sale Xansanda gunsungumin icce,
‘Y/ Amshi : Wanda ya hana shegantaka nan qasar Tara
: Qi garaje uban Meli bai xauki wargi ba,
: Dole in yaba Malam Hassan mai halin girma.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Zazzau,
Alhaji Shehu Idris (1975-)

04. *Gindin Waqa : Balaraben Sarki*[4]*,*
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Aikinka ya yi kyau sarkin Zazzau, x^2
'Y/Amshi : Balaraben Sarki. x^2

Jagora : Sarki na Alqali,
'Y/Amshi : Ya hanqure da masu yi mai hwada.
Jagora : Sarki na Alqali,
'Y/Amshi : Ya hanqure da masu yi mai hwada.
: Balaraben Sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Mijin Hadiza mijin Mariya dabaru yak kama,
'Y/Amshi : Sarki mijin Binta da Binta,
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.
Jagora : Kai mijin Hadiza mijin Mariya dabaru yak kama,
'Y/Amshi : Sarki mijin Binta da Mariya,
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Ina gida ina hutawa, x^2
'Y/Amshi : Sai nig ga saqon Sanqira. x^2
Jagora : Sai nic ce,
'Y/ Amshi : In Allah ya nuhwa ina kwana Zazzau.
Jagora : Sai nic ce,
'Y/ Amshi : In Allah ya nuhwa ina kwana Zazzau,
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Wanda yat taho Zazzau,
'Y/Amshi : Alhaji bai tsayawa Rawayya.
Jagora : Tun da na taho Zazzau,
'Y/Amshi : Alhaji ban tsayawa Rawayya.

---

4 Wannan rerawa an same ta a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsunan Nijeriya da Al'adu, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. A Faifai mai lamba AL $^1/_{374}$ $^1/_2$.

Jagora : Tun da na taho Zazzau,
'Y/Amshi : Alhaji ban tsayawa Rawayya,
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Kulkin bugun kura, x^2
'Y/Amshi : In anka sa takobi an vata. x^2

Jagora : Abin kixin sarki,
'Y/Amshi : Kai ba abin kixan ‘yan mata ba.
Jagora : E abin kixin sarki,
'Y/Amshi : Kai ba abin kixan ‘yan mata ba,
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Sarki na Alqali,
'Y/Amshi : Ya hanqure da masu yi mai hwada.
Jagora : Sarki na Alqali,
'Y/Amshi : Ya hanqure da masu yi mai hwada,
: Balaraben Sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Shehu Mani,
'Y/Amshi : Wada yan nuhwa ga rainai ya samu,
: Tun da Allah ya ba shi martabar Sarki Sambo,
: Balaraben Sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Shehu Mani, x^2
'Y/Amshi : Wada yan nuhwa ga rainai ya samu,
: Tun da Allah ya ba shi martabar Sarki Sambo, x^2
: Balaraben Sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Sarki na Alqali,
'Y/Amshi : Ya hanqure da masu yi mai hwada,
Jagora : Sarki na Alqali,
'Y/Amshi : Ya hanqure da masu yi mai hwada,
: Balaraben Sarki,

: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Jekadiyar Zariya, x^3
'Y/Amshi : Ba ta zaqe da bakin sarki ba, x^3
: Balaraben Sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Wannan Jekadiya, x^2
'Y/Amshi : Kowaz zaka sannu ta xau lamba,
: Balaraben Sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau. x^2

Jagora : Wannan Bagobira, x^3
'Y/Amshi : Wataqil ko cikin irin ‘yar gwarzo ta,
: Balaraben Sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau. x^3

Jagora : Ina gida ina hutawa, x^2
'Y/Amshi : Sai nig ga saqon Sanqira, x^2
Jagora : Sai nic ce,
‘Y/ Amshi : In Allah ya nuhwa ina kwana Zazzau.

Jagora : Sai nic ce,
‘Y/ Amshi : In Allah ya nuhwa ina kwana Zazzau,
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Tun da na taho Zazzau, x^2
'Y/Amshi : Alhaji bai tsayawa Rawayya,
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau. x^2

Jagora : Mijin Hadiza mijin Mariya dabaru yak kama,
'Y/Amshi : Sarki mijin Binta da Binta ya yi kwaru,
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Ba mamaki, x^2

: Uban zagi ba mamaki,
'Y/Amshi : Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau. x^2

Jagora : Sarkin Zazzau, x^2
: Uban zagi ba mamaki,
'Y/Amshi : Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau. x^2

Jagora : Sarki na Alqali, x^3
'Y/Amshi : Ya hanqure da masu yi mai hwada,
: Balaraben Sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau. x^3

Jagora : Kulkin bugun kura, x^2
'Y/Amshi : In anka sa takobi an vata. x^2

Jagora : Abin kixin sarki,
'Y/Amshi : Kai ba abin kixan ‘yan mata ba.

Jagora : E abin kixin sarki,
'Y/Amshi : Kai ba abin kixan ‘yan mata ba,
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : To, Shehu Mani, x^3
'Y/Amshi : Wada yan nuhwa ga rainai ya samu,
: Tun da Allah ya ba shi martabar Sarki Sambo. x^3

Jagora : To, hwaxa ma mai wargi, x^2
'Y/Amshi : Ko can da bai san wargi ba. x^2

Jagora : Shi ba ya son wargi, x^2
'Y/Amshi : Kuma Shehu ba ya son 'yan kamanci. x^2
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Ba mamaki,
: Uban zagi ba mamaki, x^2
'Y/Amshi : Balaraben sarki,

: Aikinka ya yi kyau Sarki Zazzau. x^2

Jagora : Sarkin Zazzau,
: Uban zagi ba mamaki, x^2
'Y/Amshi : Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau. x^2

Jagora : Sarki na Alqali, x^3
'Y/Amshi : Ya hanqure da masu yi mai hwada,
: Balaraben Sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau. x^3

Jagora : Sarkin uban Majidaxi,
'Y/Amshi : Barka da kai da kawon zamunna , x^2
: Balaraben Sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.
Jagora : Sarkin uban Majidaxi, x^2
'Y/Amshi : Barka da kai da kawon zamunna. x^2
Jagora : Sarkin uban Majidaxi, x^2
'Y/Amshi : Barka da kai da kawon zamunna ,
: Balaraben Sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau. x^2

Jagora : To, Shehu Mani, x^3
'Y/Amshi : Wada yan nuhwa ga rainai ya samu,
: Tun da Allah ya ba shi martabar Sarki Sambo, x^3
Jagora : Balaraben Sarki,
'Y/ Amshi : Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa,
Mai Waqa : Sarkin Zazzau, Alhaji Shehu Idris (1975-)
Gindin Waqa : Balaraben Sarki[5]*,*
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Abdulkarimu ya dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Idrisu ya dawo,

[5] An sami wannan rerawa ne a littafin *Diwanin Waqoqin Baka.* Gusau, S.M. 2009: 197-203.

'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Yamusa ya dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Sambo ya dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Jafaru ya dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Kwasau ne yad dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Aminu ya dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Ga Sidi ya dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Ni ban zuwa gulbi,
'Y/Amshi : Alhaji bai zuwa wanka tafki.
Jagora : Ba wanda zai yi mai wargi,
'Y/Amshi : Ko can Shehu bai san wargi ba.
Jagora : Abubakar da yad dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Kuma Abdu ya dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Xalhatu ya dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Ibrahim ya dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Halidu ya dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Zariya wanda yai,
'Y/Amshi : Wauta Wawa na fashe mai qwaryar kai.
Jagora : Wanda bai zuwa gulbi, x^2
'Y/Amshi : Alhaji ban zuwa wanka tafki, x^2
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.
Jagora : Ni ban kixin sarki, x^2
'Y/Amshi : Sai na ji wanda kainai yak qosa. x^2

Jagora : Ai ku tattaro ku ga, x^2
'Y/Amshi : Kaya waxanda mai girma yab ban,
: Kun gani kayan hwan xari bakwai,
: Sarkin yab ban. x^2
Jagora : Ga riguna tsadaddi iri-iri, x^2
'Y/Amshi : Waxanda sarki yab ban,
: Kuma had da alkyabbu,

: Kala biyu yab ban. x^2

Jagora : Sarki uban Madauci ,
'Y/Amshi : Ina so ka ban ni in dawo Zazzau.

Jagora : Inna uban Majidaxi,
'Y/Amshi : Sarki ubangijin Sarkin hwada.
Jagora : Sarki na Alqali, x^2
'Y/Amshi : Ya hanqure da masu yi mai hwada. x^2

Jagora : Sarkin Zazzau uban na Jika na nan, x^2
'Y/Amshi : Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau. x^2

Jagora : Shehu Mani,
'Y/Amshi : Wada yab bixa ga rainai ya samu,
: Tun da Allah ya ba shi martabar Sarki Sambo.

Jagora : Sarki na Alqali,
'Y/Amshi : Ya hanqure da masu yi mai hwada.

Jagora : To hwaxa ma mai wargi,
'Y/Amshi : Wawa yana yi mai bulala.

Jagora : Shi ba ya son wargi,
'Y/Amshi : Shehu ba ya son 'yan kamanci.

Jagora : Ina gida ina hutawa,
: Sai nig ga saqon Sanqira,
'Y/Amshi : Sai nic ce,
: In Allah ya nuhwa ina kwana Zazzau.

Jagora : Wanda yat taho Zazzau, x^2
'Y/Amshi : Alhaji bai tsayawa Rawayya. x^2

Jagora : Kulkin bugun kura,
'Y/Amshi : In anka sa takobi an vata.

Jagora : Na ce Jakadiyar Zazzau, x^2
'Y/Amshi : Haw wajen qasam Masar ta xau lamba. x^2

Jagora : Taushi abin kixin sarki, x^2
'Y/Amshi : Bai zan abin kixin 'yan mata ba. x^2

Jagora : Shata da yay yi ma waqa,
'Y/Amshi : Ya gama da roqon Jabbaru.
Jagora : Qwairo da yay yi ma waqa,
'Y/Amshi : Ya gama da roqon Jabbaru.
Jagora : Xangiwa da yay yi ma waqa,
'Y/Amshi : Ya gama da roqon Jabbaru.
Jagora : Xan'anace da yay yi ma waqa,
'Y/Amshi : Ya gama da roqon Jabbaru.
Jagora : Sa'idu ya yi ma waqa,
'Y/Amshi : Ya gama da roqon Jabbaru.
Jagora : Ko ni ina hwata, x^2
'Y/Amshi : Allah ya wa uwayenai rahama. x^2

Jagora : Shi ba ya son wargi,
'Y/Amshi : Kuma Shehu ba ya son 'yan kamanci.

Jagora : Zariya wanda yay yi wargi,
'Y/Amshi : Wawa na fashe mai qwaryar kai.

Jagora : Xan'iya uban Suliki, x^2
'Y/Amshi : Maganin marassa imani. x^2

Jagora : Ina gida ina hutawa, x^2
'Y/Amshi : Sai nig ga baqon Sanqira,
: Sai nic ce, in Allah ya nuhwa,
: Ina kwana Zazzau. x^2

Jagora : Wanda yat taho Zazzau,
'Y/Amshi : Alhaji bai tsayawa Rawayya.

Jagora : Uban Majidaxi,
'Y/Amshi : Sarki Ubangijin Sarkin Hwada,
: Ubangijin Shantali,

: Koyaushe ka ishe mai ya shirya.

Jagora : Mijin Hadiza mijin Mariya,
'Y/Amshi : Sarki mijin Binta da Binta,
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.
Jagora : Sarkin Zazzau uban Zagi ba mamaki, x^3
'Y/Amshi : Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau. x^3

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ummaru xan Salihu (1957-1966),

05. *Gindin Waqa : Na Ali xan Bajini,* [6]
: Jikan Shekara ka gama lahiya.

Jagora : Na Ali xan Bajini,
: Jikan Shekara ka gama lahiya,
'Y/Amshi : Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.

---

[6] Wannan rerawa an same ta a Xakin Tattalin Fasahar Baka da ke Sashen Harsunan Nijeriya da na Afirika, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. A faifai mai lamba AL $^0/_{50}$ $^1/_2$.

Jagora : Bunu uban Shamaki, x^2
'Y/Amshi : Xan Bawa uban Jekada kake Yakuba. x^2

Jagora : Na Ali jikan Kaso,
'Y/Amshi : Jikan Alhaji jikan Iyad duniya.
Jagora : Na Ali jikan Kaso,
'Y/Amshi : Jikan Alhaji jikan Iyad duniya,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.

Jagora : Abin da an nesa ya zaka kusa, x^2
'Y/Amshi : Taho daxa qara gusawa mukai. x^2

Jagora : Dag Gangara za mu Kurawa,
'Y/Amshi : Dac can a ba mu riqon dudduka,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.

Jagora : Dag Gangara za mu Kurawa,
'Y/Amshi : Dac can a ba mu riqon dudduka.

Jagora : Mu munka hwara zuwa birni,
'Y/Amshi : Dum masu yad da qahwa sun bari.

Jagora : Ummaru mu munka hwara zuwa birni,
'Y/Amshi : Dum masu yad da qahwa sun bari,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.

Jagora : Yara sun zaka Sabon Birni,
'Y/Amshi : Tun da an ce Kada yay yi shi,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.

Jagora : Sarki ka ja da Kada,
'Y/Amshi : In sun ka ga Sanda magajin Kada.
Jagora : Bunu ka ja da Kada,
'Y/Amshi : In sun ka ga Sanda magajin Kada,

: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.

Jagora : Duk inda xan Bawa ya zamo sarki, x^2
'Y/Amshi : Duk da mu za mu cin duniya,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau. x^2

Jagora : Mu munka hwara zuwa birni, x^2
'Y/Amshi : Dum masu yad da qahwa sun bari. x^2

Jagora : Ah! Gangara za ka ban, x^2
'Y/Amshi : Ko Gatawa ka ba mu,
: Riqe wa muke. x^2

Jagora : Sai dai ka ba ni Maigarin gona,
'Y/Amshi : Bayan baqar wahala xai yakai,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.

Jagora : Kai dai ka ba ni Maigarin gona,
'Y/Amshi : Bayan baqar wahala xai yakai.

Jagora : Kuma kak ka ba ni riqon Tara,
'Y/Amshi : Tun da na ga ba su barin shexana,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.

Jagora : Kuma kak ka ba ni riqon Tara,
'Y/Amshi : Tun da na ga ba su barin shexana.
Jagora : Kuma kak ka ba ni riqon Tara,
'Y/Amshi : Tun da na ga ba su barin shexana,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.

Jagora : Halo halin Ummaru, x^3
'Y/Amshi : In ka ji ana halin la'ada ya tsaya. x^3

Jagora : Ai na ce ran da duk ka tsaya,
'Y/Amshi : Rannan kowa ka mulki ajewa yakai,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.

Jagora : Ran da duk ka tsaya,
'Y/Amshi : Rannan kowa ka mulki ajewa yakai.

Jagora : Xan Bawa ya yi riqo, x^2
'Y/Amshi : Sai mun sha gobiya mu yi babban ciki,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau. x^2

Jagora : Uban Gada uban Gandu, x^2
'Y/Amshi : Xan Gamana mai baza mai dame. x^2
Jagora : Allah ya ba mu sa'a, x^2
'Y/Amshi : Wata rana had da gandun gamewa mukai, x^2
Jagora : Allah shi ba mu sa'a,
'Y/Amshi : Wata rana had da gandun gamewa mukai.
Jagora : Allah shi ba mu sa'a,
'Y/Amshi : Wata rana had da gandun gamewa mukai,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.
Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa
Ubangida : Sarkin Gobir Sabon Birni,
Muhammadu Bawa (1975 - 2003)[7]*,*

6. *Gindin Waqa : Kai ab bahagon gulbi,*
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Na Garkuwa bajinin Sarkin Dogarrai na Galadima,
'Y/Amshi : Gwarzon Ajiya Sarki uban Isihu uban Garba,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,

---

[7] An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{7}$.

: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Ai na Garkuwa bajinin Sarkin Dogarrai na Galadima,
'Y/Amshi : Gwarzon Ajiya Sarki uban Isihu uban Garba,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Alhaji sarkin hwadamar kanwa, x^2
'Y/Amshi : Mai kwana tsaye ko yaushe. x^2
Jagora : Alhaji sarkin hwadamar kanwa,
'Y/Amshi : Mai kwana tsaye ko yaushe,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : To, sai an yi kadankarma, x^2
'Y/Amshi : A san babba a san yaro,
: Kuma sai an yi karom batta,
: A san wane a san wane. x^2
Jagora : Ai ina da Uba Sulxanin Gobir,
‘Y/Amshi : Wanda ka hisshe ni,
: Ni dai ba ni gudun hitinar Gobir,
: Duw wada tat tashi,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.
Jagora : Ai ina da Uba Sulxanin Gobir,
‘Y/Amshi : Wanda ka hisshe ni,
: Ni dai ba ni gudun hitinar Gobir,
: Duw wada tat tashi.

Jagora : Ga ni ina son harkar zambo,
‘Y/Amshi : Amma na zama mai geme,
: Kowa yaz zama mai geme,
: Na dama shi yi shexanci,

: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Ga ni ina son harkar zambo,
‘Y/Amshi : Amma na zama mai geme,
: Kowa yaz zama mai geme,
: Na dama shi yi shexanci.

Jagora : Cikin masu biyas sarki,
‘Y/Amshi : Wasu sun hwara munahicci,
: Bari kowa ka munahicci,
: Hwaxa mai da akwai Allah,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Ai cikin masu biyas sarki,
‘Y/Amshi : Wasu sun hwara munahicci,
: Bari kowa ka munahicci,
: Hwaxa mai da akwai Allah,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : An ce wane shina hauka,
‘Y/Amshi : Ni ban san shi da hauka ba,
: Kuma ban san shi da hauka ba,
: Sai ya katse abin xarmi,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.
Jagora : An ce wane shina hauka,
‘Y/Amshi : Ni ban san shi da hauka ba,
: Kuma ban san shi da hauka ba,
: Sai ya katse abin xarmi.

Jagora : Jiya can nij ji mutane, x^3
: Na cewa wane hawa'i ne,
'Y/Amshi : Ko mu mun ji mutane ,
: Na cewa wane tavavve na, x^3
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Shi wargi da hawa'i,
'Y/Amshi : Ya xara wargi da bugun buta,
: In sun tashi rashin kunyan nan,
: In sun gamu dux xai na,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Shi wargi da hawa'i,
'Y/Amshi : Ya xara wargi da bugun buta,
: In sun tashi rashin kunyan nan,
: In sun gamu dux xai na.
Jagora : Ai wargi da hawa'i,
'Y/Amshi : Ya xara wargi da bugun buta,
: In sun tashi rashin kunyan nan,
: In sun gamu dux xai na,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Hawa'i da irin buta,
: Ai na ce muku dux xai na,
'Y/Amshi : Ai had da mashayin kansu,
: Shi ma la'ananne na,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.
Jagora : Da Hawa'i da irin buta, x^2
: Ai na ce muku dux xai na,

‘Y/Amshi : Ai had da mashayin kansu,
: Shi ma la’ananne na, x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : To, Inna qaunas sarki, x^2
‘Y/Amshi : Ta maishe ni kamax xan ta,
: Ko babu kixi,
: Sai ta ba ni abin goro. x^2
Jagora : To, Garkuwa xan Gardaye, x^2
‘Y/Amshi : A gaishe ka a gaishe ka,
: Mu yi hwata ya daxe duniya,
: Ya zam ba mu abin Allah, x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.
Jagora : To, Garkuwa in na zaka gaisai,
‘Y/Amshi : Sai yay yo min dumbulka,
: Da ya diba idanuna,
: Ya san wani abu yak kai ni,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.
Jagora : To, Garkuwa in na zaka gaisai,
‘Y/Amshi : Sai yay yo min dumbulka,
: Da ya diba idanu na,
: Ya san wani abu yak kai ni.

Jagora : To, Inna xiyas Sardauna,
‘Y/Amshi : Giwa Inna Bahillata,
: In ta kama tila min kaya,
: Sai na gaji na ratse,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,

: Uban Bunu da Baraz Zaki.
Jagora : To, Inna xiyas Sardauna,
‘Y/Amshi : Giwa Inna Bahillata,
: In ta kama tila min kaya,
: Sai na gaji na ratse.

Jagora : Ai na Garkuwa bajinin Sarkin Dogarrai na Galadima,
'Y/Amshi : Gwarzon Ajiya Sarki uban Isihu uban Garba.

Jagora : Alhaji sarkin hwadamar kanwa, x^2
'Y/Amshi : Mai kwana tsaye ko yaushe. x^2
Jagora : Alhaji sarkin hwadamar kanwa,
'Y/Amshi : Mai kwana tsaye ko yaushe,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Gohe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.
Jagora : Gauxe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.
Jagora : Tambai ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.
Jagora : Yakuba ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.
Jagora : Ibrahim ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.
Jagora : Balarabe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi
Jagora : Jadi ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.
Jagora : Jari Kada ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.
Jagora : Shawai ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.
Jagora : Salihu ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.
Jagora : Ummaru ya buga tamburra,

'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : ‘Yan Gatawa da Yakubawa,
'Y/Amshi : Kowane an sa shi ga tarihi,
: Haba sarki riqe tarihin ga,
: Da kowa ka bixa jiddun,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Gamkawa da Bacirawa,
‘Y/Amshi : Kowane an sa shi ga tarihi,
: Haba Sarki riqe tarihin ga,
: Da kowa ka bixa jiddun.
Jagora : Haba sarki riqe tarihin ga,
‘Y/Amshi : Da kowa ka bixa jiddun.

Jagora : Kai kag gane mahwarinai,
‘Y/Amshi : Kuma kai ka san wada yaq qare,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

agora : To, na san tahiyag giwa,
: Kuma na san tahiyaz zaki,
: Na san tahiyaj jaki,
: Kuma na san tahiyad doki,
: Na san maganar mata,
: Kuma na san maganar qato,
: Kowas san maganar matam,
: Bori babu kamar Inna,
'Y/Amshi : Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : To, na san tahiyag giwa,
: Kuma na san tahiyaz zaki,

: Na san tahiyaj jaki,
: Kuma na san tahiyad doki,
: Na san maganar Buzu,
: Kuma na san ta Bahillace,
: Na san maganar mata,
: Kuma na san maganar qato,
: Kowas san maganar matam,
: Bori babu kamar Inna,
'Y/Amshi : Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa
Ubangida : Sarkin Gobir Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Bawa (1975 - 2003)
Gindin Waqa : Kai ab bahagon gulbi,[8]
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Na Garkuwa bajinin Sarkin Dogarrai na Galadima,
'Y/Amshi : Gwarzon Ajiya Sarki uban Isihu uban Garba,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Ai na Garkuwa bajinin Sarkin Dogarrai na Galadima,
'Y/Amshi : Gwarzon Ajiya Sarki uban Isihu uban Garba,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,

[8] An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{53}$ $^{1}/_{2}$.

: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Alhaji sarkin hwadamar kanwa, x^2
'Y/Amshi : Mai kwana tsaye ko yaushe. x^2
Jagora : Alhaji sarkin hwadamar kanwa,
'Y/Amshi : Mai kwana tsaye ko yaushe,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Kai aj Jari da Shawai,
'Y/Amshi : Alhaji kai a Ibrahima,
: Kai ne Mainasaram mashi,
: Ina wanda ka tambaba.
Jagora : Kai aj Jari da Shawai,
'Y/Amshi : Alhaji kai a Ibrahima,
: Kai ne Mainasaram mashi,
: Ina wanda ka tambaba,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : To, sai an yi kadankarma, x^2
'Y/Amshi : A san babba a san yaro,
: Kuma sai an yi karom batta,
: A san wane a san wane. x^2

Jagora : Ai ina da Uba Sulxanin Gobir,
‘Y/Amshi : Wanda ka hisshe ni,
: Ni dai ba ni gudun hitinar Gobir,
: Duw wada tat tashi,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Ai ga taronmu na Sakkwato, x^2
'Y/Amshi : Mun gama kaya ga hawan daba,
: An shirya dawakayye,

: Amma babu kaman namu. x^2
Jagora : Doki ya hi dubu goma,
'Y/Amshi : Raqumi ya hi dubu goma,
: Duk an gamu an jera,
: Uban Shantali ya canye.
Jagora : Doki ya hi dubu goma,
'Y/Amshi : Raqumi ya hi dubu goma,
: Duk an gamu an jera,
: Uban Shantali ya canye,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Amma na ga gudan mota,
'Y/Amshi : Ga Sani makaxin Wurno,
: Sai dai ya gwada min mota,
: Na hi shi gudan doki,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Na ga Sani makaxin Wurno, x^2
'Y/Amshi : Shi an ba shi gudan mota, x^2
Jagora : Ko Sani Xandawo ya burge,
'Y/Amshi : Shi an ba shi gudan mota.

Jagora : To, ko Sanin Inyaga, x^2
'Y/Amshi : An ba shi gudan mota. x^2
Jagora : Kowa ya ba makaxinai mota,
'Y/Amshi : Ni ba ni da tau mota,
: Sarki ka qi yi min mota,
: Shin ko wani abu yag gilma.
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Kowa ya ba makaxinai mota,
'Y/Amshi : Ni ba ni da tau mota,

: Sarki ka qi yi min mota,
: Shin ko wani abu yag gilma.

Jagora : Da Garkuwa da Galadima,
'Y/Amshi : Da Baraya da Ubandoma,
: In dai ba maganak komi,
: A jawo ta a kawo ta,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Ai da Garkuwa da Galadima,
'Y/Amshi : Da Baraya da Ubandoma,
: In dai ba maganak komi,
: A jawo ta a kawo ta,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Kai aj Jari da Shawai,
'Y/Amshi : Alhaji kai a Ibrahima,
: Kai ne Mainasarar mashi,
: Ina wanda ka tambaba.

Jagora : Gohe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Duk mun ji su ga tarihi,
Jagora : Tambai ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Balarabe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Ibrahim ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Yakubu ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Jadi ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Shawai ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Jari Kada ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Salihu ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Ummaru ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Ibrahim ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,

: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : 'Yan Gatawa da Yakubawa,
'Y/Amshi : Kowane an sa shi ga tarihi,
: Haba sarki riqe tarihin ga,
: Da kowa ka bixa jiddun,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Bawa (1975 - 2003)[9]*,*
Gindin Waqa : Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki,
'Y/ Amshi : Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Na Garkuwa bajimin Sarkin Dogarrai na Galadima, x^2
'Y/Amshi : Gwarzon Ajiya Sarki uban Isihu uban Garba. x^2
: Kai ab bahagon Gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

---

[9] An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{74}$ $^{1}/_{2}$.

Jagora : Alhaji Sarkin Fadamar Kanwa, x^2
'Y/Amshi : Mai kwana shire ko yaushe. x^2

Jagora : Kai aj Jari da Shawai, x^2
'Y/Amshi : Alhaji kai a Ibrahima,
: Kai ne Mainasaram mashi,
: Ina wanda ka tambaba, x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.
Jagora : Ai ga taronmu na Sakkwato, x^2
'Y/Amshi : Mun zaka hawan daba,
: An shirya dawakayye,
: Amma babu kaman namu. x^2

Jagora : Doki ya hi dubu goma, x^2
'Y/Amshi : Raqumi ya hi dubu goma,
: Duk an gamu an jera,
: Uban Shantali ya canye, x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Na ga Sani makaxin Wurno,
'Y/Amshi : Shi an ba shi gudan mota,
Jagora : Alhaji Sani makaxin Wurno,
'Y/Amshi : Shi an ba shi gudan mota,
Jagora : Ko Sani Xandawo ya burge,
'Y/Amshi : Shi an ba shi gudan mota.
Jagora : To, har Sani Inyaga,
'Y/Amshi : Shi an ba shi gudan mota,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Kowa ya ba makaxinai mota, x^2

'Y/Amshi : Ni ba ni da tau mota,
: Sarki ka qi yi min mota,
: Shin ko wani abu yag gilma, x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Ai da Garkuwa da Galadima, x^2
'Y/Amshi : Da Baraya da Ubandoma,
: In dai ba maganak komi,
: A jawo ta a kawo ta. x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Garkuwa in na zaka na gaisai, x^2
'Y/Amshi : Sai ya yo muna sakin huska,
: Da ya duba idanuna,
: Ya san wani abu yak kai mu. x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Sarki na yi bixam mota,
: Bana han na yi zuhwah hanci,
'Y/Amshi : Ko mik kai ga zuhwah hanci,
: Ka san abu ya vaci.
Jagora : Sarki na yi bixam mota, x^2
: Bana han na yi zuhwah hanci,
'Y/Amshi : Ko mik kai ga zuhwah hanci,
: Ka san abu ya vaci, x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,

: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Kai aj Jari da Shawai, x^2
'Y/Amshi : Alhaji kai a Ibrahima,
: Kai ne Mainasarar mashi,
: Ina wanda ka tambaba. x^2

Jagora : Gohe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Duk mun ji su ga tarihi,
Jagora : Gauxe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Tambai ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Mainasara ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Ibrahim ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Jari Kada ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Balarabe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Jari Kada ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Jadi ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Shawai ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Salihu ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Ummaru ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Ibrahim ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Gwamkawa da Bacirawa, x^2
'Y/Amshi : Kowane an sa shi ga tarihi,
: Haba sarki riqe tarihin ga,
: Da kowa ka bixa jiddun.x^2

Jagora : ‘Yan Hwatawa da Yakubawa, x^2
'Y/Amshi : Kowane an sa shi ga tarihi,
: Haba sarki riqe tarihin ga,
: Da kowa ka bixa jiddun, x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.
Jagora : Haba sarki riqe tarihin ga, x^2
: Da kowa ka bixa jiddun,
'Y/Amshi : Kai kag gane mahwarinai,
: Kuma ka san wada yak qare, x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Haba sarki yi tunani, x^2
: Ka tuna tsohinka na addini,
: Na farko Abdullahi,
: Da Kaso Birnin Mai-Lalle,
: Da Dango mai Tansidi,
: Da Sardauna Sama'ila,
'Y/Amshi : Kowa ad da hwaxi Alqalawa babu kaman naka,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki. x^2

Jagora : Ai ina da Uba Sulxanin Gobir wanda ka hisshe ni, x^2
‘Y/Amshi : Ni dai ba ni gudun hitinar Gobir duw wada tat tashi, x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Ga riga mai tamburra Uban Shantali yab ba da, x^3
‘Y/Amshi : Sai yac ce mu yi cin duniya,
: Da ‘ya’yanmu da matanmu, x^3

: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Mata na ko yaushe, x^3
: Suna xunki da lishi da karen muski,
'Y/Amshi : Cikin albarkas Sarkin Gobir Bawa uban Bawa, x^3
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Sarki ya hana kamanci da Buzu da Bahillace, x^2
'Y/Amshi : Daxa kowa ya yi zavenai,
: Kai an toshe batun shirgi, x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Ga ni ina son harkar zambo, x^2
'Y/Amshi : Amma na zama mai geme,
: Kowa yaz zama mai geme,
: Ba dama shi yi shexanci, x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Ai cikin masu biyas sarki, x^2
'Y/Amshi : Wasu sun hwara munahicci,
: Bari kowa ka munahicci,
: Hwaxa mai da akwai Allah, x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,

: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Jiya can nij ji mutane, x3
: Na cewa wane hawa'i ne,
'Y/Amshi : Ko mu mun ji mutane ,
: Na cewa wane tavavve na. x3
Jagora : Alhaji sarkin hwadamar kanwa, x2
'Y/Amshi : Mai kwana shire ko yaushe. x2

Jagora : Shi wargi da hawa'i, x2
'Y/Amshi : Ya xara wargi da bugun buta,
: In sun tashi rashin kunyan nan,
: In sun gamu dux xai na, x2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Hawa'i da bugun buta ai na ce muku dux xai na, x2
'Y/Amshi : Ai had da mashayin kansu,
: Shi ma la'ananne na, x2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.
Jagora : Kai aj Jari da Shawai, x2
'Y/Amshi : Alhaji kai a Ibrahima,
: Kai ne Mainasarar mashi,
: Ina wanda ka tambaba. x2

Jagora : To, Garkuwa xan Gardaye, x2
'Y/Amshi : A gaishe ka a gaishe ka,
: Mu yi hwata ya daxe duniya,
: Ya zam ba mu abin Allah, x2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : To, Garkuwa in na zaka gaisai, x2

‘Y/Amshi : Sai yay yo min dumbulka,
: Da ya diba idanuna,
: Ya san wani abu yak kai ni. x2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Bawa (1975 - 2003)
Gindin Waqa : Kai ab bahagon gulbi,[10]
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Na Garkuwa bajimin Sarkin Dogarrai na Galadima, x2
'Y/Amshi : Gwarzon Ajiya Sarki uban Isihu uban Garba. x2
: Kai ab bahagon Gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan-Inna kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Alhaji Sarkin Fadamar Kanwa, x2
'Y/Amshi : Mai kwana shire ko yaushe. x2

Jagora : Kai aj Jari da Shawai, x2
'Y/Amshi : Alhaji kai a Ibrahima,
: Kai ne mainasaram mashi,
: Ina wanda ka tambaba. x2

Jagora : Ai ga taronmu na Sakkwato, x2
'Y/Amshi : Mun zuba kaya ga hawan daba,
: An shirya dawakayye,
: Amma babu kaman namu. x2
Jagora : Doki ya hi dubu goma, x2
'Y/Amshi : Raqumi ya hi dubu goma,
: Duk an gamu an jera,
: Uban Shantali ya canye. x2

Jagora : To, sai an yi kadankarma, x2
'Y/Amshi : A san babba a san yaro,

10 An sami wannan rerawa ne a littafin *Diwanin Waqoqin Baka.* Gusau, S.M. 2009: 204-207.

: Kuma sai an yi karon batta,
: A san wane a san wane. x^2

Jagora : Haba sarki yi tunani,
: Ka tuna tsohinka na addini, x^2
'Y/Amshi : Na farko Abdullahi,
: Da Kaso Birnin Mai-Lalle,
: Da Dango mai xan ciki,
: Da Sardauna Sama'ila,
: Kowa ad da hwaxi Alqalawa,
: Babu kaman naka. x^2

Jagora : Na ga Sani makaxin Wurno, x^2
'Y/Amshi : Shi an ba shi gudan mota, x^2
Jagora : To, ko Sanin Inyaga,
'Y/Amshi : An ba shi gudan mota,
Jagora : Ko Sani Xandawo ya burge,
'Y/Amshi : An ba shi gudan mota.
Jagora : Ko Qwairo makaxin manya, x^2
'Y/Amshi : An ba shi gudan mota. x^2
Jagora : Kowa ya ba makaxinai mota, x^2
'Y/Amshi : Ni ba ni da tau mota,
: Sarki ka qi yi min mota,
: Shin ko wani abu yag gilma. x^2

Jagora : Da Garkuwa da Galadima, x^2
'Y/Amshi : Baraya da Ubandoma,
: In dai ba maganak komi,
: A jawo ta a kawo ta. x^2
Jagora : To, Garkuwa xan Gardaye, x^2
'Y/Amshi : A gaishe ka a gaishe ni,
: Mui hwata ya daxe duniya,
: Ya zan ba mu abun Allah. x^2

Jagora : Garkuwa in na zaka na gaisai, x^2
'Y/Amshi : Sai ya yo muna sakin huska,
: Da ya duba idanuna,
: Ya san wani abu yak kai mu. x^2

Jagora : To, Inna qaunas sarki, x^2
'Y/Amshi : Ta maishe ni kamax xanta,
: Ko babu kixi naz zo,
: Sai ta ba ni abun goro. x^2

Jagora : To, Inna xiyas Sardauna, x^2
'Y/Amshi : Giwa Inna Bahillata,
: In ta kama zuba min kaya,
: Sai na gaji na rave. x^2

Jagora : Kai na Garkuwa bajimin sarki, x^2
'Y/Amshi : Gwarzon Ajiya sarki,
: Uban Isihu uban Garba. x^2
Jagora : Kai aj Jari da Shawai, x^2
'Y/Amshi : Alhaji kai a Ibrahima,
: Kai ne Mainasarar mashi,
: Ina wanda ka tambaba. x^2

Jagora : Gohe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Duk mun ji su ga tarihi,
Jagora : Gauxe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Ibrahim ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Mainasara ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Yakubu ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Tambai ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Balarabe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Na ga tsarin Yakubawa, x^2
'Y/Amshi : Kowane an sa shi ga tarihi,
: Haba sarki riqe tarihin ga,
: Da kowa ka bixa jiddun. x^{22}

Jagora : Gwamkawa da Bacirawa, x^2
'Y/Amshi : Kowane an sa shi ga tarihi,
: Haba sarki riqe tarihin ga,
: Da kowa ka bixa jiddun. x^2

Jagora : Haba sarki riqe tarihin ga,
: Da kowa ka bixa jiddun, x^2
'Y/Amshi : Kai kag gane mahwarinai,
: Kuma ka san wada yak qare. x^2
Jagora : Alhaji Sarkin Fadamar Kanwa, x^2
'Y/Amshi : Mai kwana shire koyaushe. x^2

Makaxi : Ahaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni
Waqa : Waqar Noma[11]*,*
***07.** Gindin Waqa : Na yi hamdala nai shukura da godewa,*
: Tun da na sani noma yau farilla ne.

Jagora : Maza ku kama noma noma abin yi ne,
'Y/Amshi : Don na ga ba a gumba in ba da tsaba ba,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau farilla ne.

Jagora : Maza ku kama noma noma abin yi ne,
'Y/Amshi : Yau na ga ba a gumba in ba da tsaba ba.
Jagora : Shi wanda ba shi noma ya zam abin tausai,
'Y/Amshi : Yana bixar awo mata na harara tai,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau farilla ne.

Jagora : Na zo Maraxi na ishe an sare dajinsu, x^2
'Y/Amshi : Mutum guda ya ce shi xai za shi nome su. x^2
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau farilla ne.

Jagora : Gandun Xangara yai gandu ko ga 'yan dauri, x^2
'Y/Amshi : In yanzug ga ba gandu mai misalinai. x^2
Jagora : Gandun Xangara ya yi gabas mil xari sittin,
: Na yi yamma na diba mil xari sittin,
: Gandun Xangara ya yi Gusum mil xari sittin,
: Kuma nai arewa na diba mil xai sittin,
'Y/Amshi : Abin da za a yi ciki ab ba mu gane ba,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau farilla ne.

Jagora : In za a sussukak damma sai a yo gayya, x^2
: Makobiya dubu kowace ta yi buhu maitan, x^2

---

11 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{375}$ $^1/_{13}$.

‘Y/Amshi : Ai sai a yo kiran ‘yan boko ku lisafta.
Jagora : In munka lissahwa kuma munka nunhwasa, x^2
‘Y/Amshi : Ai babu wanda bai san Allah ka iko ba.x^2
Jagora : Allah ya yi ruwa mun shisshikke gonakki,
: Sai da munka shibke,
‘Y/Amshi : Abin da za a yi ciki Allah ka gyarawa,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau farilla ne.

Jagora : Maza ku kama noma noma abin yi ne, x^2
‘Y/Amshi : Yau na ga ba a gumba in ba da tsaba ba. x^2

Jagora : Shi wanda ba shi noma ya zam abin tausai, x^2
‘Y/Amshi : Yana bixar awo mata na harara tai,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau farilla ne. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni
Waqa : Waqar Noma[12]*,*
Gindin Waqa : Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na.

Jagora : Maza ku kama noma noma abin yi na, x2
'Y/Amshi : Don na ga ba a gumba in ba da tsaba ba, x2
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na.

Jagora : Wanda ba shi noma ya zam abin tausai,
'Y/Amshi : Yana bixar awo mata na harara tai,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na.

Jagora : Qattanga masu yawo ba su kama aiki ba, x2
'Y/Amshi : Sabadda su tiyar gero ba ta shixowa, x2
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na.

Jagora : Inda wada munka noma kowa shi zai yi na,
'Y/Amshi : Da yanzu ai tiyar gero ba ta kai zangu,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na.

Jagora : Na zo Maraxi na ishe an sare dajinsu,
'Y/Amshi : Mutum guda ya ce shi xai za shi nome su,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na.

Jagora : In munka lissafa kuma in munka lumfasa,
'Y/Amshi : Babu wanda bai san Allah ka iko ba,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na.

Jagora : Allah ya yi ruwa mun shikkikke gonakki, x2

12 An sami wannan rerawa ne a littafin *Diwanin Waqoqin Baka.* Gusau, S.M. 2009: 197-203.

‘Y/Amshi : Sai da munka shikke kuma munka nomikke, x^2
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na.

Jagora : Da munka nome kuma munka maimaice, x^2
‘Y/Amshi : Abin da za a yi ciki Allah ka gyarawa, x^2
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na.

Jagora : Allah shi fallala kuma Allah shi umfana, x^2
‘Y/Amshi : Allah shi ceci mai iya aiki ga aikinai, x^2
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na.

Jagora : Xangara ka yi lambuwal kuma an yo ka lamba xai,
‘Y/Amshi : Saboda in kana nan komai ba shi motsawa,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na.

Jagora : Maza ku kama noma noma abin yi na, x^2
‘Y/Amshi : Don na ga ba a gumba in ba da tsaba ba,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni

Mai Waqa : Alhaji Hashimu D. P.O na Gusau[13]*,*

08. *Gindin Waqa : Na shira kaya za ni garai,*
: Na Alhaji D. P. O na Gusau.

Jagora : Allah ka ruwa, Allah ka hatsi,
'Y/Amshi : Kuma Allah yay yo masu gari,
: Kuma yas shirya bayam masu gari,
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.

Jagora : Tun dan nan hab bisa birnin Ikko gari, x^2
'Y/Amshi : Babu inda ba a san Yawuri ba, x^2
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.

Jagora : Toronku na Yawuri ya yi tsawo, x^2
'Y/Amshi : Jibirila yas shirya maku shi,
: Tun da ba uban wani yay yi shi ba, x^2
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.

Jagora : Abdullahi ya yi mulki Yawuri,
'Y/Amshi : Hay ya gama shi bai sava muku ba, x^2
: Tun da ko ga sohi munka cira. x^2
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.

Jagora : Sani Xandawo ya leqa mani,
'Y/Amshi : Yac ce Yawuri ta burma da gari,
: Abin da yag ga ta burma da gari,
: Tun da ko akwai manyan masana,
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.

Jagora : Na Garkuwa na Ali mai sango, x^2
'Y/Amshi : Bajinin Bunu abin ka ya koma izini,

---

13 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{51}$ $^1/_3$ - AL $^0/_{74}$ $^1/_1$.

: Ko da yaushe kura tahi gari. x^2

Jagora : Maidaji cikin daji nike,
'Y/Amshi : Hashimu yi tattalin mai da ni gari,
: Tun da ba Bahillace nike ba,
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.
Jagora : Maidaji cikin daji nike, x^2
'Y/Amshi : Hashimu yi tattalin mai da ni gari,
: Tun da ba Bahillace nike ba, x^2
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.

Jagora : Hashimu uban tawaye, x^2
'Y/Amshi : Hashimu dum mai biyak ka,
: Ya huta da tsiya sai ya sami kuxxi yai shagali, x^2
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.

Jagora : Allah ka ruwa, Allah ka hatsi, x^2
'Y/Amshi : Kuma Allah yay yo masu gari,
: Kuma yas shirya bayam masu gari. x^2

Jagora : Hashimu shira ka maisan Yawuri, x^2
'Y/Amshi : Ka san ban iya auren xauki kwari, x^2
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.

Jagora : Hashimu uban tawaye,
'Y/Amshi : Hashimu dum mai biyak ka,
: Ya huta da tsiya sai ya sami kuxxi yai shagali,
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.

Jagora : Hashimu ina yi ma hwata, x^2
'Y/Amshi : Allah dai ya qaddara Allah ya nuhwa,
: Don a karvi hwata tare da mu,

: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau. x^2

Jagora : ‘Ya’yana suna yi ma hwata, x^2
'Y/Amshi : Allah dai ya qaddara Allah ya nuhwa,
: Don ya karvi hwata tare da mu, x^2
Jagora : Matana suna yi ma hwata, x^2
'Y/Amshi : Allah dai ya qaddara Allah ya nuhwa,
: Don ya karvi hwata tare da mu, x^2
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.

Jagora : Na Garkuwa na Ali mai sango, x^2
'Y/Amshi : Bajinin Bunu abinka ya koma izini,
: Ko da yaushe kura tahi gari. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,

Alhaji Ummaru xan Salihu (1957-1966)[14]*,*

09. *Gindin Waqa : Gagari gaba na Salihu,*
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Gwamron giwa,
'Y/Amshi : Uban lihidda Bawa qanin Sahi bahago,
: Jari magajin na Abu,
: Ko da yaushe yana nan wurin jiya,
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Ashe Allah shi ka bajini, x^2
'Y/Amshi : Kuma Allah shi ka xaukaka,
: To, Allah shi ka yin mazakkari,
: Ya shirya mai abubuwa. x^2

Jagora : To Allah shi ad da duniya, x^2
'Y/Amshi : Kuma Allah shi ad da Lahira,
: Allah yay yo shirye-shiryen,
: Da za a shirawa na duniya, x^2
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Ina wani mai jan damamisau,
'Y/Amshi : Ku ce ya bari in yana bari,
: In ba ya bari sai ku bar shi,
: Tun da mu maganag gaskiya mukai.

Jagora : Yanzu ina wani mai ‘yak kara-kara,
'Y/Amshi : Ku ce ya bari in shina bari,
: In ba ya bari sai ku bar shi,
: Tun da mu maganag gaskiya mukai.

---

14 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{143}$ $^1/_4$.

Jagora : Toron giwa ya katse haqo, x^2
'Y/Amshi : Masu haqon sun yi birkixa,
: Ku kwashe haqon nan ku tashi,
: Tun da Bawa na Dango gani yakai, x^2
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Na Inna magajin sarauniya,
'Y/Amshi : Ruwan dare mai kama duniya,
: In dai kyauta ta Bawa,
: Ko da yaushe qira min wata yakai.
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Gwamron giwa,
'Y/Amshi : Uban lihidda Bawa qanin Sahi bahago,
: Jari magajin na Abu,
: Ko da yaushe yana nan wurin jiya.

Jagora : Na Inna magajin sarauniya,
'Y/Amshi : Ruwan dare mai kama duniya,
: In dai kyauta ta Bawa,
: Ko da yaushe qira min wata yakai.

Jagora : To, na zo salla uban lihidda, x^2
'Y/Amshi : Ya yi mini kaya iri-iri,
: Ga shadda anka ba ni,
: Wadda babu iri ko qasar Masar. x^2

Jagora : Ga ni ina son vacin tcibilbila,
'Y/Amshi : Zaman zauri xai nika gudu,
: In zauri ya buwaya yanzu,
: Ko ga itace zama takai.
: Gagari gaba na Salihu,

: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : To, na so in vaci hakimin sarki,
'Y/Amshi : Rowan nan da yat tcira,
: Baqar Rowan nan da yat tcira,
: Da hwari shi ka sa mu tsira xumumuwa.
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Maza ku yi wasa da dariya,
'Y/Amshi : Ku zan ki gamawa da hwara'a,
: Mai rowa ko da yaushe,
: Kag gane shi da lauje cikin naxi.
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Shin Mainasara ne Balarabe ne? x^2
'Y/Amshi : Yakuba ne ko Mayaqi ne?
: Ka koma shiri xan Halima,
: Kak ka zo ka ji tsoron mazan kawai. x^2
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni[15]*,*
Alhaji Ummaru xan Salihu (1957-1966),
Gindin Waqa : Gagari gaba na Salihu,

15 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{143}$ $^1/_5$

: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu magajin gidan Kada.

Jagora : Gwamron giwa uban lihidda Bawa qanin Sahi Bahago,
'Y/Amshi : Jari magajin na Abu ko da yaushe yana nan wurin jiya.

Jagora : Gwamron giwa,
'Y/Amshi : Uban lihidda Bawa qanin Sahi Bahago,
: Jari magajin na Abu,
: Ko da yaushe yana nan wurin jiya,
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Ashe Allah shi ka bajini, x^2
'Y/Amshi : Kuma Allah shi ka xaukaka,
: To, Allah shi ka yi mazakkari,
: Ya shirya mai abubuwa. x^2

Jagora : To Allah shi ad da duniya, x^2
'Y/Amshi : Kuma Allah shi ad da Lahira,
: Allah yay yo shirye-shiryen,
: Da za a shirawa na duniya, x^2
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Ina wani mai jan damamisau,
'Y/Amshi : Ku ce ya bari in yana bari,
: In ba ya bari sai ku bar shi,
: Tun da mu maganag gaskiya mukai.

Jagora : Yanzu ina wani mai ‘yak kara-kara,
'Y/Amshi : Ku ce ya bari in shina bari,
: In ba ya bari sai ku bar shi,
: Tun da mu maganag gaskiya mukai.

Jagora : Toron giwa ya katse haqo, x^2
'Y/Amshi : Masu haqon sun yi birkixa,
: Ku kwashe haqon nan ku tashi,

: Tun da Bawa na Dango gani yakai, x^2
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Shin Mainasara ne Balarabe ne, x^2
'Y/Amshi : Yakuba ne ko Mayaqi ne,
: Ka koma shiri xan Halima,
: Kak ka zo ka ji tsoron mazan kawai. x^2

Jagora : Kai ad da dubun arziki, x^2
'Y/Amshi : Uban Ali uban Audu Markaxe,
: Gobir babu irin wanda ya yi,
: Wadda na Sardauna yas shirya. x^2

Jagora : Ya gina makwanci na Bawa,
'Y/Amshi : Jangwarzo sannan ya yi shigihwa,
: Ko wada yai azama ya isa,
: Abin da yai nuhi an yi an gama,
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Gwamron giwa,
'Y/Amshi : Uban lihidda Bawa qanin Sahi bahago,
: Jari magajin na Abu,
: Ko da yaushe yana nan wurin jiya.

Jagora : Na Inna magajin sarauniya,
'Y/Amshi : Ruwan dare mai kama duniya,
: In dai kyauta ta Bawa,
: Ko da yaushe qira min wata yakai.

Jagora : To, na zo salla uban lihidda, x^2
'Y/Amshi : Ya yi mini kaya iri-iri,
: Ga shadda anka ba ni,
: Wadda babu iri ko qasar Masar. x^2

Jagora : Ga ni ina son vacin tcibilbila,
'Y/Amshi : Zaman zauri xai nika gudu,
: In zauri ya buwaya yanzu,
: Ko ga itace zama takai.
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : To, na so in vaci hakimin sarki,
'Y/Amshi : Rowan nan da yat tcira,
: Baqar Rowan nan da yat tcira,
: Da hwari shi ka sa mu tsira xumumuwa.
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Maza ku yi wasa da dariya,
'Y/Amshi : Ku zan ki gamawa da hwara'a,
: Mai rowa ko da yaushe,
: Kag gane shi da lauje cikin naxi.
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Gwamron giwa,
'Y/Amshi : Uban lihidda Bawa qanin Sahi bahago,
: Jari magajin na Abu,
: Ko da yaushe yana nan wurin jiya.

Jagora : To, na ji darajja ga Gobirawa, x^2
'Y/Amshi : Kullum haske taka ta yi,
: A zam magannar nan ta yanzu,
: To, a bar maganar shekaranjiya. x^2

Jagora : Ta-na-ta-hu ba Cilu-Cilu ba,
'Y/Amshi : Alhaji kai a Baranqwame,
: Tun da ina nan gare ka,
: Ba Uban da ka sa min baqingawai ,

: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Toron giwa ya katse haqo, x^2
'Y/Amshi : Masu haqon sun yi birkixa,
: Ku kwashe haqon nan ku tashi,
: Tun da Bawa na Dango gani yakai. x^2
Jagora : Ina wani mai jan damamisau,
'Y/Amshi : Ku ce ya bari in yana bari,
: In ba ya bari sai ku bar shi,
: Tun da mu maganag gaskiya mu kai.
Jagora : Yanzu ina wani mai ‘yak kara-kara,
'Y/Amshi : Ku ce ya bari in shina bari,
: In ba ya bari sai ku bar shi,
: Tun da mu maganag gaskiya mu kai.

Jagora : Lalle Gudal ya ba ni, x^2
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo. x^2
Jagora : Galadima ya yi taimako,
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo.
Jagora : A gai da Giye ya yi taimako,
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo.
Jagora : Sarkin Noma ya yi taimako,
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo.
Jagora : Sani Nalabo ya yi taimako,
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo.
Jagora : Magajin Tsamaye ya yi taimako,
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo.
Jagora : Durumbu da ya ba da taimako,
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo.
Jagora : Sarkin Rahi ya yi taimako,
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo,
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : To, na yi karatu da ilmi, x^2
'Y/Amshi : Har na sabka na yi shinhixa,
: Xiyana sun kama Sabbi,

: Yanzu diba takardu kaxai mukai, x^2
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Ashe Allah shi ka bajini, x^2
'Y/Amshi : Kuma Allah shi ka xaukaka,
: To, Allah shi ka yi mazakkari,
: Ya shirya mai abubuwa. x^2

Jagora : Ashe kyawon xan Bagobiri, x^2
'Y/Amshi : Ya kwan da shirinai,
: Shirin hwaxa ya rinqa tunawa da,
: Lanqwahe bakin maza yakai, x^2
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni
Mai Waqa : Innar Gobir Sabon Birni[16]*,*
10. *Gindin Waqa : Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,*
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa, x^2
'Y/Amshi : Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa. x^2

Jagora : Sannu da sirdi, x^2

16 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{375}$ $^1/_3$.

‘Y/Amshi : Ta Bawa da ke 'yar Muhammadu,
: Yau kasa uwar macizai ta kama sirdi, x^2
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Inna hwarar uwa,
'Y/Amshi : Ta Dango, to, gode Allah ke ar 'yar Balarabe,
: Kya san ya kamata,
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : To, Inna ina ganin ki,
'Y/Amshi : Lalle kya 'yam ma harka,
: Tun da duk abin da kic ci,
: Sai kin 'yam ma dangi,
Jagora : Ke a uwar,
'Y/Amshi : Maroqan birni da qauye,
: In kya haihwa xa kuma xa Audu,
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Darzaza,
'Y/Amshi : Ta Bawa ko ba wuri ki hurce,
: Duk inda kib biya sai kowa ya wadata,
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.
Jagora : Zamaninki da ni da yarana mun wadata, x^2
'Y/Amshi : Ita ta ba mu riguna kuma ta ba mu zanna,
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa. x^2

Jagora : Abin da ag ga amarya, x^2
'Y/Amshi : Shi taka kai ma ango,
: Abin da ag gare ni yau,
: Shi zan kai ma Inna. x^2
Jagora : Kya san ban da, x^2
'Y/Amshi : Raguna in ta zo mu yanka,
: Babu abin da ag garan sai turu da waqa, x^2
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,

: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Na zaka in yi godiyar riga in da Inna,
'Y/Amshi : To, in za ki ba ni wata kak ki fasa.
Jagora : To, Inna kwakwatad,
'Y/Amshi : Da kinka ban na bam ma yaro,
: Kai yaro ina yi ma horo don ka xauka,
: Don ka ga Inna ta ban tsaba kak ka sai da,
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Tsahe da niz zo kixa,
'Y/Amshi : Inna ta ba ni kore-koren nan,
: Ko ya zo da sa'a,
: Bara da za ni Makka can nis saisai ga hanya,
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Alhaji na xauri anniyar, x^2
'Y/Amshi : In zo gai da Inna,
: To, amma da ban zuwa sai na fara xinki. x^2
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : To, Inna kya gane ni ‘yar rigata guda ta, x^2
'Y/Amshi : Ita an nan cikin gida, ita ag ga daji,
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa. x^2

Jagora : Mai riga guda ina addini gare shi, x^2
'Y/Amshi : Ko ya so zuwa masallaci sai ya fasa,
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa. x^2

Jagora : Inna hwarar uwa ta Dango,
'Y/Amshi : Ta gode Allah,
: Ke 'yar Balarabe ta san ya kamata,
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Sannu da sirdi, x^2
‘Y/Amshi : Ta Bawa da ke 'yar Muhammadu,
: Yau kasa uwar macizai ta kama sirdi, x^2
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa, x^2
'Y/Amshi : Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni
Mai Waqa : Innar Gobir Sabon Birni[17]*,*
Gindin Waqa : Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa, x^2
'Y/Amshi : Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa. x^2

Jagora : Sannu da sirdi ta Bawa, x^2
‘Y/Amshi : Sannu da gaishe da Allah,
: Yau Kasa uwar macizai ta kama sirdi. x^2

---

17 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{143}$ $^1/_3$ - AL $^1/_{145}$ $^1/_6$.

Jagora : Inna hwarar uwa ta Dango ta gode Allah, x^2
'Y/Amshi : Jikanyar Balarabe ta san ta kamata, x^2
: Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : To, na zaka in yi godiyar riga inda Inna,
'Y/Amshi : To, in za ki ba ni wata amma kak ki hwasa,
: Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora: To, Inna kwakwatad da kib ban na bar ma yaro, x^2
'Y/Amshi : To, kai yaro ina yi ma horo don ka xauka, x^2
: To, don ka ga babu tsaba don kak ka sai da,
: Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Bara da niz zo kixi ga Inna ta ba ni Kore,
'Y/Amshi : Koren nan ko da tay yi min ya zo da sa'a,
: Bara da za ni Makka can nis saisai ga hanya,
: Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Alhaji na yi anniya in zo gai da Inna, x^2
'Y/Amshi : To, amma hwa ban zuwa sai na hwara xinki. x^2
Jagora : To, Inna kya gane ni riga ta ‘yar guda ta,
'Y/Amshi : Ita an nan cikin gida ita an nan ga daji,
: Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Mai riga guda ina addini gare shi,
'Y/Amshi : Ko ya so zuwa masallaci sai ya hwasa,
: Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Abin da ag ga amarya shi taka kai ma ango, x^2
'Y/Amshi : Abin da ag gare ni yau shi zan kai ma Inna. x^2

Jagora : Kya san ban da raguna in ta zo mu yanka,

'Y/Amshi : Babu abin da ag garan sai turu da waqa,
: Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Da zamaninki ni da yarana mun wadata, x^2
'Y/Amshi : Ita ta ba mu riguna, kuma ta ba mu zanna. x^2

Jagora : Iya ke a uwar maroqan birni da qauye,
'Y/Amshi : In kya haihwa xa kuma xa Audu,
: Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Darzaza ta Bawa ko ba wuri ki hurce,
'Y/Amshi : Duk inda kib biya sai kowa ya wadata,
: Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003)[18]*,*

11. *Gindin Waqa : Sarki Muhammadu xan Kilo,*
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Dagga abin da Allah ya shirya, x^2
'Y/Amshi : Sai wanda Annabi yas shirya,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai. x^2

Jagora : Shiryayye na Dango,
'Y/Amshi : Xan Inna fifita ni na Malam Salihu,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

---

18 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{374}$ $^1/_7$.

Jagora : Uban na Inda Baban Makama,
‘Y/Amshi : Bawa arkunniyab bakin dawa,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Yau kai a Muhammadu Babari, x^2
: Kai a Muhammadu Maijindi
‘Y/Amshi : Kai a Muhammadu na Dango,
: Wada duk ka hwaxa daidai kake, x^2
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Taron gamon Alqalawa,
‘Y/Amshi : Dac can mun wuce Sabon Birni,
: Ga yau Bawa ab babbansu,
: Ce ma kowa ya zamna lahiya,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.
Jagora : Sarki ga wasiqa na,
‘Y/Amshi : Shirya, sai na karanta ka jiya,
: Ai ko ga iska nab buga,
: Uban Yari ganewa ya kai,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Ya ban buhuhuwa a yi man tuwo,
‘Y/Amshi : Ya ban kuxi in sai miya,
: Amma kayan in mun canye su,
: Xan Inna dawowa mu kai.
Jagora : Fam goma sha biyar Sarki yab bai,
‘Y/Amshi : Yac ce mu sai kajin miya,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Zamanin Muhammadu xan Kilo,
‘Y/Amshi : An ba mu Naira zay yawa,
: An ba mu manyan riguna.
Jagora : In ka ganan da shadda tsanwa shar,

‘Y/Amshi : Garko ka shiryar man ita,
: In ka ganan da kwakwata,
: Magajin gari ka yi min ita,
: In ka gane ni da jikak Kano,
: To, wadda Inna kai min ita.
Jagora : To, kuma in ka ganan da wandon Kano,
‘Y/Amshi : To, wanda Inna tay yi na.
Jagora : A gaishe ki Inna,
‘Y/Amshi : ‘Yar Kilo xiyag Garba manyan duniya,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Shiryayye na Dango, x^2
‘Y/Amshi : Xan Inna fifita ni na Malam Salihu,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai. x^2

Jagora : Dauri babu kwano Sabon Birni,
‘Y/Amshi : To, zamanin baban Sule,
: Na ga yanzu kwano yai yawa.
Jagora : Dauri babu mota Sabon Birni,
‘Y/Amshi : To, zamanin baban Sule,
: Na ga yanzun mota tai yawa.
Jagora : Dauri babu hwanda Sabon Birni,
‘Y/Amshi : To, zamanin baban Sule,
: Na ga yanzu hwanda yai yawa.
Jagora : Dauri babu shadda Sabon Birni,
‘Y/Amshi : To, zamanin baban Sule,
: Na ga yanzu shadda tai yawa.
Jagora : Dauri babu famfo Sabon Birni,
‘Y/Amshi : To, zamanin baban Sule,
: An shirya famfo zar ruwa,
: Saura a sa mana tsakkuwa da kwalta,
: A shahe godabe,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : In dai kag ga na yi gaba Gusun,
‘Y/Amshi : Na tuna da sarkin tasha,

: Ya saba shirya man kuxi,
: Naira xari in zan kashi,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : In ko ka gan ni kunku,
'Y/Amshi : Alhaji E. O. nit tuna,
: E. O. baturen gaskiya,
: E. O. baturen gwamnati,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Sarki swahe duk roqo nikai x^2
'Y/Amshi : Da Shawai da Inna da Altine,
: Allah ya gafarta masu. x^2

Jagora : Da Jadi da Jari da Xanfama,
'Y/Amshi : Sun sare daji sun tushe,
: Mu yanzu girbi xai mu kai,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : In ka ga xan hwarauta yai shiri, x^2
'Y/Amshi : Ga karhuna ga kambuna,
: In ba kare ya taho gidan,
: Qaryah hwarauta ta yakai, x^2
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Yau kai am Muhammadu Babari, x^2
: Kai am Muhammadu Maijindi
'Y/Amshi : Kai am Muhammadu na Dango,
: Wanda duk ka hwaxa daidai kake, x^2
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Shiryayye na Dango, x^2
'Y/Amshi : Xan Inna fifita ni na Malam Salihu, x^2
: Sarki Muhammadu xan Kilo,

: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Dagga abin da Allah ya shirya, x^2
'Y/Amshi : Sai wanda Annabi yas shirya,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003)[19]*,*
Gindin Waqa : Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Sarki Muhammadu yai shiri, x^2
'Y/Amshi : Kowa ya saurara mashi,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai. x^2

Jagora : Dagga abin da Allah yas shirya,
'Y/Amshi : Sai wanda Annabi yas shirya,
: Sarki Muhammadu yai shiri,
: Kowa ya saurara mashi,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Shiryayye na Dango xan Inna, x^2

---

19 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{144}$ $^1/_3$ - AL $^1/_{145}$ $^1/_4$.

‘Y/Amshi : Qi da arna na Malam Salihu. x^2
Jagora : Uban Lihidda baban Makama,
‘Y/Amshi : Bawa arkunniyab bakin dawa,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Yau kai am Muhamman Babari,
: Kai am Muhamman Maijiddi
‘Y/Amshi : Kai am Muhamman na Dango,
: Wanda duk ka hwaxa daidai kake.
Jagora : To, kai a Muhamman Babari,
: Kai am Muhamman Maijiddi,
‘Y/Amshi : Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.
Jagora : Taron gamon Alqalawa,
‘Y/Amshi : Dac can mun wuce Sabon Birni,
: Ga yau Bawa ab babbansu,
: Ce ma kowa ya zamna lahiya,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Sarki ga wasiqa na shirya,
‘Y/Amshi : Sai na karanta ka jiya,
: Ai ko ga iska nab buga,
: Uban Yari ganewa yakai.
Jagora : Ya ban buhuhuwa a yi min tuwo,
‘Y/Amshi : Ya ban kuxi in sai miya,
: Amma kayan in mun canye su,
: Xan Inna dawowa mukai,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Zamanin Muhammadu xan Kilo, x^2
‘Y/Amshi : An ba mu Naira zay yawa,
: An ba mu manyan riguna. x^2
Jagora : In ka ganan da shadda tsanwa shar,
‘Y/Amshi : Garko ka shiryar man ita,

: In ka gane ni da kwakwata,
: Magajin gari ka yi min ita,
: In ka gane ni da jikak Kano,
: To, wadda Inna kai min ita.
Jagora : To, kuma in ka ganan da wandon Kano,
'Y/Amshi : To, wanda Inna tay yi na.
Jagora : A gaishe ki Inna 'yar Kilo,
'Y/Amshi : Xiyag Lubba manyan duniya,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Sarki swahe duk roqo nikai
'Y/Amshi : Da Shawai da Inna da Argiji,
: Allah ya gahwarta musu,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Da Jadi da Jari da Xantsara, x^2
'Y/Amshi : Sun sare daji sun tushe,
: Mu yanzu girbi xai mu kai. x^2

Jagora : Dauri babu kwano Sabon Birni,
'Y/Amshi : To, zamanin baban Sule,
: Na ga yanzu kwano yai yawa.
Jagora : Dauri babu mota Sabon Birni,
'Y/Amshi : To, zamanin baban Sule,
: Na ga yanzun mota tai yawa.
Jagora : Dauri babu hwanda Sabon Birni,
'Y/Amshi : To, zamanin baban Sule,
: Na ga yanzu hwanda yai yawa.
Jagora : Can dauri babu shadda Sabon Birni,
'Y/Amshi : To, zamanin baban Sule,
: Na ga yanzu shadda tai yawa.
Jagora : Dauri babu famfo Sabon Birni,
'Y/Amshi : To, zamanin baban Sule,
: An shirya famfo zar ruwa,
: Saura a sa mana tsakkuwa da kwalta,

: A shahe godabe,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : In ka ga xan hwarauta yai shiri,
'Y/Amshi : Ga karhuna ga kambuna,
: In ba kare ya taho gidan,
: Qaryah hwarauta ta yakai,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa,
Mai Waqa : Innar Gobir[20]*,*
12. *Gindin Waqa : Gagarabadau 'Yakkaso,*
: Ta Muhamman Dosau 'yam mayaqi.

Jagora : Hazo jice rana,
'Y/Amsh : Goge mai kashe molo,
: Gogarma ta Iro.
: Gagara badau 'yak Kaso,
: Ta Muhamman Dosau 'yam mayaqi.

Jagora : Hazo jice rana, x^2
'Y/Amsh : Goge mai kashe molo,
: Gogarma ta Iro. x^2

Jagora : Ta Alhaji Madogara, x^2
'Y/Amshi : Inna ta yi gadon Ali qanen Mayaqi. x^2
: Gagarabadau 'yak Kaso,
: Ta Muhamman Dosau 'yam mayaqi.

Jagora : In na tsira hillanci, x^2
'Y/Amshi : Inna sai ta gane,

---

20 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{143}$ $^1/_4$ - AL $^1/_{145}$ $^1/_5$.

: Ba sai na hwaxi ba. x^2
Jagora : Hillancin ga da nis samo,
'Y/Amshi : Inna ko xiyan hillani ba su yi nai,
: Gagarabadau 'yak Kaso,
: Ta Muhamman Dosau 'yam mayaqi.

Jagora : Yara ku bar wani hillanci,
'Y/Amshi : Duk abun da ta saba shi za ta ban ne.
: Gagarabadau 'yak Kaso,
: Ta Muhamman Dosau 'yam mayaqi.
Jagora : Hito bari gaugawa, x^2
'Y/Amshi : Yad durumbu Inna taka sannu-sannu. x^2
Jagora : Nan qasaf fadamar Kanwa, x^2
'Y/Amshi : Ko da wane hali,
: Ba wani mai wuce ki,
: Gagarabadau 'yak Kaso,
: Ta Muhamman Dosau 'yam mayaqi. x^2

Jagora : Jikanyar Jari shirarra,
'Y/Amshi : Sannu da niyya,
: Sannu da yau da gobe,
Jagora : Jikanyar mai hana noma,
'Y/Amshi : Sannu da niyya,
: Sannu da yau da gobe,
Jagora : 'Yam mai dala da rani,
'Y/Amshi : Sannu da niyya,
: Sannu da yau da gobe,
: Gagarabadau 'yak Kaso,
: Ta Muhamman Dosau 'yam mayaqi.

Jagora : Inna ke nika kallo, x^2
'Y/Amshi : Ke nika dibi,
: Ba dibin kawai ba. x^2

Jagora : Uwab Bunu uwas Salau, x^2
'Y/Amshi : Mai rabo ga Allah,
: Mai kullum zumunta, x^2
: Gagarabadau 'yak Kaso,
: Ta Muhamman Dosau 'yam mayaqi.

Jagora : Ta Alhaji Madogara, x^2
'Y/Amshi : Inna ta yi gadon Ali qanen Mayaqi.
: Gagarabadau 'yak Kaso,
: Ta Muhamman Dosau 'yam mayaqi. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Zazzau,
Alhaji Shehu Idris (1975-)[21]*,*

13. *Gindin Waqa : Uban Na Allah uban Madauci ,*
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Alhaji Mani ba shi qin kowa, x^2
: Komi kac ce yanai ma,
: Don bai tsare qa'ida ba, x^2
'Y/Amshi : Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki Uban Iya, x^2
'Y/Amshi : Bajimin Madami,
: Na zaka in gai da qulle-qulle. x^2

Jagora : Ga wani ya tsara qulle-qulle, x^2
'Y/Amshi : Yau daxa qarya ta qule mai,
: Yau wane ba haka nan a kai ba,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe. x^2

Jagora : Sanqira zo za ni saqo,
'Y/Amshi : Ga saqo nan zan gaya ma,
: Sai ka tashi ka iy da saqo.

Jagora : Ga motoci ba iyaka,

---

21 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{50}$ $^1/_1$.

‘Y/Amshi : Sai a sami guda a ba mu,
: Uban Na Allah uban Madauci .

Jagora : Sarki da hanquri aka tsara taro, x^2
‘Y/Amshi : Ka diba duk kwararon qasag ga,
: Duk Shehu, Alhaji ya haxe su, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.
Jagora : Aminu ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Muhammadu ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Yamusa ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Yamusa ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Kuma Kabiru ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Yamusa ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Xahiru ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Muhammadu ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Abdulkarimu ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Alhaji Shata ya hwaxa man, x^2
‘Y/Amshi : Ya ce Zariya ba a zambo,
: In makixi yas shirya zambo,

: Alhaji wawa na buge shi da gora,
: Yanzu ta hau wuyanai, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Malam Na-Allah, x^2
: Sannu da kai-da-kawo,
'Y/Amshi : Ya je Legas lahiya lau,
: Ya zaka lahiya lau, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Jekadiyar Zazzau Bagobira, x^2
'Y/Amshi : Allah ya daxe da ranta,
: Tun da ba ta buki da wasa, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : To, matana bana sun yi dace, x^2
'Y/Amshi : Kai ko da gani,
: Ga saqo ka ce ba su wuri da kansu, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki uban Iya, x^2
'Y/Amshi : Bajimin Madami,
: Na zaka in gai da qulle-qulle, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Birnin Zazzau za ni sabka, x^2
'Y/Amshi : In ishe sarki lahiya lau,
: Don mu sami abin tavawa, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Zazzau,
Alhaji Shehu Idris (1975-)[22]*,*
Gindin Waqa : Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Alhaji Mani ba shi qin kowa,
: Komi kac ce yanai ma,
: Shehu bai iya za'ida ba,
'Y/Amshi : Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Birnin Zazzau za ni sabka, x^2
'Y/Amshi : In ishe sarki lahiya lau,
: Don mu sami abin tavawa. x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki Uban Iya, x^2
'Y/Amshi : Bajimin Madami,
: Don kak ka yadda da qulle-qulle. x^2

Jagora : Ga wani ya tsira qulle-qulle,
'Y/Amshi : Ya naxa qarya ta qule mai,
: Yau wane ba haka nan a kai ba.
Jagora : Ga wani ya tsira xame-xame,
'Y/Amshi : Ya naxa qarya ta qule mai,
: Yau wane ba haka nan a kai ba,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

---

22 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{75}$ $^1/_1$.

Jagora : Alhaji Shata ya hwaxa min, x^2
‘Y/Amshi : Yac ce Zariya ba a zambo,
: Dum makixi yas shirya zambo,
: Alhaji wawa na buge shi da gora,
: Yanzu ta hau wuyanai, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Ai da hanquri aka tsara taro,
‘Y/Amshi : Ka diba duk kwararon qasag ga,
: Duk Shehu, Alhaji ya haxe su.
Jagora : Sarki da hanquri aka tsara taro,
‘Y/Amshi : Ka diba duk kwararon qasag ga,
: Duk Shehu, Alhaji ya haxe su,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Kabiru ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : To, Jahwaru ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Muhammadu ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Yamusa ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Muhammadu ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Abdulkarimu ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu,
: Uban Na Allah uban Madauci , x^3
: Shehu sannu da yau da gobe. x^3

Jagora : Sarki ya xauke marayu,
‘Y/Amshi : Ga kuma ya xau mai uwaye,
: Shehu Alhaji ya save su.
Jagora : Sarki ya xauke guramu,
‘Y/Amshi : Ga kuma ya xau mai qahwahu,
: Shehu Alhaji ya save su.
Jagora : Sarki ya xauke makahi,
‘Y/Amshi : Ga kuma ya xau mai idanu,
: Shehu Alhaji ya save su,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki uban Iya, x^2
‘Y/Amshi : Bajimin Madami,
: Don kak ka yadda da qulle-qulle. x^2

Jagora : Sanqira zo za ni saqo,
‘Y/Amshi : Ga saqo nan zan hwaxa ma,
: Sai ka tashi ka iy da saqo.
Jagora : Alhaji Sanqira zo za ni saqo,
‘Y/Amshi : Ga saqo nan zan hwaxa ma,
: Sai ka tashi ka iy da saqo,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Naira xari bakwai Sarki yab ba ni,
‘Y/Amshi : In bayanka uban Madauci ,
: Babu mai kyauta hakan ga.
Jagora : Naira xari bakwai Sarki yab bak kan,
‘Y/Amshi : In bayanka uban Madauci ,
: Babu mai kyauta hakan ga.
Jagora : Riga ishirin Sarki ya ban ni,
‘Y/Amshi : In bayanka uban Madauci ,
: Babu mai kyauta hakan ga.
Jagora : Ga riga ishirin Sarki ya ba ni,
‘Y/Amshi : In bayanka uban Madauci ,
: Babu mai kyauta hakan ga.

Jagora : Alkyabbag ga da Sarki yas shirya min,
‘Y/Amshi : In bayanka uban Madauci ,
: Babu mai kyauta hakan ga.
Jagora : Ga Xantasala da Sarki yas shirya min
‘Y/Amshi : In bayanka uban Madauci ,
: Babu mai kyauta hakan ga,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Malam Na-Allah, x^2
: Sannu da kai-da-kawo,
‘Y/Amshi : Ya zo Legas lahiya lau Na-Allah,
: Ya zaka lahiya lau, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Jekadiyar Zazzau Bagobira, x^2
‘Y/Amshi : Allah ya daxe da ranta,
: Tun da ba ta buki da wasa, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Alhaji Mani ba shi qin kowa,
: Komi kac ce yanai ma,
: Shehu bai iya za’ida ba,
‘Y/Amshi : Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki Uban Iya, x^2
‘Y/Amshi : Bajimin Madami,
: Don kak ka yadda da qulle-qulle,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe. x^2

Jagora : Sarki ya ban huhu xan takarda,
‘Y/Amshi : Sabon Birni za ni saqo,
: Can a kai shi ga masu ci nai.

Jagora : Sarki ya ban goro xan takarda,
‘Y/Amshi : Sabon Birni za ni saqo,
: Can a kai shi ga masu ci nai.

Jagora : Matana bana sun yi dace,
‘Y/Amshi : Mai kai goro ka iy da saqo,
: Ka ce a ba su su sami wuri da kansu.
Jagora : To, matana bana kun yi dace,
‘Y/Amshi : Mai kai goro ka ida saqo,
: Ka ce a ba su su sami wuri da kansu,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki ya tara taro, x^2
‘Y/Amshi : Ka diba duk kwararon jihag ga,
: Shehu, Alhaji duy ya save su, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Alhaji Mani ba shi qin kowa,
: Komi kac ce yanai ma,
: Shehu bai iya za’ida ba,
‘Y/Amshi : Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki Uban Iya,
‘Y/Amshi : Bajimin Madami,
: Don kak ka yadda da qulle-qulle.

Jagora : Ga wani ya tsira qulle-qulle,
‘Y/Amshi : Ya naxa qarya ta qule mai,
: Yau wane ba haka nan a kai ba,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Ga wani ya tsira xame-xame,
‘Y/Amshi : Ya naxa qarya ta qule mai,
: Yau wane ba haka nan a kai ba,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Zazzau, Alhaji Shehu Idris (1975-)[23]*,*
Gindin Waqa : Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki ya xauke marayu,
'Y/ Amshi : Kuma ya xau mai uwaye,
: Duka Alhaji ya save su,
'Y/Amshi : Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Alhaji Mani ba shi qin kowa,
: Komi kac ce yanai ma,
: Shehu bai iya za'ida ba,
'Y/Amshi : Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki Uban Iya, x^2
'Y/Amshi : Bajimin Madami,
: Don kak ka yadda da qulle-qulle. x^2

Jagora : Ga wani ya tsira qulle-qulle,
'Y/Amshi : Ya naxa qarya ta qule mai,
: Yau wane ba haka nan a kai ba.
Jagora : Ga wani ya tsira xame-xame,
'Y/Amshi : Ya naxa qarya ta qule mai,
: Yau wane ba haka nan a kai ba,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Birnin Zazzau za ni sabka, x^2
'Y/Amshi : In ishe sarki lahiya lau,
: Don mu sami abin tavawa. x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.
Jagora : Sarki da hanquri aka tsara taro, x^2
'Y/Amshi : Ka diba duk kwararon qasag ga,

---

23 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{75}$ $^1/_3$.

: Duk Shehu, Alhaji ya haxe su, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Jahwaru ya yi riqo Jihag ga,
'Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al'amarin Jiharsu.
Jagora : Muhammadu ya yi riqo Jihag ga,
'Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al'amarin Jiharsu.
Jagora : Kuma Kabiru ya yi riqo Jihag ga,
'Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al'amarin Jiharsu.
Jagora : Jahwaru ya yi riqo Jihag ga,
'Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al'amarin Jiharsu.
Jagora : Abdulkarimu ya yi riqo Jihag ga,
'Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al'amarin Jiharsu.
Jagora : Muhammadu ya yi riqo Jihag ga,
'Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al'amarin Jiharsu.
Jagora : Kuma Sambo ya yi riqo Jihag ga,
'Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al'amarin Jiharsu.
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki ya xauke marayu,
'Y/Amshi : Ga kuma ya xau mai uwaye,
: Shehu Alhaji ya save su.
Jagora : Sarki ya xauke makahi,
'Y/Amshi : Ga kuma ya xau mai idanu,
: Shehu Alhaji ya save su.

Jagora : Sarki ya xauke guramu,
'Y/Amshi : Ga kuma ya xau mai qahwahu,
: Shehu Alhaji ya save su,

: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki uban Iya, x^2
'Y/Amshi : Bajimin Madami,
: Don kak ka yadda da qulle-qulle. x^2

Jagora : Magaji mai hwaure da 'yan tsaka,
'Y/Amshi : Ya yi kirana ya hwaxa min,
: Gobe Kaduna za mu,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Alhaji Shata ya hwaxa min, x^2
'Y/Amshi : Yac ce Zariya ba a zambo,
: Dum makaxi yas shirya zambo,
: Alhaji wawa na buge shi da gora,
: Yanzu ta hau wuyanai, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Ai da hanquri aka tsara taro,
'Y/Amshi : Ka diba duk kwararon qasag ga,
: Duk Shehu, Alhaji ya haxe su,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Alhaji Mani ba shi qin kowa, x^2
: Komi kac ce yanai ma,
: Shehu bai iya za'ida ba, x^2
'Y/Amshi : Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Jekadiyar Zazzau Bagobira, x^2
'Y/Amshi : Allah ya daxe da ranta,
: Tun da ba ta buki da wasa, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : To, rigunan ga da kash shira min,
'Y/Amshi : In bayanka Uban Madauci ,
: Babu mai kyauta hakan ga.
Jagora : Naira xari bakwai Sarki yab bak kan, x^2
'Y/Amshi : In bayanka uban Madauci ,
: Babu mai kyauta hakan ga. x^2
Jagora : Riga ishirin Sarki ya bak kan, x^2
'Y/Amshi : In bayanka uban Madauci ,
: Babu mai kyauta hakan ga. x^2
Jagora : Alkyabbag ga da Sarki yas shirya min, x^2
'Y/Amshi : In bayanka uban Madauci ,
: Babu mai kyauta hakan ga. x^2
Jagora : Ga Xantasala da Sarki yas shirya min, x^2
'Y/Amshi : In bayanka uban Madauci ,
: Babu mai kyauta hakan ga, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki ya ban huhu xan takarda,
'Y/Amshi : Sabon Birni za ni saqo,
: Can a kai shi ga masu ci nai.
Jagora : Matana bana kun yi dace,
'Y/Amshi : Mai kai goro ka ida saqo,
: Ka ce a ba su su sami wuri da kansu.

Jagora : Malam Na Allah Sannu da kai-da-kawo, x^2
'Y/Amshi : Ya zo Legas lahiya lau,
: Na AllahYa zaka lahiya lau, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni
Mai Waqa : Alhaji Shu'aibu Salau xan Musa[24]*,*

14. *Gindin Waqa : Ya wuce tantama,*

---

24 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{143}$ $^1/_2$.

: Shi Alhaji Shu'aibu zamaninai ya kai.

Jagora : Jikan manya, jikan Alhaji yaka birnin daga,
'Y/Amshi : Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu'aibu zamaninai ya kai.

Jagora : Alhaji jikan manya,
'Y/Amshi : Jikan Alhaji yaka birnin daga.

Jagora : Allah yai maka hairan, x^2
'Y/Amshi : Allah bai yi ka don ka sha haushi ba, x^2
: Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu'aibu zamaninai ya kai.

Jagora : Sa'ad da munka tashi Sabon Birni, x^2
'Y/Amshi : Ba mu da ukku xin Tsohonai,
: In bayan sarautar Allah,
: Babu abun da yaz zama kullum,
: Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu'aibu zamaninai ya kai. x^2

Jagora : Kowas sha hura ba nono, x^2
'Y/Amshi : Ban yi zaton akwai daxi ba. x^2

Jagora : Kowas sha miya ba nama,
'Y/Amshi : Ban yi zaton akwai daxi ba,
: Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu'aibu zamaninai ya kai.

Jagora : Ni da na sauka Sabon Birni,
: To, na sauka ko han na kwan,
'Y/Amshi : Na ishe yara na wata waqa,
: To, ko yara kau ko yam mata,
: Sun ce wanda yas sai nama,
: Ya xara wanda yas sai kihi,
: Ya wuce tantama,

: Shi Alhaji Shu’aibu zamaninai ya kai.

Jagora : Ni da dai nas sauka Sabon Birni,
: To, na sauka ko han na kwan,
'Y/Amshi : Na ishe yara na wata waqa,
: To, ko yara kau ko ‘yam mata,
: Sun ce wanda yas sai nama,
: Ya xara wanda yas sai kihi.

Jagora : To kuma wanda yas sai anta,
‘Y/Amshi : Ya xara wanda yas sai hanji,
Jagora : To kuma wanda yas sai doya,
‘Y/Amshi : Ya xara wanda yas sai gwaza,
Jagora : To kuma wanda yas sai doki,
‘Y/Amshi : Ya xara wanda yas sai jakki,
: Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu’aibu zamaninai ya kai.

Jagora : Kwanakki da niz zo gaisai, x^2
: Naira arba’in yab bayat,
'Y/Amshi : To, kuma ga turamai ya bai,
: Ya kai man buhuhwan gero,
: Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu’aibu zamaninai ya kai. x^2

Jagora : Kuma ga naira xari yab bayat, x^2
‘Y/Amshi : Ya ce min a sai min gero, x^2
: Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu’aibu zamaninai ya kai.

Jagora : Alhaji xan Ciyaman xan Sarki,
‘Y/Amshi : Wada kan nuhwa sai ka yi,
: Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu’aibu zamaninai ya kai.

Jagora : Alhaji xan Ciyaman xan Sarki, x^3
‘Y/Amshi : Wada kan nuhwa sai ka yi. x^3

Jagora : Alhaji xan Salau xan Musa x^2
'Y/Amshi : Al'amarinka ya sha dama. x^2
: Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu'aibu zamaninai ya kai.

Jagora : Alhaji xan Salau xan Musa x^2
'Y/Amshi : Al'amarinka ya sha dama. x^2
: Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu'aibu zamaninai ya kai.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ibrahim (1970-1975)[25]*,*

15. *Gindin Waqa : Da shiri yat tasa,*
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.

---

25 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{144}$ $^1/_6$ - AL $^1/_{146}$ $^1/_2$.

Jagora : Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai,
'Y/Amshi : Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.

Jagora : Da arziki da wadata, x^2
'Y/Amshi : Ai zaman duniya sai an sa hanquri, x^2
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.
Jagora : Na biyo bisa hanya,
'Y/Amshi : Ko da xai ba ni wasan daji kakkarai,
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.

Jagora : Kakkarai qaqqarqa, x^2
'Y/Amshi : Kakkarai in ji zabin daji masu qwai. x^2
Jagora : Ashe mutanen birni,
'Y/Amshi : Su ka huma mutanen daji gargaxi.

Jagora : Iro mutanen birni,
'Y/Amshi : Su ka huma mutanen daji gargaxi,
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.

Jagora : Ashe duniya gishiri ta, x^2
'Y/Amshi : Wane kay ya sake ta koma daudawa,
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai. x^2
Jagora : Gaba da baya qarhin doki, x^2
'Y/Amshi : In dai batu, batun Gobir na,
: Wada kuk ka hwaxi Ibrahim na ciki,
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai. x^2

Jagora : Gidan Muhamman Jadi,
'Y/Amshi : Jadi xan Tubali sai Allah bai yi ba.

Jagora : Gidan Muhamman Jadi,
'Y/Amshi : Yau gidan Tubali sai Allah bai yi ba.

Jagora : Ina bixar iyalin Jangwarzo, x^2
'Y/Amshi : Ashe Iro na nan jikan mai gida, x^2
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.

Jagora : Iro da yab ban hwanda, x^2
'Y/Amshi : Wag ga hwandar Kano ta yac ce in hawo, x^2
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.

Jagora : Ga hwandar hwan xari biyat an ba ni,
'Y/Amshi : Tana da ‘yan gyare-gyare ni ko ban yi ba,
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.

Jagora : Ga hwandar da Iro yab ba mu,
'Y/Amshi : Tana da ‘yan gyare-gyare ni ko ban yi ba.

Jagora : Hwandar ba ta da Oda, x^2
'Y/Amshi : Ga ta ba ta da mai Musa ko na gani. x^2

Jagora : Musa ya qasaita,
'Y/Amshi : Abin da duk na hwaxi Musa kau na yi min.

Jagora : Musa ya gawurta,
'Y/Amshi : Abin da duk na hwaxi Musa kau na yi min.

Jagora : Wannan Musa ya qasaita,
'Y/Amshi : Abin da duk na hwaxi Musa kau na yi min,
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.

Jagora : Mamman bakanike ya kyauta, x^3
'Y/Amshi : Yayi min gyare-gyaren Hwanda ba kuxi, x^3
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.

Jagora : Da arziki da wadata, x^2
'Y/Amshi : Ai zaman duniya sai an sa hanquri, x^2

: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Zazzau,
Alhaji Shehu Idris (1975-)[26]*,*

24. *Gindin Waqa : Kak ka yarda da raini uban Baraya,*
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

Jagora : Kak ka yarda da raini uban Baraya, x^2
'Y/Amshi : Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma. x^2

Jagora : Zariya, Zariya, Zazzau maza da mata,
'Y/Amshi : Duk wanda ba ya da mota ya je a sai mai,

---

26 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{52}$ $^{1}/_{7}$.

: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

Jagora : Lalle ina ganin balbela da ita da shanu,
'Y/Amshi : Ai ko da yaushe nan taka samun abin da tac ci,
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.
Jagora : Ni dai ina ganin balbela da ita da shanu,
'Y/Amshi : Ai ko da yaushe nan taka samun abin da tac ci,
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

Jagora : Xan'anace ya yi jawabi shi da Shata, x^2
'Y/Amshi : Ai ko Sa'idu ya yi jawabi da shi da Qwairo. x^2

Jagora : Manyan maroqa ku taho mu tai ga sarki, x^2
'Y/Amshi : Duk wanda ba ya da mota ya zo ya sai mai, x^2
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

Jagora : Ai ga ni na zaka Zazzau mu gai da sarki,
'Y/Amshi : Banga Habiba ba kuma ban ga Mariya ba,
: Ai ko su Binta ba su da halin su daqile ni,
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.
J agora : Maidaji ya zaka Zazzau ya gai da sarki,
'Y/Amshi : Ban ga Habiba ba kuma ban ga Mariya ba,
: Ai ko su Binta ba su da halin su daqile ni,
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

Jagora : Lalle ina ganin balbela da ita da shanu,
'Y/Amshi : Ai ko da yaushe nan taka samun abin da tac ci,
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

Jagora : Kai ab ubangijin Sanqira da shi da wawa, x^2
'Y/Amshi : Sarki na Iro mai katse harshen mutum da dama, x^2
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

Jagora : Kai ab ubangijin Sanqira da shi da wawa,
'Y/Amshi : Sarki na Iro mai katse harshen mutum da dama,
Jagora : Kai ab ubangijin Kakaki da shi da Hwade,
'Y/Amshi : Sarki na Iro mai katse harshen mutum da dama,
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

Jagora : Ai ga ni na zaka Zazzau mu gai da sarki,
'Y/Amshi : Ban ga Habiba ba kuma banga Mariya ba,
: Ai ko su Binta ba su da halin su daqile ni,
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

Jagora : Ni dai ina ganin balbela da ita da shanu, x^2
'Y/Amshi : Ai ko da yaushe nan taka samun abin da tac ci, x^2
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

Jagora : Manyan maroqa ku taho mu tai ga sarki, x^2
'Y/Amshi : Duk wanda ba ya da mota ya zo a sai mai, x^2
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Buza ta Qasar Nijar,
Alhaji Abdussalam Buza [27]*,*

17. *Gindin Waqa : Xansidi amshi sandar mulki qasatai,*
: Mai Buza Xanhassan mai taro hannu.

Jagora : In dai na gyara ganguna na yi shirin kixina,
'Y/Amshi : To, Maidaji mai kixi wajjen Buza yay yi.
Jagora : In dai na gyara ganguna na yi shirin kixana,
'Y/Amshi : To, maidaji mai kixi wajjen Buza yay yi,

---

[27] An sami wannan rerawa ne a Cikin Hirar da aka Saurara Tsakanin Makaxa Maidaji da Alhaji Ibrahim Xiso, Rediyo Rima, Sakkwato. Akwai Wannan Hira a Kammalenta a Cikin Wannan Kundi a Rataye na Xaya, Shafi na 302.

: Xansidi amshi sandar mulki qasatai,
: Mai Bunza Xanhassan mai taro hannu.

Jagora : Ga ni na taho kixin sarkin Buza sabo,
‘Y/Amshi : Kakaki da ganguma kowa ga shi ya zo,
: Daxa sai wanda ba wuri xai ab bai taho ba.
Jagora : Alhaji na taho kixin sarkin Buza sabo,
‘Y/Amshi : Kakaki da ganguma kowa ga shi ya zo,
: Daxa sai wanda ba wuri xai ab bai taho ba,
: Xansidi amshi sandar mulki qasatai,
: Mai Buza Xanhassan mai taro hannu.

Jagora : Jakara namu wag ga bakka tai yamma daidai,
: Kuma wadda ag Gufur ta yare wa daidai,
‘Y/Amshi : Duy ya haske duniya kowa na ta kallo,
: Xansidi amshi sandar mulki qasatai,
: Mai Buza Xanhassan mai taro hannu.

Jagora : Jakara namu wag ga bakka tai yamma daidai,
: Kuma wadda ag Gufur ta yare wa daidai,
‘Y/Amshi : Duy ya haske duniya kowa na ta kallo.

Jagora : In dai ka ishe mutane sun taru garka,
‘Y/Amshi : In dai ba munaqisa kuma dai ba mahwari,
: Kai ka san akwai mutanen Allah wurinai.
Jagora : In dai ka ishe mutane sun taru garka,
‘Y/Amshi : In dai ba munaqisa kuma ba mahwari,
: Kai ka sana akwai mutanen Allah wurinai,
: Xansidi amshi sandar mulki qasatai,
: Mai Buza Xanhassan mai taro hannu.

Jagora : Da na samu kurciya ko ko damisa ne,
: Ko ko tantabara uwat tsuntsaye na sami,
: Da na ba da saqo,
: Saqonnin da ba ni ba za ta zo ta kwana ba,
: In tac ce gari da nisa in ba da taguwa,
: In tac ce gari da yunwa in ba da gari,
: In tac ce gari da qishirwa in ba da salka,
: In tac ce gari da xari in ba da bargo

‘Y/Amshi : In ta zo tac ce matan Falgore qasatai,
: Xansidi amshi sandar mulki qasatai,
: Mai Buza Xanhassan mai taro hannu.

Jagora : In dai ta zo tac ce matan Falgore qasatai, x^2
‘Y/Amshi : Ga darnin da yab bari ya koma katanga,
: Xansidi amshi sandar mulki qasatai,
: Mai Bunza Xanhassan mai taro hannu. x^2

Jagora : In dai na gyara ganguna na yi shirin kixana,
‘Y/Amshi : To, maidaji mai kixi wajjen Bunza yay yi,
: Xansidi amshi sandar mulki qasatai,
: Mai Buza Xanhassan mai taro hannu.

Makaxi : Alhaji Sa’idu Rambaxawa Sabon Birni,
Waqa : Waqar Noma ta ‘Yar Buhari[28]*,*

18. *Gindin Waqa : Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,*
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hasti,
‘Y/Amshi : Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.
Jagora : Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hasti,
‘Y/Amshi : Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Ka ga kayan gona iri-iri suna cikin qasanmu,
‘Y/Amshi : Don Allah ku qara shuka mana mu ga gujjiya.

---

[28] An sami wannan rerawa ne a cikin hirar da aka saurara tsakanin Makaxa Maidaji da Alhaji Ibrahim Xiso, Rediyo Rima, Sakkwato. Akwai Wannan hira a kammalenta a cikin wannan kundi a Rataye na Biyu, Shafi na 302.

Jagora : Sai an sa gero a shuka dawa da su gujjiya,
'Y/Amshi : A sa masara kuma a shuka rogo a yi lawuru.
Jagora : Sai an sa gero a shuka dawa da su gujjiya, x^2
'Y/Amshi : A sa masara kuma a shuka rogo a yi lawuru,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro. x^2

Jagora : To, ashe Likita bai da maganin yunwa,
'Y/Amshi : Wanga magani sai a bixo hura.
Jagora : Na ji Malami bai da maganin yunwa,
'Y/Amshi : Wanga magani sai a bixo hura.
Jagora : Had da 'yan Bori ba su maganin yunwa,
'Y/Amshi : Wanga magani sai a bixo hura.
Jagora : Had da Bokaye ba su maganin yunwa,
'Y/Amshi : Wanga magani sai a bixo hura.
Jagora : Maganin yunwa kudaku da rogo da quli-quli,
'Y/Amshi : In anka haxa su kuma a dawo ga hwaro-hwaro,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.
Jagora : Wanda ba tsaba ko,
'Y/Amshi : Da yaushe na ba shi zama gida,
: Sai ka ga ya bar gidansu,
: Ya kama gidan wani,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Na ji yunwa mai sa a sai da,
: Shanu da tumaki da awaki,
'Y/Amshi : Kuma har a tsai da sallah a sawo hatsi,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Na ji qohin xaki kila sa mata su sawo gado,
'Y/Amshi : Su shirya katihwa su shirga kwano su yi labule,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Maccen da babu qoshi, x^2

‘Y/Amshi : In ka gane ta kayanta baqi qirin,
: Kamat tanda ko da yaushe kayanta masat-masat,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro. x^2

Jagora : Ga maccen da ac cikin kubli, x^2
: Na gano ta da bargonta da gyantsama,
‘Y/Amshi : Tana ratsa gida-gida akan ba ta hwaro-hwaro,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro. x^2

Jagora : Ga wanda ba tsaba ko,
‘Y/Amshi : Da yaushe na ba shi zama gida,
: Sai ka ga ya bar gidansu,
: Ya kama gidan wani,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Gwanon canza wurin zama,
‘Y/Amshi : Yunwa,
: Da mutum yana canza wurin zama,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Gwanon canza wurin zama, x^2
‘Y/Amshi : Yunwa,
: Da mutum yana soke tsakad dare,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro. x^2

Jagora : Sai an sa gero a shuka dawa da su gujjiya, x^2
‘Y/Amshi : A sa masara kuma a shuka rogo a yi lawuru,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro. x^2

Jagora : Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hasti, x^2
‘Y/Amshi : Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,
Waqa : Waqar Noma ta 'Yar Buhari[29]*,*
Gindin Waqa : Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi, x^2
'Y/Amshi : Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro. x^2

Jagora : Na ji kayan gona iri-iri suna cikin qasanmu,
'Y/Amshi : Don Allah ku qara shuka mana mu ga gujjiya.

Jagora : Ka ga kayan gona iri-iri suna cikin qasanmu,
'Y/Amshi : Don Allah ku qara shuka mana mu ga gujjiya.

Jagora : Sai an sa gero a shuka dawa da su gujjiya,
'Y/Amshi : A sa masara kuma a shuka rogo a yi lawuru.
Jagora : Sai an sa gero a shuka dawa da su gujjiya,

---

[29] An sami wannan rerawa ne a cikin hirar da aka saurara tsakanin Makaxa Maidaji da Alhaji Ibrahim Xiso, Rediyo Rima, Sakkwato. Akwai wannan hira a kammalenta a cikin wannan Kundi a Rataye na Biyu, Shafi na 302.

‘Y/Amshi : A sa masara kuma a shuka rogo a yi lawuru,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : To, ashe Likita bai da maganin yunwa,
‘Y/Amshi : Wanga magani sai a bixo hura.
Jagora : Na ji Malami bai da maganin yunwa,
‘Y/Amshi : Wanga magani sai a bixo hura.
Jagora : Had da ‘yan Bori ba su maganin yunwa,
‘Y/Amshi : Wanga magani sai a bixo hura.
Jagora : Had da Bokaye ba su maganin yunwa,
‘Y/Amshi : Wanga magani sai a bixo hura.
Jagora : Maganin yunwa kudaku da rogo da quli-quli,
‘Y/Amshi : In anka haxa su kuma a dawo ga hwaro-hwaro,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.
Jagora : Wanda ba tsaba ko,
‘Y/Amshi : Da yaushe na ba shi zama gida,
: Sai ka ga ya bar gidansu,
: Ya kama gidan wani,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Na ji yunwa mai sa a sai da,
: Shanu da tumaki da awaki,
‘Y/Amshi : Kuma har a tsai da sallah a sawo hatsi,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Ga maccen da ac cikin kubli,
: Na gano ta da bargonta da gyantsama,
‘Y/Amshi : Tana ratsa gida-gida akan ba ta hwaro-hwaro,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Gwanon canza wurin zama,
‘Y/Amshi : Yunwa,
: Da mutum yana canza wurin zama,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,

: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hasti, x^3
'Y/Amshi : Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro. x^3

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Waqa : Waqar Mata[30] *,*

28. *Gindin Waqa : Mata in ba ku ba gida,*
: Wurin Allah ku ash shikashiki.

Jagora : Mata in ba ku ba gida, x^2
'Y/Amshi : Wurin Allah ku ash shikashiki. x^2

Jagora : Mata ku yi aure kuma, x^2
'Y/Amshi : Ku zan ka addini shi ag gishirin zama. x^2

Jagora : Cikin nassi aka aure, x^2
'Y/Amshi : Kuma cikin nassi aka tagazag gida, x^2
: Mata in ba ku ba gida,
: Wurin Allah ku ash shikashiki.

Jagora : Yara kun ji kixin manya ko ba ku ji,
'Y/Amshi : Ko kun yin bori ba ku jituwa,
: Mata in ba ku ba gida,
: Wurin Allah ku ash shikashiki.

---

30 An Sami Wannan Rerawa ne a Hirar da aka Saurara Tsakanin Makaxa Maidaji da Alhaji Ibrahim Xiso na Rima Rediyo, Jihar Sakkwato. Akwai Wannan Hira a Kammalenta a Cikin Rataye na Xaya na Wannan Kundi.

Jagora : Maccen da ka aure, x^2
'Y/Amshi : Tai hikima ki wanka daga ciki, x^2
: Mata in ba ku ba gida,
: Wurin Allah ku ash shikashiki.
Jagora : Maccen da ba ta aure,
'Y/Amshi : Fatsima na can na watsa mata qasa,
: Mata in ba ku ba gida,
: Wurin Allah ku ash shikashiki.

Jagora : Yara kun ji kixin manya ko ba ku ji, x^2
'Y/Amshi : Ko gun yin bori ba ku jituwa, x^2
: Mata in ba ku ba gida,
: Wurin Allah ku ash shikashiki.

Jagora : Ni shawan mata nika gani, x^3
'Y/Amshi : Wurin girki nan za ka tuwo, x^3
: Mata in ba ku ba gida,
: Wurin ku ada daga ciki.

Jagora : Komi rani ko da damina,
: A sa su daka kuma za su yi,
: Su xora dakan tsaba su yi,
'Y/Amshi : Suna waqa wasu har suna rawa,
: Mata in ba ku ba gida,
: Wurin ku ada daga ciki.

Jagora : Mata in ba ku ba gida,
'Y/Amshi : Wurin Allah ku ash shikashiki.

Jagora : Mata ku yi aure kuma,
'Y/Amshi : Ku zan ka addini shi ag gishirin zama.

Jagora : Cikin nassi aka aure,
'Y/Amshi : Kuma cikin nassi aka tagaza gida,
: Mata in ba ku ba gida,
: Wurin ku ada daga ciki.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Ali Abubakar 'Yankuzo[31]*,*

20. *Gindin Waqa : A gai min da Alhaji Ali na 'Yankuzo,*
: Duniya ya gyara wurin zama.

Jagora : A gai min da Alhaji Ali na 'Yankuzo, x^2
'Y/Amshi : Duniya ta gyara wurin zama. x^2

Jagora : Duniya ta gyara gida, x^2
'Y/Amshi : Had da lahira ya shirya wurin zama. x^2

Jagora : Ku gai min da Alhaji Ali qwarai,
'Y/Amshi : Had da mu muna gaishe shi qwarai-qwarai.

Jagora : 'Ya'yana ku gai min da Alhaji Ali qwarai,
'Y/Amshi : Had da mu muna gaishe shi qwarai-qwarai,
: A gai min da Alhaji Ali na 'Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Alhaji na Hassan sarkin hanquri, x^2
'Y/Amshi : Jalla wahidin ya ba ka halin qwarai, x^2
: A gai min da Alhaji Ali na 'Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Ka riqe sabba ka riqe danginka,

---

31 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{52}$ $^{1}/_{4}$.

‘Y/Amshi : Ya riqe kayansa kwarai,
: Wanda bai da mata sai ka ya yi mai,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Da nit taho das Sabon Birni, x^2
‘Y/Amshi : Nib bi ta Tsahe nit tahi ‘Yankuzo,
: In na yi dace ni ishe Ali sai,
: Na yi roqo nai ya yi min gida,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama. x^2

Jagora : Gobirawa ‘yan ga aiki duw,
‘Y/Amshi : Wani na niyyay ya gano gida,
: Ya za ya ce ya kama wurin zama,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Gobirawa ‘yan ga aiki duw,
‘Y/Amshi : Wani na niyyay ya gano gida,
: Ya za ya ce ya kama wurin zama.

Jagora : Ku zo ku ce na kama gida, x^2
‘Y/Amshi : Ali had da mata za shi yi min bana. x^2

Jagora : Ku zo ku ce na kama gida,
‘Y/Amshi : Ali had da mata za shi yi min bana,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Da ka ga sufar xan sarki, x^2
‘Y/Amshi : Yara kun ga mai iya ta da gida,
: Ba matsalar ka tashi gidanku na ainihi, x^2
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Xan zaki hay ya qasura, x^2
‘Y/Amshi : Hay ya yi jan wuya ya hiddo qwarai-qwarai, x^2
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Mijin Halima mijin Hajiya Mairo,
‘Y/Amshi : Allah ya ba ku hwaro-hwaro.

Jagora : Mijin Halima mijin Hajiya Mairo,
‘Y/Amshi : Allah ya ba ku hwaro-hwaro,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Gohe na gode mai,
‘Y/Amshi : Har na yi godiya ina gaishe shi qwarai-qwarai,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Na Isan Mayana Alhaji Ali,
‘Y/Amshi : Magajin Bala magajin Bello Madogara,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Duniya ta gyara gida, x^2
‘Y/Amshi : Had da lahira ya shirya wurin zama. x^2

Jagora : Ku gai min da Alhaji Ali qwarai, x^2
‘Y/Amshi : Had da mu muna gaishe shi qwarai-qwarai. x^2

Jagora : ‘Ya’yana ku gai min da Alhaji Ali qwarai, x^2
‘Y/Amshi : Had da mu muna gaishe shi qwarai-qwarai,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama. x^2

Jagora : Alhaji na Hassan sarkin hanquri,
‘Y/Amshi : Jalla wahidin ya ba ka halin qwarai.

Jagora : Alhaji goga na Abubakar sarkin hanquri, x^2
‘Y/Amshi : Jalla wahidin ya ba ka halin qwarai, x^2
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Ka riqe sabba ka riqe danginka, x^2

‘Y/Amshi : Ya riqe kayansa kwarai, x^2
: Wanda bai da mata sai ka ya yi mai,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Ku zo ku ce na kama gida,
‘Y/Amshi : Ali had da mata za shi yi min bana,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Xan zaki hay ya qasura,
‘Y/Amshi : Hay ya yi jan wuya ya hiddo qwarai-qwarai,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Mijin Halima mijin Hajiya Mairo,
‘Y/Amshi : Allah ya ba ku hwaro-hwaro,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo, x^2
‘Y/Amshi : Duniya ta gyara wurin zama. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Mamman Kuzo[32]*,*
21. *Gindin Waqa : Madogara Alhaji Mamman,*
: Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Alhaji Kuzo ka wuce gori, x^2
'Y/Amshi : Tun da kana tare da Allah,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka. x^2

Jagora : Na zo Kaduna don Alhaji Mamman, x^2
'Y/Amshi : Saboda in sami abinci, x^2
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Shi wanda ax xauke ga hanya,
'Y/Amshi : Ba ya zuwa sarma ga daji,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Ai wanda ax xauke ga hanya,
'Y/Amshi : Ba ya zuwa sarma da daji,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Alhaji mijin Turai, x^2
'Y/Amshi : Alhaji mijin Hussaina da Habiba, x^2
: Madogara Alhaji Mamman,

---

32 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{52}$ $^1/_4$.

: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Xan Bagobiri ko na ina ne, x^2
'Y/Amshi : Zuwa mu kai mui mishi gado,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka. x^2

Jagora : Ya shirya aure da zumunci, x^3
'Y/Amshi : Yana shirin yara da manya, x^3
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Kuma in magana ba ta da kyawo, x^2
'Y/Amshi : Manya ka yin zaune su gyara,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka. x^2

Jagora : Alhaji Uban Yakuba zaki,
'Y/Amshi : Ba ya gudun takula da manya,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Bajini Bala xan Sani, x^3
'Y/Amshi : Ko da yaushe bai gaji sake ba, x^3
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Alhaji Uban Yakuba zaki,
'Y/Amshi : Ba ya gudun takula da manya,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Ga Xangara ga Alhaji Mamman, x^2
'Y/Amshi : Yau ana shirin shavirigana,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka. x^2

Jagora :Ga naira xari shidda uban,
'Y/Amshi : Yakuba yab ban in buga kwano,

: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Naira xari shidda uban,
‘Y/Amshi : Yakuba yab ban in buga kwano,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Alhaji mijin Turai,
‘Y/Amshi : Alhaji mijin Hussaina da Habiba,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Xan Bagobiri ko na ina ne, x^2
‘Y/Amshi : Zuwa mu kai mui mishi gado,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka. x^2

Jagora : Ya yi shirin Jari da Jadi, x^2
‘Y/Amshi : Ya yi shirin Almu da gauxe, x^2
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Na zo Kaduna don Alhaji Mamman, x^2
‘Y/Amshi : Saboda in sami abinci, x^2
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Shi wanda ax xauke ga hanya,
‘Y/Amshi : Ba ya zuwa sarma da daji,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Ai wanda ax xauke ga hanya,
‘Y/Amshi : Ba ya zuwa sarma da daji,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Shehu Aliyu Shagari,
Tsohon Shugaban Qasar Nijeriya[33]*,*

22. *Gindin Waqa : Na yi mamakin harka tai,*
: Shehu mai daraja Shagari.

Jagora : Shugaban qasa Allah kyauta mai,
'Y/Amshi : Zaman mutane na murna tai,
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari.
Jagora : Shugaban qasa Allah kyauta mai, x^2
'Y/Amshi : Zaman mutane na murna tai, x^2
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari.

Jagora : Shugaba na can na aiki nai,
'Y/Amshi : Yana ta yin gaba bai hwasa ba,
: Yana ta yin aikin al'adu,
: Saboda koyon addini ne,
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari.

Jagora : Shugaba na can na aiki nai,
'Y/Amshi : Yana ta yin gaba bai hwasa ba,
: Yana ta yin aikin al'adu,
: Saboda koyon addini ne.

Jagora : Haba manoma ku kama noma,
'Y/Amshi : Ku zan ka yin aikin al'adu,
: Saboda koyon addini ne.
Jagora : 'Yan makaranta kui ta karatu,
'Y/Amshi : Ku zan ka yin aikin al'adu,

---

33 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{52}$ $^{1}/_{5}$.

: Saboda koyon addini ne.
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari.

Jagora : Kaduna an gyare hanya,
‘Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Zariya an gyare hanya,
‘Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Huntuwa an gyare hanya,
‘Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Tsahe an gyare hanya,
‘Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Kwatarkwashi an gyare hanya,
‘Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta,
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari.

Jagora : Hag Gusau an gyare hanya,
‘Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Qaura an gyare hanya,
‘Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora :Tsahe an gyare hanya,
‘Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Shinkahi an gyare hanya,
‘Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Har Isa an gyare hanya,
‘Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta,
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari.

Jagora : Sabon Birni mu bar garaje,
‘Y/Amshi : Han mu kwalta na kawowa,
: Kowa ga hwanho qahwa tai,
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari.

Jagora : Sabon Birni mu bar garaje,
‘Y/Amshi : Han mu kwalta na kawowa,
: Kowa ga hwanho qahwa tai.

Jagora : A sai mini gida Sabon Birni, x^2
‘Y/Amshi : Sannan kai a sa hitila qohwata,
: Kuma a sa min maigadi na,
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari. x^2

Jagora : Shagari hankali na bai kwanta ba, x^2
‘Y/Amshi : Ni dai rashin mota ya daman,
: Ashe rashin mota ciwo ne,
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari. x^2

Jagora : Ai da ni da ‘yan kamishon wajjenmu, x^2
‘Y/Amshi : Has sun hana min in sai kaji,
: Waxanda za a dahwaman in ci,
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari. x^2

Jagora : Dibi xan wuri kusa bai kai mil ba,
‘Y/Amshi : Suna hwaxin naira-naira ne,
: Abin ga shin ko cin hanci,
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari.

Jagora : Shugaban qasa Allah kyauta mai, x^2
‘Y/Amshi : Zaman mutane na murna tai, x^2
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Garba Nadama[34]*,*
Tsohon Gwamnan Jihar Sakkwato,

23. *Gindin Waqa : Allah za ni roqon ka,*
: In yi biyag gwamna mai girma.

Jagora : Allah za ni roqon ka,
: In yi biyag gwamna mai girma,
'Y/Amshi : Allah zani roqon ka,
: In yi biyag gwamna mai girma.

Jagora : Garba Nadama, x^2
'Y/Amshi : Garba irin ra'ayi nai yana yi min, x^2
: Allah za ni roqonka,
: In yi biyag gwamna mai girma.

Jagora : Garba abin da Allah, x^2
: Na Ibrahim ya kai kullum,
'Y/Amshi : Allah shi ka sa matsuwa,
: Kuma Allah shi ka sa sauqi,
: Allah za ni roqonka,
: In yi biyag gwamna mai girma. x^2

Jagora : Ko can duniya haka, x^2
: Tag gada inji mai turu,
'Y/Amshi : Ka san duniya daxa,
: Ba mai hurce iyaka tai,
: Allah za ni roqonka,
: In yi biyag gwamna mai girma. x^2

Jagora : Kullum hwata nikai, x^2
'Y/Amshi : Allah ya jiqan Shehu Kangiwa. x^2

Jagora : Allah nai addu'a,
'Y/Amshi : Allah ya jiqan Shehu Kangiwa.

---

34 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{52}$ $^1/_6$.

Jagora : Annabi nai addu'a,
'Y/Amshi : Allah ya jiqan Shehu Kangiwa.
Jagora : Sarkin Musulmi nai addu'a,
'Y/Amshi : Allah ya jiqan Shehu Kangiwa.
Jagora : Waziri da yai addu'a,
'Y/Amshi : Allah ya jiqan Shehu Kangiwa.
Jagora : Kuma Nana da tai addu'a,
'Y/Amshi : Allah ya jiqan Shehu Kangiwa,
: Allah za ni roqonka,
: In yi biyag gwamna mai girma.

Jagora : Don qudura, Irada da Attaura da Linjila, x^2
'Y/Amshi : Don Allah don Annabi,
: Ai ta ibadar riqon juna,
: Allah za ni roqonka,
: In yi biyag gwamna mai girma. x^2

Jagora : Babu abin da yai min ciwo, x^2
: Allah ni ke kallo,
'Y/Amshi : Ga ni ina kixin Gwamna,
: Ba ni da motad da zani hawa,
: Allah za ni roqonka,
: In yi biyag gwamna mai girma. x^2

Jagora : In ga Gwamna mai girma, x^2
: Kuma dai ga mutane nai,
'Y/Amshi : Motan nan dai da za a yi min,
: Ba sai na yi roqo ba,
: Allah za ni roqonka,
: In yi biyag gwamna mai girma. x^2

Jagora : Jiya na kwan cikin tihwa, x^2
: Riga ta tana masqi,
'Y/Amshi : In ba don Tabarau ba,
: Da qura ta makamce ni. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,

Mai Waqa : Alhaji Mamman xan Abubakar Malumfashi[35]*,*

24. *Gindin Waqa : Dogo xan Abubakar na Malumfashi,*
: Jikan Dabo xan Kilo gwamron giwa.

Jagora : Dogo xan Abubakar na Malumfashi,
: Jikan Dabo xan Kilo Gwamron giwa,
'Y/Amshi : Dogo xan Abubakar na Malumfashi,
: Jikan Dabo xan Kilo Gwamron giwa.

Jagora : Gidan Mamman nit taho kixi sai na gai sai,
'Y/Amshi : Sai ga Audu xan Bala ga Musa nan,
: Komi nib bixa ga yau sai an yo min,
: Dogo xan Abubakar na Malumfashi,
: Jikan Dabo xan Kilo Gwamron giwa.

Jagora : Ga wani horo da zan hwaxa ma xan Shawai, x^2
'Y/Amshi : Allah sa ka xauki horon in na yi. x^2

Jagora : Ai kyawon xa shi xauki horon tsoho nai,
'Y/Amshi : Ai ban ce ka xauki horon kowa ba.

Jagora : Ai kyawon xa shi xauki horon tsoho nai,
'Y/Amshi : Ai ban ce ka xauki horon kowa ba,
: Ni ban ce ka xauki horon kowa ba,
: Dogo xan Abubakar na Malumfashi,
: Jikan Dabo xan Kilo Gwamron giwa.

Jagora : In ka ishe xan baqo bakin garka tai, x^3
'Y/Amshi : Kai ka san akwai duhu bayan qumci, x^3
: Dogo xan Abubakar na Malumfashi,
: Jikan Dabo xan Kilo Gwamron giwa.

Jagora : Ai Xandango Nasidi na yo hadari,
'Y/Amshi : Zaki mai kamar uwaye na tun hwarko.
Jagora : Ah! Ai Xandango Nasidi na yo hadari,
'Y/Amshi : Zaki mai kamar uwaye na tun hwarko.

---

35 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{52}$ $^1/_7$.

Jagora : Na gode Gago ta yi kyau ta kai min komi,
‘Y/Amshi : Ita ce wadda tas shirya tak aiko min.

Jagora : Lalle Sule Maigari yana yo min girma,
‘Y/Amshi : Xan Aljanna yas shirya yak aiko min.
Jagora : To, Musa godiya nikai min komi,
‘Y/Amshi : Kayan nan da yas shirya yak aiko min.
Jagora : Lalle Audu ya tsare yai min komi,
‘Y/Amshi : Kayan nan da yas shirya yak aiko min.
Jagora : Kai da Dila godiya nikai yai min girma,
‘Y/Amshi : Kayan nan da yas shirya yak aiko min.
Jagora : To, Isah godiya nikai yai min komi,
‘Y/Amshi : Kayan nan da yas shirya yak aiko min.
Jagora : To, Dela godiya nikai tai min komi,
‘Y/Amshi : Kayan nan da yas shirya yak aiko min.
Jagora : To, Habsu godiya nikai tai min komi,
‘Y/Amshi : Kayan nan da yas shirya yak aiko min.
Jagora : To, Dela godiya nikai min komi,
‘Y/Amshi : Kayan nan da yas shirya yak aiko min,
: Dogo xan Abubakar na Malumfashi,
: Jikan Dabo xan Kilo Gwamron giwa.

Jagora : Ga wani horo da zan hwaxa ma xan Shawai, x^2
‘Y/Amshi : Allah sa ka xauki horon in na yi, x^2
: Dogo xan Abubakar na Malumfashi,
: Jikan Dabo xan Kilo Gwamron giwa.

Jagora : Gidan Mamman nit taho kixi sai na gai sai,
‘Y/Amshi : Sai ga Audu xan Bala ga Musa nan,
: Komi nib bixa ga yau sai an yo min,
: Dogo xan Abubakar na Malumfashi,
: Jikan Dabo xan Kilo Gwamron giwa.

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,

Mai Waqa : Alhaji Shu'aibu Kunda[36]*,*

25. *Gindin Waqa : Jikan Kunda ai ina kan zuwa gaisai,*
: Tun da na san ba ka gaji kyamar mutane ba.

Jagora : Hanqure da ni ai ko da,
: Yaushe nib biya kai ta bakka ni,
'Y/Amshi : Tun da na san ba ka gaji qyamar mutane ba,
: Jikan Kunda ai ina kan zuwa gaisai,
: Tun da na san ba ka gaji qyamar mutane ba.

Jagora : Shu'aibu zamanin yaqi, x^2
'Y/Amshi : Na ga ba a taushi Gobir ba,
: An so a karya dahin Jari,
: Amma hwa ba dama. x^2

Jagora : To, Gobirawa ko dauri, x^2
'Y/Amshi : Ba mu gaji tsoro ba,
: Tun da kayan Babari,
: Na nan ga yara nai, x^2
: Jikan Kunda ai ina kan zuwa gaisai,
: Tun da na san ba ka gaji qyamar mutane ba.

Jagora : Muna biyay 'yaj ji'el, x^2
'Y/Amshi : Muna shan miyak kalwa,
: Tun da xan hitina,
: Ba ni jin gahwarar banza. x^2
Jagora : Shi mai zaman zaure,
'Y/Amshi : Ba shi qin mai zuwa gona,
: Mui ta abin da mukai,
: Duniya ba ta son raggo.
Jagora : Shu'aibu mai zaman zaure,
'Y/Amshi : Ba shi qin mai zuwa gona,
: Mui ta abin da mu kai,
: Duniya ba ta son raggo.

Jagora : Shi mai hawan Hwanda,
'Y/Amshi : Ba shi qin sakon Jaki,

---

36 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{53}$ $^{1}/_{3}$.

: Don akwai harkar yara,
: Ba xai da babba ba,
: Jikan Kunda ai ina kan zuwa gaisai,
: Tun da na san ba ka gaji qyamar mutane ba.

Jagora : Shu'aibu zamanin yaqi, x^2
'Y/Amshi : Na ga ba a taushi Gobir ba,
: An so a karya dahin Jari,
: Amma hwa ba dama. x^2

Jagora : To, Gobirawa ko dauri,
'Y/Amshi : Ba mu gaji tsoro ba,
: Tun da kayan Babari,
: Na nan ga yara nai,
: Jikan Kunda ai ina kan zuwa gaisai, x^2
: Tun da na san ba ka gaji qyamar mutane ba. x^2

Jagora : Maza suna goshin xan barya, x^3
'Y/Amshi : Muna babbakar giwa,
: Inda nama shi ke mai yawa,
: Za ni in xebo. x^3

Jagora : Hanqure da ni kullum, x^2
'Y/Amshi : Nib biya ai ta bakka ni,
: Tun da na san,
: Ba ka gaji kyamar mutane ba, x^2
: Jikan Kunda ai ina kan zuwa gaisai,
: Tun da na san ba ka gaji qyamar mutane ba.

Jagora : Shu'aibu zamanin yaqi, x^2
'Y/Amshi : Na ga ba a taushi Gobir ba,
: An so a karya dahin Jari,
: Amma hwa ba dama. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Ali Marafa,

26. *Gindin Waqa : Malam Alo na baraz zaki*[37]*,*
: Jikan Kilo xan Marafa.

Jagora : Malam Alo na baraz zaki,
: Jikan kilo xan Marafa,
'Y/Amshi : Malam Alo na baraz zaki, x^2
: Jikan Kilo xan Marafa. x^2

Jagora : Da Ali da Yakuba, x^2
'Y/Amshi : Ku gyara kaya,
: Babu ba ya cin Gobirawa, x^2
: Malam Alo na baraz zaki,
: Jikan Kilo xan Marafa.

Jagora : Kura ba ta gasa da xan Zaki,
'Y/Amshi : Azamarsu ba ta zama xai ba.

Jagora : Don azamar su wane 'yar gajera ta,
'Y/Amshi : Har yanzu ba ta yi tsawo ba,
: Malam Alo na baraz zaki,
: Jikan Kilo xan Marafa.

Jagora : Ali mijin Sa'a, x^2
'Y/Amshi : Da ka tauhidi,
: Kuma ba ya son wani wargi. x^2

Jagora : Ali na Ali tun duniyar qarhe, x^2
'Y/Amshi : Xan Iro dodo na Musa. x^2

Jagora : Barka nikai ma da zamanin ga, x^2
'Y/Amshi : Na yanzu mai ka-ji-ka-ji,
: Malam Alo na baraz zaki,
: Jikan Kilo xan Marafa. x^2
Jagora : Kura ba ta gasa da xan Zaki,
'Y/Amshi : Azamarsu ba ta zama xai ba.
Jagora : Don azamar su wane 'yar gajera ta,

---

37 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{53}$ $^{1}/_{4}$.

‘Y/Amshi : Har yanzu ba ta yi tsawo ba,
: Malam Alo na baraz zaki,
: Jikan Kilo xan Marafa.

Jagora : Ko can da shirin hwaxa Ali yat ta sa, x^2
: Tun ba a shirya mai wuqa ba,
‘Y/Amshi : Yanzu akwai takobi akwai mashi,
: Don an shirya mai makami,
: Malam Alo na baraz zaki,
: Jikan Kilo xan Marafa. x^2

Jagora : Ko can dokin kwarai shi ka kama gudu,
: Shi daxe shina hamadanci,
‘Y/Amshi : Shi kuma dokin su wane sai bixar tsaba,
: Tun ba a gwada mai ruwa ba,
: Malam Alo na baraz zaki,
: Jikan Kilo xan Marafa.

Jagora : Na gode giye yai abin kirki, x^2
‘Y/Amshi : Ni na yaba ya yi komi, x^2
: Malam Alo na baraz zaki,
: Jikan Kilo xan Marafa.

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gobir na Sabon Birni,

Alhaji Umaru Shawai (1916-1945)[38],

27. *Gindin Waqa : Jikan Jari ginshiqi,*
: Dibirtau uban Zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Safka lahiya uban bango ginshiqin gabas,
'Y/Amshi : Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Safka lahiya,
'Y/Amshi : Uban bango gishiqin gabas.

Jagora : Sannu da sirdi na Garba, x^2
'Y/Amshi : Sannu da zowak ka lahiya. x^2

Jagora : Gambai na Halima, x^2
'Y/Amshi : Mainasara yaushe kaz zaka, x^2
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Sarki Mayaqi ne, x^2
'Y/Amshi : Ko Mamman na Dawwa ne. x^2

Jagora : Kai kag gaji Bawa,
'Y/Amshi : Jangwarzo babu gardama.
Jagora : Kuma ka gaji Bawa,
'Y/Amshi : Xangwamci babu gardama,
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Salihu xan Durumbu, x^2
'Y/Amshi : Mainasara xin da ba su so. x^2

Jagora : Gulbi ya ci mai kwari, x^2
'Y/Amshi : Bajimin Garba xan Hassan. x^2
Jagora : Uban Bakwai, x^2
'Y/Amshi : Uban Lairo had da Amadu. x^2

---

38 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$.

Jagora : Salihu xan Durumbu, x^2
'Y/Amshi : Mainasara xin da ba su so. x^2

Jagora : Ai jikan Kada riqe ni qwarai, x^2
'Y/Amshi : Tun da ka riqa. x^2

Jagora : Sarki ya riqe ni, x^2
'Y/Amshi : Ba ni da sauran shiga qaya, x^2
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Sarki za shi Sakkwato, x^2
'Y/Amshi : Mu ko mun yi rakkiya. x^2

Jagora : Baba ka zak ka lahiya, x^2
'Y/Amshi : Dawowak ka lahiya, x^2
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Salihu ya hawo da sa'as Sarki Balarabe, x^2
'Y/Amshi : Kuma ya hawo da martabar Jari qanin Balarabe. x^2
Jagora : Salihu ya hawo da sa'as Sarki Baranqwame, x^2
'Y/Amshi : Kuma ya hawo da martabar Sarki Bartuhwatuhwa. x^2

Jagora : Ko was san Bartuhwatuhwa,
'Y/Amshi : Kuma was san Baranqwame.

Jagora : To, in ba wanda yas sani ku bari,
'Y/Amshi : Ku bari in hwaxan maku.
Jagora : Wani Sarki da ag Gubur,
'Y/Amshi : Shi ab Bartuhwatuhwa.
Jagora : Wani Sarki na can Gubur,
'Y/Amshi : Shi ab Baranqwame,
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.
Jagora : Salihu kai am mayaqi, x^2
'Y/Amshi : Kai a Kannin da Hammadin. x^2
Jagora : Wasu manyan sarakuna ne,
'Y/Amshi : Kannin da Hammadin.

Jagora : Na ji xiyan mutum guda ne,
‘Y/Amshi : Kannin da Hammadin.
Jagora : Kowane sai da yay yi sarki,
‘Y/Amshi : Kannin da Hammadin.
Jagora : Ran dakak kututturu,
‘Y/Amshi : Ran nan an ka kakkashikke Kannin da Hammadin.
Jagora : Ran hwamar kututturu,
‘Y/Amshi : Ran nan an ka kakkashikke Kannin da Hammadin.

Jagora : Ran da uwarsu tai jawabi,
‘Y/Amshi : Ta ce ma Gobirawa haka kun ka kai ni,
: Ba Kannin babu Hammadin,
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : A yi larwai iri-iri,
: A yi larwan sarakuna,
: In dai an yi bincike,
: In an kama salsala,
‘Y/Amshi : In an kai ga,
: Gobirawa asalinsu ya xara.

Jagora : In an kai ga,
‘Y/Amshi : Gobirawa asalinsu ya xara.

Jagora : Ko hwamar Badar da an ka yi, x^2
‘Y/Amshi : Su an na Annabi. x^2
Jagora : Ko dagar Badar da an ka yi, x^2
‘Y/Amshi : Su an na Annabi. x^2

Jagora : Kakanninka sun ci birnin Kisira, x^2
‘Y/Amshi : Sun ci Qaura Kamusa can Badar, x^2
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.
Jagora : Wani wawa marar gaba,
‘Y/Amshi : Wai yaz zo a ba shi sarki,
: Sai D. O. ya hana.
Jagora : Wani tsoho mahaukaci,
‘Y/Amshi : Sai ya zo a ba shi sarki,
: Sai D. O. ya hana.

Jagora : Sai yac ce an qi ba ka, x^2
'Y/Amshi : Xebi da qarhin Babarbara. x^2
Jagora : Ai Kusu da yay yi sheka,
: 'Ya'yansa yay yi ma,
: Bilbili da yai gida,
: Don 'ya'yansa yay yi,
: Ummaru bai kau ba,
: Sai da yak kai ga halin na Innuwa,
'Y/Amshi : Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Ummaru Allah jiqan ka, x^3
'Y/Amshi : Allah ya kam mai da gahwara, x^3
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Sannu da sirdi na Garba,
'Y/Amshi : Sannu da zowak ka lahiya.
Jagora : Gambai na Halima,
'Y/Amshi : Mainasara yaushe kaz zaka.
Jagora : Mainasara uban sarki, x^2
'Y/Amshi : Hitila maganin duhu, x^2
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Kai kag gaji Bawa,
'Y/Amshi : Jangwarzo babu gardama.
Jagora : Kuma ka gaji Bawa,
'Y/Amshi : Xangwamci babu gardama,
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ummaru Shawai (1916-194)[39]*,*
Gindin Waqa : Jikan Jari ginshiqi,

---

39 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{1}$.

: Dibirtau uban Zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Safka lahiya uban bango gishiqin gabas,
‘Y/Amshi : Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Safka lahiya,
‘Y/Amshi : Uban bango gishiqin gabas.

Jagora : Sannu da sirdi na Garba, x^2
‘Y/Amshi : Sannu da zowak ka lahiya. x^2

Jagora : Gambai na Halima, x^2
‘Y/Amshi : Mainasara yaushe kaz zaka, x^2
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Uban Bakwai, x^2
‘Y/Amshi : Uban Lairo had da Amadu. x^2

Jagora : Salihu xan Durumbu, x^2
‘Y/Amshi : Mainasara xin da ba su so. x^2

Jagora : Sarki Mayaqi ne, x^2
‘Y/Amshi : Ko Mamman na Dawwa ne. x^2

Jagora : Kai kag gaji Bawa,
‘Y/Amshi : Jangwarzo babu gardama.
Jagora : Kuma ka gaji Bawa,
‘Y/Amshi : Xangwamci babu gardama,
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.
Jagora : Sarki za shi Sakkwato, x^2
‘Y/Amshi : Mu ko mun yi rakkiya. x^2

Jagora : Baba ka zak ka lahiya, x^2
‘Y/Amshi : Dawowak ka lahiya, x^2
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Salihu ya hawo da sa’as Sarki Balarabe, x^2

‘Y/Amshi : Kuma ya hawo da martabar Jari qanin Balarabe. x^2

Jagora : Salihu ya hawo da sa’as Sarki Baranqwame, x^2
‘Y/Amshi : Kuma ya hawo da martabar Sarki Bartuhwatuhwa. x^2

Jagora : Ko was san Bartuhwatuhwa,
‘Y/Amshi : Kuma was san Baranqwame.
Jagora : To, in ba wanda yas sani ku bari,
‘Y/Amshi : Ku bari in hwaxan maku.
Jagora : Wani Sarki da ag Gubur,
‘Y/Amshi : Shi ab Bartuhwatuhwa.
Jagora : Wani Sarki na can Gubur,
‘Y/Amshi : Shi ab Baranqwame.

Jagora : Salihu kai am mayaqi, x^2
‘Y/Amshi : Kai a Kannin da Hammadin. x^2
Jagora : Na ji xiyan mutum guda ne,
‘Y/Amshi : Kannin da Hammadin.
Jagora : Kowane sai da yay yi sarki,
‘Y/Amshi : Kannin da Hammadin.
Jagora : Ran hwamar kututturu,
‘Y/Amshi : Ran nan an ka kakkashikke Kannin da Hammadin.
Jagora : Ran dakak kututturu,
‘Y/Amshi : Ran nan an ka kakkashikke Kannin da Hammadin.
Jagora : Ran da uwarsu tai jawabi,
‘Y/Amshi : Ta ce ma Gobirawa haka kun ka kai ni,
: Ba Kannin babu Hammadin,
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.
Jagora : A yi larwai iri-iri,
: A yi larwan sarakuna,
: In dai an yi bincike,
: In an kama salsala,
‘Y/Amshi : In an kai ga,
: Gobirawa asalinsu ya xara.

Jagora : In an kai ga,
‘Y/Amshi : Gobirawa asalinsu ya xara.
Jagora : Ko hwamar Badar da an ka yi, x^2

‘Y/Amshi : Su an na Annabi. x^2
Jagora : Ko dagar Badar da an ka yi, x^2
‘Y/Amshi : Su an na Annabi. x^2

Jagora : Kakanninka sun ci birnin Kisira,
‘Y/Amshi : Sun ci Qaura Kamusa can Badar.
Jagora : Gulbi ya ci mai kwari, x^2
‘Y/Amshi : Bajimin Garba xan Hassan, x^2
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Uban Bakwai, x^2
‘Y/Amshi : Uban Lairo had da Amadu. x^2
Jagora : Yamutsa gari, yamutsa gari, x^3
: Toya gari, toya gari, x^3
‘Y/Amshi : Dibirtau uban zagi,
: Xan Mamman na Baciri.

Jagora : Uban Bakwai, x^2
‘Y/Amshi : Uban Lairo had da Amadu. x^2
Jagora : Salihu xan Durumbu, x^2
‘Y/Amshi : Mainasara xin da ba su so. x^2
Jagora : Sarki Mayaqi ne, x^2
‘Y/Amshi : Ko Mamman na Dawwa ne. x^2

Jagora : Kai kag gaji Bawa,
‘Y/Amshi : Jangwarzo babu gardama.

Jagora : Kuma ka gaji Bawa,
‘Y/Amshi : Xangwamci babu gardama,
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Sarki mai kuku-kuku,
‘Y/Amshi : Turawa duk garau suke.

Jagora : ‘Yan Soja da ag garai,

‘Y/Amshi : ‘Yan Sanda garai suke,
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ummaru Shawai (1916-1945)[40]*,*
Gindin Waqa : Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban Zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Dibirtau uban zagi,
‘Y/Amshi : Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

---

40 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{2}$.

Jagora : Sauka da lahiya,
‘Y/Amshi : Sarki farin wata.

Jagora : Salihu ya hau da sa’as sarki Balarabe,
‘Y/Amshi : Kuma ya hau da martabar Jari qanen Balarabe.

Jagora : Salihu ya hawo da sa’as sarki Baranqwame,
‘Y/Amshi : Kuma ya hawo da martabar sarki Bartuhwatuhwa.

Jagora : Was san Bartuhwatuhwa,
‘Y/Amshi : Kuma was san Baranqwame.

Jagora : In ba wanda yas sani,
‘Y/Amshi : To, ku bari in hwaxa muku.

Jagora : Wani sarki da ag Gubur,
‘Y/Amshi : Shi ab Bartuhwatuhwa,
Jagora : Kuma wani sarki da ag Gubur,
‘Y/Amshi : Shi ab Baranqwame.

Jagora : In an yi bincike,
: In an kama da salsala,
‘Y/Amshi : In an kai ga Gobirawa asalinsu yax xara.

Jagora : Ko faman Badar da an,
‘Y/Amshi : Ka yi ku an na Annabi.

Jagora : Ginshiqin gada,
‘Y/Amshi : Riqe maza tun da ka riqa.

Jagora : Gulbi ya buge gari,
‘Y/Amshi : Falalen da aw wata,
Jagora : Gawurtaccen uban zagi,
‘Y/Amshi : Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Wani wawa marar gaba,
‘Y/Amshi : Wai yaz zo a ba shi sarki,

: Sai D. O. ya hana.
Jagora : Wani tsoho mahaukaci,
'Y/Amshi : Sai ya zo a ba shi sarki,
: Sai D. O. ya hana.

Jagora : Sai yac ce an qi ba ka, x^2
'Y/Amshi : Xebi da qarhin Babarbara. x^2

Jagora : Ai Kusu da yay yi sheka,
: 'Ya'yansa yay yi ma,
: Bilbili da yai gida,
: Don 'ya'yansa yay yi,
: Ummaru bai kau ba,
: Sai da yak kai ga halin na Innuwa,
'Y/Amshi : Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Ummaru Allah jiqan ka, x^3
'Y/Amshi : Allah ya kam mai da gahwara, x^3
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,
Ubangida : Garkuwan Dutsi Innar Gobir[41]*,*

28. *Gindin Waqa : Ka buwayi maza sai na zo,*
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Bajimin Bawa Garkuwan Dutsi,
'Y/Amshi : Wa ne masu bindiga,
: Wa ne 'yan mashi,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : A gaishe ka Garkuwas sarki, x^2

---

[41] An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$.

‘Y/Amshi : Ko mi za a yi riqon Gobir sai ka ce,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye. x^2

Jagora : Don Allah Gobirawa, x^2
‘Y/Amshi : Sai ku yi niy ya,
: Ku zan ka yin wada sarki yac ce, x^2
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Ya xauke masu roqo,
‘Y/Amshi : Ya riqe haw wanda ba shi roqo.
: In ba don kai ba,
: Da mazaje sun sha yunwa,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Garkuwa ya xauke masu roqo,
‘Y/Amshi : Ya riqe haw wanda ba shi roqo.
: In ba don kai ba,
: Da mazaje sun sha yunwa,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.
Jagora : Kai nis sani qasas Sabon Birni, x^2
‘Y/Amshi : Tun da kai ka wa ‘ya’yana toshi, x^2
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Garkuwa shi wanda am musulmi,
‘Y/Amshi : In abu ya samu ba ya savo,
: Amma an so a zan ajewa wajjen Allah,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Ashe wanda am musulmi,
‘Y/Amshi : In abu ya samu ba ya savo,
: Amma an so a zan ajewa wajjen Allah,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Gudurmusun dutsi, x^3
'Y/Amshi : Mai xaukak ka shi ka ji ba 'yan kallo ba. x^3

Jagora : Ina ruwan 'yan kallo, x^2
'Y/Amshi : Kowa ya sa idanunai sai dibi, x^2
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : A gaishe ka garkuwas sarki, x^2
'Y/Amshi : Komi za a yi riqon Gobir sai ka ce, x^2
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Alhaji jikan Bagobiri,
'Y/Amshi : Dogo xan kwasau,
: Ina shirin in zo gaishe ka,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Jatau xan Bagobiri,
'Y/Amshi : Dogo xan kwasau,
: Ina shirin in zo gaishe ka.

Jagora : Alhaji jikan Bagobiri,
'Y/Amshi : Dogo xan kwasau,
: Ina shirin in zo gaishe ka,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : In ka ganan da rigash shadda,
'Y/Amshi : Alhaji wadda Garkuwa yab bayat ce.
Jagora : In ka ganan da wandon shadda,
'Y/Amshi : Alhaji wadda Garkuwa yab bayat ce.
Jagora : In ka ganan da taggon shadda,
'Y/Amshi : Alhaji wadda Garkuwa yab bayat ce,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Garkuwa barkam maza da qwazo,
'Y/Amshi : Mu kam kullum muna tahowa amsan naira,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Barkam maza da qwazo,
'Y/Amshi : Mu kam kullum muna tahowa amsan naira,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Baraya barkam maza da qwazo,
'Y/Amshi : Mu kam kullum muna tahowa amsan naira,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Garkuwan Dutsi Innar Gobir[42]*,*
Gindin Waqa : Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Bajimin Bawa Garkuwan Dutsi,
'Y/Amshi : Wa ne masu bindiga,
: Wa ne 'yan mashi,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : A gaishe ka Garkuwas sarki,
'Y/Amshi : Ko mi za a yi riqon Gobir sai ka ce,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

---

[42] An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{1}$.

Jagora : Jatau xan Bagobiri,
‘Y/Amshi : Dogo xan kwasau,
: Ina shirin in zo gaishe ka,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Don Allah Gobirawa, x^2
‘Y/Amshi : Sai ku yi niy ya,
: Ku zan ka yin wada sarki yac ce, x^2
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Ashe wanda am Musulmi,
‘Y/Amshi : In abu ya samu ba ya savo,
: Amma na so a zan ajewa wajjen Allah,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Gudurmusun dutsi, x^2
‘Y/Amshi : Mai xaukak kashi-kashi ba ‘yan kallo ba. x^2

Jagora : Ina ruwan ‘yan kallo, x^2
‘Y/Amshi : Kowa ya sa idanunai sai dibi, x^2
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Barkam maza da qwazo, x^2
‘Y/Amshi : Mu kam kullum muna tahowa amsan Naira. x^2

Jagora : Ya xauke masu roqo,
‘Y/Amshi : Ya riqe har wanda ba shi roqo.

Jagora : In ba don kai ba,
‘Y/Amshi : Mazaje sun sha yunwa,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Kai nis sani qasas Sabon Birni, x^2

‘Y/Amshi : Tun da kai ka wa ‘ya’yana toshi, x^2
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Garkuwa barkam maza da qwazo,
‘Y/Amshi : Mu kam kullum muna tahowa amsan naira,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Baraya barkam maza da qwazo,
‘Y/Amshi : Mu kam kullum muna tahowa amsan naira,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : A gaishe ka garkuwas sarki,
‘Y/Amshi : Komi za a yi riqon Gobir sai ka ce,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Salihu xan Ummaru Shawai (1916-1975)[43],

29. *Gindin Waqa : Mainasara na Isa na Musa,*
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Sarki ya kwana da hwarin ciki,
‘Y/Amshi : Hay yau bai kwan da muni ga rai ba,
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Baban Yari baban Makama, x^2
‘Y/Amshi : Baba Uban Lihidda na Barga, x^2
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Ya zo Makka ya zo Madina, x^2

---

[43] An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{147}$ $^1/_8$.

‘Y/Amshi : Alhaji ya taho lahiya lau. x^2
Jagora : Ga Alhaji ya taho za mu tarbe, x^2
‘Y/Amshi : Da wace gaisuwa zan ishe mai? x^2
Jagora : Ko waqar sarauta muka mai, x^2
‘Y/Amshi : Koko dai salati mu kai mai. x^2
Jagora : To, in dai salati mu kai mai,
‘Y/Amshi : Sun ce ko kam mu hwara da zambo,
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Baqon Jidda baqon Kano, x^2
‘Y/Amshi : Alhaji baqon ministan Arewa. x^2

Jagora : Sarkin Makka ya yo wasiqa,
‘Y/Amshi : Ya aiko ma jikan ta Barga.
Jagora : Kuma Sardauna ya yo wasiqa,
‘Y/Amshi : Ya aiko ma jikan ta Barga.

Jagora : Sun ce galibin duniyag ga,
‘Y/Amshi : Duka kowa ya koma Musulmi.
Jagora : A yi kono da salla da zakka, x^2
‘Y/Amshi : A yi ta yin abin da Allah ke qamna. x^2
Jagora : A yi aure a zan son zumunta, x^2
‘Y/Amshi : A yi ta abin da Allah ke qamna. x^2
Jagora : Kowane sarki shina na shi yayi, x^2
‘Y/Amshi : Ga namu zamani ba iri nai. x^2

Jagora : Baciri ya yi mulki gabas,
‘Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Goba ya yi mulki gabas,
‘Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Jacili ya yi mulki gabas,
‘Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Mayaqi ya yi mulki gabas,
‘Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Goba ya yi mulki gabas,
‘Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Ali ya yi mulki gabas,
‘Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Mainasara ya yi mulki gabas,

‘Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Almu ya yi mulki gabas,
‘Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Gulbi ya yi mulki gabas,
‘Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Xanmagaji ya yi mulki gabas,
‘Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Jadi ya yi mulki gabas,
‘Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Jari ya yi mulki gabas,
‘Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Shawai ya yi mulki gabas,
‘Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Salihu ya yi mulki gabas,
‘Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Tun can zamanin zamunna,
‘Y/Amshi : Alhaji tun can da manyan sarakai,
: Duk kwararon da an nan na Gobir,
: In ba a san da jikan Kilo ba,
: Ba sarkin da yak kwashi arhwa,
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Alhaji tun da ka gaji arhwa, x^2
‘Y/Amshi : Ko ni ma ina son ka sani. x^2

Jagora : ‘Yan kuxxi garan hwan tamanin,
‘Y/Amshi : Kuma in ka biya babu laihi.

Jagora : Xan guzurin da nih hwara tardawa,
‘Y/Amshi : Na duqule na yi shanu,
: To, amma kwarai sun tare su,
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Sarki ya kwana da hwarin ciki,
‘Y/Amshi : Hay yau bai kwan da muni ga rai ba,

: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Salihu xan Ummaru Shawai (1916-1975)[44]*,*
Gindin Waqa : Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Baban Yari baban Makama, x^2
'Y/Amshi : Baba Uban Lihidda na Barga, x^2
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Ya zo Makka ya zo Madina, x^2
'Y/Amshi : Alhaji ya taho lahiya lau. x^2

Jagora : Ga Alhaji ya taho za mu tarbe, x^2
'Y/Amshi : Da wace gaisuwa zan ishe mai? x^2

Jagora : Ko waqar sarauta muka mai, x^2
'Y/Amshi : Koko dai salati mu kai mai. x^2

---

44 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{375}$ $^1/_7$.

Jagora : To, in dai salati mu kai mai,
‘Y/Amshi : Sun ce ko kam mu hwara da zambo,
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Baqon Jidda baqon Kano, x^2
‘Y/Amshi : Alhaji baqon ministan Arewa. x^2

Jagora : Sarkin Makka ya yo wasiqa,
‘Y/Amshi : Ya aiko ma jikan ta Barga.
Jagora : Kuma Sardauna ya yo wasiqa,
‘Y/Amshi : Ya aiko ma jikan ta Barga.

Jagora : Sun ce galibin duniyag ga,
‘Y/Amshi : Duka kowa ya koma Musulmi.

Jagora : A yi kono da salla da zakka, x^2
‘Y/Amshi : A yi ta yin abin da Allah ke qamna. x^2

Jagora : A yi aure a zan son zumunta, x^2
‘Y/Amshi : A yi ta abin da Allah ke qamna, x^2
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : To, ni ga ni na sa tsari, x^2
‘Y/Amshi : Amma matan gari na hanawa, x^2
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Lalle matan gari, x^2
‘Y/Amshi : Sun yi varna,
: Ba sui abin da Allah ke so ba, x^2
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Wance da wance sun gaji varna, x^2

‘Y/Amshi : To, varnassu ba za ta ci ba,
: Amma ta ci Allah kiyaye, x^2
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Ga matan da nis sa tsari,
‘Y/Amshi : Yau ga su ga hanya za su tarbe,
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Sarki ya kwana da farin ciki,
‘Y/Amshi : Hay yau bai kwan da muni ga rai ba.

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gabas na Gwaranyo Alhaji Umaru[45]*,*

30. *Gindin Waqa : Namijin daga uban Gardaye,*
: *Sarkin Gwaranyo.*

Jagora : To, Allah shi ad da girma,
‘Y/Amshi : To, Allah shi ad da baiwa,
: Alhaji ya san da kwanan yaro,
: Ya san da tsoho,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Jikan sarkin gabas,
‘Y/Amshi : Mainasara xan Garba sarki,
: Allah ya ba ka girma,
: Ga gadi tsoho.

Jagora : Ran juma’a naz zo Gwaranyo,
‘Y/Amshi : Har daxi ya tsallake ni,
: ‘Ya’yana sai ku yo mun murna,
: Na iske sarki.

---

45 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{1}/_{375}$ $^{1}/_{12}$.

Jagora : Lalle na yi sa'a,
'Y/Amshi : Na ko gode ma sarkin yaqi,
: Manyan Gwaranyo.

Jagora : Ai ga riga wadda sarkin yaqi,
: Yab bai a kai man,
: Kuma ga rawani da sarkin yaqi,
: Yab bai a kai man,
: Ga takalmi da sarkin yaqi,
: Yab bai a kai man, x^2
'Y/Amshi : Lalle sarkin yaqi ya zan lamba xai,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.
Jagora : Sarkin yaqi ga dai kyauta uku,
'Y/Amshi : Yai man albarkas sarki Gwaranyo,
: Kuma dai ya ba ni kuxin mota,
: Ya ce a kai man,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Allah ya shirya sarki,
: Kuma ya koma ya shinhixa ka daji,
: Ya koma ya yoka birni,
'Y/Amshi : Duk mai son ba ka wahala,
: Ya ba ka fili,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Ina qaunar mai kama maciji, x^2
'Y/Amshi : In dai bai shaqu da ni ba,
: Bari in kwanan mutum sun qare,
: Shi za ya kausai, x^2
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Sauran kaya ina son ku riqe ni,
'Y/Amshi : Ina son ku riqe,
: Ku rungume ni,
: Ku riqe ni qwarai,

: Kamar nama ya kama kalwa.

Jagora : In nama yak kama kalwa,
‘Y/Amshi : Mata ba sai kun hwaxa ba,
: Ku ruhe shi,
: Ku tsabbattace shi,
: Kah hancin kowa ya kai mai,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Jikan sarkin gabas,
‘Y/Amshi : Mainasara xan Garba sarki,
: Allah yai ma girman duniya,
: Ka gaji komi,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Lalle Umaru xan Salo ya ba ni komi,
‘Y/Amshi : Ga riga wadda yab ba ni,
: Yac ce a kai man,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : To, Allah shi ad da girma,
‘Y/Amshi : To, Allah shi ad da baiwa,
: Alhaji ya san da kwanan yaro,
: Ya san da tsoho,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gabas na Gwaranyo Umaru[46]*,*
Gindin Waqa : Namijin daga uban Gardaye,
***:** Sarkin Gwaranyo.*

Jagora : To, Allah shi ad da girma, x^2
'Y/Amshi : To, Allah shi ad da baiwa,
: Alhaji ya san da kwanan yaro,
: Ya san da tsoho,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo. x^2

Jagora : Na taso dag gida, x^2
'Y/Amshi : 'Yar Rimawa mun ka ratso,
: To, nij ji Gusun-Gusoro,
: Ban koma ta Cunkume ba,
: Hanya ta xaukaka ta yi kwana,
: Ta yo Shinaka,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo. x^2

Jagora : Na zo in ratso Shinaka,
'Y/Amshi : Tun da mazaje ash Shinaka,
: Hanya ta tashi ta hau doki,
: Ta yo Gwaranyo,

---

46 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{54}$ $^1/_2$.

: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Ran juma'a na zo Gwaranyo,
'Y/Amshi : Har daxi ya tsallake ni,
: 'Ya'yana sai ku yo mun murna,
: Na iske sarki,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Ni ko yau na gode Allah,
: Na ko gode ma Sarki,
: Na ko gode ma Sarkin Yaqi,
: Manyan Gwaranyo,
'Y/Amshi : Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Ga riga wadda sarkin yaqi,
: Yab bai a kai man,
: Kuma ga rawani da sarkin yaqi,
: Yab bai a kai man,
: Ga takalmi da sarkin yaqi,
: Yab bai a kai man,
'Y/Amshi : Lalle sarkin yaqi ya zan lamba xai,
: Ko da sarki,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Kwasar kyauta uku yai min,
'Y/Amshi : Albarkas sarki Gwaranyo,
: Kuma dai ya ba ni kuxin mota,
: Ya ce a kai man,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : To, Allah shi ad da girma, x^2
'Y/Amshi : To, Allah shi ad da baiwa,
: Alhaji ya san da kwanan yaro,
: Ya san da tsoho.

Jagora : To, Allah ya gina Dutsi,

: Yak koma yag gina Laka,
: Allah ya haska daji,
: Yak koma yah haska birni,
: Dum mai nuqura da kai,
: Ya hwasa sun ba ka hili,
‘Y/Amshi : Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Ina qaunar mai kama maciji, x^2
‘Y/Amshi : In dai bai shaqu da ni ba,
: Bari in kwanan mutum sun qare,
: Shi za ya kausai, x^2
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Sauran kaya ina son ku riqe ni,
‘Y/Amshi : Ina son ku riqe,
: Ku rungume ni,
: Ku riqe ni qwarai,
: Kamar nama ya kama kalwa,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : In nama yak kama kalwa,
‘Y/Amshi : Mata ba sai kun hwaxa ba,
: Ku ruhe shi,
: Ku tsabbattace shi,
: Kah hancin kowa ya kai mai,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Jikan sarkin gabas,
‘Y/Amshi : Mainasara xan Garba sarki,
: Allah yai ma girman duniya,
: Ka gaji komi,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : To, Allah shi ad da girma,

‘Y/Amshi : To, Allah shi ad da baiwa,
: Alhaji ya san da kwanan yaro,
: Ya san da tsoho,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni
Ubangida : Sarkin Gobir Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003)[47]*,*

31. *Gindin Waqa : Uban Makama uban Gardaye,*
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ina mazan suke? x^2
'Y/Amshi : Sarkin Gobir ina mazan suke duk sun qare,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : 'Yan sarki kowa shi yi gona,
'Y/Amshi : Tau bayan na Habu ya kama,
: Ban san mai iya bankatai ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Bawa uban Bunu ikon Allah,
'Y/Amshi : In ya xauki mutum ya dace,
: In kau ka qi mutum ya cine,
: Ban san mai iya kwasa tai ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Alhaji xan Dango jikan Inna,
'Y/Amshi : Ya haxa ni da xan Mamman,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

---

47 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{1}/_{144}$ $^{1}/_{1}$ - AL $^{1}/_{144}$ $^{1}/_{2}$.

Jagora : Na gode maka Sarkin Gobir,
'Y/Amshi : Alhaji Makaxa ya gode,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ya gama mu da kaya,
'Y/Amshi : Kaya, ko yanzu ya gama mu da kayan iko,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ga wata riga Sarki yab ba ni,
'Y/Amshi : Ta zube qasa hat kai oba,
: Alhaji har bisaki ya share
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ga xan tasala da Sarki yab ba ni,
'Y/Amshi : Da ka naxa shi kamar xan xaki,
: Hay ya sa mani doron tilas,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : To, alkyabba ga da Sarki yab ba ni,
'Y/Amshi : Ya qara mana hasken hwada,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ga hwan talatin Sarki yab ba ni, x^2
'Y/Amshi : In yi jajibirin ras salla. x^2

Jagora : Ai kuxin sun wuce kwasar nama,
'Y/Amshi : Rago za mu saye ko xan sa,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Taron Isa da anka yi niz zo,
'Y/Amshi : Ba da kamar makaxa niz zo ba.

Jagora : 'Yan yara sun ga shiga ta Isa,
'Y/Amshi : Has sun ce wane xan sarki na.

Jagora : Don sun gane ni,
'Y/Amshi : Da 'yan gangumma,
: Da sun ce wani ma sarki na.

Jagora : Wasu sun ce, ba dai sarki ne ba,
'Y/Amshi : Yalla dai makaxin sarki na.

Jagora : Bambanta ni uban Gardaye,
'Y/Amshi : Ya sake mana sabbin kaya,
: Saura yai mana sabon doki,
: In sake masa sabon launi,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Alhaji Bakwai ya shirya Masallaci,
'Y/Amshi : Ya yo muna shi don Allah,
: Bai yi saboda bixak kuxxi ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Masallacin ga da kay yi na Juma'a,
'Y/Amshi : Jikka dubu da xari sun qare,
: Amma ba a gama shiryassai ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ga latirin ga kuxxin hwanho,
'Y/Amshi : To, kuma ba a gama tagogi ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Bawa ba ya son raini,
'Y/Amshi : Bai saba da qulle-qulle batun banza ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni
Ubangida : Sarkin Gobir Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003)[48]*,*
Gindin Waqa : Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Alhaji xan Dango jikan Geda,
'Y/Amshi : Ya haxa ta gari xan Mamman,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Alhaji xan Dango jikan Geda,
'Y/Amshi : Ya haxa ta gari xan Mamman.
Jagora : Baban Shamaki Sarki,
'Y/Amshi : Alhaji Baban Jekadiya xan Mamman.
Jagora : Baban Shinhixa Sarki,
'Y/Amshi : Alhaji Baban Jekadiya xan Mamman,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Dogo na Salihu jikan Gunda, x^2
'Y/Amshi : Uban Hassan na Baraz Zaki. x^2

Jagora : To, zamanin na Habu xan Inna, x^2
'Y/Amshi : Gobir ba a da sauran yunwa,
: To, kuma ba a da sauran ragga,
: Kowa yay yi bixa ya dace,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi. x^2

Jagora : Darzaje maqiya xan Inna, x^2
'Y/Amshi : Kowac ce ka ce shi yac ce,
: Sarki bai yi ma kowa shairi,
: To, kuma bai ci abin kowa ba,

---

48 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{374}$ $^1/_2$.

: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi. x^2
Jagora : Ina mazan suke? x^2
'Y/Amshi : Sarkin Gobir ina mazan suke duk sun qare. x^2

Jagora : 'Yan sarki kowa shi yi gona,
'Y/Amshi : Tau bayan na Habu ya kama,
: Ban san mai iya bankatai ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Bawa uban Bunu ikon Allah,
'Y/Amshi : In ya xauki mutum ya dace,
: In kau ka qi mutum ya cine,
: Ban san mai iya kwasa tai ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Darzaje maqiya xan Inna, x^2
'Y/Amshi : Kowac ce ka ce shi yac ce,
: Sarki bai yi ma kowa shairi,
: To, kuma bai ci abin kowa ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi. x^2

Jagora : To, zamanin na Habu xan Inna, x^2
'Y/Amshi : Gobir ba a da sauran yunwa,
: To, kuma ba a da sauran ragga,
: Kowa yay yi bixa ya dace,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi. x^2

Jagora : Na gode maka Sarkin Gobir, x^2
'Y/Amshi : Alhajim Makaxa ya gode.
Jagora : Alhaji ya gama mu da kaya,
'Y/Amshi : Ko yanzu ya zuba mana kayan iko.
Jagora : To, Alhaji ya gama mu da kaya,
'Y/Amshi : Ko yanzu ya zuba mana kayan iko,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ga wata riga Sarki yab ba ni,
'Y/Amshi : Ta zube qasa hat kai oba,
: Alhaji har bisaki ya share
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ga xan tasala da Sarki yab ba ni,
'Y/Amshi : Da ka naxa shi kamar xan xaki,
: Hay ya sa mani doron tilas,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : To, alkyabba ga da Sarki yab ba ni,
'Y/Amshi : Ya qara mana hasken hwada,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ga hwan talatin Sarki yab ba ni, x^2
'Y/Amshi : In yi jajibirin ras salla. x^2

Jagora : Ai kuxin sun wuce kwasar nama,
'Y/Amshi : Rago za mu saye ko xan sa,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Uban Salau ya zo rangadi,
'Y/Amshi : Amma Alhaji ni ban zo ba,
: Sai dai yanzu niz zo gaisai,
: Da mai da xari da biyat yab ba ni.

Jagora : Kyautar na Iro uban Gardaye,
'Y/Amshi : Kyautar ta hi gaban na gode,
: Sai dai ai ladabi ko shukura,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : In da na gadi sarauta birni, x^2
'Y/Amshi : Da ko ba ni da kuxxi an ban. x^2

Jagora : Da in ba ka ba ni gari Idi ba, x^2
'Y/Amshi : To, ka naxa mana kojan zaki. x^2

Jagora : Amma don za ni ga ‘yan sarki ta,
'Y/Amshi : Da sarautar makaxa nik kama.
Jagora : Sarki don za ni ga ‘yan sarki ta,
'Y/Amshi : Ida sarautar makaxa nik kama.

Jagora : To, qwamma ka ba ni garin Idi, x^2
'Y/Amshi : Ko da na ga ba su da kanwar hwari. x^2

Jagora : Diba sa’an da maxa tak kama, x^2
'Y/Amshi : Kullum niz zaka sai sun ba ni. x^2

Jagora : Na gode ma garin Idi,
'Y/Amshi : Hatta mazansu da ‘yan matansu,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Alhaji Bakwai ya shirya Masallaci,
'Y/Amshi : Ya yo muna shi don Allah,
: Bai yi saboda bixak kuxxi ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Masallacin ga da kay yi na Juma’a,
'Y/Amshi : Jikka dubu da xari sun qare,
: Amma ba a gama shiryassai ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.
Jagora : Ga latirin ga kuxxin hwanho,
'Y/Amshi : To, kuma ba a gama tagogi ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Bawa ba ya son raini,
'Y/Amshi : Bai saba da qulle-qulle batun banza ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.
Jagora : Dogo na Salihu jikan Qunda,

'Y/Amshi : Uban Hassan xan Barayaz Zaki.
Jagora : Kai qyale maqiya xan Inna,
: Kowac ce ka ce shi yac ce,
: Sarki bai ci abin kowa ba,
'Y/Amshi : To, kuma bai yi ma kowa sharri,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Bai ci abin kowa ba,
'Y/Amshi : To, kuma bai yi ma kowa sharri.
Jagora : A gaishe ka Alhaji Gonab Baye,
'Y/Amshi : Ina ruwanta da kai mata taki.
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ga wani ya aje goronai,
'Y/Amshi : Kowane ya sagale mai.
Jagora : Ga wani ya xau goron sarki,
: Ya dahe shi ga hannun dama,
: Na iske shi qanin, x^2
'Y/Amshi : Xan wannan ba ya da sauran kunya, x^2
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ga wani ya yi gina ya faxa,
'Y/Amshi : Bai saba da ginar ramu ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Alhaji xan Dango jikan Geda,
'Y/Amshi : Ya haxa ta gari xan Mamman.
Jagora : Baban Shamaki Sarki,
'Y/Amshi : Alhaji Baban Jekadiya xan Mamman.
Jagora : Baban Shinhixa Sarki,
'Y/Amshi : Alhaji Baban Jekadiya xan Mamman,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.
Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,

Mai Waqa : Ubandawaki, Alhaji Bala Xanladi[49]*,*

32. *Gindin Waqa : Ginshiqin Zakari Baqadire,*
: Qasaitacce uban Dawaki,
: Na Isaka gamda'aren mai daga.

Jagora : Zaki mai sulke da bindiga mai masu, x^2
'Y/Amshi : Kar ka so ka ji tsoro,
: Abin da ba ka gada ba,
: Ginshiqin Zakari Baqadire,
: Qasaitacce uban Dawaki,
: Na Isaka gamda'aren mai daga. x^2

Jagora : Ya xauki mashi, x^3
'Y/Amshi : Ya xauki Babarbaren Kakanai,
: Ga yanzu kayan Xanladi
: Duk suna jikkatai. x^3

Jagora : Ko shi xarma sirdi, x^3
'Y/Amshi : Kullum ka zan zuwa sa-rani,
: Inda kag ga tumaki,
: Ka zan iza su da shanu,
: In Bahillace yay yi gardama sare shi,
: Ginshiqin Zakari Baqadire,
: Qasaitacce uban Dawaki,
: Na Isaka gamda'aren mai daga. x^3

Jagora : Ga zanga-zanga, x^2
'Y/Amshi : Ya tashi zamanin xan A'i,
: Baba giye shira kayanka,
: Ba ni son ka da wargi,
: Ginshiqin Zakari Baqadire,
: Qasaitacce uban Dawaki,
: Na Isaka gamda'aren mai daga. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa,
Waqa : Waqar Ilmi[50]*,*

---

49 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{374}$ $^1/_7$.

33. *Gindin Waqa : Harka da ilmi mu kai,*
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya.

Jagora : Harka da ilmi mu kai, x^2
: Allah ya gyara mana,
'Y/Amshi : Mu gama da ban-gaskiya. x^2

Jagora : In dai mutum yav vace, x^2
: Maisai ga hanya mu kai,
'Y/Amshi : In ko mutum ya qiya,
: Mu iza shi bayan gida,
: Harka da ilmi mu kai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya. x^2

Jagora : In noma mutum za shi yi, x^2
'Y/Amshi : Kuma in hwatauci ya kai,
: Ya gama da ban-gaskiya,
: Harka da ilmi mu kai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya. x^2

Jagora : Gwamnati gyara aiki ta kai,
: Ta gyara aikin dawa,
: Ka na ta dawo gida,
'Y/Amshi : Harka da ilmi mu kai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya.

Jagora : Gwamnati gyara aiki ta kai, x^2
'Y/Amshi : Ta gyara aikin dawa,
: Kuma za ta gyaran gida. x^2

Jagora : Lalle tun da ga shigihhu, x^2
'Y/Amshi : Ga xakuna an shirya,
: Ni ba ni kwana wuri, x^2

---

50 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{147}$ $^1/_2$.

: Harka da ilmi mu kai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya.

Jagora : Mu yawon aminci mu kai, x^2
'Y/Amshi : In ya hito dag gabas,
: Ya yi yamma sai ya diras, x^2
: Harka da ilmi mu kai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya.

Jagora : Mu yawon aminci mu kai, x^2
'Y/Amshi : In ya hito dag gabas,
: Ya yi yamma sai ya diras. x^2

Jagora : Tun dak Kaduna har Zariya,
: Had da manyan Kano,
'Y/Amshi : Komi mutum za shi yi,
: Ya gama da 'yan Sakkwato,
: Harka da ilmi mu kai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya.

Jagora : Lalle dak Kaduna har Zariya, x^3
: Had da manyan Kano,
'Y/Amshi : Komi mutum za shi yi,
: Ya gama da 'yan Sakkwato. x^3

Jagora : In noma mutum za shi yi, x^2
'Y/Amshi : Kuma in hwatauci ya kai,
: Ya gama da ban-gaskiya,
: Harka da ilmi mu kai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya. x^2

Jagora : To, mu tun da ga shigihhu,
'Y/Amshi : Ga xakuna an shirya,
: Ni ba ni kwana wuri.

Jagora : Lalle tun da ga shigihhu, x2
‘Y/Amshi : Ga xakuna an shirya,
: Ni ba ni kwana wuri, x2
: Harka da ilmi mu kai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya.

Jagora : To, ashe zaman duniya, x3
‘Y/Amshi : Kowa na shi aiki shi kai,
: Abin da wani ba shi so,
: Wani na bixa tai kwarai,
: Harka da ilmi mu kai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya. x3

Jagora : In dai mutum yav vace, x2
: Maisai ga hanya mu kai,
‘Y/Amshi : In ko mutum ya qiya,
: Mu iza shi bayan gida,
: Harka da ilmi mu kai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya. x2

Jagora : Harka da ilmi mu kai, x2
: Allah ya gyara mana,
‘Y/Amshi : Mu gama da ban-gaskiya. x2

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Tashar Motar Garin Sabon Birni,

Alhaji Idi xan Argiji[51],

34. *Gindin Waqa : Ya kwan yana aikin mota,*
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure.

Jagora : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure,
'Y/Amshi : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure.

Jagora : Ga wani can yana satar hanya, x^2
: Sarkin tasha ya kam mai,
: Komi za shi yi hwadamar kanwa,
: Dangi suna kallo nai,
'Y/Amshi : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure. x^2

Jagora : Lalle sarkin tashar Sabon Birni, x^2
: Harkat ta nai min daxi,
: Kullum ni ishe shi wurin mota,
: Sai ya shirya min kuxxi,
'Y/Amshi : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure. x^2
Jagora : Ko mai Basukur ko mai Hwanda,
: Ko mai hayat 'yat qwama,
: To, duw wanda ba lasin,

---

51 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{54}$ $^1/_5$.

: ‘Yan Sanda na daka mai kashi,
‘Y/Amshi : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure.

Jagora : Ko mai Basukur ko mai mota, x^2
: Ko mai hayat ‘yat qwama,
: To, duw wanda ba lasin,
: ‘Yan Sanda na daka mai kashi,
‘Y/Amshi : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure. x^2

Jagora : Gogan Ila gogarman Mamman, x^2
: Zaki magajin mani,
: To, Allah ya sa ma albarkar,
: Sarkin fulanin Shawai,
‘Y/Amshi : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure. x^2

Jagora : To, na zo tashar ‘yan Jakkai,
: Ban ga ana shirin komi ba,
: Sai niy yo tasha wajjen mota,
: Can nig ga dalar kaya,
‘Y/Amshi : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure.

Jagora : To, na zo tashar ‘yan Jakkai,
: Ban ga ana shirin komi ba,
: Sai niy yo tasha wajjen mota,
: Can nig ga dalar kaya.

Jagora : To, na zo tashar raqumma,
: Ban ga ana shirin komi ba,
: Sai niy yo tasha wajjen mota,
: Can nig ga dalar kaya,
‘Y/Amshi : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure.

Jagora : Ga ni ina shirin tahiya Zazzau, x^2
: Kuma ga ni ba ‘yan kuxxi,
: Ina nuhin tahiya Zazzau,
: Kuma ga ni ba ‘yan kuxxi,
: Ina dibin mota ni ko suna kallo na,
: ‘Yan kamishon suna dibin mota,
: Ni ko suna kallo na,
: Don sun gane ni da taron,
: Yara zay yawa baya na,
: Har an yi jinga na tada,
: Ban zan biyan kuxxi ba,
‘Y/Amshi : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure. x^2

Jagora : To, sarkin tasha don albarkar, x^2
: Manyan mutanen hwarko,
: Bari son shiga harkar yaro,
: In ya yi ba daidai ba,
‘Y/Amshi : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure. x^2

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Rambaxawa,
Mai Waqa : Xan Sarkin Hillani,

Alhaji Muhammadu Dikko Xanmaliki[52]*,*

35. *Gindin Waqa : Alhaji xan sarkin hillani,*
: Masu abin baiwa xan yashi.

Jagora : Alhaji xan sarkin hillani, x^2
: Masu abin baiwa xan yashi,
'Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : Ni Alhaji azama tai gado na, x^2
: Sai wajjen sarkin hillani,
: Sai wajjen mamomin Gobir,
'Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : Kowaz zaka Sabon Birnin Gobir, x^2
: Ya zaka garka tai ran narba,
: Ya ga abin kuxxi ya samu,
'Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : Bisimilla maganar malammai, x^2
: Walijam maganar hillani,
: Tarakkumas sai 'yan buzaye,
'Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : In ka ishe gulbi na tozaye, x^2
'Y/Amshi : Alhaji bayan kai ash shaqe. x^2

Jagora : In dai bari ba ta samo qari ba, x^2
: Ya ishe gulbi ya lalace,
'Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : Ai zuwa Kano ba banza ne ba, x^2
: Kun sha daxi kun sha qura,
: Da ku da kwana sai kun sauka,

---

52 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{144}$ $^1/_7$.

‘Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : Ai zuwa Kano ba banza ne ba, x^2
: Kun sha daxi kun sha qura,
: Da ku da kwana sai ran narba,
‘Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : Mada Nanu da ya aje kuxxi,
‘Y/Amshi : Ya yi hayaqi kuma ya yi bisashe,
: Bai yi zaton wani ha’inci ba.

Jagora : Mada Kura da ya aje kuxxi,
‘Y/Amshi : Ya yi hayaqi kuma ya yi bisashe,
: Bai yi zaton wani ha’inci ba.

Jagora : Ko Samagi da ya aje kuxxi,
‘Y/Amshi : Ya yi hayaqi kuma ya yi bisashe,
: Bai yi zaton wani ha’inci ba.

Jagora : Qohin nan ba su san tsahi ba, x^2
: Kuma babu ma mai kai gumba,
: Abin su duk baiwar Allah ne,
‘Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : Da masu qin ku da mai vacinku, x^2
: Mutum dai bai yi kamar Allah ba,
: Mai sama shi as sarkin jinqai,
‘Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : Alhaji gadon qarhe nir roqa, x^2
‘Y/Amshi : Ga ya ga hannu ya shirya min. x^2

Jagora : Ya ban katihwa ya ban bargo, x^2
: Had da matashi ya shirya min,
: Alhaji lallai ya kyauta min,
‘Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : Ni tun da gadon kwana ya samu, x^2
‘Y/Amshi : Ban iya noma sai hutawa,
: Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : Kowaz zaka Sabon Birnin Gobir, x^2
: Ya zaka garka tai ran narba,
: Ya ga abin kuxxi ya taru,
‘Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : Ni Alhaji azama tai gado na, x^2
: Sai wajjen sarkin hillani,
: Sai wajjen mamomin Gobir,
‘Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,

Mai Waqa : Sarkin Maraxi Xangara[53]*,*
Alhaji Bala xan Sani,

36. *Gindin Waqa : Xangara jikan xan lahiya,*
: Bala xan Sani gaisai mu kai.

Jagora : Da ni da xiya na murna mu kai, x^3
'Y/Amshi : Mu kwana Maraxi gidan Xangara,
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai. x^3

Jagora : Na Mamman Cana, x^2
'Y/Amshi : Na Mamman Jatau abin xan Sani ya kai ciki. x^2

Jagora : Maraxi akwai kuxxi, x^2
'Y/Amshi : Ai buhuhuwan kuxxi,
: Wasu has sun ruve.
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai. x^2

Jagora : Wanda ba shi da mota,
'Y/Amshi : In ya zaka,
: Bala xan Sani sai mai ya kai.
Jagora : Wanda ba shi da Hwanda,
'Y/Amshi : In ya zaka,
: Bala xan Sani sai mai ya kai.
Jagora : Wanda ba shi da doki,
'Y/Amshi : In ya zaka,
: Bala xan Sani sai mai ya kai.
Jagora : Wanda ba shi da shadda,
'Y/Amshi : In ya zaka,
: Bala xan Sani sai mai ya kai,
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai.
Jagora : Jikan Musa,
'Y/Amshi : Jikan saraki,

---

53 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{144}$ $^1/_5$ - AL $^1/_{146}$ $^1/_6$.

: Kun zama qusoshin duniya.
Jagora : In an bixi qusoshin duniya,
'Y/Amshi : Ina wani bayan kai Xangara?
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai.

Jagora : Tun dab bisa Azbin, x^2
'Y/Amshi : Hab bisa Kano,
: Uban kowa ya san Xangara. x^2
Jagora : Da Tawa da Tasawa, x^2
'Y/Amshi : Had Damagaran,
: Kowa ya san Xangara. x^2

Jagora : Da Buza da Madawa,
'Y/Amshi : Had da mu da as Sabon Birni mun sani.
Jagora : Xangara kai as sinadari,
'Y/Amshi : Ko da xai abin kallo,
: Kallo nai a kai,
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai.

Jagora : Xangara kai am muzakkari,
'Y/Amshi : Ko da xai abin kallo,
: Kallonai a kai,
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai.

Jagora : Tun da Allah yay yi ni, x^2
'Y/Amshi : Hay yanzu ban ga,
: Kyakyandi ba gidan duniya. x^2
Jagora : Mutane ku zo ku gani, x^2
'Y/Amshi : Ku ga abin da,
: Xan Sani yash shiryo mana. x^2
Jagora : Da riga goma, x^2
'Y/Amshi : Da riga uku,
: Bala xan Sani yay yo mana. x^2

Jagora : Na Alhajiya Gwamma,
'Y/Amshi : Wanga zamani,
: Ku am manyan duniya.

Jagora : Qanin Hajiya Gwamma,
‘Y/Amshi : Wanga zamani,
: Ku am manyan duniya.
Jagora : Shi na iya ba da wa,
‘Y/Amshi : Ko da yaushe ‘yan amsa,
: Amsa xai su kai,
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai.

Jagora : Shi na iya ba da wa, x^2
‘Y/Amshi : Ko da yaushe ‘yan amsa,
: Amsa xai su kai. x^2
Jagora : Ga riguna yab bai, x^2
‘Y/Amshi : Ga naira xari biyat,
: Xan Sani yak kai mana,
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai. x^2

Jagora : Tun da Allah as sarki, x^2
‘Y/Amshi : Yanzu ko,
: Bala xan Sani ag girgije. x^2
Jagora : Ina iya in gane, x^2
‘Y/Amshi : Yanzu ba kamar,
: Xan Sani sai ya wuce,
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai. x^2

Jagora : Jikan Musa jikan, x^2
‘Y/Amshi : Jikan Saraki,
: Kun zama qusoshin duniya. x^2
Jagora : In an bixi qusoshin duniya, x^2
‘Y/Amshi : Ina wani bayan kai Xangara?
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai. x^2

Jagora : Qanin Hajiya Gwamma,
‘Y/Amshi : Wanga zamani,
: Ku am manyan duniya.
Jagora : Maraxi akwai kuxxi, x^2

‘Y/Amshi : Ai buhuhuwan kuxxi,
: Wasu has sun ruve.
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai. x^2

Jagora : Wanda ba shi da Hwanda,
‘Y/Amshi : In ya zaka,
: Bala xan Sani sai mai ya kai.
Jagora : Wanda ba shi da doki,
‘Y/Amshi : In ya zaka,
: Bala xan Sani sai mai ya kai.
Jagora : Wanda ba shi da shadda,
‘Y/Amshi : In ya zaka,
: Bala xan Sani sai mai ya kai,
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai.

Jagora : Da mu makaxan garka, x^2
‘Y/Amshi : Had da mu makaxan noma,
: Sun san Dangara. x^2

Jagora : Jikan Musa jikan, x^2
‘Y/Amshi : Jikan Saraki,
: Kun zama qusoshin duniya. x^2

Jagora : Ina iya in gane, x^2
‘Y/Amshi : Yanzu ba kamar xan Sani sai ya wuce. x^2
Jagora : Tun da Allah as sarki, x^2
‘Y/Amshi : Yanzu ko Bala xan Sani ag girgije,
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai. x^2

Jagora : Maraxi akwai kuxxi, x^2
‘Y/Amshi : Ba ka yin irin wada xan Sani,
: Yas shirya. x^2

Jagora : Ko ka hi Bala kuxxi, x^2
‘Y/Amshi : Ba ka yin irin wada xan Sani,
: Yas shirya,
: Xangara jikan xan lahiya,

: Bala xan Sani gaisai mu kai. x^2

Jagora : Da ni da xiya na murna mu kai, x^2
'Y/Amshi : Mu kwana Maraxi gidan Xangara,
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Jam'iyyar N. P. N.[54]

[54] An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{147}$ $^1/_1$.

37. *Gindin Waqa : Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi,*
: Gwamnati N. P. N. mai biyak ku ba shi da haushi.

Jagora : Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi, x^2
'Y/Amshi : Gwamnati N. P. N mai biyak ku ba shi da haushi. x^2

Jagora : Ga masara ga gero to, kuma ga shinkahwa, x^2
'Y/Amshi : Gwamnati ta shirya babu mai rigan mu da daxi,
: Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi,
: Gwamnati N. P. N mai biyak ku ba shi da haushi. x^2

Jagora : Gwamnati ta ba mu ruwa, x^2
: To, har yanzu da saura,
: Tai mana lantarki don garinmu yai mana haske,
'Y/Amshi : Gwamnati ta shirya babu mai rigan mu da daxi,
: Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi,
: Gwamnati N. P. N mai biyak ku ba shi da haushi. x^2

Jagora : Ga masara ga gero to, kuma ga shinkahwa, x^2
'Y/Amshi : Gwamnati ta shirya babu mai rigan mu da daxi. x^2

Jagora : To, Shehu Kangiwa, x^2
'Y/Amshi : Wada kash shirya mana ta yi,
: Abin da yas shirya,
: Ba kamar shirin maqiya ba,
: Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi,
: Gwamnati N. P. N mai biyak ku ba shi da haushi. x^2

Jagora : To, na ga jam'iyyar su wane sun shirya mana qarya, x^2
'Y/Amshi : Tun da qarya ta shugabanmu ba shi da qarya,
: Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi,
: Gwamnati N. P. N mai biyak ku ba shi da haushi. x^2

Jagora : Sun ce sui mana gulbin hura su sa mana gulbi,
'Y/Amshi : Bayan nuhwar Allah babu mai hana mana noma.

Jagora : Bayan nuhwar Allah, x^3
'Y/Amshi : Babu mai hana mana noma. x^3

Jagora : Sun ce sui mana gulbin hura su sa mana gulbi, x^2

‘Y/Amshi : Bayan nuhwar Allah babu mai hana mana noma,
: Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi,
: Gwamnati N. P. N mai biyak ku ba shi da haushi. x^2

Jagora : Shehu Kangiwa,
‘Y/Amshi : Wada kash shirya mana ta yi,
: Abin da yas shirya,
: Ba kamar shirin maqiya ba,
: Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi,
: Gwamnati N. P. N mai biyak ku ba shi da haushi.

Jagora : To, Shehu Kangiwa, x^2
‘Y/Amshi : Wada kash shirya mana ta yi,
: Abin da yas shirya,
: Ba kamar shirin maqiya ba,
: Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi,
: Gwamnati N. P. N mai biyak ku ba shi da haushi. x^2

Jagora : To, na ga jam’iyyar su wane sun shirya mana qarya, x^2
‘Y/Amshi : Tun da qarya ta shugabanmu ba shi da qarya,
: Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi,
: Gwamnati N. P. N mai biyak ku ba shi da haushi. x^2

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ibrahim (1970-1975)[55],

38. *Gindin Waqa : Uban Zagi na Muhamman mai Sabon Birni,*

---

55 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{147}$ $^1/_{11}$.

: Iro ya cika zakka yau ya zama sarki.

Jagora : Zauna da shiri baban yari mai Alqalawa, x^2
‘Y/Amshi : Na bawa ya shira du wanda kakanai yay yi. x^2

Jagora : Zauna da shiri baban yari mai Alqalawa,
‘Y/Amshi : Na bawa ya shira du wanda kakanai yay yi.
: Uban Zagi na Muhamman mai Sabon Birni,
: Iro ya cika zakka yau ya zama sarki.

Jagora : Mainasara ne ko ko Kada ne yad dawo, x^2
‘Y/Amshi : Yau Ibrahim ya gaji rumhwaj Jangwarzo,
: Ga yanzu ba ka da ratsin da ba xan Shawai ba,
: Uban Zagi na Muhamman mai Sabon Birni,
: Iro ya cika zakka yau ya zama sarki. x^2

Jagora : Balarabe xan Yari, x^2
‘Y/Amshi : Kai a Hassan da Hussaini,
: Ga yanzu kai muka dibi,
: Ba wani bayan kai. x^2

Jagora : Ga shinfixan mai nasara, x^2
‘Y/Amshi : Na Janjona ya hau,
: Ga ni na zaka murna da gangar Xantsara. x^2

Jagora : To, na taho al’adak kixin Sabon Sarki,
‘Y/Amshi : Had da ni makaxin na Garba yau na zama sabo,
: Uban Zagi na Muhamman mai Sabon Birni,
: Iro ya cika zakka yau ya zama sarki.

Jagora : Masu bixak kuxxi kui ta tahiyan neman kuxxi, x^2
‘Y/Amshi : Masu aiki ku yi anniyya gyara gona,
: Ga zamanin Ibrahim ba a zaman banza,
: Uban Zagi na Muhamman mai Sabon Birni,
: Iro ya cika zakka yau ya zama sarki. x^2

Jagora : Balarabe xan Yari, x^2
‘Y/Amshi : Kai a Hassan da Hussaini,

: Ga yanzu kai muka dibi,
: Ba wani bayan kai. x^2

Jagora : Na yi shekara biyu ban zo kixi ba gidan kowa,
'Y/Amshi : Anka ce Ibrahim na Dango as sarki,
: Marahwa kui mana tuqi mu ba tabshi kashi,
: Uban Zagi na Muhamman mai Sabon Birni,
: Iro ya cika zakka yau ya zama sarki.

Jagora : Sarkin ruwan Isa yana kaxi yay yi min komi, x^2
'Y/Amshi : Ya zuba mini shadda domin Jangwarzo. x^2

Jagora : Jekadan Waziri Ahmadu, x^2
'Y/Amshi : Yay taimako yay min komai,
: Ya zuba mini shadda domin Jangwarzo. x^2

Jagora : Zauna da shiri baban yari mai Alqalawa, x^2
'Y/Amshi : Na bawa ya shira du wanda kakanai yay yi.
: Uban Zagi na Muhamman mai Sabon Birni,
: Iro ya cika zakka yau ya zama sarki. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir,
Alhaji Umar xan Salihu (1957-1966)[56]*,*

39. *Gindin Waqa : Gwarzon Galadima ya ci arna,*
: Uban yari baban barga na bango.

---

56 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{147}$ $^1/_9$.

Jagora : Sarki na Jekada, x^2
'Y/Amshi : Ginshimin Ali,
: Ya mai da kura baban Marahwa,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^2

Jagora : Shi wanda yas saba yana ba ka, x^2
'Y/Amshi : In ka ga ya qyale ya qi ‘yamma,
: Ai sai ka tone shi ka san mahwari,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^2

Jagora : Baba tun ran da xan Inna yay yi sarki, x^2
'Y/Amshi : Gidajen mu mun huta mun ji daxi,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^2

Jagora : Zamaninka xan Inna mun yi sarki, x^2
'Y/Amshi : Mun sha hwuran nono mun ci kalwa,
: Mun hau dawakai mun yi zama,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^2

Jagora : Ran da ya rabke tamburran Yakubawa, x^2
'Y/Amshi : Ya xebe haushi baban uban Doma,
: Ya gade kayan Gohe na Tambari,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^2

Jagora : Kai dai tsare kayan nan na Kakanka,
'Y/Amshi : Shawai da yay mulkin Gobirawa,
: Ya mulke kowa balle qasatai,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango.

Jagora : Ummaru ya shige gida yay zama nai, x^2
'Y/Amshi : Dun masu ja mai da su banza,
: Ka san nuhwan Allah ta hi komi,

: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^2

Jagora : Ga kaya da xan Inna ya sawo min,
'Y/Amshi : Waxanda ba canji yas sawo min,
Jagora : Alkyabbu da xan Inna yas sawo min,
'Y/Amshi : Waxanda ba canji yas sawo min,
Jagora : Doki da xan Inna yas sawo min,
'Y/Amshi : Sai wanda ba canji yas sawo min,
Jagora : Riga da xan Inna yas sawo min,
'Y/Amshi : Sai wanda ba canji yas sawo min,
Jagora : Rawani da xan Inna yas sawo min,
'Y/Amshi : Sai wanda ba canji yas sawo min,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango.

Jagora : Komi nih hwaxi xan Ganjona ya ban, x^2
'Y/Amshi : Hay yanzu amma ban kai qawa ba,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^2

Jagora : Mai raba riguna xan Dango,
'Y/Amshi : Sarki mai dubun doki xan baraz zaki,
: Kai ad da dubun-dubbai na komi,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango.

Jagora : Iro je xan baraz zaki, x^3
‘Y/Amshi : Sanda xan Bawa xan Inna,
: Ja sha’anin Gobirawa,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^3

Jagora : Sai ran hawan salla niy yi kuka,
'Y/Amshi : Maidaminasa nir roqa wurin sanda,
: In ya buqata in kai qawa ta,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,

: Uban yari baban barga na bango.

Jagora : Kai mai yawan yawo ka yi banza, x^2
'Y/Amshi : Wandon ka ya kece ka yi wajje. x^2

Jagora : Ni ba ni son yawon nan na banza, x^2
'Y/Amshi : Haba wane xaure zauna wuri xai,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^2

Jagora : A gaishe ki balbela kin yi haske, x^2
'Y/Amshi : Kin zarce mai dauxa ya yi xauri,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^2

Jagora : Sarki na Jekada, x^2
'Y/Amshi : Ginshimin Ali,
: Ya mai da kura baban Marahwa,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ummaru xan Salihu (1957-1966)[57]*,*
Gindin Waqa : Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango.

Jagora : Iro je xan baraz zaki, x^3
'Y/Amshi : Sanda xan Bawa xan Inna,
: Ja sha'anin Gobirawa,

[57] An sami wannan rerawa a Littafin Xahiru, G. (1990: 107-110).

: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x3

Jagora : Sarki na Jekada, x2
'Y/Amshi : Ginshimin Ali,
: Ya mai da kura baban Marahwa,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x2

Jagora : Shi wanda yas saba ma yana baka, x2
'Y/Amshi : In ka ga ya qyale ya qi samma,
: Sai ka tona shi ka sam mahwari,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x2

Jagora : Tun ran da xan Inna yay yi sarki, x2
'Y/Amshi : Gidajenmu sun huta mun ji daxi,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x2

Jagora : Zamaninka xan Inna mun yi sarki, x2
'Y/Amshi : Mun sha huran nono mun ci kalwa,
: Mun hau dawakayye mun yi zama,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x2

Jagora : Ran da ya rabka tamburran Yakubawa, x2
'Y/Amshi : Ya xebe haushi baba Ubandoma,
: Ya gade kayan Gohe na Tambai,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x2

Jagora : Kai dai tsare kayan nan na Kakanka, x2
'Y/Amshi : Shawai da yai mulkin Gobirawa,
: Ya mulke kowa balle qasatai,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x2

Jagora : Umaru ya shige gina yay zama nai, x2

‘Y/Amshi : Dum masu ja ma da su banza,
: Ka san nuhwa Allah ta hi komi,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^2

Jagora : Ga kaya da xan Inna yas sawo min, x^2
‘Y/Amshi : waxanda ba canji yas sawo min. x^2
Jagora : Doki da xan Inna yas sawo min,
‘Y/Amshi : Sai wanda ba canji yas sawo min.
Jagora : Riga da xan Inna yas sawo min,
‘Y/Amshi : Sai wanda ba canji yas sawo min.
Jagora : Rawani da xan Inna yas sawo min,
‘Y/Amshi : Sai wanda ba canji yas sawo min.
Jagora : Komi nih hwaxi xan Janjoni ya ban,
‘Y/Amshi : Amma hay yanzu ban kai qahwa ba,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango.

Jagora : Sai ran hawan salla niy yi kuka,
‘Y/ Amshi : Maidamisa nir roqa wurin sanda,
: In ya buqata in kai qahwata,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni
Alhaji Ummaru xan Salihu (1957-1966)[58]*,*

40. *Gindin Waqa : Umaru ginshimin Ali ci hwansa,*
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Umaru ginshimin Ali ci hwansa, x^2
'Y/Amshi : Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi,
: Na Shekarau. x^2

---

58 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{147}$ $^1/_4$.

Jagora : Masu kallon sarki ku zo ga kada ya zo, x^2
'Y/Amshi : Ya yi kamab Baciri,
: Sanda yay martabas Shawai,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Ummaru sarki ka gode Allah da Manzo nai, x^2
'Y/Amshi : Baba uban Yari da gaskiya za ya cin arna,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Hankali na ya tashi xan Iro ba ya gida, x^2
'Y/Amshi : Ummaru ya zaka komi ga ciwo yana sauqi,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Zamanka Zariya xan Inna gagon Majidaxi, x^2
'Y/Amshi : Ka cika aiki daidai da daidai na Alqali,
: An yi hirwai ba a kai ga jikan Tazabga ba,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Sarkin musulmi,
'Y/Amshi : Yay yo jawabi ga yara nai,
: Ummaru jikan Sardauna ‘yan bagalan girma.
Jagora : Waziri shi ma,
'Y/Amshi : Yay yo jawabi ga yara nai,
: Ummaru jikan Sardauna yau bagalar girma.
Jagora : Malasa shi ma,
'Y/Amshi : Yay yo jawabi ga yara nai,
: Ummaru jikan Sardauna yau bagalar girma,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Bacirawa yau Sanda shi anka ba sarki,
'Y/Amshi : Haba maza ga roqon da Allah ya yi kullum.

Jagora : Yakubawa yau Sanda shi anka ba sarki,
'Y/Amshi : Haba maza ga roqon da Allah ya yi kullum.
Jagora : Hayatawa yau Sanda shi anka ba sarki,
'Y/Amshi : Haba maza ga roqon da Allah ya yi kullum,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Na ga sabkon bubuquwa ta tsaya wanka, x^2
'Y/Amshi : Ga mu mun tashi da swahe ham mun wuccikketa,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Ummaru na yi kwararenka an ce kana hwake, x^2
'Y/Amshi : Mun ka zo mun ishe Sanda jikan kilo ya hau,
: Sai mu zarce xan Inna an ce yana kalgo,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Dag Gangara sai Xankura zaki yake kwana, x^2
'Y/Amshi : Ko hwa sai Gamji xan Muhamman yake kwana,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Rambaxawa ku taho ku duqa wa baqona,
'Y/Amshi : Yau hwa baqo ni adda shi ba ni ba kowa,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Ummaru miqe da yawonka kai ni sani sarki,
'Y/Amshi : ‘Yan adawa sun zo su hwada ka ba dama,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Na ga kura da karen gida ba su yin daxi, x^2
'Y/Amshi : Marahwa ban gane abin da yas sa su gaba ba,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Hanqure da mutanenka xan Iro mai daga, x^2
'Y/Amshi : Ummaru kyawon babba ya daure da yara nai,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Abin da dun nir roqa ga jikan kilo ya ban,
'Y/Amshi : Ummaru jikan Alhajiya bai hana min ba,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Ummaru ga doki ukku ya bai masarta nai,
'Y/Amshi : Kuma da alkyabba had da koren Kano ya bai,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Ummaru ga kyankyandi da yab ba masarta nai,
'Y/Amshi : A xebe maki yac ce a buxe a ba kowa,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Ko da gani an san wanda yas samu san sarki,
'Y/Amshi : Mutum ya diba ga jikin mu ko ba hwaxa mai ba,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Ummaru na zagi ya gaji yaqi ga Kakanai,
'Y/Amshi : Da shi da kakana babu zangon da ba su kwan ba,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Kakanka ya ci Ganiyya,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana.
Jagora : Ya ci birnin ‘Yandoto,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana.
Jagora : Ya ci birnin Bardava,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana.

Jagora : Ya ci birnin Anganba,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Maza cikin tabki sun ka hwaxa suna voyo, x^2
'Y/Amshi : Duniya na ji dashe-dashenta na Alqali,
: Mu yi zaman Xantsara da jadi da Jari kuma,
: Mu yi zaman Salihu,
: Shi da xan Dada mai tabshi,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Abu ga Allah yake sai mu koma ga roqo nai, x^2
'Y/Amshi : Du inda kar roqi baqin mutum ya hanas sa ma,
: Mu zo gida mu yi roqo ga Allah ya ban sabo,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni
Alhaji Ummaru xan Salihu (1957-1966)[59]*,*
Gindin Waqa : Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Masu kallon sarki ku zo ga kada ya zo, x^2
'Y/Amshi : Ya yi kamab Baciri,
: Sanda yay martabas Shawai,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Ummaru sarki ka gode Allah da Manzo nai, x^2
'Y/Amshi : Baba uban Yari da gaskiya za ya cin arna,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,

59 An sami wannan rerawa a Littafin Xahiru, G. (1990: 107-110).

: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Hankali na ya tashi xan Iro ba ya gida, x^2
'Y/Amshi : Ummaru ya zaka komi ga ciwo yana sauqi,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Zamanka Zariya xan Inna gagon Majidaxi, x^2
'Y/Amshi : Ka cika aiki daidai da daidai na Alqali,
: An yi hirwai ba a kai ga jikan Tazabga ba,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Sarkin musulmi, x^2
'Y/Amshi : Yay yo jawabi ga yara nai,
: Ummaru jikan Sardauna ‘yan bagalan girma. x^2
Jagora : Waziri shi ma,
'Y/Amshi : Yay yo jawabi ga yara nai,
: Ummaru jikan Sardauna yau bagalar girma.
Jagora : Minista shi ma,
'Y/Amshi : Yay yo jawabi ga yara nai,
: Ummaru jikan Sardauna yau bagalar girma.

Jagora : Bacirawa yau Sanda shi anka ba sarki,
'Y/Amshi : Haba maza ga roqon da Allah ya yi kullum.
Jagora : Yakubawa yau Sanda shi anka ba sarki,
'Y/Amshi : Haba maza ga roqon da Allah ya yi kullum.
Jagora : Hayatawa yau Sanda shi anka ba sarki,
'Y/Amshi : Haba maza ga roqon da Allah ya yi kullum,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Na ga sabkon bubuquwa ta tsaya wanka, x^2
'Y/Amshi : Ga mu mun tashi da swahe ham mun wuccikketa,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Ummaru na yi kwararenka an ce kana tulki x^2
'Y/Amshi : Mun ka zo mun ishe Sanda jikan kilo ya hau,
: Sai mu zarce xan Inna an ce yana kalgo,

: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Dag Gangara sai Xankura zaki yake kwana, x^2
'Y/Amshi : Ko hwa sai Gamji xan Muhamman yake kwana,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2
Jagora : Rambaxawa ku taho ku duqa wa baqona,
'Y/Amshi : Yau hwa baqo ni adda shi ba ni ba kowa,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Abu ga Allah yake sai mu koma ga roqo nai, x^2
'Y/Amshi : Du inda kar roqi baqin mutum ya hanas sa ma,
: Mu zo gida mu yi roqo ga Allah ya ban sabo,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Audu xan Malam[60]*,*
41. *Gindin Waqa : Ya gade gidan gardaye,*
: Saraki uban xan Malam.

Jagora : Alhaji Audu na Alhaji Dawai, x^2
'Y/Amshi : Goga mai yi ma shanu hanya,
: Ya gade gidan gardaye,
: Saraki uban xan Malam. x^2

Jagora : Kai am Malam Masaki na Arzika, x^2
'Y/Amshi : Ko can ba shi aboki gunki,
: Ya gade gidan gardaye,
: Saraki uban xan Malam. x^2

Jagora : Ashe haka nan duniya tag gada,

---

60 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{147}$ $^1/_3$.

'Y/Amshi : In dai wanga gida ya kwanta,
: To, sai wanga gida ya tashi,
: Ya gade gidan gardaye,
: Saraki uban xan Malam.

Jagora : Ai ashe haka nan duniya tag gada,
'Y/Amshi : In dai wanga gida ya kwanta,
: To, sai wanga gida ya tashi,
: Ya gade gidan gardaye,
: Saraki uban xan Malam.

Jagora : Ai wada mun ka jiya tun hwarin, x^2
'Y/Amshi : Tun can dauri akwai tsohinmu,
: In ba mu da xan mandawa,
: In dai ga su gidan ‘yan Qirya,
: Mu ko ba mu da su duk xai na,
: Ya gade gidan gardaye,
: Saraki uban xan Malam. x^2

Jagora : Ku duka kau haka nan ‘yan qirya, x^2
'Y/Amshi : Taronku babbanku da yaro,
: Duk killan ga Habu yay yo ta,
: Ya gade gidan gardaye,
: Saraki uban xan Malam. x^2

Jagora : Na gaishe ku xiyan ‘yan Qirya, x^2
'Y/Amshi : Tun da ba ku haihi xiyan banza ba. x^2

Jagora : Alhaji ya gaishe ku xiyan ‘yan Qirya, x^2
'Y/Amshi : Don ba ku haihi xiyan banza ba,
: Ya gade gidan gardaye,
: Saraki uban xan Malam. x^2

Jagora : Alhaji Audu na Alhaji Dawai, x^2
'Y/Amshi : Goga mai yi ma shanu hanya,
: Ya gade gidan gardaye,
: Saraki uban xan Malam. x^2

Jagora : Kai am Malam Masaki na Arzika, x^2

'Y/Amshi : Ko can ba shi aboki gunki,
: Ya gade gidan gardaye,
: Saraki uban xan Malam. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ibrahim (1970-1975)

42. *Gindin Waqa : Kak ka xau reni*[61]*,*
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Durumbu Ibrahim xan sarki, x^3
'Y/Amshi : Kamakka ka ba ya riqon xan komi, x^3
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Uban Bunu uban baraz zaki, x^2
'Y/Amshi : Kai qwazo ka gade Sarkin Gobir Shawai. x^2

Jagora : An ce min ana ganin hadari, x^3
'Y/Amshi : Ni ban san da shi ba sai iska ya taso, x^3
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

---

61 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{147}$ $^1/_4$.

Jagora : Xan Ummaru xan Inna, x3
'Y/Amshi : Jikan Jari maganin tahiya sai gwamko, x3
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Zamanin akwai manya, x3
'Y/Amshi : Ai Kakanka bai yi kyamar Kakana ba, x3
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Can zamanin akwai Jadi, x3
'Y/Amshi : Jadi ko da yaushe ba ya gudun Xantsara, x3
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Jikokin Jari da Mainasara,
'Y/Amshi : Ku duk kak ku yada irin Xantsara,
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Durumbu Ibrahim xan sarki, x3
'Y/Amshi : Kamakka ka ba ya riqon xan komi, x3
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Uban Bunu uban baraz zaki, x2
'Y/Amshi : Kai qwazo ka gade Sarkin Gobir Shawai. x2

Jagora : Dango na gode, x2
'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi. x2
Jagora : Dango xan Galadima,
'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi.
Jagora : Salihu Marahwa na gode,
'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi.
Jagora : Mamman na gode,
'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi.
Jagora : Malam Garba na gode, x2
'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi. x2

Jagora : Malam Garba na gode,
'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi.

Jagora : Ga kaya da Garba yab ba da,
'Y/Amshi : Don albarkacin Durumbu magajin Shawai.
Jagora : Kaya da Garba yab ba da,
'Y/Amshi : Don albarkacin Durumbu magajin Shawai.
Jagora : Mamman na gode,
'Y/Amshi : Don albarkacin Durumbu magajin Shawai.
Jagora : Ga kaya da Garba yab ba da,
'Y/Amshi : Don albarkacin Durumbu magajin Shawai,
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ibrahim (1970-1975)[62]*,*
Gindin Waqa : Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Birnin Mako wane sai sha'awa, x^2
'Y/Amshi : An shiryad da hakimi Allah ya shiryo,
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai. x^2

Jagora : Durumbu Ibrahim xan sarki, x^2
'Y/Amshi : Kamakka ka ba ya riqon xan komi,
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai. x^2

Jagora : Uban Bala uban Mamman, x^2
'Y/Amshi : Allah dai ya ba ka albarkar Xangwamci. x^2
Jagora : Mamman na gode,
'Y/Amshi : Don albarkacin Durumbu magajin Shawai.
Jagora : Mamman na gode,

---

62 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{11}$.

'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi.
Jagora : Ga kaya wanda yab ba da, x^2
'Y/Amshi : Don albarkacin Durumbu magajin Shawai. x^2
Jagora : Dango na gode,
'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi.
Jagora : Dango xan Galadima,
'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi.
Jagora : Salihu Marahwa na gode,
'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi.
Jagora : Garba na gode,
'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi.
Jagora : Malam Garba na gode,
'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi.
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.
Jagora : Ga kaya wanda yab ba da,
'Y/Amshi : Don albarkacin Durumbu magajin Shawai,
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Zamanin akwai manya ko,
'Y/Amshi : Tsuntsu da yaushe ba ya gudun Xantsara.
Jagora : Zamanin akwai Jadi,
'Y/Amshi : Jadi ko da yaushe ba ya gudun Xantsara,
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Zamanin akwai manya,
'Y/Amshi : Ai Kakanku bai yi kyamar Kaka na ba,
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Zamanin akwai Jadi,
'Y/Amshi : Jadi ko da yaushe ba ya gudun Xantsara,
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Jikokin Jari da Mainasara,
'Y/Amshi : Ko Daita ku zo ku yada irin Xantsara,

: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Uban Bala uban Mamman,
'Y/Amshi : Kai qwazo ka gane shin kirkin Xangwamci,
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gandu, Alhaji Suntau[63]*,*
43. *Gindin Waqa : Sarkin Gandu ubangijin gutsun gawo,*
: Iro mijin A'i gandu mai xakin Kande.

Jagora : Gandu mijin A'i goriba tai mai taho, x^2
'Y/Amshi : Allah yai ma ruwan itace ga danni,
: Sarkin Gandu ubangijin gutsun gawo,
: Iro mijin A'i gandu mai xakin Kande. x^2

Jagora : Garin Bature can za ni in ga al'adar Tsintau,
'Y/Amshi : Galadima mun yi gahwara ya ce in zo,
: Sarkin Gandu ubangijin gutsun gawo,
: Iro mijin A'i gandu mai xakin Kande.

Jagora : Kai ina can wajjenmu nij ji labarin Tsintau, x^2
'Y/Amshi : Mijin Tunikai nis sani kana xaukar kwaxi,
: Sarkin Gandu ubangijin gutsun gawo,
: Iro mijin A'i gandu mai xakin Kande. x^2

63 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{143}$ $^1/_9$.

Jagora : Garin Bature can za ni in ga al'adar Tsintau,
'Y/Amshi : Galadima mun yi gahwara ya ce in zo,
: Sarkin Gandu ubangijin gutsun gawo,
: Iro mijin A'i gandu mai xakin Kande.

Jagora : Gandu mijin A'i goriba tai mai taho, x^2
'Y/Amshi : Allah yai ma ruwan itace ga danni,
: Sarkin Gandu ubangijin gutsun gawo,
: Iro mijin A'i gandu mai xakin Kande. x^2

Jagora : Bara na iske masassaqa suna xibar hwaru,
: Su ko su ukku ne suna cajin hwaru,
: Guda sai yac ce tsaya gabas ka yi saurare,
: Guda kuma yac ce tsaya arewa ka yi saurare,
: Guda kuma yac ce tsaya gabas ka yi saurare,
: Tun ba su gama gardama ba ko sai ga Tsintau,
'Y/Amshi : Su duka sun shirya shawara don su vace mai
: Yac ce duw wanda yag gusa kau zai harbai,
: Sarkin Gandu ubangijin gutsun gawo,
: Iro mijin A'i gandu mai xakin Kande. x^2

Jagora : To, hwaxa ma makiyaya su sha zuwa dajin Tsintau, x^2
'Y/Amshi : In Tsintau ya ishe su ba ni zuwa ceto, x^2

Jagora : Alhajin Allah ga ni za ni roqon Alhazzai, x^2
'Y/Amshi : Saboda muqaminsu za mu bi mu yi amhwani,
: Sarkin Gandu ubangijin gutsun gawo,
: Iro mijin A'i gandu mai xakin Kande. x^2

Jagora : To, kun yi xawafi Alhaji kun yo Saffa da Marwa, x^2
'Y/Amshi : Dan nan aikin ku ya wuce dutsen Arfa,
: Sarkin Gandu ubangijin gutsun gawo,
: Iro mijin A'i gandu mai xakin Kande. x^2

Jagora : Gandu mijin A'i goriba tai mai taho, x^2
'Y/Amshi : Allah yai ma ruwan itace ga danni,

: Sarkin Gandu ubangijin gutsun gawo,
: Iro mijin A'i gandu mai xakin Kande. x²

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Sabo Shibkau xan Makau[64]*,*

44. *Gindin Waqa : Hali nai girma,*
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa.

Jagora : Ije inda shanu gaba, x²
'Y/Amshi : Ga wasu can su tahe,
: Ga wasu sun tashi,
: Sun hau kadarko lahiya,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa. x²

Jagora : Ije inda shanu gaba, x²
'Y/Amshi : Ga wasu can su tahe,
: Ga wasu sun tashi,
: Sun hau kadarko lahiya.
Jagora : To, akwai wasu na nan gida, x²
'Y/Amshi : Qara tardawa a kai,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa. x²

---

64 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{1}$.

Jagora : Kuxi xan Makau, x^2
'Y/Amshi : Kuxin isgilishi yai yawa. x^2
Jagora : Akwai kuxi gidan xan Makau, x^2
'Y/Amshi : Mazaje da mataye duka. x^2

Jagora : Akwai sule akwai sisi, x^2
'Y/Amshi : Akwai jilai kuma,
: Da cinko xan Masar,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa. x^2
Jagora : Alhaji Sabon Shibkau, x^2
'Y/Amshi : Mijin Laddi manyan danqumai. x^2
Jagora : Ashe zuma kake, x^2
'Y/Amshi : Banga mai lashe dauxar hannuwa. x^2
Jagora : In ko ka qiya,
'Y/Amshi : Magabci ya hi ka datsi a saurara maka,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa.

Jagora : Attajirin da ba shi da rana,
'Y/Amshi : Ina ruwan mu da gaishe shi,
: Ko ya yi manyan jikkuna,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa.

Jagora : Na gano wani attajiri da yaro da kwando,
'Y/Amshi : Kaico! Shin wanga irin yaro,
: Ya zo wurin shin arkane,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan mai daqquwa.

Jagora : Na gano wani attajiri da jallinsa ukku,
'Y/Amshi : Ga guda ya ci tururruvi gudan yai sagan,
: Gudan had da zaki ya kashe,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,

: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa.

Jagora : Kan ka shi zo baba ban xauka tai,
'Y/Amshi : Zamani harara ta ya kai,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa. x^2

Jagora : Wane kana hushi da ni,
'Y/Amshi : Ba ni nih hana ka cin riba ba,
: Yi kuka da Allah wahidun,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa.

Jagora : Alhaji jikka dubu ka zo mai ba dum,
: Ga wasu jikka dubu suna dawowa,
'Y/Amshi : Akwai wasu jikka dubu suna nan rumbu,
: Can an kai su banki an aje,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa.

Jagora : Mai gida da siminti,
'Y/Amshi : Na malka mai kuraye,
: Halo an ka shahwa can gabas,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa.

Jagora : Inyamirin da yai maka gugag gidan ga,
'Y/Amshi : Ya zama ma'in ko ko hakimi na yab buga,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa.

Jagora : Ashe zuma kake, x^2
'Y/Amshi : Banga na lashe dauxah hannuw,

: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ummaru xan Salihu (1957-1966)[65],

45. *Gindin Waqa : Ina anniyan ishe mai,*
: Ummaru jikan mayaqi kai nib biyo.

Jagora : Giwa za ta haihwa toro, x^2
'Y/Amshi : Nan ga na Garba am matakin 'yan'uwa,
: Ina anniyan ishe mai,
: Ummaru jikan mayaqi kai nib biyo. x^2

Jagora : Garin Bature za ni da kwana, x^2
'Y/Amshi : Ummaru ko don saboda kai nit taho. x^2

Jagora : In dai na zaka gidansu Ummaru, x^2
'Y/Amshi : Ba ni da haushi saboda na zo gida,
: Ina anniyan ishe mai,
: Ummaru jikan mayaqi kai nib biyo. x^2

Jagora : Ga hwata za ni yo ma Tsintau,
'Y/Amshi : Tsintau Allah ya sa ka yaxu,
: Ka yaxu kamad dankali kamar 'yanduma,
: Ina anniyan ishe mai,
: Ummaru jikan mayaqi kai nib biyo.

Jagora : Ga hwata za ni yo ma Tsintau,
'Y/Amshi : Tsintau Allah ya sa ka yaxu,

---

65 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{147}$ $^1/_6$.

: Ka yaxu kamad dankali kamar ‘yanduma.

Jagora : Inda Allah na barin mutane, x^2
'Y/Amshi : Da sai ya bar mu da ni da Tsintau,
: Ya zo ya zauna da ni sahe dut,
: Ina anniyan ishe mai,
: Ummaru jikan mayaqi kai nib biyo. x^2

Jagora : Xan Idi xan Bakwai da Delu, x^2
'Y/Amshi : Ummaru xan Jimma gangararren maza. x^2
Jagora : Xan Lairo in kwana riqo na,
'Y/Amshi : Ka nuna dokin da za ni zama gida,
: Ina anniyan ishe mai,
: Ummaru jikan mayaqi kai nib biyo. x^2

Jagora : Garin Bature za ni da kwana, x^2
'Y/Amshi : Ummaru ko don saboda kai nit taho. x^2

Jagora : In dai na zaka gidansu Ummaru, x^2
'Y/Amshi : Ba ni da haushi saboda na zo gida,
: Ina anniyan ishe mai,
: Ummaru jikan mayaqi kai nib biyo. x^2

Jagora : Giwa za ta haihwa toro, x^2
'Y/Amshi : Nan ga na Garba am matakin ‘yan’uwa,
: Ina anniyan ishe mai,
: Ummaru jikan mayaqi kai nib biyo. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Xansanda na Gangara[66]*,*
46. *Gindin Waqa : Na taho gaida babba gardaye,*
: Baba xan Inna mai gandun daji.

Jagora : A gaishe ka babba na babba xan Bawa, x^2
'Y/Amshi : Abin da Allah ka hwasau na daji,
: Na taho gaida babba gardaye,
: Babba xan Inna mai gandun daji. x^2

Jagora : A gaishe ka babba na babba xan Bawa,
'Y/Amshi : Abin da Allah ka hwasau na daji.

Jagora : Alhaji Xansanda mai dogon yaro, x^2
'Y/Amshi : Na ta kai-wa-da-kawo sun tohwa,
: Na taho gaida babba gardaye,
: Babba xan Inna mai gandun daji. x^2

Jagora : Na ishe tsamiya ta yi kyaun kunne,
'Y/Amshi : Ga makiyaya da ko gittocinsu,
: Ga tumakinsu mai takin oda,
: Babu damar a sara sai dibi,
: Na taho gaida babba gardaye,
: Babba xan Inna mai gandun daji.

Jagora : Na ishe tsamiya ta yi kyaun kunne,
'Y/Amshi : Ga makiyaya da ko gittocinsu,
: Ga tumakinsu mai takin oda,
: Babu damar a sara sai dibi.

---

66 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{143}$ $^1/_7$ - AL $^1/_{147}$ $^1/_7$.

Jagora : Ina manoma ga ‘yan takin oda,
'Y/Amshi : Wanda ya iske gawo yas sare,
: Ya yi kashi da kai nai ya tasa,
: Na taho gaida babba gardaye,
: Babba xan Inna mai gandun daji.
Jagora : Ina makiyayan ga sun sukar mulki,
'Y/Amshi : Wanda ya iske gawo yas sare,
: Ya yi kashi da kai nai ya tasa,
: Na taho gaida babba gardaye,
: Babba xan Inna mai gandun daji.

Jagora : Shin ina Lawwali shi da Zaqoli,
'Y/Amshi : Ku zo ku shaida wa babba gardaye,
: Na taho in yi mai kukan yunwa,
: Yau gidajenmu ba sauran tsaba,
: Na taho gaida babba gardaye,
: Babba xan Inna mai gandun daji.

Jagora : Ga takardu Galadima ya bai, x^2
'Y/Amshi : Gangara za ni in samo tsaba,
: Na taho gaida babba gardaye,
: Babba xan Inna mai gandun daji. x^2

Jagora : Alhaji Xansanda mai dogon yaro, x^2
'Y/Amshi : Na ta kai-wa-da-kawo sun tohwa,
: Na taho gaida babba gardaye,
: Babba xan Inna mai gandun daji. x^2

Jagora : A gaishe ka babba na babba xan Bawa, x^2
'Y/Amshi : Abin da Allah ka hwasau na daji,
: Na taho gaida babba gardaye,
: Babba xan Inna mai gandun daji. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Salihu (1945-1956),
47. *Gindin Waqa : Iro na Bawa baqon dole*[67]*,*
: Jikan na Sanda baban Yari.

Jagora : Mai ban tsoro uban Galadima, x^2
: Sarkin gida jikan na Jekada,
: Mai raba kaya baqon dole,
'Y/Amshi : Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari. x^2

Jagora : Ga hwata na uban Galadima,
'Y/Amshi : Sarkin gida jikan na Jekada,
: Mai raba kaya baqon dole.

Jagora : Mai ban tsoro uban Galadima,
'Y/Amshi : Sarkin gida jikan na Jekada,
: Mai raba kaya baqon dole,
: Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari.

Jagora : Salihu xan Shekara na Dango, x^2
'Y/Amshi : Bai yadda ta haushi wandon Malam,
: Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari. x^2

---

67 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{50}$ $^1/_1$ - AL $^0/_{54}$ $^1/_1$.

Jagora : Ku dangana ‘ya’uwa ku bi sarki,
‘Y/Amshi : Ba banza ka yin sarki ba,
: Sai da rabo da cewar Allah.
Jagora : Ku hanqura ‘yan’uwa ku bi sarki,
‘Y/Amshi : Ba banza ka yin sarki ba,
: Sai da rabo da cewar Allah.
Jagora : Sarki ba ya kyamar kowa,
‘Y/Amshi : Ko ko sarki ba ya kyamar sarki,
: Sarki ba ya ce mai komi,
: Amma ya zura mai Allah,
: Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari.

Jagora : Mai horon maza uban Galadima, x^2
‘Y/Amshi : Iro na Bawa baban Doma,
: Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari. x^2

Jagora : Salihu xan Shekara na Dango, x^2
‘Y/Amshi : Bai yadda ta haushi wandon Malam,
: Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari. x^2

Jagora : Sarki za ya tarben D.O.,
‘Y/Amshi : Ni ko za ni kixaun na Baba,
: Ki xauke shi ki sauke shi lahiya don Allah.
Jagora : Sarki za ya tarben Gwamna,
‘Y/Amshi : Ni ko za ni kixaun na Baba
: Ki xauke shi ki sauke shi lahiya don Allah.

Jagora : Taron shawara na yaz zo,
‘Y/Amshi : Mun zo rakkiya mun dawo,
: An yo kixan manya ta sarki,
: Ban san inda zai kwana ba,
: Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari.

Jagora : Ni dai ban san inda zai kwana ba,
‘Y/Amshi : Gobir zai tsaya ko Durvi,
: Sarki bai tsaya dun nan ba,
: Amma ya wuce sai Wurno,

: Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari.
Jagora : In an koma yin wani taro,
‘Y/Amshi : Ko ni mai kixi sai na zo,
: Amma ban zuwa huntu na,
: Sai an koma ban wata riga,
: Sai an koma ban wani doki,
: Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari.

Jagora : Ai koma shiri Magajin Mani,
‘Y/Amshi : Kogin duniya ya tashi.
Jagora : Haba koma shiri Magajin Mani,
‘Y/Amshi : Kogin duniya ya tashi.
Jagora : Kai dai koma shiri Magajin Mani,
‘Y/Amshi : Kogin duniya ya tashi.
Jagora : Ko wacce akwai dole Gobir, x^2
‘Y/Amshi : Jagoran hwaxa ya tashi. x^2

Jagora : Jari da yai irin nashi ya yi,
‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Almu da yai irin nashi ya yi,
‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Gohe da yai irin nashi ya yi,
‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Maso xan Danga da yai irin nashi ya yi,
‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Ko Baciri da yai irin nashi ya yi,
‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Sobe da yai irin nashi ya yi,
‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Mayaqi da yai irin nashi ya yi,
‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Jangwarzo da yai irin nashi ya yi,
‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Xangwamci da yai irin nashi ya yi,
‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Xan mai Jadi da yai irin nashi ya yi,
‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Ko Jari Kada da yai irin nashi ya yi,

‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Ko Ummaru da yai irin nashi ya yi,
‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Kai ba ka jan wani sarki,
‘Y/Amshi : Tsoro ba ya jan wani kaxo.
Jagora : Salihu ba ya jan wani sarki,
‘Y/Amshi : Tsoro ba ya jan wani kaxo.

Jagora : Kai ka xauki ragamar musulmi,
‘Y/Amshi : Wannan ba a hana ka na Malam,
: Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari.

Jagora : Mai ban tsoro uban Galadima,
: Sarkin gida jikan na Jekada,
: Mai raba kaya baqon dole.

Jagora : Ga hwata na uban Galadima,
'Y/Amshi : Sarkin gida jikan na Jekada,
: Mai raba kaya baqon dole,
: Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari.

Jagora : Salihu xan Shekara na Dango, x^2
‘Y/Amshi : Bai yadda ta haushi wandon Malam,
: Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Jadi (1915-1916)[68]*,*

48. *Gindin Waqa : Da yaqi ya ci maza,*
: Uban Yari jikan Madauci .

Jagora : Maza raba gardama Jadi, x2
'Y/Amshi : Xan Babari gaishe ka,
: Allah wanda ya shiryo,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci . x2

Jagora : Sarki Labo, x2
'Y/Amshi : Baban Jekadiya zamaninka,
: Na Dango da qarhi ka zo,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci . x2

Jagora : Tsibiri Gobirawa hwarilla,
'Y/Amshi : Ka isko na goya qarhi da iko da qarhi,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci .

Jagora : Jikan Ali jikan Alhassan, x2
'Y/Amshi : Jikan Almu sarki waliyyi,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci . x2

Jagora : Gamji xan Magajin gari,
'Y/Amshi : Ba hwasawa na Jekadiya,
: mai shiga hwada da qarhi,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci .
Jagora : Duniya tsohuwar runhwa,

---

68 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$ - AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{1}$.

'Y/Amshi : Wada kag gani kak ka sake,
: Ka ce ka gyara da qarhi,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci .

Jagora : Alhaji talakka talban ka ne,
'Y/Amshi : Bari yai gadon ka ko can,
: Da hwari da qarhi,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci .

Jagora : Na yi nuhwar tahowa biki,
'Y/Amshi : Allah bai nuhe ni ba da zowa,
: Tun ban kai ba birni lalura,
: Ta Kam min da qarhi,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci .

Jagora : Buri nikai in zo Tsibiri, x^2
'Y/Amshi : Akwai cibiya ta na can. x^2
Jagora : In yo ziyarar kakana, x^2
'Y/Amshi : Da sarki na Gome,
: Mai tura wa da qarhi,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci . x^2

Jagora : Taron nan da kaz zo Yamai,
'Y/Amshi : ‘Yan Dozo suna Almu ya zo,
: Sun hwaxi gaskiya ba hilahwa,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci .

Jagora : Dogon Dutsi suna Almu ya zo,
'Y/Amshi : Sun hwaxi gaskiya ba hilahwa.
Jagora : Vannawa suna Almu ya zo,
'Y/Amshi : Sun hwaxi gaskiya ba hilahwa.
Jagora : Madawa suna Almu ya zo,
'Y/Amshi : Sun hwaxi gaskiya ba hilahwa.
Jagora : Gidan Rumji suna Almu ya zo,
'Y/Amshi : Sun hwaxi gaskiya ba hilahwa.

Jagora : Ibirawa suna Almu ya zo,
'Y/Amshi : Sun hwaxi gaskiya ba hilahwa.
Jagora : Mayanawa suna Almu ya zo,
'Y/Amshi : Sun hwaxi gaskiya ba hilahwa,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci .

Jagora : Kowag gan ka ya qare kallo,
'Y/Amshi : Sai ya taho gida ba ya koma kallo,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci .

Jagora : Jikan Ali jikan Alhassan, x^2
'Y/Amshi : Jikan Almu sarki waliyyi,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci . x^2

Jagora : Hitila tocilan babu batir, x^2
'Y/Amshi : Ba ta da martaba ta hanga,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci . x^2

Jagora : Xan sarkin da ba shi da saurauta,
: To, kuma ga ya nan kusa da suqi,
: Suqi ne macijin dabatai,
: Kuma ya daxe yana nan ga rana,
'Y/Amshi : Ya daxe tabbata ba ya kai,
: Kai nai hukunci da qarhi,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci .

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gobir na Sabon Birni,

Alhaji Balarabe (1902-1904)[69],

49. *Gindin Waqa : Xangara Dabo xan Kasau,*
: Sarkin yamma wan maza.

Jagora : In dai sarki Mayaqi ne,
: Ko Mamman na Dawwa,
'Y/Amshi : Mainasara na Almu,
: Ka zama zauri mijin gida.

Jagora : Lalle sarki Mayaqi ne, x^2
: Ko Mamman na Dawwa,
'Y/Amshi : Mainasara na Almu,
: Ka zama zauri mijin gida,
: Xangara Dabo xan Kasau,
: Sarki yamma wan maza. x^2

Jagora : Balarabe jikan Balarabe,
'Y/Amshi : Giwa ba ta zamkuwa. x^2

Jagora : Balarabe kai ak kada,
'Y/Amshi : Ka na hana ‘yan su zuwa ruwa,
: Xangara Dabo xan Kasau,
: Sarki yamma wan maza.

Jagora : Jinin sarkin sarakuna, x^2
'Y/Amshi : Dunku mai shirin qwarai. x^2

Jagora : Xan hurgi kasam nikai, x^2
'Y/Amshi : Kai az zaure mijin gida,
: Xangara Dabo xan Kasau,
: Sarki yamma wan maza. x^2

Jagora : Ashe hanya ta zo gida,
'Y/Amshi : Bara a ce ko qiris,
: Kakana da na ka,

---

69 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{376}$ $^1/_2$.

: Sun wuce dajin ga mai tsawo,
: Xangara Dabo xan Kasau,
: Sarki yamma wan maza.

Jagora : Ashe Mainasara da yay yi daga,
'Y/Amshi : Na maza shina ciki.
Jagora : Muhamman Jadi da yay yi daga,
'Y/Amshi : Na maza shina ciki.

Jagora : Sun hwasa Xanmagori,
'Y/Amshi : Sun hwasa Qaura da daddare,
: Xangara Dabo xan Kasau,
: Sarki yamma wan maza.

Jagora : Tun da ina ganin zuma,
'Y/Amshi : Ni ban hwasa kallo,
: Ba dama ga raguna,
: Ka san ba ni cin damo,
: Xangara Dabo xan Kasau,
: Sarki yamma wan maza.

Jagora : Ka yo min halin Sallau, x^2
'Y/Amshi : Ka sai mini doki ina hawa. x^2

Jagora : Sarki ya ba mu riguna,
'Y/Amshi : Sai niyyaz zuwa gida,
: Xangara Dabo xan Kasau,
: Sarki yamma wan maza.

Jagora : Jinin sarkin sarakuna, x^2
'Y/Amshi : Runhu mai shirin kwarai. x^2

Jagora : Uban sarkin dogari,
'Y/Amshi : Uban Gwandu ginshiqin zagi,
: Xangara Dabo xan Kasau,
: Sarki yamma wan maza.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,

Alhaji Salihu xan Ummaru (1945-1956)[70],

50. *Gindin Waqa : Toya matsahwa baqon dole,*
: Jikan Sanda baban Yari.

Jagora : Salihu xan Shekara na dango,
'Y/Amshi : Mai daxa haushi wan xan Malam,
: Toya matsahwa baqon dole,
: Jikan Sanda baban Yari.

Jagora : Mai horon maza uban mazaje,
'Y/Amshi : Qi hana tohwa baban Garba.
Jagora : Darzaje maza uban mazaje,
'Y/Amshi : Qi hana tohwa wan xan Garba,
: Toya matsahwa baqon dole,
: Jikan Sanda baban Yari.

Jagora : Giwa ba ta tsoron tarko,
'Y/Amshi : Giwa ba ta tsoron golo,
: Ta kwashe tarakkan yara,
: Toya matsahwa baqon dole,
: Jikan Sanda baban Yari.

Jagora : Yaro yay haqon tarko nai,
'Y/Amshi : Giwa ta biya ta kwashe,
: Toya matsahwa baqon dole,
: Jikan Sanda baban Yari.

Jagora : Ashe dai kyauta mai yawa sai Allah,
'Y/Amshi : Kyauta mai yawa sai sarki,
: In ya yarda ba tambaba,
: Toya matsahwa baqon dole,
: Jikan Sanda baban Yari.

Jagora : Sarki ya yi kyautau wando,
'Y/Amshi : Sarki ya yi kyautad doki,
: Ga sirdin Masar ya bayar,

---

70 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$ - AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{1}$.

: Jikka an ka ce ya xebe,
: Toya matsahwa baqon dole,
: Jikan Sanda baban Yari.

Jagora : Ku dangana ‘yan’uwa ku bi sarki,
'Y/Amshi : Ba banza ka yin sarki ba,
: Sai da rabo da cewar Allah,
: Toya matsahwa baqon dole,
: Jikan Sanda baban Yari.

Jagora : Sarki ba ya kyamak kowa,
'Y/Amshi : Kwacce ba ya qaunas sarki,
: Sarki ba ya ce mai komi,
: Amma ya aza mai Allah,
: Toya matsahwa baqon dole,
: Jikan Sanda baban Yari.

Jagora : An koma shiri na Ali na Gambai,
'Y/Amshi : Motsin duniya ya tashi.

Jagora : Sarki za shi tarben gwamna,
'Y/Amshi : Ke mota je ki xauki baba,
: Ki kai shi da lahiya don Allah.

Jagora : Taron shawara ne yaz zo,
'Y/Amshi : Mun yo rakkiya mun dawo,
: An yit tambaya ba sarki,
: Ban san inda zai kwana ba.

Jagora : Ni dai ban san inda zai kwana ba,
'Y/Amshi : Ko birnin Kabbi ko Dutse,
: Sarki bai tsaya dun nan ba,
: Amma ya wuce sai wurno.

Jagora : In an kuma yin wani taro,
: Ko ni mai kixi sai na zo,
: Amma ban zuwa huntu na,
'Y/Amshi : Sai an kuma ban wata riga,
: Sai an kuma ban wani doki,

: Toya matsahwa baqon dole,
: Jikan Sanda baban Yari.

Jagora : Kowac ce a gundumi Gobir,
'Y/Amshi : Da gurin hwaxa ya tashi.
Jagora : Babari da yay irin nashi ya yi,
'Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Mayaqi da yay irin nashi ya yi,
'Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Ali da yay irin nashi ya yi,
'Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Buba da yay irin nashi ya yi,
'Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Balarabe da yay irin nashi ya yi,
'Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba,
: Toya matsahwa baqon dole,
: Jikan Sanda baban Yari.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Bawa (1975 - 2003)[71],

[71] An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{1}/_{142}$ $^{1}/_{4}$.

51. *Gindin Waqa : Bawa na Jekadiya,*
: Na Dango mai saje.

Jagora : Sarki na Argiji na Magajin Gari,
'Y/Amshi : Mijin Maitakalmi,
: Na 'Yab Baraya ina gaishe ka,
: Don kanai man unhwani da gaskiya,
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje.

Jagora : Xankilo,
'Y/Amshi : Alhaji xan shekara Magajin Buhari,
: Wanda duk ka jiye ma,
: Ba ya koma albarka gobe ya walkamo,
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje.

Jagora : In dai ana dara,
'Y/Amshi : A yi qwazo a zam kashe mugun baki,
: Ko da wai ko da munahicci,
: Kissa ta xara su kashi daidai,
: Ku zam gani,
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje.

Jagora : Na ga ana son vacin tambari, x^2
'Y/Amshi : Ana shakkag ganga,
: Maza suna son su yi wasa da kai,
: Halinka suke tsoro uban qasa,
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje. x^2

Jagora : Ku masu aikin sarki, x^2
'Y/Amshi : Ku yi kula ku kama aiki daidai,
: Kada ku zo ku yi wauta,
: Ku yi abin da sarki bai ce ba,
: Ku bak qasag, x^2
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje.

Jagora : Ga wani ya yi gabas, x^2
‘Y/Amshi : Ko Bawa Xankilo ya hurgaxai,
: Yalla ko maganan nan wanda ya shira,
: Ta rinjayai ya baq qasa, x^2
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje.

Jagora : Duk wanda sarki yar runguma, x^2
‘Y/Amshi : Yana xebi ginda,
: Ya yi qiba ga xuwayya,
: Tun da hankalinsa yana kwance ya bag gado,
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje. x^2

Jagora : Ni tun da sarki ya rungume ni,
‘Y/Amshi : Ba ni zuwa gabce,
: Sai ya ba ni takardu,
: Kuma ya ba ni kaya tsadaddi mu ranqwaso,
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje.

Jagora : Sarki shi ba ni gida,
‘Y/Amshi : Kuma ya ban kuxin ginab burshi,
: Sai ya yo mana sanadin,
: Da za ni aure mai tsada,
: Mu kai gida,
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje.

Jagora : Giwa masha dahi, x^2
‘Y/Amshi : Baba uban Nari ya hwashe mugun taro,
: Uban Baraz Zaki uban Abdu,
: Kwangaren Dikkon Gande wuce maza, x^2
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje.

Jagora : Zuwanmu Sakkwato kwananmu takwas,

: Gidan Dikkon Gande, x^2
‘Y/Amshi : Ana ta ba mu abinci,
: Mun qoshi, mun hole birjik kamad duma.
Jagora : Sakkwato mun ci abinci iri-iri, x^2
‘Y/Amshi : Kala-kala, ham munka sake hwata,
: Jikinmu yak koma jawur kamaj jini. x^2

Jagora : Hanqurin hwari, x^2
‘Y/Amshi : Sai tofa, jimirin hwaxa sai mai sanda,
: Wanda ba ya da sanda,
: Sai ya yi hwaxa ya shammatai ya yo gida.

Jagora : Uban Galadima, x^2
‘Y/Amshi : Kai dai bixo tsuman geza gyare,
: Talakka jaki ne sai an bugai,
: Wurin kunne, zai gane gaskiya.

Jagora : Ga Balarabe ya dawo, x^2
‘Y/Amshi : Ba ka koma jin wani na hauka. x^2
Jagora : Jari Kada ya dawo, x^2
‘Y/Amshi : Ba ka koma jin wani na hauka. x^2
Jagora : Mainasara ya dawo,
‘Y/Amshi : Ba ka koma jin wani na hauka,
Jagora : Tun da Bawa Jangwarzo na, x^2
‘Y/Amshi : Ba ka koma jin wani na haukab bixaq qasa, x^2
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje.

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Muhammadu Sani na Ummu[72]*,*

52. *Gindin Waqa : In zo kixa inda Sani na Ummu,*
: Bai san iyaka ba in ya ga noma.

Jagora : A gaishe ka xan Yari Ubandawaki,
‘Y/Amshi : Samun kwatankwacinka sai an yi tawa,

---

72 An Sami Wannan Rerawa ne a Kundin Gusau (1983: 475-476).

: In zo kixi inda Sani na Ummu,
: Bai san iyaka ba in ya ga noma.

Jagora : Kai yaro bai san Sani na Umbu ba,
'Y/ Amshi : Bai san na kogo ba sai an yi sulu,
: In zo kixi inda Sani na Ummu,
: Bai san iyaka ba in ya ga noma.

Jagora : Kai na zo kixi inda Sani na Umbu,
'Y/ Amshi : Ban zo kixi inda raggon maza ba,
: Sai na Sulvau na Salmanu na Alhaji,
: In zo kixi inda Sani na Ummu,
: Bai san iyaka ba in ya ga noma.

Jagora : Kai na zo kixi inda Sani na Umbu,
'Y/ Amshi : Ban zo kixi inda raggon maza ba.

Jagora : Kai yaro bai san Sani na Umbu ba,
'Y/ Amshi : Bai san na kogo ba sai an yi sulu,
: In zo kixi inda Sani na Ummu,
: Bai san iyaka ba in ya ga noma.

Jagora : Waxanga maza cutarsu ta fi su, x^2
'Y/ Amshi : Duk qulle-qullensu ya zan na banza. x^2

Jagora : Ko an ce an qulle Sani na Alhaji,
'Y/ Amshi : Ba za mu yarda da qarya qasa ba,
: In zo kixi inda Sani na Ummu,
: Bai san iyaka ba in ya ga noma.
Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Katsinan Gusau,
Alhaji Muhammad Kabir Xanbaba (1984-)[73]*,*

53. *Gindin Waqa : Ginshimin Yari Magajin Magaji,*
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya.

---

73 A Sami Wannan Rerawa ne Daga Littafin *Diwanin Waqoqin Baka*. Gusau, S. M. 2009: 209-210.

Jagora : Ashe zaman duniya, x²
‘Y/Amshi : Juyi yakai cikin yara da manya,
: Wanda Allah yab ba,
: Son nikai mu zo mui ta biyatai,
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya. x²

Jagora : Kokowak kare da kura, x²
‘Y/Amshi : Ai na hana ta tun bara da rani,
: Karen gida yac ce,
: Ni wanga gargaxi yai mani daxi,
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya. x²

Jagora : Mai abu ya zo ga abunai, x²
: Saboda shi ad da abunai,
: Tun da shi ad da abunai,
‘Y/Amshi : A ba shi tun bai yi wuya ba,
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya. x²

Jagora : Ashe zaman duniya, x²
‘Y/Amshi : Juyi yakai cikin yara da manya,
: Wanda Allah yab ba,
: Son nikai mu zo mui ta biyatai,
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya. x²

Jagora : Alhaji Muhammadu Xanbaba, x²
‘Y/Amshi : Ko da xai ba ka da haushi,

: Tun da ka gade gidanku,
: Sai ka qara mashi soro,
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya. x^2

Jagora : Maidaji nai niyya, x^2
'Y/Amshi : Sai na zaka Gusau in ishe sarki,
: Mu yo gudun yunwa,
: Aikawa nikai iyalinmu su taso.
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya. x^2

Jagora : Da ni da bayata, x^2
'Y/Amshi : Mu wajjen mutun xari yara da mata,
: Babu mai iya xaukanmu,
: Sai Muhamman Nata'ala,
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya. x^2

Jagora : Kokowar kare da kura, x^2
'Y/Amshi : Ai na hana ta tun bara da rani,
: Karen gida yac ce,
: Ni wanga gargaxi yai mani daxi. x^2
Jagora : Ga wani ya shiga kokowa, x^2
: Ashe-ashe ba ya da qarhi,
'Y/Amshi : Ko da anka taga ya hwaxi,
: Babu jigon da ka tasai,
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya. x^2

Jagora : Tun da ya rasa mai tassai, x^4
'Y/Amshi : Halama ko ba ya da karfa. x^4
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya. x^2

Jagora : Ashe zaman duniya, x^2
'Y/Amshi : Juyi yakai cikin yara da manya,
: Wanda Allah yab ba son nikai,
: A zo ai ta biyatai,
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkak ka da hwama,
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya. x^2

Jagora : Alhaji Muhamadu Xanbaba, x^2
'Y/Amshi : Ko kaxan ba ya da haushi,
: Tun da ka gade gidanku,
: Sai ka qara mashi soro,
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Bazai na Jangeru,
Alhaji Muhammadu[74]*,*

54. *Gindin Waqa : Dogo na Jekadiya,*
: Na Saraki Sarkin Bazai.

Jagora : Kai Jangeru za ni kwana, x^2
'Y/Amshi : Don in ga Sarkin Bazai,
: In dai na ga Sarkn Bazai,

---

[74] An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{379}$ $^1/_3$.

: Allah na yi min magani,
: Dogo na Jekadiya,
: Na Saraki Sarkin Bazai. x^2

Jagora : Ai jikan Buhari, x^2
'Y/Amshi : Xan Amadu mai halin arziki,
: Ga abin da duk ya nuhwa,
: Allah na nuhwatai da shi, x^2
: Dogo na Jekadiya,
: Na Saraki Sarkin Bazai.

Jagora : To, Sarkin Bazai na Alhaji, x^2
'Y/Amshi : Ka san zaman zamani,
: Kowas san zaman zamani,
: Sharri ba ya komi da shi,
: Dogo na Jekadiya,
: Na Saraki Sarkin Bazai. x^2

Jagora : Lalle, x^2
'Y/Amshi : An nuhwa an nuhwa,
: Aniya makomam mutum,
: Duk mai mugunyan nuhwa,
: Allah sa ta dawo garai, x^2
: Dogo na Jekadiya,
: Na Saraki Sarkin Bazai.
Jagora : Ni Maidaji na yi zave, x^2
'Y/Amshi : Amma sai da nik qwangara,
: Na zavi Sarkin Bazai,
: Tun da ba kamatai garan,
: Dogo na Jekadiya,
: Na Saraki Sarkin Bazai. x^2

Jagora : To, komi dubum mutane, x^2
'Y/Amshi : Komi mutum yag gamu,
: In dai na ga Sarkin Bazai,
: Duka ba ruwana da su.
: Dogo na Jekadiya,
: Na Saraki Sarkin Bazai. x^2

Jagora : Alhaji na taho gudun yunwa, x2
: Inda Sarkin Bazai,
: Dajinmu babu gero,
: To, kuma can gida babu shi,
'Y/Amshi : Dawanmu ta mace,
: Kuma wakenmu ya qarmashe,
: Mu yi inda Sarkin Bazai,
: Can mu samu gero mu ci.

Jagora : Ai jikan Buhari, x3
'Y/Amshi : Xan Amadu mai halin arziki,
: Da abin da duk ya nuhwa,
: Allah na nuhwatai da shi. x3

Jagora : Ko can damo, x3
'Y/Amshi : Uban Jekada hanquri ag garai,
: Hay yau ban ji kukanka ba,
: Dogo na Jekadiya,
: Na Saraki Sarkin Bazai. x3

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Zazzau,
Alhaji Shehu Idris (1975-)[75]*,*

55. *Gindin Waqa : Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,*
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa.

Jagora : Akwai maza suna ga duniya, x2
: Duk ba a gane ba,
'Y/Amshi : Sai an bincika an tona za a ganewa,
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa. x2

Jagora : Maidaji na yi tonon duniya, x2

75 An sami wannan rerawa a Kundin Gusau, S. M. (1988: 612-615).

: Ga nawa xan wayo,
‘Y/Amshi : Wanda duk ka sa ma sharri ba ka mance shi,
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa. x^2

Jagora : Ko da kag ga sarkin Zazzau, x^2
: Ka ishe lamba xai,
‘Y/Amshi : Duk sarakuna sun kwanta ba su motsawa,
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa. x^2

Jagora : Sanqira ina faxa ma magana, x^2
: Ina yi ma saqo,
‘Y/Amshi : Sai a ban ‘yar mota na yi ma koke, x^2
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa.

Jagora : Sarkin ruwan mutanen Zazzau, x^2
‘Y/Amshi : Ya yi man saqo,
: Tun da ya zuba man shadda,
: Ba ni mancewa. x^2
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa. x^2
Jagora : Ko Alhaji Audu ya zuba man, x^2
‘Y/Amshi : Naira, ba ni mancewa. x^2
Jagora : Ga rawani da Sale yab ban,
: Yac ce saboda kai Baba,
‘Y/Amshi : Sale yai kira niz zo ba ni mancewa, ko
: Sale yai kira niz zo ba ni rainawa,
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa.

Jagora : Shehu damina ta kashe ni ban yi dawa ba, x^2
‘Y/Amshi : Tun da na ishe ma yunwa ba ta kama ni. x^2
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa.

Jagora : Wanda yay yi ma alheri ba ka mance shi, x^2
‘Y/Amshi : Wanda ya shirya ma sharri ba ka mance shi,

: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa. x^2

Jagora : Munahikin zuma mai saqa dab bayan qoqo, x^2
'Y/Amshi : Ga shi na tava na lasa ban ji zaqin ba,
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa. x^2

Jagora : Shehu na Xanmadami babban hadari,
'Y/Amshi : Mai ruwa sannu,
: Ran da yay yi malka ni'ima ba ta qarewa.
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa.

Jagora : Sarkin ruwan mutanen Zazzau na yi ma kyauta, x^2
'Y/Amshi : Tun da yaz zuba min shadda ba ni mancewa,
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa. x^2
Jagora : Alhaji Audu ya zuba min,
'Y/Amshi : Man Naira ba ni mancewa,
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa.

Jagora : Aminu ya yi mulkin Zazzau,
: Bai ci amana ba,
'Y/Amshi : Ya yi ya gama ya hurce ana marabatai.
Jagora : Kabiru ya yi mulkin duniya,
'Y/Amshi : Bai ci amana ba,
: Ya yi ya gama ya hurce ana marabatai.
Jagora : Hamza ya yi mulkin duniya,
'Y/Amshi : Bai ci amana ba,
: Ya yi ya gama ya hurce ana marabatai.
Jagora : Yamusa ya yi mulkin duniya,
'Y/Amshi : Bai ci amana ba,
: Ya yi ya gama ya hurce ana marabatai.
Jagora : Abdullahi ya yi mulkin duniya,
'Y/Amshi : Bai ci amana ba,
: Ya yi ya gama ya hurce ana marabatai.
Jagora : Malam Musa da yay yi mulkin duniya,

‘Y/Amshi : Bai ci amana ba,
: Ya yi ya gama ya hurce, ana maraba tai,
Jagora : Yamusa ya yi mulkin duniya,
‘Y/Amshi : Bai ci amana ba,
: Ya yi ya gama ya hurce, ana maraba tai,
Jagora : Kuma Audu ya yi mulkin duniya,
: Bai ci amana ba,
‘Y/Amshi : Ya yi ya gama ya hurce, ana maraba tai,
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa.

Jagora : Aminu ya yi babban ganxo,
‘Y/Amshi : Nan qasar Zariya,
: Wanda nis sani ko Binuwai ba ta banke su.

Jagora : Kabiru ya yi babban ganxo,
‘Y/Amshi : Nan qasar Zariya,
: Wanda nis sani ko Binuwai ba ta banke su,
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa.

Jagora : Akwai maza suna ga duniya, x^2
: Duk ba a gane ba,
‘Y/Amshi : Sai in bincika an tona za a ganewa,
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa. x^2

Jagora : Ni Maidaji na yi tonon duniya, x^2
: Ga nawa xan wayo,
‘Y/Amshi : Wanda duk ka sa ma sharri ba ka mance shi. x^2

Jagora : Ai cikin kashi biyu, Allah ba ya mance su, x^2
: Wanda yay yi ma alheri,
‘Y/Amshi : Wanda yay yi ma sharri ba ka mance shi, x^2
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa.

Jagora : Duk wanda yay yi man alheri, x^2
: Ina ta gaida shi,

‘Y/Amshi : Wanda ba shi ban alheri, ba ni gai da shi.
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa. x^2

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alqalin Sabon Birni,
Alhaji Malam Ahmad[76]*,*

56. *Gindin Waqa : Barka da shirin zamani,*
: Malam sannu da gyaran gari.

Jagora : Alqalin Sabon Birni, x^2
‘Y/Amshi : Maganatai yanzu tana Ingila,
: Barka da shirin zamani,
: Malam sannu da gyaran gari. x^2

Jagora : Sakkwato birnin Shehu ta mu bi su, x^2
‘Y/Amshi : Mu taru mu zan gai da su, x^2
: Barka da shirin zamani,
: Malam sannu da gyaran gari.

---

[76] An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{378}$ $^1/_4$.

Jagora : Ana magana an ce zamani, x²
‘Y/Amshi : Ashe Allah shi az zamani,
: Sai Allah ya kiyaye gaba,
: Da wanga irin mugun zamani,
: Barka da shirin zamani,
: Malam sannu da gyaran gari. x²

Jagora : Masu ruwan kihi na su na, x²
‘Y/Amshi : Talakkawa sarki ad da su,
: Kai kau masu gari naka na, x²
: Barka da shirin zamani,
: Malam sannu da gyaran gari.

Jagora : Cikin nassi magana ta fita, x²
: In ka ce a bari ka a yi,
‘Y/Amshi : In ka ce a yi kowa ya yi,
: Malam sai wada kal lissahwa, x²
: Barka da shirin zamani,
: Malam sannu da gyaran gari.

Jagora : Yanzu ina Malam Madugu,
‘Y/Amshi : Ina Mamman duk yaranka ne,
: Barka da shirin zamani,
: Malam sannu da gyaran gari.

Jagora : Ga wani ya aje jikka xari, x²
: Ga wani bai aje ko ahu ba,
‘Y/Amshi : Ga wani ya rasa yadda zai yi da su,
: Barka da shirin zamani,
: Malam sannu da gyaran gari. x²

Jagora : Na gode Alqali, x²
‘Y/Amshi : Abin da yas shirya mana ya kyauta, x²
: Barka da shirin zamani,
: Malam sannu da gyaran gari.

Jagora : Kullum na zaka in gai da shi, x²
‘Y/Amshi : Sai ya ba ni sule arba’in,
: Ya ce ga shi mu sai kudaku, x²

: Barka da shirin zamani,
: Malam sannu da gyaran gari.

Jagora : Sakkwato dai birnin Shehu ta, x2
: Mu bi su,
'Y/Amshi : Mu taru mu zan gai da su,
: Barka da shirin zamani,
: Malam sannu da gyaran gari. x2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Hillani,
Alhaji Muhammadu Dikko Xanmaliki[77]*,*

57. *Gindin Waqa : Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,*
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada.

Jagora : Dikko farin sarki, x2
'Y/Amshi : Biyakka tai min anhwani,
: In da duk nis same shi,
: Na zai min kyauta,
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada. x2

Jagora : Na daxe ina son, x2
'Y/Amshi : In zo ga sarkin Hillani,
: To, Alhaji ta yi daidai, x2
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,

[77] An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{1}/_{143}$ $^{1}/_{9}$.

: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada.

Jagora : Jikan Hassan, x^2
‘Y/Amshi : Jikan Hussaini sarkin Hillani,
: Da munka zo gogana,
: Hwan xari yas shirya min, x^2
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada.

Jagora : Ai Dikko san ga da kab ba ni,
‘Y/Amshi : Sai na gyara shi,
: Ran da duk nas saishe shi,
: Sai ya wo tsada,
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada.

Jagora : Al’amarin jikan Nana ikon, x^2
‘Y/Amshi : Allah ne,
: Ba ya barin hwansa tai ta kai ranag gobe,
: In da yan nune shi, nan zai ramawa,
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada. x^2

Jagora : To, Ali Dogo bai haihi xa,
‘Y/Amshi : Xan iska ba,
: Kwag ga kamannunsa ka san a raba dai,
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada.

Jagora : Zuwanmu Xanmaliki ni da sarkin Hillani,
‘Y/Amshi : Rambaxawa sun je ni,
: Has sun yo tarbe,
: Tun da dai sun tarbe mu,
: Ai sun yo kyauta,
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada.

Jagora : Dibi garin Idi,

‘Y/Amshi : Had da su sun yo tarbe,
: Tun da dai sun tarbe mu,
: Ai sun yo kyauta,
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada.

Jagora : ‘Yan Tufkawa,
‘Y/Amshi : Sun biyo ni,
: Has sun yo tarbe,
: Tun da dai sun tarbe mu,
: Ai sun yo kyauta,
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada.

Jagora : To, mun bi Gatawa, x^2
‘Y/Amshi : Had da su sun yo tarbe,
: Tun da dai sun tarbe mu,
: Ai sun yo kyauta,
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada. x^2

Jagora : To, mun bi Sardauna, x^2
‘Y/Amshi : Had da su sun yo tarbe,
: Tun da dai sun tarbe mu,
: Ai sun yo kyauta, x^2
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada.

Jagora : Baqon Baura, baqon,
‘Y/Amshi : Sarkin noma Kassu,
: Alhaji lalle wannan mutum ya san kara,
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada.

Jagora : Na biyo jikan Nana,
: Sarkin Hillani, x^2
‘Y/Amshi : Ko da xai tsatson Shehu girma yag gada,

: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Muhammadu Xanqoqari[78]*,*

58. *Gindin Waqa :Ya hana aikin yini,*
: Muhammadu xan qoqari.

Jagora : Asha banza za ni, x^2
: In ga Muhammadu Namijin maza,
'Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari. x^2

Jagora : Bi Muhammadu jikan Tudu,
: Na Garba ya ci garin gyazama,
'Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari.

Jagora : Yau Asha banza za ni,
: In ga Muhammadu garken maza.
'Y/ Amshi : Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari.
Jagora : Ya hana aikin yini,
: Ga Muhammadu gandun maza,
: Asha banza za ni,

78 An Sami Wannan Rerawa ne a Kundin Gusau (1983: 470-473).

: Don in ga Muhammadu qirgin maza.
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari.

Jagora : Bi Muhammadu jikan Tudu,
: Na Garba ya ci garin gyazama,
: Xan qoqari yake,
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari.

Jagora : Asha banza za ni,
: Don in ga Muhammadu garken maza
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari.
Jagora : Kowa aje gero da dawa,
: Ya aje dangin zama,
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari.
Jagora : Kowa aje gero da dawa, x^2
: Ya aje tushen zama,
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari. x^2

Jagora : Wani ya yi gida ba dame, x^2
: Ka ga kamar an yi ba a yi ba.
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari. x^2

Jagora : Asha banza sun aje rogo, x^2
: Sun aje dangin zama,
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari. x^2

Jagora : Shi ya kashe dajin gabas, x^2
: Kuma ya kashe dam qaruwa.
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari. x^2

Jagora : Ga rana ga ruwa, x^2

: Yau ana shagalin damana,
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari. x^2

Jagora : Kowa aje gero da dawa,
: Ya aje tushen zama,
‘Y/ Amshi : Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari.

Jagora : Wani ya yi gida ba dame, x^2
: Ka ga ya yi kamar ba a yi ba.
‘Y/ Amshi : Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari. x^2

Jagora : Bara mun zo qi rabon dubu,
: Hammu nan ba a manta mu ba,
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari.
Jagora : Mun kwana da yinwar dawo, x^2
: Mun kwana da yinwar tuwo,
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari. x^2
Jagora : Mun kwana da yinwar dawo, x^2
: Mun kwana da yinwar hura,
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari. x^2
Jagora : Daxa za mu gida ba kwabo, x^2
: Ka raka mu da qaton dubu,
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari. x^2

Jagora : Su wane sun yi dubun tanbaxa, x^2
: Dubun da an yi kamar ba a yi ba,
: Dubun da babu hura ba tuwo, x^2
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari.
Jagora : Su wane sun yi dubun tambaxa,
: Dubun da babu hura ba tuwo,
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,

: Muhammadu xan qoqari.

Jagora : Bi Muhammadu jikan Tudu, x^2
: Na Garba ya ci garin gyazama,
'Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari. x^2
Jagora : Muhammadu nai godiya,
: Ka ga ban yada raina ka ba,
: Xan Battu nai godiya,
: Ka ga ban yada raina ka ba,
'Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Mamman Xankaltu,

59. *Gindin Waqa : Wuce maza xan kurma*[79]*,*
: A gaida Mamman xan Kaltu.

Jagora : Sai dare jikan mata,
: Hatsi ga Mamman sun taru,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu.

Jagora : Na Kaka Mamman xan Kaltu, x^2
: Damamisan mai turaye.
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu. x^2

Jagora : Garin Idi za ni,
: Akwai mazan da ka xauka ta,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu.

Jagora : Na Magaji garin Idi za ni,
: Akwai mazan da ka xauka ta,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu.

---

79 An Sami Wannan Rerawa ne Kundin Gusau (1983: 476- 478).

Jagora : Na yi godiya ga Mamman ya kyauta, x^2
: Saboda damma yab ban kan,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu. x^2

Jagora : Allahu ya umfana,
: Saboda damma yab ban kan,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu.

Jagora : Sani uban dawaki ya kyauta, x^2
: Saboda Mamman ya kyauta,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu. x^2

Jagora : Abin da Allah ya rena,
: Baqin mutum bai ta da mai,
: Abin da Allah ya rena,
: Baqin mutum bai matsa shi,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu.

Jagora : Mun taho ga aiki don kara, x^2
: Ashe maza na nan Korau,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu. x^2

Jagora : Na Arxo maza na nan Korau,
: Ku zan ka jefa min galma,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu.

Jagora : Ban ja mutum ba ya bar jana,
: Rabi da jefa min galma,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu.

Jagora : Lalle su wane ai shagguna ku, x^2
: Ka san Uban shagguna nan. x^2

Jagora : Ni uban mutum nika vacewa, x^2
: Ba ya da halin ramawa,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu. x^2

Jagora : A gaida Mamman xan Kaltu, x^2
: Damamisan mai turaye,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu. x^2

Jagora : Sai dare jikan mata, x^2
: Hatsi ga Mamman sun taru,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu. x^2

Jagora : Na Magani garin Idi za ni, x^2
: Akwai mazan da ka xauka ta,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu. x^2

Jagora : Mu je ga Mamman xan Kaltu, x^2
: Damamisan mai turaye,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu. x^2

Jagora : Amiya xiyar mai turaye,
: Saboda Mamman ta kyauta,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu.

Jagora : Mai gari ban rena ba, x^2
: Saboda Mamman ta kyauta,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu. x^2

Jagora : ‘Yar Gajera Allah umfana, x^2
: Saboda Mamman ta kyauta,
‘Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu. x^2

Makaxi : Alhaji Sa’idu Rambaxawa Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Umar Na’Allah (1966-1975-)[80],
60. *Gindin Waqa : Gagara gasa na Alhaji Gardaye,*
: Umaru gagon Bala uban Sarkin fada.

Jagora : Baba kan hana, x^2
‘Y/Amshi : Taron maza uban sarki Mamman,
: Faxa masu kowa ka ja ma sarki ya fasa,
: Gagara gasa na Alhaji Gardaye,
: Umaru gagon Bala uban Sarkin fada. x^2

Jagora : Xan Inna, x^2
‘Y/Amshi : Xan sarauniya, xan mai Runji,
: Umaru xan Bawa,
: Ba a kai ma ‘yan kamanci, x^2
: Gagara gasa na Alhaji Gardaye,
: Umaru gagon Bala uban Sarkin fada.

Jagora : Alhaji ka rabu da dibin maza, x^2
‘Y/Amshi : Su nai ma bakanta,
: Umaru ka san abin da Shawai yas shirya,
: Gagara gasa na Alhaji Gardaye,
: Umaru gagon Bala uban Sarkin fada. x^2

---

80 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{54}$ $^1/_4$.

Jagora : In don xan Hakimin ga mai, x^2
‘Y/Amshi : Mugun hali,
: Umaru na so a warware mai hakimci, x^2
: Gagara gasa na Alhaji Gardaye,
: Umaru gagon Bala uban Sarkin fada.

Jagora : Ashe kokuwar kare da kura,
‘Y/Amshi : Ta qare,
: Gagara gasa na Alhaji Gardaye,
: Umaru gagon Bala uban Sarkin fada.

Jagora : Gagara gasa na Alhaji Gardaye,
‘Y/Amshi : Umaru tsatson Bala uban sarkin fada,

Jagora : Baba kana hana, x^2
‘Y/Amshi : Taron maza uban sarki Mamman,
: Faxa masu kowa ka ja ma sarki,
: Ya fasa.
: Gagara gasa na Alhaji Gardaye,
: Umaru tsatson Bala uban sarki fada. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Madawa, Alhaji Muhammadu[81]*,*

61. *Gindin Waqa : Na zaka barka da azzukka,*
: Sarkin Madawa Muhammadu,
: Ko yanzu duniya ta yo mai haske.

Jagora : Ko can na san gidan kadannu, x^2
'Y/Amshi : Sai 'yan taru,
: Yaqi ya hwaxi 'yan hawa sun dawo ganga,
: Na zaka barka da azzukka,
: Sarkin Madawa Muhammadu,
: Ko yanzu duniya ta yo mai haske. x^2

Jagora : Wanga gidan tawaye ne, x^2
'Y/Amshi : Gidan Jibo sarki yag gado,
: Hwaxa masu ba mai shiga gidan,
: Sai in bayan kai,
: Na zaka barka da azzukka,
: Sarkin Madawa Muhammadu,
: Ko yanzu duniya ta yo mai haske. x^2

Jagora : Ashe sabilin kaza, x^2
'Y/Amshi : Qadangare yag ga ruwan kasko,
: Ashe ko na san,
: Qadangare ya sha daxi nai. x^2
Jagora : Ni Alhaji Maidaji xan mutanen, x^2
'Y/Amshi : Sabon Birni Sabilin sarkin ga,
: Za ni in kwan huxu Madawa. x^2

---

81 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{376}$ $^1/_7$.

Jagora : Hwadawan Madawa ina masoya, x²
'Y/Amshi : Sabon sarki ku yo mana kaya,
: Da za ni sa wa sabon sarki,
: Na zaka barka da azzukka,
: Sarkin Madawa Muhammadu,
: Ko yanzu duniya ta yo mai haske. x²
Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni
Mai Waqa : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ibrahim (1970-1975)[82],

62. *Gindin Waqa : Sadauki Bala gagon Salihu,*
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho.

Jagora : Da girma da imani, x²
'Y/Amshi : Wanda duk yab buqata ga Allah,
: Ya biya mai,
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho. x²

Jagora : Alhaji ya san biyar,
'Y/Amshi : Allah, tun da ya sa zumunta,
: Yana xaukan 'yan'uwa,
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho.

Jagora : Kai ko yau da,
'Y/Amshi : Mazan birni gidan Sanda,
: Birnin da Sanda yai shubka ya fito,
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho.

Jagora : Iron gidan Bawa Jangwarzo, x²
'Y/Amshi : Iron xan Inna ya hau kamaj jari ya hawo,
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho. x²

Jagora : Sarki niqatau, x²

---

82 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{1}/_{375}$ $^{1}/_{10}$.

‘Y/Amshi : Uban Jabau uban xan Inna,
: Ya gyara kulkin horon maza, x^2
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho.

Jagora : Duk wanda Bawa yai, x^2
‘Y/Amshi : Mulkin Gobirawa,
: Ga naka zamani yah hito. x^2
Jagora : Duk wada Halliru,
‘Y/Amshi : Yai mulkin Gobirawa,
: Ga naka zamani yah hito.
Jagora : Duk wada Jari yai,
‘Y/Amshi : Mulkin Gobirawa,
: Ga naka zamani yah hito.
Jagora : Duk wada Sambo,
‘Y/Amshi : Yai mulkin Gobirawa,
: Ga naka zamani yah hito.
Jagora : To, yanzu ga naka,
‘Y/Amshi : Zamani, Iro xan Inna,
: Ba wanda yam motsa an yi shu,
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho.

Jagora : Sarki niqatau, x^2
‘Y/Amshi : Uban Jabau uban xan Inna,
: Ya gyara kulkin horon maza,
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho. x^2

Jagora : Duk wada nig ga dama haka,
‘Y/Amshi : Haka zan faxi
: Tun da Alhaji Isa na nan gidanai,
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho.

Jagora : Sarki ya ba ni doki kyauta, x^2
‘Y/Amshi : Sannan ya ba ni ‘yar hanya,
: Kuma ga ta Faranshi ‘yar Nijar,
: To, yau kyautakka ta wuce godewa,

: Sai in tashi in durqusa in tuba xai. x^2

Jagora : Alhaji Isa ina gode mai,
'Y/Amshi : Don ga dammeman da yas shirya man,
: Alhaji Maidaji ya gode ma qwarai.
Jagora : Alhaji Abubakar,
'Y/Amshi : Ya kyauta,
: Don ga takardun da yas shirya man,
: Alhaji Maidaji ya gode ma qwarai.
Jagora : Alhaji Dango,
'Y/Amshi : Ina gode mai,
: Don ga takardun da yas shirya man,
: Alhaji Maidaji ya gode ma qwarai,
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho.

Jagora : Jikan Kunda magajin Dango, x^2
'Y/Amshi : Na kama ni hau uban Mamman swahe dut,
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho. x^2

Jagora : Iro jikan mazajen Gobir, x^2
'Y/Amshi : Jikan Jadi da sarki Jari,
: Sarki roqon ga ne da swahai yay yi ma, x^2
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho.

Jagora : Alhaji ya san biyar, x^2
'Y/Amshi : Allah, tun da ya sa zumunta,
: Yana xaukan 'yan'uwa,
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho. x^2

Jagora : Da girma da imani, x^2
'Y/Amshi : Wanda duk yab buqata ga Allah,
: Ya biya mai,
: Sadauki Bala gagon Salihu,

: Inda Alhaji Ibrahim nit taho. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Tsibirin Gabas,
Alhaji Ali Kambakarwa[83]*,*

63. *Gindin Waqa : Na zo ganin bajinin qani,*
: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya.

Jagora : Dogo da gado na Muhammadu, x^2
'Y/Amshi : Giwa maganin qaramin dawa,
: Na zo ganin bajinin Ali,
: Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya. x^2

Jagora : Gobir na Bawa uwah hwaxa, x^2
'Y/Amshi : Kakanka ya yi kwararrame,
: Ya koma yai tsibirin gabas,
: Na zo ganin bajinin qani,
: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya. x^2

Jagora : Nai marmari in zo Gubur, x^3
'Y/Amshi : Tsibirin gidanmu na Awwali,
: Babban gida na nan duniya,
: Na zo ganin bajinin qani,
: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya.x^3

Jagora : Yakubu, x^2
'Y/Amshi : Shi da Ade da Hwankale,
: Na san gidansu na can gabas. x^2

Jagora : Da baranqwame da Kututturu, x^2

---

83 Wannan rerawa an same ta a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. A Faifai mai lamba AL $^1/_{376}$ $^1/_4$.

‘Y/Amshi : Na san gidansu na can gabas. x^2

Jagora : Na san gidansu gabaccin Makka,
‘Y/Amshi : Gani da anka gano muna.
Jagora : Xan sanda ko dai ba ka nan, x^2
‘Y/Amshi : Na san kana da mazan hwaxa,
: Na zo ganin bajinin qani,
: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya. x^2

Jagora : Galadima na Yashe, x^2
‘Y/Amshi : Da yaz zaka ya ishe Alhaji Xantsumi,
: To, ha madami da shi a kai. x^2
Jagora : Da gidan Magaji da Xantsumi, x^2
‘Y/Amshi : An ba mu abinci iri-iri,
: Kullum shira muna shi ya kai. x^2

Jagora : Alhaji na zaka godiya,
‘Y/Amshi : Dokin da ya aikan mana,
: Dum murna xai mu kai,
: Na zo ganin bajinin qani,
: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya.

Jagora : Gobirawa kui muna gahwara, x^3
‘Y/Amshi : Alhaji ban kwana ya kai,
: Ba mu san ta rai ba ga duniya,
: Na zo ganin bajinin qani,
: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya. x^3

Jagora : Na gode mushe Abubakar, x^3
‘Y/Amshi : Jekada yai komi,
: Albarkacin bajimin Ali. x^3
Jagora : Mushe Umaru na gode maka, x^3
‘Y/Amshi : Riga ta hwan tara yay yi min,
: Albarkacin bajimin Ali.
: Na zo ganin bajinin qani,

: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya. x^3

Jagora : Mushe Musa na gode maka, x^2
'Y/Amshi : Don ga akwati da yai mana,
: Duk ya cika shi da riguna. x^2

Jagora : Bayan ya cika shi da riguna, x^3
'Y/Amshi : Ya ba ni zanen jikka bakwai,
: Albarkacin bajimin Ali.
: Na zo ganin bajinin qani,
: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya. x^3

Jagora : Alhaji ya zaka lahiya, x^3
'Y/Amshi : Ya zo gida da hwarin ciki. x^3

Jagora : Kai tun rad da Alhaji yaz zaka, x^2
'Y/Amshi : Tscibiri zama maka xai a kai. x^2

Jagora : Ga Tscibirin da had danginka,
'Y/Amshi : Han mu gama maka xai mu kai,
: Na zo ganin bajinin qani,
: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya.

Jagora : Sarki na Amina, na Isaka,
'Y/Amshi : Mi kaka shawara,
: Kai an ka bam ma qasag gabas,
: Na zo ganin bajinin qani,
: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya.

Jagora : Allah da ya tsira duniya, x^2
'Y/Amshi : Ya yo ta don a yi shawara. x^2
: Na zo ganin bajinin qani,
: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Bawa (1975- 2003)[84]*,*

64. *Gindin Waqa : Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,*
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni.

Jagora : Taqamad da nikai ta ka ta uban 'yan kwana, x²
'Y/Amshi : Lokaci ya kama ka ba ni sabbin kaya,
: Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni. x²

Jagora : Bawa uban Balarabe shirya zamanka, x²
'Y/Amshi : Tun da ka zama sarki,
: Tun da kai sarki yau ba ka da haushin kowa, x²
: Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni.

Jagora : Sarki ka ta da Tawam Makau,
'Y/Amshi : Ka ta da Alqalawa,
: Ka shirya Sabon Birni wanda Shawai yay yi,
: Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni.

Jagora : Baba uban Ali uban Sallau, x²
'Y/Amshi : Uban Xan'isa shi a uban mu gurin,
: Xa ag garai ya cim mai. x²

Jagora : Daga Jari kada tat taho ga sarki Shawai, x²
: Dag garai Salihu xan Durumbu yaz zama sarki,
: Dag garai Ummaru xan sarauniya yai sarki,
'Y/Amshi : Dag garai Ibrahim na Bawa yaz zama sarki,
: Mu leqa hwadar Inna Bawa shi ma ya kai,
: Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni. x²

---

84 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{1}/_{144}$ $^{1}/_{4}$.

Jagora : Gobirawa ku yi hankali ku bag ganganci, x^2
‘Y/Amshi : Inda nis saba ya hi inda nis sha daxi,
: Don wuya ta ni ban kula da daxin wani ba, x^2
: Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni.

Jagora : Shirya zamanka tun da ka zama sarki, x^2
‘Y/Amshi : Tun da kai sarki yau ba ka da haushin kowa. x^2

Jagora : In kwana bai qare ba ba a saurin kuka, x^2
‘Y/Amshi : Bawa ka san Allah ka gyara kayan kowa,
: Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni. x^2

Jagora : Allah mai gyara mutum guda ya wo mai baiwa, x^2
‘Y/Amshi : Ya shirya sauran dangi su bi shi don baiwa tai,
: Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni. x^2

Jagora : Dikkon Gande xan Muhammad inda kak kai ya kai,
‘Y/Amshi : Don shi ak kyawon mutum a san halinai,
: Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni.

Jagora : Dikko na biyo in gaisai hwan xari yab bayat,
‘Y/Amshi : Alhaji ya dai gode abin da yas shiryo mai.
Jagora : Uban Dawaki riguna ya aiko min,
‘Y/Amshi : Alhaji ya dai gode abin da yas shirya mai.
Jagora : Garkuwa na dai gode ya biya ni yai komi,
‘Y/Amshi : Alhaji ya dai gode abin da yas shiryo mai.
Jagora : Ai dole in gai da Waziri wanda al Lajinge,
‘Y/Amshi : Alhaji ya dai gode abin da yas shiryo mai.
Jagora : To kuma na gode ma Alhaji xan Adamawa,
‘Y/Amshi : Alhaji ya dai gode abin da yas shirya mai,
: Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni.

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,

Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ibrahim(1970-1975)[85]*,*

65. *Gindin Waqa : Madogara na Alhaji Isa,*
: Iro xan Magaji Uban Yari,
: Ginshiqin Gabas na Baraya.

Jagora : Sarkin sarakuna kake xan, x^2
'Y/Amshi : Inna maraji ga Bamfai. x^2

Jagora : Ibrahim xan Ibrahim,
'Y/Amshi : Madogara na Alhaji Isa,
: Iro xan Magaji uban Yari,
: Ginshiqin gabas na Baraya.

Jagora : Ga dauri ka hana wanka, x^2
'Y/Amshi : Sarki uban makama da Bango,
: Maza su bak haye maka Barde,
: Saboda na ga ba ka da daxi,
: Madogara na Alhaji Isa,
: Iro xan Magaji Uban Yari,
: Ginshiqin Gabas na Baraya. x^2

Jagora : Sarki da hankali shi ka aiki, x^2
'Y/Amshi : Wanda yah hi yi da agogo,
: Don mutum shi na da agogo,
: Bai yi shawara ba kama tai,
: Madogara na Alhaji Isa,
: Iro xan Magaji Uban Yari,
: Ginshiqin Gabas na Baraya. x^2

Jagora : Na Bawa tun kana xan sarki, x^2
'Y/Amshi : Bai yi qa'ida ba da kowa,
: Don mutum na ra'ayi nai,
: Iro bai kula da mutum ba. x^2
Jagora : Tun daq qasar Gobir, x^2
'Y/Amshi : Hat Tscibiri,

---

[85] An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{375}$ $^1/_9$.

: Haka za da Alqalawa,
: Iro an aza maka girma,
: Ka xauki anniyar riqe baya,
: Madogara na Alhaji Isa,
: Iro xan Magaji Uban Yari,
: Ginshiqin Gabas na Baraya. x^2

Jagora : Balle abin da zai kashe kuwa, x^2
'Y/Amshi : Na san ba zai rage ma kare ba,
: Abin da yac ci uban Garba,
: Ya gama da Alhaji Isa, x^2
: Madogara na Alhaji Isa,
: Iro xan Magaji Uban Yari,
: Ginshiqin Gabas na Baraya.

Jagora : Ni dai ina ta horonku mazanmu, x^2
'Y/Amshi : Ku dai ku xauki batu na,
: Duk wanda yay yi matan aure,
: Sai ya zan riqe su gaba xai,
: Sarki ka zan riqe mu gaba xai
: Zavi son ka ba shi da daxi,
: Madogara na Alhaji Isa,
: Iro xan Magaji Uban Yari,
: Ginshiqin Gabas na Baraya. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa,
Mai Waqa : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Umaru Na-Allah (1957-1966),

66. *Gindin Waqa : Uban Jekadiya*[86]*,*
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin magatakarda.

Jagora : Gyara shirin zama da kai da mutanenka, x^2
'Y/Amshi : Kar ka ce ga wani wanda ba ya son ka,
: Uban Jekadiya,
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin magatakarda. x^2

Jagora : Allah xai ka qin mutum ya ji zahi, x^2
'Y/Amshi : Don mutum ya ce ba ya son ka me yake ma. x^2

Jagora : Giwa ta hi gangarawa kuma tahi gewaye, x^2
'Y/Amshi : Darzaze take ga rahi. x^2

Jagora : Katakoren gidan Muhamman, x^2
'Y/Amshi : Bajimin gidan kada. x^2

Jagora : Ummaru, Ummarun gidan Ummaru, x^2
'Y/Amshi : Sa maza ladab Ummaru sa maza lavewa,
: Uban Jekadiya,
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin magatakarda. x^2

Jagora : Allahu duniya mui ta abin da za mu yi, x^2
'Y/Amshi : Ba nan za mu tabbata ba. x^2

Jagora : Ni ba abin da yay yi min zahi da duniya, x^2
'Y/Amshi : Sai Allah da yas shira mutuwa yag gama ta shexa. x^2

Jagora : In hairan ka ke, x^2
'Y/Amshi : Ka iske hairan yana jiranka. x^2

Jagora : In sheri ka ke, x^2
'Y/Amshi : Ka iske sheri na jiranka. x^2

[86] Wannan rerawa an same ta ne a wajen Xahiru, G. 1990: 103-105.

Jagora : Lalle abin da ka haihwa, x^2
'Y/Amshi : Du kana ishewa. x^2

Jagora : In kai ta shwaran sheri, x^2
'Y/Amshi : Su da xa uwayensu sun ji dai kumya,
: Tun da sun qi yarda,
: Uban Jekadiya,
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin magatakarda. x^2

Jagora : Sarkin hula da babban dango, x^2
'Y/Amshi : Wanda yay yi riqo yay yi anniyar yi. x^2

Jagora : Xan sarauniya xan Dango, x^2
'Y/Amshi : Ummaru giwa tarbe shirin maharb,
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin magatakarda. x^2

Jagora : Sarki uban salau xan dodo, x^2
'Y/Amshi : Sarki uban Galadima ya haye aduwai. x^2

Jagora : Uban lihidda, x^2
'Y/Amshi : Sarkin Gobir abin da kay yi,
: Nuhi shi ka kai ga ranka,
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin magatakarda. x^2

Jagora : Bari shawara da mai makalamanka, x^2
'Y/Amshi : Saboda sarki ba shawara ya kai ba,
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin magatakarda. x^2

Jagora : Taron nan da kun ka zo, x^2
'Y/Amshi : Ni ban zo ba na ji wai,
: Bango da Labbo Jekada,
: Su suka hwaxa min,
: Sanda ubangijin Makama,

: Bajimin magatakarda. x^2

Jagora : Sarauniya da tas sabka tay yi girgiza,
'Y/Amshi : Sai tac ce ma Garba,
: Wannan sarkin wace jiha ne,
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin magatakarda. x^2

Jagora : Sai Garba xan Hassan,
'Y/Amshi : Yac ce mat Babacire ne.

Jagora : In ka ji Bawa Jangwarzo nan cikin takarda, x^2
'Y/Amshi : Shi na aka rubuta,
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin magatakarda. x^2

Jagora : Riqa qwrai qwarai, x^2
'Y/Amshi : Bar tsoron uban zagi,
: Jikan Sanda gaskiya Allah ta hi yin mutane.
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin magatakarda. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Umar Shawai (1957-1966)[87],

87 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{143}$ $^1/_{12}$.

67. *Gindin Waqa : Baban yari baban Makama,*
: Baba uban Lihidda na Sardauna.

Jagora : Sarki ya kwana da hwarin ciki, x^2
'Y/Amshi : Har yau bai kwan da muni garai ba,
: Baban yari baban Makama,
: Baba uban Lihidda na Sardauna. x^2

Jagora : Ya zo Makka ya zo Madina, x^2
'Y/Amshi : Alhaji ya taho lahiya lau,
: Baban yari baban Makama,
: Baba uban Lihidda na Sardauna. x^2

Jagora : Ga Alhaji ya taho za mu tarbe,
'Y/Amshi : Da wace gaisuwa zan ishe mai.

Jagora : Ko waqar …., x^2
'Y/Amshi : Sarauta mu kai mai,
: Koko dai salati mu kai mai. x^2

Jagora : To, in kau salati mu kai mai, x^2
'Y/Amshi : To, sun ce, "'Yan'uwa babu zambo",
: Baban yari baban Makama,
: Baba uban Lihidda na Sardauna. x^2

Jagora : Baqon Jidda baqon Kano,
'Y/Amshi : Alhaji baqon Ministan Arewa,
: Baban yari baban Makama,
: Baba uban Lihidda na Sardauna.

Jagora : Sarkin Makka ya aiko wasiqa,
'Y/Amshi : Ya aiko ma jikan ta Barga.
Jagora : Kuma Sardauna ya aiko wasiqa,
'Y/Amshi : Ya aiko ma jikan ta Barga,
Jagora : Sun ce,
'Y/Amshi : Galibin duniyag ga,
: Duka kowa ya kama musulunci,
: Baban yari baban Makama,
: Baba uban Lihidda na Sardauna.

Jagora : A yi kono da salla da zakka, x^2
'Y/Amshi : Ai ta abin da Allah ka qamna. x^2

Jagora : A yi amre a zam son zumunta, x^2
'Y/Amshi : A zam son zumunta,
: Ai ta abin da Allah ke qamna,
: Baban yari baban Makama,
: Baba uban Lihidda na Sardauna. x^2

Jagora : To, ni ga ni na sa tsari,
'Y/Amshi : Amma matan gari na hanawa.

Jagora : Lalle matan gari na ta vanna, x^2
'Y/Amshi : Don ba su san abin da Allah ka so ba. x^2

Jagora : Wance da wance sun gadi vanna, x^2
'Y/Amshi : To, vannassu ba za ta ci ba,
: In ma ta ci Allah kiyaye. x^2

Jagora : Ga matan da nas sa tsari, x^2
'Y/Amshi : Yau ga su ga rariya za su tarbe. x^2
: Baban yari baban Makama,
: Baba uban Lihidda na Sardauna.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Xan Bawa[88]*,*
68. *Gindin Waqa : Ya tara dame mai dama,*
: Xan Bawa qanen mai gona.

Jagora : Xan Bawa magajin Jimro, x^2

88 An sami wannan rerawa ne a Cikin Kundin Gusau, S. M. 1983: 469-470.

: Na Badiga jikan Mana,
'Y/ Amshi : Kai mun ka sani gun qwazo,
: Ya tara dame mai dama,
: Xan Bawa qanen mai gona. x^2

Jagora : Dubun Xan Bawa faxin Allah ne, x^2
'Y/ Amshi : Allah yai bayu ba mai tasai,
: Ya tara dame mai dama,
: Xan Bawa qanen mai gona. x^2

Jagora : In dai na zaka Jauri yawona, x^2
'Y/ Amshi : In na iske manun 'Yar Kuta,
: Sai ya bani dame in xauko. x^2

Jagora : Kullum dai na zaka yawona, x^2
'Y/ Amshi : In na iske mijin 'Yar Kuta,
: Sai ya ba ni dame in xauko, x^2
: Ya tara dame mai dama,
: Xan Bawa qanen mai gona.

Jagora : Xan Bawa inai ma horo, x^2
'Y/ Amshi : Kai dai ka tsare horo na. x^2

Jagora : To, horon da nikai muku Anna, x^2
'Y/ Amshi : Kowa ya riqe kwasa tai.
: Ya tara dame mai dama,
: Xan Bawa qanen mai gona. x^2

Jagora : Kowa yi dubu har yay yi rabo, x^2
'Y/ Amshi : Ya xau maganar kaka nai. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,
Mai waqa : Alhaji Isyaka Abarshi[89]*,*

69. *Gindin Waqa : Abarshi xan mai damma xan shibo,*
: Xan Shaku da niyya nig ga nai.

Jagora : Ina na mani ga Anne xan Bawa, x^2
'Y/Amshi : Mai katakka da aiki swahe duk,

---

89 An sami wannan rerawa ne a Cikin Kundin Gusau, S. M. 1983: 467-469.

: Abarshi xan mai damma xan shibo,
: Xan Shaku da niyya nig ga nai. x^2

Jagora : Abarshi na xan Kura xan Nomau, x^2
'Y/Amshi : Biyakka ta hi biyas shaggun xiya. x^2

Jagora : Abarshi ya kashe canjin kuxxi,
'Y/Amshi : Koyaushe yay yi kirana nit taho,
: Sai ya haxa mu da Naira sabuwa,
: Abarshi xan mai damma xan shibo,
: Xan Shaku da niyya nig ga nai.

Jagora : Ina na Mani ga Anne xan Bawa, x^2
'Y/Amshi : Mai katakka da aiki swahe duk. x^2

Jagora : Ya aje dawa ya aje gero, x^2
'Y/Amshi : Abarshi ya aje tarin gujiya. x^2

Jagora : Annen da ba ya da damman gero,
'Y/Amshi : Ba ni kixa mashi turayen dubu,
: Abarshi xan mai damma xan shibo,
: Xan Shaku da niyya nig ga nai.

Jagora : Ka ishe xan Anne na noma, x^2
'Y/Amshi : Azzahwari ta kama yai gida
: Halama bai iya kishin zucci ba. x^2

Jagora : Mu zo ganinka halalin 'Yar Gwaggo, x^2
'Y/Amshi : Masu dambe da aiki swahe duk. x^2
Jagora : Abarshi na xan Kura na Nomau, x^2
'Y/Amshi : Biyakka tahi biyas shaggun xiya. x^2

Jagora : Ya aje dawa ya aje gero,
'Y/Amshi : Abarshi ya aje tarin gujiya.

Jagora : Anne da ba shi da damman gero,
'Y/Amshi : Ba ni kixa masa turayen dubu,
: Abarshi xan mai damma xan shibo,
: Xan Shaku da niyya nig ga nai.

Jagora : Anne da ba shi da damman gero,
‘Y/Amshi : Ba ni kixa masa turaye qwarai,
: Abarshi xan mai damma xan shibo,
: Xan Shaku da niyya nig ga nai.

Jagora : Ina na Mani ga Anne xan Bawa, x²
‘Y/Amshi : Mai katakka da aiki swahe duk. x²

Jagora : Mu zo ganinka halalin ‘Yar Gwaggo, x²
‘Y/Amshi : Masu dambe da aiki swahe duk. x²

Jagora : Abarshi ya kashe canjin kuxxi,
‘Y/Amshi : Koyaushe yay yi kirana nit taho,
: Sai ya haxa mu da Naira sabuwa,
: Abarshi xan mai damma xan shibo,
: Xan Shaku da niyya nig ga nai.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa,
Mai Waqa : Sarkin Gobir Umaru[90]*,*
70. *Gindin Waqa : Niqatau na Jekada bajimin magajin gari,*
: Ummaru gam da ram bulgu wayayyen sarki.

Jagora : Giwa mai raba kaya baban Galadima, x²
'Y/Amshi : Baban Magajin gari mai sabon Birni. x²

Jagora : Ka zama lahiya na zagi, x²

[90] An Sami Wannan Rerawa ne a Kundin Xahiru, G. (1990: 105-107).

'Y/Amshi : Jikan Kilo Luna baban Bangu,
: Ubangijin Yari baban ‘yan kwana,
: Niqatau na Jekada bajimin magajin gari,
:Ummaru gam da ram bulgu wayayyen sarki. x^2

Jagora : Jikan Alhaji ya riqe ‘yan uba, x^2
'Y/Amshi : Ba kwamre da su na Jekadiya,
: Sarkin daga, x^2
: Niqatau na Jekada bajimin magajin gari,
:Ummaru gam da ram bulgu wayayyen sarki.

Jagora : Baban mai hwada Barmo, x^2
'Y/Amshi : Uban Ajiya hau lahiya,
: Xan Alu gatan mazaba, x^2
: Niqatau na Jekada bajimin magajin gari,
: Ummaru gam da ram bulgu wayayyen sarki.

Jagora : Wanda yaj ja ma sarki, x^2
'Y/Amshi : Ko Allah ya hana ja ma domin qarhi nai. x^2

Jagora : Haba Gobirawa ga Ummarun naku ya dawo,
'Y/Amshi : Ga Ummarun naku ya zo ya gode,
: Gidan nan da Gohe yab bar mai.

Jagora : Haba Gobirawa ga Ummarun naku ya dawo,
'Y/Amshi : Ga Ummarun naku ya zo ya buga,
: Tamburan nan da Gohe yab bar mai.
Jagora : Haba Gobirawa kun yi sake, x^2
'Y/Amshi : Kun bar zakara ya shige akurki. x^2

Jagora : Har ya cera ya hid da toro, x^2
'Y/Amshi : To ku yi anniya tun da tsawa,
: Ta yi tsawo. x^2

Jagora : Ku bar mishi akurki, x^2
'Y/Amshi : Shure mutum ya kai,
: Tun da gawa ta yi tsawo,
: Niqatau na Jekada bajimin magajin gari,
: Ummaru gam da ram bulgu wayayyen sarki. x^2

Jagora : Haba Gobirawa ga tsarinku ya zama kada, x^2
'Y/Amshi : Har ya aza qanquna sun miqe. x^2

Jagora : Yanzu hwaranta ta kai,
'Y/Amshi : In da goshi ya yi tsawo,
: Niqatau na Jekada bajimin magajin gari,
: Ummaru gam da ram bulgu wayayyen sarki.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,
Mai Waqa : Magajin Garin Sabon Birni,
Alhaji Magaji Tangaxi Tsibiri[91]*,*

71. *GindinWaqa : Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,*
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari.

Jagora : Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari,
'Y/ Amshi : Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,

[91] An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{54}$ $^1/_1$.

: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari.

Jagora : ‘Yan tsibiri sun yi agogo don hwaxin lokaci, x²
‘Y/Amshi : Tun da ya kasa ba a shawara sai da shi,
: Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari. x²

Jagora : Magaji jirgin zinariya da tsohin gaci, x²
‘Y/Amshi : Wanga jirgi ham mucciyar azurhwa garai, x²
: Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari.

Jagora : Shi wanga jirgi hay ya hi martaba hankali,
‘Y/Amshi : Rad da za a hito had da mu muna zakkowa,
: Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari.
Jagora : Ai wanga jirgi hay ya hi martaba hankali, x²
‘Y/Amshi : Rad da za a hito had da mu muna zakkowa, x²
: Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari.

Jagora : Ai dauri an Magajin gari na shinkinkimi, x³
‘Y/Amshi : Tun da an canza yanzu duniya ta mu ta, x³
: Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari.
Jagora : Ai yara wanga Magajin gari irin namu ne, x²
‘Y/Amshi : Mu da qilli wancan mai abun rashin hankali,
: Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari. x²

Jagora : Wanga gidan Alhaji ne da shi da Alhajiya, x²
‘Y/Amshi : Alhaji Xantsita taka azama ta isa,
: Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari.

Jagora : Magaji jirgin zinariya da tsohin gaci, x²
‘Y/Amshi : Wanga jirgi ham mucciyar azurhwa garai, x²
: Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari.

Jagora : ‘Yan tsibiri sun yi agogo don hwaxin lokaci, x^2
‘Y/Amshi : Tun da ya kasa ba a shawara sai da shi,
: Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari. x^2

Jagora : Gobirawa kun sha kunun baqaz zuciya, x^2
‘Y/Amshi : Don cikin duniya babu inda ba a san ku ba, x^2
: Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari.

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Xangaran Sabon Birni,
Alhaji Ibrahim Makoxa Xangara[92]*,*
72. *Gindin Waqa : Ibrahim Xanmakoxa rai nai yay haske,*
: Na zaka in gai da Xangaran Sabon Birni.

Jagora : Maraxi an yi Xangara, x^2
‘Y/Amshi : Kuma ga shi an naxa sabon Birni,
: Ina musu roqon Ubangiji kullum-kullum,
: Ibrahim Xanmakoxa rai nai yay haske,
: Na zaka in gai da Xangaran Sabon Birni. x^2

---

92 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{377}$ $^1/_2$.

Jagora : Bajinin Shi'itu, x²
: Abin da yas shira tun can hwarko,
'Y/Amshi : Hay yau bai saba qulle-qullen banza ba,
: Ibrahim Xanmakoxa rai nai yay haske,
: Na zaka in gai da Xangaran Sabon Birni. x²

Jagora : Ashe daka sai mata, x²
'Y/Amshi : Kashin bisasshe sai kura,
: Hawan doki sai Ba'auzine sai 'yan sarki,
: Ga mu muna kallon mai kixi ana kallon kura,
: Su Alhaji Maidaji yau ana kallon kallo,
: Ibrahim Xanmakoxa rai nai yay haske,
: Na zaka in gai da Xangaran Sabon Birni. x²

Jagora : Yara mi an ma'anad da za ku yin kallon-kallon, x²
'Y/Amshi : Mu ba mu gane ba tun da ba mu zama birni,
: Ibrahim Xanmakoxa rai nai yay haske,
: Na zaka in gai da Xangaran Sabon Birni. x²

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai waqa : Alhaji Idi Falalen Karo[93]*,*

73. *Gindin Waqa : A gaishe ka na Amadu,*
: Idi falalen karo.

Jagora : 'Yan samari a yo aniya, x²
'Y/Amshi : A dai taushe hakin dawa,
: A gaishe ka na Amadu,
: Idi falalen karo. x²

Jagora : A gishe ka Idi kan Daudu, x²
'Y/Amshi : Ba ya wargi da hwashin qasa,
: A gaishe ka na Amadu,

---

93 An Sami Wannan Rerawa a Kundin Gusau, S. M. (1983: 475)

: Idi falalen karo. x²

Jagora : ‘Yan samari a yom aniya, x²
‘Y/Amshi : A dai taushe hakin dawa,
: A gaishe ka na Amadu,
: Idi falalen karo. x²

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003)[94]*,*
74. *Gindin Waqa : Lahiya na Muhamman,*
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara.

Jagora : Sarki na Arzika xan mage, x²
: Barka nikai da gabata kullum,
‘Y/Amshi : Lahiya na Muhamman,
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara. x²

Jagora : Na yi roqo ga Allah, x³
‘Y/Amshi : Alhaji ya yi roqo wajen Rabbani, x³
: Lahiya na Muhamman,

---

94 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{1}/_{178}$ $^{1}/_{8}$.

: Sarki kak ka yarda da rainin tsara.

Jagora : Jangwarzo da yar roqi Allah, x^3
'Y/Amshi : Har yar roqi Annabi Mamman,
: Yac ce dum mazaje su koma mata,
: Lahiya na Muhamman,
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara. x^3

Jagora : Sarkin Arewa ka lelanta ni, x^2
'Y/Amshi : Kamam Mayaqi da Gauxe,
: Ka san duniya aka xaukag girma, x^2
: Lahiya na Muhamman,
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara.

Jagora : Duniya aka yawo, x^2
'Y/Amshi : Ka san Lahira ba a san yau ciza. x^2

Jagora : Ai da kihi da nama, x^2
'Y/Amshi : Ka san ba a ce masu xai na,
: Tun daw wurin biya aka bambantasu,
: Lahiya na Muhamman,
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara. x^2
Jagora : Kuma da jaki da doki,
'Y/Amshi : Ka san ba a ce masu xai na,
: Tun daw wurin biya aka bambantasu,
: Lahiya na Muhamman,
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara.

Jagora : Ai da jaki da doki,
'Y/Amshi : Ka san ba a ce masu xai na,
: Tun daw wurin biya aka bambantasu,
: Lahiya na Muhamman,
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara.

Jagora : Kuma da zarqi da zoro,
'Y/Amshi : Ka san ba a ce masu xai na,
: Tun daw wurin biya aka bambantasu,
: Lahiya na Muhamman,
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara.

Jagora : Gobirawa na Baciri, x3
'Y/Amshi : Ko can ba ku tsoron a kama,
: Don kau kunhi zaune da ku ba daxi,
: Lahiya na Muhamman,
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara. x3

Jagora : Na yi roqo ga Allah,
'Y/Amshi : Alhaji ya yi roqo wajen Rabbani,
: Lahiya na Muhamman,
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara.

Jagora : Jangwarzo da yar roqi Allah, x2
'Y/Amshi : Har yar roqi Annabi Mamman,
: Yac ce dum mazaje su koma mata,
: Lahiya na Muhamman,
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara. x2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gidan Rumji, Alhaji Kaso Sanda[95]*,*
75. *Gindin Waqa : Jikan goye Kaso xan Kaso,*
: Sarki xan Sanda mai duniya.

Jagora : Ai wada Allah ka yi ya gama,
'Y/Amshi : Allah ba ya yin shawara,
: Komi yat tashi yi nai ya kai.

Jagora : Du wada Allah ka yi ya gama,
'Y/Amshi : Shi Allah ba ya yin shawara,
: Komi yat tashi yi nai ya kai,
: Jikan goye Kaso xan Kaso,
: Sarki xan Sanda mai duniya.

---

95 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{1}$.

Jagora : Du wada Allah ka yi ya gama,
‘Y/Amshi : Shi Allah ba ya yin shawara,
: Komi yat tashi yi nai ya kai.

Jagora : Ko can haka nan duniya tay iya, x^2
‘Y/Amshi : In wasu sun kwan suna lahiya,
: Wasu ko sun tashi ba lahiya, x^2
: Jikan goye Kaso xan Kaso,
: Sarki xan Sanda mai duniya.

Jagora : Ga wasu can sun aje jikkuna, x^2
‘Y/Amshi : Wasu kau sun tashi ba ko kwabo. x^2

Jagora : Wasu sun yi dawaki suna riguna, x^2
‘Y/Amshi : Wasu kau sai xarma walki su kai, x^2
: Jikan goye Kaso xan Kaso,
: Sarki xan Sanda mai duniya.

Jagora : Mamakin Gobirawa nikai, x^2
‘Y/Amshi : Babari da yai riqon duniya,
: Matsayin sarki tamanin ya kai. x^2
Jagora : Nahwata da yai riqon duniya,
‘Y/Amshi : Matsayin sarki tamanin ya kai.
Jagora : Kuma Soba da yai riqon duniya,
‘Y/Amshi : Matsayin sarki tamanin ya kai.
Jagora : Mainasara da yai riqon duniya,
‘Y/Amshi : Matsayin sarki tamanin ya kai.
Jagora : Almu da yai riqon duniya,
‘Y/Amshi : Matsayin sarki tamanin ya kai.
Jagora : Gulbi da yai riqon duniya,
‘Y/Amshi : Matsayin sarki tamanin ya kai.
Jagora : Tumbulki da yai riqon duniya,
‘Y/Amshi : Matsayin sarki tamanin ya kai,
: Jikan goye Kaso xan Kaso,
: Sarki xan Sanda mai duniya.

Jagora : Ga mu muna tono muna rabkana, x^2
‘Y/Amshi : Sarkin kwaxayi bakwai nis sani,

: Ka rubuta had da sittin su kai, x^2
: Jikan goye Kaso xan Kaso,
: Sarki xan Sanda mai duniya.

Jagora : Allah shi ma tsari duniya, x^2
'Y/Amshi : Kuma dai ya yi ma tsari lahira,
: Don kau na san dai Musulmi kake, x^2
: Jikan goye Kaso xan Kaso,
: Sarki xan Sanda mai duniya.

Jagora : Baban Tsitau uban Kashe, x^2
'Y/Amshi : Xanbarno mai da qura ya kai, x^2
: Jikan goye Kaso xan Kaso,
: Sarki xan Sanda mai duniya.

Jagora : Sarki qwam ma ruwa na vwamnar hwari, x^2
'Y/Amshi : In sun bi ga qorama sun wuce,
: Mu kau Koyaushe kwaxi mu kai, x^2
: Jikan goye Kaso xan Kaso,
: Sarki xan Sanda mai duniya.

Jagora : Mu gode ma ta Malam ta Rimin Kwari, x^2
'Y/Amshi : Da zane tab ba mu domin Kaso. x^2

Jagora : Ga ta Malam Gobirawa hwaxa,
: 'Yan Kurawa da sun kai hwaxa,
'Y/Amshi : Rannan kau na yi kallon hwaxa,
: To, amma na tsaya na raba,
: In ba don ni ba da ta buga,
: Jikan goye Kaso xan Kaso,
: Sarki xan Sanda mai duniya.

Jagora : Ko can haka nan duniya tay iya, x^2
'Y/Amshi : In wasu sun kwan suna lahiya,
: Wasu ko sun tashi ba lahiya, x^2
: Jikan goye Kaso xan Kaso,

: Sarki xan Sanda mai duniya.

Jagora : Du wada Allah ka yi ya gama,
'Y/Amshi : Shi Allah ba ya yin shawara,
: Komi yat tashi yi nai ya kai,
: Jikan goye Kaso xan Kaso,
: Sarki xan Sanda mai duniya.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Muhammadu Xanqoqari[96]*,*

76. *Gindin Waqa : Sai mu taru mu yi roqon Allah,*
: Inda Alhaji Bakwai N.P.N.

Jagora : Ai sai mu yi roqon Allah, x^2
: Inda Alhaji Bakwai N.P.N,
'Y/Amshi : Sai mu taru mu yi roqon Allah,
: Inda Alhaji Bakwai N.P.N. x^2

Jagora : In ka ji an yi magana ta zaune, x^2
'Y/Amshi : Yanzu ba wata magana sai Legas. x^2
Jagora : To, kowa shi hanqure, Babari, x^3
'Y/Amshi : Da Gwamna sun yi magana ta zauna,
: Sai mu taru mu yi roqon Allah,
: Inda Alhaji Bakwai N.P.N. x^3

Jagora : Uban xan Jari kutunvun vauna, x^3
'Y/Amshi : Babu mai iya tare ma hanya,
: Sai mu taru mu yi roqon Allah,

---

96 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{75}$ $^1/_{10.}$

: Inda Alhaji Bakwai N.P.N. x^3

Jagora : Alheri shi kai mu Sabon Birni, x^3
'Y/Amshi : Tun da can aka shirawad duniya,
: Sai mu taru mu yi roqon Allah,
: Inda Alhaji Bakwai N.P.N. x^3

Jagora : Sabon Birni mu taru ga hwatana,
'Y/Amshi : Tun da masu hitina sun kasa,
: Sai mu taru mu yi roqon Allah,
: Inda Alhaji Bakwai N.P.N.

Jagora : Gobir babu sauran shairi,
'Y/Amshi : Tun da masu hitina sun qare
: Sai mu taru mu yi roqon Allah,
: Inda Alhaji Bakwai N.P.N.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Sarkin Gobir na Sabon,
Alhaji Abdulhamid (2003-)[97]

77. *Gindin Waqa : Ya kwan cikin shiri ya tashi tsaye,*
: Malam Balarabe Bunu xan Niqatau.

Jagora : Wallahi duniya ta ba ni tsoro, x^2
'Y/Amshi : Wata rana waxansu sui kuka da kansu, x^2
: Ya kwan cikin shiri ya tashi tsaye,
: Malam Balarabe Bunu xan Niqatau.

Jagora : Dogo xan Durumbu xan sarkin Musulmi, x^2
'Y/Amshi : Wani ya tara duniya ta tashi kai nai, x^2
: Ya kwan cikin shiri ya tashi tsaye,
: Malam Balarabe Bunu xan Niqatau.

Jagora : In ka kama salsalash Shawai da Jari, x^2

---

[97] Makaxa Maidaji Sabon Birni ya rera wannan waqa ne tun zamanin Alhaji Abdulhamid yana xan sarki. An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{75}$ $^1/_{12}$ - AL $^1/_{375}$ $^1/_6$.

‘Y/Amshi : Tarihin da nis sani shi zan hwaxa ma, x^2
: Ya kwan cikin shiri ya tashi tsaye,
: Malam Balarabe Bunu xan Niqatau.

Jagora : To, tun daq qasar Gubur han nan qasag ga, x^2
‘Y/Amshi : To, duk xan na Baciri ya san mu tare, x^2
: Ya kwan cikin shiri ya tashi tsaye,
: Malam Balarabe Bunu xan Niqatau.

Jagora : Mainasara da yai riqo ya gade sosai, x^2
‘Y/Amshi : Duk harkar da za shi yi sai ya hwaxa min. x^2
Jagora : Kuma da yai riqe Xantsara qasag ga, x^2
‘Y/Amshi : Duk harkar da za shi yi sai ya hwaxa mai. x^2
Jagora : Salihu ya riqe ni ga ni kwarai da gaske, x^2
‘Y/Amshi : Duk harkar da za shi yi sai ya hwaxa min. x^2
Jagora : Ummaru ya riqe ni ko ni babu xumi, x^2
‘Y/Amshi : Duk harkar da za shi yi sai ya hwaxa min. x^2
Jagora : Alhaji ya riqe ni ko ni babu xumi,
‘Y/Amshi : Duk harkar da za shi yi sai ya hwaxa min.
Jagora : Alhaji ya riqe ni ko ni babu xumi,
‘Y/Amshi : Duk harkar da za shi yi sai ya hwaxa min,
: Ya kwan cikin shiri ya tashi tsaye,
: Malam Balarabe Bunu xan Niqatau.

Jagora : Bana in kun aje ni ba ni zama qasag ga, x^2
‘Y/Amshi : Sai in sake gahwara in hau bisashe, x^2
: Ya kwan cikin shiri ya tashi tsaye,
: Malam Balarabe Bunu xan Niqatau.

Jagora : Dogo xan Durumbu xan sarkin Musulmi, x^2
‘Y/Amshi : Wani ya tara duniya ta tashi kai nai, x^2
: Ya kwan cikin shiri ya tashi tsaye,
: Malam Balarabe Bunu xan Niqatau.

Jagora : Ni dai wallahi duniya ta ba ni tsoro, x^2
‘Y/Amshi : Wata rana waxansu sui kuka da kansu, x^2
: Ya kwan cikin shiri ya tashi tsaye,
: Malam Balarabe Bunu xan Niqatau.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Xan Sarkin Gangara[98]*,*
Alhaji Isa Baraz Zaki,

78. *Gindin Waqa : Yai halin mazan jiya Isa maqi garaje,*
: Tun da yai kira Alhaji bai kahwat tsayawa.

Jagora : Can za ni Gangara, x^2
'Y/Amshi : Tun da garin Balarabe na,
: A gurin Balarabe,
: Ka san ai wurin zuwa na, x^2
: Yai halin mazan jiya Isa maqi garaje,
: Tun da yai kira Alhaji bai kahwat tsayawa.

Jagora : Don Allah Gobirawa, x^2
'Y/Amshi : Kowa ya kintsa kai nai,
: Don ku sani,
: Akwai wani zarto yana tahowa, x^2
: Yai halin mazan jiya Isa maqi garaje,
: Tun da yai kira Alhaji bai kahwat tsayawa.

Jagora : Duk xan Bagobiri, x^2

---

98 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{378}$ $^1/_9$.

‘Y/Amshi : In dai xan na Baciri na,
: Da ya bar batun hwaxa,
: Gwara ya kwana bai da komi, x^2
: Yai halin mazan jiya Isa maqi garaje,
: Tun da yai kira Alhaji bai kahwat tsayawa.

Jagora : Alhaji don ganin gero, x^2
‘Y/Amshi : Ba ni tsinka tambo,
: In don batun hwaxa,
: Ban ga batun ture-turenga, x^2
: Yai halin mazan jiya Isa maqi garaje,
: Tun da yai kira Alhaji bai kahwat tsayawa.

Jagora : In don mutum yana iko, x^2
‘Y/Amshi : Ba ya ba mu kyauta,
: Ka kama shawara,
: Gwara mu kwan gidan mutane. x^2

Jagora : Na san gidan Bahaushe,
‘Y/Amshi : Na san gidan mutane,
: Gari-gari muke,
: Babu garin da ban sani ba.
Jagora : Can za ni gangara, x^2
‘Y/Amshi : Tun da garin Balarabe na,
: A gurin Balarabe,
: Ka san ai wurin zuwa na, x^2
: Yai halin mazan jiya Isa maqi garaje,
: Tun da yai kira Alhaji bai kahwat tsayawa.

Jagora : Isah da kai da Isah, x^2
‘Y/Amshi : Kun zam kamat tawaye,
: Ya yo kamah Hassan,
: Shi ko ya yo kama da yaro, x^2
: Yai halin mazan jiya Isa maqi garaje,
: Tun da yai kira Alhaji bai kahwat tsayawa.

Jagora : Ni dai ina biyax xan sarki, x^3
‘Y/Amshi : Shi ko yana gudu na
: Ku ce ya bar gudu,

: Ba hakan niy yi xammara ba. x^3

Jagora : Mata tai tana hwaxi, x^2
‘Y/Amshi : Wataqil wane mai kixin ga,
: Xa nai shi na hwaxin,
: Baba shige cikin itace. x^2

Jagora : Haba wane don gani na, x^2
‘Y/Amshi : Bari bar shiga itace akwai kububuwa,
: Mai zane tana kashe ka, x^2
: Yai halin mazan jiya Isa maqi garaje,
: Tun da yai kira Alhaji bai kahwat tsayawa.

RATAYE NA BIYU
MATANIN WASU WAQOQIN MAKAXA
SA'IDU MAIDAJI SABON BIRNI

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Waqar Noma ta Arzika[99]*,*
01. *Gindin Waqa : Sarki yai abin daka ya huta,*
: Zaki xan Abubakar xan Buda.

Jagora : Baba mijin Shibo mijin Maryama,
'Y/Amshi : Giwa maganin itacen daji,
: Sarki yai abin daka ya huta,
: Zaki xan Abubakar xan Buda.

Jagora : Ah Baba mijin Shibo mijin Maryama,
'Y/Amshi : Giwa maganin itacen daji.

Jagora : Arzika jikan Salau magajin Sanda, x^2
: Zaki mai kasam ma kai nainama, x^2
'Y/Amshi : Sarki yai abin daka ya huta,
: Zaki xan Abubakar xan Buda.

Jagora : Ina Arzika xan Imamu bawan Alllah, x^2
: Bai ci amanar gida ba balle daji, x^2
'Y/Amshi : Sarki yai abin daka ya huta,
: Zaki xan Abubakar xan Buda.

Jagora : Kullum fata nikai wurin Jabbaru,
: Don albarkacin Sabilillahi,
: Kuma albarkacin mutanen Makka,
: Ka sallace dubu kahin jinmu,
'Y/Amshi : Sarki yai abin daka ya huta,
: Zaki xan Abubakar xan Buda.
Jagora : Arzika tun zamanin kana xan yaro, x^2

---

[99] An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{50}$ $^1/_2$.

: Hak kak kai kana cikin qarninka,
: To hay yau ba ka raina matar wani ba,
‘Y/Amshi : Sarki yai abin daka ya huta,
: Zaki xan Abubakar xan Buda. x^2

Jagora : Hwaxa ma samarin ga masu son matanmu,
: Hwaxa musu Alhaji mai kixi ya gane,
‘Y/Amshi : Sarki yai abin daka ya huta,
: Zaki xan Abubakar xan Buda.

Jagora : Arzika jikan Salau magajin Sanda,
: Zaki mai kasam ma kainai nama.
‘Y/Amshi : Sarki yai abin daka ya huta,
: Zaki xan Abubakar xan Buda.

Jagora : To ku yi min godiya ga horon Buda,
: Buda rigar da ni hwaxi ya ba ni,
‘Y/Amshi : Sarki yai abin daka ya huta,
: Zaki xan Abubakar xan Buda.

Jagora : To, kai Ali kai da Salisu Mamman,
: To, ni ga ni na yi baqon doki,
: Amma ba ku ba ni abin da zan ci sai ba,
‘Y/Amshi : Sarki yai abin daka ya huta,
: Zaki xan Abubakar xan Buda.

Jagora : Ina Arzika xan Imamu bawan Alllah,
‘Y/Amshi : Bai ci amanar gida ba balle daji.

Jagora : To, na gode ma Argiji, na gode, x^2
‘Y/Amshi : Don ga binjimin zane ta ba da. x^2
Jagora : Godiya mai yi Rabbana yab ban ‘yan Makka,
: Ga kuxxin sayen zane yab ban.
Jagora : Godiya mai yi Rabbana yab ban ‘yan Makka,
: Ga kuxxin sayen zane yab ban.
‘Y/Amshi : Sarki yai abin daka ya huta,
: Zaki xan Abubakar xan Buda.
Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,

Alhaji UmmaruNa-Allah (1957-1966),

02. *Gindin Waqa : Binu xan baraz Zaki Xanbawa*[100]*,*
: Jikan Kilo gwamron giwa.

Jagora : Binu xan baraz zaki Xanbawa,
'Y/Amshi : Jikan Kilo gwamron giwa,
: Na Malam gwanin daga,
: Na-Allah jikan hillani xan Musa na Malam.

Jagora : Shin Ummaru ne ko Yakubu Daudu, x^2
'Y/Amshi : Ko ko Kada ne yad dawo. x^2

Jagora : Shin Ummaru ne ko Yakubu Daudu,
'Y/Amshi : Ko ko Kada ne yad dawo,
: Na Malam gwanin daga,
: Na-Allah jikan hillani xan Musa na Malam.

Jagora : Kakanka ya mulki Gobir, x^2
'Y/Amshi : Sai ya mulke mulkin,
: Da kakanai yay yi. x^2

Jagora : Dur ran da na Yakuba yai sarki,
'Y/Amshi : Da mu za a shan kalwa birni,
: Na Malam gwanin daga,
: Na-Allah jikan hillani xan Musa na Malam.

Jagora : Dur ran da na Yakubu yay sarki,
'Y/Amshi : Da mu za a shan kalwa birni.
Jagora : Da mu za a shan kalwa,
'Y/Amshi : Ran nan da mu za a tarboso ne birni.
Jagora : To! Da mu za a shan kalwa,
'Y/Amshi : Ran nan da mu za a tarboso ne birni.
Jagora : Mu mulke waxan birni, x^2
'Y/Amshi : Mu biya mu mulke mutanen Kurawa. x^2
Jagora : Mu mulke waxan Tara, x^2

---

[100] Wannan rerawa an same ta a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsunan Nijeriya da Al'adu, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. A Faifai mai lamba AL $^1/_{147}$ $^1/_6$.

‘Y/Amshi : Mu biya mu mulke mutanen Gatawa. x^2
Jagora : Gangara da xam Maliki, x^2
‘Y/Amshi : Kai ad da mulkinsu,
: Ba wani bayan kai,
: Na Malam gwanin daga,
: Na-Allah jikan hillani xan Musa na Malam. x^2

Jagora : To, ina masu son sarki, x^2
‘Y/Amshi : In anka shaqa mijina as sarki. x^2

Jagora : Ga wani na jiran sarki,
‘Y/Amshi : Daxa sai shi koma jiran Sarkin Karma,
: Na Malam gwanin daga,
: Na-Allah jikan hillani xan Musa na Malam.

Jagora : Mu sai ma takobi da hamilo,
‘Y/Amshi : Da taggo da wandon dirbanci,
: Na Malam gwanin daga,
: Na-Allah jikan hillani xan Musa na Malam.

Jagora : Ya muradi kake Musa,
‘Y/Amshi : Allah ya yi ma xaukakar Sarki Shawai,
Jagora : Ya muradi kake Musa,
‘Y/Amshi : Allah ya yi ma xaukakar Sarki Shawai,
: Na Malam gwanin daga,
: Na-Allah jikan hillani xan Musa na Malam.

Jagora : Shin Ummaru ne ko Yakubu Daudu,
‘Y/Amshi : Ko ko Kada ne yad dawo,
Jagora : Shin Ummaru ne ko Yakubu Daudu,
‘Y/Amshi : Ko ko Kada ne yad dawo,
: Na Malam gwanin daga,
: Na Allah jikan hillani xan Musa na Malam.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa,
Mai Waqa : Malam Hassan Xansanda,

03. *Gindin Waqa : Qi garaje uban Meli bai xauki wargi ba*[101]*,*
: Dole in yaba Malam Hassan mai halin girma.

Jagora : A gai da Sale Xansanda gasurgumin icce, x^2
'Y/ Amshi : Wanda ya hana shegantaka nan qasar Tara,
: Qi garaje uban Meli bai xauki wargi ba,
: Dole in yaba Malam Hassan mai halin girma. x^2

Jagora : Ga shi giwa na saraki ya dankwashe gaba,
: Na Umma ruwan wanke dartsa Uban Makau,
'Y/ Amshi : Ga Uban Sule ya mai da kora na xan mantai,
: Qi garaje uban Meli bai xauki wargi ba,
: Dole in yaba Malam Hassan mai halin girma.

Jagora : Lalle ashe harkar malami na da ban da tsoro,
: Ce ma 'yan makaranta su bar ja da Xansanda,
'Y/ Amshi : Yanzu ya wuce harkarsu ba za su immai ba,
: Qi garaje uban Meli bai xauki wargi ba,
: Dole in yaba Malam Hassan mai halin girma.

Jagora : Malami mai kyauta kama tai Uban Makau,
: Sai Malam Sidi sai malamin Tsadau,
: Sai Malam Habaru wancan na Samaru,
'Y/ Amshi : Yaushe niz zaka ni ma yana ba ni in na zo,
: Qi garaje uban Meli bai xauki wargi ba,
: Dole in yaba Malam Hassan mai halin girma.

Jagora : Ka gani ba kukan Uba nai ma Allah ba,
: Ni ba kukan Uwa nai ma Allah ba,
Jagora : Don mutuwa ba ni tsoran ta sha raina,

[101] An sami wannan rerawa ne a Kundin Fasahar Baka. Gusau, S. M. (ed), 2004.

: Kwancin qabari shi xai ka ban tsoro,
: Kana kwance cikin duhu ba ka motsawa,
: In ka yi gaba bango ya tarbe ka,
: In ka yi yamma bango ya tarbe ka,
: Ba ka tashi tsaye sai itace shi kwabre ka,
: Kuma kana so ka ga naka ba a ba ka hanya ba,
‘Y/ Amshi : Allah ka yo mana halin zuwa mui zaman kewa,
: Qi garaje uban Meli bai xauki wargi ba,
: Dole in yaba Malam Hassan mai halin girma.

Jagora : Marafa na gane duniya zamanin yanzu,
: In zama yai daxi mutane ka vata shi,
: Tun da ban cuci mutun ba kar ya cuta ni,
‘Y/ Amshi : In mutum ya cuce ni Allah ya rama min,
: Tun da na tsare Allah yana yo min komi,
: Qi garaje uban Meli bai xauki wargi ba,
: Dole in yaba Malam Hassan mai halin girma.

Jagora : A gai da Sale Xansanda gunsungumin icce,
‘Y/ Amshi : Wanda ya hana shegantaka nan qasar Tara
: Qi garaje uban Meli bai xauki wargi ba,
: Dole in yaba Malam Hassan mai halin girma.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Zazzau,
Alhaji Shehu Idris (1975-)

04. *Gindin Waqa : Balaraben Sarki*[102]*,*
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Aikinka ya yi kyau sarkin Zazzau, x^2
'Y/Amshi : Balaraben Sarki. x^2

Jagora : Sarki na Alqali,
'Y/Amshi : Ya hanqure da masu yi mai hwada.
Jagora : Sarki na Alqali,
'Y/Amshi : Ya hanqure da masu yi mai hwada.
: Balaraben Sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Mijin Hadiza mijin Mariya dabaru yak kama,
'Y/Amshi : Sarki mijin Binta da Binta,
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.
Jagora : Kai mijin Hadiza mijin Mariya dabaru yak kama,
'Y/Amshi : Sarki mijin Binta da Mariya,
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Ina gida ina hutawa, x^2
'Y/Amshi : Sai nig ga saqon Sanqira. x^2
Jagora : Sai nic ce,
'Y/ Amshi : In Allah ya nuhwa ina kwana Zazzau.
Jagora : Sai nic ce,
'Y/ Amshi : In Allah ya nuhwa ina kwana Zazzau,
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Wanda yat taho Zazzau,
'Y/Amshi : Alhaji bai tsayawa Rawayya.
Jagora : Tun da na taho Zazzau,
'Y/Amshi : Alhaji ban tsayawa Rawayya.

---

102 Wannan rerawa an same ta a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsunan Nijeriya da Al'adu, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. A Faifai mai lamba AL $^1/_{374}$ $^1/_2$.

Jagora : Tun da na taho Zazzau,
'Y/Amshi : Alhaji ban tsayawa Rawayya,
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Kulkin bugun kura, x^2
'Y/Amshi : In anka sa takobi an vata. x^2

Jagora : Abin kixin sarki,
'Y/Amshi : Kai ba abin kixan ‘yan mata ba.
Jagora : E abin kixin sarki,
'Y/Amshi : Kai ba abin kixan ‘yan mata ba,
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Sarki na Alqali,
'Y/Amshi : Ya hanqure da masu yi mai hwada.
Jagora : Sarki na Alqali,
'Y/Amshi : Ya hanqure da masu yi mai hwada,
: Balaraben Sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Shehu Mani,
'Y/Amshi : Wada yan nuhwa ga rainai ya samu,
: Tun da Allah ya ba shi martabar Sarki Sambo,
: Balaraben Sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Shehu Mani, x^2
'Y/Amshi : Wada yan nuhwa ga rainai ya samu,
: Tun da Allah ya ba shi martabar Sarki Sambo, x^2
: Balaraben Sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Sarki na Alqali,
'Y/Amshi : Ya hanqure da masu yi mai hwada,
Jagora : Sarki na Alqali,
'Y/Amshi : Ya hanqure da masu yi mai hwada,
: Balaraben Sarki,

: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Jekadiyar Zariya, x^3
'Y/Amshi : Ba ta zaqe da bakin sarki ba, x^3
: Balaraben Sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Wannan Jekadiya, x^2
'Y/Amshi : Kowaz zaka sannu ta xau lamba,
: Balaraben Sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau. x^2

Jagora : Wannan Bagobira, x^3
'Y/Amshi : Wataqil ko cikin irin ‘yar gwarzo ta,
: Balaraben Sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau. x^3

Jagora : Ina gida ina hutawa, x^2
'Y/Amshi : Sai nig ga saqon Sanqira, x^2
Jagora : Sai nic ce,
‘Y/ Amshi : In Allah ya nuhwa ina kwana Zazzau.

Jagora : Sai nic ce,
‘Y/ Amshi : In Allah ya nuhwa ina kwana Zazzau,
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Tun da na taho Zazzau, x^2
'Y/Amshi : Alhaji bai tsayawa Rawayya,
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau. x^2

Jagora : Mijin Hadiza mijin Mariya dabaru yak kama,
'Y/Amshi : Sarki mijin Binta da Binta ya yi kwaru,
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Ba mamaki, x^2

: Uban zagi ba mamaki,
'Y/Amshi : Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau. x^2

Jagora : Sarkin Zazzau, x^2
: Uban zagi ba mamaki,
'Y/Amshi : Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau. x^2

Jagora : Sarki na Alqali, x^3
'Y/Amshi : Ya hanqure da masu yi mai hwada,
: Balaraben Sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau. x^3

Jagora : Kulkin bugun kura, x^2
'Y/Amshi : In anka sa takobi an vata. x^2

Jagora : Abin kixin sarki,
'Y/Amshi : Kai ba abin kixan ‘yan mata ba.

Jagora : E abin kixin sarki,
'Y/Amshi : Kai ba abin kixan ‘yan mata ba,
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : To, Shehu Mani, x^3
'Y/Amshi : Wada yan nuhwa ga rainai ya samu,
: Tun da Allah ya ba shi martabar Sarki Sambo. x^3

Jagora : To, hwaxa ma mai wargi, x^2
'Y/Amshi : Ko can da bai san wargi ba. x^2

Jagora : Shi ba ya son wargi, x^2
'Y/Amshi : Kuma Shehu ba ya son 'yan kamanci. x^2
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Ba mamaki,
: Uban zagi ba mamaki, x^2
'Y/Amshi : Balaraben sarki,

: Aikinka ya yi kyau Sarki Zazzau. x^2

Jagora : Sarkin Zazzau,
: Uban zagi ba mamaki, x^2
'Y/Amshi : Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau. x^2

Jagora : Sarki na Alqali, x^3
'Y/Amshi : Ya hanqure da masu yi mai hwada,
: Balaraben Sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau. x^3

Jagora : Sarkin uban Majidaxi,
'Y/Amshi : Barka da kai da kawon zamunna , x^2
: Balaraben Sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.
Jagora : Sarkin uban Majidaxi, x^2
'Y/Amshi : Barka da kai da kawon zamunna. x^2
Jagora : Sarkin uban Majidaxi, x^2
'Y/Amshi : Barka da kai da kawon zamunna ,
: Balaraben Sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau. x^2

Jagora : To, Shehu Mani, x^3
'Y/Amshi : Wada yan nuhwa ga rainai ya samu,
: Tun da Allah ya ba shi martabar Sarki Sambo, x^3
Jagora : Balaraben Sarki,
'Y/ Amshi : Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa,
Mai Waqa : Sarkin Zazzau, Alhaji Shehu Idris (1975-)
Gindin Waqa : Balaraben Sarki[103]*,*
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.

Jagora : Abdulkarimu ya dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Idrisu ya dawo,

[103] An sami wannan rerawa ne a littafin *Diwanin Waqoqin Baka.* Gusau, S.M. 2009: 197-203.

'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Yamusa ya dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Sambo ya dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Jafaru ya dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Kwasau ne yad dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Aminu ya dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Ga Sidi ya dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Ni ban zuwa gulbi,
'Y/Amshi : Alhaji bai zuwa wanka tafki.
Jagora : Ba wanda zai yi mai wargi,
'Y/Amshi : Ko can Shehu bai san wargi ba.
Jagora : Abubakar da yad dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Kuma Abdu ya dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Xalhatu ya dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Ibrahim ya dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Halidu ya dawo,
'Y/Amshi : Kullum ana buga mai tamburra,
Jagora : Zariya wanda yai,
'Y/Amshi : Wauta Wawa na fashe mai qwaryar kai.
Jagora : Wanda bai zuwa gulbi, x^2
'Y/Amshi : Alhaji ban zuwa wanka tafki, x^2
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.
Jagora : Ni ban kixin sarki, x^2
'Y/Amshi : Sai na ji wanda kainai yak qosa. x^2

Jagora : Ai ku tattaro ku ga, x^2
'Y/Amshi : Kaya waxanda mai girma yab ban,
: Kun gani kayan hwan xari bakwai,
: Sarkin yab ban. x^2
Jagora : Ga riguna tsadaddi iri-iri, x^2
'Y/Amshi : Waxanda sarki yab ban,
: Kuma had da alkyabbu,

: Kala biyu yab ban. x^2

Jagora : Sarki uban Madauci ,
'Y/Amshi : Ina so ka ban ni in dawo Zazzau.

Jagora : Inna uban Majidaxi,
'Y/Amshi : Sarki ubangijin Sarkin hwada.
Jagora : Sarki na Alqali, x^2
'Y/Amshi : Ya hanqure da masu yi mai hwada. x^2

Jagora : Sarkin Zazzau uban na Jika na nan, x^2
'Y/Amshi : Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau. x^2

Jagora : Shehu Mani,
'Y/Amshi : Wada yab bixa ga rainai ya samu,
: Tun da Allah ya ba shi martabar Sarki Sambo.

Jagora : Sarki na Alqali,
'Y/Amshi : Ya hanqure da masu yi mai hwada.

Jagora : To hwaxa ma mai wargi,
'Y/Amshi : Wawa yana yi mai bulala.

Jagora : Shi ba ya son wargi,
'Y/Amshi : Shehu ba ya son 'yan kamanci.

Jagora : Ina gida ina hutawa,
: Sai nig ga saqon Sanqira,
'Y/Amshi : Sai nic ce,
: In Allah ya nuhwa ina kwana Zazzau.

Jagora : Wanda yat taho Zazzau, x^2
'Y/Amshi : Alhaji bai tsayawa Rawayya. x^2

Jagora : Kulkin bugun kura,
'Y/Amshi : In anka sa takobi an vata.

Jagora : Na ce Jakadiyar Zazzau, x^2
'Y/Amshi : Haw wajen qasam Masar ta xau lamba. x^2

Jagora : Taushi abin kixin sarki, x^2
'Y/Amshi : Bai zan abin kixin 'yan mata ba. x^2

Jagora : Shata da yay yi ma waqa,
'Y/Amshi : Ya gama da roqon Jabbaru.
Jagora : Qwairo da yay yi ma waqa,
'Y/Amshi : Ya gama da roqon Jabbaru.
Jagora : Xangiwa da yay yi ma waqa,
'Y/Amshi : Ya gama da roqon Jabbaru.
Jagora : Xan'anace da yay yi ma waqa,
'Y/Amshi : Ya gama da roqon Jabbaru.
Jagora : Sa'idu ya yi ma waqa,
'Y/Amshi : Ya gama da roqon Jabbaru.
Jagora : Ko ni ina hwata, x^2
'Y/Amshi : Allah ya wa uwayenai rahama. x^2

Jagora : Shi ba ya son wargi,
'Y/Amshi : Kuma Shehu ba ya son 'yan kamanci.

Jagora : Zariya wanda yay yi wargi,
'Y/Amshi : Wawa na fashe mai qwaryar kai.

Jagora : Xan'iya uban Suliki, x^2
'Y/Amshi : Maganin marassa imani. x^2

Jagora : Ina gida ina hutawa, x^2
'Y/Amshi : Sai nig ga baqon Sanqira,
: Sai nic ce, in Allah ya nuhwa,
: Ina kwana Zazzau. x^2

Jagora : Wanda yat taho Zazzau,
'Y/Amshi : Alhaji bai tsayawa Rawayya.

Jagora : Uban Majidaxi,
'Y/Amshi : Sarki Ubangijin Sarkin Hwada,
: Ubangijin Shantali,

: Koyaushe ka ishe mai ya shirya.

Jagora : Mijin Hadiza mijin Mariya,
'Y/Amshi : Sarki mijin Binta da Binta,
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.
Jagora : Sarkin Zazzau uban Zagi ba mamaki, x^3
'Y/Amshi : Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau. x^3

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ummaru xan Salihu (1957-1966),

05. *Gindin Waqa : Na Ali xan Bajini,* [104]
: Jikan Shekara ka gama lahiya.

Jagora : Na Ali xan Bajini,
: Jikan Shekara ka gama lahiya,
'Y/Amshi : Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.

---

[104] Wannan rerawa an same ta a Xakin Tattalin Fasahar Baka da ke Sashen Harsunan Nijeriya da na Afirika, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. A faifai mai lamba AL $^0/_{50}$ $^1/_2$.

Jagora : Bunu uban Shamaki, x^2
'Y/Amshi : Xan Bawa uban Jekada kake Yakuba. x^2

Jagora : Na Ali jikan Kaso,
'Y/Amshi : Jikan Alhaji jikan Iyad duniya.
Jagora : Na Ali jikan Kaso,
'Y/Amshi : Jikan Alhaji jikan Iyad duniya,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.

Jagora : Abin da an nesa ya zaka kusa, x^2
'Y/Amshi : Taho daxa qara gusawa mukai. x^2

Jagora : Dag Gangara za mu Kurawa,
'Y/Amshi : Dac can a ba mu riqon dudduka,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.

Jagora : Dag Gangara za mu Kurawa,
'Y/Amshi : Dac can a ba mu riqon dudduka.

Jagora : Mu munka hwara zuwa birni,
'Y/Amshi : Dum masu yad da qahwa sun bari.

Jagora : Ummaru mu munka hwara zuwa birni,
'Y/Amshi : Dum masu yad da qahwa sun bari,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.

Jagora : Yara sun zaka Sabon Birni,
'Y/Amshi : Tun da an ce Kada yay yi shi,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.

Jagora : Sarki ka ja da Kada,
'Y/Amshi : In sun ka ga Sanda magajin Kada.
Jagora : Bunu ka ja da Kada,
'Y/Amshi : In sun ka ga Sanda magajin Kada,

: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.

Jagora : Duk inda xan Bawa ya zamo sarki, x^2
'Y/Amshi : Duk da mu za mu cin duniya,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau. x^2

Jagora : Mu munka hwara zuwa birni, x^2
'Y/Amshi : Dum masu yad da qahwa sun bari. x^2

Jagora : Ah! Gangara za ka ban, x^2
'Y/Amshi : Ko Gatawa ka ba mu,
: Riqe wa muke. x^2

Jagora : Sai dai ka ba ni Maigarin gona,
'Y/Amshi : Bayan baqar wahala xai yakai,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.

Jagora : Kai dai ka ba ni Maigarin gona,
'Y/Amshi : Bayan baqar wahala xai yakai.

Jagora : Kuma kak ka ba ni riqon Tara,
'Y/Amshi : Tun da na ga ba su barin shexana,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.

Jagora : Kuma kak ka ba ni riqon Tara,
'Y/Amshi : Tun da na ga ba su barin shexana.
Jagora : Kuma kak ka ba ni riqon Tara,
'Y/Amshi : Tun da na ga ba su barin shexana,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.

Jagora : Halo halin Ummaru, x^3
'Y/Amshi : In ka ji ana halin la'ada ya tsaya. x^3

Jagora : Ai na ce ran da duk ka tsaya,
'Y/Amshi : Rannan kowa ka mulki ajewa yakai,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.

Jagora : Ran da duk ka tsaya,
'Y/Amshi : Rannan kowa ka mulki ajewa yakai.

Jagora : Xan Bawa ya yi riqo, x^2
'Y/Amshi : Sai mun sha gobiya mu yi babban ciki,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau. x^2

Jagora : Uban Gada uban Gandu, x^2
'Y/Amshi : Xan Gamana mai baza mai dame. x^2
Jagora : Allah ya ba mu sa'a, x^2
'Y/Amshi : Wata rana had da gandun gamewa mukai, x^2
Jagora : Allah shi ba mu sa'a,
'Y/Amshi : Wata rana had da gandun gamewa mukai.
Jagora : Allah shi ba mu sa'a,
'Y/Amshi : Wata rana had da gandun gamewa mukai,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.
Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa
Ubangida : Sarkin Gobir Sabon Birni,
Muhammadu Bawa (1975 - 2003)[105],

6. *Gindin Waqa : Kai ab bahagon gulbi,*
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Na Garkuwa bajinin Sarkin Dogarrai na Galadima,
'Y/Amshi : Gwarzon Ajiya Sarki uban Isihu uban Garba,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,

---

105 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{50}$ $^1/_7$.

: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Ai na Garkuwa bajinin Sarkin Dogarrai na Galadima,
'Y/Amshi : Gwarzon Ajiya Sarki uban Isihu uban Garba,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Alhaji sarkin hwadamar kanwa, x^2
'Y/Amshi : Mai kwana tsaye ko yaushe. x^2
Jagora : Alhaji sarkin hwadamar kanwa,
'Y/Amshi : Mai kwana tsaye ko yaushe,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : To, sai an yi kadankarma, x^2
'Y/Amshi : A san babba a san yaro,
: Kuma sai an yi karom batta,
: A san wane a san wane. x^2
Jagora : Ai ina da Uba Sulxanin Gobir,
‘Y/Amshi : Wanda ka hisshe ni,
: Ni dai ba ni gudun hitinar Gobir,
: Duw wada tat tashi,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.
Jagora : Ai ina da Uba Sulxanin Gobir,
‘Y/Amshi : Wanda ka hisshe ni,
: Ni dai ba ni gudun hitinar Gobir,
: Duw wada tat tashi.

Jagora : Ga ni ina son harkar zambo,
‘Y/Amshi : Amma na zama mai geme,
: Kowa yaz zama mai geme,
: Na dama shi yi shexanci,

: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Ga ni ina son harkar zambo,
‘Y/Amshi : Amma na zama mai geme,
: Kowa yaz zama mai geme,
: Na dama shi yi shexanci.

Jagora : Cikin masu biyas sarki,
‘Y/Amshi : Wasu sun hwara munahicci,
: Bari kowa ka munahicci,
: Hwaxa mai da akwai Allah,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Ai cikin masu biyas sarki,
‘Y/Amshi : Wasu sun hwara munahicci,
: Bari kowa ka munahicci,
: Hwaxa mai da akwai Allah,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : An ce wane shina hauka,
‘Y/Amshi : Ni ban san shi da hauka ba,
: Kuma ban san shi da hauka ba,
: Sai ya katse abin xarmi,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.
Jagora : An ce wane shina hauka,
‘Y/Amshi : Ni ban san shi da hauka ba,
: Kuma ban san shi da hauka ba,
: Sai ya katse abin xarmi.

Jagora : Jiya can nij ji mutane, x^3
: Na cewa wane hawa'i ne,
'Y/Amshi : Ko mu mun ji mutane ,
: Na cewa wane tavavve na, x^3
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Shi wargi da hawa'i,
'Y/Amshi : Ya xara wargi da bugun buta,
: In sun tashi rashin kunyan nan,
: In sun gamu dux xai na,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Shi wargi da hawa'i,
'Y/Amshi : Ya xara wargi da bugun buta,
: In sun tashi rashin kunyan nan,
: In sun gamu dux xai na.
Jagora : Ai wargi da hawa'i,
'Y/Amshi : Ya xara wargi da bugun buta,
: In sun tashi rashin kunyan nan,
: In sun gamu dux xai na,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Hawa'i da irin buta,
: Ai na ce muku dux xai na,
'Y/Amshi : Ai had da mashayin kansu,
: Shi ma la'ananne na,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.
Jagora : Da Hawa'i da irin buta, x^2
: Ai na ce muku dux xai na,

‘Y/Amshi : Ai had da mashayin kansu,
: Shi ma la’ananne na, x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : To, Inna qaunas sarki, x^2
‘Y/Amshi : Ta maishe ni kamax xan ta,
: Ko babu kixi,
: Sai ta ba ni abin goro. x^2
Jagora : To, Garkuwa xan Gardaye, x^2
‘Y/Amshi : A gaishe ka a gaishe ka,
: Mu yi hwata ya daxe duniya,
: Ya zam ba mu abin Allah, x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.
Jagora : To, Garkuwa in na zaka gaisai,
‘Y/Amshi : Sai yay yo min dumbulka,
: Da ya diba idanuna,
: Ya san wani abu yak kai ni,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.
Jagora : To, Garkuwa in na zaka gaisai,
‘Y/Amshi : Sai yay yo min dumbulka,
: Da ya diba idanu na,
: Ya san wani abu yak kai ni.

Jagora : To, Inna xiyas Sardauna,
‘Y/Amshi : Giwa Inna Bahillata,
: In ta kama tila min kaya,
: Sai na gaji na ratse,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,

: Uban Bunu da Baraz Zaki.
Jagora : To, Inna xiyas Sardauna,
‘Y/Amshi : Giwa Inna Bahillata,
: In ta kama tila min kaya,
: Sai na gaji na ratse.

Jagora : Ai na Garkuwa bajinin Sarkin Dogarrai na Galadima,
'Y/Amshi : Gwarzon Ajiya Sarki uban Isihu uban Garba.

Jagora : Alhaji sarkin hwadamar kanwa, x^2
'Y/Amshi : Mai kwana tsaye ko yaushe. x^2
Jagora : Alhaji sarkin hwadamar kanwa,
'Y/Amshi : Mai kwana tsaye ko yaushe,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Gohe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.
Jagora : Gauxe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.
Jagora : Tambai ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.
Jagora : Yakuba ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.
Jagora : Ibrahim ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.
Jagora : Balarabe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi
Jagora : Jadi ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.
Jagora : Jari Kada ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.
Jagora : Shawai ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.
Jagora : Salihu ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.
Jagora : Ummaru ya buga tamburra,

'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : ‘Yan Gatawa da Yakubawa,
'Y/Amshi : Kowane an sa shi ga tarihi,
: Haba sarki riqe tarihin ga,
: Da kowa ka bixa jiddun,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Gamkawa da Bacirawa,
‘Y/Amshi : Kowane an sa shi ga tarihi,
: Haba Sarki riqe tarihin ga,
: Da kowa ka bixa jiddun.
Jagora : Haba sarki riqe tarihin ga,
‘Y/Amshi : Da kowa ka bixa jiddun.

Jagora : Kai kag gane mahwarinai,
‘Y/Amshi : Kuma kai ka san wada yaq qare,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

agora : To, na san tahiyag giwa,
: Kuma na san tahiyaz zaki,
: Na san tahiyaj jaki,
: Kuma na san tahiyad doki,
: Na san maganar mata,
: Kuma na san maganar qato,
: Kowas san maganar matam,
: Bori babu kamar Inna,
'Y/Amshi : Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : To, na san tahiyag giwa,
: Kuma na san tahiyaz zaki,

: Na san tahiyaj jaki,
: Kuma na san tahiyad doki,
: Na san maganar Buzu,
: Kuma na san ta Bahillace,
: Na san maganar mata,
: Kuma na san maganar qato,
: Kowas san maganar matam,
: Bori babu kamar Inna,
'Y/Amshi : Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa
Ubangida : Sarkin Gobir Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Bawa (1975 - 2003)
Gindin Waqa : Kai ab bahagon gulbi,[106]
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Na Garkuwa bajinin Sarkin Dogarrai na Galadima,
'Y/Amshi : Gwarzon Ajiya Sarki uban Isihu uban Garba,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Ai na Garkuwa bajinin Sarkin Dogarrai na Galadima,
'Y/Amshi : Gwarzon Ajiya Sarki uban Isihu uban Garba,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,

106 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{53}$ $^{1}/_{2}$.

: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Alhaji sarkin hwadamar kanwa, x^2
'Y/Amshi : Mai kwana tsaye ko yaushe. x^2
Jagora : Alhaji sarkin hwadamar kanwa,
'Y/Amshi : Mai kwana tsaye ko yaushe,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Kai aj Jari da Shawai,
'Y/Amshi : Alhaji kai a Ibrahima,
: Kai ne Mainasaram mashi,
: Ina wanda ka tambaba.
Jagora : Kai aj Jari da Shawai,
'Y/Amshi : Alhaji kai a Ibrahima,
: Kai ne Mainasaram mashi,
: Ina wanda ka tambaba,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : To, sai an yi kadankarma, x^2
'Y/Amshi : A san babba a san yaro,
: Kuma sai an yi karom batta,
: A san wane a san wane. x^2

Jagora : Ai ina da Uba Sulxanin Gobir,
‘Y/Amshi : Wanda ka hisshe ni,
: Ni dai ba ni gudun hitinar Gobir,
: Duw wada tat tashi,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Ai ga taronmu na Sakkwato, x^2
'Y/Amshi : Mun gama kaya ga hawan daba,
: An shirya dawakayye,

: Amma babu kaman namu. x^2
Jagora : Doki ya hi dubu goma,
'Y/Amshi : Raqumi ya hi dubu goma,
: Duk an gamu an jera,
: Uban Shantali ya canye.
Jagora : Doki ya hi dubu goma,
'Y/Amshi : Raqumi ya hi dubu goma,
: Duk an gamu an jera,
: Uban Shantali ya canye,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Amma na ga gudan mota,
'Y/Amshi : Ga Sani makaxin Wurno,
: Sai dai ya gwada min mota,
: Na hi shi gudan doki,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Na ga Sani makaxin Wurno, x^2
'Y/Amshi : Shi an ba shi gudan mota, x^2
Jagora : Ko Sani Xandawo ya burge,
'Y/Amshi : Shi an ba shi gudan mota.

Jagora : To, ko Sanin Inyaga, x^2
'Y/Amshi : An ba shi gudan mota. x^2
Jagora : Kowa ya ba makaxinai mota,
'Y/Amshi : Ni ba ni da tau mota,
: Sarki ka qi yi min mota,
: Shin ko wani abu yag gilma.
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Kowa ya ba makaxinai mota,
'Y/Amshi : Ni ba ni da tau mota,

: Sarki ka qi yi min mota,
: Shin ko wani abu yag gilma.

Jagora : Da Garkuwa da Galadima,
'Y/Amshi : Da Baraya da Ubandoma,
: In dai ba maganak komi,
: A jawo ta a kawo ta,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Ai da Garkuwa da Galadima,
'Y/Amshi : Da Baraya da Ubandoma,
: In dai ba maganak komi,
: A jawo ta a kawo ta,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Kai aj Jari da Shawai,
'Y/Amshi : Alhaji kai a Ibrahima,
: Kai ne Mainasarar mashi,
: Ina wanda ka tambaba.

Jagora : Gohe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Duk mun ji su ga tarihi,
Jagora : Tambai ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Balarabe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Ibrahim ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Yakubu ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Jadi ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Shawai ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Jari Kada ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Salihu ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Ummaru ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Ibrahim ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,

: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : 'Yan Gatawa da Yakubawa,
'Y/Amshi : Kowane an sa shi ga tarihi,
: Haba sarki riqe tarihin ga,
: Da kowa ka bixa jiddun,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Bawa (1975 - 2003)[107],
Gindin Waqa : Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki,
'Y/ Amshi : Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Na Garkuwa bajimin Sarkin Dogarrai na Galadima, x^2
'Y/Amshi : Gwarzon Ajiya Sarki uban Isihu uban Garba. x^2
: Kai ab bahagon Gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

---

107 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{74}$ $^1/_2$.

Jagora : Alhaji Sarkin Fadamar Kanwa, x^2
'Y/Amshi : Mai kwana shire ko yaushe. x^2

Jagora : Kai aj Jari da Shawai, x^2
'Y/Amshi : Alhaji kai a Ibrahima,
: Kai ne Mainasaram mashi,
: Ina wanda ka tambaba, x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.
Jagora : Ai ga taronmu na Sakkwato, x^2
'Y/Amshi : Mun zaka hawan daba,
: An shirya dawakayye,
: Amma babu kaman namu. x^2

Jagora : Doki ya hi dubu goma, x^2
'Y/Amshi : Raqumi ya hi dubu goma,
: Duk an gamu an jera,
: Uban Shantali ya canye, x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Na ga Sani makaxin Wurno,
'Y/Amshi : Shi an ba shi gudan mota,
Jagora : Alhaji Sani makaxin Wurno,
'Y/Amshi : Shi an ba shi gudan mota,
Jagora : Ko Sani Xandawo ya burge,
'Y/Amshi : Shi an ba shi gudan mota.
Jagora : To, har Sani Inyaga,
'Y/Amshi : Shi an ba shi gudan mota,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Kowa ya ba makaxinai mota, x^2

'Y/Amshi : Ni ba ni da tau mota,
: Sarki ka qi yi min mota,
: Shin ko wani abu yag gilma, x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Ai da Garkuwa da Galadima, x^2
'Y/Amshi : Da Baraya da Ubandoma,
: In dai ba maganak komi,
: A jawo ta a kawo ta. x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Garkuwa in na zaka na gaisai, x^2
'Y/Amshi : Sai ya yo muna sakin huska,
: Da ya duba idanuna,
: Ya san wani abu yak kai mu. x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Sarki na yi bixam mota,
: Bana han na yi zuhwah hanci,
'Y/Amshi : Ko mik kai ga zuhwah hanci,
: Ka san abu ya vaci.
Jagora : Sarki na yi bixam mota, x^2
: Bana han na yi zuhwah hanci,
'Y/Amshi : Ko mik kai ga zuhwah hanci,
: Ka san abu ya vaci, x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,

: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Kai aj Jari da Shawai, x^2
'Y/Amshi : Alhaji kai a Ibrahima,
: Kai ne Mainasarar mashi,
: Ina wanda ka tambaba. x^2

Jagora : Gohe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Duk mun ji su ga tarihi,
Jagora : Gauxe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Tambai ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Mainasara ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Ibrahim ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Jari Kada ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Balarabe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Jari Kada ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Jadi ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Shawai ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Salihu ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Ummaru ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Ibrahim ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Gwamkawa da Bacirawa, x^2
'Y/Amshi : Kowane an sa shi ga tarihi,
: Haba sarki riqe tarihin ga,
: Da kowa ka bixa jiddun.x^2

Jagora : ‘Yan Hwatawa da Yakubawa, x2
'Y/Amshi : Kowane an sa shi ga tarihi,
: Haba sarki riqe tarihin ga,
: Da kowa ka bixa jiddun, x2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.
Jagora : Haba sarki riqe tarihin ga, x2
: Da kowa ka bixa jiddun,
'Y/Amshi : Kai kag gane mahwarinai,
: Kuma ka san wada yak qare, x2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Haba sarki yi tunani, x2
: Ka tuna tsohinka na addini,
: Na farko Abdullahi,
: Da Kaso Birnin Mai-Lalle,
: Da Dango mai Tansidi,
: Da Sardauna Sama'ila,
'Y/Amshi : Kowa ad da hwaxi Alqalawa babu kaman naka,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki. x2

Jagora : Ai ina da Uba Sulxanin Gobir wanda ka hisshe ni, x2
‘Y/Amshi : Ni dai ba ni gudun hitinar Gobir duw wada tat tashi, x2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Ga riga mai tamburra Uban Shantali yab ba da, x3
‘Y/Amshi : Sai yac ce mu yi cin duniya,
: Da ‘ya’yanmu da matanmu, x3

: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Mata na ko yaushe, x^3
: Suna xunki da lishi da karen muski,
'Y/Amshi : Cikin albarkas Sarkin Gobir Bawa uban Bawa, x^3
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Sarki ya hana kamanci da Buzu da Bahillace, x^2
'Y/Amshi : Daxa kowa ya yi zavenai,
: Kai an toshe batun shirgi, x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Ga ni ina son harkar zambo, x^2
'Y/Amshi : Amma na zama mai geme,
: Kowa yaz zama mai geme,
: Ba dama shi yi shexanci, x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Ai cikin masu biyas sarki, x^2
'Y/Amshi : Wasu sun hwara munahicci,
: Bari kowa ka munahicci,
: Hwaxa mai da akwai Allah, x^2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,

: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Jiya can nij ji mutane, x3
: Na cewa wane hawa'i ne,
'Y/Amshi : Ko mu mun ji mutane ,
: Na cewa wane tavavve na. x3
Jagora : Alhaji sarkin hwadamar kanwa, x2
'Y/Amshi : Mai kwana shire ko yaushe. x2

Jagora : Shi wargi da hawa'i, x2
'Y/Amshi : Ya xara wargi da bugun buta,
: In sun tashi rashin kunyan nan,
: In sun gamu dux xai na, x2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Hawa'i da bugun buta ai na ce muku dux xai na, x2
'Y/Amshi : Ai had da mashayin kansu,
: Shi ma la'ananne na, x2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.
Jagora : Kai aj Jari da Shawai, x2
'Y/Amshi : Alhaji kai a Ibrahima,
: Kai ne Mainasarar mashi,
: Ina wanda ka tambaba. x2

Jagora : To, Garkuwa xan Gardaye, x2
'Y/Amshi : A gaishe ka a gaishe ka,
: Mu yi hwata ya daxe duniya,
: Ya zam ba mu abin Allah, x2
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : To, Garkuwa in na zaka gaisai, x2

‘Y/Amshi : Sai yay yo min dumbulka,
: Da ya diba idanuna,
: Ya san wani abu yak kai ni. x2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Bawa (1975 - 2003)
Gindin Waqa : Kai ab bahagon gulbi,[108]
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Na Garkuwa bajimin Sarkin Dogarrai na Galadima, x2
'Y/Amshi : Gwarzon Ajiya Sarki uban Isihu uban Garba. x2
: Kai ab bahagon Gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan-Inna kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Jagora : Alhaji Sarkin Fadamar Kanwa, x2
'Y/Amshi : Mai kwana shire ko yaushe. x2

Jagora : Kai aj Jari da Shawai, x2
'Y/Amshi : Alhaji kai a Ibrahima,
: Kai ne mainasaram mashi,
: Ina wanda ka tambaba. x2

Jagora : Ai ga taronmu na Sakkwato, x2
'Y/Amshi : Mun zuba kaya ga hawan daba,
: An shirya dawakayye,
: Amma babu kaman namu. x2
Jagora : Doki ya hi dubu goma, x2
'Y/Amshi : Raqumi ya hi dubu goma,
: Duk an gamu an jera,
: Uban Shantali ya canye. x2

Jagora : To, sai an yi kadankarma, x2
'Y/Amshi : A san babba a san yaro,

108 An sami wannan rerawa ne a littafin *Diwanin Waqoqin Baka.* Gusau, S.M. 2009: 204-207.

: Kuma sai an yi karon batta,
: A san wane a san wane. x^2

Jagora : Haba sarki yi tunani,
: Ka tuna tsohinka na addini, x^2
'Y/Amshi : Na farko Abdullahi,
: Da Kaso Birnin Mai-Lalle,
: Da Dango mai xan ciki,
: Da Sardauna Sama'ila,
: Kowa ad da hwaxi Alqalawa,
: Babu kaman naka. x^2

Jagora : Na ga Sani makaxin Wurno, x^2
'Y/Amshi : Shi an ba shi gudan mota, x^2
Jagora : To, ko Sanin Inyaga,
'Y/Amshi : An ba shi gudan mota,
Jagora : Ko Sani Xandawo ya burge,
'Y/Amshi : An ba shi gudan mota.
Jagora : Ko Qwairo makaxin manya, x^2
'Y/Amshi : An ba shi gudan mota. x^2
Jagora : Kowa ya ba makaxinai mota, x^2
'Y/Amshi : Ni ba ni da tau mota,
: Sarki ka qi yi min mota,
: Shin ko wani abu yag gilma. x^2

Jagora : Da Garkuwa da Galadima, x^2
'Y/Amshi : Baraya da Ubandoma,
: In dai ba maganak komi,
: A jawo ta a kawo ta. x^2
Jagora : To, Garkuwa xan Gardaye, x^2
'Y/Amshi : A gaishe ka a gaishe ni,
: Mui hwata ya daxe duniya,
: Ya zan ba mu abun Allah. x^2

Jagora : Garkuwa in na zaka na gaisai, x^2
'Y/Amshi : Sai ya yo muna sakin huska,
: Da ya duba idanuna,
: Ya san wani abu yak kai mu. x^2

Jagora : To, Inna qaunas sarki, x^2
'Y/Amshi : Ta maishe ni kamax xanta,
: Ko babu kixi naz zo,
: Sai ta ba ni abun goro. x^2

Jagora : To, Inna xiyas Sardauna, x^2
'Y/Amshi : Giwa Inna Bahillata,
: In ta kama zuba min kaya,
: Sai na gaji na rave. x^2

Jagora : Kai na Garkuwa bajimin sarki, x^2
'Y/Amshi : Gwarzon Ajiya sarki,
: Uban Isihu uban Garba. x^2
Jagora : Kai aj Jari da Shawai, x^2
'Y/Amshi : Alhaji kai a Ibrahima,
: Kai ne Mainasarar mashi,
: Ina wanda ka tambaba. x^2

Jagora : Gohe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Duk mun ji su ga tarihi,
Jagora : Gauxe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Ibrahim ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Mainasara ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Yakubu ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Tambai ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Balarabe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi,
Jagora : Na ga tsarin Yakubawa, x^2
'Y/Amshi : Kowane an sa shi ga tarihi,
: Haba sarki riqe tarihin ga,
: Da kowa ka bixa jiddun. x^{22}

Jagora : Gwamkawa da Bacirawa, x^2
'Y/Amshi : Kowane an sa shi ga tarihi,
: Haba sarki riqe tarihin ga,
: Da kowa ka bixa jiddun. x^2

Jagora : Haba sarki riqe tarihin ga,
: Da kowa ka bixa jiddun, x^2
'Y/Amshi : Kai kag gane mahwarinai,
: Kuma ka san wada yak qare. x^2
Jagora : Alhaji Sarkin Fadamar Kanwa, x^2
'Y/Amshi : Mai kwana shire koyaushe. x^2

Makaxi : Ahaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni
Waqa : Waqar Noma[109] *,*
07. *Gindin Waqa : Na yi hamdala nai shukura da godewa,*
: Tun da na sani noma yau farilla ne.

Jagora : Maza ku kama noma noma abin yi ne,
'Y/Amshi : Don na ga ba a gumba in ba da tsaba ba,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau farilla ne.

Jagora : Maza ku kama noma noma abin yi ne,
'Y/Amshi : Yau na ga ba a gumba in ba da tsaba ba.
Jagora : Shi wanda ba shi noma ya zam abin tausai,
'Y/Amshi : Yana bixar awo mata na harara tai,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau farilla ne.

Jagora : Na zo Maraxi na ishe an sare dajinsu, x^2
'Y/Amshi : Mutum guda ya ce shi xai za shi nome su. x^2
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau farilla ne.

Jagora : Gandun Xangara yai gandu ko ga 'yan dauri, x^2
'Y/Amshi : In yanzug ga ba gandu mai misalinai. x^2
Jagora : Gandun Xangara ya yi gabas mil xari sittin,
: Na yi yamma na diba mil xari sittin,
: Gandun Xangara ya yi Gusum mil xari sittin,
: Kuma nai arewa na diba mil xai sittin,
'Y/Amshi : Abin da za a yi ciki ab ba mu gane ba,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau farilla ne.

Jagora : In za a sussukak damma sai a yo gayya, x^2
: Makobiya dubu kowace ta yi buhu maitan, x^2

---

109 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{375}$ $^1/_{13}$.

‘Y/Amshi : Ai sai a yo kiran ‘yan boko ku lisafta.
Jagora : In munka lissahwa kuma munka nunhwasa, x^2
‘Y/Amshi : Ai babu wanda bai san Allah ka iko ba.x^2
Jagora : Allah ya yi ruwa mun shisshikke gonakki,
: Sai da munka shibke,
‘Y/Amshi : Abin da za a yi ciki Allah ka gyarawa,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau farilla ne.

Jagora : Maza ku kama noma noma abin yi ne, x^2
‘Y/Amshi : Yau na ga ba a gumba in ba da tsaba ba. x^2

Jagora : Shi wanda ba shi noma ya zam abin tausai, x^2
‘Y/Amshi : Yana bixar awo mata na harara tai,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau farilla ne. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni
Waqa : Waqar Noma[110]*,*
Gindin Waqa : Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na.

Jagora : Maza ku kama noma noma abin yi na, x^2
'Y/Amshi : Don na ga ba a gumba in ba da tsaba ba, x^2
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na.

Jagora : Wanda ba shi noma ya zam abin tausai,
'Y/Amshi : Yana bixar awo mata na harara tai,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na.

Jagora : Qattanga masu yawo ba su kama aiki ba, x^2
'Y/Amshi : Sabadda su tiyar gero ba ta shixowa, x^2
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na.

Jagora : Inda wada munka noma kowa shi zai yi na,
'Y/Amshi : Da yanzu ai tiyar gero ba ta kai zangu,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na.

Jagora : Na zo Maraxi na ishe an sare dajinsu,
'Y/Amshi : Mutum guda ya ce shi xai za shi nome su,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na.

Jagora : In munka lissafa kuma in munka lumfasa,
'Y/Amshi : Babu wanda bai san Allah ka iko ba,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na.

Jagora : Allah ya yi ruwa mun shikkikke gonakki, x^2

---

110 An sami wannan rerawa ne a littafin *Diwanin Waqoqin Baka.* Gusau, S.M. 2009: 197-203.

‘Y/Amshi : Sai da munka shikke kuma munka nomikke, x^2
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na.

Jagora : Da munka nome kuma munka maimaice, x^2
‘Y/Amshi : Abin da za a yi ciki Allah ka gyarawa, x^2
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na.

Jagora : Allah shi fallala kuma Allah shi umfana, x^2
‘Y/Amshi : Allah shi ceci mai iya aiki ga aikinai, x^2
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na.

Jagora : Xangara ka yi lambuwal kuma an yo ka lamba xai,
‘Y/Amshi : Saboda in kana nan komai ba shi motsawa,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na.

Jagora : Maza ku kama noma noma abin yi na, x^2
‘Y/Amshi : Don na ga ba a gumba in ba da tsaba ba,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau abin yi na. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni

Mai Waqa : Alhaji Hashimu D. P.O na Gusau[111],

08. *Gindin Waqa : Na shira kaya za ni garai,*
: Na Alhaji D. P. O na Gusau.

Jagora : Allah ka ruwa, Allah ka hatsi,
'Y/Amshi : Kuma Allah yay yo masu gari,
: Kuma yas shirya bayam masu gari,
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.

Jagora : Tun dan nan hab bisa birnin Ikko gari, x^2
'Y/Amshi : Babu inda ba a san Yawuri ba, x^2
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.

Jagora : Toronku na Yawuri ya yi tsawo, x^2
'Y/Amshi : Jibirila yas shirya maku shi,
: Tun da ba uban wani yay yi shi ba, x^2
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.

Jagora : Abdullahi ya yi mulki Yawuri,
'Y/Amshi : Hay ya gama shi bai sava muku ba, x^2
: Tun da ko ga sohi munka cira. x^2
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.

Jagora : Sani Xandawo ya leqa mani,
'Y/Amshi : Yac ce Yawuri ta burma da gari,
: Abin da yag ga ta burma da gari,
: Tun da ko akwai manyan masana,
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.

Jagora : Na Garkuwa na Ali mai sango, x^2
'Y/Amshi : Bajinin Bunu abin ka ya koma izini,

---

111 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{51}$ $^1/_3$ - AL $^0/_{74}$ $^1/_1$.

: Ko da yaushe kura tahi gari. x^2

Jagora : Maidaji cikin daji nike,
'Y/Amshi : Hashimu yi tattalin mai da ni gari,
: Tun da ba Bahillace nike ba,
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.
Jagora : Maidaji cikin daji nike, x^2
'Y/Amshi : Hashimu yi tattalin mai da ni gari,
: Tun da ba Bahillace nike ba, x^2
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.

Jagora : Hashimu uban tawaye, x^2
'Y/Amshi : Hashimu dum mai biyak ka,
: Ya huta da tsiya sai ya sami kuxxi yai shagali, x^2
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.

Jagora : Allah ka ruwa, Allah ka hatsi, x^2
'Y/Amshi : Kuma Allah yay yo masu gari,
: Kuma yas shirya bayam masu gari. x^2

Jagora : Hashimu shira ka maisan Yawuri, x^2
'Y/Amshi : Ka san ban iya auren xauki kwari, x^2
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.

Jagora : Hashimu uban tawaye,
'Y/Amshi : Hashimu dum mai biyak ka,
: Ya huta da tsiya sai ya sami kuxxi yai shagali,
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.

Jagora : Hashimu ina yi ma hwata, x^2
'Y/Amshi : Allah dai ya qaddara Allah ya nuhwa,
: Don a karvi hwata tare da mu,

: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau. x^2

Jagora : ‘Ya’yana suna yi ma hwata, x^2
'Y/Amshi : Allah dai ya qaddara Allah ya nuhwa,
: Don ya karvi hwata tare da mu, x^2
Jagora : Matana suna yi ma hwata, x^2
'Y/Amshi : Allah dai ya qaddara Allah ya nuhwa,
: Don ya karvi hwata tare da mu, x^2
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.

Jagora : Na Garkuwa na Ali mai sango, x^2
'Y/Amshi : Bajinin Bunu abinka ya koma izini,
: Ko da yaushe kura tahi gari. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,

Alhaji Ummaru xan Salihu (1957-1966)[112]*,*

09. *Gindin Waqa : Gagari gaba na Salihu,*
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Gwamron giwa,
'Y/Amshi : Uban lihidda Bawa qanin Sahi bahago,
: Jari magajin na Abu,
: Ko da yaushe yana nan wurin jiya,
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Ashe Allah shi ka bajini, x^2
'Y/Amshi : Kuma Allah shi ka xaukaka,
: To, Allah shi ka yin mazakkari,
: Ya shirya mai abubuwa. x^2

Jagora : To Allah shi ad da duniya, x^2
'Y/Amshi : Kuma Allah shi ad da Lahira,
: Allah yay yo shirye-shiryen,
: Da za a shirawa na duniya, x^2
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Ina wani mai jan damamisau,
'Y/Amshi : Ku ce ya bari in yana bari,
: In ba ya bari sai ku bar shi,
: Tun da mu maganag gaskiya mukai.

Jagora : Yanzu ina wani mai ‘yak kara-kara,
'Y/Amshi : Ku ce ya bari in shina bari,
: In ba ya bari sai ku bar shi,
: Tun da mu maganag gaskiya mukai.

---

112 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{143}$ $^1/_4$.

Jagora : Toron giwa ya katse haqo, x^2
'Y/Amshi : Masu haqon sun yi birkixa,
: Ku kwashe haqon nan ku tashi,
: Tun da Bawa na Dango gani yakai, x^2
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Na Inna magajin sarauniya,
'Y/Amshi : Ruwan dare mai kama duniya,
: In dai kyauta ta Bawa,
: Ko da yaushe qira min wata yakai.
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Gwamron giwa,
'Y/Amshi : Uban lihidda Bawa qanin Sahi bahago,
: Jari magajin na Abu,
: Ko da yaushe yana nan wurin jiya.

Jagora : Na Inna magajin sarauniya,
'Y/Amshi : Ruwan dare mai kama duniya,
: In dai kyauta ta Bawa,
: Ko da yaushe qira min wata yakai.

Jagora : To, na zo salla uban lihidda, x^2
'Y/Amshi : Ya yi mini kaya iri-iri,
: Ga shadda anka ba ni,
: Wadda babu iri ko qasar Masar. x^2

Jagora : Ga ni ina son vacin tcibilbila,
'Y/Amshi : Zaman zauri xai nika gudu,
: In zauri ya buwaya yanzu,
: Ko ga itace zama takai.
: Gagari gaba na Salihu,

: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : To, na so in vaci hakimin sarki,
'Y/Amshi : Rowan nan da yat tcira,
: Baqar Rowan nan da yat tcira,
: Da hwari shi ka sa mu tsira xumumuwa.
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Maza ku yi wasa da dariya,
'Y/Amshi : Ku zan ki gamawa da hwara'a,
: Mai rowa ko da yaushe,
: Kag gane shi da lauje cikin naxi.
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Shin Mainasara ne Balarabe ne? x^2
'Y/Amshi : Yakuba ne ko Mayaqi ne?
: Ka koma shiri xan Halima,
: Kak ka zo ka ji tsoron mazan kawai. x^2
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni[113]*,*
Alhaji Ummaru xan Salihu (1957-1966),
Gindin Waqa : Gagari gaba na Salihu,

---

113 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{143}$ $^1/_5$

: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu magajin gidan Kada.

Jagora : Gwamron giwa uban lihidda Bawa qanin Sahi Bahago,
'Y/Amshi : Jari magajin na Abu ko da yaushe yana nan wurin jiya.

Jagora : Gwamron giwa,
'Y/Amshi : Uban lihidda Bawa qanin Sahi Bahago,
: Jari magajin na Abu,
: Ko da yaushe yana nan wurin jiya,
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Ashe Allah shi ka bajini, x^2
'Y/Amshi : Kuma Allah shi ka xaukaka,
: To, Allah shi ka yi mazakkari,
: Ya shirya mai abubuwa. x^2

Jagora : To Allah shi ad da duniya, x^2
'Y/Amshi : Kuma Allah shi ad da Lahira,
: Allah yay yo shirye-shiryen,
: Da za a shirawa na duniya, x^2
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Ina wani mai jan damamisau,
'Y/Amshi : Ku ce ya bari in yana bari,
: In ba ya bari sai ku bar shi,
: Tun da mu maganag gaskiya mukai.

Jagora : Yanzu ina wani mai ‘yak kara-kara,
'Y/Amshi : Ku ce ya bari in shina bari,
: In ba ya bari sai ku bar shi,
: Tun da mu maganag gaskiya mukai.

Jagora : Toron giwa ya katse haqo, x^2
'Y/Amshi : Masu haqon sun yi birkixa,
: Ku kwashe haqon nan ku tashi,

: Tun da Bawa na Dango gani yakai, x^2
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Shin Mainasara ne Balarabe ne, x^2
'Y/Amshi : Yakuba ne ko Mayaqi ne,
: Ka koma shiri xan Halima,
: Kak ka zo ka ji tsoron mazan kawai. x^2

Jagora : Kai ad da dubun arziki, x^2
'Y/Amshi : Uban Ali uban Audu Markaxe,
: Gobir babu irin wanda ya yi,
: Wadda na Sardauna yas shirya. x^2

Jagora : Ya gina makwanci na Bawa,
'Y/Amshi : Jangwarzo sannan ya yi shigihwa,
: Ko wada yai azama ya isa,
: Abin da yai nuhi an yi an gama,
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Gwamron giwa,
'Y/Amshi : Uban lihidda Bawa qanin Sahi bahago,
: Jari magajin na Abu,
: Ko da yaushe yana nan wurin jiya.

Jagora : Na Inna magajin sarauniya,
'Y/Amshi : Ruwan dare mai kama duniya,
: In dai kyauta ta Bawa,
: Ko da yaushe qira min wata yakai.

Jagora : To, na zo salla uban lihidda, x^2
'Y/Amshi : Ya yi mini kaya iri-iri,
: Ga shadda anka ba ni,
: Wadda babu iri ko qasar Masar. x^2

Jagora : Ga ni ina son vacin tcibilbila,
'Y/Amshi : Zaman zauri xai nika gudu,
: In zauri ya buwaya yanzu,
: Ko ga itace zama takai.
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : To, na so in vaci hakimin sarki,
'Y/Amshi : Rowan nan da yat tcira,
: Baqar Rowan nan da yat tcira,
: Da hwari shi ka sa mu tsira xumumuwa.
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Maza ku yi wasa da dariya,
'Y/Amshi : Ku zan ki gamawa da hwara'a,
: Mai rowa ko da yaushe,
: Kag gane shi da lauje cikin naxi.
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Gwamron giwa,
'Y/Amshi : Uban lihidda Bawa qanin Sahi bahago,
: Jari magajin na Abu,
: Ko da yaushe yana nan wurin jiya.

Jagora : To, na ji darajja ga Gobirawa, x^2
'Y/Amshi : Kullum haske taka ta yi,
: A zam magannar nan ta yanzu,
: To, a bar maganar shekaranjiya. x^2

Jagora : Ta-na-ta-hu ba Cilu-Cilu ba,
'Y/Amshi : Alhaji kai a Baranqwame,
: Tun da ina nan gare ka,
: Ba Uban da ka sa min baqingawai ,

: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Toron giwa ya katse haqo, x^2
'Y/Amshi : Masu haqon sun yi birkixa,
: Ku kwashe haqon nan ku tashi,
: Tun da Bawa na Dango gani yakai. x^2
Jagora : Ina wani mai jan damamisau,
'Y/Amshi : Ku ce ya bari in yana bari,
: In ba ya bari sai ku bar shi,
: Tun da mu maganag gaskiya mu kai.
Jagora : Yanzu ina wani mai ‘yak kara-kara,
'Y/Amshi : Ku ce ya bari in shina bari,
: In ba ya bari sai ku bar shi,
: Tun da mu maganag gaskiya mu kai.

Jagora : Lalle Gudal ya ba ni, x^2
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo. x^2
Jagora : Galadima ya yi taimako,
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo.
Jagora : A gai da Giye ya yi taimako,
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo.
Jagora : Sarkin Noma ya yi taimako,
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo.
Jagora : Sani Nalabo ya yi taimako,
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo.
Jagora : Magajin Tsamaye ya yi taimako,
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo.
Jagora : Durumbu da ya ba da taimako,
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo.
Jagora : Sarkin Rahi ya yi taimako,
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo,
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : To, na yi karatu da ilmi, x^2
'Y/Amshi : Har na sabka na yi shinhixa,
: Xiyana sun kama Sabbi,

: Yanzu diba takardu kaxai mukai, x^2
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : Ashe Allah shi ka bajini, x^2
'Y/Amshi : Kuma Allah shi ka xaukaka,
: To, Allah shi ka yi mazakkari,
: Ya shirya mai abubuwa. x^2

Jagora : Ashe kyawon xan Bagobiri, x^2
'Y/Amshi : Ya kwan da shirinai,
: Shirin hwaxa ya rinqa tunawa da,
: Lanqwahe bakin maza yakai, x^2
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni
Mai Waqa : Innar Gobir Sabon Birni[114]*,*
10. *Gindin Waqa : Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,*
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa, x^2
'Y/Amshi : Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa. x^2

Jagora : Sannu da sirdi, x^2

114 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{375}$ $^1/_3$.

‘Y/Amshi : Ta Bawa da ke 'yar Muhammadu,
: Yau kasa uwar macizai ta kama sirdi, x^2
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Inna hwarar uwa,
'Y/Amshi : Ta Dango, to, gode Allah ke ar 'yar Balarabe,
: Kya san ya kamata,
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : To, Inna ina ganin ki,
'Y/Amshi : Lalle kya 'yam ma harka,
: Tun da duk abin da kic ci,
: Sai kin 'yam ma dangi,
Jagora : Ke a uwar,
'Y/Amshi : Maroqan birni da qauye,
: In kya haihwa xa kuma xa Audu,
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Darzaza,
'Y/Amshi : Ta Bawa ko ba wuri ki hurce,
: Duk inda kib biya sai kowa ya wadata,
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.
Jagora : Zamaninki da ni da yarana mun wadata, x^2
'Y/Amshi : Ita ta ba mu riguna kuma ta ba mu zanna,
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa. x^2

Jagora : Abin da ag ga amarya, x^2
'Y/Amshi : Shi taka kai ma ango,
: Abin da ag gare ni yau,
: Shi zan kai ma Inna. x^2
Jagora : Kya san ban da, x^2
'Y/Amshi : Raguna in ta zo mu yanka,
: Babu abin da ag garan sai turu da waqa, x^2
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,

: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Na zaka in yi godiyar riga in da Inna,
'Y/Amshi : To, in za ki ba ni wata kak ki fasa.
Jagora : To, Inna kwakwatad,
'Y/Amshi : Da kinka ban na bam ma yaro,
: Kai yaro ina yi ma horo don ka xauka,
: Don ka ga Inna ta ban tsaba kak ka sai da,
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Tsahe da niz zo kixa,
'Y/Amshi : Inna ta ba ni kore-koren nan,
: Ko ya zo da sa'a,
: Bara da za ni Makka can nis saisai ga hanya,
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Alhaji na xauri anniyar, x^2
'Y/Amshi : In zo gai da Inna,
: To, amma da ban zuwa sai na fara xinki. x^2
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : To, Inna kya gane ni ‘yar rigata guda ta, x^2
'Y/Amshi : Ita an nan cikin gida, ita ag ga daji,
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa. x^2

Jagora : Mai riga guda ina addini gare shi, x^2
'Y/Amshi : Ko ya so zuwa masallaci sai ya fasa,
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa. x^2

Jagora : Inna hwarar uwa ta Dango,
'Y/Amshi : Ta gode Allah,
: Ke 'yar Balarabe ta san ya kamata,
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Sannu da sirdi, x^2
‘Y/Amshi : Ta Bawa da ke 'yar Muhammadu,
: Yau kasa uwar macizai ta kama sirdi, x^2
: Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa, x^2
'Y/Amshi : Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni
Mai Waqa : Innar Gobir Sabon Birni[115]*,*
Gindin Waqa : Kina da martabaj Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa, x^2
'Y/Amshi : Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa. x^2

Jagora : Sannu da sirdi ta Bawa, x^2
‘Y/Amshi : Sannu da gaishe da Allah,
: Yau Kasa uwar macizai ta kama sirdi. x^2

---

115 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{143}$ $^1/_3$ - AL $^1/_{145}$ $^1/_6$.

Jagora : Inna hwarar uwa ta Dango ta gode Allah, x^2
'Y/Amshi : Jikanyar Balarabe ta san ta kamata, x^2
: Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : To, na zaka in yi godiyar riga inda Inna,
'Y/Amshi : To, in za ki ba ni wata amma kak ki hwasa,
: Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora: To, Inna kwakwatad da kib ban na bar ma yaro, x^2
'Y/Amshi : To, kai yaro ina yi ma horo don ka xauka, x^2
: To, don ka ga babu tsaba don kak ka sai da,
: Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Bara da niz zo kixi ga Inna ta ba ni Kore,
'Y/Amshi : Koren nan ko da tay yi min ya zo da sa'a,
: Bara da za ni Makka can nis saisai ga hanya,
: Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Alhaji na yi anniya in zo gai da Inna, x^2
'Y/Amshi : To, amma hwa ban zuwa sai na hwara xinki. x^2
Jagora : To, Inna kya gane ni riga ta ‘yar guda ta,
'Y/Amshi : Ita an nan cikin gida ita an nan ga daji,
: Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Mai riga guda ina addini gare shi,
'Y/Amshi : Ko ya so zuwa masallaci sai ya hwasa,
: Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Abin da ag ga amarya shi taka kai ma ango, x^2
'Y/Amshi : Abin da ag gare ni yau shi zan kai ma Inna. x^2

Jagora : Kya san ban da raguna in ta zo mu yanka,

'Y/Amshi : Babu abin da ag garan sai turu da waqa,
: Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Da zamaninki ni da yarana mun wadata, x^2
'Y/Amshi : Ita ta ba mu riguna, kuma ta ba mu zanna. x^2

Jagora : Iya ke a uwar maroqan birni da qauye,
'Y/Amshi : In kya haihwa xa kuma xa Audu,
: Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Jagora : Darzaza ta Bawa ko ba wuri ki hurce,
'Y/Amshi : Duk inda kib biya sai kowa ya wadata,
: Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003)[116]*,*

11. *Gindin Waqa : Sarki Muhammadu xan Kilo,*
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Dagga abin da Allah ya shirya, x^2
'Y/Amshi : Sai wanda Annabi yas shirya,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai. x^2

Jagora : Shiryayye na Dango,
'Y/Amshi : Xan Inna fifita ni na Malam Salihu,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

---

116 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{374}$ $^1/_7$.

Jagora : Uban na Inda Baban Makama,
‘Y/Amshi : Bawa arkunniyab bakin dawa,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Yau kai a Muhammadu Babari, x^2
: Kai a Muhammadu Maijindi
‘Y/Amshi : Kai a Muhammadu na Dango,
: Wada duk ka hwaxa daidai kake, x^2
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Taron gamon Alqalawa,
‘Y/Amshi : Dac can mun wuce Sabon Birni,
: Ga yau Bawa ab babbansu,
: Ce ma kowa ya zamna lahiya,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.
Jagora : Sarki ga wasiqa na,
‘Y/Amshi : Shirya, sai na karanta ka jiya,
: Ai ko ga iska nab buga,
: Uban Yari ganewa ya kai,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Ya ban buhuhuwa a yi man tuwo,
‘Y/Amshi : Ya ban kuxi in sai miya,
: Amma kayan in mun canye su,
: Xan Inna dawowa mu kai.
Jagora : Fam goma sha biyar Sarki yab bai,
‘Y/Amshi : Yac ce mu sai kajin miya,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Zamanin Muhammadu xan Kilo,
‘Y/Amshi : An ba mu Naira zay yawa,
: An ba mu manyan riguna.
Jagora : In ka ganan da shadda tsanwa shar,

‘Y/Amshi : Garko ka shiryar man ita,
: In ka ganan da kwakwata,
: Magajin gari ka yi min ita,
: In ka gane ni da jikak Kano,
: To, wadda Inna kai min ita.
Jagora : To, kuma in ka ganan da wandon Kano,
‘Y/Amshi : To, wanda Inna tay yi na.
Jagora : A gaishe ki Inna,
‘Y/Amshi : ‘Yar Kilo xiyag Garba manyan duniya,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Shiryayye na Dango, x^2
‘Y/Amshi : Xan Inna fifita ni na Malam Salihu,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai. x^2

Jagora : Dauri babu kwano Sabon Birni,
‘Y/Amshi : To, zamanin baban Sule,
: Na ga yanzu kwano yai yawa.
Jagora : Dauri babu mota Sabon Birni,
‘Y/Amshi : To, zamanin baban Sule,
: Na ga yanzun mota tai yawa.
Jagora : Dauri babu hwanda Sabon Birni,
‘Y/Amshi : To, zamanin baban Sule,
: Na ga yanzu hwanda yai yawa.
Jagora : Dauri babu shadda Sabon Birni,
‘Y/Amshi : To, zamanin baban Sule,
: Na ga yanzu shadda tai yawa.
Jagora : Dauri babu famfo Sabon Birni,
‘Y/Amshi : To, zamanin baban Sule,
: An shirya famfo zar ruwa,
: Saura a sa mana tsakkuwa da kwalta,
: A shahe godabe,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : In dai kag ga na yi gaba Gusun,
‘Y/Amshi : Na tuna da sarkin tasha,

: Ya saba shirya man kuxi,
: Naira xari in zan kashi,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : In ko ka gan ni kunku,
'Y/Amshi : Alhaji E. O. nit tuna,
: E. O. baturen gaskiya,
: E. O. baturen gwamnati,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Sarki swahe duk roqo nikai x^2
'Y/Amshi : Da Shawai da Inna da Altine,
: Allah ya gafarta masu. x^2

Jagora : Da Jadi da Jari da Xanfama,
'Y/Amshi : Sun sare daji sun tushe,
: Mu yanzu girbi xai mu kai,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : In ka ga xan hwarauta yai shiri, x^2
'Y/Amshi : Ga karhuna ga kambuna,
: In ba kare ya taho gidan,
: Qaryah hwarauta ta yakai, x^2
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Yau kai am Muhammadu Babari, x^2
: Kai am Muhammadu Maijindi
'Y/Amshi : Kai am Muhammadu na Dango,
: Wanda duk ka hwaxa daidai kake, x^2
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Shiryayye na Dango, x^2
'Y/Amshi : Xan Inna fifita ni na Malam Salihu, x^2
: Sarki Muhammadu xan Kilo,

: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Dagga abin da Allah ya shirya, x^2
'Y/Amshi : Sai wanda Annabi yas shirya,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003)[117]*,*
Gindin Waqa : Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Sarki Muhammadu yai shiri, x^2
'Y/Amshi : Kowa ya saurara mashi,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai. x^2

Jagora : Dagga abin da Allah yas shirya,
'Y/Amshi : Sai wanda Annabi yas shirya,
: Sarki Muhammadu yai shiri,
: Kowa ya saurara mashi,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Shiryayye na Dango xan Inna, x^2

---

117 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{144}$ $^1/_3$ - AL $^1/_{145}$ $^1/_4$.

‘Y/Amshi : Qi da arna na Malam Salihu. x^2
Jagora : Uban Lihidda baban Makama,
‘Y/Amshi : Bawa arkunniyab bakin dawa,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Yau kai am Muhamman Babari,
: Kai am Muhamman Maijiddi
‘Y/Amshi : Kai am Muhamman na Dango,
: Wanda duk ka hwaxa daidai kake.
Jagora : To, kai a Muhamman Babari,
: Kai am Muhamman Maijiddi,
‘Y/Amshi : Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.
Jagora : Taron gamon Alqalawa,
‘Y/Amshi : Dac can mun wuce Sabon Birni,
: Ga yau Bawa ab babbansu,
: Ce ma kowa ya zamna lahiya,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Sarki ga wasiqa na shirya,
‘Y/Amshi : Sai na karanta ka jiya,
: Ai ko ga iska nab buga,
: Uban Yari ganewa yakai.
Jagora : Ya ban buhuhuwa a yi min tuwo,
‘Y/Amshi : Ya ban kuxi in sai miya,
: Amma kayan in mun canye su,
: Xan Inna dawowa mukai,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Zamanin Muhammadu xan Kilo, x^2
‘Y/Amshi : An ba mu Naira zay yawa,
: An ba mu manyan riguna. x^2
Jagora : In ka ganan da shadda tsanwa shar,
‘Y/Amshi : Garko ka shiryar man ita,

: In ka gane ni da kwakwata,
: Magajin gari ka yi min ita,
: In ka gane ni da jikak Kano,
: To, wadda Inna kai min ita.
Jagora : To, kuma in ka ganan da wandon Kano,
'Y/Amshi : To, wanda Inna tay yi na.
Jagora : A gaishe ki Inna 'yar Kilo,
'Y/Amshi : Xiyag Lubba manyan duniya,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Sarki swahe duk roqo nikai
'Y/Amshi : Da Shawai da Inna da Argiji,
: Allah ya gahwarta musu,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : Da Jadi da Jari da Xantsara, x^2
'Y/Amshi : Sun sare daji sun tushe,
: Mu yanzu girbi xai mu kai. x^2

Jagora : Dauri babu kwano Sabon Birni,
'Y/Amshi : To, zamanin baban Sule,
: Na ga yanzu kwano yai yawa.
Jagora : Dauri babu mota Sabon Birni,
'Y/Amshi : To, zamanin baban Sule,
: Na ga yanzun mota tai yawa.
Jagora : Dauri babu hwanda Sabon Birni,
'Y/Amshi : To, zamanin baban Sule,
: Na ga yanzu hwanda yai yawa.
Jagora : Can dauri babu shadda Sabon Birni,
'Y/Amshi : To, zamanin baban Sule,
: Na ga yanzu shadda tai yawa.
Jagora : Dauri babu famfo Sabon Birni,
'Y/Amshi : To, zamanin baban Sule,
: An shirya famfo zar ruwa,
: Saura a sa mana tsakkuwa da kwalta,

: A shahe godabe,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Jagora : In ka ga xan hwarauta yai shiri,
'Y/Amshi : Ga karhuna ga kambuna,
: In ba kare ya taho gidan,
: Qaryah hwarauta ta yakai,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa,
Mai Waqa : Innar Gobir[118]*,*
12. *Gindin Waqa : Gagarabadau 'Yakkaso,*
: Ta Muhamman Dosau 'yam mayaqi.

Jagora : Hazo jice rana,
'Y/Amsh : Goge mai kashe molo,
: Gogarma ta Iro.
: Gagara badau 'yak Kaso,
: Ta Muhamman Dosau 'yam mayaqi.

Jagora : Hazo jice rana, x^2
'Y/Amsh : Goge mai kashe molo,
: Gogarma ta Iro. x^2

Jagora : Ta Alhaji Madogara, x^2
'Y/Amshi : Inna ta yi gadon Ali qanen Mayaqi. x^2
: Gagarabadau 'yak Kaso,
: Ta Muhamman Dosau 'yam mayaqi.

Jagora : In na tsira hillanci, x^2
'Y/Amshi : Inna sai ta gane,

---

118 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{143}$ $^1/_4$ - AL $^1/_{145}$ $^1/_5$.

: Ba sai na hwaxi ba. x^2
Jagora : Hillancin ga da nis samo,
'Y/Amshi : Inna ko xiyan hillani ba su yi nai,
: Gagarabadau 'yak Kaso,
: Ta Muhamman Dosau 'yam mayaqi.

Jagora : Yara ku bar wani hillanci,
'Y/Amshi : Duk abun da ta saba shi za ta ban ne.
: Gagarabadau 'yak Kaso,
: Ta Muhamman Dosau 'yam mayaqi.
Jagora : Hito bari gaugawa, x^2
'Y/Amshi : Yad durumbu Inna taka sannu-sannu. x^2
Jagora : Nan qasaf fadamar Kanwa, x^2
'Y/Amshi : Ko da wane hali,
: Ba wani mai wuce ki,
: Gagarabadau 'yak Kaso,
: Ta Muhamman Dosau 'yam mayaqi. x^2

Jagora : Jikanyar Jari shirarra,
'Y/Amshi : Sannu da niyya,
: Sannu da yau da gobe,
Jagora : Jikanyar mai hana noma,
'Y/Amshi : Sannu da niyya,
: Sannu da yau da gobe,
Jagora : 'Yam mai dala da rani,
'Y/Amshi : Sannu da niyya,
: Sannu da yau da gobe,
: Gagarabadau 'yak Kaso,
: Ta Muhamman Dosau 'yam mayaqi.

Jagora : Inna ke nika kallo, x^2
'Y/Amshi : Ke nika dibi,
: Ba dibin kawai ba. x^2

Jagora : Uwab Bunu uwas Salau, x^2
'Y/Amshi : Mai rabo ga Allah,
: Mai kullum zumunta, x^2
: Gagarabadau 'yak Kaso,
: Ta Muhamman Dosau 'yam mayaqi.

Jagora : Ta Alhaji Madogara, x^2
'Y/Amshi : Inna ta yi gadon Ali qanen Mayaqi.
: Gagarabadau 'yak Kaso,
: Ta Muhamman Dosau 'yam mayaqi. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Zazzau,
Alhaji Shehu Idris (1975-)[119]*,*

13. *Gindin Waqa : Uban Na Allah uban Madauci ,*
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Alhaji Mani ba shi qin kowa, x^2
: Komi kac ce yanai ma,
: Don bai tsare qa'ida ba, x^2
'Y/Amshi : Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki Uban Iya, x^2
'Y/Amshi : Bajimin Madami,
: Na zaka in gai da qulle-qulle. x^2

Jagora : Ga wani ya tsara qulle-qulle, x^2
'Y/Amshi : Yau daxa qarya ta qule mai,
: Yau wane ba haka nan a kai ba,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe. x^2

Jagora : Sanqira zo za ni saqo,
'Y/Amshi : Ga saqo nan zan gaya ma,
: Sai ka tashi ka iy da saqo.

Jagora : Ga motoci ba iyaka,

---

119 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{50}$ $^1/_1$.

‘Y/Amshi : Sai a sami guda a ba mu,
: Uban Na Allah uban Madauci .

Jagora : Sarki da hanquri aka tsara taro, x^2
‘Y/Amshi : Ka diba duk kwararon qasag ga,
: Duk Shehu, Alhaji ya haxe su, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.
Jagora : Aminu ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Muhammadu ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Yamusa ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Yamusa ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Kuma Kabiru ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Yamusa ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Xahiru ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Muhammadu ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Abdulkarimu ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Alhaji Shata ya hwaxa man, x^2
‘Y/Amshi : Ya ce Zariya ba a zambo,
: In makixi yas shirya zambo,

: Alhaji wawa na buge shi da gora,
: Yanzu ta hau wuyanai, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Malam Na-Allah, x^2
: Sannu da kai-da-kawo,
'Y/Amshi : Ya je Legas lahiya lau,
: Ya zaka lahiya lau, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Jekadiyar Zazzau Bagobira, x^2
'Y/Amshi : Allah ya daxe da ranta,
: Tun da ba ta buki da wasa, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : To, matana bana sun yi dace, x^2
'Y/Amshi : Kai ko da gani,
: Ga saqo ka ce ba su wuri da kansu, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki uban Iya, x^2
'Y/Amshi : Bajimin Madami,
: Na zaka in gai da qulle-qulle, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Birnin Zazzau za ni sabka, x^2
'Y/Amshi : In ishe sarki lahiya lau,
: Don mu sami abin tavawa, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Zazzau,
Alhaji Shehu Idris (1975-)[120]*,*
Gindin Waqa : Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Alhaji Mani ba shi qin kowa,
: Komi kac ce yanai ma,
: Shehu bai iya za'ida ba,
'Y/Amshi : Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Birnin Zazzau za ni sabka, x^2
'Y/Amshi : In ishe sarki lahiya lau,
: Don mu sami abin tavawa. x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki Uban Iya, x^2
'Y/Amshi : Bajimin Madami,
: Don kak ka yadda da qulle-qulle. x^2

Jagora : Ga wani ya tsira qulle-qulle,
'Y/Amshi : Ya naxa qarya ta qule mai,
: Yau wane ba haka nan a kai ba.
Jagora : Ga wani ya tsira xame-xame,
'Y/Amshi : Ya naxa qarya ta qule mai,
: Yau wane ba haka nan a kai ba,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

---

120 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{75}$ $^1/_1$.

Jagora : Alhaji Shata ya hwaxa min, x^2
‘Y/Amshi : Yac ce Zariya ba a zambo,
: Dum makixi yas shirya zambo,
: Alhaji wawa na buge shi da gora,
: Yanzu ta hau wuyanai, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Ai da hanquri aka tsara taro,
‘Y/Amshi : Ka diba duk kwararon qasag ga,
: Duk Shehu, Alhaji ya haxe su.
Jagora : Sarki da hanquri aka tsara taro,
‘Y/Amshi : Ka diba duk kwararon qasag ga,
: Duk Shehu, Alhaji ya haxe su,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Kabiru ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : To, Jahwaru ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Muhammadu ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Yamusa ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Muhammadu ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu.
Jagora : Abdulkarimu ya yi riqo Jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al’amarin Jiharsu,
: Uban Na Allah uban Madauci , x^3
: Shehu sannu da yau da gobe. x^3

Jagora : Sarki ya xauke marayu,
‘Y/Amshi : Ga kuma ya xau mai uwaye,
: Shehu Alhaji ya save su.
Jagora : Sarki ya xauke guramu,
‘Y/Amshi : Ga kuma ya xau mai qahwahu,
: Shehu Alhaji ya save su.
Jagora : Sarki ya xauke makahi,
‘Y/Amshi : Ga kuma ya xau mai idanu,
: Shehu Alhaji ya save su,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki uban Iya, x^2
‘Y/Amshi : Bajimin Madami,
: Don kak ka yadda da qulle-qulle. x^2

Jagora : Sanqira zo za ni saqo,
‘Y/Amshi : Ga saqo nan zan hwaxa ma,
: Sai ka tashi ka iy da saqo.
Jagora : Alhaji Sanqira zo za ni saqo,
‘Y/Amshi : Ga saqo nan zan hwaxa ma,
: Sai ka tashi ka iy da saqo,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Naira xari bakwai Sarki yab ba ni,
‘Y/Amshi : In bayanka uban Madauci ,
: Babu mai kyauta hakan ga.
Jagora : Naira xari bakwai Sarki yab bak kan,
‘Y/Amshi : In bayanka uban Madauci ,
: Babu mai kyauta hakan ga.
Jagora : Riga ishirin Sarki ya ban ni,
‘Y/Amshi : In bayanka uban Madauci ,
: Babu mai kyauta hakan ga.
Jagora : Ga riga ishirin Sarki ya ba ni,
‘Y/Amshi : In bayanka uban Madauci ,
: Babu mai kyauta hakan ga.

Jagora : Alkyabbag ga da Sarki yas shirya min,
‘Y/Amshi : In bayanka uban Madauci ,
: Babu mai kyauta hakan ga.
Jagora : Ga Xantasala da Sarki yas shirya min
‘Y/Amshi : In bayanka uban Madauci ,
: Babu mai kyauta hakan ga,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Malam Na-Allah, x^2
: Sannu da kai-da-kawo,
‘Y/Amshi : Ya zo Legas lahiya lau Na-Allah,
: Ya zaka lahiya lau, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Jekadiyar Zazzau Bagobira, x^2
‘Y/Amshi : Allah ya daxe da ranta,
: Tun da ba ta buki da wasa, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Alhaji Mani ba shi qin kowa,
: Komi kac ce yanai ma,
: Shehu bai iya za’ida ba,
‘Y/Amshi : Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki Uban Iya, x^2
‘Y/Amshi : Bajimin Madami,
: Don kak ka yadda da qulle-qulle,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe. x^2

Jagora : Sarki ya ban huhu xan takarda,
‘Y/Amshi : Sabon Birni za ni saqo,
: Can a kai shi ga masu ci nai.

Jagora : Sarki ya ban goro xan takarda,
‘Y/Amshi : Sabon Birni za ni saqo,
: Can a kai shi ga masu ci nai.

Jagora : Matana bana sun yi dace,
‘Y/Amshi : Mai kai goro ka iy da saqo,
: Ka ce a ba su su sami wuri da kansu.
Jagora : To, matana bana kun yi dace,
‘Y/Amshi : Mai kai goro ka ida saqo,
: Ka ce a ba su su sami wuri da kansu,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki ya tara taro, x^2
‘Y/Amshi : Ka diba duk kwararon jihag ga,
: Shehu, Alhaji duy ya save su, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Alhaji Mani ba shi qin kowa,
: Komi kac ce yanai ma,
: Shehu bai iya za’ida ba,
‘Y/Amshi : Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki Uban Iya,
‘Y/Amshi : Bajimin Madami,
: Don kak ka yadda da qulle-qulle.

Jagora : Ga wani ya tsira qulle-qulle,
‘Y/Amshi : Ya naxa qarya ta qule mai,
: Yau wane ba haka nan a kai ba,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Ga wani ya tsira xame-xame,
‘Y/Amshi : Ya naxa qarya ta qule mai,
: Yau wane ba haka nan a kai ba,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Zazzau, Alhaji Shehu Idris (1975-)[121]*,*
Gindin Waqa : Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki ya xauke marayu,
'Y/ Amshi : Kuma ya xau mai uwaye,
: Duka Alhaji ya save su,
'Y/Amshi : Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Alhaji Mani ba shi qin kowa,
: Komi kac ce yanai ma,
: Shehu bai iya za'ida ba,
'Y/Amshi : Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki Uban Iya, x^2
'Y/Amshi : Bajimin Madami,
: Don kak ka yadda da qulle-qulle. x^2

Jagora : Ga wani ya tsira qulle-qulle,
'Y/Amshi : Ya naxa qarya ta qule mai,
: Yau wane ba haka nan a kai ba.
Jagora : Ga wani ya tsira xame-xame,
'Y/Amshi : Ya naxa qarya ta qule mai,
: Yau wane ba haka nan a kai ba,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Birnin Zazzau za ni sabka, x^2
'Y/Amshi : In ishe sarki lahiya lau,
: Don mu sami abin tavawa. x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.
Jagora : Sarki da hanquri aka tsara taro, x^2
'Y/Amshi : Ka diba duk kwararon qasag ga,

---

121 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{75}$ $^1/_3$.

: Duk Shehu, Alhaji ya haxe su, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Jahwaru ya yi riqo Jihag ga,
'Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al'amarin Jiharsu.
Jagora : Muhammadu ya yi riqo Jihag ga,
'Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al'amarin Jiharsu.
Jagora : Kuma Kabiru ya yi riqo Jihag ga,
'Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al'amarin Jiharsu.
Jagora : Jahwaru ya yi riqo Jihag ga,
'Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al'amarin Jiharsu.
Jagora : Abdulkarimu ya yi riqo Jihag ga,
'Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al'amarin Jiharsu.
Jagora : Muhammadu ya yi riqo Jihag ga,
'Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al'amarin Jiharsu.
Jagora : Kuma Sambo ya yi riqo Jihag ga,
'Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqonsu,
: Ya riqe al'amarin Jiharsu.
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki ya xauke marayu,
'Y/Amshi : Ga kuma ya xau mai uwaye,
: Shehu Alhaji ya save su.
Jagora : Sarki ya xauke makahi,
'Y/Amshi : Ga kuma ya xau mai idanu,
: Shehu Alhaji ya save su.

Jagora : Sarki ya xauke guramu,
'Y/Amshi : Ga kuma ya xau mai qahwahu,
: Shehu Alhaji ya save su,

: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki uban Iya, x^2
'Y/Amshi : Bajimin Madami,
: Don kak ka yadda da qulle-qulle. x^2

Jagora : Magaji mai hwaure da 'yan tsaka,
'Y/Amshi : Ya yi kirana ya hwaxa min,
: Gobe Kaduna za mu,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Alhaji Shata ya hwaxa min, x^2
'Y/Amshi : Yac ce Zariya ba a zambo,
: Dum makaxi yas shirya zambo,
: Alhaji wawa na buge shi da gora,
: Yanzu ta hau wuyanai, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Ai da hanquri aka tsara taro,
'Y/Amshi : Ka diba duk kwararon qasag ga,
: Duk Shehu, Alhaji ya haxe su,
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Alhaji Mani ba shi qin kowa, x^2
: Komi kac ce yanai ma,
: Shehu bai iya za'ida ba, x^2
'Y/Amshi : Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Jekadiyar Zazzau Bagobira, x^2
'Y/Amshi : Allah ya daxe da ranta,
: Tun da ba ta buki da wasa, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : To, rigunan ga da kash shira min,
'Y/Amshi : In bayanka Uban Madauci ,
: Babu mai kyauta hakan ga.
Jagora : Naira xari bakwai Sarki yab bak kan, x^2
'Y/Amshi : In bayanka uban Madauci ,
: Babu mai kyauta hakan ga. x^2
Jagora : Riga ishirin Sarki ya bak kan, x^2
'Y/Amshi : In bayanka uban Madauci ,
: Babu mai kyauta hakan ga. x^2
Jagora : Alkyabbag ga da Sarki yas shirya min, x^2
'Y/Amshi : In bayanka uban Madauci ,
: Babu mai kyauta hakan ga. x^2
Jagora : Ga Xantasala da Sarki yas shirya min, x^2
'Y/Amshi : In bayanka uban Madauci ,
: Babu mai kyauta hakan ga, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Jagora : Sarki ya ban huhu xan takarda,
'Y/Amshi : Sabon Birni za ni saqo,
: Can a kai shi ga masu ci nai.
Jagora : Matana bana kun yi dace,
'Y/Amshi : Mai kai goro ka ida saqo,
: Ka ce a ba su su sami wuri da kansu.

Jagora : Malam Na Allah Sannu da kai-da-kawo, x^2
'Y/Amshi : Ya zo Legas lahiya lau,
: Na AllahYa zaka lahiya lau, x^2
: Uban Na Allah uban Madauci ,
: Shehu sannu da yau da gobe.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni
Mai Waqa : Alhaji Shu'aibu Salau xan Musa[122]*,*

14. *Gindin Waqa : Ya wuce tantama,*

---

122 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{143}$ $^1/_2$.

: Shi Alhaji Shu'aibu zamaninai ya kai.

Jagora : Jikan manya, jikan Alhaji yaka birnin daga,
'Y/Amshi : Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu'aibu zamaninai ya kai.

Jagora : Alhaji jikan manya,
'Y/Amshi : Jikan Alhaji yaka birnin daga.

Jagora : Allah yai maka hairan, x^2
'Y/Amshi : Allah bai yi ka don ka sha haushi ba, x^2
: Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu'aibu zamaninai ya kai.

Jagora : Sa'ad da munka tashi Sabon Birni, x^2
'Y/Amshi : Ba mu da ukku xin Tsohonai,
: In bayan sarautar Allah,
: Babu abun da yaz zama kullum,
: Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu'aibu zamaninai ya kai. x^2

Jagora : Kowas sha hura ba nono, x^2
'Y/Amshi : Ban yi zaton akwai daxi ba. x^2

Jagora : Kowas sha miya ba nama,
'Y/Amshi : Ban yi zaton akwai daxi ba,
: Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu'aibu zamaninai ya kai.

Jagora : Ni da na sauka Sabon Birni,
: To, na sauka ko han na kwan,
'Y/Amshi : Na ishe yara na wata waqa,
: To, ko yara kau ko yam mata,
: Sun ce wanda yas sai nama,
: Ya xara wanda yas sai kihi,
: Ya wuce tantama,

: Shi Alhaji Shu’aibu zamaninai ya kai.

Jagora : Ni da dai nas sauka Sabon Birni,
: To, na sauka ko han na kwan,
'Y/Amshi : Na ishe yara na wata waqa,
: To, ko yara kau ko ‘yam mata,
: Sun ce wanda yas sai nama,
: Ya xara wanda yas sai kihi.

Jagora : To kuma wanda yas sai anta,
‘Y/Amshi : Ya xara wanda yas sai hanji,
Jagora : To kuma wanda yas sai doya,
‘Y/Amshi : Ya xara wanda yas sai gwaza,
Jagora : To kuma wanda yas sai doki,
‘Y/Amshi : Ya xara wanda yas sai jakki,
: Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu’aibu zamaninai ya kai.

Jagora : Kwanakki da niz zo gaisai, x^2
: Naira arba’in yab bayat,
'Y/Amshi : To, kuma ga turamai ya bai,
: Ya kai man buhuhwan gero,
: Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu’aibu zamaninai ya kai. x^2

Jagora : Kuma ga naira xari yab bayat, x^2
‘Y/Amshi : Ya ce min a sai min gero, x^2
: Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu’aibu zamaninai ya kai.

Jagora : Alhaji xan Ciyaman xan Sarki,
‘Y/Amshi : Wada kan nuhwa sai ka yi,
: Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu’aibu zamaninai ya kai.

Jagora : Alhaji xan Ciyaman xan Sarki, x^3
‘Y/Amshi : Wada kan nuhwa sai ka yi. x^3

Jagora : Alhaji xan Salau xan Musa x^2
'Y/Amshi : Al'amarinka ya sha dama. x^2
: Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu'aibu zamaninai ya kai.

Jagora : Alhaji xan Salau xan Musa x^2
'Y/Amshi : Al'amarinka ya sha dama. x^2
: Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu'aibu zamaninai ya kai.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ibrahim (1970-1975)[123]*,*

15. *Gindin Waqa : Da shiri yat tasa,*
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.

---

123 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{144}$ $^1/_6$ - AL $^1/_{146}$ $^1/_2$.

Jagora : Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai,
'Y/Amshi : Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.

Jagora : Da arziki da wadata, x^2
'Y/Amshi : Ai zaman duniya sai an sa hanquri, x^2
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.
Jagora : Na biyo bisa hanya,
'Y/Amshi : Ko da xai ba ni wasan daji kakkarai,
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.

Jagora : Kakkarai qaqqarqa, x^2
'Y/Amshi : Kakkarai in ji zabin daji masu qwai. x^2
Jagora : Ashe mutanen birni,
'Y/Amshi : Su ka huma mutanen daji gargaxi.

Jagora : Iro mutanen birni,
'Y/Amshi : Su ka huma mutanen daji gargaxi,
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.

Jagora : Ashe duniya gishiri ta, x^2
'Y/Amshi : Wane kay ya sake ta koma daudawa,
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai. x^2
Jagora : Gaba da baya qarhin doki, x^2
'Y/Amshi : In dai batu, batun Gobir na,
: Wada kuk ka hwaxi Ibrahim na ciki,
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai. x^2

Jagora : Gidan Muhamman Jadi,
'Y/Amshi : Jadi xan Tubali sai Allah bai yi ba.

Jagora : Gidan Muhamman Jadi,
'Y/Amshi : Yau gidan Tubali sai Allah bai yi ba.

Jagora : Ina bixar iyalin Jangwarzo, x^2
'Y/Amshi : Ashe Iro na nan jikan mai gida, x^2
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.

Jagora : Iro da yab ban hwanda, x^2
'Y/Amshi : Wag ga hwandar Kano ta yac ce in hawo, x^2
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.

Jagora : Ga hwandar hwan xari biyat an ba ni,
'Y/Amshi : Tana da ‘yan gyare-gyare ni ko ban yi ba,
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.

Jagora : Ga hwandar da Iro yab ba mu,
'Y/Amshi : Tana da ‘yan gyare-gyare ni ko ban yi ba.

Jagora : Hwandar ba ta da Oda, x^2
'Y/Amshi : Ga ta ba ta da mai Musa ko na gani. x^2

Jagora : Musa ya qasaita,
'Y/Amshi : Abin da duk na hwaxi Musa kau na yi min.

Jagora : Musa ya gawurta,
'Y/Amshi : Abin da duk na hwaxi Musa kau na yi min.

Jagora : Wannan Musa ya qasaita,
'Y/Amshi : Abin da duk na hwaxi Musa kau na yi min,
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.

Jagora : Mamman bakanike ya kyauta, x^3
'Y/Amshi : Yayi min gyare-gyaren Hwanda ba kuxi, x^3
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.

Jagora : Da arziki da wadata, x^2
'Y/Amshi : Ai zaman duniya sai an sa hanquri, x^2

: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Zazzau,
Alhaji Shehu Idris (1975-)[124]*,*

24. *Gindin Waqa : Kak ka yarda da raini uban Baraya,*
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

Jagora : Kak ka yarda da raini uban Baraya, x^2
'Y/Amshi : Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma. x^2

Jagora : Zariya, Zariya, Zazzau maza da mata,
'Y/Amshi : Duk wanda ba ya da mota ya je a sai mai,

---

124 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{52}$ $^{1}/_{7}$.

: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

Jagora : Lalle ina ganin balbela da ita da shanu,
'Y/Amshi : Ai ko da yaushe nan taka samun abin da tac ci,
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.
Jagora : Ni dai ina ganin balbela da ita da shanu,
'Y/Amshi : Ai ko da yaushe nan taka samun abin da tac ci,
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

Jagora : Xan'anace ya yi jawabi shi da Shata, x^2
'Y/Amshi : Ai ko Sa'idu ya yi jawabi da shi da Qwairo. x^2

Jagora : Manyan maroqa ku taho mu tai ga sarki, x^2
'Y/Amshi : Duk wanda ba ya da mota ya zo ya sai mai, x^2
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

Jagora : Ai ga ni na zaka Zazzau mu gai da sarki,
'Y/Amshi : Banga Habiba ba kuma ban ga Mariya ba,
: Ai ko su Binta ba su da halin su daqile ni,
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.
J agora : Maidaji ya zaka Zazzau ya gai da sarki,
'Y/Amshi : Ban ga Habiba ba kuma ban ga Mariya ba,
: Ai ko su Binta ba su da halin su daqile ni,
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

Jagora : Lalle ina ganin balbela da ita da shanu,
'Y/Amshi : Ai ko da yaushe nan taka samun abin da tac ci,
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

Jagora : Kai ab ubangijin Sanqira da shi da wawa, x^2
'Y/Amshi : Sarki na Iro mai katse harshen mutum da dama, x^2
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

Jagora : Kai ab ubangijin Sanqira da shi da wawa,
'Y/Amshi : Sarki na Iro mai katse harshen mutum da dama,
Jagora : Kai ab ubangijin Kakaki da shi da Hwade,
'Y/Amshi : Sarki na Iro mai katse harshen mutum da dama,
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

Jagora : Ai ga ni na zaka Zazzau mu gai da sarki,
'Y/Amshi : Ban ga Habiba ba kuma banga Mariya ba,
: Ai ko su Binta ba su da halin su daqile ni,
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

Jagora : Ni dai ina ganin balbela da ita da shanu, x^2
'Y/Amshi : Ai ko da yaushe nan taka samun abin da tac ci, x^2
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

Jagora : Manyan maroqa ku taho mu tai ga sarki, x^2
'Y/Amshi : Duk wanda ba ya da mota ya zo a sai mai, x^2
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Buza ta Qasar Nijar,
Alhaji Abdussalam Buza [125]*,*
17. *Gindin Waqa : Xansidi amshi sandar mulki qasatai,*
: Mai Buza Xanhassan mai taro hannu.

Jagora : In dai na gyara ganguna na yi shirin kixina,
'Y/Amshi : To, Maidaji mai kixi wajjen Buza yay yi.
Jagora : In dai na gyara ganguna na yi shirin kixana,
'Y/Amshi : To, maidaji mai kixi wajjen Buza yay yi,

---

125 An sami wannan rerawa ne a Cikin Hirar da aka Saurara Tsakanin Makaxa Maidaji da Alhaji Ibrahim Xiso, Rediyo Rima, Sakkwato. Akwai Wannan Hira a Kammalenta a Cikin Wannan Kundi a Rataye na Xaya, Shafi na 302.

: Xansidi amshi sandar mulki qasatai,
: Mai Bunza Xanhassan mai taro hannu.

Jagora : Ga ni na taho kixin sarkin Buza sabo,
‘Y/Amshi : Kakaki da ganguma kowa ga shi ya zo,
: Daxa sai wanda ba wuri xai ab bai taho ba.
Jagora : Alhaji na taho kixin sarkin Buza sabo,
‘Y/Amshi : Kakaki da ganguma kowa ga shi ya zo,
: Daxa sai wanda ba wuri xai ab bai taho ba,
: Xansidi amshi sandar mulki qasatai,
: Mai Buza Xanhassan mai taro hannu.

Jagora : Jakara namu wag ga bakka tai yamma daidai,
: Kuma wadda ag Gufur ta yare wa daidai,
‘Y/Amshi : Duy ya haske duniya kowa na ta kallo,
: Xansidi amshi sandar mulki qasatai,
: Mai Buza Xanhassan mai taro hannu.

Jagora : Jakara namu wag ga bakka tai yamma daidai,
: Kuma wadda ag Gufur ta yare wa daidai,
‘Y/Amshi : Duy ya haske duniya kowa na ta kallo.

Jagora : In dai ka ishe mutane sun taru garka,
‘Y/Amshi : In dai ba munaqisa kuma dai ba mahwari,
: Kai ka san akwai mutanen Allah wurinai.
Jagora : In dai ka ishe mutane sun taru garka,
‘Y/Amshi : In dai ba munaqisa kuma ba mahwari,
: Kai ka sana akwai mutanen Allah wurinai,
: Xansidi amshi sandar mulki qasatai,
: Mai Buza Xanhassan mai taro hannu.

Jagora : Da na samu kurciya ko ko damisa ne,
: Ko ko tantabara uwat tsuntsaye na sami,
: Da na ba da saqo,
: Saqonnin da ba ni ba za ta zo ta kwana ba,
: In tac ce gari da nisa in ba da taguwa,
: In tac ce gari da yunwa in ba da gari,
: In tac ce gari da qishirwa in ba da salka,
: In tac ce gari da xari in ba da bargo

‘Y/Amshi : In ta zo tac ce matan Falgore qasatai,
: Xansidi amshi sandar mulki qasatai,
: Mai Buza Xanhassan mai taro hannu.

Jagora : In dai ta zo tac ce matan Falgore qasatai, x^2
‘Y/Amshi : Ga darnin da yab bari ya koma katanga,
: Xansidi amshi sandar mulki qasatai,
: Mai Bunza Xanhassan mai taro hannu. x^2

Jagora : In dai na gyara ganguna na yi shirin kixana,
‘Y/Amshi : To, maidaji mai kixi wajjen Bunza yay yi,
: Xansidi amshi sandar mulki qasatai,
: Mai Buza Xanhassan mai taro hannu.

Makaxi : Alhaji Sa’idu Rambaxawa Sabon Birni,
Waqa : Waqar Noma ta ‘Yar Buhari[126]*,*

18. *Gindin Waqa : Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,*
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hasti,
‘Y/Amshi : Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.
Jagora : Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hasti,
‘Y/Amshi : Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Ka ga kayan gona iri-iri suna cikin qasanmu,
‘Y/Amshi : Don Allah ku qara shuka mana mu ga gujjiya.

---

126 An sami wannan rerawa ne a cikin hirar da aka saurara tsakanin Makaxa Maidaji da Alhaji Ibrahim Xiso, Rediyo Rima, Sakkwato. Akwai Wannan hira a kammalenta a cikin wannan kundi a Rataye na Biyu, Shafi na 302.

Jagora : Sai an sa gero a shuka dawa da su gujjiya,
‘Y/Amshi : A sa masara kuma a shuka rogo a yi lawuru.
Jagora : Sai an sa gero a shuka dawa da su gujjiya, x^2
‘Y/Amshi : A sa masara kuma a shuka rogo a yi lawuru,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro. x^2

Jagora : To, ashe Likita bai da maganin yunwa,
‘Y/Amshi : Wanga magani sai a bixo hura.
Jagora : Na ji Malami bai da maganin yunwa,
‘Y/Amshi : Wanga magani sai a bixo hura.
Jagora : Had da ‘yan Bori ba su maganin yunwa,
‘Y/Amshi : Wanga magani sai a bixo hura.
Jagora : Had da Bokaye ba su maganin yunwa,
‘Y/Amshi : Wanga magani sai a bixo hura.
Jagora : Maganin yunwa kudaku da rogo da quli-quli,
‘Y/Amshi : In anka haxa su kuma a dawo ga hwaro-hwaro,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.
Jagora : Wanda ba tsaba ko,
‘Y/Amshi : Da yaushe na ba shi zama gida,
: Sai ka ga ya bar gidansu,
: Ya kama gidan wani,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Na ji yunwa mai sa a sai da,
: Shanu da tumaki da awaki,
‘Y/Amshi : Kuma har a tsai da sallah a sawo hatsi,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Na ji qohin xaki kila sa mata su sawo gado,
‘Y/Amshi : Su shirya katihwa su shirga kwano su yi labule,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Maccen da babu qoshi, x^2

‘Y/Amshi : In ka gane ta kayanta baqi qirin,
: Kamat tanda ko da yaushe kayanta masat-masat,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro. x^2

Jagora : Ga maccen da ac cikin kubli, x^2
: Na gano ta da bargonta da gyantsama,
‘Y/Amshi : Tana ratsa gida-gida akan ba ta hwaro-hwaro,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro. x^2

Jagora : Ga wanda ba tsaba ko,
‘Y/Amshi : Da yaushe na ba shi zama gida,
: Sai ka ga ya bar gidansu,
: Ya kama gidan wani,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Gwanon canza wurin zama,
‘Y/Amshi : Yunwa,
: Da mutum yana canza wurin zama,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Gwanon canza wurin zama, x^2
‘Y/Amshi : Yunwa,
: Da mutum yana soke tsakad dare,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro. x^2

Jagora : Sai an sa gero a shuka dawa da su gujjiya, x^2
‘Y/Amshi : A sa masara kuma a shuka rogo a yi lawuru,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro. x^2

Jagora : Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hasti, x^2
‘Y/Amshi : Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,
Waqa : Waqar Noma ta 'Yar Buhari[127]*,*
Gindin Waqa : Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi, x^2
'Y/Amshi : Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro. x^2

Jagora : Na ji kayan gona iri-iri suna cikin qasanmu,
'Y/Amshi : Don Allah ku qara shuka mana mu ga gujjiya.

Jagora : Ka ga kayan gona iri-iri suna cikin qasanmu,
'Y/Amshi : Don Allah ku qara shuka mana mu ga gujjiya.

Jagora : Sai an sa gero a shuka dawa da su gujjiya,
'Y/Amshi : A sa masara kuma a shuka rogo a yi lawuru.
Jagora : Sai an sa gero a shuka dawa da su gujjiya,

127 An sami wannan rerawa ne a cikin hirar da aka saurara tsakanin Makaxa Maidaji da Alhaji Ibrahim Xiso, Rediyo Rima, Sakkwato. Akwai wannan hira a kammalenta a cikin wannan Kundi a Rataye na Biyu, Shafi na 302.

‘Y/Amshi : A sa masara kuma a shuka rogo a yi lawuru,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : To, ashe Likita bai da maganin yunwa,
‘Y/Amshi : Wanga magani sai a bixo hura.
Jagora : Na ji Malami bai da maganin yunwa,
‘Y/Amshi : Wanga magani sai a bixo hura.
Jagora : Had da ‘yan Bori ba su maganin yunwa,
‘Y/Amshi : Wanga magani sai a bixo hura.
Jagora : Had da Bokaye ba su maganin yunwa,
‘Y/Amshi : Wanga magani sai a bixo hura.
Jagora : Maganin yunwa kudaku da rogo da quli-quli,
‘Y/Amshi : In anka haxa su kuma a dawo ga hwaro-hwaro,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.
Jagora : Wanda ba tsaba ko,
‘Y/Amshi : Da yaushe na ba shi zama gida,
: Sai ka ga ya bar gidansu,
: Ya kama gidan wani,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Na ji yunwa mai sa a sai da,
: Shanu da tumaki da awaki,
‘Y/Amshi : Kuma har a tsai da sallah a sawo hatsi,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Ga maccen da ac cikin kubli,
: Na gano ta da bargonta da gyantsama,
‘Y/Amshi : Tana ratsa gida-gida akan ba ta hwaro-hwaro,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Gwanon canza wurin zama,
‘Y/Amshi : Yunwa,
: Da mutum yana canza wurin zama,
: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,

: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

Jagora : Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hasti, x^3
'Y/Amshi : Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro. x^3

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Waqa : Waqar Mata[128]*,*

28. *Gindin Waqa : Mata in ba ku ba gida,*
: Wurin Allah ku ash shikashiki.

Jagora : Mata in ba ku ba gida, x^2
'Y/Amshi : Wurin Allah ku ash shikashiki. x^2

Jagora : Mata ku yi aure kuma, x^2
'Y/Amshi : Ku zan ka addini shi ag gishirin zama. x^2

Jagora : Cikin nassi aka aure, x^2
'Y/Amshi : Kuma cikin nassi aka tagazag gida, x^2
: Mata in ba ku ba gida,
: Wurin Allah ku ash shikashiki.

Jagora : Yara kun ji kixin manya ko ba ku ji,
'Y/Amshi : Ko kun yin bori ba ku jituwa,
: Mata in ba ku ba gida,
: Wurin Allah ku ash shikashiki.

---

128 An Sami Wannan Rerawa ne a Hirar da aka Saurara Tsakanin Makaxa Maidaji da Alhaji Ibrahim Xiso na Rima Rediyo, Jihar Sakkwato. Akwai Wannan Hira a Kammalenta a Cikin Rataye na Xaya na Wannan Kundi.

Jagora : Maccen da ka aure, x^2
'Y/Amshi : Tai hikima ki wanka daga ciki, x^2
: Mata in ba ku ba gida,
: Wurin Allah ku ash shikashiki.
Jagora : Maccen da ba ta aure,
'Y/Amshi : Fatsima na can na watsa mata qasa,
: Mata in ba ku ba gida,
: Wurin Allah ku ash shikashiki.

Jagora : Yara kun ji kixin manya ko ba ku ji, x^2
'Y/Amshi : Ko gun yin bori ba ku jituwa, x^2
: Mata in ba ku ba gida,
: Wurin Allah ku ash shikashiki.

Jagora : Ni shawan mata nika gani, x^3
'Y/Amshi : Wurin girki nan za ka tuwo, x^3
: Mata in ba ku ba gida,
: Wurin ku ada daga ciki.

Jagora : Komi rani ko da damina,
: A sa su daka kuma za su yi,
: Su xora dakan tsaba su yi,
'Y/Amshi : Suna waqa wasu har suna rawa,
: Mata in ba ku ba gida,
: Wurin ku ada daga ciki.

Jagora : Mata in ba ku ba gida,
'Y/Amshi : Wurin Allah ku ash shikashiki.

Jagora : Mata ku yi aure kuma,
'Y/Amshi : Ku zan ka addini shi ag gishirin zama.

Jagora : Cikin nassi aka aure,
'Y/Amshi : Kuma cikin nassi aka tagaza gida,
: Mata in ba ku ba gida,
: Wurin ku ada daga ciki.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Ali Abubakar 'Yankuzo[129]*,*
20. *Gindin Waqa : A gai min da Alhaji Ali na 'Yankuzo,*
: Duniya ya gyara wurin zama.

Jagora : A gai min da Alhaji Ali na 'Yankuzo, x^2
'Y/Amshi : Duniya ta gyara wurin zama. x^2

Jagora : Duniya ta gyara gida, x^2
'Y/Amshi : Had da lahira ya shirya wurin zama. x^2

Jagora : Ku gai min da Alhaji Ali qwarai,
'Y/Amshi : Had da mu muna gaishe shi qwarai-qwarai.

Jagora : 'Ya'yana ku gai min da Alhaji Ali qwarai,
'Y/Amshi : Had da mu muna gaishe shi qwarai-qwarai,
: A gai min da Alhaji Ali na 'Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Alhaji na Hassan sarkin hanquri, x^2
'Y/Amshi : Jalla wahidin ya ba ka halin qwarai, x^2
: A gai min da Alhaji Ali na 'Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Ka riqe sabba ka riqe danginka,

---

129 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{52}$ $^{1}/_{4}$.

‘Y/Amshi : Ya riqe kayansa kwarai,
: Wanda bai da mata sai ka ya yi mai,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Da nit taho das Sabon Birni, x^2
‘Y/Amshi : Nib bi ta Tsahe nit tahi ‘Yankuzo,
: In na yi dace ni ishe Ali sai,
: Na yi roqo nai ya yi min gida,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama. x^2

Jagora : Gobirawa ‘yan ga aiki duw,
‘Y/Amshi : Wani na niyyay ya gano gida,
: Ya za ya ce ya kama wurin zama,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Gobirawa ‘yan ga aiki duw,
‘Y/Amshi : Wani na niyyay ya gano gida,
: Ya za ya ce ya kama wurin zama.

Jagora : Ku zo ku ce na kama gida, x^2
‘Y/Amshi : Ali had da mata za shi yi min bana. x^2

Jagora : Ku zo ku ce na kama gida,
‘Y/Amshi : Ali had da mata za shi yi min bana,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Da ka ga sufar xan sarki, x^2
‘Y/Amshi : Yara kun ga mai iya ta da gida,
: Ba matsalar ka tashi gidanku na ainihi, x^2
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Xan zaki hay ya qasura, x^2
‘Y/Amshi : Hay ya yi jan wuya ya hiddo qwarai-qwarai, x^2
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Mijin Halima mijin Hajiya Mairo,
‘Y/Amshi : Allah ya ba ku hwaro-hwaro.

Jagora : Mijin Halima mijin Hajiya Mairo,
‘Y/Amshi : Allah ya ba ku hwaro-hwaro,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Gohe na gode mai,
‘Y/Amshi : Har na yi godiya ina gaishe shi qwarai-qwarai,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Na Isan Mayana Alhaji Ali,
‘Y/Amshi : Magajin Bala magajin Bello Madogara,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Duniya ta gyara gida, x^2
‘Y/Amshi : Had da lahira ya shirya wurin zama. x^2

Jagora : Ku gai min da Alhaji Ali qwarai, x^2
‘Y/Amshi : Had da mu muna gaishe shi qwarai-qwarai. x^2

Jagora : ‘Ya’yana ku gai min da Alhaji Ali qwarai, x^2
‘Y/Amshi : Had da mu muna gaishe shi qwarai-qwarai,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama. x^2

Jagora : Alhaji na Hassan sarkin hanquri,
‘Y/Amshi : Jalla wahidin ya ba ka halin qwarai.

Jagora : Alhaji goga na Abubakar sarkin hanquri, x^2
‘Y/Amshi : Jalla wahidin ya ba ka halin qwarai, x^2
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Ka riqe sabba ka riqe danginka, x^2

‘Y/Amshi : Ya riqe kayansa kwarai, x^2
: Wanda bai da mata sai ka ya yi mai,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Ku zo ku ce na kama gida,
‘Y/Amshi : Ali had da mata za shi yi min bana,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Xan zaki hay ya qasura,
‘Y/Amshi : Hay ya yi jan wuya ya hiddo qwarai-qwarai,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : Mijin Halima mijin Hajiya Mairo,
‘Y/Amshi : Allah ya ba ku hwaro-hwaro,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.

Jagora : A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo, x^2
‘Y/Amshi : Duniya ta gyara wurin zama. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Mamman Kuzo[130]*,*
21. *Gindin Waqa : Madogara Alhaji Mamman,*
: Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Alhaji Kuzo ka wuce gori, x^2
'Y/Amshi : Tun da kana tare da Allah,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka. x^2

Jagora : Na zo Kaduna don Alhaji Mamman, x^2
'Y/Amshi : Saboda in sami abinci, x^2
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Shi wanda ax xauke ga hanya,
'Y/Amshi : Ba ya zuwa sarma ga daji,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Ai wanda ax xauke ga hanya,
'Y/Amshi : Ba ya zuwa sarma da daji,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Alhaji mijin Turai, x^2
'Y/Amshi : Alhaji mijin Hussaina da Habiba, x^2
: Madogara Alhaji Mamman,

---

130 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{52}$ $^1/_4$.

: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Xan Bagobiri ko na ina ne, x^2
'Y/Amshi : Zuwa mu kai mui mishi gado,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka. x^2

Jagora : Ya shirya aure da zumunci, x^3
'Y/Amshi : Yana shirin yara da manya, x^3
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Kuma in magana ba ta da kyawo, x^2
'Y/Amshi : Manya ka yin zaune su gyara,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka. x^2

Jagora : Alhaji Uban Yakuba zaki,
'Y/Amshi : Ba ya gudun takula da manya,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Bajini Bala xan Sani, x^3
'Y/Amshi : Ko da yaushe bai gaji sake ba, x^3
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Alhaji Uban Yakuba zaki,
'Y/Amshi : Ba ya gudun takula da manya,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Ga Xangara ga Alhaji Mamman, x^2
'Y/Amshi : Yau ana shirin shavirigana,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka. x^2

Jagora :Ga naira xari shidda uban,
'Y/Amshi : Yakuba yab ban in buga kwano,

: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Naira xari shidda uban,
‘Y/Amshi : Yakuba yab ban in buga kwano,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Alhaji mijin Turai,
‘Y/Amshi : Alhaji mijin Hussaina da Habiba,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Xan Bagobiri ko na ina ne, x^2
‘Y/Amshi : Zuwa mu kai mui mishi gado,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka. x^2

Jagora : Ya yi shirin Jari da Jadi, x^2
‘Y/Amshi : Ya yi shirin Almu da gauxe, x^2
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Na zo Kaduna don Alhaji Mamman, x^2
‘Y/Amshi : Saboda in sami abinci, x^2
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Shi wanda ax xauke ga hanya,
‘Y/Amshi : Ba ya zuwa sarma da daji,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Ai wanda ax xauke ga hanya,
‘Y/Amshi : Ba ya zuwa sarma da daji,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Shehu Aliyu Shagari,
Tsohon Shugaban Qasar Nijeriya[131]*,*

22. *Gindin Waqa : Na yi mamakin harka tai,*
: Shehu mai daraja Shagari.

Jagora : Shugaban qasa Allah kyauta mai,
'Y/Amshi : Zaman mutane na murna tai,
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari.
Jagora : Shugaban qasa Allah kyauta mai, x^2
'Y/Amshi : Zaman mutane na murna tai, x^2
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari.

Jagora : Shugaba na can na aiki nai,
'Y/Amshi : Yana ta yin gaba bai hwasa ba,
: Yana ta yin aikin al'adu,
: Saboda koyon addini ne,
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari.

Jagora : Shugaba na can na aiki nai,
'Y/Amshi : Yana ta yin gaba bai hwasa ba,
: Yana ta yin aikin al'adu,
: Saboda koyon addini ne.

Jagora : Haba manoma ku kama noma,
'Y/Amshi : Ku zan ka yin aikin al'adu,
: Saboda koyon addini ne.
Jagora : 'Yan makaranta kui ta karatu,
'Y/Amshi : Ku zan ka yin aikin al'adu,

---

131 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{52}$ $^{1}/_{5}$.

: Saboda koyon addini ne.
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari.

Jagora : Kaduna an gyare hanya,
‘Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Zariya an gyare hanya,
‘Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Huntuwa an gyare hanya,
‘Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Tsahe an gyare hanya,
‘Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Kwatarkwashi an gyare hanya,
‘Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta,
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari.

Jagora : Hag Gusau an gyare hanya,
‘Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Qaura an gyare hanya,
‘Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora :Tsahe an gyare hanya,
‘Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Shinkahi an gyare hanya,
‘Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Har Isa an gyare hanya,
‘Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta,
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari.

Jagora : Sabon Birni mu bar garaje,
‘Y/Amshi : Han mu kwalta na kawowa,
: Kowa ga hwanho qahwa tai,
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari.

Jagora : Sabon Birni mu bar garaje,
‘Y/Amshi : Han mu kwalta na kawowa,
: Kowa ga hwanho qahwa tai.

Jagora : A sai mini gida Sabon Birni, x^2
‘Y/Amshi : Sannan kai a sa hitila qohwata,
: Kuma a sa min maigadi na,
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari. x^2

Jagora : Shagari hankali na bai kwanta ba, x^2
‘Y/Amshi : Ni dai rashin mota ya daman,
: Ashe rashin mota ciwo ne,
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari. x^2

Jagora : Ai da ni da ‘yan kamishon wajjenmu, x^2
‘Y/Amshi : Has sun hana min in sai kaji,
: Waxanda za a dahwaman in ci,
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari. x^2

Jagora : Dibi xan wuri kusa bai kai mil ba,
‘Y/Amshi : Suna hwaxin naira-naira ne,
: Abin ga shin ko cin hanci,
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari.

Jagora : Shugaban qasa Allah kyauta mai, x^2
‘Y/Amshi : Zaman mutane na murna tai, x^2
: Na yi mamakin harka tai,
: Shehu mai daraja Shagari.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Garba Nadama[132]*,*
Tsohon Gwamnan Jihar Sakkwato,

23. *Gindin Waqa : Allah za ni roqon ka,*
: In yi biyag gwamna mai girma.

Jagora : Allah za ni roqon ka,
: In yi biyag gwamna mai girma,
'Y/Amshi : Allah zani roqon ka,
: In yi biyag gwamna mai girma.

Jagora : Garba Nadama, x^2
'Y/Amshi : Garba irin ra'ayi nai yana yi min, x^2
: Allah za ni roqonka,
: In yi biyag gwamna mai girma.

Jagora : Garba abin da Allah, x^2
: Na Ibrahim ya kai kullum,
'Y/Amshi : Allah shi ka sa matsuwa,
: Kuma Allah shi ka sa sauqi,
: Allah za ni roqonka,
: In yi biyag gwamna mai girma. x^2

Jagora : Ko can duniya haka, x^2
: Tag gada inji mai turu,
'Y/Amshi : Ka san duniya daxa,
: Ba mai hurce iyaka tai,
: Allah za ni roqonka,
: In yi biyag gwamna mai girma. x^2

Jagora : Kullum hwata nikai, x^2
'Y/Amshi : Allah ya jiqan Shehu Kangiwa. x^2

Jagora : Allah nai addu'a,
'Y/Amshi : Allah ya jiqan Shehu Kangiwa.

---

132 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{52}$ $^{1}/_{6}$.

Jagora : Annabi nai addu'a,
'Y/Amshi : Allah ya jiqan Shehu Kangiwa.
Jagora : Sarkin Musulmi nai addu'a,
'Y/Amshi : Allah ya jiqan Shehu Kangiwa.
Jagora : Waziri da yai addu'a,
'Y/Amshi : Allah ya jiqan Shehu Kangiwa.
Jagora : Kuma Nana da tai addu'a,
'Y/Amshi : Allah ya jiqan Shehu Kangiwa,
: Allah za ni roqonka,
: In yi biyag gwamna mai girma.

Jagora : Don qudura, Irada da Attaura da Linjila, x^2
'Y/Amshi : Don Allah don Annabi,
: Ai ta ibadar riqon juna,
: Allah za ni roqonka,
: In yi biyag gwamna mai girma. x^2

Jagora : Babu abin da yai min ciwo, x^2
: Allah ni ke kallo,
'Y/Amshi : Ga ni ina kixin Gwamna,
: Ba ni da motad da zani hawa,
: Allah za ni roqonka,
: In yi biyag gwamna mai girma. x^2

Jagora : In ga Gwamna mai girma, x^2
: Kuma dai ga mutane nai,
'Y/Amshi : Motan nan dai da za a yi min,
: Ba sai na yi roqo ba,
: Allah za ni roqonka,
: In yi biyag gwamna mai girma. x^2

Jagora : Jiya na kwan cikin tihwa, x^2
: Riga ta tana masqi,
'Y/Amshi : In ba don Tabarau ba,
: Da qura ta makamce ni. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,

Mai Waqa : Alhaji Mamman xan Abubakar Malumfashi[133]*,*

24. *Gindin Waqa : Dogo xan Abubakar na Malumfashi,*
: Jikan Dabo xan Kilo gwamron giwa.

Jagora : Dogo xan Abubakar na Malumfashi,
: Jikan Dabo xan Kilo Gwamron giwa,
'Y/Amshi : Dogo xan Abubakar na Malumfashi,
: Jikan Dabo xan Kilo Gwamron giwa.

Jagora : Gidan Mamman nit taho kixi sai na gai sai,
'Y/Amshi : Sai ga Audu xan Bala ga Musa nan,
: Komi nib bixa ga yau sai an yo min,
: Dogo xan Abubakar na Malumfashi,
: Jikan Dabo xan Kilo Gwamron giwa.

Jagora : Ga wani horo da zan hwaxa ma xan Shawai, x^2
'Y/Amshi : Allah sa ka xauki horon in na yi. x^2

Jagora : Ai kyawon xa shi xauki horon tsoho nai,
'Y/Amshi : Ai ban ce ka xauki horon kowa ba.

Jagora : Ai kyawon xa shi xauki horon tsoho nai,
'Y/Amshi : Ai ban ce ka xauki horon kowa ba,
: Ni ban ce ka xauki horon kowa ba,
: Dogo xan Abubakar na Malumfashi,
: Jikan Dabo xan Kilo Gwamron giwa.

Jagora : In ka ishe xan baqo bakin garka tai, x^3
'Y/Amshi : Kai ka san akwai duhu bayan qumci, x^3
: Dogo xan Abubakar na Malumfashi,
: Jikan Dabo xan Kilo Gwamron giwa.

Jagora : Ai Xandango Nasidi na yo hadari,
'Y/Amshi : Zaki mai kamar uwaye na tun hwarko.
Jagora : Ah! Ai Xandango Nasidi na yo hadari,
'Y/Amshi : Zaki mai kamar uwaye na tun hwarko.

---

133 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{52}$ $^{1}/_{7}$.

Jagora : Na gode Gago ta yi kyau ta kai min komi,
‘Y/Amshi : Ita ce wadda tas shirya tak aiko min.

Jagora : Lalle Sule Maigari yana yo min girma,
‘Y/Amshi : Xan Aljanna yas shirya yak aiko min.
Jagora : To, Musa godiya nikai min komi,
‘Y/Amshi : Kayan nan da yas shirya yak aiko min.
Jagora : Lalle Audu ya tsare yai min komi,
‘Y/Amshi : Kayan nan da yas shirya yak aiko min.
Jagora : Kai da Dila godiya nikai yai min girma,
‘Y/Amshi : Kayan nan da yas shirya yak aiko min.
Jagora : To, Isah godiya nikai yai min komi,
‘Y/Amshi : Kayan nan da yas shirya yak aiko min.
Jagora : To, Dela godiya nikai tai min komi,
‘Y/Amshi : Kayan nan da yas shirya yak aiko min.
Jagora : To, Habsu godiya nikai tai min komi,
‘Y/Amshi : Kayan nan da yas shirya yak aiko min.
Jagora : To, Dela godiya nikai min komi,
‘Y/Amshi : Kayan nan da yas shirya yak aiko min,
: Dogo xan Abubakar na Malumfashi,
: Jikan Dabo xan Kilo Gwamron giwa.

Jagora : Ga wani horo da zan hwaxa ma xan Shawai, x^2
‘Y/Amshi : Allah sa ka xauki horon in na yi, x^2
: Dogo xan Abubakar na Malumfashi,
: Jikan Dabo xan Kilo Gwamron giwa.

Jagora : Gidan Mamman nit taho kixi sai na gai sai,
‘Y/Amshi : Sai ga Audu xan Bala ga Musa nan,
: Komi nib bixa ga yau sai an yo min,
: Dogo xan Abubakar na Malumfashi,
: Jikan Dabo xan Kilo Gwamron giwa.

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,

Mai Waqa : Alhaji Shu'aibu Kunda[134]*,*

25. *Gindin Waqa : Jikan Kunda ai ina kan zuwa gaisai,*
: Tun da na san ba ka gaji kyamar mutane ba.

Jagora : Hanqure da ni ai ko da,
: Yaushe nib biya kai ta bakka ni,
'Y/Amshi : Tun da na san ba ka gaji qyamar mutane ba,
: Jikan Kunda ai ina kan zuwa gaisai,
: Tun da na san ba ka gaji qyamar mutane ba.

Jagora : Shu'aibu zamanin yaqi, x^2
'Y/Amshi : Na ga ba a taushi Gobir ba,
: An so a karya dahin Jari,
: Amma hwa ba dama. x^2

Jagora : To, Gobirawa ko dauri, x^2
'Y/Amshi : Ba mu gaji tsoro ba,
: Tun da kayan Babari,
: Na nan ga yara nai, x^2
: Jikan Kunda ai ina kan zuwa gaisai,
: Tun da na san ba ka gaji qyamar mutane ba.

Jagora : Muna biyay 'yaj ji'el, x^2
'Y/Amshi : Muna shan miyak kalwa,
: Tun da xan hitina,
: Ba ni jin gahwarar banza. x^2
Jagora : Shi mai zaman zaure,
'Y/Amshi : Ba shi qin mai zuwa gona,
: Mui ta abin da mukai,
: Duniya ba ta son raggo.
Jagora : Shu'aibu mai zaman zaure,
'Y/Amshi : Ba shi qin mai zuwa gona,
: Mui ta abin da mu kai,
: Duniya ba ta son raggo.

Jagora : Shi mai hawan Hwanda,
'Y/Amshi : Ba shi qin sakon Jaki,

---

134 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{53}$ $^{1}/_{3}$.

: Don akwai harkar yara,
: Ba xai da babba ba,
: Jikan Kunda ai ina kan zuwa gaisai,
: Tun da na san ba ka gaji qyamar mutane ba.

Jagora : Shu'aibu zamanin yaqi, x^2
'Y/Amshi : Na ga ba a taushi Gobir ba,
: An so a karya dahin Jari,
: Amma hwa ba dama. x^2

Jagora : To, Gobirawa ko dauri,
'Y/Amshi : Ba mu gaji tsoro ba,
: Tun da kayan Babari,
: Na nan ga yara nai,
: Jikan Kunda ai ina kan zuwa gaisai, x^2
: Tun da na san ba ka gaji qyamar mutane ba. x^2

Jagora : Maza suna goshin xan barya, x^3
'Y/Amshi : Muna babbakar giwa,
: Inda nama shi ke mai yawa,
: Za ni in xebo. x^3

Jagora : Hanqure da ni kullum, x^2
'Y/Amshi : Nib biya ai ta bakka ni,
: Tun da na san,
: Ba ka gaji kyamar mutane ba, x^2
: Jikan Kunda ai ina kan zuwa gaisai,
: Tun da na san ba ka gaji qyamar mutane ba.

Jagora : Shu'aibu zamanin yaqi, x^2
'Y/Amshi : Na ga ba a taushi Gobir ba,
: An so a karya dahin Jari,
: Amma hwa ba dama. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Ali Marafa,

26. *Gindin Waqa : Malam Alo na baraz zaki*[135]*,*
: Jikan Kilo xan Marafa.

Jagora : Malam Alo na baraz zaki,
: Jikan kilo xan Marafa,
'Y/Amshi : Malam Alo na baraz zaki, x^2
: Jikan Kilo xan Marafa. x^2

Jagora : Da Ali da Yakuba, x^2
'Y/Amshi : Ku gyara kaya,
: Babu ba ya cin Gobirawa, x^2
: Malam Alo na baraz zaki,
: Jikan Kilo xan Marafa.

Jagora : Kura ba ta gasa da xan Zaki,
'Y/Amshi : Azamarsu ba ta zama xai ba.

Jagora : Don azamar su wane 'yar gajera ta,
'Y/Amshi : Har yanzu ba ta yi tsawo ba,
: Malam Alo na baraz zaki,
: Jikan Kilo xan Marafa.

Jagora : Ali mijin Sa'a, x^2
'Y/Amshi : Da ka tauhidi,
: Kuma ba ya son wani wargi. x^2

Jagora : Ali na Ali tun duniyar qarhe, x^2
'Y/Amshi : Xan Iro dodo na Musa. x^2

Jagora : Barka nikai ma da zamanin ga, x^2
'Y/Amshi : Na yanzu mai ka-ji-ka-ji,
: Malam Alo na baraz zaki,
: Jikan Kilo xan Marafa. x^2
Jagora : Kura ba ta gasa da xan Zaki,
'Y/Amshi : Azamarsu ba ta zama xai ba.
Jagora : Don azamar su wane 'yar gajera ta,

---

135 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{53}$ $^{1}/_{4}$.

‘Y/Amshi : Har yanzu ba ta yi tsawo ba,
: Malam Alo na baraz zaki,
: Jikan Kilo xan Marafa.

Jagora : Ko can da shirin hwaxa Ali yat ta sa, x^2
: Tun ba a shirya mai wuqa ba,
‘Y/Amshi : Yanzu akwai takobi akwai mashi,
: Don an shirya mai makami,
: Malam Alo na baraz zaki,
: Jikan Kilo xan Marafa. x^2

Jagora : Ko can dokin kwarai shi ka kama gudu,
: Shi daxe shina hamadanci,
‘Y/Amshi : Shi kuma dokin su wane sai bixar tsaba,
: Tun ba a gwada mai ruwa ba,
: Malam Alo na baraz zaki,
: Jikan Kilo xan Marafa.

Jagora : Na gode giye yai abin kirki, x^2
‘Y/Amshi : Ni na yaba ya yi komi, x^2
: Malam Alo na baraz zaki,
: Jikan Kilo xan Marafa.

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gobir na Sabon Birni,

Alhaji Umaru Shawai (1916-1945)[136],

27. *Gindin Waqa : Jikan Jari ginshiqi,*
: Dibirtau uban Zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Safka lahiya uban bango ginshiqin gabas,
'Y/Amshi : Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Safka lahiya,
'Y/Amshi : Uban bango gishiqin gabas.

Jagora : Sannu da sirdi na Garba, x^2
'Y/Amshi : Sannu da zowak ka lahiya. x^2

Jagora : Gambai na Halima, x^2
'Y/Amshi : Mainasara yaushe kaz zaka, x^2
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Sarki Mayaqi ne, x^2
'Y/Amshi : Ko Mamman na Dawwa ne. x^2

Jagora : Kai kag gaji Bawa,
'Y/Amshi : Jangwarzo babu gardama.
Jagora : Kuma ka gaji Bawa,
'Y/Amshi : Xangwamci babu gardama,
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Salihu xan Durumbu, x^2
'Y/Amshi : Mainasara xin da ba su so. x^2

Jagora : Gulbi ya ci mai kwari, x^2
'Y/Amshi : Bajimin Garba xan Hassan. x^2
Jagora : Uban Bakwai, x^2
'Y/Amshi : Uban Lairo had da Amadu. x^2

---

136 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$.

Jagora : Salihu xan Durumbu, x^2
'Y/Amshi : Mainasara xin da ba su so. x^2

Jagora : Ai jikan Kada riqe ni qwarai, x^2
'Y/Amshi : Tun da ka riqa. x^2

Jagora : Sarki ya riqe ni, x^2
'Y/Amshi : Ba ni da sauran shiga qaya, x^2
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Sarki za shi Sakkwato, x^2
'Y/Amshi : Mu ko mun yi rakkiya. x^2

Jagora : Baba ka zak ka lahiya, x^2
'Y/Amshi : Dawowak ka lahiya, x^2
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Salihu ya hawo da sa'as Sarki Balarabe, x^2
'Y/Amshi : Kuma ya hawo da martabar Jari qanin Balarabe. x^2
Jagora : Salihu ya hawo da sa'as Sarki Baranqwame, x^2
'Y/Amshi : Kuma ya hawo da martabar Sarki Bartuhwatuhwa. x^2

Jagora : Ko was san Bartuhwatuhwa,
'Y/Amshi : Kuma was san Baranqwame.

Jagora : To, in ba wanda yas sani ku bari,
'Y/Amshi : Ku bari in hwaxan maku.
Jagora : Wani Sarki da ag Gubur,
'Y/Amshi : Shi ab Bartuhwatuhwa.
Jagora : Wani Sarki na can Gubur,
'Y/Amshi : Shi ab Baranqwame,
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.
Jagora : Salihu kai am mayaqi, x^2
'Y/Amshi : Kai a Kannin da Hammadin. x^2
Jagora : Wasu manyan sarakuna ne,
'Y/Amshi : Kannin da Hammadin.

Jagora : Na ji xiyan mutum guda ne,
'Y/Amshi : Kannin da Hammadin.
Jagora : Kowane sai da yay yi sarki,
'Y/Amshi : Kannin da Hammadin.
Jagora : Ran dakak kututturu,
'Y/Amshi : Ran nan an ka kakkashikke Kannin da Hammadin.
Jagora : Ran hwamar kututturu,
'Y/Amshi : Ran nan an ka kakkashikke Kannin da Hammadin.

Jagora : Ran da uwarsu tai jawabi,
'Y/Amshi : Ta ce ma Gobirawa haka kun ka kai ni,
: Ba Kannin babu Hammadin,
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : A yi larwai iri-iri,
: A yi larwan sarakuna,
: In dai an yi bincike,
: In an kama salsala,
'Y/Amshi : In an kai ga,
: Gobirawa asalinsu ya xara.

Jagora : In an kai ga,
'Y/Amshi : Gobirawa asalinsu ya xara.

Jagora : Ko hwamar Badar da an ka yi, x^2
'Y/Amshi : Su an na Annabi. x^2
Jagora : Ko dagar Badar da an ka yi, x^2
'Y/Amshi : Su an na Annabi. x^2

Jagora : Kakanninka sun ci birnin Kisira, x^2
'Y/Amshi : Sun ci Qaura Kamusa can Badar, x^2
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.
Jagora : Wani wawa marar gaba,
'Y/Amshi : Wai yaz zo a ba shi sarki,
: Sai D. O. ya hana.
Jagora : Wani tsoho mahaukaci,
'Y/Amshi : Sai ya zo a ba shi sarki,
: Sai D. O. ya hana.

Jagora : Sai yac ce an qi ba ka, x^2
'Y/Amshi : Xebi da qarhin Babarbara. x^2
Jagora : Ai Kusu da yay yi sheka,
: 'Ya'yansa yay yi ma,
: Bilbili da yai gida,
: Don 'ya'yansa yay yi,
: Ummaru bai kau ba,
: Sai da yak kai ga halin na Innuwa,
'Y/Amshi : Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Ummaru Allah jiqan ka, x^3
'Y/Amshi : Allah ya kam mai da gahwara, x^3
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Sannu da sirdi na Garba,
'Y/Amshi : Sannu da zowak ka lahiya.
Jagora : Gambai na Halima,
'Y/Amshi : Mainasara yaushe kaz zaka.
Jagora : Mainasara uban sarki, x^2
'Y/Amshi : Hitila maganin duhu, x^2
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Kai kag gaji Bawa,
'Y/Amshi : Jangwarzo babu gardama.
Jagora : Kuma ka gaji Bawa,
'Y/Amshi : Xangwamci babu gardama,
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ummaru Shawai (1916-194)[137],
Gindin Waqa : Jikan Jari ginshiqi,

---

137 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{1}$.

: Dibirtau uban Zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Safka lahiya uban bango gishiqin gabas,
‘Y/Amshi : Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Safka lahiya,
‘Y/Amshi : Uban bango gishiqin gabas.

Jagora : Sannu da sirdi na Garba, x^2
‘Y/Amshi : Sannu da zowak ka lahiya. x^2

Jagora : Gambai na Halima, x^2
‘Y/Amshi : Mainasara yaushe kaz zaka, x^2
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Uban Bakwai, x^2
‘Y/Amshi : Uban Lairo had da Amadu. x^2

Jagora : Salihu xan Durumbu, x^2
‘Y/Amshi : Mainasara xin da ba su so. x^2

Jagora : Sarki Mayaqi ne, x^2
‘Y/Amshi : Ko Mamman na Dawwa ne. x^2

Jagora : Kai kag gaji Bawa,
‘Y/Amshi : Jangwarzo babu gardama.
Jagora : Kuma ka gaji Bawa,
‘Y/Amshi : Xangwamci babu gardama,
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.
Jagora : Sarki za shi Sakkwato, x^2
‘Y/Amshi : Mu ko mun yi rakkiya. x^2

Jagora : Baba ka zak ka lahiya, x^2
‘Y/Amshi : Dawowak ka lahiya, x^2
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Salihu ya hawo da sa’as Sarki Balarabe, x^2

‘Y/Amshi : Kuma ya hawo da martabar Jari qanin Balarabe. x^2

Jagora : Salihu ya hawo da sa’as Sarki Baranqwame, x^2
‘Y/Amshi : Kuma ya hawo da martabar Sarki Bartuhwatuhwa. x^2

Jagora : Ko was san Bartuhwatuhwa,
‘Y/Amshi : Kuma was san Baranqwame.
Jagora : To, in ba wanda yas sani ku bari,
‘Y/Amshi : Ku bari in hwaxan maku.
Jagora : Wani Sarki da ag Gubur,
‘Y/Amshi : Shi ab Bartuhwatuhwa.
Jagora : Wani Sarki na can Gubur,
‘Y/Amshi : Shi ab Baranqwame.

Jagora : Salihu kai am mayaqi, x^2
‘Y/Amshi : Kai a Kannin da Hammadin. x^2
Jagora : Na ji xiyan mutum guda ne,
‘Y/Amshi : Kannin da Hammadin.
Jagora : Kowane sai da yay yi sarki,
‘Y/Amshi : Kannin da Hammadin.
Jagora : Ran hwamar kututturu,
‘Y/Amshi : Ran nan an ka kakkashikke Kannin da Hammadin.
Jagora : Ran dakak kututturu,
‘Y/Amshi : Ran nan an ka kakkashikke Kannin da Hammadin.
Jagora : Ran da uwarsu tai jawabi,
‘Y/Amshi : Ta ce ma Gobirawa haka kun ka kai ni,
: Ba Kannin babu Hammadin,
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.
Jagora : A yi larwai iri-iri,
: A yi larwan sarakuna,
: In dai an yi bincike,
: In an kama salsala,
‘Y/Amshi : In an kai ga,
: Gobirawa asalinsu ya xara.

Jagora : In an kai ga,
‘Y/Amshi : Gobirawa asalinsu ya xara.
Jagora : Ko hwamar Badar da an ka yi, x^2

‘Y/Amshi : Su an na Annabi. x^2
Jagora : Ko dagar Badar da an ka yi, x^2
‘Y/Amshi : Su an na Annabi. x^2

Jagora : Kakanninka sun ci birnin Kisira,
‘Y/Amshi : Sun ci Qaura Kamusa can Badar.
Jagora : Gulbi ya ci mai kwari, x^2
‘Y/Amshi : Bajimin Garba xan Hassan, x^2
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Uban Bakwai, x^2
‘Y/Amshi : Uban Lairo had da Amadu. x^2
Jagora : Yamutsa gari, yamutsa gari, x^3
: Toya gari, toya gari, x^3
‘Y/Amshi : Dibirtau uban zagi,
: Xan Mamman na Baciri.

Jagora : Uban Bakwai, x^2
‘Y/Amshi : Uban Lairo had da Amadu. x^2
Jagora : Salihu xan Durumbu, x^2
‘Y/Amshi : Mainasara xin da ba su so. x^2
Jagora : Sarki Mayaqi ne, x^2
‘Y/Amshi : Ko Mamman na Dawwa ne. x^2

Jagora : Kai kag gaji Bawa,
‘Y/Amshi : Jangwarzo babu gardama.

Jagora : Kuma ka gaji Bawa,
‘Y/Amshi : Xangwamci babu gardama,
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Sarki mai kuku-kuku,
‘Y/Amshi : Turawa duk garau suke.

Jagora : ‘Yan Soja da ag garai,

‘Y/Amshi : ‘Yan Sanda garai suke,
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ummaru Shawai (1916-1945)[138]*,*
Gindin Waqa : Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban Zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Dibirtau uban zagi,
‘Y/Amshi : Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

---

138 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{2}$.

Jagora : Sauka da lahiya,
‘Y/Amshi : Sarki farin wata.

Jagora : Salihu ya hau da sa’as sarki Balarabe,
‘Y/Amshi : Kuma ya hau da martabar Jari qanen Balarabe.

Jagora : Salihu ya hawo da sa’as sarki Baranqwame,
‘Y/Amshi : Kuma ya hawo da martabar sarki Bartuhwatuhwa.

Jagora : Was san Bartuhwatuhwa,
‘Y/Amshi : Kuma was san Baranqwame.

Jagora : In ba wanda yas sani,
‘Y/Amshi : To, ku bari in hwaxa muku.

Jagora : Wani sarki da ag Gubur,
‘Y/Amshi : Shi ab Bartuhwatuhwa,
Jagora : Kuma wani sarki da ag Gubur,
‘Y/Amshi : Shi ab Baranqwame.

Jagora : In an yi bincike,
: In an kama da salsala,
‘Y/Amshi : In an kai ga Gobirawa asalinsu yax xara.

Jagora : Ko faman Badar da an,
‘Y/Amshi : Ka yi ku an na Annabi.

Jagora : Ginshiqin gada,
‘Y/Amshi : Riqe maza tun da ka riqa.

Jagora : Gulbi ya buge gari,
‘Y/Amshi : Falalen da aw wata,
Jagora : Gawurtaccen uban zagi,
‘Y/Amshi : Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Wani wawa marar gaba,
‘Y/Amshi : Wai yaz zo a ba shi sarki,

: Sai D. O. ya hana.
Jagora : Wani tsoho mahaukaci,
'Y/Amshi : Sai ya zo a ba shi sarki,
: Sai D. O. ya hana.

Jagora : Sai yac ce an qi ba ka, x^2
'Y/Amshi : Xebi da qarhin Babarbara. x^2

Jagora : Ai Kusu da yay yi sheka,
: 'Ya'yansa yay yi ma,
: Bilbili da yai gida,
: Don 'ya'yansa yay yi,
: Ummaru bai kau ba,
: Sai da yak kai ga halin na Innuwa,
'Y/Amshi : Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Jagora : Ummaru Allah jiqan ka, x^3
'Y/Amshi : Allah ya kam mai da gahwara, x^3
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,
Ubangida : Garkuwan Dutsi Innar Gobir[139]*,*

28. *Gindin Waqa : Ka buwayi maza sai na zo,*
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Bajimin Bawa Garkuwan Dutsi,
'Y/Amshi : Wa ne masu bindiga,
: Wa ne 'yan mashi,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : A gaishe ka Garkuwas sarki, x^2

---

[139] An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{50}$ $^1/_1$.

‘Y/Amshi : Ko mi za a yi riqon Gobir sai ka ce,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye. x^2

Jagora : Don Allah Gobirawa, x^2
‘Y/Amshi : Sai ku yi niy ya,
: Ku zan ka yin wada sarki yac ce, x^2
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Ya xauke masu roqo,
‘Y/Amshi : Ya riqe haw wanda ba shi roqo.
: In ba don kai ba,
: Da mazaje sun sha yunwa,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Garkuwa ya xauke masu roqo,
‘Y/Amshi : Ya riqe haw wanda ba shi roqo.
: In ba don kai ba,
: Da mazaje sun sha yunwa,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.
Jagora : Kai nis sani qasas Sabon Birni, x^2
‘Y/Amshi : Tun da kai ka wa ‘ya’yana toshi, x^2
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Garkuwa shi wanda am musulmi,
‘Y/Amshi : In abu ya samu ba ya savo,
: Amma an so a zan ajewa wajjen Allah,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Ashe wanda am musulmi,
‘Y/Amshi : In abu ya samu ba ya savo,
: Amma an so a zan ajewa wajjen Allah,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Gudurmusun dutsi, x^3
‘Y/Amshi : Mai xaukak ka shi ka ji ba ‘yan kallo ba. x^3

Jagora : Ina ruwan ‘yan kallo, x^2
‘Y/Amshi : Kowa ya sa idanunai sai dibi, x^2
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : A gaishe ka garkuwas sarki, x^2
‘Y/Amshi : Komi za a yi riqon Gobir sai ka ce, x^2
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Alhaji jikan Bagobiri,
‘Y/Amshi : Dogo xan kwasau,
: Ina shirin in zo gaishe ka,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Jatau xan Bagobiri,
‘Y/Amshi : Dogo xan kwasau,
: Ina shirin in zo gaishe ka.

Jagora : Alhaji jikan Bagobiri,
‘Y/Amshi : Dogo xan kwasau,
: Ina shirin in zo gaishe ka,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : In ka ganan da rigash shadda,
‘Y/Amshi : Alhaji wadda Garkuwa yab bayat ce.
Jagora : In ka ganan da wandon shadda,
‘Y/Amshi : Alhaji wadda Garkuwa yab bayat ce.
Jagora : In ka ganan da taggon shadda,
‘Y/Amshi : Alhaji wadda Garkuwa yab bayat ce,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Garkuwa barkam maza da qwazo,
‘Y/Amshi : Mu kam kullum muna tahowa amsan naira,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Barkam maza da qwazo,
‘Y/Amshi : Mu kam kullum muna tahowa amsan naira,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Baraya barkam maza da qwazo,
‘Y/Amshi : Mu kam kullum muna tahowa amsan naira,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Garkuwan Dutsi Innar Gobir[140]*,*
Gindin Waqa : Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Bajimin Bawa Garkuwan Dutsi,
‘Y/Amshi : Wa ne masu bindiga,
: Wa ne ‘yan mashi,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : A gaishe ka Garkuwas sarki,
‘Y/Amshi : Ko mi za a yi riqon Gobir sai ka ce,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

---

[140] An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{1}$.

Jagora : Jatau xan Bagobiri,
‘Y/Amshi : Dogo xan kwasau,
: Ina shirin in zo gaishe ka,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Don Allah Gobirawa, x^2
‘Y/Amshi : Sai ku yi niy ya,
: Ku zan ka yin wada sarki yac ce, x^2
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Ashe wanda am Musulmi,
‘Y/Amshi : In abu ya samu ba ya savo,
: Amma na so a zan ajewa wajjen Allah,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Gudurmusun dutsi, x^2
‘Y/Amshi : Mai xaukak kashi-kashi ba ‘yan kallo ba. x^2

Jagora : Ina ruwan ‘yan kallo, x^2
‘Y/Amshi : Kowa ya sa idanunai sai dibi, x^2
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Barkam maza da qwazo, x^2
‘Y/Amshi : Mu kam kullum muna tahowa amsan Naira. x^2

Jagora : Ya xauke masu roqo,
‘Y/Amshi : Ya riqe har wanda ba shi roqo.

Jagora : In ba don kai ba,
‘Y/Amshi : Mazaje sun sha yunwa,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Kai nis sani qasas Sabon Birni, x^2

‘Y/Amshi : Tun da kai ka wa ‘ya’yana toshi, x^2
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Garkuwa barkam maza da qwazo,
‘Y/Amshi : Mu kam kullum muna tahowa amsan naira,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : Baraya barkam maza da qwazo,
‘Y/Amshi : Mu kam kullum muna tahowa amsan naira,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Jagora : A gaishe ka garkuwas sarki,
‘Y/Amshi : Komi za a yi riqon Gobir sai ka ce,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Salihu xan Ummaru Shawai (1916-1975)[141],

29. *Gindin Waqa : Mainasara na Isa na Musa,*
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Sarki ya kwana da hwarin ciki,
‘Y/Amshi : Hay yau bai kwan da muni ga rai ba,
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Baban Yari baban Makama, x^2
‘Y/Amshi : Baba Uban Lihidda na Barga, x^2
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

---

141 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{147}$ $^1/_8$.

Jagora : Ya zo Makka ya zo Madina, x^2
'Y/Amshi : Alhaji ya taho lahiya lau. x^2
Jagora : Ga Alhaji ya taho za mu tarbe, x^2
'Y/Amshi : Da wace gaisuwa zan ishe mai? x^2
Jagora : Ko waqar sarauta muka mai, x^2
'Y/Amshi : Koko dai salati mu kai mai. x^2
Jagora : To, in dai salati mu kai mai,
'Y/Amshi : Sun ce ko kam mu hwara da zambo,
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Baqon Jidda baqon Kano, x^2
'Y/Amshi : Alhaji baqon ministan Arewa. x^2

Jagora : Sarkin Makka ya yo wasiqa,
'Y/Amshi : Ya aiko ma jikan ta Barga.
Jagora : Kuma Sardauna ya yo wasiqa,
'Y/Amshi : Ya aiko ma jikan ta Barga.

Jagora : Sun ce galibin duniyag ga,
'Y/Amshi : Duka kowa ya koma Musulmi.
Jagora : A yi kono da salla da zakka, x^2
'Y/Amshi : A yi ta yin abin da Allah ke qamna. x^2
Jagora : A yi aure a zan son zumunta, x^2
'Y/Amshi : A yi ta abin da Allah ke qamna. x^2
Jagora : Kowane sarki shina na shi yayi, x^2
'Y/Amshi : Ga namu zamani ba iri nai. x^2

Jagora : Baciri ya yi mulki gabas,
'Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Goba ya yi mulki gabas,
'Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Jacili ya yi mulki gabas,
'Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Mayaqi ya yi mulki gabas,
'Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Goba ya yi mulki gabas,
'Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Ali ya yi mulki gabas,
'Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.

Jagora : Mainasara ya yi mulki gabas,
‘Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Almu ya yi mulki gabas,
‘Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Gulbi ya yi mulki gabas,
‘Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Xanmagaji ya yi mulki gabas,
‘Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Jadi ya yi mulki gabas,
‘Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Jari ya yi mulki gabas,
‘Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Shawai ya yi mulki gabas,
‘Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
Jagora : Salihu ya yi mulki gabas,
‘Y/Amshi : Shi ma bai zo da yara gabas ba.
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Tun can zamanin zamunna,
‘Y/Amshi : Alhaji tun can da manyan sarakai,
: Duk kwararon da an nan na Gobir,
: In ba a san da jikan Kilo ba,
: Ba sarkin da yak kwashi arhwa,
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Alhaji tun da ka gaji arhwa, x^2
‘Y/Amshi : Ko ni ma ina son ka sani. x^2

Jagora : ‘Yan kuxxi garan hwan tamanin,
‘Y/Amshi : Kuma in ka biya babu laihi.

Jagora : Xan guzurin da nih hwara tardawa,
‘Y/Amshi : Na duqule na yi shanu,
: To, amma kwarai sun tare su,
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Sarki ya kwana da hwarin ciki,

‘Y/Amshi : Hay yau bai kwan da muni ga rai ba,
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Salihu xan Ummaru Shawai (1916-1975)[142]*,*
Gindin Waqa : Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Baban Yari baban Makama, x^2
‘Y/Amshi : Baba Uban Lihidda na Barga, x^2
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Ya zo Makka ya zo Madina, x^2
‘Y/Amshi : Alhaji ya taho lahiya lau. x^2

Jagora : Ga Alhaji ya taho za mu tarbe, x^2
‘Y/Amshi : Da wace gaisuwa zan ishe mai? x^2

142 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{375}$ $^1/_7$.

Jagora : Ko waqar sarauta muka mai, x^2
'Y/Amshi : Koko dai salati mu kai mai. x^2

Jagora : To, in dai salati mu kai mai,
'Y/Amshi : Sun ce ko kam mu hwara da zambo,
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Baqon Jidda baqon Kano, x^2
'Y/Amshi : Alhaji baqon ministan Arewa. x^2

Jagora : Sarkin Makka ya yo wasiqa,
'Y/Amshi : Ya aiko ma jikan ta Barga.
Jagora : Kuma Sardauna ya yo wasiqa,
'Y/Amshi : Ya aiko ma jikan ta Barga.

Jagora : Sun ce galibin duniyag ga,
'Y/Amshi : Duka kowa ya koma Musulmi.

Jagora : A yi kono da salla da zakka, x^2
'Y/Amshi : A yi ta yin abin da Allah ke qamna. x^2

Jagora : A yi aure a zan son zumunta, x^2
'Y/Amshi : A yi ta abin da Allah ke qamna, x^2
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : To, ni ga ni na sa tsari, x^2
'Y/Amshi : Amma matan gari na hanawa, x^2
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Lalle matan gari, x^2
'Y/Amshi : Sun yi varna,
: Ba sui abin da Allah ke so ba, x^2
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Wance da wance sun gaji varna, x^2
'Y/Amshi : To, varnassu ba za ta ci ba,
: Amma ta ci Allah kiyaye, x^2
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Ga matan da nis sa tsari,
'Y/Amshi : Yau ga su ga hanya za su tarbe,
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.

Jagora : Sarki ya kwana da farin ciki,
'Y/Amshi : Hay yau bai kwan da muni ga rai ba.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gabas na Gwaranyo Alhaji Umaru[143]*,*
30. *Gindin Waqa : Namijin daga uban Gardaye,*
: *Sarkin Gwaranyo.*

Jagora : To, Allah shi ad da girma,
'Y/Amshi : To, Allah shi ad da baiwa,
: Alhaji ya san da kwanan yaro,
: Ya san da tsoho,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Jikan sarkin gabas,
'Y/Amshi : Mainasara xan Garba sarki,
: Allah ya ba ka girma,
: Ga gadi tsoho.

Jagora : Ran juma'a naz zo Gwaranyo,
'Y/Amshi : Har daxi ya tsallake ni,
: 'Ya'yana sai ku yo mun murna,

---

143 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{1}/_{375}$ $^{1}/_{12}$.

: Na iske sarki.

Jagora : Lalle na yi sa'a,
'Y/Amshi : Na ko gode ma sarkin yaqi,
: Manyan Gwaranyo.

Jagora : Ai ga riga wadda sarkin yaqi,
: Yab bai a kai man,
: Kuma ga rawani da sarkin yaqi,
: Yab bai a kai man,
: Ga takalmi da sarkin yaqi,
: Yab bai a kai man, x^2
'Y/Amshi : Lalle sarkin yaqi ya zan lamba xai,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.
Jagora : Sarkin yaqi ga dai kyauta uku,
'Y/Amshi : Yai man albarkas sarki Gwaranyo,
: Kuma dai ya ba ni kuxin mota,
: Ya ce a kai man,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Allah ya shirya sarki,
: Kuma ya koma ya shinhixa ka daji,
: Ya koma ya yoka birni,
'Y/Amshi : Duk mai son ba ka wahala,
: Ya ba ka fili,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Ina qaunar mai kama maciji, x^2
'Y/Amshi : In dai bai shaqu da ni ba,
: Bari in kwanan mutum sun qare,
: Shi za ya kausai, x^2
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Sauran kaya ina son ku riqe ni,
'Y/Amshi : Ina son ku riqe,

: Ku rungume ni,
: Ku riqe ni qwarai,
: Kamar nama ya kama kalwa.

Jagora : In nama yak kama kalwa,
‘Y/Amshi : Mata ba sai kun hwaxa ba,
: Ku ruhe shi,
: Ku tsabbattace shi,
: Kah hancin kowa ya kai mai,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Jikan sarkin gabas,
‘Y/Amshi : Mainasara xan Garba sarki,
: Allah yai ma girman duniya,
: Ka gaji komi,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Lalle Umaru xan Salo ya ba ni komi,
‘Y/Amshi : Ga riga wadda yab ba ni,
: Yac ce a kai man,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : To, Allah shi ad da girma,
‘Y/Amshi : To, Allah shi ad da baiwa,
: Alhaji ya san da kwanan yaro,
: Ya san da tsoho,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gabas na Gwaranyo Umaru[144]*,*
Gindin Waqa : Namijin daga uban Gardaye,
***:** Sarkin Gwaranyo.*

Jagora : To, Allah shi ad da girma, x^2
'Y/Amshi : To, Allah shi ad da baiwa,
: Alhaji ya san da kwanan yaro,
: Ya san da tsoho,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo. x^2

Jagora : Na taso dag gida, x^2
'Y/Amshi : 'Yar Rimawa mun ka ratso,
: To, nij ji Gusun-Gusoro,
: Ban koma ta Cunkume ba,
: Hanya ta xaukaka ta yi kwana,
: Ta yo Shinaka,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo. x^2

Jagora : Na zo in ratso Shinaka,
'Y/Amshi : Tun da mazaje ash Shinaka,

144 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{2}$.

: Hanya ta tashi ta hau doki,
: Ta yo Gwaranyo,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Ran juma'a na zo Gwaranyo,
'Y/Amshi : Har daxi ya tsallake ni,
: 'Ya'yana sai ku yo mun murna,
: Na iske sarki,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Ni ko yau na gode Allah,
: Na ko gode ma Sarki,
: Na ko gode ma Sarkin Yaqi,
: Manyan Gwaranyo,
'Y/Amshi : Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Ga riga wadda sarkin yaqi,
: Yab bai a kai man,
: Kuma ga rawani da sarkin yaqi,
: Yab bai a kai man,
: Ga takalmi da sarkin yaqi,
: Yab bai a kai man,
'Y/Amshi : Lalle sarkin yaqi ya zan lamba xai,
: Ko da sarki,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Kwasar kyauta uku yai min,
'Y/Amshi : Albarkas sarki Gwaranyo,
: Kuma dai ya ba ni kuxin mota,
: Ya ce a kai man,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : To, Allah shi ad da girma, x^2
'Y/Amshi : To, Allah shi ad da baiwa,
: Alhaji ya san da kwanan yaro,
: Ya san da tsoho.

Jagora : To, Allah ya gina Dutsi,
: Yak koma yag gina Laka,
: Allah ya haska daji,
: Yak koma yah haska birni,
: Dum mai nuqura da kai,
: Ya hwasa sun ba ka hili,
'Y/Amshi : Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Ina qaunar mai kama maciji, x^2
'Y/Amshi : In dai bai shaqu da ni ba,
: Bari in kwanan mutum sun qare,
: Shi za ya kausai, x^2
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Sauran kaya ina son ku riqe ni,
'Y/Amshi : Ina son ku riqe,
: Ku rungume ni,
: Ku riqe ni qwarai,
: Kamar nama ya kama kalwa,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : In nama yak kama kalwa,
'Y/Amshi : Mata ba sai kun hwaxa ba,
: Ku ruhe shi,
: Ku tsabbattace shi,
: Kah hancin kowa ya kai mai,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : Jikan sarkin gabas,
'Y/Amshi : Mainasara xan Garba sarki,
: Allah yai ma girman duniya,
: Ka gaji komi,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Jagora : To, Allah shi ad da girma,
'Y/Amshi : To, Allah shi ad da baiwa,
: Alhaji ya san da kwanan yaro,
: Ya san da tsoho,
: Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni
Ubangida : Sarkin Gobir Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003)[145]*,*

31. *Gindin Waqa : Uban Makama uban Gardaye,*
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ina mazan suke? x^2
'Y/Amshi : Sarkin Gobir ina mazan suke duk sun qare,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : 'Yan sarki kowa shi yi gona,
'Y/Amshi : Tau bayan na Habu ya kama,
: Ban san mai iya bankatai ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Bawa uban Bunu ikon Allah,
'Y/Amshi : In ya xauki mutum ya dace,
: In kau ka qi mutum ya cine,
: Ban san mai iya kwasa tai ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Alhaji xan Dango jikan Inna,
'Y/Amshi : Ya haxa ni da xan Mamman,

---

145 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{144}$ $^1/_1$ - AL $^1/_{144}$ $^1/_2$.

: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Na gode maka Sarkin Gobir,
'Y/Amshi : Alhaji Makaxa ya gode,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ya gama mu da kaya,
'Y/Amshi : Kaya, ko yanzu ya gama mu da kayan iko,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ga wata riga Sarki yab ba ni,
'Y/Amshi : Ta zube qasa hat kai oba,
: Alhaji har bisaki ya share
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ga xan tasala da Sarki yab ba ni,
'Y/Amshi : Da ka naxa shi kamar xan xaki,
: Hay ya sa mani doron tilas,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : To, alkyabba ga da Sarki yab ba ni,
'Y/Amshi : Ya qara mana hasken hwada,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ga hwan talatin Sarki yab ba ni, x^2
'Y/Amshi : In yi jajibirin ras salla. x^2

Jagora : Ai kuxin sun wuce kwasar nama,
'Y/Amshi : Rago za mu saye ko xan sa,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Taron Isa da anka yi niz zo,

'Y/Amshi : Ba da kamar makaxa niz zo ba.

Jagora : 'Yan yara sun ga shiga ta Isa,
'Y/Amshi : Has sun ce wane xan sarki na.

Jagora : Don sun gane ni,
'Y/Amshi : Da 'yan gangumma,
: Da sun ce wani ma sarki na.

Jagora : Wasu sun ce, ba dai sarki ne ba,
'Y/Amshi : Yalla dai makaxin sarki na.

Jagora : Bambanta ni uban Gardaye,
'Y/Amshi : Ya sake mana sabbin kaya,
: Saura yai mana sabon doki,
: In sake masa sabon launi,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Alhaji Bakwai ya shirya Masallaci,
'Y/Amshi : Ya yo muna shi don Allah,
: Bai yi saboda bixak kuxxi ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Masallacin ga da kay yi na Juma'a,
'Y/Amshi : Jikka dubu da xari sun qare,
: Amma ba a gama shiryassai ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ga latirin ga kuxxin hwanho,
'Y/Amshi : To, kuma ba a gama tagogi ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Bawa ba ya son raini,
'Y/Amshi : Bai saba da qulle-qulle batun banza ba,

: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni
Ubangida : Sarkin Gobir Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003)[146],
Gindin Waqa : Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Alhaji xan Dango jikan Geda,
'Y/Amshi : Ya haxa ta gari xan Mamman,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Alhaji xan Dango jikan Geda,
'Y/Amshi : Ya haxa ta gari xan Mamman.
Jagora : Baban Shamaki Sarki,
'Y/Amshi : Alhaji Baban Jekadiya xan Mamman.
Jagora : Baban Shinhixa Sarki,
'Y/Amshi : Alhaji Baban Jekadiya xan Mamman,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Dogo na Salihu jikan Gunda, x^2
'Y/Amshi : Uban Hassan na Baraz Zaki. x^2

Jagora : To, zamanin na Habu xan Inna, x^2
'Y/Amshi : Gobir ba a da sauran yunwa,
: To, kuma ba a da sauran ragga,
: Kowa yay yi bixa ya dace,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi. x^2

Jagora : Darzaje maqiya xan Inna, x^2
'Y/Amshi : Kowac ce ka ce shi yac ce,

---

146 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{374}$ $^1/_2$.

: Sarki bai yi ma kowa shairi,
: To, kuma bai ci abin kowa ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi. x^2
Jagora : Ina mazan suke? x^2
'Y/Amshi : Sarkin Gobir ina mazan suke duk sun qare. x^2

Jagora : 'Yan sarki kowa shi yi gona,
'Y/Amshi : Tau bayan na Habu ya kama,
: Ban san mai iya bankatai ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Bawa uban Bunu ikon Allah,
'Y/Amshi : In ya xauki mutum ya dace,
: In kau ka qi mutum ya cine,
: Ban san mai iya kwasa tai ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Darzaje maqiya xan Inna, x^2
'Y/Amshi : Kowac ce ka ce shi yac ce,
: Sarki bai yi ma kowa shairi,
: To, kuma bai ci abin kowa ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi. x^2

Jagora : To, zamanin na Habu xan Inna, x^2
'Y/Amshi : Gobir ba a da sauran yunwa,
: To, kuma ba a da sauran ragga,
: Kowa yay yi bixa ya dace,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi. x^2

Jagora : Na gode maka Sarkin Gobir, x^2
'Y/Amshi : Alhajim Makaxa ya gode.
Jagora : Alhaji ya gama mu da kaya,
'Y/Amshi : Ko yanzu ya zuba mana kayan iko.
Jagora : To, Alhaji ya gama mu da kaya,
'Y/Amshi : Ko yanzu ya zuba mana kayan iko,

: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ga wata riga Sarki yab ba ni,
'Y/Amshi : Ta zube qasa hat kai oba,
: Alhaji har bisaki ya share
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ga xan tasala da Sarki yab ba ni,
'Y/Amshi : Da ka naxa shi kamar xan xaki,
: Hay ya sa mani doron tilas,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : To, alkyabba ga da Sarki yab ba ni,
'Y/Amshi : Ya qara mana hasken hwada,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ga hwan talatin Sarki yab ba ni, x^2
'Y/Amshi : In yi jajibirin ras salla. x^2

Jagora : Ai kuxin sun wuce kwasar nama,
'Y/Amshi : Rago za mu saye ko xan sa,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Uban Salau ya zo rangadi,
'Y/Amshi : Amma Alhaji ni ban zo ba,
: Sai dai yanzu niz zo gaisai,
: Da mai da xari da biyat yab ba ni.

Jagora : Kyautar na Iro uban Gardaye,
'Y/Amshi : Kyautar ta hi gaban na gode,
: Sai dai ai ladabi ko shukura,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : In da na gadi sarauta birni, x^2
'Y/Amshi : Da ko ba ni da kuxxi an ban. x^2

Jagora : Da in ba ka ba ni gari Idi ba, x^2
'Y/Amshi : To, ka naxa mana kojan zaki. x^2

Jagora : Amma don za ni ga ‘yan sarki ta,
'Y/Amshi : Da sarautar makaxa nik kama.
Jagora : Sarki don za ni ga ‘yan sarki ta,
'Y/Amshi : Ida sarautar makaxa nik kama.

Jagora : To, qwamma ka ba ni garin Idi, x^2
'Y/Amshi : Ko da na ga ba su da kanwar hwari. x^2

Jagora : Diba sa’an da maxa tak kama, x^2
'Y/Amshi : Kullum niz zaka sai sun ba ni. x^2

Jagora : Na gode ma garin Idi,
'Y/Amshi : Hatta mazansu da ‘yan matansu,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Alhaji Bakwai ya shirya Masallaci,
'Y/Amshi : Ya yo muna shi don Allah,
: Bai yi saboda bixak kuxxi ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Masallacin ga da kay yi na Juma’a,
'Y/Amshi : Jikka dubu da xari sun qare,
: Amma ba a gama shiryassai ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.
Jagora : Ga latirin ga kuxxin hwanho,
'Y/Amshi : To, kuma ba a gama tagogi ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Bawa ba ya son raini,
'Y/Amshi : Bai saba da qulle-qulle batun banza ba,

: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.
Jagora : Dogo na Salihu jikan Qunda,
'Y/Amshi : Uban Hassan xan Barayaz Zaki.
Jagora : Kai qyale maqiya xan Inna,
: Kowac ce ka ce shi yac ce,
: Sarki bai ci abin kowa ba,
'Y/Amshi : To, kuma bai yi ma kowa sharri,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Bai ci abin kowa ba,
'Y/Amshi : To, kuma bai yi ma kowa sharri.
Jagora : A gaishe ka Alhaji Gonab Baye,
'Y/Amshi : Ina ruwanta da kai mata taki.
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ga wani ya aje goronai,
'Y/Amshi : Kowane ya sagale mai.
Jagora : Ga wani ya xau goron sarki,
: Ya dahe shi ga hannun dama,
: Na iske shi qanin, x^2
'Y/Amshi : Xan wannan ba ya da sauran kunya, x^2
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ga wani ya yi gina ya faxa,
'Y/Amshi : Bai saba da ginar ramu ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Alhaji xan Dango jikan Geda,
'Y/Amshi : Ya haxa ta gari xan Mamman.
Jagora : Baban Shamaki Sarki,
'Y/Amshi : Alhaji Baban Jekadiya xan Mamman.
Jagora : Baban Shinhixa Sarki,
'Y/Amshi : Alhaji Baban Jekadiya xan Mamman,
: Uban Makama uban Gardaye,

: Bawa sannu da kwanan yaqi.
Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Ubandawaki, Alhaji Bala Xanladi[147]*,*

32. *Gindin Waqa : Ginshiqin Zakari Baqadire,*
: Qasaitacce uban Dawaki,
: Na Isaka gamda'aren mai daga.

Jagora : Zaki mai sulke da bindiga mai masu, x²
'Y/Amshi : Kar ka so ka ji tsoro,
: Abin da ba ka gada ba,
: Ginshiqin Zakari Baqadire,
: Qasaitacce uban Dawaki,
: Na Isaka gamda'aren mai daga. x²

Jagora : Ya xauki mashi, x³
'Y/Amshi : Ya xauki Babarbaren Kakanai,
: Ga yanzu kayan Xanladi
: Duk suna jikkatai. x³

Jagora : Ko shi xarma sirdi, x³
'Y/Amshi : Kullum ka zan zuwa sa-rani,
: Inda kag ga tumaki,
: Ka zan iza su da shanu,
: In Bahillace yay yi gardama sare shi,
: Ginshiqin Zakari Baqadire,
: Qasaitacce uban Dawaki,
: Na Isaka gamda'aren mai daga. x³

Jagora : Ga zanga-zanga, x²
'Y/Amshi : Ya tashi zamanin xan A'i,
: Baba giye shira kayanka,
: Ba ni son ka da wargi,
: Ginshiqin Zakari Baqadire,
: Qasaitacce uban Dawaki,
: Na Isaka gamda'aren mai daga. x²

---

147 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{1}/_{374}$ $^{1}/_{7}$.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa,
Waqa : Waqar Ilmi[148]*,*

33. *Gindin Waqa : Harka da ilmi mu kai,*
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya.

Jagora : Harka da ilmi mu kai, x^2
: Allah ya gyara mana,
'Y/Amshi : Mu gama da ban-gaskiya. x^2

Jagora : In dai mutum yav vace, x^2
: Maisai ga hanya mu kai,
'Y/Amshi : In ko mutum ya qiya,
: Mu iza shi bayan gida,
: Harka da ilmi mu kai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya. x^2

Jagora : In noma mutum za shi yi, x^2
'Y/Amshi : Kuma in hwatauci ya kai,
: Ya gama da ban-gaskiya,
: Harka da ilmi mu kai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya. x^2

Jagora : Gwamnati gyara aiki ta kai,
: Ta gyara aikin dawa,
: Ka na ta dawo gida,
'Y/Amshi : Harka da ilmi mu kai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya.

Jagora : Gwamnati gyara aiki ta kai, x^2
'Y/Amshi : Ta gyara aikin dawa,
: Kuma za ta gyaran gida. x^2

Jagora : Lalle tun da ga shigihhu, x^2

---

148 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{147}$ $^1/_2$.

‘Y/Amshi : Ga xakuna an shirya,
: Ni ba ni kwana wuri, x^2
: Harka da ilmi mu kai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya.

Jagora : Mu yawon aminci mu kai, x^2
‘Y/Amshi : In ya hito dag gabas,
: Ya yi yamma sai ya diras, x^2
: Harka da ilmi mu kai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya.

Jagora : Mu yawon aminci mu kai, x^2
‘Y/Amshi : In ya hito dag gabas,
: Ya yi yamma sai ya diras. x^2

Jagora : Tun dak Kaduna har Zariya,
: Had da manyan Kano,
‘Y/Amshi : Komi mutum za shi yi,
: Ya gama da ‘yan Sakkwato,
: Harka da ilmi mu kai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya.

Jagora : Lalle dak Kaduna har Zariya, x^3
: Had da manyan Kano,
‘Y/Amshi : Komi mutum za shi yi,
: Ya gama da ‘yan Sakkwato. x^3

Jagora : In noma mutum za shi yi, x^2
‘Y/Amshi : Kuma in hwatauci ya kai,
: Ya gama da ban-gaskiya,
: Harka da ilmi mu kai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya. x^2

Jagora : To, mu tun da ga shigihhu,
‘Y/Amshi : Ga xakuna an shirya,

: Ni ba ni kwana wuri.

Jagora : Lalle tun da ga shigihhu, x2
'Y/Amshi : Ga xakuna an shirya,
: Ni ba ni kwana wuri, x2
: Harka da ilmi mu kai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya.

Jagora : To, ashe zaman duniya, x3
'Y/Amshi : Kowa na shi aiki shi kai,
: Abin da wani ba shi so,
: Wani na bixa tai kwarai,
: Harka da ilmi mu kai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya. x3

Jagora : In dai mutum yav vace, x2
: Maisai ga hanya mu kai,
'Y/Amshi : In ko mutum ya qiya,
: Mu iza shi bayan gida,
: Harka da ilmi mu kai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya. x2

Jagora : Harka da ilmi mu kai, x2
: Allah ya gyara mana,
'Y/Amshi : Mu gama da ban-gaskiya. x2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Tashar Motar Garin Sabon Birni,

Alhaji Idi xan Argiji[149],

34. *Gindin Waqa : Ya kwan yana aikin mota,*
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure.

Jagora : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure,
'Y/Amshi : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure.

Jagora : Ga wani can yana satar hanya, x^2
: Sarkin tasha ya kam mai,
: Komi za shi yi hwadamar kanwa,
: Dangi suna kallo nai,
'Y/Amshi : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure. x^2

Jagora : Lalle sarkin tashar Sabon Birni, x^2
: Harkat ta nai min daxi,
: Kullum ni ishe shi wurin mota,
: Sai ya shirya min kuxxi,
'Y/Amshi : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure. x^2
Jagora : Ko mai Basukur ko mai Hwanda,
: Ko mai hayat 'yat qwama,
: To, duw wanda ba lasin,

---

149 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{54}$ $^1/_5$.

: ‘Yan Sanda na daka mai kashi,
‘Y/Amshi : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure.

Jagora : Ko mai Basukur ko mai mota, x^2
: Ko mai hayat ‘yat qwama,
: To, duw wanda ba lasin,
: ‘Yan Sanda na daka mai kashi,
‘Y/Amshi : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure. x^2

Jagora : Gogan Ila gogarman Mamman, x^2
: Zaki magajin mani,
: To, Allah ya sa ma albarkar,
: Sarkin fulanin Shawai,
‘Y/Amshi : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure. x^2

Jagora : To, na zo tashar ‘yan Jakkai,
: Ban ga ana shirin komi ba,
: Sai niy yo tasha wajjen mota,
: Can nig ga dalar kaya,
‘Y/Amshi : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure.

Jagora : To, na zo tashar ‘yan Jakkai,
: Ban ga ana shirin komi ba,
: Sai niy yo tasha wajjen mota,
: Can nig ga dalar kaya.

Jagora : To, na zo tashar raqumma,
: Ban ga ana shirin komi ba,
: Sai niy yo tasha wajjen mota,
: Can nig ga dalar kaya,
‘Y/Amshi : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure.

Jagora : Ga ni ina shirin tahiya Zazzau, x^2
: Kuma ga ni ba ‘yan kuxxi,
: Ina nuhin tahiya Zazzau,
: Kuma ga ni ba ‘yan kuxxi,
: Ina dibin mota ni ko suna kallo na,
: ‘Yan kamishon suna dibin mota,
: Ni ko suna kallo na,
: Don sun gane ni da taron,
: Yara zay yawa baya na,
: Har an yi jinga na tada,
: Ban zan biyan kuxxi ba,
‘Y/Amshi : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure. x^2

Jagora : To, sarkin tasha don albarkar, x^2
: Manyan mutanen hwarko,
: Bari son shiga harkar yaro,
: In ya yi ba daidai ba,
‘Y/Amshi : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin vaure. x^2

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Rambaxawa,
Mai Waqa : Xan Sarkin Hillani,

Alhaji Muhammadu Dikko Xanmaliki[150],

35. *Gindin Waqa : Alhaji xan sarkin hillani,*
: Masu abin baiwa xan yashi.

Jagora : Alhaji xan sarkin hillani, x^2
: Masu abin baiwa xan yashi,
'Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : Ni Alhaji azama tai gado na, x^2
: Sai wajjen sarkin hillani,
: Sai wajjen mamomin Gobir,
'Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : Kowaz zaka Sabon Birnin Gobir, x^2
: Ya zaka garka tai ran narba,
: Ya ga abin kuxxi ya samu,
'Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : Bisimilla maganar malammai, x^2
: Walijam maganar hillani,
: Tarakkumas sai 'yan buzaye,
'Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : In ka ishe gulbi na tozaye, x^2
'Y/Amshi : Alhaji bayan kai ash shaqe. x^2

Jagora : In dai bari ba ta samo qari ba, x^2
: Ya ishe gulbi ya lalace,
'Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : Ai zuwa Kano ba banza ne ba, x^2
: Kun sha daxi kun sha qura,
: Da ku da kwana sai kun sauka,

---

150 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{144}$ $^1/_7$.

‘Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : Ai zuwa Kano ba banza ne ba, x^2
: Kun sha daxi kun sha qura,
: Da ku da kwana sai ran narba,
‘Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : Mada Nanu da ya aje kuxxi,
‘Y/Amshi : Ya yi hayaqi kuma ya yi bisashe,
: Bai yi zaton wani ha’inci ba.

Jagora : Mada Kura da ya aje kuxxi,
‘Y/Amshi : Ya yi hayaqi kuma ya yi bisashe,
: Bai yi zaton wani ha’inci ba.

Jagora : Ko Samagi da ya aje kuxxi,
‘Y/Amshi : Ya yi hayaqi kuma ya yi bisashe,
: Bai yi zaton wani ha’inci ba.

Jagora : Qohin nan ba su san tsahi ba, x^2
: Kuma babu ma mai kai gumba,
: Abin su duk baiwar Allah ne,
‘Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : Da masu qin ku da mai vacinku, x^2
: Mutum dai bai yi kamar Allah ba,
: Mai sama shi as sarkin jinqai,
‘Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : Alhaji gadon qarhe nir roqa, x^2
‘Y/Amshi : Ga ya ga hannu ya shirya min. x^2

Jagora : Ya ban katihwa ya ban bargo, x^2
: Had da matashi ya shirya min,
: Alhaji lallai ya kyauta min,
‘Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : Ni tun da gadon kwana ya samu, x^2
‘Y/Amshi : Ban iya noma sai hutawa,
: Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : Kowaz zaka Sabon Birnin Gobir, x^2
: Ya zaka garka tai ran narba,
: Ya ga abin kuxxi ya taru,
‘Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Jagora : Ni Alhaji azama tai gado na, x^2
: Sai wajjen sarkin hillani,
: Sai wajjen mamomin Gobir,
‘Y/Amshi : Alhaji xan sarkin hillani,
: Masu abin baiwa xan yashi. x^2

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,

Mai Waqa : Sarkin Maraxi Xangara[151]*,*
Alhaji Bala xan Sani,

36. *Gindin Waqa : Xangara jikan xan lahiya,*
: Bala xan Sani gaisai mu kai.

Jagora : Da ni da xiya na murna mu kai, x^3
'Y/Amshi : Mu kwana Maraxi gidan Xangara,
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai. x^3

Jagora : Na Mamman Cana, x^2
'Y/Amshi : Na Mamman Jatau abin xan Sani ya kai ciki. x^2

Jagora : Maraxi akwai kuxxi, x^2
'Y/Amshi : Ai buhuhuwan kuxxi,
: Wasu has sun ruve.
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai. x^2

Jagora : Wanda ba shi da mota,
'Y/Amshi : In ya zaka,
: Bala xan Sani sai mai ya kai.
Jagora : Wanda ba shi da Hwanda,
'Y/Amshi : In ya zaka,
: Bala xan Sani sai mai ya kai.
Jagora : Wanda ba shi da doki,
'Y/Amshi : In ya zaka,
: Bala xan Sani sai mai ya kai.
Jagora : Wanda ba shi da shadda,
'Y/Amshi : In ya zaka,
: Bala xan Sani sai mai ya kai,
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai.
Jagora : Jikan Musa,
'Y/Amshi : Jikan saraki,

---

151 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{144}$ $^1/_5$ - AL $^1/_{146}$ $^1/_6$.

: Kun zama qusoshin duniya.
Jagora : In an bixi qusoshin duniya,
'Y/Amshi : Ina wani bayan kai Xangara?
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai.

Jagora : Tun dab bisa Azbin, x^2
'Y/Amshi : Hab bisa Kano,
: Uban kowa ya san Xangara. x^2
Jagora : Da Tawa da Tasawa, x^2
'Y/Amshi : Had Damagaran,
: Kowa ya san Xangara. x^2

Jagora : Da Buza da Madawa,
'Y/Amshi : Had da mu da as Sabon Birni mun sani.
Jagora : Xangara kai as sinadari,
'Y/Amshi : Ko da xai abin kallo,
: Kallo nai a kai,
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai.

Jagora : Xangara kai am muzakkari,
'Y/Amshi : Ko da xai abin kallo,
: Kallonai a kai,
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai.

Jagora : Tun da Allah yay yi ni, x^2
'Y/Amshi : Hay yanzu ban ga,
: Kyakyandi ba gidan duniya. x^2
Jagora : Mutane ku zo ku gani, x^2
'Y/Amshi : Ku ga abin da,
: Xan Sani yash shiryo mana. x^2
Jagora : Da riga goma, x^2
'Y/Amshi : Da riga uku,
: Bala xan Sani yay yo mana. x^2

Jagora : Na Alhajiya Gwamma,
'Y/Amshi : Wanga zamani,
: Ku am manyan duniya.

Jagora : Qanin Hajiya Gwamma,
‘Y/Amshi : Wanga zamani,
: Ku am manyan duniya.
Jagora : Shi na iya ba da wa,
‘Y/Amshi : Ko da yaushe ‘yan amsa,
: Amsa xai su kai,
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai.

Jagora : Shi na iya ba da wa, x^2
‘Y/Amshi : Ko da yaushe ‘yan amsa,
: Amsa xai su kai. x^2
Jagora : Ga riguna yab bai, x^2
‘Y/Amshi : Ga naira xari biyat,
: Xan Sani yak kai mana,
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai. x^2

Jagora : Tun da Allah as sarki, x^2
‘Y/Amshi : Yanzu ko,
: Bala xan Sani ag girgije. x^2
Jagora : Ina iya in gane, x^2
‘Y/Amshi : Yanzu ba kamar,
: Xan Sani sai ya wuce,
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai. x^2

Jagora : Jikan Musa jikan, x^2
‘Y/Amshi : Jikan Saraki,
: Kun zama qusoshin duniya. x^2
Jagora : In an bixi qusoshin duniya, x^2
‘Y/Amshi : Ina wani bayan kai Xangara?
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai. x^2

Jagora : Qanin Hajiya Gwamma,
‘Y/Amshi : Wanga zamani,
: Ku am manyan duniya.
Jagora : Maraxi akwai kuxxi, x^2

‘Y/Amshi : Ai buhuhuwan kuxxi,
: Wasu has sun ruve.
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai. x^2

Jagora : Wanda ba shi da Hwanda,
‘Y/Amshi : In ya zaka,
: Bala xan Sani sai mai ya kai.
Jagora : Wanda ba shi da doki,
‘Y/Amshi : In ya zaka,
: Bala xan Sani sai mai ya kai.
Jagora : Wanda ba shi da shadda,
‘Y/Amshi : In ya zaka,
: Bala xan Sani sai mai ya kai,
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai.

Jagora : Da mu makaxan garka, x^2
‘Y/Amshi : Had da mu makaxan noma,
: Sun san Dangara. x^2

Jagora : Jikan Musa jikan, x^2
‘Y/Amshi : Jikan Saraki,
: Kun zama qusoshin duniya. x^2

Jagora : Ina iya in gane, x^2
‘Y/Amshi : Yanzu ba kamar xan Sani sai ya wuce. x^2
Jagora : Tun da Allah as sarki, x^2
‘Y/Amshi : Yanzu ko Bala xan Sani ag girgije,
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai. x^2

Jagora : Maraxi akwai kuxxi, x^2
‘Y/Amshi : Ba ka yin irin wada xan Sani,
: Yas shirya. x^2

Jagora : Ko ka hi Bala kuxxi, x^2
‘Y/Amshi : Ba ka yin irin wada xan Sani,
: Yas shirya,
: Xangara jikan xan lahiya,

: Bala xan Sani gaisai mu kai. x^2

Jagora : Da ni da xiya na murna mu kai, x^2
'Y/Amshi : Mu kwana Maraxi gidan Xangara,
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Jam'iyyar N. P. N.[152]

[152] An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{147}$ $^1/_1$.

37. *Gindin Waqa : Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi,*
: Gwamnati N. P. N. mai biyak ku ba shi da haushi.

Jagora : Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi, x^2
'Y/Amshi : Gwamnati N. P. N mai biyak ku ba shi da haushi. x^2

Jagora : Ga masara ga gero to, kuma ga shinkahwa, x^2
'Y/Amshi : Gwamnati ta shirya babu mai rigan mu da daxi,
: Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi,
: Gwamnati N. P. N mai biyak ku ba shi da haushi. x^2

Jagora : Gwamnati ta ba mu ruwa, x^2
: To, har yanzu da saura,
: Tai mana lantarki don garinmu yai mana haske,
'Y/Amshi : Gwamnati ta shirya babu mai rigan mu da daxi,
: Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi,
: Gwamnati N. P. N mai biyak ku ba shi da haushi. x^2

Jagora : Ga masara ga gero to, kuma ga shinkahwa, x^2
'Y/Amshi : Gwamnati ta shirya babu mai rigan mu da daxi. x^2

Jagora : To, Shehu Kangiwa, x^2
'Y/Amshi : Wada kash shirya mana ta yi,
: Abin da yas shirya,
: Ba kamar shirin maqiya ba,
: Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi,
: Gwamnati N. P. N mai biyak ku ba shi da haushi. x^2

Jagora : To, na ga jam'iyyar su wane sun shirya mana qarya, x^2
'Y/Amshi : Tun da qarya ta shugabanmu ba shi da qarya,
: Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi,
: Gwamnati N. P. N mai biyak ku ba shi da haushi. x^2

Jagora : Sun ce sui mana gulbin hura su sa mana gulbi,
'Y/Amshi : Bayan nuhwar Allah babu mai hana mana noma.

Jagora : Bayan nuhwar Allah, x^3
'Y/Amshi : Babu mai hana mana noma. x^3

Jagora : Sun ce sui mana gulbin hura su sa mana gulbi, x^2

‘Y/Amshi : Bayan nuhwar Allah babu mai hana mana noma,
: Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi,
: Gwamnati N. P. N mai biyak ku ba shi da haushi. x^2

Jagora : Shehu Kangiwa,
‘Y/Amshi : Wada kash shirya mana ta yi,
: Abin da yas shirya,
: Ba kamar shirin maqiya ba,
: Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi,
: Gwamnati N. P. N mai biyak ku ba shi da haushi.

Jagora : To, Shehu Kangiwa, x^2
‘Y/Amshi : Wada kash shirya mana ta yi,
: Abin da yas shirya,
: Ba kamar shirin maqiya ba,
: Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi,
: Gwamnati N. P. N mai biyak ku ba shi da haushi. x^2

Jagora : To, na ga jam’iyyar su wane sun shirya mana qarya, x^2
‘Y/Amshi : Tun da qarya ta shugabanmu ba shi da qarya,
: Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi,
: Gwamnati N. P. N mai biyak ku ba shi da haushi. x^2

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ibrahim (1970-1975)[153],

38. *Gindin Waqa : Uban Zagi na Muhamman mai Sabon Birni,*

153 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{147}$ $^1/_{11}$.

: Iro ya cika zakka yau ya zama sarki.

Jagora : Zauna da shiri baban yari mai Alqalawa, x^2
‘Y/Amshi : Na bawa ya shira du wanda kakanai yay yi. x^2

Jagora : Zauna da shiri baban yari mai Alqalawa,
‘Y/Amshi : Na bawa ya shira du wanda kakanai yay yi.
: Uban Zagi na Muhamman mai Sabon Birni,
: Iro ya cika zakka yau ya zama sarki.

Jagora : Mainasara ne ko ko Kada ne yad dawo, x^2
‘Y/Amshi : Yau Ibrahim ya gaji rumhwaj Jangwarzo,
: Ga yanzu ba ka da ratsin da ba xan Shawai ba,
: Uban Zagi na Muhamman mai Sabon Birni,
: Iro ya cika zakka yau ya zama sarki. x^2

Jagora : Balarabe xan Yari, x^2
‘Y/Amshi : Kai a Hassan da Hussaini,
: Ga yanzu kai muka dibi,
: Ba wani bayan kai. x^2

Jagora : Ga shinfixan mai nasara, x^2
‘Y/Amshi : Na Janjona ya hau,
: Ga ni na zaka murna da gangar Xantsara. x^2

Jagora : To, na taho al’adak kixin Sabon Sarki,
‘Y/Amshi : Had da ni makaxin na Garba yau na zama sabo,
: Uban Zagi na Muhamman mai Sabon Birni,
: Iro ya cika zakka yau ya zama sarki.

Jagora : Masu bixak kuxxi kui ta tahiyan neman kuxxi, x^2
‘Y/Amshi : Masu aiki ku yi anniyya gyara gona,
: Ga zamanin Ibrahim ba a zaman banza,
: Uban Zagi na Muhamman mai Sabon Birni,
: Iro ya cika zakka yau ya zama sarki. x^2

Jagora : Balarabe xan Yari, x^2
‘Y/Amshi : Kai a Hassan da Hussaini,

: Ga yanzu kai muka dibi,
: Ba wani bayan kai. x^2

Jagora : Na yi shekara biyu ban zo kixi ba gidan kowa,
'Y/Amshi : Anka ce Ibrahim na Dango as sarki,
: Marahwa kui mana tuqi mu ba tabshi kashi,
: Uban Zagi na Muhamman mai Sabon Birni,
: Iro ya cika zakka yau ya zama sarki.

Jagora : Sarkin ruwan Isa yana kaxi yay yi min komi, x^2
'Y/Amshi : Ya zuba mini shadda domin Jangwarzo. x^2

Jagora : Jekadan Waziri Ahmadu, x^2
'Y/Amshi : Yay taimako yay min komai,
: Ya zuba mini shadda domin Jangwarzo. x^2

Jagora : Zauna da shiri baban yari mai Alqalawa, x^2
'Y/Amshi : Na bawa ya shira du wanda kakanai yay yi.
: Uban Zagi na Muhamman mai Sabon Birni,
: Iro ya cika zakka yau ya zama sarki. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir,
Alhaji Umar xan Salihu (1957-1966)[154]*,*

39. *Gindin Waqa : Gwarzon Galadima ya ci arna,*
: Uban yari baban barga na bango.

---

154 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{147}$ $^1/_9$.

Jagora : Sarki na Jekada, x^2
'Y/Amshi : Ginshimin Ali,
: Ya mai da kura baban Marahwa,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^2

Jagora : Shi wanda yas saba yana ba ka, x^2
'Y/Amshi : In ka ga ya qyale ya qi ‘yamma,
: Ai sai ka tone shi ka san mahwari,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^2

Jagora : Baba tun ran da xan Inna yay yi sarki, x^2
'Y/Amshi : Gidajen mu mun huta mun ji daxi,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^2

Jagora : Zamaninka xan Inna mun yi sarki, x^2
'Y/Amshi : Mun sha hwuran nono mun ci kalwa,
: Mun hau dawakai mun yi zama,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^2

Jagora : Ran da ya rabke tamburran Yakubawa, x^2
'Y/Amshi : Ya xebe haushi baban uban Doma,
: Ya gade kayan Gohe na Tambari,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^2

Jagora : Kai dai tsare kayan nan na Kakanka,
'Y/Amshi : Shawai da yay mulkin Gobirawa,
: Ya mulke kowa balle qasatai,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango.

Jagora : Ummaru ya shige gida yay zama nai, x^2
'Y/Amshi : Dun masu ja mai da su banza,
: Ka san nuhwan Allah ta hi komi,

: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^2

Jagora : Ga kaya da xan Inna ya sawo min,
'Y/Amshi : Waxanda ba canji yas sawo min,
Jagora : Alkyabbu da xan Inna yas sawo min,
'Y/Amshi : Waxanda ba canji yas sawo min,
Jagora : Doki da xan Inna yas sawo min,
'Y/Amshi : Sai wanda ba canji yas sawo min,
Jagora : Riga da xan Inna yas sawo min,
'Y/Amshi : Sai wanda ba canji yas sawo min,
Jagora : Rawani da xan Inna yas sawo min,
'Y/Amshi : Sai wanda ba canji yas sawo min,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango.

Jagora : Komi nih hwaxi xan Ganjona ya ban, x^2
'Y/Amshi : Hay yanzu amma ban kai qawa ba,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^2

Jagora : Mai raba riguna xan Dango,
'Y/Amshi : Sarki mai dubun doki xan baraz zaki,
: Kai ad da dubun-dubbai na komi,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango.

Jagora : Iro je xan baraz zaki, x^3
‘Y/Amshi : Sanda xan Bawa xan Inna,
: Ja sha’anin Gobirawa,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^3

Jagora : Sai ran hawan salla niy yi kuka,
'Y/Amshi : Maidaminasa nir roqa wurin sanda,
: In ya buqata in kai qawa ta,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,

: Uban yari baban barga na bango.

Jagora : Kai mai yawan yawo ka yi banza, x^2
'Y/Amshi : Wandon ka ya kece ka yi wajje. x^2

Jagora : Ni ba ni son yawon nan na banza, x^2
'Y/Amshi : Haba wane xaure zauna wuri xai,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^2

Jagora : A gaishe ki balbela kin yi haske, x^2
'Y/Amshi : Kin zarce mai dauxa ya yi xauri,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^2

Jagora : Sarki na Jekada, x^2
'Y/Amshi : Ginshimin Ali,
: Ya mai da kura baban Marahwa,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ummaru xan Salihu (1957-1966)[155]*,*
Gindin Waqa : Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango.

Jagora : Iro je xan baraz zaki, x^3
'Y/Amshi : Sanda xan Bawa xan Inna,
: Ja sha'anin Gobirawa,

155 An sami wannan rerawa a Littafin Xahiru, G. (1990: 107-110).

: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x3

Jagora : Sarki na Jekada, x2
'Y/Amshi : Ginshimin Ali,
: Ya mai da kura baban Marahwa,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x2

Jagora : Shi wanda yas saba ma yana baka, x2
'Y/Amshi : In ka ga ya qyale ya qi samma,
: Sai ka tona shi ka sam mahwari,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x2

Jagora : Tun ran da xan Inna yay yi sarki, x2
'Y/Amshi : Gidajenmu sun huta mun ji daxi,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x2

Jagora : Zamaninka xan Inna mun yi sarki, x2
'Y/Amshi : Mun sha huran nono mun ci kalwa,
: Mun hau dawakayye mun yi zama,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x2

Jagora : Ran da ya rabka tamburran Yakubawa, x2
'Y/Amshi : Ya xebe haushi baba Ubandoma,
: Ya gade kayan Gohe na Tambai,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x2

Jagora : Kai dai tsare kayan nan na Kakanka, x2
'Y/Amshi : Shawai da yai mulkin Gobirawa,
: Ya mulke kowa balle qasatai,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x2

Jagora : Umaru ya shige gina yay zama nai, x2

‘Y/Amshi : Dum masu ja ma da su banza,
: Ka san nuhwa Allah ta hi komi,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango. x^2

Jagora : Ga kaya da xan Inna yas sawo min, x^2
‘Y/Amshi : waxanda ba canji yas sawo min. x^2
Jagora : Doki da xan Inna yas sawo min,
‘Y/Amshi : Sai wanda ba canji yas sawo min.
Jagora : Riga da xan Inna yas sawo min,
‘Y/Amshi : Sai wanda ba canji yas sawo min.
Jagora : Rawani da xan Inna yas sawo min,
‘Y/Amshi : Sai wanda ba canji yas sawo min.
Jagora : Komi nih hwaxi xan Janjoni ya ban,
‘Y/Amshi : Amma hay yanzu ban kai qahwa ba,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango.

Jagora : Sai ran hawan salla niy yi kuka,
‘Y/ Amshi : Maidamisa nir roqa wurin sanda,
: In ya buqata in kai qahwata,
: Gwarzon Galadima ya ci arna,
: Uban yari baban barga na bango.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni
Alhaji Ummaru xan Salihu (1957-1966)[156]*,*

40. *Gindin Waqa : Umaru ginshimin Ali ci hwansa,*
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Umaru ginshimin Ali ci hwansa, x^2
'Y/Amshi : Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi,
: Na Shekarau. x^2

---

156 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{147}$ $^1/_4$.

Jagora : Masu kallon sarki ku zo ga kada ya zo, x^2
'Y/Amshi : Ya yi kamab Baciri,
: Sanda yay martabas Shawai,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Ummaru sarki ka gode Allah da Manzo nai, x^2
'Y/Amshi : Baba uban Yari da gaskiya za ya cin arna,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Hankali na ya tashi xan Iro ba ya gida, x^2
'Y/Amshi : Ummaru ya zaka komi ga ciwo yana sauqi,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Zamanka Zariya xan Inna gagon Majidaxi, x^2
'Y/Amshi : Ka cika aiki daidai da daidai na Alqali,
: An yi hirwai ba a kai ga jikan Tazabga ba,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Sarkin musulmi,
'Y/Amshi : Yay yo jawabi ga yara nai,
: Ummaru jikan Sardauna ‘yan bagalan girma.
Jagora : Waziri shi ma,
'Y/Amshi : Yay yo jawabi ga yara nai,
: Ummaru jikan Sardauna yau bagalar girma.
Jagora : Malasa shi ma,
'Y/Amshi : Yay yo jawabi ga yara nai,
: Ummaru jikan Sardauna yau bagalar girma,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Bacirawa yau Sanda shi anka ba sarki,
'Y/Amshi : Haba maza ga roqon da Allah ya yi kullum.

Jagora : Yakubawa yau Sanda shi anka ba sarki,
'Y/Amshi : Haba maza ga roqon da Allah ya yi kullum.
Jagora : Hayatawa yau Sanda shi anka ba sarki,
'Y/Amshi : Haba maza ga roqon da Allah ya yi kullum,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Na ga sabkon bubuquwa ta tsaya wanka, x^2
'Y/Amshi : Ga mu mun tashi da swahe ham mun wuccikketa,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Ummaru na yi kwararenka an ce kana hwake, x^2
'Y/Amshi : Mun ka zo mun ishe Sanda jikan kilo ya hau,
: Sai mu zarce xan Inna an ce yana kalgo,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Dag Gangara sai Xankura zaki yake kwana, x^2
'Y/Amshi : Ko hwa sai Gamji xan Muhamman yake kwana,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Rambaxawa ku taho ku duqa wa baqona,
'Y/Amshi : Yau hwa baqo ni adda shi ba ni ba kowa,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Ummaru miqe da yawonka kai ni sani sarki,
'Y/Amshi : ‘Yan adawa sun zo su hwada ka ba dama,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Na ga kura da karen gida ba su yin daxi, x^2
'Y/Amshi : Marahwa ban gane abin da yas sa su gaba ba,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Hanqure da mutanenka xan Iro mai daga, x^2
'Y/Amshi : Ummaru kyawon babba ya daure da yara nai,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Abin da dun nir roqa ga jikan kilo ya ban,
'Y/Amshi : Ummaru jikan Alhajiya bai hana min ba,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Ummaru ga doki ukku ya bai masarta nai,
'Y/Amshi : Kuma da alkyabba had da koren Kano ya bai,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Ummaru ga kyankyandi da yab ba masarta nai,
'Y/Amshi : A xebe maki yac ce a buxe a ba kowa,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Ko da gani an san wanda yas samu san sarki,
'Y/Amshi : Mutum ya diba ga jikin mu ko ba hwaxa mai ba,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Ummaru na zagi ya gaji yaqi ga Kakanai,
'Y/Amshi : Da shi da kakana babu zangon da ba su kwan ba,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Kakanka ya ci Ganiyya,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana.
Jagora : Ya ci birnin ‘Yandoto,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana.
Jagora : Ya ci birnin Bardava,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana.

Jagora : Ya ci birnin Anganba,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Maza cikin tabki sun ka hwaxa suna voyo, x^2
'Y/Amshi : Duniya na ji dashe-dashenta na Alqali,
: Mu yi zaman Xantsara da jadi da Jari kuma,
: Mu yi zaman Salihu,
: Shi da xan Dada mai tabshi,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Abu ga Allah yake sai mu koma ga roqo nai, x^2
'Y/Amshi : Du inda kar roqi baqin mutum ya hanas sa ma,
: Mu zo gida mu yi roqo ga Allah ya ban sabo,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni
Alhaji Ummaru xan Salihu (1957-1966)[157]*,*
Gindin Waqa : Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Masu kallon sarki ku zo ga kada ya zo, x^2
'Y/Amshi : Ya yi kamab Baciri,
: Sanda yay martabas Shawai,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Ummaru sarki ka gode Allah da Manzo nai, x^2
'Y/Amshi : Baba uban Yari da gaskiya za ya cin arna,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,

157 An sami wannan rerawa a Littafin Xahiru, G. (1990: 107-110).

: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Hankali na ya tashi xan Iro ba ya gida, x^2
'Y/Amshi : Ummaru ya zaka komi ga ciwo yana sauqi,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Zamanka Zariya xan Inna gagon Majidaxi, x^2
'Y/Amshi : Ka cika aiki daidai da daidai na Alqali,
: An yi hirwai ba a kai ga jikan Tazabga ba,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Sarkin musulmi, x^2
'Y/Amshi : Yay yo jawabi ga yara nai,
: Ummaru jikan Sardauna ‘yan bagalan girma. x^2
Jagora : Waziri shi ma,
'Y/Amshi : Yay yo jawabi ga yara nai,
: Ummaru jikan Sardauna yau bagalar girma.
Jagora : Minista shi ma,
'Y/Amshi : Yay yo jawabi ga yara nai,
: Ummaru jikan Sardauna yau bagalar girma.

Jagora : Bacirawa yau Sanda shi anka ba sarki,
'Y/Amshi : Haba maza ga roqon da Allah ya yi kullum.
Jagora : Yakubawa yau Sanda shi anka ba sarki,
'Y/Amshi : Haba maza ga roqon da Allah ya yi kullum.
Jagora : Hayatawa yau Sanda shi anka ba sarki,
'Y/Amshi : Haba maza ga roqon da Allah ya yi kullum,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Na ga sabkon bubuquwa ta tsaya wanka, x^2
'Y/Amshi : Ga mu mun tashi da swahe ham mun wuccikketa,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Ummaru na yi kwararenka an ce kana tulki x^2
'Y/Amshi : Mun ka zo mun ishe Sanda jikan kilo ya hau,
: Sai mu zarce xan Inna an ce yana kalgo,

: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Jagora : Dag Gangara sai Xankura zaki yake kwana, x^2
'Y/Amshi : Ko hwa sai Gamji xan Muhamman yake kwana,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2
Jagora : Rambaxawa ku taho ku duqa wa baqona,
'Y/Amshi : Yau hwa baqo ni adda shi ba ni ba kowa,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.

Jagora : Abu ga Allah yake sai mu koma ga roqo nai, x^2
'Y/Amshi : Du inda kar roqi baqin mutum ya hanas sa ma,
: Mu zo gida mu yi roqo ga Allah ya ban sabo,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Audu xan Malam[158]*,*
41. *Gindin Waqa : Ya gade gidan gardaye,*
: Saraki uban xan Malam.

Jagora : Alhaji Audu na Alhaji Dawai, x^2
'Y/Amshi : Goga mai yi ma shanu hanya,
: Ya gade gidan gardaye,
: Saraki uban xan Malam. x^2

Jagora : Kai am Malam Masaki na Arzika, x^2
'Y/Amshi : Ko can ba shi aboki gunki,
: Ya gade gidan gardaye,
: Saraki uban xan Malam. x^2

Jagora : Ashe haka nan duniya tag gada,

---

158 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{147}$ $^1/_3$.

'Y/Amshi : In dai wanga gida ya kwanta,
: To, sai wanga gida ya tashi,
: Ya gade gidan gardaye,
: Saraki uban xan Malam.

Jagora : Ai ashe haka nan duniya tag gada,
'Y/Amshi : In dai wanga gida ya kwanta,
: To, sai wanga gida ya tashi,
: Ya gade gidan gardaye,
: Saraki uban xan Malam.

Jagora : Ai wada mun ka jiya tun hwarin, x^2
'Y/Amshi : Tun can dauri akwai tsohinmu,
: In ba mu da xan mandawa,
: In dai ga su gidan ‘yan Qirya,
: Mu ko ba mu da su duk xai na,
: Ya gade gidan gardaye,
: Saraki uban xan Malam. x^2

Jagora : Ku duka kau haka nan ‘yan qirya, x^2
'Y/Amshi : Taronku babbanku da yaro,
: Duk killan ga Habu yay yo ta,
: Ya gade gidan gardaye,
: Saraki uban xan Malam. x^2

Jagora : Na gaishe ku xiyan ‘yan Qirya, x^2
'Y/Amshi : Tun da ba ku haihi xiyan banza ba. x^2

Jagora : Alhaji ya gaishe ku xiyan ‘yan Qirya, x^2
'Y/Amshi : Don ba ku haihi xiyan banza ba,
: Ya gade gidan gardaye,
: Saraki uban xan Malam. x^2

Jagora : Alhaji Audu na Alhaji Dawai, x^2
'Y/Amshi : Goga mai yi ma shanu hanya,
: Ya gade gidan gardaye,
: Saraki uban xan Malam. x^2

Jagora : Kai am Malam Masaki na Arzika, x^2

'Y/Amshi : Ko can ba shi aboki gunki,
: Ya gade gidan gardaye,
: Saraki uban xan Malam. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ibrahim (1970-1975)

42. *Gindin Waqa : Kak ka xau reni*[159]*,*
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Durumbu Ibrahim xan sarki, x^3
'Y/Amshi : Kamakka ka ba ya riqon xan komi, x^3
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Uban Bunu uban baraz zaki, x^2
'Y/Amshi : Kai qwazo ka gade Sarkin Gobir Shawai. x^2

Jagora : An ce min ana ganin hadari, x^3
'Y/Amshi : Ni ban san da shi ba sai iska ya taso, x^3
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

---

159 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{147}$ $^1/_4$.

Jagora : Xan Ummaru xan Inna, x^3
'Y/Amshi : Jikan Jari maganin tahiya sai gwamko, x^3
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Zamanin akwai manya, x^3
'Y/Amshi : Ai Kakanka bai yi kyamar Kakana ba, x^3
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Can zamanin akwai Jadi, x^3
'Y/Amshi : Jadi ko da yaushe ba ya gudun Xantsara, x^3
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Jikokin Jari da Mainasara,
'Y/Amshi : Ku duk kak ku yada irin Xantsara,
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Durumbu Ibrahim xan sarki, x^3
'Y/Amshi : Kamakka ka ba ya riqon xan komi, x^3
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Uban Bunu uban baraz zaki, x^2
'Y/Amshi : Kai qwazo ka gade Sarkin Gobir Shawai. x^2

Jagora : Dango na gode, x^2
'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi. x^2
Jagora : Dango xan Galadima,
'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi.
Jagora : Salihu Marahwa na gode,
'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi.
Jagora : Mamman na gode,
'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi.
Jagora : Malam Garba na gode, x^2
'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi. x^2

Jagora : Malam Garba na gode,
'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi.

Jagora : Ga kaya da Garba yab ba da,
'Y/Amshi : Don albarkacin Durumbu magajin Shawai.
Jagora : Kaya da Garba yab ba da,
'Y/Amshi : Don albarkacin Durumbu magajin Shawai.
Jagora : Mamman na gode,
'Y/Amshi : Don albarkacin Durumbu magajin Shawai.
Jagora : Ga kaya da Garba yab ba da,
'Y/Amshi : Don albarkacin Durumbu magajin Shawai,
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ibrahim (1970-1975)[160]*,*
Gindin Waqa : Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Birnin Mako wane sai sha'awa, x^2
'Y/Amshi : An shiryad da hakimi Allah ya shiryo,
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai. x^2

Jagora : Durumbu Ibrahim xan sarki, x^2
'Y/Amshi : Kamakka ka ba ya riqon xan komi,
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai. x^2

Jagora : Uban Bala uban Mamman, x^2
'Y/Amshi : Allah dai ya ba ka albarkar Xangwamci. x^2
Jagora : Mamman na gode,
'Y/Amshi : Don albarkacin Durumbu magajin Shawai.
Jagora : Mamman na gode,

160 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{54}$ $^1/_{11}$.

'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi.
Jagora : Ga kaya wanda yab ba da, x^2
'Y/Amshi : Don albarkacin Durumbu magajin Shawai. x^2
Jagora : Dango na gode,
'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi.
Jagora : Dango xan Galadima,
'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi.
Jagora : Salihu Marahwa na gode,
'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi.
Jagora : Garba na gode,
'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi.
Jagora : Malam Garba na gode,
'Y/Amshi : Allah dai ya qara imani yai komi.
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.
Jagora : Ga kaya wanda yab ba da,
'Y/Amshi : Don albarkacin Durumbu magajin Shawai,
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Zamanin akwai manya ko,
'Y/Amshi : Tsuntsu da yaushe ba ya gudun Xantsara.
Jagora : Zamanin akwai Jadi,
'Y/Amshi : Jadi ko da yaushe ba ya gudun Xantsara,
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Zamanin akwai manya,
'Y/Amshi : Ai Kakanku bai yi kyamar Kaka na ba,
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Zamanin akwai Jadi,
'Y/Amshi : Jadi ko da yaushe ba ya gudun Xantsara,
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Jikokin Jari da Mainasara,
'Y/Amshi : Ko Daita ku zo ku yada irin Xantsara,

: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Jagora : Uban Bala uban Mamman,
'Y/Amshi : Kai qwazo ka gane shin kirkin Xangwamci,
: Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gandu, Alhaji Suntau[161],
43. *Gindin Waqa : Sarkin Gandu ubangijin gutsun gawo,*
: Iro mijin A'i gandu mai xakin Kande.

Jagora : Gandu mijin A'i goriba tai mai taho, x^2
'Y/Amshi : Allah yai ma ruwan itace ga danni,
: Sarkin Gandu ubangijin gutsun gawo,
: Iro mijin A'i gandu mai xakin Kande. x^2

Jagora : Garin Bature can za ni in ga al'adar Tsintau,
'Y/Amshi : Galadima mun yi gahwara ya ce in zo,
: Sarkin Gandu ubangijin gutsun gawo,
: Iro mijin A'i gandu mai xakin Kande.

Jagora : Kai ina can wajjenmu nij ji labarin Tsintau, x^2
'Y/Amshi : Mijin Tunikai nis sani kana xaukar kwaxi,
: Sarkin Gandu ubangijin gutsun gawo,
: Iro mijin A'i gandu mai xakin Kande. x^2

---

161 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{143}$ $^1/_9$.

Jagora : Garin Bature can za ni in ga al'adar Tsintau,
'Y/Amshi : Galadima mun yi gahwara ya ce in zo,
: Sarkin Gandu ubangijin gutsun gawo,
: Iro mijin A'i gandu mai xakin Kande.

Jagora : Gandu mijin A'i goriba tai mai taho, x^2
'Y/Amshi : Allah yai ma ruwan itace ga danni,
: Sarkin Gandu ubangijin gutsun gawo,
: Iro mijin A'i gandu mai xakin Kande. x^2

Jagora : Bara na iske masassaqa suna xibar hwaru,
: Su ko su ukku ne suna cajin hwaru,
: Guda sai yac ce tsaya gabas ka yi saurare,
: Guda kuma yac ce tsaya arewa ka yi saurare,
: Guda kuma yac ce tsaya gabas ka yi saurare,
: Tun ba su gama gardama ba ko sai ga Tsintau,
'Y/Amshi : Su duka sun shirya shawara don su vace mai
: Yac ce duw wanda yag gusa kau zai harbai,
: Sarkin Gandu ubangijin gutsun gawo,
: Iro mijin A'i gandu mai xakin Kande. x^2

Jagora : To, hwaxa ma makiyaya su sha zuwa dajin Tsintau, x^2
'Y/Amshi : In Tsintau ya ishe su ba ni zuwa ceto, x^2

Jagora : Alhajin Allah ga ni za ni roqon Alhazzai, x^2
'Y/Amshi : Saboda muqaminsu za mu bi mu yi amhwani,
: Sarkin Gandu ubangijin gutsun gawo,
: Iro mijin A'i gandu mai xakin Kande. x^2

Jagora : To, kun yi xawafi Alhaji kun yo Saffa da Marwa, x^2
'Y/Amshi : Dan nan aikin ku ya wuce dutsen Arfa,
: Sarkin Gandu ubangijin gutsun gawo,
: Iro mijin A'i gandu mai xakin Kande. x^2

Jagora : Gandu mijin A'i goriba tai mai taho, x^2
'Y/Amshi : Allah yai ma ruwan itace ga danni,

: Sarkin Gandu ubangijin gutsun gawo,
: Iro mijin A'i gandu mai xakin Kande. x²

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Sabo Shibkau xan Makau[162]*,*

44. *Gindin Waqa : Hali nai girma,*
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa.

Jagora : Ije inda shanu gaba, x²
'Y/Amshi : Ga wasu can su tahe,
: Ga wasu sun tashi,
: Sun hau kadarko lahiya,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa. x²

Jagora : Ije inda shanu gaba, x²
'Y/Amshi : Ga wasu can su tahe,
: Ga wasu sun tashi,
: Sun hau kadarko lahiya.
Jagora : To, akwai wasu na nan gida, x²
'Y/Amshi : Qara tardawa a kai,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa. x²

---

162 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{1}$.

Jagora : Kuxi xan Makau, x^2
'Y/Amshi : Kuxin isgilishi yai yawa. x^2
Jagora : Akwai kuxi gidan xan Makau, x^2
'Y/Amshi : Mazaje da mataye duka. x^2

Jagora : Akwai sule akwai sisi, x^2
'Y/Amshi : Akwai jilai kuma,
: Da cinko xan Masar,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa. x^2
Jagora : Alhaji Sabon Shibkau, x^2
'Y/Amshi : Mijin Laddi manyan danqumai. x^2
Jagora : Ashe zuma kake, x^2
'Y/Amshi : Banga mai lashe dauxar hannuwa. x^2
Jagora : In ko ka qiya,
'Y/Amshi : Magabci ya hi ka datsi a saurara maka,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa.

Jagora : Attajirin da ba shi da rana,
'Y/Amshi : Ina ruwan mu da gaishe shi,
: Ko ya yi manyan jikkuna,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa.

Jagora : Na gano wani attajiri da yaro da kwando,
'Y/Amshi : Kaico! Shin wanga irin yaro,
: Ya zo wurin shin arkane,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan mai daqquwa.

Jagora : Na gano wani attajiri da jallinsa ukku,
'Y/Amshi : Ga guda ya ci tururruvi gudan yai sagan,
: Gudan had da zaki ya kashe,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,

: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa.

Jagora : Kan ka shi zo baba ban xauka tai,
'Y/Amshi : Zamani harara ta ya kai,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa. x^2

Jagora : Wane kana hushi da ni,
'Y/Amshi : Ba ni nih hana ka cin riba ba,
: Yi kuka da Allah wahidun,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa.

Jagora : Alhaji jikka dubu ka zo mai ba dum,
: Ga wasu jikka dubu suna dawowa,
'Y/Amshi : Akwai wasu jikka dubu suna nan rumbu,
: Can an kai su banki an aje,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa.

Jagora : Mai gida da siminti,
'Y/Amshi : Na malka mai kuraye,
: Halo an ka shahwa can gabas,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa.

Jagora : Inyamirin da yai maka gugag gidan ga,
'Y/Amshi : Ya zama ma'in ko ko hakimi na yab buga,
: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa.

Jagora : Ashe zuma kake, x^2
'Y/Amshi : Banga na lashe dauxah hannuw,

: Hali nai girma,
: Halin qara gode mai ya kai,
: Na Alhaji Sallau na Alhaji xan Maidaqquwa. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ummaru xan Salihu (1957-1966)[163],

45. *Gindin Waqa : Ina anniyan ishe mai,*
: Ummaru jikan mayaqi kai nib biyo.

Jagora : Giwa za ta haihwa toro, x^2
'Y/Amshi : Nan ga na Garba am matakin 'yan'uwa,
: Ina anniyan ishe mai,
: Ummaru jikan mayaqi kai nib biyo. x^2

Jagora : Garin Bature za ni da kwana, x^2
'Y/Amshi : Ummaru ko don saboda kai nit taho. x^2

Jagora : In dai na zaka gidansu Ummaru, x^2
'Y/Amshi : Ba ni da haushi saboda na zo gida,
: Ina anniyan ishe mai,
: Ummaru jikan mayaqi kai nib biyo. x^2

Jagora : Ga hwata za ni yo ma Tsintau,
'Y/Amshi : Tsintau Allah ya sa ka yaxu,
: Ka yaxu kamad dankali kamar 'yanduma,
: Ina anniyan ishe mai,
: Ummaru jikan mayaqi kai nib biyo.

Jagora : Ga hwata za ni yo ma Tsintau,
'Y/Amshi : Tsintau Allah ya sa ka yaxu,

163 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{147}$ $^1/_6$.

: Ka yaxu kamad dankali kamar ‘yanduma.

Jagora : Inda Allah na barin mutane, x^2
'Y/Amshi : Da sai ya bar mu da ni da Tsintau,
: Ya zo ya zauna da ni sahe dut,
: Ina anniyan ishe mai,
: Ummaru jikan mayaqi kai nib biyo. x^2

Jagora : Xan Idi xan Bakwai da Delu, x^2
'Y/Amshi : Ummaru xan Jimma gangararren maza. x^2
Jagora : Xan Lairo in kwana riqo na,
'Y/Amshi : Ka nuna dokin da za ni zama gida,
: Ina anniyan ishe mai,
: Ummaru jikan mayaqi kai nib biyo. x^2

Jagora : Garin Bature za ni da kwana, x^2
'Y/Amshi : Ummaru ko don saboda kai nit taho. x^2

Jagora : In dai na zaka gidansu Ummaru, x^2
'Y/Amshi : Ba ni da haushi saboda na zo gida,
: Ina anniyan ishe mai,
: Ummaru jikan mayaqi kai nib biyo. x^2

Jagora : Giwa za ta haihwa toro, x^2
'Y/Amshi : Nan ga na Garba am matakin ‘yan’uwa,
: Ina anniyan ishe mai,
: Ummaru jikan mayaqi kai nib biyo. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Xansanda na Gangara[164]*,*

46. *Gindin Waqa : Na taho gaida babba gardaye,*
: Baba xan Inna mai gandun daji.

Jagora : A gaishe ka babba na babba xan Bawa, x^2
'Y/Amshi : Abin da Allah ka hwasau na daji,
: Na taho gaida babba gardaye,
: Babba xan Inna mai gandun daji. x^2

Jagora : A gaishe ka babba na babba xan Bawa,
'Y/Amshi : Abin da Allah ka hwasau na daji.

Jagora : Alhaji Xansanda mai dogon yaro, x^2
'Y/Amshi : Na ta kai-wa-da-kawo sun tohwa,
: Na taho gaida babba gardaye,
: Babba xan Inna mai gandun daji. x^2

Jagora : Na ishe tsamiya ta yi kyaun kunne,
'Y/Amshi : Ga makiyaya da ko gittocinsu,
: Ga tumakinsu mai takin oda,
: Babu damar a sara sai dibi,
: Na taho gaida babba gardaye,
: Babba xan Inna mai gandun daji.

Jagora : Na ishe tsamiya ta yi kyaun kunne,
'Y/Amshi : Ga makiyaya da ko gittocinsu,
: Ga tumakinsu mai takin oda,
: Babu damar a sara sai dibi.

---

164 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{143}$ $^1/_7$ - AL $^1/_{147}$ $^1/_7$.

Jagora : Ina manoma ga ‘yan takin oda,
'Y/Amshi : Wanda ya iske gawo yas sare,
: Ya yi kashi da kai nai ya tasa,
: Na taho gaida babba gardaye,
: Babba xan Inna mai gandun daji.
Jagora : Ina makiyayan ga sun sukar mulki,
'Y/Amshi : Wanda ya iske gawo yas sare,
: Ya yi kashi da kai nai ya tasa,
: Na taho gaida babba gardaye,
: Babba xan Inna mai gandun daji.

Jagora : Shin ina Lawwali shi da Zaqoli,
'Y/Amshi : Ku zo ku shaida wa babba gardaye,
: Na taho in yi mai kukan yunwa,
: Yau gidajenmu ba sauran tsaba,
: Na taho gaida babba gardaye,
: Babba xan Inna mai gandun daji.

Jagora : Ga takardu Galadima ya bai, x^2
'Y/Amshi : Gangara za ni in samo tsaba,
: Na taho gaida babba gardaye,
: Babba xan Inna mai gandun daji. x^2

Jagora : Alhaji Xansanda mai dogon yaro, x^2
'Y/Amshi : Na ta kai-wa-da-kawo sun tohwa,
: Na taho gaida babba gardaye,
: Babba xan Inna mai gandun daji. x^2

Jagora : A gaishe ka babba na babba xan Bawa, x^2
'Y/Amshi : Abin da Allah ka hwasau na daji,
: Na taho gaida babba gardaye,
: Babba xan Inna mai gandun daji. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Salihu (1945-1956),
47. *Gindin Waqa : Iro na Bawa baqon dole*[165]*,*
: Jikan na Sanda baban Yari.

Jagora : Mai ban tsoro uban Galadima, x^2
: Sarkin gida jikan na Jekada,
: Mai raba kaya baqon dole,
'Y/Amshi : Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari. x^2

Jagora : Ga hwata na uban Galadima,
'Y/Amshi : Sarkin gida jikan na Jekada,
: Mai raba kaya baqon dole.

Jagora : Mai ban tsoro uban Galadima,
‘Y/Amshi : Sarkin gida jikan na Jekada,
: Mai raba kaya baqon dole,
: Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari.

Jagora : Salihu xan Shekara na Dango, x^2
‘Y/Amshi : Bai yadda ta haushi wandon Malam,
: Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari. x^2

---

165 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{50}$ $^1/_1$ - AL $^0/_{54}$ $^1/_1$.

Jagora : Ku dangana ‘ya’uwa ku bi sarki,
‘Y/Amshi : Ba banza ka yin sarki ba,
: Sai da rabo da cewar Allah.
Jagora : Ku hanqura ‘yan’uwa ku bi sarki,
‘Y/Amshi : Ba banza ka yin sarki ba,
: Sai da rabo da cewar Allah.
Jagora : Sarki ba ya kyamar kowa,
‘Y/Amshi : Ko ko sarki ba ya kyamar sarki,
: Sarki ba ya ce mai komi,
: Amma ya zura mai Allah,
: Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari.

Jagora : Mai horon maza uban Galadima, x^2
‘Y/Amshi : Iro na Bawa baban Doma,
: Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari. x^2

Jagora : Salihu xan Shekara na Dango, x^2
‘Y/Amshi : Bai yadda ta haushi wandon Malam,
: Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari. x^2

Jagora : Sarki za ya tarben D.O.,
‘Y/Amshi : Ni ko za ni kixaun na Baba,
: Ki xauke shi ki sauke shi lahiya don Allah.
Jagora : Sarki za ya tarben Gwamna,
‘Y/Amshi : Ni ko za ni kixaun na Baba
: Ki xauke shi ki sauke shi lahiya don Allah.

Jagora : Taron shawara na yaz zo,
‘Y/Amshi : Mun zo rakkiya mun dawo,
: An yo kixan manya ta sarki,
: Ban san inda zai kwana ba,
: Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari.

Jagora : Ni dai ban san inda zai kwana ba,
‘Y/Amshi : Gobir zai tsaya ko Durvi,
: Sarki bai tsaya dun nan ba,
: Amma ya wuce sai Wurno,

: Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari.
Jagora : In an koma yin wani taro,
‘Y/Amshi : Ko ni mai kixi sai na zo,
: Amma ban zuwa huntu na,
: Sai an koma ban wata riga,
: Sai an koma ban wani doki,
: Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari.

Jagora : Ai koma shiri Magajin Mani,
‘Y/Amshi : Kogin duniya ya tashi.
Jagora : Haba koma shiri Magajin Mani,
‘Y/Amshi : Kogin duniya ya tashi.
Jagora : Kai dai koma shiri Magajin Mani,
‘Y/Amshi : Kogin duniya ya tashi.
Jagora : Ko wacce akwai dole Gobir, x^2
‘Y/Amshi : Jagoran hwaxa ya tashi. x^2

Jagora : Jari da yai irin nashi ya yi,
‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Almu da yai irin nashi ya yi,
‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Gohe da yai irin nashi ya yi,
‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Maso xan Danga da yai irin nashi ya yi,
‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Ko Baciri da yai irin nashi ya yi,
‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Sobe da yai irin nashi ya yi,
‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Mayaqi da yai irin nashi ya yi,
‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Jangwarzo da yai irin nashi ya yi,
‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Xangwamci da yai irin nashi ya yi,
‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Xan mai Jadi da yai irin nashi ya yi,
‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Ko Jari Kada da yai irin nashi ya yi,

‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Ko Ummaru da yai irin nashi ya yi,
‘Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Kai ba ka jan wani sarki,
‘Y/Amshi : Tsoro ba ya jan wani kaxo.
Jagora : Salihu ba ya jan wani sarki,
‘Y/Amshi : Tsoro ba ya jan wani kaxo.

Jagora : Kai ka xauki ragamar musulmi,
‘Y/Amshi : Wannan ba a hana ka na Malam,
: Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari.

Jagora : Mai ban tsoro uban Galadima,
: Sarkin gida jikan na Jekada,
: Mai raba kaya baqon dole.

Jagora : Ga hwata na uban Galadima,
'Y/Amshi : Sarkin gida jikan na Jekada,
: Mai raba kaya baqon dole,
: Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari.

Jagora : Salihu xan Shekara na Dango, x^2
‘Y/Amshi : Bai yadda ta haushi wandon Malam,
: Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Jadi (1915-1916)[166]*,*

48. *Gindin Waqa : Da yaqi ya ci maza,*
: Uban Yari jikan Madauci .

Jagora : Maza raba gardama Jadi, x^2
'Y/Amshi : Xan Babari gaishe ka,
: Allah wanda ya shiryo,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci . x^2

Jagora : Sarki Labo, x^2
'Y/Amshi : Baban Jekadiya zamaninka,
: Na Dango da qarhi ka zo,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci . x^2

Jagora : Tsibiri Gobirawa hwarilla,
'Y/Amshi : Ka isko na goya qarhi da iko da qarhi,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci .

Jagora : Jikan Ali jikan Alhassan, x^2
'Y/Amshi : Jikan Almu sarki waliyyi,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci . x^2

Jagora : Gamji xan Magajin gari,
'Y/Amshi : Ba hwasawa na Jekadiya,
: mai shiga hwada da qarhi,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci .
Jagora : Duniya tsohuwar runhwa,

---

166 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$ - AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{1}$.

'Y/Amshi : Wada kag gani kak ka sake,
: Ka ce ka gyara da qarhi,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci .

Jagora : Alhaji talakka talban ka ne,
'Y/Amshi : Bari yai gadon ka ko can,
: Da hwari da qarhi,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci .

Jagora : Na yi nuhwar tahowa biki,
'Y/Amshi : Allah bai nuhe ni ba da zowa,
: Tun ban kai ba birni lalura,
: Ta Kam min da qarhi,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci .

Jagora : Buri nikai in zo Tsibiri, x^2
'Y/Amshi : Akwai cibiya ta na can. x^2
Jagora : In yo ziyarar kakana, x^2
'Y/Amshi : Da sarki na Gome,
: Mai tura wa da qarhi,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci . x^2

Jagora : Taron nan da kaz zo Yamai,
'Y/Amshi : ‘Yan Dozo suna Almu ya zo,
: Sun hwaxi gaskiya ba hilahwa,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci .

Jagora : Dogon Dutsi suna Almu ya zo,
'Y/Amshi : Sun hwaxi gaskiya ba hilahwa.
Jagora : Vannawa suna Almu ya zo,
'Y/Amshi : Sun hwaxi gaskiya ba hilahwa.
Jagora : Madawa suna Almu ya zo,
'Y/Amshi : Sun hwaxi gaskiya ba hilahwa.
Jagora : Gidan Rumji suna Almu ya zo,
'Y/Amshi : Sun hwaxi gaskiya ba hilahwa.

Jagora : Ibirawa suna Almu ya zo,
'Y/Amshi : Sun hwaxi gaskiya ba hilahwa.
Jagora : Mayanawa suna Almu ya zo,
'Y/Amshi : Sun hwaxi gaskiya ba hilahwa,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci .

Jagora : Kowag gan ka ya qare kallo,
'Y/Amshi : Sai ya taho gida ba ya koma kallo,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci .

Jagora : Jikan Ali jikan Alhassan, x^2
'Y/Amshi : Jikan Almu sarki waliyyi,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci . x^2

Jagora : Hitila tocilan babu batir, x^2
'Y/Amshi : Ba ta da martaba ta hanga,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci . x^2

Jagora : Xan sarkin da ba shi da saurauta,
: To, kuma ga ya nan kusa da suqi,
: Suqi ne macijin dabatai,
: Kuma ya daxe yana nan ga rana,
'Y/Amshi : Ya daxe tabbata ba ya kai,
: Kai nai hukunci da qarhi,
: Da yaqi ya ci maza,
: Uban Yari jikan Madauci .

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gobir na Sabon Birni,

Alhaji Balarabe (1902-1904)[167],

49. *Gindin Waqa : Xangara Dabo xan Kasau,*
: Sarkin yamma wan maza.

Jagora : In dai sarki Mayaqi ne,
: Ko Mamman na Dawwa,
'Y/Amshi : Mainasara na Almu,
: Ka zama zauri mijin gida.

Jagora : Lalle sarki Mayaqi ne, x^2
: Ko Mamman na Dawwa,
'Y/Amshi : Mainasara na Almu,
: Ka zama zauri mijin gida,
: Xangara Dabo xan Kasau,
: Sarki yamma wan maza. x^2

Jagora : Balarabe jikan Balarabe,
'Y/Amshi : Giwa ba ta zamkuwa. x^2

Jagora : Balarabe kai ak kada,
'Y/Amshi : Ka na hana ‘yan su zuwa ruwa,
: Xangara Dabo xan Kasau,
: Sarki yamma wan maza.

Jagora : Jinin sarkin sarakuna, x^2
'Y/Amshi : Dunku mai shirin qwarai. x^2

Jagora : Xan hurgi kasam nikai, x^2
'Y/Amshi : Kai az zaure mijin gida,
: Xangara Dabo xan Kasau,
: Sarki yamma wan maza. x^2

Jagora : Ashe hanya ta zo gida,
'Y/Amshi : Bara a ce ko qiris,
: Kakana da na ka,

---

167 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{376}$ $^1/_2$.

: Sun wuce dajin ga mai tsawo,
: Xangara Dabo xan Kasau,
: Sarki yamma wan maza.

Jagora : Ashe Mainasara da yay yi daga,
'Y/Amshi : Na maza shina ciki.
Jagora : Muhamman Jadi da yay yi daga,
'Y/Amshi : Na maza shina ciki.

Jagora : Sun hwasa Xanmagori,
'Y/Amshi : Sun hwasa Qaura da daddare,
: Xangara Dabo xan Kasau,
: Sarki yamma wan maza.

Jagora : Tun da ina ganin zuma,
'Y/Amshi : Ni ban hwasa kallo,
: Ba dama ga raguna,
: Ka san ba ni cin damo,
: Xangara Dabo xan Kasau,
: Sarki yamma wan maza.

Jagora : Ka yo min halin Sallau, x^2
'Y/Amshi : Ka sai mini doki ina hawa. x^2

Jagora : Sarki ya ba mu riguna,
'Y/Amshi : Sai niyyaz zuwa gida,
: Xangara Dabo xan Kasau,
: Sarki yamma wan maza.

Jagora : Jinin sarkin sarakuna, x^2
'Y/Amshi : Runhu mai shirin kwarai. x^2

Jagora : Uban sarkin dogari,
'Y/Amshi : Uban Gwandu ginshiqin zagi,
: Xangara Dabo xan Kasau,
: Sarki yamma wan maza.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,

Alhaji Salihu xan Ummaru (1945-1956)[168],

50. *Gindin Waqa : Toya matsahwa baqon dole,*
: Jikan Sanda baban Yari.

Jagora : Salihu xan Shekara na dango,
'Y/Amshi : Mai daxa haushi wan xan Malam,
: Toya matsahwa baqon dole,
: Jikan Sanda baban Yari.

Jagora : Mai horon maza uban mazaje,
'Y/Amshi : Qi hana tohwa baban Garba.
Jagora : Darzaje maza uban mazaje,
'Y/Amshi : Qi hana tohwa wan xan Garba,
: Toya matsahwa baqon dole,
: Jikan Sanda baban Yari.

Jagora : Giwa ba ta tsoron tarko,
'Y/Amshi : Giwa ba ta tsoron golo,
: Ta kwashe tarakkan yara,
: Toya matsahwa baqon dole,
: Jikan Sanda baban Yari.

Jagora : Yaro yay haqon tarko nai,
'Y/Amshi : Giwa ta biya ta kwashe,
: Toya matsahwa baqon dole,
: Jikan Sanda baban Yari.

Jagora : Ashe dai kyauta mai yawa sai Allah,
'Y/Amshi : Kyauta mai yawa sai sarki,
: In ya yarda ba tambaba,
: Toya matsahwa baqon dole,
: Jikan Sanda baban Yari.

Jagora : Sarki ya yi kyautau wando,
'Y/Amshi : Sarki ya yi kyautad doki,
: Ga sirdin Masar ya bayar,

---

168 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$ - AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{1}$.

: Jikka an ka ce ya xebe,
: Toya matsahwa baqon dole,
: Jikan Sanda baban Yari.

Jagora : Ku dangana ‘yan’uwa ku bi sarki,
'Y/Amshi : Ba banza ka yin sarki ba,
: Sai da rabo da cewar Allah,
: Toya matsahwa baqon dole,
: Jikan Sanda baban Yari.

Jagora : Sarki ba ya kyamak kowa,
'Y/Amshi : Kwacce ba ya qaunas sarki,
: Sarki ba ya ce mai komi,
: Amma ya aza mai Allah,
: Toya matsahwa baqon dole,
: Jikan Sanda baban Yari.

Jagora : An koma shiri na Ali na Gambai,
'Y/Amshi : Motsin duniya ya tashi.

Jagora : Sarki za shi tarben gwamna,
'Y/Amshi : Ke mota je ki xauki baba,
: Ki kai shi da lahiya don Allah.

Jagora : Taron shawara ne yaz zo,
'Y/Amshi : Mun yo rakkiya mun dawo,
: An yit tambaya ba sarki,
: Ban san inda zai kwana ba.

Jagora : Ni dai ban san inda zai kwana ba,
'Y/Amshi : Ko birnin Kabbi ko Dutse,
: Sarki bai tsaya dun nan ba,
: Amma ya wuce sai wurno.

Jagora : In an kuma yin wani taro,
: Ko ni mai kixi sai na zo,
: Amma ban zuwa huntu na,
'Y/Amshi : Sai an kuma ban wata riga,
: Sai an kuma ban wani doki,

: Toya matsahwa baqon dole,
: Jikan Sanda baban Yari.

Jagora : Kowac ce a gundumi Gobir,
'Y/Amshi : Da gurin hwaxa ya tashi.
Jagora : Babari da yay irin nashi ya yi,
'Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Mayaqi da yay irin nashi ya yi,
'Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Ali da yay irin nashi ya yi,
'Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Buba da yay irin nashi ya yi,
'Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba.
Jagora : Balarabe da yay irin nashi ya yi,
'Y/Amshi : Bai xau shawarak kowa ba,
: Toya matsahwa baqon dole,
: Jikan Sanda baban Yari.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Bawa (1975 - 2003)[169],

169 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{1}/_{142}$ $^{1}/_{4}$.

51. *Gindin Waqa : Bawa na Jekadiya,*
: Na Dango mai saje.

Jagora : Sarki na Argiji na Magajin Gari,
'Y/Amshi : Mijin Maitakalmi,
: Na 'Yab Baraya ina gaishe ka,
: Don kanai man unhwani da gaskiya,
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje.

Jagora : Xankilo,
'Y/Amshi : Alhaji xan shekara Magajin Buhari,
: Wanda duk ka jiye ma,
: Ba ya koma albarka gobe ya walkamo,
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje.

Jagora : In dai ana dara,
'Y/Amshi : A yi qwazo a zam kashe mugun baki,
: Ko da wai ko da munahicci,
: Kissa ta xara su kashi daidai,
: Ku zam gani,
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje.

Jagora : Na ga ana son vacin tambari, x^2
'Y/Amshi : Ana shakkag ganga,
: Maza suna son su yi wasa da kai,
: Halinka suke tsoro uban qasa,
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje. x^2

Jagora : Ku masu aikin sarki, x^2
'Y/Amshi : Ku yi kula ku kama aiki daidai,
: Kada ku zo ku yi wauta,
: Ku yi abin da sarki bai ce ba,
: Ku bak qasag, x^2
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje.

Jagora : Ga wani ya yi gabas, x^2
‘Y/Amshi : Ko Bawa Xankilo ya hurgaxai,
: Yalla ko maganan nan wanda ya shira,
: Ta rinjayai ya baq qasa, x^2
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje.

Jagora : Duk wanda sarki yar runguma, x^2
‘Y/Amshi : Yana xebi ginda,
: Ya yi qiba ga xuwayya,
: Tun da hankalinsa yana kwance ya bag gado,
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje. x^2

Jagora : Ni tun da sarki ya rungume ni,
‘Y/Amshi : Ba ni zuwa gabce,
: Sai ya ba ni takardu,
: Kuma ya ba ni kaya tsadaddi mu ranqwaso,
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje.

Jagora : Sarki shi ba ni gida,
‘Y/Amshi : Kuma ya ban kuxin ginab burshi,
: Sai ya yo mana sanadin,
: Da za ni aure mai tsada,
: Mu kai gida,
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje.

Jagora : Giwa masha dahi, x^2
‘Y/Amshi : Baba uban Nari ya hwashe mugun taro,
: Uban Baraz Zaki uban Abdu,
: Kwangaren Dikkon Gande wuce maza, x^2
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje.

Jagora : Zuwanmu Sakkwato kwananmu takwas,

: Gidan Dikkon Gande, x^2
'Y/Amshi : Ana ta ba mu abinci,
: Mun qoshi, mun hole birjik kamad duma.
Jagora : Sakkwato mun ci abinci iri-iri, x^2
'Y/Amshi : Kala-kala, ham munka sake hwata,
: Jikinmu yak koma jawur kamaj jini. x^2

Jagora : Hanqurin hwari, x^2
'Y/Amshi : Sai tofa, jimirin hwaxa sai mai sanda,
: Wanda ba ya da sanda,
: Sai ya yi hwaxa ya shammatai ya yo gida.

Jagora : Uban Galadima, x^2
'Y/Amshi : Kai dai bixo tsuman geza gyare,
: Talakka jaki ne sai an bugai,
: Wurin kunne, zai gane gaskiya.

Jagora : Ga Balarabe ya dawo, x^2
'Y/Amshi : Ba ka koma jin wani na hauka. x^2
Jagora : Jari Kada ya dawo, x^2
'Y/Amshi : Ba ka koma jin wani na hauka. x^2
Jagora : Mainasara ya dawo,
'Y/Amshi : Ba ka koma jin wani na hauka,
Jagora : Tun da Bawa Jangwarzo na, x^2
'Y/Amshi : Ba ka koma jin wani na haukab bixaq qasa, x^2
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Muhammadu Sani na Ummu[170]*,*
52. *Gindin Waqa : In zo kixa inda Sani na Ummu,*
: Bai san iyaka ba in ya ga noma.

Jagora : A gaishe ka xan Yari Ubandawaki,
'Y/Amshi : Samun kwatankwacinka sai an yi tawa,

170 An Sami Wannan Rerawa ne a Kundin Gusau (1983: 475-476).

: In zo kixi inda Sani na Ummu,
: Bai san iyaka ba in ya ga noma.

Jagora : Kai yaro bai san Sani na Umbu ba,
'Y/ Amshi : Bai san na kogo ba sai an yi sulu,
: In zo kixi inda Sani na Ummu,
: Bai san iyaka ba in ya ga noma.

Jagora : Kai na zo kixi inda Sani na Umbu,
'Y/ Amshi : Ban zo kixi inda raggon maza ba,
: Sai na Sulvau na Salmanu na Alhaji,
: In zo kixi inda Sani na Ummu,
: Bai san iyaka ba in ya ga noma.

Jagora : Kai na zo kixi inda Sani na Umbu,
'Y/ Amshi : Ban zo kixi inda raggon maza ba.

Jagora : Kai yaro bai san Sani na Umbu ba,
'Y/ Amshi : Bai san na kogo ba sai an yi sulu,
: In zo kixi inda Sani na Ummu,
: Bai san iyaka ba in ya ga noma.

Jagora : Waxanga maza cutarsu ta fi su, x^2
'Y/ Amshi : Duk qulle-qullensu ya zan na banza. x^2

Jagora : Ko an ce an qulle Sani na Alhaji,
'Y/ Amshi : Ba za mu yarda da qarya qasa ba,
: In zo kixi inda Sani na Ummu,
: Bai san iyaka ba in ya ga noma.
Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Katsinan Gusau,
Alhaji Muhammad Kabir Xanbaba (1984-)[171],

53. *Gindin Waqa : Ginshimin Yari Magajin Magaji,*
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya.

---

171 A Sami Wannan Rerawa ne Daga Littafin *Diwanin Waqoqin Baka*. Gusau, S. M. 2009: 209-210.

Jagora : Ashe zaman duniya, x^2
'Y/Amshi : Juyi yakai cikin yara da manya,
: Wanda Allah yab ba,
: Son nikai mu zo mui ta biyatai,
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya. x^2

Jagora : Kokowak kare da kura, x^2
'Y/Amshi : Ai na hana ta tun bara da rani,
: Karen gida yac ce,
: Ni wanga gargaxi yai mani daxi,
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya. x^2

Jagora : Mai abu ya zo ga abunai, x^2
: Saboda shi ad da abunai,
: Tun da shi ad da abunai,
'Y/Amshi : A ba shi tun bai yi wuya ba,
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya. x^2

Jagora : Ashe zaman duniya, x^2
'Y/Amshi : Juyi yakai cikin yara da manya,
: Wanda Allah yab ba,
: Son nikai mu zo mui ta biyatai,
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya. x^2

Jagora : Alhaji Muhammadu Xanbaba, x^2
'Y/Amshi : Ko da xai ba ka da haushi,

: Tun da ka gade gidanku,
: Sai ka qara mashi soro,
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya. x^2

Jagora : Maidaji nai niyya, x^2
'Y/Amshi : Sai na zaka Gusau in ishe sarki,
: Mu yo gudun yunwa,
: Aikawa nikai iyalinmu su taso.
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya. x^2

Jagora : Da ni da bayata, x^2
'Y/Amshi : Mu wajjen mutun xari yara da mata,
: Babu mai iya xaukanmu,
: Sai Muhamman Nata'ala,
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya. x^2

Jagora : Kokowar kare da kura, x^2
'Y/Amshi : Ai na hana ta tun bara da rani,
: Karen gida yac ce,
: Ni wanga gargaxi yai mani daxi. x^2
Jagora : Ga wani ya shiga kokowa, x^2
: Ashe-ashe ba ya da qarhi,
'Y/Amshi : Ko da anka taga ya hwaxi,
: Babu jigon da ka tasai,
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya. x^2

Jagora : Tun da ya rasa mai tassai, x^4
'Y/Amshi : Halama ko ba ya da karfa. x^4
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya. x^2

Jagora : Ashe zaman duniya, x^2
'Y/Amshi : Juyi yakai cikin yara da manya,
: Wanda Allah yab ba son nikai,
: A zo ai ta biyatai,
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkak ka da hwama,
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya. x^2

Jagora : Alhaji Muhamadu Xanbaba, x^2
'Y/Amshi : Ko kaxan ba ya da haushi,
: Tun da ka gade gidanku,
: Sai ka qara mashi soro,
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkak ka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Bazai na Jangeru,
Alhaji Muhammadu[172]*,*

54. *Gindin Waqa : Dogo na Jekadiya,*
: Na Saraki Sarkin Bazai.

Jagora : Kai Jangeru za ni kwana, x^2
'Y/Amshi : Don in ga Sarkin Bazai,
: In dai na ga Sarkn Bazai,

---

[172] An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{379}$ $^1/_3$.

: Allah na yi min magani,
: Dogo na Jekadiya,
: Na Saraki Sarkin Bazai. x^2

Jagora : Ai jikan Buhari, x^2
'Y/Amshi : Xan Amadu mai halin arziki,
: Ga abin da duk ya nuhwa,
: Allah na nuhwatai da shi, x^2
: Dogo na Jekadiya,
: Na Saraki Sarkin Bazai.

Jagora : To, Sarkin Bazai na Alhaji, x^2
'Y/Amshi : Ka san zaman zamani,
: Kowas san zaman zamani,
: Sharri ba ya komi da shi,
: Dogo na Jekadiya,
: Na Saraki Sarkin Bazai. x^2

Jagora : Lalle, x^2
'Y/Amshi : An nuhwa an nuhwa,
: Aniya makomam mutum,
: Duk mai mugunyan nuhwa,
: Allah sa ta dawo garai, x^2
: Dogo na Jekadiya,
: Na Saraki Sarkin Bazai.
Jagora : Ni Maidaji na yi zave, x^2
'Y/Amshi : Amma sai da nik qwangara,
: Na zavi Sarkin Bazai,
: Tun da ba kamatai garan,
: Dogo na Jekadiya,
: Na Saraki Sarkin Bazai. x^2

Jagora : To, komi dubum mutane, x^2
'Y/Amshi : Komi mutum yag gamu,
: In dai na ga Sarkin Bazai,
: Duka ba ruwana da su.
: Dogo na Jekadiya,
: Na Saraki Sarkin Bazai. x^2

Jagora : Alhaji na taho gudun yunwa, x2
: Inda Sarkin Bazai,
: Dajinmu babu gero,
: To, kuma can gida babu shi,
‘Y/Amshi : Dawanmu ta mace,
: Kuma wakenmu ya qarmashe,
: Mu yi inda Sarkin Bazai,
: Can mu samu gero mu ci.

Jagora : Ai jikan Buhari, x3
‘Y/Amshi : Xan Amadu mai halin arziki,
: Da abin da duk ya nuhwa,
: Allah na nuhwatai da shi. x3

Jagora : Ko can damo, x3
‘Y/Amshi : Uban Jekada hanquri ag garai,
: Hay yau ban ji kukanka ba,
: Dogo na Jekadiya,
: Na Saraki Sarkin Bazai. x3

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Zazzau,
Alhaji Shehu Idris (1975-)[173]*,*

55. *Gindin Waqa : Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,*
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa.

Jagora : Akwai maza suna ga duniya, x2
: Duk ba a gane ba,
‘Y/Amshi : Sai an bincika an tona za a ganewa,
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa. x2

Jagora : Maidaji na yi tonon duniya, x2

173 An sami wannan rerawa a Kundin Gusau, S. M. (1988: 612-615).

: Ga nawa xan wayo,
‘Y/Amshi : Wanda duk ka sa ma sharri ba ka mance shi,
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa. x^2

Jagora : Ko da kag ga sarkin Zazzau, x^2
: Ka ishe lamba xai,
‘Y/Amshi : Duk sarakuna sun kwanta ba su motsawa,
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa. x^2

Jagora : Sanqira ina faxa ma magana, x^2
: Ina yi ma saqo,
‘Y/Amshi : Sai a ban ‘yar mota na yi ma koke, x^2
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa.

Jagora : Sarkin ruwan mutanen Zazzau, x^2
‘Y/Amshi : Ya yi man saqo,
: Tun da ya zuba man shadda,
: Ba ni mancewa. x^2
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa. x^2
Jagora : Ko Alhaji Audu ya zuba man, x^2
‘Y/Amshi : Naira, ba ni mancewa. x^2
Jagora : Ga rawani da Sale yab ban,
: Yac ce saboda kai Baba,
‘Y/Amshi : Sale yai kira niz zo ba ni mancewa, ko
: Sale yai kira niz zo ba ni rainawa,
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa.

Jagora : Shehu damina ta kashe ni ban yi dawa ba, x^2
‘Y/Amshi : Tun da na ishe ma yunwa ba ta kama ni. x^2
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa.

Jagora : Wanda yay yi ma alheri ba ka mance shi, x^2
‘Y/Amshi : Wanda ya shirya ma sharri ba ka mance shi,

: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa. x^2

Jagora : Munahikin zuma mai saqa dab bayan qoqo, x^2
'Y/Amshi : Ga shi na tava na lasa ban ji zaqin ba,
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa. x^2

Jagora : Shehu na Xanmadami babban hadari,
'Y/Amshi : Mai ruwa sannu,
: Ran da yay yi malka ni'ima ba ta qarewa.
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa.

Jagora : Sarkin ruwan mutanen Zazzau na yi ma kyauta, x^2
'Y/Amshi : Tun da yaz zuba min shadda ba ni mancewa,
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa. x^2
Jagora : Alhaji Audu ya zuba min,
'Y/Amshi : Man Naira ba ni mancewa,
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa.

Jagora : Aminu ya yi mulkin Zazzau,
: Bai ci amana ba,
'Y/Amshi : Ya yi ya gama ya hurce ana marabatai.
Jagora : Kabiru ya yi mulkin duniya,
'Y/Amshi : Bai ci amana ba,
: Ya yi ya gama ya hurce ana marabatai.
Jagora : Hamza ya yi mulkin duniya,
'Y/Amshi : Bai ci amana ba,
: Ya yi ya gama ya hurce ana marabatai.
Jagora : Yamusa ya yi mulkin duniya,
'Y/Amshi : Bai ci amana ba,
: Ya yi ya gama ya hurce ana marabatai.
Jagora : Abdullahi ya yi mulkin duniya,
'Y/Amshi : Bai ci amana ba,
: Ya yi ya gama ya hurce ana marabatai.
Jagora : Malam Musa da yay yi mulkin duniya,

‘Y/Amshi : Bai ci amana ba,
: Ya yi ya gama ya hurce, ana maraba tai,
Jagora : Yamusa ya yi mulkin duniya,
‘Y/Amshi : Bai ci amana ba,
: Ya yi ya gama ya hurce, ana maraba tai,
Jagora : Kuma Audu ya yi mulkin duniya,
: Bai ci amana ba,
‘Y/Amshi : Ya yi ya gama ya hurce, ana maraba tai,
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa.

Jagora : Aminu ya yi babban ganxo,
‘Y/Amshi : Nan qasar Zariya,
: Wanda nis sani ko Binuwai ba ta banke su.

Jagora : Kabiru ya yi babban ganxo,
‘Y/Amshi : Nan qasar Zariya,
: Wanda nis sani ko Binuwai ba ta banke su,
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa.

Jagora : Akwai maza suna ga duniya, x^2
: Duk ba a gane ba,
‘Y/Amshi : Sai in bincika an tona za a ganewa,
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa. x^2

Jagora : Ni Maidaji na yi tonon duniya, x^2
: Ga nawa xan wayo,
‘Y/Amshi : Wanda duk ka sa ma sharri ba ka mance shi. x^2

Jagora : Ai cikin kashi biyu, Allah ba ya mance su, x^2
: Wanda yay yi ma alheri,
‘Y/Amshi : Wanda yay yi ma sharri ba ka mance shi, x^2
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa.

Jagora : Duk wanda yay yi man alheri, x^2
: Ina ta gaida shi,

‘Y/Amshi : Wanda ba shi ban alheri, ba ni gai da shi.
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqonAllah ba ya tavewa. x^2

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alqalin Sabon Birni,
Alhaji Malam Ahmad[174]*,*

56. *Gindin Waqa : Barka da shirin zamani,*
: Malam sannu da gyaran gari.

Jagora : Alqalin Sabon Birni, x^2
‘Y/Amshi : Maganatai yanzu tana Ingila,
: Barka da shirin zamani,
: Malam sannu da gyaran gari. x^2

Jagora : Sakkwato birnin Shehu ta mu bi su, x^2
‘Y/Amshi : Mu taru mu zan gai da su, x^2
: Barka da shirin zamani,
: Malam sannu da gyaran gari.

---

174 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{378}$ $^1/_4$.

Jagora : Ana magana an ce zamani, x²
‘Y/Amshi : Ashe Allah shi az zamani,
: Sai Allah ya kiyaye gaba,
: Da wanga irin mugun zamani,
: Barka da shirin zamani,
: Malam sannu da gyaran gari. x²

Jagora : Masu ruwan kihi na su na, x²
‘Y/Amshi : Talakkawa sarki ad da su,
: Kai kau masu gari naka na, x²
: Barka da shirin zamani,
: Malam sannu da gyaran gari.

Jagora : Cikin nassi magana ta fita, x²
: In ka ce a bari ka a yi,
‘Y/Amshi : In ka ce a yi kowa ya yi,
: Malam sai wada kal lissahwa, x²
: Barka da shirin zamani,
: Malam sannu da gyaran gari.

Jagora : Yanzu ina Malam Madugu,
‘Y/Amshi : Ina Mamman duk yaranka ne,
: Barka da shirin zamani,
: Malam sannu da gyaran gari.

Jagora : Ga wani ya aje jikka xari, x²
: Ga wani bai aje ko ahu ba,
‘Y/Amshi : Ga wani ya rasa yadda zai yi da su,
: Barka da shirin zamani,
: Malam sannu da gyaran gari. x²

Jagora : Na gode Alqali, x²
‘Y/Amshi : Abin da yas shirya mana ya kyauta, x²
: Barka da shirin zamani,
: Malam sannu da gyaran gari.

Jagora : Kullum na zaka in gai da shi, x²
‘Y/Amshi : Sai ya ba ni sule arba’in,
: Ya ce ga shi mu sai kudaku, x²

: Barka da shirin zamani,
: Malam sannu da gyaran gari.

Jagora : Sakkwato dai birnin Shehu ta, x2
: Mu bi su,
'Y/Amshi : Mu taru mu zan gai da su,
: Barka da shirin zamani,
: Malam sannu da gyaran gari. x2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Hillani,
Alhaji Muhammadu Dikko Xanmaliki[175]*,*

57. *Gindin Waqa : Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,*
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada.

Jagora : Dikko farin sarki, x2
'Y/Amshi : Biyakka tai min anhwani,
: In da duk nis same shi,
: Na zai min kyauta,
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada. x2

Jagora : Na daxe ina son, x2
'Y/Amshi : In zo ga sarkin Hillani,
: To, Alhaji ta yi daidai, x2
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,

---

175 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL 1/143 1/9.

: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada.

Jagora : Jikan Hassan, x^2
‘Y/Amshi : Jikan Hussaini sarkin Hillani,
: Da munka zo gogana,
: Hwan xari yas shirya min, x^2
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada.

Jagora : Ai Dikko san ga da kab ba ni,
‘Y/Amshi : Sai na gyara shi,
: Ran da duk nas saishe shi,
: Sai ya wo tsada,
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada.

Jagora : Al’amarin jikan Nana ikon, x^2
‘Y/Amshi : Allah ne,
: Ba ya barin hwansa tai ta kai ranag gobe,
: In da yan nune shi, nan zai ramawa,
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada. x^2

Jagora : To, Ali Dogo bai haihi xa,
‘Y/Amshi : Xan iska ba,
: Kwag ga kamannunsa ka san a raba dai,
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada.

Jagora : Zuwanmu Xanmaliki ni da sarkin Hillani,
‘Y/Amshi : Rambaxawa sun je ni,
: Has sun yo tarbe,
: Tun da dai sun tarbe mu,
: Ai sun yo kyauta,
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada.

Jagora : Dibi garin Idi,

‘Y/Amshi : Had da su sun yo tarbe,
: Tun da dai sun tarbe mu,
: Ai sun yo kyauta,
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada.

Jagora : ‘Yan Tufkawa,
‘Y/Amshi : Sun biyo ni,
: Has sun yo tarbe,
: Tun da dai sun tarbe mu,
: Ai sun yo kyauta,
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada.

Jagora : To, mun bi Gatawa, x^2
‘Y/Amshi : Had da su sun yo tarbe,
: Tun da dai sun tarbe mu,
: Ai sun yo kyauta,
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada. x^2

Jagora : To, mun bi Sardauna, x^2
‘Y/Amshi : Had da su sun yo tarbe,
: Tun da dai sun tarbe mu,
: Ai sun yo kyauta, x^2
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada.

Jagora : Baqon Baura, baqon,
‘Y/Amshi : Sarkin noma Kassu,
: Alhaji lalle wannan mutum ya san kara,
: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada.

Jagora : Na biyo jikan Nana,
: Sarkin Hillani, x^2
‘Y/Amshi : Ko da xai tsatson Shehu girma yag gada,

: Na biyo jikan Nana sarkin Hillani,
: Ko da xai gagon Shehu girma yag gada.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Muhammadu Xanqoqari[176]*,*

58. *Gindin Waqa :Ya hana aikin yini,*
: Muhammadu xan qoqari.

Jagora : Asha banza za ni, x^2
: In ga Muhammadu Namijin maza,
'Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari. x^2

Jagora : Bi Muhammadu jikan Tudu,
: Na Garba ya ci garin gyazama,
'Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari.

Jagora : Yau Asha banza za ni,
: In ga Muhammadu garken maza.
'Y/ Amshi : Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari.
Jagora : Ya hana aikin yini,
: Ga Muhammadu gandun maza,
: Asha banza za ni,

176 An Sami Wannan Rerawa ne a Kundin Gusau (1983: 470-473).

: Don in ga Muhammadu qirgin maza.
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari.

Jagora : Bi Muhammadu jikan Tudu,
: Na Garba ya ci garin gyazama,
: Xan qoqari yake,
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari.

Jagora : Asha banza za ni,
: Don in ga Muhammadu garken maza
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari.
Jagora : Kowa aje gero da dawa,
: Ya aje dangin zama,
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari.
Jagora : Kowa aje gero da dawa, x^2
: Ya aje tushen zama,
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari. x^2

Jagora : Wani ya yi gida ba dame, x^2
: Ka ga kamar an yi ba a yi ba.
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari. x^2

Jagora : Asha banza sun aje rogo, x^2
: Sun aje dangin zama,
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari. x^2

Jagora : Shi ya kashe dajin gabas, x^2
: Kuma ya kashe dam qaruwa.
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari. x^2

Jagora : Ga rana ga ruwa, x^2

: Yau ana shagalin damana,
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari. x^2

Jagora : Kowa aje gero da dawa,
: Ya aje tushen zama,
‘Y/ Amshi : Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari.

Jagora : Wani ya yi gida ba dame, x^2
: Ka ga ya yi kamar ba a yi ba.
‘Y/ Amshi : Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari. x^2

Jagora : Bara mun zo qi rabon dubu,
: Hammu nan ba a manta mu ba,
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari.
Jagora : Mun kwana da yinwar dawo, x^2
: Mun kwana da yinwar tuwo,
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari. x^2
Jagora : Mun kwana da yinwar dawo, x^2
: Mun kwana da yinwar hura,
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari. x^2
Jagora : Daxa za mu gida ba kwabo, x^2
: Ka raka mu da qaton dubu,
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari. x^2

Jagora : Su wane sun yi dubun tanbaxa, x^2
: Dubun da an yi kamar ba a yi ba,
: Dubun da babu hura ba tuwo, x^2
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari.
Jagora : Su wane sun yi dubun tambaxa,
: Dubun da babu hura ba tuwo,
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,

: Muhammadu xan qoqari.

Jagora : Bi Muhammadu jikan Tudu, x^2
: Na Garba ya ci garin gyazama,
'Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari. x^2
Jagora : Muhammadu nai godiya,
: Ka ga ban yada raina ka ba,
: Xan Battu nai godiya,
: Ka ga ban yada raina ka ba,
'Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Mamman Xankaltu,

59. *Gindin Waqa : Wuce maza xan kurma*[177]*,*
: A gaida Mamman xan Kaltu.

Jagora : Sai dare jikan mata,
: Hatsi ga Mamman sun taru,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu.

Jagora : Na Kaka Mamman xan Kaltu, x^2
: Damamisan mai turaye.
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu. x^2

Jagora : Garin Idi za ni,
: Akwai mazan da ka xauka ta,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu.

Jagora : Na Magaji garin Idi za ni,
: Akwai mazan da ka xauka ta,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu.

177 An Sami Wannan Rerawa ne Kundin Gusau (1983: 476- 478).

Jagora : Na yi godiya ga Mamman ya kyauta, x^2
: Saboda damma yab ban kan,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu. x^2

Jagora : Allahu ya umfana,
: Saboda damma yab ban kan,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu.

Jagora : Sani uban dawaki ya kyauta, x^2
: Saboda Mamman ya kyauta,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu. x^2

Jagora : Abin da Allah ya rena,
: Baqin mutum bai ta da mai,
: Abin da Allah ya rena,
: Baqin mutum bai matsa shi,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu.

Jagora : Mun taho ga aiki don kara, x^2
: Ashe maza na nan Korau,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu. x^2

Jagora : Na Arxo maza na nan Korau,
: Ku zan ka jefa min galma,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu.

Jagora : Ban ja mutum ba ya bar jana,
: Rabi da jefa min galma,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu.

Jagora : Lalle su wane ai shagguna ku, x^2
: Ka san Uban shagguna nan. x^2

Jagora : Ni uban mutum nika vacewa, x^2
: Ba ya da halin ramawa,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu. x^2

Jagora : A gaida Mamman xan Kaltu, x^2
: Damamisan mai turaye,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu. x^2

Jagora : Sai dare jikan mata, x^2
: Hatsi ga Mamman sun taru,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu. x^2

Jagora : Na Magani garin Idi za ni, x^2
: Akwai mazan da ka xauka ta,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu. x^2

Jagora : Mu je ga Mamman xan Kaltu, x^2
: Damamisan mai turaye,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu. x^2

Jagora : Amiya xiyar mai turaye,
: Saboda Mamman ta kyauta,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu.

Jagora : Mai gari ban rena ba, x^2
: Saboda Mamman ta kyauta,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu. x^2

Jagora : ‘Yar Gajera Allah umfana, x^2
: Saboda Mamman ta kyauta,
‘Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gaida Mamman xan Kaltu. x^2

Makaxi : Alhaji Sa’idu Rambaxawa Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Umar Na’Allah (1966-1975-)[178],
60. *Gindin Waqa : Gagara gasa na Alhaji Gardaye,*
: Umaru gagon Bala uban Sarkin fada.

Jagora : Baba kan hana, x^2
‘Y/Amshi : Taron maza uban sarki Mamman,
: Faxa masu kowa ka ja ma sarki ya fasa,
: Gagara gasa na Alhaji Gardaye,
: Umaru gagon Bala uban Sarkin fada. x^2

Jagora : Xan Inna, x^2
‘Y/Amshi : Xan sarauniya, xan mai Runji,
: Umaru xan Bawa,
: Ba a kai ma ‘yan kamanci, x^2
: Gagara gasa na Alhaji Gardaye,
: Umaru gagon Bala uban Sarkin fada.

Jagora : Alhaji ka rabu da dibin maza, x^2
‘Y/Amshi : Su nai ma bakanta,
: Umaru ka san abin da Shawai yas shirya,
: Gagara gasa na Alhaji Gardaye,
: Umaru gagon Bala uban Sarkin fada. x^2

178 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{54}$ $^1/_4$.

Jagora : In don xan Hakimin ga mai, x^2
‘Y/Amshi : Mugun hali,
: Umaru na so a warware mai hakimci, x^2
: Gagara gasa na Alhaji Gardaye,
: Umaru gagon Bala uban Sarkin fada.

Jagora : Ashe kokuwar kare da kura,
‘Y/Amshi : Ta qare,
: Gagara gasa na Alhaji Gardaye,
: Umaru gagon Bala uban Sarkin fada.

Jagora : Gagara gasa na Alhaji Gardaye,
‘Y/Amshi : Umaru tsatson Bala uban sarkin fada,

Jagora : Baba kana hana, x^2
‘Y/Amshi : Taron maza uban sarki Mamman,
: Faxa masu kowa ka ja ma sarki,
: Ya fasa.
: Gagara gasa na Alhaji Gardaye,
: Umaru tsatson Bala uban sarki fada. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Madawa, Alhaji Muhammadu[179]*,*

61. *Gindin Waqa : Na zaka barka da azzukka,*
: Sarkin Madawa Muhammadu,
: Ko yanzu duniya ta yo mai haske.

Jagora : Ko can na san gidan kadannu, x²
'Y/Amshi : Sai 'yan taru,
: Yaqi ya hwaxi 'yan hawa sun dawo ganga,
: Na zaka barka da azzukka,
: Sarkin Madawa Muhammadu,
: Ko yanzu duniya ta yo mai haske. x²

Jagora : Wanga gidan tawaye ne, x²
'Y/Amshi : Gidan Jibo sarki yag gado,
: Hwaxa masu ba mai shiga gidan,
: Sai in bayan kai,
: Na zaka barka da azzukka,
: Sarkin Madawa Muhammadu,
: Ko yanzu duniya ta yo mai haske. x²

Jagora : Ashe sabilin kaza, x²
'Y/Amshi : Qadangare yag ga ruwan kasko,
: Ashe ko na san,
: Qadangare ya sha daxi nai. x²
Jagora : Ni Alhaji Maidaji xan mutanen, x²
'Y/Amshi : Sabon Birni Sabilin sarkin ga,
: Za ni in kwan huxu Madawa. x²

---

179 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{1}/_{376}$ $^{1}/_{7}$.

Jagora : Hwadawan Madawa ina masoya, x^2
'Y/Amshi : Sabon sarki ku yo mana kaya,
: Da za ni sa wa sabon sarki,
: Na zaka barka da azzukka,
: Sarkin Madawa Muhammadu,
: Ko yanzu duniya ta yo mai haske. x^2
Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni
Mai Waqa : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ibrahim (1970-1975)[180],

62. *Gindin Waqa : Sadauki Bala gagon Salihu,*
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho.

Jagora : Da girma da imani, x^2
'Y/Amshi : Wanda duk yab buqata ga Allah,
: Ya biya mai,
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho. x^2

Jagora : Alhaji ya san biyar,
'Y/Amshi : Allah, tun da ya sa zumunta,
: Yana xaukan 'yan'uwa,
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho.

Jagora : Kai ko yau da,
'Y/Amshi : Mazan birni gidan Sanda,
: Birnin da Sanda yai shubka ya fito,
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho.

Jagora : Iron gidan Bawa Jangwarzo, x^2
'Y/Amshi : Iron xan Inna ya hau kamaj jari ya hawo,
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho. x^2

Jagora : Sarki niqatau, x^2

---

180 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{375}$ $^1/_{10}$.

‘Y/Amshi : Uban Jabau uban xan Inna,
: Ya gyara kulkin horon maza, x^2
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho.

Jagora : Duk wanda Bawa yai, x^2
‘Y/Amshi : Mulkin Gobirawa,
: Ga naka zamani yah hito. x^2
Jagora : Duk wada Halliru,
‘Y/Amshi : Yai mulkin Gobirawa,
: Ga naka zamani yah hito.
Jagora : Duk wada Jari yai,
‘Y/Amshi : Mulkin Gobirawa,
: Ga naka zamani yah hito.
Jagora : Duk wada Sambo,
‘Y/Amshi : Yai mulkin Gobirawa,
: Ga naka zamani yah hito.
Jagora : To, yanzu ga naka,
‘Y/Amshi : Zamani, Iro xan Inna,
: Ba wanda yam motsa an yi shu,
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho.

Jagora : Sarki niqatau, x^2
‘Y/Amshi : Uban Jabau uban xan Inna,
: Ya gyara kulkin horon maza,
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho. x^2

Jagora : Duk wada nig ga dama haka,
‘Y/Amshi : Haka zan faxi
: Tun da Alhaji Isa na nan gidanai,
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho.

Jagora : Sarki ya ba ni doki kyauta, x^2
‘Y/Amshi : Sannan ya ba ni ‘yar hanya,
: Kuma ga ta Faranshi ‘yar Nijar,
: To, yau kyautakka ta wuce godewa,

: Sai in tashi in durqusa in tuba xai. x^2

Jagora : Alhaji Isa ina gode mai,
'Y/Amshi : Don ga dammeman da yas shirya man,
: Alhaji Maidaji ya gode ma qwarai.
Jagora : Alhaji Abubakar,
'Y/Amshi : Ya kyauta,
: Don ga takardun da yas shirya man,
: Alhaji Maidaji ya gode ma qwarai.
Jagora : Alhaji Dango,
'Y/Amshi : Ina gode mai,
: Don ga takardun da yas shirya man,
: Alhaji Maidaji ya gode ma qwarai,
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho.

Jagora : Jikan Kunda magajin Dango, x^2
'Y/Amshi : Na kama ni hau uban Mamman swahe dut,
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho. x^2

Jagora : Iro jikan mazajen Gobir, x^2
'Y/Amshi : Jikan Jadi da sarki Jari,
: Sarki roqon ga ne da swahai yay yi ma, x^2
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho.

Jagora : Alhaji ya san biyar, x^2
'Y/Amshi : Allah, tun da ya sa zumunta,
: Yana xaukan 'yan'uwa,
: Sadauki Bala gagon Salihu,
: Inda Alhaji Ibrahim nit taho. x^2

Jagora : Da girma da imani, x^2
'Y/Amshi : Wanda duk yab buqata ga Allah,
: Ya biya mai,
: Sadauki Bala gagon Salihu,

: Inda Alhaji Ibrahim nit taho. x²

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Tsibirin Gabas,
Alhaji Ali Kambakarwa[181]*,*

63. *Gindin Waqa : Na zo ganin bajinin qani,*
: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya.

Jagora : Dogo da gado na Muhammadu, x²
'Y/Amshi : Giwa maganin qaramin dawa,
: Na zo ganin bajinin Ali,
: Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya. x²

Jagora : Gobir na Bawa uwah hwaxa, x²
'Y/Amshi : Kakanka ya yi kwararrame,
: Ya koma yai tsibirin gabas,
: Na zo ganin bajinin qani,
: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya. x²

Jagora : Nai marmari in zo Gubur, x³
'Y/Amshi : Tsibirin gidanmu na Awwali,
: Babban gida na nan duniya,
: Na zo ganin bajinin qani,
: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya.x³

Jagora : Yakubu, x²
'Y/Amshi : Shi da Ade da Hwankale,
: Na san gidansu na can gabas. x²

Jagora : Da baranqwame da Kututturu, x²

---

181 Wannan rerawa an same ta a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. A Faifai mai lamba AL $^{1}/_{376}$ $^{1}/_{4}$.

‘Y/Amshi : Na san gidansu na can gabas. x^2

Jagora : Na san gidansu gabaccin Makka,
‘Y/Amshi : Gani da anka gano muna.
Jagora : Xan sanda ko dai ba ka nan, x^2
‘Y/Amshi : Na san kana da mazan hwaxa,
: Na zo ganin bajinin qani,
: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya. x^2

Jagora : Galadima na Yashe, x^2
‘Y/Amshi : Da yaz zaka ya ishe Alhaji Xantsumi,
: To, ha madami da shi a kai. x^2
Jagora : Da gidan Magaji da Xantsumi, x^2
‘Y/Amshi : An ba mu abinci iri-iri,
: Kullum shira muna shi ya kai. x^2

Jagora : Alhaji na zaka godiya,
‘Y/Amshi : Dokin da ya aikan mana,
: Dum murna xai mu kai,
: Na zo ganin bajinin qani,
: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya.

Jagora : Gobirawa kui muna gahwara, x^3
‘Y/Amshi : Alhaji ban kwana ya kai,
: Ba mu san ta rai ba ga duniya,
: Na zo ganin bajinin qani,
: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya. x^3

Jagora : Na gode mushe Abubakar, x^3
‘Y/Amshi : Jekada yai komi,
: Albarkacin bajimin Ali. x^3
Jagora : Mushe Umaru na gode maka, x^3
‘Y/Amshi : Riga ta hwan tara yay yi min,
: Albarkacin bajimin Ali.
: Na zo ganin bajinin qani,

: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya. x^3

Jagora : Mushe Musa na gode maka, x^2
'Y/Amshi : Don ga akwati da yai mana,
: Duk ya cika shi da riguna. x^2

Jagora : Bayan ya cika shi da riguna, x^3
'Y/Amshi : Ya ba ni zanen jikka bakwai,
: Albarkacin bajimin Ali.
: Na zo ganin bajinin qani,
: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya. x^3

Jagora : Alhaji ya zaka lahiya, x^3
'Y/Amshi : Ya zo gida da hwarin ciki. x^3

Jagora : Kai tun rad da Alhaji yaz zaka, x^2
'Y/Amshi : Tscibiri zama maka xai a kai. x^2

Jagora : Ga Tscibirin da had danginka,
'Y/Amshi : Han mu gama maka xai mu kai,
: Na zo ganin bajinin qani,
: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya.

Jagora : Sarki na Amina, na Isaka,
'Y/Amshi : Mi kaka shawara,
: Kai an ka bam ma qasag gabas,
: Na zo ganin bajinin qani,
: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya.

Jagora : Allah da ya tsira duniya, x^2
'Y/Amshi : Ya yo ta don a yi shawara. x^2
: Na zo ganin bajinin qani,
: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Bawa (1975- 2003)[182]*,*

64. *Gindin Waqa : Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,*
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni.

Jagora : Taqamad da nikai ta ka ta uban 'yan kwana, x²
'Y/Amshi : Lokaci ya kama ka ba ni sabbin kaya,
: Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni. x²

Jagora : Bawa uban Balarabe shirya zamanka, x²
'Y/Amshi : Tun da ka zama sarki,
: Tun da kai sarki yau ba ka da haushin kowa, x²
: Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni.

Jagora : Sarki ka ta da Tawam Makau,
'Y/Amshi : Ka ta da Alqalawa,
: Ka shirya Sabon Birni wanda Shawai yay yi,
: Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni.

Jagora : Baba uban Ali uban Sallau, x²
'Y/Amshi : Uban Xan'isa shi a uban mu gurin,
: Xa ag garai ya cim mai. x²

Jagora : Daga Jari kada tat taho ga sarki Shawai, x²
: Dag garai Salihu xan Durumbu yaz zama sarki,
: Dag garai Ummaru xan sarauniya yai sarki,
'Y/Amshi : Dag garai Ibrahim na Bawa yaz zama sarki,
: Mu leqa hwadar Inna Bawa shi ma ya kai,
: Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni. x²

---

182 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{1}/_{144}$ $^{1}/_{4}$.

Jagora : Gobirawa ku yi hankali ku bag ganganci, x^2
‘Y/Amshi : Inda nis saba ya hi inda nis sha daxi,
: Don wuya ta ni ban kula da daxin wani ba, x^2
: Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni.

Jagora : Shirya zamanka tun da ka zama sarki, x^2
‘Y/Amshi : Tun da kai sarki yau ba ka da haushin kowa. x^2

Jagora : In kwana bai qare ba ba a saurin kuka, x^2
‘Y/Amshi : Bawa ka san Allah ka gyara kayan kowa,
: Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni. x^2

Jagora : Allah mai gyara mutum guda ya wo mai baiwa, x^2
‘Y/Amshi : Ya shirya sauran dangi su bi shi don baiwa tai,
: Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni. x^2

Jagora : Dikkon Gande xan Muhammad inda kak kai ya kai,
‘Y/Amshi : Don shi ak kyawon mutum a san halinai,
: Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni.

Jagora : Dikko na biyo in gaisai hwan xari yab bayat,
‘Y/Amshi : Alhaji ya dai gode abin da yas shiryo mai.
Jagora : Uban Dawaki riguna ya aiko min,
‘Y/Amshi : Alhaji ya dai gode abin da yas shirya mai.
Jagora : Garkuwa na dai gode ya biya ni yai komi,
‘Y/Amshi : Alhaji ya dai gode abin da yas shiryo mai.
Jagora : Ai dole in gai da Waziri wanda al Lajinge,
‘Y/Amshi : Alhaji ya dai gode abin da yas shiryo mai.
Jagora : To kuma na gode ma Alhaji xan Adamawa,
‘Y/Amshi : Alhaji ya dai gode abin da yas shirya mai,
: Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni.

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,

Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ibrahim(1970-1975)[183]*,*

65. *Gindin Waqa : Madogara na Alhaji Isa,*
: Iro xan Magaji Uban Yari,
: Ginshiqin Gabas na Baraya.

Jagora : Sarkin sarakuna kake xan, x^2
'Y/Amshi : Inna maraji ga Bamfai. x^2

Jagora : Ibrahim xan Ibrahim,
'Y/Amshi : Madogara na Alhaji Isa,
: Iro xan Magaji uban Yari,
: Ginshiqin gabas na Baraya.

Jagora : Ga dauri ka hana wanka, x^2
'Y/Amshi : Sarki uban makama da Bango,
: Maza su bak haye maka Barde,
: Saboda na ga ba ka da daxi,
: Madogara na Alhaji Isa,
: Iro xan Magaji Uban Yari,
: Ginshiqin Gabas na Baraya. x^2

Jagora : Sarki da hankali shi ka aiki, x^2
'Y/Amshi : Wanda yah hi yi da agogo,
: Don mutum shi na da agogo,
: Bai yi shawara ba kama tai,
: Madogara na Alhaji Isa,
: Iro xan Magaji Uban Yari,
: Ginshiqin Gabas na Baraya. x^2

Jagora : Na Bawa tun kana xan sarki, x^2
'Y/Amshi : Bai yi qa'ida ba da kowa,
: Don mutum na ra'ayi nai,
: Iro bai kula da mutum ba. x^2
Jagora : Tun daq qasar Gobir, x^2
'Y/Amshi : Hat Tscibiri,

---

183 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{375}$ $^1/_9$.

: Haka za da Alqalawa,
: Iro an aza maka girma,
: Ka xauki anniyar riqe baya,
: Madogara na Alhaji Isa,
: Iro xan Magaji Uban Yari,
: Ginshiqin Gabas na Baraya. x^2

Jagora : Balle abin da zai kashe kuwa, x^2
'Y/Amshi : Na san ba zai rage ma kare ba,
: Abin da yac ci uban Garba,
: Ya gama da Alhaji Isa, x^2
: Madogara na Alhaji Isa,
: Iro xan Magaji Uban Yari,
: Ginshiqin Gabas na Baraya.

Jagora : Ni dai ina ta horonku mazanmu, x^2
'Y/Amshi : Ku dai ku xauki batu na,
: Duk wanda yay yi matan aure,
: Sai ya zan riqe su gaba xai,
: Sarki ka zan riqe mu gaba xai
: Zavi son ka ba shi da daxi,
: Madogara na Alhaji Isa,
: Iro xan Magaji Uban Yari,
: Ginshiqin Gabas na Baraya. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa,
Mai Waqa : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Umaru Na-Allah (1957-1966),

66. *Gindin Waqa : Uban Jekadiya*[184]*,*
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin magatakarda.

Jagora : Gyara shirin zama da kai da mutanenka, x²
'Y/Amshi : Kar ka ce ga wani wanda ba ya son ka,
: Uban Jekadiya,
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin magatakarda. x²

Jagora : Allah xai ka qin mutum ya ji zahi, x²
'Y/Amshi : Don mutum ya ce ba ya son ka me yake ma. x²

Jagora : Giwa ta hi gangarawa kuma tahi gewaye, x²
'Y/Amshi : Darzaze take ga rahi. x²

Jagora : Katakoren gidan Muhamman, x²
'Y/Amshi : Bajimin gidan kada. x²

Jagora : Ummaru, Ummarun gidan Ummaru, x²
'Y/Amshi : Sa maza ladab Ummaru sa maza lavewa,
: Uban Jekadiya,
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin magatakarda. x²

Jagora : Allahu duniya mui ta abin da za mu yi, x²
'Y/Amshi : Ba nan za mu tabbata ba. x²

Jagora : Ni ba abin da yay yi min zahi da duniya, x²
'Y/Amshi : Sai Allah da yas shira mutuwa yag gama ta shexa. x²

Jagora : In hairan ka ke, x²
'Y/Amshi : Ka iske hairan yana jiranka. x²

Jagora : In sheri ka ke, x²
'Y/Amshi : Ka iske sheri na jiranka. x²

[184] Wannan rerawa an same ta ne a wajen Xahiru, G. 1990: 103-105.

Jagora : Lalle abin da ka haihwa, x^2
'Y/Amshi : Du kana ishewa. x^2

Jagora : In kai ta shwaran sheri, x^2
'Y/Amshi : Su da xa uwayensu sun ji dai kumya,
: Tun da sun qi yarda,
: Uban Jekadiya,
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin magatakarda. x^2

Jagora : Sarkin hula da babban dango, x^2
'Y/Amshi : Wanda yay yi riqo yay yi anniyar yi. x^2

Jagora : Xan sarauniya xan Dango, x^2
'Y/Amshi : Ummaru giwa tarbe shirin maharb,
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin magatakarda. x^2

Jagora : Sarki uban salau xan dodo, x^2
'Y/Amshi : Sarki uban Galadima ya haye aduwai. x^2

Jagora : Uban lihidda, x^2
'Y/Amshi : Sarkin Gobir abin da kay yi,
: Nuhi shi ka kai ga ranka,
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin magatakarda. x^2

Jagora : Bari shawara da mai makalamanka, x^2
'Y/Amshi : Saboda sarki ba shawara ya kai ba,
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin magatakarda. x^2

Jagora : Taron nan da kun ka zo, x^2
'Y/Amshi : Ni ban zo ba na ji wai,
: Bango da Labbo Jekada,
: Su suka hwaxa min,
: Sanda ubangijin Makama,

: Bajimin magatakarda. x^2

Jagora : Sarauniya da tas sabka tay yi girgiza,
'Y/Amshi : Sai tac ce ma Garba,
: Wannan sarkin wace jiha ne,
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin magatakarda. x^2

Jagora : Sai Garba xan Hassan,
'Y/Amshi : Yac ce mat Babacire ne.

Jagora : In ka ji Bawa Jangwarzo nan cikin takarda, x^2
'Y/Amshi : Shi na aka rubuta,
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin magatakarda. x^2

Jagora : Riqa qwrai qwarai, x^2
'Y/Amshi : Bar tsoron uban zagi,
: Jikan Sanda gaskiya Allah ta hi yin mutane.
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin magatakarda. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Umar Shawai (1957-1966)[185],

185 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{143}$ $^1/_{12}$.

67. *Gindin Waqa : Baban yari baban Makama,*
: Baba uban Lihidda na Sardauna.

Jagora : Sarki ya kwana da hwarin ciki, x^2
'Y/Amshi : Har yau bai kwan da muni garai ba,
: Baban yari baban Makama,
: Baba uban Lihidda na Sardauna. x^2

Jagora : Ya zo Makka ya zo Madina, x^2
'Y/Amshi : Alhaji ya taho lahiya lau,
: Baban yari baban Makama,
: Baba uban Lihidda na Sardauna. x^2

Jagora : Ga Alhaji ya taho za mu tarbe,
'Y/Amshi : Da wace gaisuwa zan ishe mai.

Jagora : Ko waqar …., x^2
'Y/Amshi : Sarauta mu kai mai,
: Koko dai salati mu kai mai. x^2

Jagora : To, in kau salati mu kai mai, x^2
'Y/Amshi : To, sun ce, "'Yan'uwa babu zambo",
: Baban yari baban Makama,
: Baba uban Lihidda na Sardauna. x^2

Jagora : Baqon Jidda baqon Kano,
'Y/Amshi : Alhaji baqon Ministan Arewa,
: Baban yari baban Makama,
: Baba uban Lihidda na Sardauna.

Jagora : Sarkin Makka ya aiko wasiqa,
'Y/Amshi : Ya aiko ma jikan ta Barga.
Jagora : Kuma Sardauna ya aiko wasiqa,
'Y/Amshi : Ya aiko ma jikan ta Barga,
Jagora : Sun ce,
'Y/Amshi : Galibin duniyag ga,
: Duka kowa ya kama musulunci,
: Baban yari baban Makama,
: Baba uban Lihidda na Sardauna.

Jagora : A yi kono da salla da zakka, x^2
'Y/Amshi : Ai ta abin da Allah ka qamna. x^2

Jagora : A yi amre a zam son zumunta, x^2
'Y/Amshi : A zam son zumunta,
: Ai ta abin da Allah ke qamna,
: Baban yari baban Makama,
: Baba uban Lihidda na Sardauna. x^2

Jagora : To, ni ga ni na sa tsari,
'Y/Amshi : Amma matan gari na hanawa.

Jagora : Lalle matan gari na ta vanna, x^2
'Y/Amshi : Don ba su san abin da Allah ka so ba. x^2

Jagora : Wance da wance sun gadi vanna, x^2
'Y/Amshi : To, vannassu ba za ta ci ba,
: In ma ta ci Allah kiyaye. x^2

Jagora : Ga matan da nas sa tsari, x^2
'Y/Amshi : Yau ga su ga rariya za su tarbe. x^2
: Baban yari baban Makama,
: Baba uban Lihidda na Sardauna.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Xan Bawa[186]*,*
68. *Gindin Waqa : Ya tara dame mai dama,*
: Xan Bawa qanen mai gona.

Jagora : Xan Bawa magajin Jimro, x^2

186 An sami wannan rerawa ne a Cikin Kundin Gusau, S. M. 1983: 469-470.

: Na Badiga jikan Mana,
'Y/ Amshi : Kai mun ka sani gun qwazo,
: Ya tara dame mai dama,
: Xan Bawa qanen mai gona. x^2

Jagora : Dubun Xan Bawa faxin Allah ne, x^2
'Y/ Amshi : Allah yai bayu ba mai tasai,
: Ya tara dame mai dama,
: Xan Bawa qanen mai gona. x^2

Jagora : In dai na zaka Jauri yawona, x^2
'Y/ Amshi : In na iske manun 'Yar Kuta,
: Sai ya bani dame in xauko. x^2

Jagora : Kullum dai na zaka yawona, x^2
'Y/ Amshi : In na iske mijin 'Yar Kuta,
: Sai ya ba ni dame in xauko, x^2
: Ya tara dame mai dama,
: Xan Bawa qanen mai gona.

Jagora : Xan Bawa inai ma horo, x^2
'Y/ Amshi : Kai dai ka tsare horo na. x^2

Jagora : To, horon da nikai muku Anna, x^2
'Y/ Amshi : Kowa ya riqe kwasa tai.
: Ya tara dame mai dama,
: Xan Bawa qanen mai gona. x^2

Jagora : Kowa yi dubu har yay yi rabo, x^2
'Y/ Amshi : Ya xau maganar kaka nai. x^2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,
Mai waqa : Alhaji Isyaka Abarshi[187]*,*

69. *Gindin Waqa : Abarshi xan mai damma xan shibo,*
: Xan Shaku da niyya nig ga nai.

Jagora : Ina na mani ga Anne xan Bawa, x^2
'Y/Amshi : Mai katakka da aiki swahe duk,

187 An sami wannan rerawa ne a Cikin Kundin Gusau, S. M. 1983: 467-469.

: Abarshi xan mai damma xan shibo,
: Xan Shaku da niyya nig ga nai. x^2

Jagora : Abarshi na xan Kura xan Nomau, x^2
'Y/Amshi : Biyakka ta hi biyas shaggun xiya. x^2

Jagora : Abarshi ya kashe canjin kuxxi,
'Y/Amshi : Koyaushe yay yi kirana nit taho,
: Sai ya haxa mu da Naira sabuwa,
: Abarshi xan mai damma xan shibo,
: Xan Shaku da niyya nig ga nai.

Jagora : Ina na Mani ga Anne xan Bawa, x^2
'Y/Amshi : Mai katakka da aiki swahe duk. x^2

Jagora : Ya aje dawa ya aje gero, x^2
'Y/Amshi : Abarshi ya aje tarin gujiya. x^2

Jagora : Annen da ba ya da damman gero,
'Y/Amshi : Ba ni kixa mashi turayen dubu,
: Abarshi xan mai damma xan shibo,
: Xan Shaku da niyya nig ga nai.

Jagora : Ka ishe xan Anne na noma, x^2
'Y/Amshi : Azzahwari ta kama yai gida
: Halama bai iya kishin zucci ba. x^2

Jagora : Mu zo ganinka halalin 'Yar Gwaggo, x^2
'Y/Amshi : Masu dambe da aiki swahe duk. x^2
Jagora : Abarshi na xan Kura na Nomau, x^2
'Y/Amshi : Biyakka tahi biyas shaggun xiya. x^2

Jagora : Ya aje dawa ya aje gero,
'Y/Amshi : Abarshi ya aje tarin gujiya.

Jagora : Anne da ba shi da damman gero,
'Y/Amshi : Ba ni kixa masa turayen dubu,
: Abarshi xan mai damma xan shibo,
: Xan Shaku da niyya nig ga nai.

Jagora : Anne da ba shi da damman gero,
'Y/Amshi : Ba ni kixa masa turaye qwarai,
: Abarshi xan mai damma xan shibo,
: Xan Shaku da niyya nig ga nai.

Jagora : Ina na Mani ga Anne xan Bawa, x²
'Y/Amshi : Mai katakka da aiki swahe duk. x²

Jagora : Mu zo ganinka halalin 'Yar Gwaggo, x²
'Y/Amshi : Masu dambe da aiki swahe duk. x²

Jagora : Abarshi ya kashe canjin kuxxi,
'Y/Amshi : Koyaushe yay yi kirana nit taho,
: Sai ya haxa mu da Naira sabuwa,
: Abarshi xan mai damma xan shibo,
: Xan Shaku da niyya nig ga nai.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa,
Mai Waqa : Sarkin Gobir Umaru[188]*,*
70. *Gindin Waqa : Niqatau na Jekada bajimin magajin gari,*
: Ummaru gam da ram bulgu wayayyen sarki.

Jagora : Giwa mai raba kaya baban Galadima, x²
'Y/Amshi : Baban Magajin gari mai sabon Birni. x²

Jagora : Ka zama lahiya na zagi, x²

[188] An Sami Wannan Rerawa ne a Kundin Xahiru, G. (1990: 105-107).

'Y/Amshi : Jikan Kilo Luna baban Bangu,
: Ubangijin Yari baban ‘yan kwana,
: Niqatau na Jekada bajimin magajin gari,
:Ummaru gam da ram bulgu wayayyen sarki. x^2

Jagora : Jikan Alhaji ya riqe ‘yan uba, x^2
'Y/Amshi : Ba kwamre da su na Jekadiya,
: Sarkin daga, x^2
: Niqatau na Jekada bajimin magajin gari,
:Ummaru gam da ram bulgu wayayyen sarki.

Jagora : Baban mai hwada Barmo, x^2
'Y/Amshi : Uban Ajiya hau lahiya,
: Xan Alu gatan mazaba, x^2
: Niqatau na Jekada bajimin magajin gari,
: Ummaru gam da ram bulgu wayayyen sarki.

Jagora : Wanda yaj ja ma sarki, x^2
'Y/Amshi : Ko Allah ya hana ja ma domin qarhi nai. x^2

Jagora : Haba Gobirawa ga Ummarun naku ya dawo,
'Y/Amshi : Ga Ummarun naku ya zo ya gode,
: Gidan nan da Gohe yab bar mai.

Jagora : Haba Gobirawa ga Ummarun naku ya dawo,
'Y/Amshi : Ga Ummarun naku ya zo ya buga,
: Tamburan nan da Gohe yab bar mai.
Jagora : Haba Gobirawa kun yi sake, x^2
'Y/Amshi : Kun bar zakara ya shige akurki. x^2

Jagora : Har ya cera ya hid da toro, x^2
'Y/Amshi : To ku yi anniya tun da tsawa,
: Ta yi tsawo. x^2

Jagora : Ku bar mishi akurki, x^2
'Y/Amshi : Shure mutum ya kai,
: Tun da gawa ta yi tsawo,
: Niqatau na Jekada bajimin magajin gari,
: Ummaru gam da ram bulgu wayayyen sarki. x^2

Jagora : Haba Gobirawa ga tsarinku ya zama kada, x^2
'Y/Amshi : Har ya aza qanquna sun miqe. x^2

Jagora : Yanzu hwaranta ta kai,
'Y/Amshi : In da goshi ya yi tsawo,
: Niqatau na Jekada bajimin magajin gari,
: Ummaru gam da ram bulgu wayayyen sarki.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,
Mai Waqa : Magajin Garin Sabon Birni,
Alhaji Magaji Tangaxi Tsibiri[189]*,*

71. *GindinWaqa : Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,*
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari.

Jagora : Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari,
'Y/ Amshi : Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,

---

189 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{54}$ $^1/_1$.

: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari.

Jagora : ‘Yan tsibiri sun yi agogo don hwaxin lokaci, x²
‘Y/Amshi : Tun da ya kasa ba a shawara sai da shi,
: Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari. x²

Jagora : Magaji jirgin zinariya da tsohin gaci, x²
‘Y/Amshi : Wanga jirgi ham mucciyar azurhwa garai, x²
: Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari.

Jagora : Shi wanga jirgi hay ya hi martaba hankali,
‘Y/Amshi : Rad da za a hito had da mu muna zakkowa,
: Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari.
Jagora : Ai wanga jirgi hay ya hi martaba hankali, x²
‘Y/Amshi : Rad da za a hito had da mu muna zakkowa, x²
: Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari.

Jagora : Ai dauri an Magajin gari na shinkinkimi, x³
‘Y/Amshi : Tun da an canza yanzu duniya ta mu ta, x³
: Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari.
Jagora : Ai yara wanga Magajin gari irin namu ne, x²
‘Y/Amshi : Mu da qilli wancan mai abun rashin hankali,
: Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari. x²

Jagora : Wanga gidan Alhaji ne da shi da Alhajiya, x²
‘Y/Amshi : Alhaji Xantsita taka azama ta isa,
: Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari.

Jagora : Magaji jirgin zinariya da tsohin gaci, x²
‘Y/Amshi : Wanga jirgi ham mucciyar azurhwa garai, x²
: Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari.

Jagora : ‘Yan tsibiri sun yi agogo don hwaxin lokaci, x^2
‘Y/Amshi : Tun da ya kasa ba a shawara sai da shi,
: Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari. x^2

Jagora : Gobirawa kun sha kunun baqaz zuciya, x^2
‘Y/Amshi : Don cikin duniya babu inda ba a san ku ba, x^2
: Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari.

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Xangaran Sabon Birni,
Alhaji Ibrahim Makoxa Xangara[190]*,*
72. *Gindin Waqa : Ibrahim Xanmakoxa rai nai yay haske,*
: Na zaka in gai da Xangaran Sabon Birni.

Jagora : Maraxi an yi Xangara, x^2
‘Y/Amshi : Kuma ga shi an naxa sabon Birni,
: Ina musu roqon Ubangiji kullum-kullum,
: Ibrahim Xanmakoxa rai nai yay haske,
: Na zaka in gai da Xangaran Sabon Birni. x^2

---

190 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{377}$ $^1/_2$.

Jagora : Bajinin Shi'itu, x²
: Abin da yas shira tun can hwarko,
'Y/Amshi : Hay yau bai saba qulle-qullen banza ba,
: Ibrahim Xanmakoxa rai nai yay haske,
: Na zaka in gai da Xangaran Sabon Birni. x²

Jagora : Ashe daka sai mata, x²
'Y/Amshi : Kashin bisasshe sai kura,
: Hawan doki sai Ba'auzine sai 'yan sarki,
: Ga mu muna kallon mai kixi ana kallon kura,
: Su Alhaji Maidaji yau ana kallon kallo,
: Ibrahim Xanmakoxa rai nai yay haske,
: Na zaka in gai da Xangaran Sabon Birni. x²

Jagora : Yara mi an ma'anad da za ku yin kallon-kallon, x²
'Y/Amshi : Mu ba mu gane ba tun da ba mu zama birni,
: Ibrahim Xanmakoxa rai nai yay haske,
: Na zaka in gai da Xangaran Sabon Birni. x²

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai waqa : Alhaji Idi Falalen Karo[191]*,*

73. *Gindin Waqa : A gaishe ka na Amadu,*
: Idi falalen karo.

Jagora : 'Yan samari a yo aniya, x²
'Y/Amshi : A dai taushe hakin dawa,
: A gaishe ka na Amadu,
: Idi falalen karo. x²

Jagora : A gishe ka Idi kan Daudu, x²
'Y/Amshi : Ba ya wargi da hwashin qasa,
: A gaishe ka na Amadu,

191 An Sami Wannan Rerawa a Kundin Gusau, S. M. (1983: 475)

: Idi falalen karo. x²

Jagora : ‘Yan samari a yom aniya, x²
‘Y/Amshi : A dai taushe hakin dawa,
: A gaishe ka na Amadu,
: Idi falalen karo. x²

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003)[192]*,*

74. *Gindin Waqa : Lahiya na Muhamman,*
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara.

Jagora : Sarki na Arzika xan mage, x²
: Barka nikai da gabata kullum,
‘Y/Amshi : Lahiya na Muhamman,
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara. x²

Jagora : Na yi roqo ga Allah, x³
‘Y/Amshi : Alhaji ya yi roqo wajen Rabbani, x³

192 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{1}/_{178}$ $^{1}/_{8}$.

: Lahiya na Muhamman,
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara.

Jagora : Jangwarzo da yar roqi Allah, x^3
'Y/Amshi : Har yar roqi Annabi Mamman,
: Yac ce dum mazaje su koma mata,
: Lahiya na Muhamman,
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara. x^3

Jagora : Sarkin Arewa ka lelanta ni, x^2
'Y/Amshi : Kamam Mayaqi da Gauxe,
: Ka san duniya aka xaukag girma, x^2
: Lahiya na Muhamman,
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara.

Jagora : Duniya aka yawo, x^2
'Y/Amshi : Ka san Lahira ba a san yau ciza. x^2

Jagora : Ai da kihi da nama, x^2
'Y/Amshi : Ka san ba a ce masu xai na,
: Tun daw wurin biya aka bambantasu,
: Lahiya na Muhamman,
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara. x^2
Jagora : Kuma da jaki da doki,
'Y/Amshi : Ka san ba a ce masu xai na,
: Tun daw wurin biya aka bambantasu,
: Lahiya na Muhamman,
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara.

Jagora : Ai da jaki da doki,
'Y/Amshi : Ka san ba a ce masu xai na,
: Tun daw wurin biya aka bambantasu,
: Lahiya na Muhamman,
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara.

Jagora : Kuma da zarqi da zoro,
'Y/Amshi : Ka san ba a ce masu xai na,
: Tun daw wurin biya aka bambantasu,
: Lahiya na Muhamman,
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara.

Jagora : Gobirawa na Baciri, x3
'Y/Amshi : Ko can ba ku tsoron a kama,
: Don kau kunhi zaune da ku ba daxi,
: Lahiya na Muhamman,
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara. x3

Jagora : Na yi roqo ga Allah,
'Y/Amshi : Alhaji ya yi roqo wajen Rabbani,
: Lahiya na Muhamman,
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara.

Jagora : Jangwarzo da yar roqi Allah, x2
'Y/Amshi : Har yar roqi Annabi Mamman,
: Yac ce dum mazaje su koma mata,
: Lahiya na Muhamman,
: Sarki kak ka yarda da rainin tsara. x2

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Sarkin Gidan Rumji, Alhaji Kaso Sanda[193]*,*
75. *Gindin Waqa : Jikan goye Kaso xan Kaso,*
: Sarki xan Sanda mai duniya.

Jagora : Ai wada Allah ka yi ya gama,
'Y/Amshi : Allah ba ya yin shawara,
: Komi yat tashi yi nai ya kai.

Jagora : Du wada Allah ka yi ya gama,
'Y/Amshi : Shi Allah ba ya yin shawara,
: Komi yat tashi yi nai ya kai,
: Jikan goye Kaso xan Kaso,

193 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{1}$.

: Sarki xan Sanda mai duniya.

Jagora : Du wada Allah ka yi ya gama,
‘Y/Amshi : Shi Allah ba ya yin shawara,
: Komi yat tashi yi nai ya kai.

Jagora : Ko can haka nan duniya tay iya, x^2
‘Y/Amshi : In wasu sun kwan suna lahiya,
: Wasu ko sun tashi ba lahiya, x^2
: Jikan goye Kaso xan Kaso,
: Sarki xan Sanda mai duniya.

Jagora : Ga wasu can sun aje jikkuna, x^2
‘Y/Amshi : Wasu kau sun tashi ba ko kwabo. x^2

Jagora : Wasu sun yi dawaki suna riguna, x^2
‘Y/Amshi : Wasu kau sai xarma walki su kai, x^2
: Jikan goye Kaso xan Kaso,
: Sarki xan Sanda mai duniya.

Jagora : Mamakin Gobirawa nikai, x^2
‘Y/Amshi : Babari da yai riqon duniya,
: Matsayin sarki tamanin ya kai. x^2
Jagora : Nahwata da yai riqon duniya,
‘Y/Amshi : Matsayin sarki tamanin ya kai.
Jagora : Kuma Soba da yai riqon duniya,
‘Y/Amshi : Matsayin sarki tamanin ya kai.
Jagora : Mainasara da yai riqon duniya,
‘Y/Amshi : Matsayin sarki tamanin ya kai.
Jagora : Almu da yai riqon duniya,
‘Y/Amshi : Matsayin sarki tamanin ya kai.
Jagora : Gulbi da yai riqon duniya,
‘Y/Amshi : Matsayin sarki tamanin ya kai.
Jagora : Tumbulki da yai riqon duniya,
‘Y/Amshi : Matsayin sarki tamanin ya kai,
: Jikan goye Kaso xan Kaso,
: Sarki xan Sanda mai duniya.

Jagora : Ga mu muna tono muna rabkana, x^2
‘Y/Amshi : Sarkin kwaxayi bakwai nis sani,
: Ka rubuta had da sittin su kai, x^2
: Jikan goye Kaso xan Kaso,
: Sarki xan Sanda mai duniya.

Jagora : Allah shi ma tsari duniya, x^2
‘Y/Amshi : Kuma dai ya yi ma tsari lahira,
: Don kau na san dai Musulmi kake, x^2
: Jikan goye Kaso xan Kaso,
: Sarki xan Sanda mai duniya.

Jagora : Baban Tsitau uban Kashe, x^2
‘Y/Amshi : Xanbarno mai da qura ya kai, x^2
: Jikan goye Kaso xan Kaso,
: Sarki xan Sanda mai duniya.

Jagora : Sarki qwam ma ruwa na vwamnar hwari, x^2
‘Y/Amshi : In sun bi ga qorama sun wuce,
: Mu kau Koyaushe kwaxi mu kai, x^2
: Jikan goye Kaso xan Kaso,
: Sarki xan Sanda mai duniya.

Jagora : Mu gode ma ta Malam ta Rimin Kwari, x^2
‘Y/Amshi : Da zane tab ba mu domin Kaso. x^2

Jagora : Ga ta Malam Gobirawa hwaxa,
: ‘Yan Kurawa da sun kai hwaxa,
‘Y/Amshi : Rannan kau na yi kallon hwaxa,
: To, amma na tsaya na raba,
: In ba don ni ba da ta buga,
: Jikan goye Kaso xan Kaso,
: Sarki xan Sanda mai duniya.

Jagora : Ko can haka nan duniya tay iya, x^2
‘Y/Amshi : In wasu sun kwan suna lahiya,

: Wasu ko sun tashi ba lahiya, x²
: Jikan goye Kaso xan Kaso,
: Sarki xan Sanda mai duniya.

Jagora : Du wada Allah ka yi ya gama,
'Y/Amshi : Shi Allah ba ya yin shawara,
: Komi yat tashi yi nai ya kai,
: Jikan goye Kaso xan Kaso,
: Sarki xan Sanda mai duniya.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Muhammadu Xanqoqari[194]*,*

76. *Gindin Waqa : Sai mu taru mu yi roqon Allah,*
: Inda Alhaji Bakwai N.P.N.

Jagora : Ai sai mu yi roqon Allah, x²
: Inda Alhaji Bakwai N.P.N,
'Y/Amshi : Sai mu taru mu yi roqon Allah,
: Inda Alhaji Bakwai N.P.N. x²

Jagora : In ka ji an yi magana ta zaune, x²
'Y/Amshi : Yanzu ba wata magana sai Legas. x²
Jagora : To, kowa shi hanqure, Babari, x³
'Y/Amshi : Da Gwamna sun yi magana ta zauna,
: Sai mu taru mu yi roqon Allah,
: Inda Alhaji Bakwai N.P.N. x³

Jagora : Uban xan Jari kutunvun vauna, x³

194 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^{0}/_{75}$ $^{1}/_{10.}$

‘Y/Amshi : Babu mai iya tare ma hanya,
: Sai mu taru mu yi roqon Allah,
: Inda Alhaji Bakwai N.P.N. x^3

Jagora : Alheri shi kai mu Sabon Birni, x^3
‘Y/Amshi : Tun da can aka shirawad duniya,
: Sai mu taru mu yi roqon Allah,
: Inda Alhaji Bakwai N.P.N. x^3

Jagora : Sabon Birni mu taru ga hwatana,
‘Y/Amshi : Tun da masu hitina sun kasa,
: Sai mu taru mu yi roqon Allah,
: Inda Alhaji Bakwai N.P.N.

Jagora : Gobir babu sauran shairi,
‘Y/Amshi : Tun da masu hitina sun qare
: Sai mu taru mu yi roqon Allah,
: Inda Alhaji Bakwai N.P.N.

Makaxi : Alhaji Sa’idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Alhaji Sarkin Gobir na Sabon,
Alhaji Abdulhamid (2003-)[195]

77. *Gindin Waqa : Ya kwan cikin shiri ya tashi tsaye,*
: Malam Balarabe Bunu xan Niqatau.

Jagora : Wallahi duniya ta ba ni tsoro, x^2
‘Y/Amshi : Wata rana waxansu sui kuka da kansu, x^2
: Ya kwan cikin shiri ya tashi tsaye,
: Malam Balarabe Bunu xan Niqatau.

Jagora : Dogo xan Durumbu xan sarkin Musulmi, x^2
‘Y/Amshi : Wani ya tara duniya ta tashi kai nai, x^2
: Ya kwan cikin shiri ya tashi tsaye,
: Malam Balarabe Bunu xan Niqatau.

---

195 Makaxa Maidaji Sabon Birni ya rera wannan waqa ne tun zamanin Alhaji Abdulhamid yana xan sarki. An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al’adun Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^0/_{75}$ $^1/_{12}$ - AL $^1/_{375}$ $^1/_6$.

Jagora : In ka kama salsalash Shawai da Jari, x^2
‘Y/Amshi : Tarihin da nis sani shi zan hwaxa ma, x^2
: Ya kwan cikin shiri ya tashi tsaye,
: Malam Balarabe Bunu xan Niqatau.

Jagora : To, tun daq qasar Gubur han nan qasag ga, x^2
‘Y/Amshi : To, duk xan na Baciri ya san mu tare, x^2
: Ya kwan cikin shiri ya tashi tsaye,
: Malam Balarabe Bunu xan Niqatau.

Jagora : Mainasara da yai riqo ya gade sosai, x^2
‘Y/Amshi : Duk harkar da za shi yi sai ya hwaxa min. x^2
Jagora : Kuma da yai riqe Xantsara qasag ga, x^2
‘Y/Amshi : Duk harkar da za shi yi sai ya hwaxa mai. x^2
Jagora : Salihu ya riqe ni ga ni kwarai da gaske, x^2
‘Y/Amshi : Duk harkar da za shi yi sai ya hwaxa min. x^2
Jagora : Ummaru ya riqe ni ko ni babu xumi, x^2
‘Y/Amshi : Duk harkar da za shi yi sai ya hwaxa min. x^2
Jagora : Alhaji ya riqe ni ko ni babu xumi,
‘Y/Amshi : Duk harkar da za shi yi sai ya hwaxa min.
Jagora : Alhaji ya riqe ni ko ni babu xumi,
‘Y/Amshi : Duk harkar da za shi yi sai ya hwaxa min,
: Ya kwan cikin shiri ya tashi tsaye,
: Malam Balarabe Bunu xan Niqatau.

Jagora : Bana in kun aje ni ba ni zama qasag ga, x^2
‘Y/Amshi : Sai in sake gahwara in hau bisashe, x^2
: Ya kwan cikin shiri ya tashi tsaye,
: Malam Balarabe Bunu xan Niqatau.

Jagora : Dogo xan Durumbu xan sarkin Musulmi, x^2
‘Y/Amshi : Wani ya tara duniya ta tashi kai nai, x^2
: Ya kwan cikin shiri ya tashi tsaye,
: Malam Balarabe Bunu xan Niqatau.

Jagora : Ni dai wallahi duniya ta ba ni tsoro, x^2
‘Y/Amshi : Wata rana waxansu sui kuka da kansu, x^2
: Ya kwan cikin shiri ya tashi tsaye,

: Malam Balarabe Bunu xan Niqatau.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Mai Waqa : Xan Sarkin Gangara[196]*,*
Alhaji Isa Baraz Zaki,

78. *Gindin Waqa : Yai halin mazan jiya Isa maqi garaje,*
: Tun da yai kira Alhaji bai kahwat tsayawa.

Jagora : Can za ni Gangara, x^2
'Y/Amshi : Tun da garin Balarabe na,
: A gurin Balarabe,
: Ka san ai wurin zuwa na, x^2
: Yai halin mazan jiya Isa maqi garaje,
: Tun da yai kira Alhaji bai kahwat tsayawa.

Jagora : Don Allah Gobirawa, x^2
'Y/Amshi : Kowa ya kintsa kai nai,
: Don ku sani,
: Akwai wani zarto yana tahowa, x^2
: Yai halin mazan jiya Isa maqi garaje,
: Tun da yai kira Alhaji bai kahwat tsayawa.

196 An sami wannan rerawa a Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U), Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. 1985: Faifai mai lamba AL $^1/_{378}$ $^1/_9$.

Jagora : Duk xan Bagobiri, x²
'Y/Amshi : In dai xan na Baciri na,
: Da ya bar batun hwaxa,
: Gwara ya kwana bai da komi, x²
: Yai halin mazan jiya Isa maqi garaje,
: Tun da yai kira Alhaji bai kahwat tsayawa.

Jagora : Alhaji don ganin gero, x²
'Y/Amshi : Ba ni tsinka tambo,
: In don batun hwaxa,
: Ban ga batun ture-turenga, x²
: Yai halin mazan jiya Isa maqi garaje,
: Tun da yai kira Alhaji bai kahwat tsayawa.

Jagora : In don mutum yana iko, x²
'Y/Amshi : Ba ya ba mu kyauta,
: Ka kama shawara,
: Gwara mu kwan gidan mutane. x²

Jagora : Na san gidan Bahaushe,
'Y/Amshi : Na san gidan mutane,
: Gari-gari muke,
: Babu garin da ban sani ba.
Jagora : Can za ni gangara, x²
'Y/Amshi : Tun da garin Balarabe na,
: A gurin Balarabe,
: Ka san ai wurin zuwa na, x²
: Yai halin mazan jiya Isa maqi garaje,
: Tun da yai kira Alhaji bai kahwat tsayawa.

Jagora : Isah da kai da Isah, x²
'Y/Amshi : Kun zam kamat tawaye,
: Ya yo kamah Hassan,
: Shi ko ya yo kama da yaro, x²
: Yai halin mazan jiya Isa maqi garaje,
: Tun da yai kira Alhaji bai kahwat tsayawa.

Jagora : Ni dai ina biyax xan sarki, x³

‘Y/Amshi : Shi ko yana gudu na
: Ku ce ya bar gudu,
: Ba hakan niy yi xammara ba. x^3

Jagora : Mata tai tana hwaxi, x^2
‘Y/Amshi : Wataqil wane mai kixin ga,
: Xa nai shi na hwaxin,
: Baba shige cikin itace. x^2

Jagora : Haba wane don gani na, x^2
‘Y/Amshi : Bari bar shiga itace akwai kububuwa,
: Mai zane tana kashe ka, x^2
: Yai halin mazan jiya Isa maqi garaje,
: Tun da yai kira Alhaji bai kahwat tsayawa.

RATAYE NA BIYU

FASALIN GANAWA DA AKA YI DA MAKAXA SA'IDU MAIDAJI SABON BIRNI

Ganawa Tsakanin Makaxa Maidaji Sabon Birni

Tare Da Malam B. S. Y. Alhassan,

Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya, Jihar Kaduna.

Gabatarwa

A wajen wannan hira Malam Bello S. Y. Alhassan ya fara ne da bayyana cewa:

> "A yau sha xaya ga watan biyu shekarar alif xari tara da tamanin da uku (11/2/1983) ga mu nan Rambaxawa ta qaramar hukumar Sabon Birni. Wato abokin aikina Anthony King da ni Bello Alhassan muna hira da shararren mawaqin nan Alhaji Maidaji Sabon Birni".

Daga nan kuma sai ya ci gaba da gabatar da tambayoyi domin jin amsarsu daga bakin makaxa Maidaji Sabon Birni kamar haka:

B. S. Y. Alhassan : Alhaji barka da wuni?

Makaxa Maidaji : Barka dai Mallam.

B. S. Y. Alhassan **:** Muna Lahiya?

Makaxa Maidaji : Lafiya lau Mallam.

B. S. Y. Alhassan : To madalla!

Makaxa Maidaji : Lahiya.

B. S. Y. Alhassan : To da farko Alhaji muna son mu san cikakken sunanka?

Makaxa Maidaji : Sunana Sa'idu.

B. S. Y. Alhassan: Sa'idu?

Makaxa Maidaji : Eh!

B. S. Y. Alhassan : Wato Sa'idu Maidaji ke nan?

Makaxa Maidaji : Eh!

B. S. Y. Alhassan : Sa'idu Maidaji Sabon Birni. To Madalla, wato wannan sana'a ta ka, ka gaje ta ne ko kuma ka xauka daga sama saboda ganin Allah dai ya yi mala hikima?

Makaxa Maidaji : Na gade ta ne.

B. S. Y. Alhassan : To ka gade ta?

Makaxa Maidaji : Eh!

B. S. Y. Alhassan : Daga wa ke nan?

Makaxa Maidaji : Daga Makaxa Xantsara.

B. S. Y. Alhassan : To wace irin dangantaka ke tsakaninka da wannan wanda ka gaji waqa a wurinsa?

Makaxa Maidaji : Shi ya haihi tsoho na.

B. S. Y. Alhassan : Wato shi ne kakanka ke nan?

Makaxa Maidaji : Eh!

B. S. Y. Alhassan : To ta hannun wa wannan sana'a ta biyo har ta hwaxo kanka?

Makaxa Maidaji : Daga hannun Roqo.

B. S. Y. Alhassan : Wane ne Roqo?

Makaxa Maidaji : Shi ne tsoho na.

B. S. Y. Alhassan : Wato daga Kakanka sai Roqo?

Makaxa Maidaji : Eh!

Dr. B. Alhassan: To daga Roqo sai kuma hannun wa?

Makaxa Maidaji : Sai Nadada Malam Musa.

B. S. Y. Alhassan : To! Shi ainihin Kakanka wanda ka gadi wannan waqa a hannunsa, shi makaxin wa ne ne?

Makaxa Maidaji : Makaxin Sarkin Gobir Jadi.

B. S. Y. Alhassan : Makaxin Sarkin Gobir Jadi?

Makaxa Maidaji : Eh!

B. S. Y. Alhassan : Mahaifinka makaxin wane ne?

Makaxa Maidaji : To shi mahaihi na bai yi kixin sarakuna ba sai na manoma.

B. S. Y. Alhassan : Kixn manoma yay yi?

Makaxa Maidaji : Eh!

B. S. Y. Alhassan : To, Allah sarki. To, shi magajinka da ka amsa daga hannunsa fa kuma?

Makaxa Maidaji : Shi ko Nadada ya yi wa Sarkin Gobir Salihu kixi.

B. S. Y. Alhassan : To madalla, daga gare shi sai gare ka?

Makaxa Maidaji : Eh! Sai gare ni.

B. S. Y. Alhassan : To kai kuma makaxin wane ne?

Makaxa Maidaji : To ni na fara tun daga Sarkin Gobir Ummaru xan Sarki Salihu. Tak kai ga Sarkin Gobir Ibrahim qanin Sarki Salihu. Hat tak kai ga Sarkin Gobir Muhammad qanin Sarki Salihu.

B. S. Y. Alhassan : Wato yanzu kamar shekaru nawa ke nan kana wannan sana'a ta ka?

Makaxa Maidaji : Ina dibi na shekara kamar talatin har da 'yan kai.

B. S. Y. Alhassan : To, Allah sarki. Da wane irin kixa kas soma, ko kixin sarauta ko kixin maza. Wane irin kixa ne ka soma da shi?

Makaxa Maidaji : To tun farko na soma da kixin noma.

B. S. Y. Alhassan : Kixin noma?

Makaxa Maidaji : Eh!

B. S. Y. Alhassan : To yanzu kana iya tuna waqar da ka fara rerawa ta noma. Kuma kana iya jingina mini ita?

Makaxa Maidaji : Eh! Ina iya wa. Ga kaxan daga cikin waqar:

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,

Mai Waqa : Waqar Noma ta Arzika[197]*,*

Gindin Waqa : Sarki yai abin daka ya huta,

: Zaki xan Abubakar xan Buda.

Jagora : Baba mijin Shibo mijin Maryama,

'Y/Amshi : Giwa maganin itacen daji,

: Sarki yai abin daka ya huta,

: Zaki xan Abubakar xan Buda.

B. S. Y. Alhassan : To madalla Alhaji, mun gode da wannan waqa kwarai da gaske, na ji kana cewa sarki?

Makaxa Maidaji : Au, Sarkin Noma ba!

B. S. Y. Alhassan : Na ji waqa raqwai-raqwai na yi zaton sarkin gari ne da waqar?

Makaxa Maidaji : Sarkin Noma ne!

B. S. Y. Alhassan : To, wannan ita ce waqar farko da ka fara yi ta noma?

Makaxa Maidaji : Eh!

B. S. Y. Alhassan : Daga nan kuma bayan waqoqin noma sai ka faxa waxanne irin waqoqi?

Makaxa Maidaji : Sai nik kama Sarkin Gobir Ummaru.

B. S. Y. Alhassan : Sarkin Gobir Ummaru?

---

197 Domin samun wannan waqa a kammalenta sai a duba Rataye na Xaya a wannan aikin a shafi na 314-315.

Makaxa Maidaji : Eh! Tun shina xan sarki ina yi mai kixi. Daga nan har Allah yab ba shi sarauta. Shi ke nan sai yaq qara jawo ni daxa. Sai nish shiga garai.

B. S. Y. Alhassan : Ko za ka iya jingina mani waqar farko da ka yi mishi?

Makaxa Maidaji : Eh! Ga waqar kamar haka:

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir Ummaru xan Salihu,
Gindin Waqa : Binu xan baraz zaki Xanbawa[198]*,*
: Jikan Kilo gwamron giwa.

Daga nan kuma sai kuma ya rera wannan waqar:

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,
Ubangida : Sarkin Gobir Ummaru xan Salihu,
Gindin Waqa : Na Ali xan Bajini[199]*,*
: Jikan Shekara ka gama lahiya.

B. S. Y. Alhassan : Madalla! Kai ai wannan waqa kam ba dama?

---

198 Domin samun wannan waqa a kammalenta sai a duba Rataye na Xaya a wannan aikin a shafi na 316-317.

199 Domin samun wannan waqa a kammalenta sai a duba Rataye na Xaya na wannan aikin a shafi na 329-331.

Makaxa Maidaji : Eh! Ba laihi!

B. S. Y. Alhassan : Ai na ga ko Malam Anthony yana kaxa kai. Wato wannan duk waqoqin da ka yi wa Sarkin Gobir Ummaru ne, Bayan Sarakunan Gobir, akwai Sarakuna kuma da ka yi wa waqa?

Makaxa Maidaji : Eh! Akwai Sarkin Gobir Ibrahim, sai Sarki Muhammad wanga Sarkin Gobir na yanzu!

B. S. Y. Alhassan : Abin da nake so in sani shi ne, waxansu mawaqa sukan yi gadon waqoqi daga ko mahaifinsu ko kuma wani magabacinsu. To ko kai ka yi irin wannan abu ko kuwa waqoqinqa tsantsa kake yi. Ko kuwa har da waxanda ka yi gado?

Makaxa Maidaji : Eh! Tun daga waqoqin Nadada nik kamo har nik kai ga waxanga.

B. S. Y. Alhassan : Yanzu ka san wasu daga cikin waqoqin Nadada?

Makaxa Maidaji : Eh! Na sani tun da da ni anka yi su.

B. S. Y. Alhassan : To! da kai anka yi su?

Makaxa Maidaji : Eh! Da ni anka yi su.

B. S. Y. Alhassan : Sannan kana amshi ke nan?

Makaxa Maidaji : Eh! Sannan ina karvi.

B. S. Y. Alhassan : Amma ba kana qullawa ba?

Makaxa Maidaji : Eh! Sannan ina yi wa xan Sarkin Gobir Kixi. Shi ko shina yi wa Sarkin Gobir Salihu kixi.

B. S. Y. Alhassan : To in za shi waqa sai ku tahi ka aje naka?

Makaxa Maidaji : Eh!

B. S. Y. Alhassan : Wace waqa kai kahi so a ranka cikin waqoqin ka duka?

Makaxa Maidaji : To! Abin dama gare su.

B. S. Y. Alhassan : Ai sai ka lalubo mana wadda zuciyarka tahi zuwa kusa gare ta, ka waqa mana ita mu ji ko?

Makaxa Maidaji : To!

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa

Ubangida : Sarkin Gobir na Sabon Birni,

Muhammadu Bawa (1975 - 2003)

Gindin Waqa : Kai ab bahagon gulbi[200]*,*

: Uban Shantali xan Mamman,

: Xan'inna Kilo sarki,

: Uban Bunu da Baraz Zaki.

B. S. Y. Alhassan : Lalle wannan waqa kam ba kai kaxai ba kam, ni ma na kawo ta gab da zuciya ta kwarai da gaske ai na ga Makaxa shi ma da kansa rausayawa ba kaxam ba kam. To amma wani abu dake xaure wa musamman manazarta waqoqi kai shi ne, sanin

---

200 Domin samun wannan waqa a kammalenta sai a duba Rataye na Xaya na wannan aikin a shafi na 332-352.

yadda kuke shirya waqoqinku. Wato xaya daga cikin misalan shi ne za ka ji waxansu Makaxa sun yi iqirarin nan take suke shirya waqa. Wasu kuma su ce a'a, su kam sai sun yi ma waqarsu wani abi da suke kira fasali?

Makaxa Maidaji : To! Kamar wannan abi iri-iri ne ga Makaxa. In ka ji Makaxi na cewa yana qira waqa iri goma xai rana, to, amman suna yi sai su kamo waqar wani su haxa da ta wani. To shi ke sa a shiga irin wannan sabgar.

B. S. Y. Alhassan : Wato waqar wani ta sai a birkitata?

Makaxa Maidaji : Eh! Sai a yi wa wani can, sai a taho, sai a raba biyu, a yi wa wani. Ai fasaha iri-iri ta.

B. S. Y. Alhassan : Yanzu kama in za ka shirya waqa guda, kuna kwana nawa kuna qullata kan ta haxu?

Makaxa Maidaji : To dai in abin yav vullomana nan take muna qira wata waqa. Bayan mun qira munka tahi gida sai mu yi ta mata iyali, tana qaruwa, tana yin gaba, har dai in wanda aka yi wa ita shina da hannu, to, tahi ma'ana.

B. S. Y. Alhassan : To mi aka nuhi da hannu. Don na ga ban yi tsammanin za ka yi wa marar hannu waqa ba, tun da na ga daga sarakuna sai manyan manoma kake yi wa waqa. Na ko san wanda duk as Sarkin Noma hannuwa nai biyu na na kama fartanya?

Makaxa Maidaji : Abin da ah hannu, wanda ad da alheri. Hakan ga idan ka qira wa mutum waqa, to, ko baka zo da kixin ba kag ganshi sai ya sami wani abu ya ba ka, shi ne ah hannu.

B. S. Y. Alhassan : Misali, idan za ka qulla waqa haka, idan ka samu waqa a zuciyakka, to, kixin waqar duk kai kake cewa ga yadda kake buqata?

Makaxa Maidaji : Eh! Sai a hwaxa ma yara ga wada aka bugawa.

B. S. Y. Alhassan : To sai an hwara waqar ke nan?

Makaxa Maidaji : A'ah! Sai an hwara bugawa. Wato sai na hwaxa musu wada aka kixin sannan a yi waqar. To in munka yi ta tana sabuwarta in anka tashi sai a yi ta cigaba da ita.

B. S. Y. Alhassan : Cikin waqoqinka da munka saurara na ga da alamar har yanzu ba ka daina yi wa manoma kixi ba, ko ka bari?

Makaxa Maidaji : Wani bi ina xan tavawa.

B. S. Y. Alhassan : Misali a cikin waxannan waqoqin da ka yi wa manoma kowacce da taushi kake bugawa kamar yadda kake yi wa sarakuna?

Makaxa Maidaji : To! Wani azanci muke yi, ita wannan zagag da muka sa wa, to, in munka tashi yi wa manoma kixi, sai mu cire ta a maishe ta xai waje. Su manoma ba a sa musu zaga saboda ana buga taushin kwarai, wanda wani salo ne na kixi. Ita zaga tana yin amo ne na sarakuna.

B. S. Y. Alhassan : To bayan an cire ta ha yanzu abin kixin yana nan matsayin taushi?

Makaxa Maidaji : Eh! Shina nan.

B. S. Y. Alhassan : Kuma su sarakuna sun san da haka, ba su yi hushi ba?

Makaxa Maidaji : Eh! Sun sani.

B. S. Y. Alhassan : Yanzu ina son in xan ji waqar manoma wadda ka yi ta qarshe, wadda daga gare ta baka sake yin wata waqar noma ba?

Makaxa Maidaji : To! Ta daga baya ke nan. Uhum.

Makaxi : Sa'idu Maidaji Rambaxawa, Sabon Birni

Waqar : Noma (Rerawa ta Biyu)

Gindin Waqa : Na yi hamdala nai shukura da godewa[201]*,*

: Tun da na sani noma yau farilla ne.

B. S. Y. Alhassan : To madalla! Wato wani abin mamaki shi ne cikin waxannan waqoqi ban ji ta yar wa ba. Wannan ya sa in yi tambaya. Shin idan za ka qulla waqa Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni, sai ka tsaya ka xauko wani kari idan ka ji bai dace ba ka yi watsi da shi har sai ka ji tatacce, kuma sahihi wanda ka kammaluwa. Ko kuwa kai tsaye in ka xauko kari sai ya miqe?

Makaxa Maidaji : To dai ina tsayawa in shirya. Wani sa'i sai Allah ya ba ni hanya in hurce.

B. S. Y. Alhassan : Bayan haka na ji mutane da dama ka yi musu waqa, ga waqoqi ka yi ma sarakuna, ga waqoqi ka yi wa manoma, sannan ka yi wa wani wanda na ji kana cewa "Koma gyara kaya gwani ka hi koyo, za ni in ishe Mamman uban Jari". Abin da nake so in sani shi ne, a lokacin da zaka yi ma mutum xin

[201] Domin samun wannan waqa a kammalenta sai a duba Rataye na Xaya na wannan aikin a shafi na 31-33.

waqa, mutum shi zai zo ya ce ka yi min waqa, ko kuwa kai ne ganin alherin da yake yi maka kake ganin ya cancanta ka yi masa waqa?

Makaxa Maidaji : Eh! Mutane na yi min qoqari, saboda in nig game da mutum ga hanya, sai shi yi kirana shi ba ni alheri. Gobe in mun sake gamewa ya qara yi min alheri. Sai in ce na san abin da wane ka bixa, shi ne ni ko sai in zo in yi godiya ta gadonmu. In nig ga mutum na yi min alherin nan sai in aza irin abin nan namu na gado shika bixa, ni ko sai in zo in in godiya da tau sana'a. Tun da kwanakkin ga wani ya kira ni can Gusau, ban san shi ba. Kawai sai ya aiko takarda in tahi yana kirana amma kar in zo da yara, in tahi ni xai. Shi ke nan sai nic ciri wannan babban wa na munka tahi, aiko ya zumbugo mana alheri. Da yaz zumbugo mana alheri shi ke nan da munka zaka gida, sai nic ce zan yi tau sana'a in aika da tau godiya. Sai nit tarda yara nanniya, sai munka samu hwaihwai munka sa, ni ko sai niyyi tawa godiya nik aika mai da ita. Ban je da kai na ba amma sai nik aika mai da ita.

B. S. Y. Alhassan : Wato idan mutum ya yi maka kyauta mai yawa ko sau xaya ne sai ka yi mishi godiya. Ko kuwa har da alheri kaxan?

Makaxa Maidaji : To! Shi ka san alheri ba shi da kaxan, in dai mutum yana son ka, wada duy yab ba ka, to, mu kuwa irin tamu godiya an nan.

B. S. Y. Alhassan : Wannan waqa wadda kay yi wa mutumin Gusau kana ji da can cikin xauke-xauken da mu kai mun xauke ta?

Makaxa Maidaji : A'ah!

B. S. Y. Alhassan : To sai a jingina mana ita mu ji ko?

Makaxa Maidaji : To!

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni

Mai Waqa : Alhaji D. P.O na Gusau

Gindin Waqa : Na shira kaya za ni garai[202]*,*

: Na Alhaji D. P. O na Gusau.

B. S. Y. Alhassan : To Madalla! Wannan mutum kamar yada kacce zumbugo muku alheri yay yi ko?

Makaxa Maidaji : Eh! kwarai da gaske.

B. S. Y. Alhassan : Lalle waqa dai kam ta yi daidai da aherin da yay yi. To na ga duk abin da yay yi wa mutum yawa wani lokaci yana xibar xan kaxan yayi sadaka?

Makaxa Maidaji : Eh!

B. S. Y. Alhassan : To ko ka tava yi ma wani waqa sadaka ka ba shi ita da kyauta. Don abin da ya sani na ga bani da halin zumbuxo irin wannan kyauta kuma ga ni ina son waqa. Ko ina xan samu a qira man ita sadaka. Wani abi da nake so in tambaya shi ne, na ji a cikin waqoqinka waxanda ka ambata can baya na ji ka ambaci waxansu mawaqa. Kuma na san mawaqa suna suka ko kuma yi ma yi ma ‘yan’uwansu mawaqa zambo. Amma ban ji ka yi ba sai maganar ba’a kakai, ko ba gaskiya ba. Kuma sai in ji ka ce wane ya shaida maka. Wannan kuma

---

202 Domin samun wannan waqa a kammalenta sai a duba Rataye na Xaya na wannan aikin a shafi na 357-359.

alama ce ta ka xauka shi xan'uwanka ne makaxi. To ko mene ne ke kawo irin hassadar nan tsakanin makaxa da makaxa a ganinka?

Makaxa Maidaji : Ai ba abu mai yawa ka kawo hassada ba sakanin makaxa. Yanzu kamar ga mu mu zo kixi ga wani sarki, to, sai mun zo kixi ga wani sarki, to, sai shi wannan makaxin na shi, shi sa wata mugunyar zucciya. Kamar bai amince da zuwanmu ba, shi dibi wani abu za a bamu wanda ba a bashi ba. To ai shi ka sa hassada. To, mu ko, tun azal ga wanmu, wadda munka ga ana yi har gare mu, in munka zo ga wuri munka ga makaxin ya hi mu son shi yi kixi, to, mu ba mu yi. Sai dai mu yi zamanmu, sai dai in ya qare mu tahi abin da Allah yac cishe mu a bamu.

B. S. Y. Alhassan : Ai wannan dattaku ne kwarai. To, bayan kai, don saboda sai mu ce bayan kai, yanzu akwai waxansu mawaqa nan qasar Sabon Birni kuwa?

Makaxa Maidaji : Eh akwai su.

B. S. Y. Alhassan : Su wa da wane ne kake ji ka yaba da su a wajen waqa?

Makaxa Maidaji : To dai dukkansu makaxan noma ne.

B. S. Y. Alhassan : Kamar su wane ne da wane ne ke nan?

Makaxa Maidaji : To! Yanzu akwai waxansu makaxa nan Kurawa, to, amma daxa dai kixin ma har sun kusa bari nai.

B. S. Y. Alhassan : Subhana! Dalili?

Makaxa Maidaji : To! Abin da yas sa idan mutum na abu yag ga bai karvai ba, ba ya kama shi da daraja.

B. S. Y. Alhassan : To bayan makaxan noma, akwai wani makaxin sarauta nan bayan kai?

Makaxa Maidaji : To! Nan qasar Gobir bayan ni dai ban ji wani ba.

B. S. Y. Alhassan : Kuma wannan sana'a ka ce ka yi shekara nawa kana yin ta?

Makaxa Maidaji : Na shekara talatin har da 'yan kai.

B. S. Y. Alhassan : Na ji in kana waqa kana cewa 'ya'yana. Duka masu yi maka amshi xiyanka ne?

Makaxa Maidaji : Eh! Duka xiyana ne sai wannan babban wanmu ne, sai wannan tsohonmu dukkansu suna amshi. Shi wannan tsohon namu ko da nih hwara kixi tare da shi nih hwara. Waxanda nihwara da su kuma mutum biyu ko babu su. Biyu daga qannena sun kama makaranta.

B. S. Y. Alhassan : Yanzu wannan sana'a ko cikin masu yi maka amshi yanzu akwai wani wanda yake sha'awar ya karva gare ka da ganinka lokacin da kake ganin ya kamata ka huta. Kuma ya sunan shi?

Makaxa Maidaji : Eh! Akwai domin hi kan shi ya hwara na shi waqoqi. Sunan shi Hana.

B. S. Y. Alhassan : Cikin waqoqin da kaka shiryawa, ko kana da irin waqar nan da ake ce ma Bakandamiya?

Makaxa Maidaji : To! akwai ta domin ba a rasawa.

B. S. Y. Alhassan : To sai a jingina mana Bakandamiya mu ji ko?

Makaxa Maidaji : To!

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa,

Ubangida : Sarkin Gobir Umaru,

Gindin Waqa : Gagari gaba na Salihu[203]*,*

: Mai nasara xan Durumbu,

: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

B. S. Y. Alhassan : To ni wannan waqa na tava jin ta, kuma gaskiyar Allah tana cikin waqoqinka waxanda ni ba jinin sarauta nike ba, amma sai in ji tana girgiza ni. Wato, shi ne nake son in san dalilin da yas sa kai kan ka ka kira ta Bakandamiya?

Makaxa Maidaji : To! Abin dama gare su, saboda akwai wasu manya-manya.

B. S. Y. Alhassan : Amma ita wagga mi da kak kirata Bakandamiya ko kuma kaj ji kamar ita ce Bakandamiyar. Wato saboda ta hi saura tsawo ne, saboda ta hi su daxi ne, saboda tahi saura qaqarfar magana?

Makaxa Maidaji : To! Abin da yas sa, su can Gobirawa in muna yin ta, duka ciccika su kai, sui ta zanzana, zuciyarsu ta kaxe. Maza sun so hwaxa ke nan.

B. S. Y. Alhassan : Kuma akwai wani abu da ban gane ba, "Magaji gidan Kada", ina ne gidan kada?

Makaxa Maidaji : Shi Kada kakan sarkin Gobir ne. Wato Sarkin Gobir Jari Kada, shi ne kakan sarakunan Gobir.

B. S. Y. Alhassan : Sannan kuma, lokacin da ake waqa na ji kana xaga muryarka kwarai, kamar a cikin waqar Sarkin Zazzau akwai inda yara masu yi maka waqa suna amshi sannu-sannu, sai na ji kana xaga muryarka

---

203 Domin samun wannan waqa a kammalenta sai a duba Rataye na Xaya na wannan aikin a shafi na 360-367.

sama kana cewa “Sarkin Zazzau uban Zagi ba mamaki”. Saboda haka kuma da irin wannan wanda kayyi yanzu na “Ci hwansa xan Kilo na Salihu Dunga birnin Kada”. Mi aka ce ma waxannan cikin waqa?

Makaxa Maidaji : Ita ake ce ma hawazzuwa sama. Kana ji idan makaxa suna yi ma sarki kixi suna kirari ciki, kuma ba Mabo ba, to, hawazzuwa sama ce. A hau da waqa sama an nan.

B. S. Y. Alhassan : To, wani abu kuma shi ne har wa yau, na ji wannan waqa akwai zambo cikinta?

Makaxa Maidaji : A’ah! Ai mu ba mu zambo mallam.

B. S. Y. Alhassan : A’ah! Makaxa “Mai rowa ko da yaushe ga gane shi dalauje cikin zane”. Kuma ka hwaxi tscibilbila, na san duk ba tsuntsu kake ba, dole da wani mutum kake?

Makaxa Maidaji : Eh! Wannan habaici ne ba cikin zambo shike ba.

B. S. Y. Alhassan : Ah! Wato akwai bambanci tsakanin habaici da zambo. To mi ah bambancin habaici da zambo?

Makaxa Maidaji : Eh! Akwai bambanci. To, abin da ah habaici, shi habaici in kay yi shi, to, wanda kaw wa shi bai ganewa. Shi ko zambo wanda kaw wa sai shi gane. Wanga shi ah bambancin habaici da zambo.

B. S. Y. Alhassan : Amma ai habaici kai ka san wanda kay yi ma?

Makaxa Maidaji : Eh! Amma shi bai sani ba.

B. S. Y. Alhassan : Zambo ka san wanda kay yi ma, shi ko ya sani?

Makaxa Maidaji : Eh! Shi ko ya san da shi ake.

B. S. Y. Alhassan : Lalle wannan kyakkyawan bambanci ne kwarai da gaske. To, rowa ita ah abinda ke sa ku yi wa mutum habaici xin?

Makaxa Maidaji : Eh! Ita rowa in ana yi mana ita shi ka sa habaici, domin ita ke sa rai ya kaxa.

B. S. Y. Alhassan : Lalle rowa kam ba ta da daxi, ai wannan kowa ya sani.

Makaxa Maidaji : Eh! Bata da kyawo. Yanzu kamar Hakimmai su jera nan wurin, to, muna nan muna namu sana'a, wancan shi ba mu, wan can shi ba mu. Sai mu ga wani ya daqile. Kuma gobe in mun ka koma, wancan shi ba mu, wancan shi ba mu. Amma sai mu ga wanga ya kwanta. To, shi ka sa mu jehwa habaici. To, bai ganewa, mu ko, mun san ko da wa muke.

B. S. Y. Alhassan : To, wane irin laihi mutum zai yi muku ku yi mishi zambo ba habaici kawai ba?

Makaxa Maidaji : Shi laihin zambo yawa garai. Mutum dai shi tsare ka shi na ci ma mutunci ba gaira ba sabad. Eh! Kai ba ka ji baka gani ba shi tsare ka, shinai ci maka mutunci, to, sai rai shi kaxa. To wannan shina sa zambo. To, akwai wani kuma in kana son matakka wani ya aure ta, in ka kasa dangana sai ka yi mai zambo.

B. S. Y. Alhassan : Ah! Ko ban iya waqa ba sai na yi mai ita, don wannan kam ina gangama zambo. To, Gaskiya ne. To, na ji wata waqa inda kake cewa "Ga wani mai gyara can da xan vace-vace, ko da yac cira gyaran ba don ya iya ba". Wato wannan mai gyaran akwai shi ko?

Makaxa Maidaji : Eh! Akwai shi kuma shina vace-vacen.

B. S. Y. Alhassan : To, akwai wata waqa ta Sarkin Zazzau "Kak ka yadda da raini uban baraya, Shehu Alhaji Allah shi taimaka ma". Na mance, akwai inda kake cewa kamar haka domin na manta haqiqanin abin da kake cewa "Ko ga shi mun zaka Zazzau mu gaida sarki, ban ga su Binta ba kuma banga Mariya ba. Banga Habiba kuma banga Mariya ba. Ku su Binta ba ku da halin ku daqile ni". To mi ad daqilewa?

Makaxa Maidaji : Wato mu zo mu yi ta kixi, su ko ba su hito sun ka ba da komi ba. Sun daqile ke nan, tun da ba su aiko da komi ba.

B. S. Y. Alhassan : Bayan wannan waqa da kayyi ma Sarkin Zazzau ta 'Kak ka yarda da raini uban baraya', akwai wata waqa wadda kas sake yi mashi gada baya?

Makaxa Maidaji : Eh! Na yi wata, aiko ko da Rediyo ban sa ta ba.

B. S. Y. Alhassan : Ah! Ba ka sata ba ga Rediyo, to, a hwara ba mu ita, kan a ba kowa.

Makaxa Maidaji : To!

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,

Mai Waqa : Sarkin Zazzau,

Alhaji Shehu Idris (1975-),

Gindin Waqa : Uban Na Allah uban madauci[204]*,*

: Shehu sannu da yau da gobe.

---

204 Domin samun wannan waqa a kammalenta sai a duba Rataye na Xaya na wannan aikin a shafi na 382-393.

Daga bisani kuma ya rera wannan waqar ta:

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,

Mai Waqa : Sarkin Zazzau,

Alhaji Shehu Idris (1975-),

Gindin Waqa : Kak ka yarda da raini uban Baraya[205]*,*

: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

B. S. Y. Alhassan : Ai wato, gaskiyar Allah ka san ba yau muka hwara xaukar wannan waqar ba, mun tava xaukar ta, amma duk sanda anka hwara ta, ko ina son in ce a dakanta sai in ji na kasa. Don wata irin kewa nike ji a cikin zucciya ta. Inji kamar ga wani abu nesa ina so nai ban same shi ba. Waqar sai in ji kamar tausai taka ba ni. Kai in kana yin ta sai inji kana ban tausai. Ni sai in riqa jin kewa da sauransu. Ko ku mawaqa irin wannan abu kuna ji nai in kuna yin wata waqa?

Makaxa Maidaji : Eh! Muna ji nai. Shi ka sa wata waqar ta zan kamar salati. Ai ka san salati shi ka ban tausai. Ita waqa in tak koro tay yi daxi sai ta zan kamar salati.

B. S. Y. Alhassan : Wayyo! Ai wagga waqa gaskiya tana ba ni kewa qwarai da gaske. To kamar akwai waxansu abubuwa inda kake cewa "Sarki na Iro mai save harkar mutum da dama". To, na ga kamar in ance

---

205 Domin samun wannan waqa a kammalenta sai a duba Rataye na Xaya na wannan aikin a shafi na 400-401.

an save wane wajen dambe an buge shi ke nan. Mi an ma'anar 'save harkar mutum da dama' cikin wannan waqa?

Makaxa Maidaji : Wato kamar duk jihag ga, su zan ga wuyan mutum guda suke. To, wato ya save harkarsu ke nan. Kamar sava sanda ga kafaxa, a xauke duk jama'u. Kamar in mutum yat tashi aure sai shi taimakai shi yi mai, in yat ta shi buki sai shi taimakai shi yi mai. Kuma shi taimakai da wani abu shi ci da gida nai. To, ya save harkar su ke nan.

B. S. Y. Alhassan : Kamar wurin da kake cewa "Ina ganin balbela da ita da shanu ko yaushe nan taka samun abin da tac ci?

Makaxa Maidaji : Kamar mu makaxa da mu da 'yan mabanmu, in munka zo dukka shina unhwaninmu.

B. S. Y. Alhassan : Ai ni da ina tunanin kana nuhin kana ganin hwadawa kusa da sarki. Ah! Don ko su in aka duba balbela na da shanu. Ai sarki jigon jama'a na, ba ku makaxa ba dud da mu wasu abubuwa sai ka ga sun cije, sai an jawo sarki an sa ciki sai ka ga an samu nasara. Lalle balbela kan tare da shanu take tun da tana bixax abinci. Ah, mi yas sa cikin waqa sai ka ji ana ce ma sarki na wane. Bayan kuma duk mutum na sarki na, amma sai ka ji ana cewa na wane, na wane?

Makaxa Maidaji : Ana amfani ne da manyan hwadawa da manyan qannai da kuma manyan yayye, musamman kuma uwaye da kakanni.

B. S. Y. Alhassan : Wannan waqa ta "Kak ka yarda da raini" ina kash shirya ta, nan kay yi ta?

Makaxa Maidaji : A'ah! Can Zariya niyyi ta, tun lokacin da munka hwara zuwan farko. Da niz zo da wannan waqa ta hwarin, to, shi ke nan da mun ka kwan huxu muna yinta. Sai nic ce a qara yi mai gyara. Amma waqar sau guda mun ka yi ta can Zariya.

B. S. Y. Alhassan : Wannan waqa ai ina ganin ya kamata a qara mata tsawo, saboda waqa ce mai jinjina qwarai da gaske. To, yanzu Alhaji muna son ka tava mana waqoqinka waxanda suke sababbi kau. Don saboda mu ji su.

Makaxa Maidaji : To!

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,

Mai Waqa : Alhaji Mamman Kuzo,

Gindin Waqa : Madogara Alhaji Mamman[206]*,*

: Duniya ga ta gare ka.

Jagora : Alhaji Kuzo ka wuce gori,

'Y/Amshi : Tun da kana tare da Allah,

: Madogara Alhaji Mamman,

: Duniya Duniya ga ta gare ka.

Daga nan ya rera wannan waqar ta tsohon Shugaban Qasa Shagari:

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,

---

206 Za a samu wannan waqa a kammalenta a Rataye na Biyu na wannan aikin a shafi na 215-417.

Mai Waqa : Alhaji Shehu Shagari,

Tsohon Shugaban Qasar Nijeriya,

Gindin Waqa : Na yi mamakin harka tai[207]*,*

: Shehu mai daraja Shagari.

Sai kuma ya kawo wannan waqar:

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,

Mai Waqa : Alhaji Garba Nadama,

Tsohon Gwamnan Jihar Sakkwato,

Gindin Waqa : Allah za ni roqon ka[208]*,*

: In yi biyag gwamna mai girma.

Jagora : Ko can duniya haka,

: Tag gada inji mai tulu,

'Y/Amshi : Ka san duniya daxa,

: Ba mai hurce iyaka tai,

: Allah za ni roqonka,

: In yi biyag gwamna mai girma.

Haka kuma ya rera wannan waqar:

---

[207] Za a samu wannan waqa a kammalenta a Rataye na Biyu na wannan aikin a shafi na 418-420.

[208] Za a samu wannan waqa a kammalenta a Rataye na Biyu na wannan aikin a shafi na 421-422.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,

Mai Waqa : Alhaji Mamman xan Abubakar Malumfashi,

Gindin Waqa : Dogo xan Abubakar na Malumfashi[209]*,*

: Jikan Dabo xan Kilo gwamron giwa.

B. S. Y. Alhassan : To, madallah! Tambayar da nike son in yi ma wajen guda uku ce. Da farko akwai inda kac ce ga wane ga wane, ko 'shaviri gana'. Mi at 'shaviri gana'?

Makaxa Maidaji : 'Shaviri gana' na nuhin shagali in yak koro. Wato, shagali in yak kai matuqa. A yi biki mai yawa.

B. S. Y. Alhassan : Sannan ka ce 'wanda ab bisa hanya kuma bai zuwa sarma ga daji'. Mi as sarma?

Makaxa Maidaji : Abin da as sarma, wato shi ne kana biye da hanyarka. Sai ka ratse ka tahi ka tako qaya ko ka tako wani mugun bayan gari.

B. S. Y. Alhassan : Sannan kuma ka ce idan wani ya yi sarauta da ku za a yi darmoso ko darhoso. Mi ad darmoso?

Makaxa Maidaji : Wato jin daxi. Ai dumu-dumu da kayayyaki, shi ne darmoso.

B. S. Y. Alhassan : To, kamar xazu mun tavo maganar da kay yi cewa ga dalilan da ke sa a yi wa mutum zambo. Ko

---

209 Za a samu wannan waqa a kammalenta a Rataye na Biyu na wannan aikin a shafi na 423-424.

akwai waqarka wadda kay yi zambo daga hwarko har qarshe zambo na zalla kay yi?

Makaxa Maidaji : Ai babu.

B. S. Y. Alhassan : Ni ban ga kana son yi ma mutane zambo da yawa ba. Kuma na ga mutane suna sha'awar zambo ga waqa. Sai kai, in kay yanka kuma vatacce kake yi?

Makaxa Maidaji : Eh! Muna ji suna ta yi.

B. S. Y. Alhassan : Kuma na ga ko da maganar mawaqa zaka yi sai dai ka yi maganar alheri. Wato, kai ba ka yin zambo sai ta kama dole ke nan?

Makaxa Maidaji : Eh! To, sai bana mun ka xan yi wani xan kaxan. Saboda wani na yake wa sarki shegantaka.

B. S. Y. Alhassan : To, ko za ka xan yi mana ita mu jiya?

Makaxa Maidaji : Eh! To, ai mun yi ta.

B. S. Y. Alhassan : Au to wace waqa ke nan?

Makaxa Maidaji : Wannan wadda mun ka hwara yi ta 'Uban Shantali xan Mamman. Duk da dai, da aka xauka yau bata kai can inda ake yin zambon ba.

B. S. Y. Alhassan : To don Allah sai a xan tava mana zambon mu ji yadda ake goge shaqiyi masu yi wa sarki shegantaka?

Makaxa Maidaji : To!

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa

Ubangida : Sarkin Gobir Sabon Birni,

Muhammadu Bawa (1975 - 2003)

Gindin Waqa : Kai ab bahagon gulbi[210]*,*

: Uban Shantali xan Mamman,

: Xan'inna Kilo sarki,

: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Sai kuma ya rera wannan waqar:

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,

Mai Waqa : Alhaji shu'aibu Kunda,

Gindin Waqa : Jikan Kunda ai ina kan zuwa gaisai[211]*,*

: Tun da na san ba ka gaji kyamar mutane ba.

Jagora : Hanqure da ni ai ko da,

: Yaushe nib biya kai ta bakka ni,

'Y/Amshi : Tun da na san ba ka gaji qyamar mutane ba,

: Jikan Kunda ai ina kan zuwa gaisai,

: Tun da na san ba ka gaji qyamar mutane ba.

Haka kuma ya rera waqar nan ta:

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,

---

210 Za a samu wannan waqa a kammalenta a Rataye na Biyu na wannan aikin a shafi na 332-352.

211 Za a samu wannan waqa a kammalenta a Rataye na Biyu na wannan aikin a shafi na 425-426.

Mai Waqa : Alhaji Ali Marafa,

Gindin Waqa : Malam Alo na baraz zaki[212]*,*

: Jikan Kilo xan Marafa.

B. S. Y. Alhassan : To, Madalla! Ban katsi hanzarinka ba,tambayoyi ne gare ni. Domin ina gudun a yi nisa in mance su. Saboda haka idan na gama muna iya mu ci gaba daga inda aka aje. Ni dai cikin waqoqin da na ji kana yi ma sarakuna da sauran mutane na Gobir. Ina jin kana yawan ambatar "Inna'. To, ni ban san ma'anar wannan kalma ba. Sai dai na san ana kwatanta ta da wata ne. To, kuma na ji ka ce qaunar sarki. Ni kuma ina ganin kalmar 'Inna' na nuhin 'uwa'?

Makaxa Maidaji : Eh! Akwai qauna tai 'Inna' akwai kakatai 'Inna', akwai kuma qanne nai biyu waxanda kowace ta ci 'Inna'. A nan qasar Gobir 'Inna'sarki ce. In qarhin ta yak kama shi ke nan ta zama 'Inna', daga kuma ya wuce sai a naxa wata. Ita ma tana buga tambari kamar wada sarki yaka bugawa, idan aka naxa ta. To, wadda ax xiyas sarki ita ke cin Inna a na garin.

B. S. Y. Alhassan: To, shina yiwuwa a samu Inna biyu a lokaci guda?

Makaxa Maidaji : A'ah! Sai an hidda wata sannan a naxa wata. Kamas sarki, ai ba a sarki biyu. Sai an hidda sarki, sannan aka naxa wani.

---

212 Za a samu wannan waqa a kammalenta a Rataye na Biyu na wannan aikin a shafi na 427-428.

B. S. Y. Alhassan : Sai nij ji kana hwaxin duw wada mutum yas san tahiyar ‘yan bori bai kai kamar ‘Inna’ ba. To, mi ad dangantakar ta da bori?

Makaxa Maidaji : To, ai ita sarautar ta ta ‘yan bori ta. Ita ‘yan bori taka hukuntaswa. Ita ba ta da wasu talakkawa. Duk ta san halin ‘yan bori. Nan taka ci taka sha gare su. Ko sun xauko wata kisisina ta su, ta sani.

B. S. Y. Alhassan : A wannan waqa ta zambo, ko da yake, ba luguden waqar zambo ba ce. Tun da ka ce za ka goge mai yi wa sarki ashararanci ne. To, amma sai nij ji ka ce in mutum ya aza gemi, ya kamata shi dakata da wasu abubuwa. Sannan kuma sai kay yi kwanci-kwancin-kwana kak qwala. To, idan mutum ya yi wa sarki wani abu sarki yakan kira ku ne, ya ce wane ya yi min kaza-da-kaza?

Makaxa Maidaji : A’ah! Sarki ba shi hwaxi. In dai anka yi wato munka mayar da martani shi na so. Amma bai cewa ga wane nan a taho a yi mai kaza.

B. S. Y. Alhassan : To ya kuke yi ku san cewa wani na yi wa sarki shexana?

Makaxa Maidaji : Eh! Ai ganewa mu kai.

B. S. Y. Alhassan : To, shi mutumin nan sai kac ce ‘hawa’i’ na. Mi ake nuhi da hawa’i?

Makaxa Maidaji : Hakan ga hauka-hauka. Da shi da bugun buda.

B. S. Y. Alhassan : Amma can sai kac ce bai isa ba sai ya katse abin xauri. Wane abin xaurin zai katse?

Makaxa Maidaji : Wando!

B. S. Y. Alhassan : Ah! Lalle ya zan babban mahaukaci in ya yi wannan abu. To mi aka nuhi da 'Babu'?

Makaxa Maidaji : Abin da ab babu shi ne kamar wani shi hito daga wata qasa, shi zaka, ya zamanto yana nuna hihiko. Yana nuna ba shi da kaxan. Yana nuna kamar ya hi su. Kuma shinai musu xauke-xauke hakan ga da xagawa. Su kuma suna dibi nai kamar iska.

B. S. Y. Alhassan : To, na ji ka matsawa Buzu da Bahillace. Ko mi ad dalili?

Makaxa Maidaji : Abin da ad dalili shi ne can dauri, in talakkawa suka xan yi ayyukansu. Sai makiyaya suna zuwa suna canyewa. To, shi zamanin wanga sarki duy ya hana irin waxanga abubuwa. Yanzu, ko shinge ba a yi ga gona. Kuma ba mai kwana daji wurin tsaro, tun da duy ya hana. Saboda haka, idan aka yi wa talakka varna, kamar ya xan yi gona tai a kyaye. To, tsaye wannan sarkin shi ke yi nan da nan a biya haqqin mai gona.

B. S. Y. Alhassan : To, sai kuma waxansu mawaqa da nij ji kana ta zanawa kamar su Ibrahim da Shawai da salihu da sauransu.

Makaxa Maidaji : Au! Ai duk waxannan sarakuna ne.

B. S. Y. Alhassan : Mhm! Ai na ji kana cewa sun kaxa tambari?

Makaxa Maidaji : Ai ka san sai sarki ya buga tambari.

B. S. Y. Alhassan : Wato, duk manyan sarakunan Gobir sai sun buga tambari. Ai ka ga shi ya sa ake neman bayani. Don in da ka banni sai dai in ce ai Gobir shi

na ta zayyana mana manyan makaxa. Ashe duk sarakuna ne.

Makaxa Maidaji : Ai, in an ka naxa sabon sarki, ba a kai shi gida nai sai an girke mai tambarin nan ya buga shi sau goma sha biyu. Daxa sarautar ta tabbata ke nan. Amma in bai buga ba, to, abu bai yi ba. Domin bai zan sarki ba.

B. S. Y. Alhassan : Waxannan waqoqi guda biyu da kay yi daga baya duk na sarauta ne?

Makaxa Maidaji : Eh! Amma duka na xiyan sarki na.

B. S. Y. Alhassan : Wato mutum yakan zavi wasu daga cikin ‘ya’yan sarki ya yi musu waqa. Ko kuma duw wada suke za a yi musu tun da duk xiyan sarki na?

Makaxa Maidaji : Eh! Duk waxanda suke da muhimmanci yi musu ake yi. Wato, musamman wanda yake da alheri. Domin shi alheri babar qohwa ce gare mu ga mutum shi sami waqa. Shi mai matse hannu sai matse mai waqa. Domin daga cikin waxanan yara waxanda nay yi ma waqar nan guda biyu. Kowane daga cikinsu shi na kira na in yi mai kixi. Duk sun kira ni ne a loluta mabambanta ni ko niq qira ma kowanne waqarsa. Domin cikin waxanga yaran akwai wanda nike gamewa da shi, shi ban hwan xari.

B. S. Y. Alhassan : To, ai ka ji, sai ka sa ni ma in ji kamar a sassaqa min nawa. In da ina samun mai gamuwa da ni ya ban hwan xari ai ba ni riqon alli. Kullum qura na cika min hanci. Sai in sami wuri in zauna ana amsa min. To, amma ka san ita hikima sai wanda Allah yab bawa. Duk komi kwaxayin mutum shi na son shi yi waqa ya

amshi abin hannun jama'a, in dai bai da hikima bain bai yi ba. To ko cikin waqoqin kakanni akwai waxanda kar riqe?

Makaxa Maidaji : To, waqoqin nan na Kakanni ban gane su ba.

B. S. Y. Alhassan : To, na tsoho hwa?

Makaxa Maidaji : Har su ban gane su ba tun da ba a yi su da ni ba.

B. S. Y. Alhassan : To, cikin waqoqin wa, ka san waqa tai ta hwarko?

Makaxa Maidaji: Kai! Waqar Nadada ta hwarko. Ai ina, ban sani ba.

B. S. Y. Alhassan : Allahu Akbar! Allah ya jiqan shi. To ka san waqar shi ta qarshe?

Makaxa Maidaji : Eh! Na sani.

B. S. Y. Alhassan : Kuma kana iya rera ta?

Makaxa Maidaji : Eh!

B. S. Y. Alhassan : To, ai sai a jingina mana ita mu ji ko?

Makaxa Maidaji : To!

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,

Mai Waqa : Sarkin Gobir Umaru,

Gindin Waqa : Jikan Jari ginshiqi[213]*,*

: Dibirtau uban Zagi xan Mamman na Baciri.

Daga bisani kuma ya rera wannan waqar:

---

213 Za a samu wannan waqa a kammalenta a Rataye na Biyu na wannan aikin a shafi na 429-438.

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,

Mai Waqa : Sarkin Gabas na Gwaranyo Umaru,

Gindin Waqa : Namijin daga uban Gardaye[214]*,*

***:** Sarkin Gwaranyo.*

B. S. Y. Alhassan : Madalla! Abin da yas sa nid dakatar da mu shi ne, ina son mu koma kan waccan waqa da kay yi kahin wannan. Wato na ji ta dai waqa ce mai shiga jiki, ga kuma ban-dariya, ga kuma tausai kuma ga harzuqa zuciya baki xaya. Ga kuma ainihin amfani da adon harshe da salo kyakkyawa ga kuma cikakken tarihi tana bayarwa. Yau kamar shekara nawa da rasuwar shi mai wannan waqar?

Makaxa Maidaji : Ai, ina dibin Marigayi Nadada ya shahe ma shekara goma da rasuwa.

B. S. Y. Alhassan : A lokacin duk kana yi mishi karvi ke nan da yay yi wannan waqar?

Makaxa Maidaji : Eh! Ina yi mishi karvi ne lokacin.

B. S. Y. Alhassan : Wato, wannan waqa sai bayan rasuwarshi ka koye ta. Ko kuwa dama kahin ya rasu ka ji ka iya ta?

Makaxa Maidaji : Eh! An yi waqa ne tare da ni.

B. S. Y. Alhassan : Akwai na ka taimako cikin waqar. Wato, akwai abun da ka qara a cikin waqar?

---

214 Za a samu wannan waqa a kammalenta a Rataye na Biyu na wannan aikin a shafi na 449-454.

Makaxa Maidaji : Eh! Ina nau taimako ciki.

B. S. Y. Alhassan : Akwai wata Hausa ko wadda kay yi, ka ce sarki iri biyu ne kuma wanda bai sani ba shi ka hwaxi?

Makaxa Maidaji : Eh! Haka ne, wato, Kannin da Hammadin da Baranqwame da Kututturu.

B. S. Y. Alhassan : Yawwa, wane iri kac ce as sarki Baranqwame?

Makaxa Maidaji : To, waxannan dai sarakunan qasar Gobir ne na da can. Akwai Sarkin Gobir Baranqwame da Sarkin Gobir Kututturu da Sarkin Gobir Nafata da Sarkin Gobir Tanatahu. Akwai kuma Sarkin Gobir Babari da Sarkin Gobir Xanguxe. Waxannan sarakuna duk an buga an barsu a wancan zangon zamani. Wato dalilin ambatonsu a cikin waqa shi ne, su nan qasar Gobirawa, in ba su ka ambata ba, duk abu bai yi ba. Ai kowa ya hi son a hito mai da gwarzo nai. Haka kuma kowa so shi kai shi ji gwarzo nai domin ita ce jinjina. Su kuwa gwarzaye ba raggaye ba ne ko alama.

B. S. Y. Alhassan : Wato, akwai inda kac ce a yi lirwin iri-iri. To mi aka nuhi da lirwin?

Makaxa Maidaji : Abin da ake nuhi da larwan shi ne a yi zaven mazaje. Wato, dai a bincika shi ne larwan.

B. S. Y. Alhassan : Wani abu kuma da ka ba ni sha'awa. Idan kana waqa ko da ka yi abin nan da ake ce ma hauzuwa. Sai in ga waqa ta dawo ta bi daidai da kixi. Akwai lokaci kila kamin zuwan yanzu, kamar lokacin da kake koyo a hannun makaxa. Akwai lokacin da kake kixi bai zo daidai da waqa ba?

Makaxa Maidaji : To, lokacin da munka hwara su manyan muka biya. Wada suke bugawa muke yi har mun ka iya. Ana yin kuskure ana gyarawa musamman idan mutane na da yawa ba a gane kuskuren mutum. To, amma shi ko yaro in shi na da Hausa, dakantawa ya kai sai ya ji wada manya ka bugawa, kuma suke hwaxi, sannan sai ya bi su. Wato, idan bai sani ba, sai ya dakanta sai ya ji wada suka ce.

B. S. Y. Alhassan : Xaya daga cikin tambayoyin da nike so in rufe da su, su ne, bayan wannan sana'a ta waqa, kana da wata sana'a?

Makaxa Maidaji : To, ina yin noma.

B. S. Y. Alhassan : Cikin waqoqin da kake yi ka tava waqa ta yabon kanka?

Makaxa Maidaji : A'ah! Ban yi ba, don kuwa ban damu da ita ba.

B. S. Y. Alhassan : Ah! Ba ka yi ba? Ai ni, ina ganin in na iya waqa, kai na nika hwara yi wa, kamin in yi wa wani, kowa shi jiya. Wato, sai dai ka saukarwa mutanenka waxanda ka ji ka shaqu da su. To, yanzu kamar mai nama, wato, mai sayar da nama. Kag ga bai yankawa yana samma baki nai, ai, ka san yana qwaruwar kai nai. Domin yana tura wa mutane daxi, shi kuwa sai ya kilinge da jar yaxi xai ka kwasar shi. Ai, ina ganin ka samu lokaci ka hetsa ma kanka waqa. Na tabbata yadda kake koxa mazaje haka, idan ka koxa kanka kowa zai yi sha'awa. Domin ba mu xai masu nazari ne za mu yi sha'awar waqar ba har ma da masu sauraro. Musamman, ni zan yi sha'awar in ji ka yi wa kanka waqa.

Makaxa Maidaji : Wato, irin wadda Shata ya yi wa kai nai?

B. S. Y. Alhassan : Eh! Irin ta. Waqar ba makawa za ta yi sha'awa qwarai da gaske. Kuma za ta yi ma'ana. Haka kuma, wani lokaci nakan ji kana yabon mutum, misali akwai wanda kac ce gona tai mil xari sittin. To, na san kana qara yin wannan ne don ka qara azzaba mutum. To, me ku ke ce ma irin wannan?

Makaxa Maidaji : Idan an yi wa mutum irin haka, qara tunzura shi a kai. Domin ai da niz zo niy yi wannan waqat, sai da yak kai ni hag gandun na shi. Mun ka yini muna yi ma gandun kixi. To, bayan mun taho, duk gonakin mutanen dake raxe da shi, sai ya saye duk iyakar gonakin mutanen na kusa da shi yag game su da gandun nasa. Akwai kuma daji rave da gonakin, duka yas sa mota an ka zabe dajin. To, yanzu gandun ba misali. Dalilin yin hakan kuwa shi ne saboda wannan waqa da an ka yi mai.

B. S. Y. Alhassan : Kixi, na ga alamu komi muqamin mutum in dai an ka yi mai shi hawa shi kai, ke nan?

Makaxa Maidaji : In Allah ya so. Domin kixi na sa vannan wani sa'i. Kamar su Alhaji Musa Xanqwairo, in shi na kixi, sai suna yi wa 'ya'yan sarki zambo. Ai shi ka sa vanna.

B. S. Y. Alhassan : To, vanna tsakanin nai da makaxi na?

Makaxa Maidaji : A'ah! Da shi da dangi nai, wani lokaci kuma har ga shi kan shi makaxin. Misali, yanzu kana kixi, ka yi wa sarki waqa kana mai zambo ko ka na ko wa nai, ko xa nai, ko qani nai, ko mahaifi nai. To, ai ko ka san abun nan in ba an

yi hanquri ba, to, ba za shi yi daxi ba. Vannan shi ka zama. Misali, irin wannan ya faru har ga shi Narambaxa. Ga waqar na ta shi da yake cewa “wani xan sarki ya gano ni tahe ya nasa xaka”. To, ai ka san abin nan bai yi ma’ana ba. To, shi dai Narambaxa zambo ya yi wa xan sarki. Sai kuma ya tahi gaida shi. Shi kuma xan sarki a lokacin yana zaune bisa agalaimi nai. Ko da ya tsinkayi Narambaxa tahe, sai yaj janye agalaimi nai yas shige gida. To, shi am mahwarin ya ja qirgi ya nasa xaka.

B. S. Y. Alhassan : To, kai waxanne mawaqa ne na Hausa kake sha’awar waqoqinsu?

Makaxa Maidaji : To, lalle daga cikin makaxan Hausa ina jin sha’awar kixin Xanqwairo, ina jin sha’awar kixin Xan’anace, kuma ina jin sha’awar kixin Sa’idu Faru. Sai kuma wanga yaro da yat tashi yanzu Sani Aliyu Xandawo. Duk ina jin sha’awar waqoqinsu.

B. S. Y. Alhassan : To, ko kana da dalili?

Makaxa Maidaji : Haka nan kawai. Domin in na ishe wani yana kixi. Sai zucciyan nan ta Gobirawa ta taso mini kamar in tashi in sare mutum.

B. S. Y. Alhassan : Au! To, bari in janye kujera ta nesa ka da a sare ni ko?

Makaxa Maidaji : Ai ka san shi Maigida ya sa ni kixi Zariya da ni da Sa’idu Faru. To, ko da Sai’du na kixin nan. Ni, ina can, ina ta zanzana, zucciya ta kawo min kamat in tashi in sare mutum.

B. S. Y. Alhassan : To, kixin Gobirawa na shi kai?

Makaxa Maidaji : A'ah! Can na sarakunansu ne shi kai.

B. S. Y. Alhassan : Ashe ku ma dai kixin bai bakku ba, hawa dai ku ke yi. To, kuma dai ina ganin duw waqoqinka maza kaxai nij ji kana yi wa waqa. Ban ji kana yi wa mata ba?

Makaxa Maidaji : Na yi wa Inna waqa har guda ukku, wagga ta yanzu.

B. S. Y. Alhassan : To, muna da waqoqin?

Makaxa Maidaji : An ya ban yi muku su ba.

B. S. Y. Alhassan : To, ai sai a tava mana mu ji ko?

Makaxa Maidaji : To!

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa,

Mai Waqa : Innar Gobir,

Gindin Waqa : Gagara badau 'Yakkaso[215]*,*

: Ta Muhamman Dosau 'yam mayaqi.

Jagora : Hazo jice rana,

'Y/Amsh : Goge mai kashe molo,

: Gogarma ta Iro.

: Gagara badau 'yak Kaso,

: Ta Muhamman Dosau 'yam mayaqi.

---

215 Za a samu wannan waqa a kammalenta a Rataye na Biyu na wannan aikin a shafi na 380-381.

Daga nan kuma ya rera wannan waqar:

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Rambaxawa,

Mai Waqa : Sarkin Tashar Sabon Birni Alhaji

Idi xan Argiji

Gindin Waqa : Ya kwan yana aikin mota[216]*,*

: Xan Argiji xan Shawai,

: Sarkin tasha jikan Idi,

: Jikan fulanin vaure.

Daga bisani kuma Dr. Bello Alhassan Sodangi ya rufe wannan hira tsakaninsa da Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni kamar haka:

> To, Makaxa mun gode qwarai da gaske da wannan hira da tarihinka da waxansu waqoqi waxanda ba mu tava samu ba waxanda kay yi mana. Kuma mun ji daxi qwarai da gaske, don an ce shimfixar fuska ta hi ta tabarma. Wannan, mu ka ce mu qara dawo wa ke nan, ko ba gaskiya ba.
>
> Tun da kamar yadda ake cewa 'inda yaro ya tsinci wuri, nan ya hi tunawa. Mu malamai ne kuma mu xalibai ne. Kullum cikin neman ilmi mu ke. Kuma ilmi ba abu mai qarewa ba ne. Kullum muna qaruwa da ilmi kwarai daga waqoqinka. Saboda haka, ka da ka yi mamakin bayan 'yan kwanaki kaxan ka ga mun qara dawowa wajenka; da sahe, ko da rana, ko da maraice. Wato dai, duk lokacin da Allah ya

216 Za a samu wannan waqa a kammalenta a Rataye na Biyu na wannan aikin a shafi na 367-369.

saukar da mu. Kuma mu ba za mu yi mamakin mu gane ka wata rana ba.

Har wa yau, muna godiya gare ka qwarai da gaske. Kuma ka da ka manta da cewa na ce, ka yi kwanci-kwancin-kwana ka kwantsama ma kan ka taka waqar. Mun gode matuqa.

Ganawa Tsakanin Makaxa Maidaji Sabon Birni Tare Da

Alhaji Ibrahim Xiso,Tashar Rima Rediyo Sokoto,

Jihar Sakkwato.

Gabatarwa

Alhaji Ibrahim Ahmad Xiso a shirin *Daga Bakin Mai Ita* na Rediyo Rima dake jihar Sakkwato ya fara gabatar da shirin da:

> Jama'a masu sauraronmu Assalamu Alaikum, barkanmu da sake saduwa daku a cikin wani sabon shirin. Shirin dake kawo muku hira da makaxanmu da mawaqa dake gare mu a nan jihar Sakkwato. Kuma ana jinsu yau da gobe a cikin wannan shirin.
>
> To, ko yau dai mun sadu da wani jigo wanda ba voyayye ba ne ta fuskar kixa da waqa musamman kixan sarauta da na noma. Kuma ba shakka akan ji shi akai-akai a wannan gidan Rediyo na Rima Rediyo Jihar Sakkwato da sauran gidajen Rediyo na jihohin arewa inda ake amfani da wannan harshe namu na Hausa. To ba dai zan cinye hilin ba, da farko bari in tambayi sunan mawaqin da muke hira da shi a yau:

Alhaji Ibrahim X: Sunan baqon namu?

Makaxa Maidaji : Alhaji Makaxa Maidaji Sabon Birni.

Alhaji Ibrahim X: To Alhaji Maidaji kahin mu ci gaba dai nakan so in tambayeka cikakken ko kuma sunanka na zane tun da yake Maidaji sunanka ne na laqani?

Makaxa Maidaji : Eh!

Alhaji Ibrahim X: To mi sunanka na yanka?

Makaxa Maidaji : Sa'idu.

Alhaji Ibrahim X: To! Sa'idu Kake?

Makaxa Maidaji : Eh!

Alhaji Ibrahim X: To madallah! Na tabbata ba mutum duy yassan da wannan sunan b. Domin an hi saninka da Maidaji Sabon Birni. To, mukan hwara wannan shirin da tambayar xan taqaitaccen tarihin rayuwar mawaqin da muke magana da shi. Ko za ka xan iya ba mu taqaitaccen tarihinka na rayuwarka. Misali, kamar yau shekarunka nawa a duniya?

Makaxa Maidaji : Ina ganin na shekara hamsin da biyar (55).

Alhaji Ibrahim X: To, Alhaji Maidaji kai mutumin wane gari ne. Ko da yake ga shi ana cewa Maidaji Sabon Birni?

Makaxa Maidaji : To, tun can muhwarin mutasabbibin mutum muna cikin Tara. Tun da kakanninmu suka taho daga Kunya, sunka zaka Tara. Sannan daxa da ruwa sunka cimma Tara sai kowa yab bi daji yab bi gona.

Alhaji Ibrahim X: Mil nawa ne ke tsakanin Tara da Sabon Birni?

Makaxa Maidaji : Ina ganin ya yi mil bakwai (7km).

Alhaji Ibrahim X: To Alhaji Maidaji ya kuke da marigayi Alhaji Nadada Sabon Birni?

Makaxa Maidaji : Wa na ne.

Alhaji Ibrahim X: Xaki guda?

Makaxa Maidaji : Eh!

Alhaji Ibrahim X: To, wannan bayani ya xan faxakar da mu abubuwa game da kai. Da kuma wannan suna na Maidaji. Ko da yake kahin mu ci gaba muna son ka ba mu dalilin da ya sa ake kiranka da wannan suna Maidaji?

Makaxa Maidaji : Wato wata ‘yar mahwara aka yi tsakanin talakkawa da masu gari. Zamanin ana hauga-hauga, don sannan gaskiya ana iko. Sai sunka yi hushi sunka watsu. Lokacin an yi shuka, shuka ta isa noma, sai kowane ya koma gona tai ya gina bukka. To, sai anka haihai ni can wurin zaman noma. Shi am mahwarin can dauri Maidaji Xanbugaje ake ce man.

Alhaji Ibrahim X: To, da yake dai mun san irin waqoqin da kake yi a halin yanzu musamman na sarauta da noma. Kana iya hwaxa mana da irin waqar da ka hwara. Ko da yake kahin mu ci gaba, ina son in san ya waqa take gare ka. Ka gada ne ko a’a?

Makaxa Maidaji : Au kwarai da gaske.

Alhaji Ibrahim X: Wajen shi Tsoho?

Makaxa Maidaji : Au tun dak kakanni.

Alhaji Ibrahim X: To, tun dak kakanni?

Makaxa Maidaji : Au tun dag Gabas wato Gubur suka kixi har suka zaka Tcibiri suna tare da Gobirawa har anka zaka Sabon Birni. Tun zamanin Sarki Salihu yana xan sarki, kahin ya zama sarki lokacin da aka kawo shi Gangara.

Alhaji Ibrahim X: To, ya anka yi kas soma, ka yi zamani tare da shi Dattijo kahin yai qaura ko ko dai?

Makaxa Maidaji : A'a! Ko da munka tasa ya bar kixi. Na tashi ne wajen Makaxa Nadada.

Alhaji Ibrahim X: To, bayan ya kau ne, sannan ka hwara kixi?

Makaxa Maidaji : Shi Nadada tun yana da rai nih hwara nau kixi. In yat tashi nashi sai in bar nau in tahi, lokacin da munka dawo sai in ci gaba da nawa kixin.

Alhaji Ibrahim X: Waton Sarki Ummaru dai kai kawwa waqa?

Makaxa Maidaji : Eh! Shi nih hwara yi wa waqa.

Alhaji Ibrahim X: Kuma ina ganin shina da rai har yanzu ko?

Makaxa Maidaji : Eh! Shina da rai.

Alhaji Ibrahim X: To ni da masu sauraro ina ganin za mu so mu ji waqar nan ta ka ta farko da ka soma yi sai a tavo mana ita?

Makaxa Maidaji : To!

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,

Ubangida : Sarkin Gobir Ummaru xan Salihu,

Gindin Waqa : Binu xan baraz zaki Xanbawa[217]*,*

: Jikan Kilo gwamron giwa.

Alhaji Ibrahim X: To madalla Alhaji Maidaji. To ai ina ganin ai an sha kalwa ko, tun da ya samu sarautar ba.

---

[217] Domin samun wannan waqa a kammalenta sai a duba Rataye na Biyu a cikin wannan kundi a shafi na 316-317.

Ina ganin ka yi hwata ne cikin wannan waqar kahin ya zama sarki ba?

Makaxa Maidaji : Eh! To, mun gode, tun ran da nis soma waqar ga abin kalwa dai bai katse ba, sai dai abin da yac ci gaba.

Alhaji Ibrahim X: To, daxa bayan wannan waqar da yake ta sarauta ce, tun daga sannan ka hwara na noma ko ko?

Makaxa Maidaji : A'ah! Na daxe ina yin na noma kahin nan.

Alhaji Ibrahim X: To, yanzu cikin na noma wace ka hwara yi. Ko da yake ka yi waqoqi daban-daban na noma, wace waqar kake iya tunawa ta noma wadda ita ce ka hwara yi?

Makaxa Maidaji : Lokacin da nih hwara kixin noma waxanga yaran duk ba a haihaisu. Domin tun lokacin da ban yi aure ba na hwara. Waxanda nih hwara kixi da su, sai Tsohon ga wanda ak qanin uwayenmu. Sauran duk da nih hwara da su babu su.

Alhaji Ibrahim X: Ai ina ganin akwai wadda kun ka yi tare da su daga cikin waqoqin noma xin. Wacce daga cikin waqoqin tahi shiga ranka?

Makaxa Maidaji : Ai waqoqin noma ne duk sun shige cikin duhu. Musamman waxanda nih hwara yi.

Alhaji Ibrahim X: Eh! Gaskiya ne, ka rera mana wadda das bisani ka rera tare da waxannan yaran na yanzu. Amma wadda tahi shiga ranka.

Makaxa Maidaji : To za a tavata ko ko?

Alhaji Ibrahim X: Eh! Haka nike so, tun da, da su anka san ka, waqoqin sarauta da na noma. To, tun da mun hwara tava ta sarauta, yanzu sai mu tava ta noma ko?

Makaxa Maidaji : To amma sai mu yi wadda suke ganewa ba ma yi waxanda ba su sani ba.

Alhaji Ibrahim X: Eh! Sai a tavo mana guda ta noman ko?

Makaxa Maidaji : To!

Makaxi : Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni,

Mai Waqa : Waqar Noma ta Arzika[218]*,*

Gindin Waqa : Sarki yai abin daka ya huta,

: Zaki xan Abubakar xan Buda.

Alhaji Ibrahim X: To, madalla Alhaji Makaxa Maidaji, to, waqar wa ke nan?

Makaxa Maidaji : Waqar Arzika sarkin noma na garin Rambaxawa. Yana cikin waxanda nih hwara yi wa kixi tun muna 'yan yara. Tana daga cikin tsofaffin waqoqin noma waxanda suka zan ganiyya ga duk waxannan yaran.

Alhaji Ibrahim X: To Alhaji Maidaji, cikin waqoqin da ka yi duka, da na noma da na sarauta, ka san kowane mawaqi yana da bakandamiya. Wadda muke

218 Domin samun wannan waqa a kammalenta sai a duba Rataye na Xaya a wannan aikin a shafi na 314-315.

kira Bakandamiyar waqa, wato, fitacciyar waqa wadda shi kan shi makaxi ya hi son wannan waqar, duk da waqoqin da yay yi. Ba ana nuhin ya zan kahi son mai wannan waqar ba, a'a, ai duk waxanda kaw wa waqa masoya ne. Amma dai to daxa wace daga cikin waqoqin naka ta hi shiga ranka ko da yaushe, wadda ko kwana kake yi kana iya tuna wannan waqar?

Makaxa Maidaji : To, wanda ka yi min alheri shi nika wa waqa ina kwana!

Alhaji Ibrahim X: To, ai ka ga Allah ya yi yawa da su. To, shi na nika son kamar cikin duk waqoqin da ka yi iya rayuwarka. Wace ta guda wadda tahi shiga cikin ranka nike so?

Makaxa Maidaji : To! Yanzu dai na yi wa sabon Sarkin Gobir na Sabon Birni wata waqa na yanzu.

Alhaji Ibrahim X: Yanzu ita tah hi zama hitatta cikin waqoqinka?

Makaxa Maidaji : A'ah! Ba ita tah hi zama halitta ba.

Alhaji Ibrahim X: Ai wadda tahi zama hitatta nike so, wadda ko hita wasa wani wuri ko waqoqi kake yi wani wuri ko waqoqi kake yi wani wuri ana sa ka yi wannan waqa saboda karvuwarta ga mutane. Ita nike son ka tuno cikin waqoqin da kay yi. Daxa ko na sarauta ko na noma ko na wani hali?

Makaxa Maidaji : To! Mu tava ma Sarkin Bunza ke nan:

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,

Mai Waqa : Sarkin Buza,

Alhaji Abdussalam Buza,

Gindin Waqa : Xansidi amshi sandar mulki qasa tai[219]*,*

: Mai Bunza Xanhassan mai taro hannu.

Alhaji Ibrahim X: To, madalla, wato, sarautar nan kake nuhi yak koma katanga Alhaji Maidaji ko ko?

Makaxa Maidaji : Eh! In da nic ce 'darnin da anka bari ya koma katanga'. Domin ina gida ya dinga aiko min da dukiya.

Alhaji Ibrahim X: Wac ce qasar Buza?

Makaxa Maidaji : Arewa.

Alhaji Ibrahim X: Alhaji Maidaji na tuna da wata waqa ta noma wadda kay yi, waqa ce karvavviya kwarai da gaske ga mutane. Shin wane lokaci kay yi wannan waqa wadda kake cewa 'ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro'?

Makaxa Maidaji : Sunan waqar 'yar Buhari. Ga waqar nan:

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,

Mai Waqa : Waqar Noma ta 'Yar Buhari,

Gindin Waqa : Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi[220]*,*

: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.

---

219 Domin samun wannan waqa a kammalenta sai a duba Rataye na Xaya a wannan aikin a shafi na 402-403.

220 Domin samun wannan waqa a kammalenta sai a duba Rataye na Xaya a wannan aikin a shafi na 404-408.

Alhaji Ibrahim X: To, madalla, waqar yunwa ke nan da aka yi wa Buhari ko?

Makaxa Maidaji : Eh!

Alhaji Ibrahim X: Waton , mutanen nan guda uku ba yadda za a yi su iya maganin yunwa ka ce da likita da malami da boka?

Makaxa Maidaji : Eh! Sai in kuxxi sun ka saciccike na mutane. Amma yunwa kam ba su da maganinta. Sai dai su gero da su rogo da quli-quli.

Alhaji Ibrahim X: To da kyau, Alhaji Maidaji mun gode da wannan waqa. Sai dai Alhaji Maidaji ina son in sani, yanzu, waqoqin nan da kake duka. Ya ya kuke yinsu. Sai kun tsaya kun yi yarjeje da mutanenka ko ko, ko'ina waqa tas samu yi kuke yi?

Makaxa Maidaji : Eh! Tun da yanzu muna rage abin ne ai waqa ba ta yin yawa. Yanzu da munka kwan biyu sai mu tahiyar mu gona mu hita batun kixi.

Alhaji Ibrahim X: To, amma ina ganin akwai wata waqa wadda kay yi, sabuwa ce dai a taqaice a wani karon lokaci da ka zo mana. Kuma ina ganin wannan waqa nan take kay yi ta, ta mata. Sai dai ina ganin kana kallon gudunmuwar da mata suke bayarwa tana da yawa ne yas sa kay yi wannan waqa. Ko wane dalili ne ya sa?

Makaxa Maidaji : Eh! Wani taro ne da anka gayyace ni a garin Anka. Sai anka ce mata su as shugabannin taro. To, komi da komi gehen mata yas shahwa. Sai an ka ce in samu wuri in yi musu kixi, shi niq qira ta nan take.

Alhaji Ibrahim X: Eh! Ai ni ma na san nan take kay yi ta, saboda haka, yanzu sai ka daddage ko yanzu ka yi mana wannan waqar a ga hikimar da ke ciki ko?

Makaxa Maidaji : Uhm!

Makaxi : Alhaji Sa'idu Rambaxawa Sabon Birni,

Mai Waqa : Waqar Mata

Gindin Waqa : Mata in ba ku ba gida[221]*,*

: Wurin Allah ku ad daga ciki.

Alhaji Ibrahim X: To, haka yake Alhaji Maidaji. Waton dai mata suna da martaba musamman dai waxanda suke da aure. A cikin waqar akwai inda kake cewa 'hikima', me kake nuhi?

Makaxa Maidaji : Eh! Ta ma'aikin Allah ba, can gobe.

Alhaji Ibrahim X: To, ashe sai mata su dage su yi aure tun da sun ji wannan alqawali. To, madalla, Alhaji Maidaji mun gode da wannan waqa. Sai dai Alhaji Maidaji, ina son in sani cikin 'yan'uwa mawaqa, waxanne daga cikinsu kake sauraron waqoqinsu?

Makaxa Maidaji : Ina ganin ina sauraron waqar Xan'anace.

Alhaji Ibrahim X: Cikin waqoqin kuma akwai guda wadda ina ganin kahi son sauraronta. Kuma ka hi son ka zam kana yin ta ko da yaushe?

Makaxa Maidaji : Eh! In nij je gona, ina sassabe ina yin ta.

---

221 Domin samun wannan waqa a kammalenta sai a duba Rataye na Xaya a wannan aikin a shafi na 409-410.

Alhaji Ibrahim X: Wace waqa ke nan?

Makaxa Maidaji : Waqar da yake yi ta Bagobiri Xandambe.

Alhaji Ibrahim X: To, Alhaji Maidaji na tabbata tun da kana son wannan waqar mai yiwuwa ne kila ka ari bakin shi, ka masa albasa a wannan waqa.

Makaxa Maidaji : Yanzu?

Alhaji Ibrahim X: Eh! Kamar ka kwaikwaye shi. Ko da yake shi kalangu yake amfani da shi, kai kuma ga shi da taushi ne. Amma kila kana iya ka kwaikwayeshi tun da kana son wannan waqar ta shi. Ka xan yi ta mu jiya?

Makaxa Maidaji : Mhm!

Jagora : Yaqi sabon Bagobiri mai kayan hwaxa,

'Y/Amshi : Yaqi sabon bagobiri mai kayan hwaxa.

Jagora : Dawo-dawo Bagobiri,

'Y/Amshi : Dakata zan bari,

: Yaqi sabon Bagobiri,

: Mai kayan hwaxa.

Jagora : In kana hwagen hwaxa,

: Ka zan ki maza kiran maza,

'Y/Amshi : In ji suna hito kamar raquma,

: Yaqi sabon Bagobiri,

: Mai kayan hwaxa.

Jagora : Yaqi sabon Bagobiri,

‘Y/Amshi : Mai kayan hwaxa.

Alhaji Ibrahim X: Bari mu tsaya nan Alhaji Maidaji. Da yake an ce ‘waqa bakin mai ita’. Da a ce shi ma ya yi irin waqarka za a ji bambanci. Musamman da yake kayan kixan daban-daban ne.

Daga bisani kuma Alhaji Ibrahim Ahmad Xiso ya kawo jawabin kammala wannan shiri na *Daga Bakin Mai Ita* na Rediyo Rima dake jihar Sakkwato kamar haka:

> To, Alhaji Maidaji, mun gode da wannan hira da ka bamu a cikin wannan hili na *Daga Mai ita*. Kuma nan gaba sadda duk kas sake dawowa muna maraba da kai. Jama’a masu sauraronmu kun ji yadda hirarmu ta kasance tare da Alhaji Maidaji Sabon Birni. Kuma ina fatan kun ji daxin wannan shirin. A madadin abokan aiki na da ke tare da ni, ni, Ibrahim Ahmad Xiso ke cewa da ku a kasance lafiya.

GODIYA

Ina matuqar godiya ga Allah, mahaliccin kowa da komai, wanda yake ba xan'adam basira da hazaqa da azancin shirya waqa wadda yake amfani da ita wajen shiryar da al'umma zuwa ga rayuwa mai inganci. Tsira da amincin Allah su tabbata ga Manzon Rahama, Annabin Tsira, sallallahu alaihi wa sallama.

Da farko, ina miqa godiya ta musamman ga Dr. Muhammad Lawal Amin, malamina kuma jagoran wannan aiki na xaya, mai ba ni shawara da gyara wannan aiki. Sannan kuma, ina qara miqa godiya ga malamina, Dr. Magaji Tsoho Yakawada, wanda shi ne mai duba wannan aiki na biyu. Waxannan malamai nawa sun ba ni shawarwari kyawawa, sannan sun yi haquri da ni, musamman samun su da nake yi a ko da yaushe cikin suna da lokaci ko ba su da lokaci. Sun karve ni sosai tare da sakin fuska. Allah ya saka musu da alherinsa, amin. Allah ya kyautata zuri'arsu baki xaya tare da samun nagartacciyar rayuwa mai yalwa mai albarka, amin.

Haka kuma, ina mai matuqar farin cikin isar da kevantacciyar godiyata ga mahaifana; Farfesa Sa'idu Muhammad Gusau da mahaifiyata Hajiya Lubabatu Abubakar Buba Maigoro waxanda suka sha xawainiya da ni tun daga farkon ruhin rayuwata. Tabbas sun yi haquri da ni matuqa gaya, ba ni da wani abu da zan saka musu da shi face addu'a da kuma fatan alheri duniya da lahira, Allah ya yi masu luxufi da rahamarsa, kuma Allah ya sa Aljanna ce makomarsu, amin.

Ina matuqar isar da kevantacciyar godiya ga Farfesa Abubakar Adamu Rasheed, Shugaban Jami'ar Bayero, Kano. Wannan baba nawa ya nuna mani so da qauna, a kowane lokaci ina cikin ransa. Ya

yi ta qara mani qaimi tare da horona a kan naciya da qwazo. A ko da yaushe, sai dai in ba mu haxu ba, a gida ne ko a waje, yana gani na, bayan gaisuwa, to, abin da zai tambaya shi ne ya ya karatu? Allah ya qara masa xaukaka, ya kuma albarkaci iyalansa da zuri'arsa baki xaya, amin.

Ina matuqar godiya ga Farfesa Xalhatu Muhammad na Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello Zariya. Ba zan tava mantawa da kulawa da yake nunawa a gare ni ba, musamman a matsayina na jikansa. Allah ya qara masa lafiya, ya ci gaba da tallafa masa a dukkan abun da ya sa a gaba. Allah ya albarkaci iyalansa da zuri'arsa baki xaya, amin.

Ba zan tava mantawa da taimako wanda Dr. Ahmad Magaji da ke Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya da Kimiyyar Harshe, Jami'ar Bayero, Kano yake ba ni ba domin ganin aikina ya bunqasa kama daga littafi ne ko maqala ko kuma wani kundi ne. Ba tare da nuna qosawa ba, ko da yaushe qofa a buxe take tsakanina da shi. Allah ya saka masa da alherinsa ya kuma kyautaci bayansa baki xaya, amin. Ina godiya matuqa.

Har wa yau, godiya ta musamman ga malamina Dr. S. Y. Alhassan, wanda ya qara inganta wannan aiki a matsayinsa na Mai Duba Bincike na Cikin Gida da Dr. Balarabe Abdullahi da dukkan sauran malaman Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello Zariya. Ina godiya matuqa.

Ina qara miqa kevantacciyar godiya ta musamman da ban gajiya ga malamina Dr. Bello Bala Usman wanda ya duba wannan aiki ya kuma tace shi a matsayinsa na Mai Duba Bincike na Waje da Farfesa

Abdullahi Bayero Yahya da dukkan sauran malamai na Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Xanfodiyo da ke Sakkwato. Ina godiya gare su matuqa.

Har wa yau, ina gode wa dukkan malaman Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya da Kimiyyar Harshe, Jami'ar Bayero, Kano. Musamman a kan koyar da ni da suka yi da qaunar da suke nuna mani a ko da yaushe. Allah ya saka musu da alheri.

Har kullum, ba zan tava mantawa da ku ba, marigayi Sheikh Muhammadu Xankullum da Hajiya A'ishatu Indo da kuma Hajiya A'ishatu Abubakar Buba Maigoro. Allah ya jiqan su da rahamarsa ya sa aljanna ce makomarsu, Allah ya kuma kyautata namu lokacin cikin karimcinsa da yardarsa. Sai Alhaji Garba Xan'aya Gusau da Hajiya Amarya duk kakanni ne da suka rigaye mu gidan gaskiya. Allah ya jiqan su da rahamarsa ya sa kuma Aljanna ce makomarsu baki xaya.

Ina kuma gode wa Alhaji Abubakar Buba Maigoro da Malam Alhaji Muhammad Tukur (Alhaji Tsoho) da sauran ilahirin iyayena saboda taimakon da suke mana tare da yin addu'a. Allah ya saka musu da alherinsa, amin. Ina kuma godiya ga dukkan kakannina; Hajiya Hauwa Muhammad Xankullum (Hajiya Yawo) da Hajiya A'isha Muhammad Xankullum (Hajiya Lela) da Hajiya A'isha Abubakar Maigoro (Hajiya A'isa) da Hajiya Hauwa Abubakar Maigoro da gwaggonni da innonina da sauran magabatana na jini.

Godiya ta musamman ga Babana Dr. Bawa Hassan Gusau da ke Sashen Kimiyyar Siyasa, Jami'ar Bayero, Kano da Kawu Namadi da Dr. Aliyu Mu'azu. Ba zan tava mantawa da qoqarin da suka yi ba musamman ganin aikin nan nawa ya yi kyau. Sai kuma Malam Jibril

Shu’aibu Adamu da Malam Manu Abdu da Malam Ibrahim Ahmadu Samaru da ke Sashen Larabci, Jami’ar Ahmadu Bello Zariya, ina godiya matuqa gaya zuwa gare su.

Ban manta da ku ba; Kaka Ibrahim Shehu Liman Zariya da Alhaji Hassan Elkanemi Excellency, Jihar Nasarawa da Alhaji Abdurrahman Ibn Muhammad, Manajan NTA Jos da Oga Arxo da ke Ofishin Karvar Haraji a Jihar Nasarawa. Ina godiya a gare ku baki xaya.

Godiya ga Magajin Garin Sabon Birni, Alhaji Garba Magajin Gari da Bangon Gobir a kan karramawa da karvar baquncinmu da kuma tagomashi cikin haiba. Sai kuma waxanda suka yi mana rakiya zuwa gidan Makaxa Maidaji suka sada mu da iyalansa, Hassan Muhammad (Mamman Maidankali) da Abdullahi Abubakar (Maiwake). Allah saka muku da alherinsa, amin.

Sai kuma iyalan Makaxa Maidaji waxanda suka nuna mana karimci tare da nuna qauna. Sun ba ni haxin kai wajen samun duk bayanin da nake buqata. Alhaji Ibrahim Musa Nadada (Hana) da Alhaji Adamu Sa’idu Maidaji (Baciri) da Muhammad Sa’idu Maidaji (Rani) da Alhaji Garba (Namaiqosai) duk ina godiya matuqa gaya, Allah ya saka muku da alherinsa, ya jiqan Makaxa Sa’idu Maidaji.

Ina godiya ga yayyena; Binta Sa’idu Muhammad da Zahra’u Sa’idu Muhammad, da qannena; Hindatu Sa’idu Muhammad da Rahina Sa’idu Muhammad da Umama Sa’idu Muhammad da Yusha’u Sa’idu Muhammad da A’isha Sa’idu Muhammad (Ummi) da Muhammad Sa’idu Muhammad (Khalifa) da Asma’u Sa’idu Muhammad (Husna) da Muhammad Sa’idu Muhammad (Sadiqu) da

Muhammad Sa’idu Muhammad (Shafi’u) da Sa’id Sa’idu Muhammad (Junior) da kuma marigayiya Khadija Sa’idu Muhammad (Munaya), Allah ya jiqan ta da rahamarsa ya sa ta zama qarin kariya gare mu baki xaya wajen ceto a ranar gobe da duk sauran al’ummar Musulmai, amin.

Sai kuma ‘ya’yana, yara manyan gobe, ku ma abin tunawa ne abin bege, wato da Maryam Yahaya da Hafsa Bashir Muhammad (Nuwaira) da Khuzaifa Aminu da Sa’id Bashir Muhammad (Almilal) da Anas Abubakar Zanwa Masi.

Haka kuma ina godiya ga dukkan ‘yan’uwana maza da mata da abokaina da mutanen arzikina kamar Zanwan Manoman Kileman Lafiya, Jihar Nasarawa Malam Abubakar Zanwa Masi da Alhaji Nasidi Buhari Ahmad da Alfa Hashim Zariya da Malam Maharazu da Malam Lawali Gusau da Sani Abubakar Sadiq (Likita) da Abdulqadir Xan Alhaji da Ibrahim Sulaiman Zariya da Abubakar Yusuf Zariya da Bashir Gajam da Nura Sabon Birni da Safiyanu Bayero da Umar Inuwa Musa (Dash) da Shamsiyya Bashir Adam da sauransu da dama saboda irin tasu gudunmuwar da suka bayar wajen ganin wannan aiki ya kammala, musamman addu’a da sukan yi ta fatan alheri. Dukkan ‘yan ajinmu maza da mata da sauran dangi waxanda ba zai yiwu a faxi kowa da kowa a nan ba, ina roqon Allah ya saka musu da alherinsa. Ina bayar da haquri ga dukkan ‘yan’uwana da abokaina da kuma dukkan waxanda na sani, da ba a faxi sunayensu a nan ba. Ina yi wa kowa da kowa fatan alheri.

GABATARWA

Nazarin waqoqi, musamman na baka, wani al'amari ne da yake buqatar zuzzurfan bincike cikin kaifafa tunani. Waqa tana xauke ne da duk wani nau'i na hikimar harshen xan'adam.

"Waqa wata abu ce wadda ke nuna hoton rayuwar al'umma ta fuskar zamantakewarta da addininta da tattalin arzikinta da sauran abubuwa da suka shafi harkoki na rayuwar yau da kullum" (Gusau, 2002[a]:68).

Skinner (1971) da Muhammad (1978, 1979, 2006) da Umar (1984) Xangambo (2007) da Ibrahim (1983) da Gusau (1996/2005) da Zarruq (1990) da Muhammad (2003) da sauransu sun bayyana waqa tamkar madubi wadda ke bayyana hoton rayuwar al'umma. Satatima (2009: 2-5) yana cewa:

> Masana da manazarta ilimin rayuwar al'umma da takwarorinsu da ke nazarin walwalar xan'adam sun bayyana cewa fasahar al'umma kan taka muhimmiyar rawa wajen ingantawa tare da havaka wannan al'umma dangane da adabinta. Adabi kuma fanni ne na fasaha wanda ya qunshi abubuwa da dama kamar waqe-waqe na baka da rubutattu, da tatsuniyoyi, da labarai na baka da na zube (Qagaggun Labarai) da sauran al'amuran da adabi yake tafiya da su.

A wajen al'ummar Hausawa waqa na da muhimman sassa guda biyu, wato waqar baka wadda al'umma ta buxi ido da ita da kuma waqa rubutacciya wadda aka samu bayan Hausawa sun iya karatu da rubutu.

Waqa na tafiya da darasi xauke da manufa mai qayatarwa ta hanyar kwaikwayo da sauwarawa tare da ayyanawa da kuma tsara aukuwar ko a yi hasashen aukuwar wani abu a rayuwa.

An gudanar da wannan aiki ne bisa tsari na babi-babi domin samun sauqin isar da saqo. An kuma kasa babobin ne zuwa gidaje kamar haka:

Babi na xaya yana xauke ne da sharar fage, wato shimfixa inda aka bayyana manufar da ta haddasa aiwatar da wannan bincike. An qalailaice hanyoyin da akan bi wajen ganin kwalliya ta biya kuxin sabulun galabar tattara bayanai da aka yi amfani da su domin kammaluwar wannan bincike.

Babi na biyu kuma ya yi bitar ayyukan da suka gabata ne. An kawo ayyukan magabata waxanda suka riga suka taka rawar gani domin samun qarin haske da madogara wajen inganta wannan aiki.

Har wa yau, a wannan babi na biyu an yi bitar tarihin rayuwa da asali na Makaxa Maidaji Sabon Birni kamar bayanin haihuwarsa da quruciyarsa da ayyukansa da ma'amalolinsa da kuma bayani dangane da qungiyar Makaxa Maidaji Sabon Birni, har ya zuwa ranar da Allah, maxaukaki, ya karvi rayuwarsa.

Babi na uku yana tattare ne da bayanin jigo da kuma nau'o'insa inda aka kalli jigo a waqoqin Makaxa Sa'idu Sabon Birni. An kuma yi bayani a kan fara waqarsa da yadda yake shirya waqa da bayanin waqoqinsa na farko waxanda ya gabatar. Daga bisani kuma aka bayyana ire-iren waqoqin Makaxa Maidaji.

Daga nan ne aka fitar da muhimman manufofi na waqoqin Makaxa Maidaji. Sai kuma aka yi warwarar jigo da muhallin jigo duka a waqoqin na Makaxa Maidaji.

Babi na huxu shi kuma ya qunshi tsari da ma'auni wanda ya qunshi fasalin yadda mawaqi yake sassarqa saqonninsa a cikin layukan xiyan waqa. An kawo cikakken bayanin takidi da salo da sarrafa harshe na waqoqin Makaxa Maidaji Sabon Birni inda aka duba

tsarin xiya a waqoqinsa da kuma tsarin da yake amfani da shi wajen rera waqoqinsa.

Babi na biyar na wannan aiki yana xauke ne da kammalawa da manazarta da kuma rataye.

ABSTRACT

This corpus with English rendition, 'The Study on the songs of Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni" examine the works of art in Maidaji's performance and some aspect of his life.

The work in corpus studied the songs of Makaxa Sa'idu Maidaji in scholarly point of view with respect to the theme, the stainzaic structure, the stainzaic forms, the iterations, the figures of speech and other stylistic devices in Maidaji's work of art.

On the theme aspect, the corpus studied the thematic components in Maidaji's performances such as the eulogues, the praise, the englightenment and the political perspective. The corpus also studied the thematics constituents in Maidaji's arts such as the genetive, the religious, the egocentric speech and then the innuendo.

This study perceived the majority of Maidaji's art is build upon eulogues and enligtenment. Usually, Makaxa Maidaji shun satire in his compositions.

Also, the flow of stanza in Maidaji's Performance, is by virtue of Maidaji being the composer and have those that carried the chorus. He adorn this format (Jagora + qulli +qari + tarbe + karvevveniya/ rakiya +takidi +gindin waqa).

Maidaji's is an artist who composes poem with words filled with devices that beutifies his language. And his language of expression is Sokoto dialect. Some expressions found in his work of art include the simile, the metaphor, the mutation, the epithet, the proverbs, the enjambment and so on.

TSAKURE

A wannan bincike mai suna: Nazarin Ayyukan Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni an yi waiyaye ne dangane da ayyukan Makaxa Maidaji tare da kallon yadda ya gudanar da wani vangaren rayuwarsa wajen shiryawa da rera waqoqin baka ga al'ummar Hausawa.

A ciki an duba matani na waqoqin wannan makaxi; Sa'idu Maidaji inda aka xora su a bisa wasu matakai na nazari waxanda suka shafi jigo da tsarin xiya da tsarin rerawa da takidi da adon harshe da salo da kuma sarrafa harshe. Sannan da yadda yake aiwatar da kalmomi da sauransu.

A vangaren jigo, nazarin ya duba jigogi na waqoqin Makaxa Maidaji waxanda suka haxa da jigon yabo da na zuga da na faxakarwa da kuma na siyasa. Sannan kuma da tubalan ginin jigo waxanda yakan yi amfani da su a cikin waqoqinsa kamar nasaba da addini da ta'aziyya da koxa-kai da kuma habaici.

A wannan nazari an fahimci, Makaxa Sa'idu Maidaji ya fi yawaita shirya waqoqi na yabo da kuma faxakarwa. Ba kasafai yake son gina zambo a waqoqinsa ba.

Haka kuma tsarin waqoqinsa, tsari ne wanda ya shafi makaxi na jagora da masu yi masa amshi a matsayi na 'yan amshi. Ke nan, yakan yi tsari ne na Jagora + qulli +qari + tarbe + karvevveniya/ rakiya +takidi +gindin waqa.

Makaxa Maidaji, makaxi ne wanda yake yawaita kawo dabarar kwalliya da alamtarwa da jinsintarwa da kinaya da qarangiya da karin magana da savi zarce da sauransu. Sannan waqoqi ne da ke tattare da karin harshen Sakkwatanci.

BABI NA XAYA: SHIMFIXA

1.0 Gabatarwa

Makaxa da mawaqa mutane ne waxanda ke “daxa tallatawa tare da tallafa wa bunqasar harshe” (Amin, 2011:119). Masana sun bayyana “waqa ta bambanta daga maganar xabi’a wadda mutane suke yi a yau da kullum” (Xangambo, 2007:40). Ashe ke nan, “waqa wata hanya ce ta sadarwa zuwa ga wata manufa da ake buqatar a fahimta a xai-xayan mutane na al’umma ko a jimlataninta” (Gusau, 2003: viii-xiii).

Waqa wata baiwa ce inda ma’abota zalaqa da hikima da fasaha da gwanintar harshe ke baje kolinsu a cikinta. Idan aka xauki waqoqin baka, za a tarar suna amfani da adon harshe da azanci da sakaya zance da sauran hanyoyin nuna gwaninta. Masana da manazarta adabin Hausa irin su Yahaya (1979) da Umar (1984) da Tajo (1980) da Xangambo (1981, 2007) da Gusau (1983, 1988, 2003, 2008, 2011) da Yahya (1997, 2001) da sauransu sun bayyana waqa magana ce ta hikima wadda ake tsarawa ta hanyar rerawa tare da azanci da fasaha da balaga cikin nuna naqaltar harshe, ana yi ana daidaita furucin daki-daki. Sannan kuma ana amfani da zavavven rauji

cikin karin murya mai jan hankali, ga ta kuma xauke da saqo ayyananne.

Waqa na bunqasa tunanin xan'adam tare da wasa qwaqwalwa da kuma daidaita mahanga da tsinkayar al'umma. Haka kuma waqa na xaukaka alfarma ta xan'adam da kare mutuncinsa tare da qarfafa darajarsa da inganta rayuwar al'umma bisa jumla. Sannan waqa takan zama mai nagarta ko abar kushewa. Dubi yadda aka sarqa tunani tun daga waqoqin dandalin Hausawa na gargajiya a matsayi na misali:

: Mai gambara ina wata kama,
: Mai xan zane ta Baushe,
: Mai xan zane Iya,
: Kaluluwa ta Baushe,
: Shagixai-shagixai na gan ta,
: Mangarai-mangarai na gan ta,
: Karkatai-karkatai na gan ta.
(Gusau, 2003:8)

Ta hanyar waqa ana ajiyar abubuwa da suka shafi rayuwar al'umma cikin harshe mai zalaqa, mai daxi, mai armashi mai nishaxantarwa. Wani lokaci yakan zama mai ban-haushi ko mai ba da takaici ko mai saka juyayi ko kuma mai ba da ban-tsoro. "Ayyukan adabi na waqa suna zama masu armashi, masu havaka tunani kuma masu ratsa qwaqwalwa" (Yahya, 1997: 1-4).

A wannan babi za a yi shimfixa ce ta yin hasashe game da abubuwan da wannan aiki ya qunsa. Sannan a fito da manufarsa da qunshiyarsa da kuma dabaru waxanda aka yi amfani da su wajen gudanar da aiki. Ga bayanin waxannan abubuwa kamar haka:

1.1 Hasashen Bincike

Bisa al'adar mutum ta yin kintacen abin da zai yi yayin da yake qoqarin gabatar da wani abu, yana daga hasashen wannan bincike:

- Tantance tarihin rayuwar shi Sa'idu Maidaji Sabon Birni da gwagwamayar da ya yi a fagen shiryawa da rera waqoqin baka na Hausa;
- Qwanqwance zalaqar Makaxa Maidaji wajen amfani da ilimin addinin Musulunci da yadda Musuluncin yake kallon zamani tare kuma yadda yake cusa rayuwar da take dabaibaiye da shi a cikin tsari na waqoqinsa;
- Gano hanyoyin da Makaxa Maidaji yake bi ta kansu ya gina saqonni, manya da qanana a waqoqinsa tare da rarrabe manyan jigogi na matanonin waqoqi nasa;
- Qididdige yanayin tsari a waqoqin Makaxa Maidaji, musamman yadda yake qullawa da qari a layuka da xiya na

waqoqinsa. Daga nan kuma aka tantance tsarin rerawa da tsarin xa da takidi da sauransu;

- Rarrabe matakai waxanda Makaxa Maidaji Sabon Birni yake sassarqa tunaninsa da dabaru na yi wa harshe kwalliya da kuma zaven kalmomi da aiwatar da jimloli;
- Keve wasu kalmomi na fannu waxanda Makaxa Maidaji Sabon Birni ya jejjefa su a cikin mabambantan waqoqinsa.

1.2 Manufar Bincike

Muhimmin maqasudi na gudanar da bincike a kan wannan mashahurin makaxi wanda ya yi fice bisa zalaqarsa shi ne fito da ainihin fasaharsa quru-quru tare da zaqulo yanayin gwanintarsa da hikimominsa da luggoginsa waxanda ya aiwatar yayin rera waqoqinsa.

Wasu daga cikin manufofi na wannan bincike sun haxa da:

Wane ne Sa'idu Maidaji Rambaxawa Sabon Birni? Ina ne asalinsa? Yaya kuma ya gudanar da rayuwarsa ta quruciya zuwa tsufa zuwa rasuwa?

- Yaushe ne Makaxa Maidaji ya soma waqa? Ko shi makaxi ne na gado ko na haye?

- Waxanne irin waqoqi ne Makaxa Maidaji yake rerawa? Su wa da wa ya yi wa waqoqi? Ko za a iya tantance adadin waqoqin da Makaxa Maidaji ya yi?

- Zuwa yau, waqoqin nawa aka samu na waqoqin Maidaji Sabon Birni?

- Yaya dangantakarsa da yaransa take? Wane ne ya gaji Maidaji Sabon Birni bayan rasuwarsa?

- Bisa waxanne jigogi ne Makaxa Maidaji ya gina waqoqinsa a kansu?

- Yaya tsari na waqoqin Maidaji Sabon Birni yake? Waxanne matakai ne yake amfani da su wajen shirya waqoqinsa?

- Waxanne dabaru na adon harshe ne Makaxa Maidaji ya yi amfani da su wajen aiwatarwa da rera waqoqinsa? Yaya yake zaven kalmomi? Yaya yake shirya jimloli da rassansu a waqoqin nasa?

- Mene ne matsayin Makaxa Maidaji ta fuskar kaifin tunani da basira da zalaqa da sauran dabaru na aiwatar da harshe?

- Shin ko Makaxa Maidaji Sabon Birni ya xauki waqar baka ne a matsayin sana’a ko kuma yana aiwatar da ita ne domin raya adabin Hausa?

- Shin mafi akasari, waxanne tasirori ne al'ummar Hausawa suke samu daga waqoqin Makaxa Maidaji Sabon Birni?

1.3 Farfajiyar Bincike

Farfajiyar wannan bincike ta qunshi fito da hikimomi da kuma bayyana muhimman ayyuka waxanda Makaxa Maidaji Sabon Birni ya gudanar a vangare na adabin baka na waqa. Muhimman abubuwa waxanda binciken ya qunsa sun haxa da:

- Nazari da tsokaci a kan tarihin rayuwar Makaxa Maidaji Sabon Birni, tare da daidaita tarihin rayuwar tasa a yayin bitar ayyuka da suka gabata masu dangantaka da wannan aiki;
- Nazarin jigogi na waqoqin Makaxa Maidaji da ayyana nau'o'insu da tubalan gininsu tare da qoqarin tantance jigogi waxanda ya fi gina waqoqinsa a kansu;
- Bayanin salo da sarrafa harshe da nuna yadda suka shafi waqoqin baka na Hausa. Sannan da bayyana ire-iren adon harshe waxanda Makaxa Maidaji ya yi amfani da su wajen gina waqoqinsa;

- Nazarin tsari, musamman maqunshiyarsa da nau'o'insa, daga nan a yi magana a kan yadda Makaxa Maidaji yake tsara saxara da xiya na waqoqinsa da kuma yadda yake rera su;

- Zaqulo matanoni na waqoqin Makaxa Maidaji Sabon Birni tare da tattara su a waje xaya da za a xora nazarin nan a kansu kuma a dauwana su a matsayin rataye.

1.4 Iyakancewar Bincike

Wannan nazari ne wanda aka gabatar game da Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni da waqoqinsa. Domin haka fagen wannan nazari shi ne adabin waqa ta baka wadda makaxi na gargajiya ya aiwatar, mai basira, mai hikima, mai kuma azanci da zalaqa Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni.

An tattaro kimanin waqoqi saba'in da takwas (78) na Makaxa Maidaji Sabon Birni waxanda aka kafa misalai da su a wannan nazari. Kuma su ne aka yi rataye na biyu da su a juzu'i na biyu na aikin.

Hausawa na cewa 'waiwaye adon tafiya', akwai masana da manazarta waqoqin baka na Hausa irin su Abdulqadir (1975) da Daba (1978) Yusuf (1979) da Umar (1985) da Gusau (2002[a]) da Sheme da wasu (2006) da Bunza (2009) da sauransu, sun inganta ayyukan makaxa irinsu Mamman Shata da Narambaxa da Xanmaraya Jos da

Salihu Jankixi da Hamza Caji da sauransu da dama a fasalin kundayen digiri tun daga na biyu har ya zuwa na uku da kuma a matsayin littattafai bugaggu.

Duk da kasancewar Makaxa Maidaji Rambaxawa shahararren mawaqi ne, har yanzu ba a sami wani fitaccen aiki wanda aka ba da kevantaccen muhalli a kansa ba duk da bunqasarsa da balagarsa da matuqar fasaharsa. Amma na fahimci akwai wasu ayyuka da aka gabatar a matsayin kundaye na digirin farko na Gambo (1990) da Qaura (1993).

Duk da dai wani hanzari ba gudu ba Gusau (1983) a kundin digirinsa na biyu ya yi xan tsokaci a kan rayuwar makaxa Maidaji inda ya kawo wasu daga cikin waqoqinsa na noma kawai tare da sauran makaxan baka na noma da ke a qasar Hausa. Sannan a kundin digirinsa na uku wato Gusau (1988) sai ya sake juyawa ya kalli wasu daga cikin yanaye-yanaye da sigogin makaxan fada na qasar Hausa. A nan ma daga cikin makaxan fada da Gusau (1988) ya tavo akwai Makaxa Maidaji Sabon Birni inda ya kalli waqoqinsa na fada.

Abin lura da kuma dubawa a nan shi ne, duk da an tavo wani qyas da ya shafi Makaxa Maidaji ba zai hana a ware wannan makaxi a yi nazarin waqoqinsa a jimlace.

1.5 Hanyoyin Gudanar da Binciken

A wajen gabatar da wannan bincike an bi dabaru da hanyoyi daban-daban don gabatar da shi. Daga cikin dabarun da aka yi amfani da su wajen tafiyar da binciken akwai:

- An Ziyarci Qaramar Hukumar Sabon Birni dake Jihar Sakkwato da kuma Rambaxawa dake a garin Tara inda yake mahaifar Makaxa Maidaji Sabon Birni. Kuma a nan ne ya gudanar da rayuwarsa, tun daga quruciya har zuwa mutuwarsa;

- An gudanar da nazari cikin xakunan karatu da cibiyoyin bincike da kuma Hukumomin Adana Kayan Tarihi, musamman ma littattafan da hannu ya kai kansu da nufin ba da madosa mai kyau ga wannan aiki. Xakunan karatu na jami'o'i da aka ziyarta sun haxa da na Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya, da na Jami'ar Bayero, Kano, sannan da xakin karatu na Jami'ar Usmanu Xanfodiyo, Sakkwato;

- An kuma halarci Cibiyoyin bincike da suka haxa da Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya ta Jami'ar Bayero, Kano, da Cibiyar Nazarin Hausa ta Jami'ar Usmanu Xanfodiyo, Sakkwato, da sauransu;

- Haka nan kuma an leqa wasu hukumomin adana kayan tarihi da suka haxa da Hukumar Adana Kayan Tarihi ta Jihar Sakkwato da

Hukumar Adana Kayan Tarihi ta Jihar Kano, sannan kuma da Gidan Tarihi na Kaduna (Arewa House);

- An yi amfani da Rakoda da kaset da fayafaye saboda samun sauqin tafiyar da wannan aiki da tabbatar da abubuwan da aka binciko. An samu waxannan kasakasai da fayafayaye ne a Xakin Karatu na Farfesa Sa'idu Muhammad Gusau da Xakin Tattalin Fasahar Baka (O.D.U.) na Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. Wasu kuma daga waxannan kasa-kasai an same su ne a gidan Rediyon Rima, Jihar Sakkwato. Sannan da wasu kasakasai waxanda aka samu a wurin iyalan Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni;

- Har wa yau kuma an ziyarci gidajen Rediyo kamar Rediyon Tarayya Kaduna da Rediyon Rima na Sakkwato da Rediyon Zamfara na Gusau da Rediyon Jihar Katsina da Rediyo Freedom Kano, da kuma Rediyo na Tarayya Lafiya, Jihar Nasarawa;

- An yi amfani da sabuwar hanyar zamani ta Intanet wajen samun bayanai a kan wasu sassa na wannan aiki. Kuma an nazarci kundayen Encyclopaedia Britanica a cikin Intanet da na bugaggun littattafai;

- An kuma saurari wasu kasakasai waxanda wasu masana suka yi hira da Alhaji Sa’idu Midaji Sabon Birni ko da iyalinsa ko kuma waxanda wasu gidajen rediyo suka yi da shi. Wannan duka qari ne a kan hirar da na yi da iyalan nasa a lokacin duganar da wannan bincike.

1.6 Naxewa

A wannan babi an yi hasashe game da fuskar da wannan nazari zai kalla. Daga nan, aka fito da babbar manufar nazari da kuma qananan manufofinsa, sai kuma aka bayyana dalilai na aiwatar da wannan nazari da kuma da’irar da zai xauka. Haka kuma an yi bayani dangane da hanyoyin da aka bi ta kansu aka gudanar da wannan nazari.

BABI NA BIYU : BITAR AYYUKAN DA SUKA GABATA

2.0 Gabatarwa

Waqa, ko da yake magana ce, amma ana yin ta bisa zubin sauti a tsare, a kan kari ba a kara zube ba. Waqa tana zuwa “tamkar yadda zuciya take bugawa, a tsare, ba barkatai ba, tare da maimai na sauti bisa tsari takamaimai” (Yahya, 1997: v).

Haqiqa, Hausawa na cewa ‘sanin wurin bugu shi ne qira,’ marigayi Makaxa Sa’idu Maidaji Sabon Birni xaya ne daga cikin fitattun mawaqan da aka tava yi a qasar Hausa irin su Makaxa Abubakar Akwara da Makaxa Aliyu Xandawo da Salihu Jankixi da Makaxa Ibrahim Narambaxa da Makaxa Mamman Shata da Makaxa Sani Wurno da Makaxa Sani Inyaga da sauransu.

Wannan babi zai waiwayi wasu ayyuka waxanda aka gabatar dangane da Makaxa Maidaji Sabon Birni da kuma sauran mashahuran makaxa ‘yan’uwansa. Daga bisani kuma, babi zai kalli wasu ayyuka waxanda aka aiwatar dangane da waqa da kuma adabin Hausa baki xaya. Daga bisani a cikin wannan babi za a kawo wasu qarin bayanai dangane da Makaxa Maidaji Sabon Birni.

2.1 Tarken Ayyukan da Suka Kawo

Tarihin Rayuwar Makaxa Maidaji

Akwai wasu ayyuka waxanda suka tavo tarihin rayuwa da ayyuka na Sa'idu Maidaji Sabon Birni kamar haka:

Manazarta da masana da masharhanta har yau ba su kammala qwalqwale tsokoki da qasusuwan hikimomi da Makaxa Maidaji ya nuna a cikin waqoqinsa ba. Akwai ayyuka na Gusau (1983 da 1988 da 2005 da 2008 da 2009) da na King (1986) da na Xahiru (1990) da na Kamba & Aliyu (1993) da na Yakasai (1994) da suka yi magana dangane da tarihin rayuwar Makaxa Maidaji.

Da farko, ayyukan Gusau (1983 da 2005) da Yakasai (1994) sun yi tarayya a kan bisa asali, iyayen Makaxa Maidaji sun fara zama ne a garin Tara. Sannan suna xauke da hasashen an haifi Makaxa Maidaji a shekara ta 1938, cikin qauyen Rambaxawa a Qaramar Hukumar Sabon Birni da ke qasar Gobir ta Jihar Sakkwato. Sunan Makaxa Maidaji na ainihi wato na yanka shi ne Sa'idu.

Wannan bincike ya tabbatar da gundumar Tara tsohon gari ne mai babban tarihi, wannan gari ya bunqasa sosai tun da nisan wannan gari ya kai kimanin kilomita goma sha biyu (12) gabas da Sabon Birni.

Garin Tara shi ne inda Hakimi yake zama, wanda yake a matsayin sarkin garin. Sunan Sarautar garin Tara ita ce ‘Saraki Tara’. Sarkin Tara na yanzu shi ne Alhaji Rabi’u Saraki Tara wanda aka yi naxin sarautarsa a ranar 20 ga watan Agusta, 2005.

Rambaxawa na qarqashin gundumar Tara ne, a Qaramar Hukumar Sabon Birni ta Jihar Sakkwato. Garin Rambaxawa na da nisan kilomita uku (3) da garin Tara. Garuruwan da za a shige zuwa garin Rambaxawa su ne: Daga garin Sabon Birni ⟶ Katsira ⟶ Matsewuya ⟶ Sulmawa ⟶ Zaqi Ganga ⟶ Tsauna ⟶ Xangari ⟶ Tudun Wada ⟶ Rambaxawa. Makaxa Maidaji Sabon Birni ya gudanar da mafi akasarin zaman rayuwarsa ne a duniya a Rambaxawa.

Yakasai (1994) ya jaddada batun nan da ke nuni da kowace al’umma a faxin duniyan nan tana da fasalin fasahar harshenta wanda ya kevanta gare ta. Waqoqi kuwa, suna daga kevavvun sinadarai waxanda akan yi amfani da su domin a isar da saqo ko manufa bisa tadodin al’umma. Daga bisani, Yakasai (1994) ya kawo ire-iren saqonnin da waqoqin Makaxa Maidaji suke xauke da su. Yakasai (1994) ya qara da bayyana Makaxa Maidaji mutum ne wanda yake nuna karimci a cikin waqoqinsa, kuma waqoqinsa suna bunqasa

adabin al'ummar Hausawa da kalmomi masu kwaranya da tasirin gargajiya. Sannan Yakasai (1994) ya fito da fasahar Makaxa Maidaji ta nuna buqatunsa a cikin kinaya tare da sakaya zance a cikin waqoqinsa. Daga bisani, Yakasai (1994) ya bayyana Makaxa Maidaji da zama mutum mai girmama sauran 'yan'uwansa mawaqa.

Haka zalika, wannan bincike ya gano ana yi ma Makaxa Maidaji da laqabi da sunan Xanbugaje a lokacin da yake qarami da kuma Maidaji. Amma daga bisani sunan Maidaji Sabon Birni ya zame masa game-gari wanda duniya ta san shi da shi. Har wa yau Gusau (1983: 133-134) ya qara da cewa:

> Dalilin kiran sa Maidaji shi ne, a lokacin rayuwar mahaifinsa suna zaune ne a garin Tara. Rigima ta faxace-faxace ta haddasu tsakanin mutanen garin Tara inda aka yi ta tashi ana barin garin, bayan kuwa har sun yi shuka. Saboda haka, Mahaifinsa ya ce shi kam ba zai bar shukarsa ta lalace a banza ba, sai dai su koma cikin gonarsu su yi mazauni. A gonar ya gyara wurin zama, suka zauna tare da sauran 'yan'uwansa cikin zaman 'me gari zai waya'. To, bayan da aka koma wannan gidan gona ne aka haifi Makaxa Maidaji wanda dama an tafi da cikinsa yana tsoho. Daga nan, sai mahaifinsa ya ce an sami "Maidaji" wato xan gidan gona. A wannan gidan gona Makaxa Maidaji Sabon Birni da iyayensa suke zaune har ya girma.

Sannan wannan bincike ya tabbatar da sunan mahaifinsa Muhammadu Dango wanda aka fi sani da (Maigari). Sunan mahaifiyar Makaxa Maidaji Hauwa'u wadda aka fi sani da (Jimma). An fi sanin kakan Makaxa Maidaji da sunan Xantsara.

A qiyasi, Marigayi Muhammadu Dango (Maigari) ya rasu a lokacin Makaxa Maidaji yana kimanin shekaru talatin (30) a duniya wato wajejen shekara ta 1968. Sannan kuma wannan bincike ya gano cewa Makaxa Maidaji su shida (6) ne a gidansu, kuma yana da yayye guda biyu, ke nan shi ne na uku a gidansu:

a) Alhaji Muhammadu Muhammad Dango (Marafa)

b) Alhaji Musa Nadada Muhammad Dango

c) Alhaji Sa'idu Muhammad Dango (Maidaji)

Yana kuma da qannai guda uku:

a) Alhaji Shu'aibu Muhammad Dango

b) Alhaji Adamu Muhammad Dango (Xan Malam)

c) Alhaji Abdullahi Muhammad Dango (Xan Barno)

Wannan bincike ya qara gano cikin nufar Allah, Makaxa Maidaji, yana da matan aure guda uku. Waxannan mata, har ya rasu suna nan raye kuma yana tare da su. A waqoqinsa da dama yakan ambaci sunayen waxannan mata nasa musamman a waqar Innar Gobir

inda yake nuna godiyarsa bisa abun alheri da ake yi wa iyalan nasa. Sunan matan kuwa su ne:

a) Ta-Allah

b) Mai Kuxi

c) ‘Yar Maigoro.

Wannan bincike ya qara gano cewa Allah ya wadata Makaxa Sa’idu Maidaji da ‘ya’ya guda takwas maza huxu mata huxu waxanda har ya rasu suna raye. Sunayen ‘ya’yan kuwa su ne:

a) Adamu Sa’idu Maidaji (Baciri)

b) Sabi’u Sa’idu Maidaji

c) Abdurrahman Sa’idu Maidaji

d) Muhammadu Sa’idu Maidaji (Rani)

e) Zulaihatu Sa’idu Maidaji (Zali)

f) Salamatu Sa’idu Maidaji (Salmu)

g) Hauwa’u Sa’idu Maidaji (Barno)

h) Hadiza Sa’idu Maidaji (Taladi)

Har ila yau, wannan bincike ya gano akasarin yaran qungiyar Makaxa Maidaji jininsa ne, tun da dama gidansu tun asali, gidan waqa ne. Dahiru (1990: 4) ya bayyana cewa:

Fitar Makaxa Maidaji Sabon Birni waqa ta farko, ya tafi shi xaya ne, waqar da ya fara rerawa, ita ce wadda ya yi a lokacin da wani manomi ya yi gayyar noma a qauyensu. Bayan an yi wata gayyar sai ya tafi da wasu yara guda biyu suna yi masa kixa shi kuma yana waqarsa.

Makaxa Maidaji ya bayyana alaqarsa da ‘yan qungiyarsa a hirarsa da Dr. Alhassan, B. S. Y. kamar haka:

B.S.Y. Alhassan: Na ji in kana waqa kana cewa ‘ya’yana. Duka masu yi maka amshi xiyanka ne?

Makaxa Maidaji: Eh! Duka xiyana ne sai wannan babban wanmu ne, sai wannan tsohonmu dukkansu suna amshi. Shi wannan tsohon namu ko da nih hwara kixi tare da shi nih hwara. Waxanda nihwara da su kuma mutum biyu ko babu su. Biyu daga qannena sun kama makaranta.

B.S.Y. Alhassan: Yanzu wannan sana’a ko cikin masu yi maka amshi yanzu akwai wani wanda yake sha’awar ya karva gare ka da ganinka lokacin da kake ganin ya kamata ka huta. Kuma ya sunan shi?

Makaxa Maidaji: Eh! Akwai domin shi kan shi ya hwara nashi waqoqi. Sunan shi Hana.

Makaxa Maidaji yana cikin makaxa waxanda suke aiwatar da waqoqi a cikin qungiya wadda ta haxa da jagora da ‘yan amshi da kixa da sauran yara masu xaukar kayan kixa. Daga cikinsu akwai:

a) Alhaji Ibrahim (Tanko); qanen mahaifinsa ne; baransa ne kuma maroqinsa

b) Alhaji Maigari; yayansa ne

c) Alhaji Ibrahim Musa (Hana); babban xan Makaxa Nadada

d) Alhaji Adamu (Baciri); babban xan Makaxa Saidu Maidaji

e) Alhaji Adamu (Abara);

f) Alhaji Adamu (Xan Malam)

g) Alhaji Usman (Salau);

h) Alhaji Garba (Na-Maiqosai);

i) Alhaji Garba (Abbu)

j) Alhaji Ummaru (Dogo);

k) Alhaji Abdullahi (Xan Barno);

l) Alhaji Shu'aibu

Alhaji Ibrahim Musa Nadada (Hana) babban xa ga Makaxa Musa Nadada, *Daudun Kixa* ko kuma *Galadiman Kixa* na Makaxa Sa'idu Maidaji shi ne wanda ya gaji kixa a hannun Makaxa Maidaji Sabon Birni a halin yanzu.

Makaxa Hana ya bayyana cewa:

> Makaxa Maidaji mutum ne mai kyakkyawar alaqa da yaran qungiyarsa, sun zauna, zama na 'tsintsiya maxaurinki xaya'. Yana zama tare da su cikin koyi na tarbiyya da girmamawa a tsakaninsu, duk da idan ka gan

> su yadda ka san abokai. Idan ba gaya wa mutum aka yi ba, ko kuma in ba ya sani ba, ba za a ce yaransa ne ba. Ko da yaushe, suna zaune wuri guda, abin dai gwanin ban sha'awa, duk da cewa wasu daga cikin yaran nasa yayyensa ne. Babu gardama a tsakaninsu. Wannan ya sa Makaxa Hana yake cewa shi kam yana da yaqinin cewa an haifi Makaxa Maidaji da waqa ne domin ya yi ta.

Gusau (1988) ya kalli waqoqin makaxan fada waxanda ke cikin tsohuwar jihar Sakkwato; da suka qunshi jihar Zamfara da jihar Kebbi da jihar Sakkwato ta yanzu. Haka kuma dai Gusau (1988) ya dubi waqoqin ne ta yin la'akari da sigogi waxanda ya kamata a ce kowace waqa ta fada ta kasance tana qunshe da su, da yanaye-yanayen waxannan waqoqi. Wannan bakandamen aiki na Gusau (1988) abokin tafiyar wanda za a gabatar ne, wato dai 'da na gaba akan ga zurfin ruwa'.

Domin wannan bincike ya kandamo akasarin makaxa da mawaqan baka na Hausa aqalla guda talatin da uku (33) ne da waqoqinsu, tun da mafi akasarin makaxan baka na Hausa sun fito ne daga yankin tsohuwar jihar Sakkwato.

Aikin Gusau (1988) yana da alaqa da wanda za a gabatar dalilin kuwa shi ne, daga cikin mawaqan da Gusau (1988) ya tavo har da

Makaxa Maidaji Sabon Birni. Sauran makaxan da Gusau (1988) ya kawo kuma sun haxa da Makaxa Salihu Jankixi da Makaxa Sa'idu Faru da Makaxa Ibrahim Narambaxa da Makaxa Aliyu Xandawo da Makaxa Nadada Sabon Birni da Makaxa Abubakar Akwara Sabon Birni da da Makaxa Musa Xanqwairo da Makaxa Sani Mamman Inyaga da Makaxa Abdurrahman Sarkin Kotso, Kano da sauransu.Wannan binciken da za a gudanar ya taqaita ne a kan waqoqin Makaxa Maidaji bisa tubalin nazarin waqar baka.

Har wa yau dai tamkar yadda Hausawa ke cewa 'in kixa ya sake, rawa sai ta sake, Gusau (1983) ya gudanar da wani bincike inda ya bayyana ma'ana da asalin kalmar noma tare da bayyana fasalin damuna da yanayin qasar noma da kayan aikin gona da rabe-raben noma da ire-iren abubuwan nomawa da kuma rabe-raben manoma.

Haka kuma, an bayyana muhimmancin noma ga rayuwa a wannan aiki. Daga bisani, a wannan aiki an bayyana waqoqin noma da kuma makaxan noma na baka dangane da jigoginsu da zubi da kuma salo da sarrafa harshen waqoqin.

Daga cikin makaxan noman da aka kawo a wannan aiki har da Makaxa Sa'idu Maidaji. Sauran makaxan noma da Gusau (1983) ya ambata a bincikensa sun haxa da Alhaji Abu Xan Kurma da Alhaji

Wakkala Gusau da Sarkin Taushi Salihu Jankixi da Alhaji Mamman Xan Anace da Alhaji Musa Xanqwairo da Umaru Mai Xan Hannu da Umaru Daudun Kixa da Mamman Yaro Hore da Audu Faru da Bawa Sakkarawa da Na-Mallam Mahuta da Ladan Mai Ganga da Isa Xan Makaho da Illon Kalgo da kuma Audu Wazirin Xanduna. Gusau (1983:133) ya bayyana:

> Makaxa Maidaji bai yi ilmin boko ba. Sannan cikin matakan neman iliminsa, Makaxa Maidaji ya halarci makarantar yaqi da jahilci tun farkon kafa makarantar a qauyensu, duk da bai daxe a ciki ba.

Tamkar faxar Hausawa ‘Himma dai, ba ta ga raggo’ amma bisa al’adun qasar Hausa, Makaxa Maidaji ya yi karatun Al’qur’ani ne da sauran littattafan addinin Musulunci. Wannan karatu ya ba shi makamar yin ibada da kaifafa masa tunani da basirar yin amfani da harshensa na Hausa. Makaxa Maidaji Sabon Birni ya yi tafiye-tafiye don neman ilimi inda ya ziyarci Mai Lalle da Tsamaye.

> Garuruwa da ya ziyarta domin neman ilimi, an sheda Makaxa Maidaji bai yi yawon bara ba. Shi da abokansa, mafi akasari, idan suka yi tafiya zuwa wani gari wajen neman ilmi sukan sauka ne a wajen Sarkin Garin ko

> Hakimi wanda suka tabbata yana da abinci. Za su yi yarjejeniya da mai masaukinsu da ya dinga ciyar da su. Su kuwa, su riqa yi masa noma. Idan sun dawo daga aikin gona, sai kuma su tafi makarantar allo da ke garin domin su yi karatunsu (Gusau, 1983:133-135).

Makaxa Maidaji tun yana qarami yake da himma da qwazo kan duk abin da ya sa gaba domin ya sami biyan bukata mai amfani. Mutum ne mai sha'awar bunqasar al'ummar qasar Hausa a ko da yaushe 'Allah ya ce tashi in taimake ka'. Saboda haka, aikin Gusau (1983) zai taimaka wajen samun waqoqin noma na Makaxa Maidaji.

Wata sabuwar magana a nan ita ce, Xahiru (1990) ya gudanar da bincike a kan Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni da Waqoqinsa. A wannan aiki, an bayyana tarihin rayuwar Maidaji da yadda Maidaji yake shirya waqoqinsa da hanyoyin da yakan bi wajen matakan shirya waqoqinsa da kuma tarihin wanda zai yi wa waqa. Xahiru (1990) ya kawo bayanin jigon waqoqin Maidaji daga bisani kuma aka bayyana salo a waqoqin Maidaji da kuma abubuwan da jama'a za su koya a cikin waqoqin Maidaji.

Gusau (1983 & 2005) da Xahiru (1990) da Yakasai (1994) sun yi tarayya a kan cewa tun Makaxa Sa'idu Maidaji yana xan shekara

aqalla goma sha biyu (12) ya bar gidansu ya koma gidan yayansa Malam Musa Nadada da zama yana barance.

> Makaxa Maidaji ya riqa bin yayansa Makaxa Nadada suna yawon kixa da waqa a gidajen sarakunan qasar Gobir. Ko da ya cika shekara biyar (5), a qarqashin jagorancin yayansa Makaxa Nadada, aka naxa Makaxa Maidaji matsayin *Daudun Kixa* wato *Galadiman* Makaxa Nadada ke nan (Gusau, 2005:171-174 da Xahiru, 1990: 2-7).

To amma ‘ana dara ga dare ya yi’ domin aikin Xahiru (1990) duk jirgi xaya ya kwaso aikinsa da na wannan kundi, amma inda ‘gizo ke saqar’ kuwa shi ne, Xahiru (1990) ya aiwatar da bincike ne tun Makaxa Maidaji yana da rai, wannan nazari kuma ya gano cikakken tarihin Maidaji ne dangane da iyalansa da ‘yan’uwansa da kuma gwagwarmayar da ya sha a rayuwarsa.

Wato dai, wannan bincike ya kawo nasabar Makaxa Maidaji tun daga haihuwarsa har zuwa lokacin da Allah, tabara wa ta’ala, ya karvi rayuwarsa. Wato dai akwai bambancin shekaru aqalla ashirin da xaya (21) daga lokacin da Xahiru (1990) ya aiwatar da aikinsa da kuma na wannan kundi.

Haka zalika Hausawa na cewa ‘in ka daka rawar wani da sannu ka rasa turmin daka taka’, dalilin faxar haka kuwa shi ne Xahiru (1990) ya yi nazarin waqoqin Makaxa Maidaji ne aqalla guda ashirin da huxu (24) ne. Wannan kundi kuwa ya qunshi waqoqin Makaxa Sa’idu Maidaji aqalla guda saba’in da takwas (78) ne. Har wa yau dai, kasancewar Xahiru (1990) ya gudanar da bincike a matakin neman digiri na farko ne ya sa aikinsa ya taqaita. Amma tun da wannan kundin bincike ne a matakin neman digiri na biyu, akwai buqatar qara faxaxa bincike game da wannan mashahuri kuma ‘gwani na gwanaye’ a cikin zaratan makaxan baka na Hausa.

Sannan kuma, binciken xauke yake da hujjoji domin jama’a su amfana da irin fasahar da ke tattare a cikin waqoqin Makaxa Maidaji da ke kwaranya birjik a doron qasar nan tamu ta Hausa.

An qalailaice waxannan waqoqi na Makaxa Maidaji ta hanyar amfani da matakan nazarin waqar baka ta Hausa inda aka bayyana salsalar waqoqin da jigoginsu da kuma salo da sarrafa harshen waqoqin.

Har wa yau, Gusau (2005) ya kawo bayanin rayuwar mawaqa da makaxan baka na Hausa tun daga haihuwa da quruciya, har zuwa shahara a fagen waqa na aqalla makaxa da mawaqa guda talatin da

uku (33). Daga bisani kuma, Gusau (2008[a]) ya bayyana adabin baka tamkar hoton rayuwar al'umma ne da ke bayyana hanyoyin fasahar ta wajen gudanar da rayuwa. Sannan kuma Gusau (2008[a]) ya qara da bayyana asalin mazauna qasar Hausa da muhimman garuruwan qasar Hausa da suka haxa da Sakkwato da Gobir da tsohuwar daular Zamfara da Zazzau da Kano. Sannan ya bayyana kayan kixa na Hausa da ire-irensu. Haka kuma Gusau (2008[a]) ya kawo cikakken bayani dangane da asaliyya da tasowar makaxan baka na Hausa da yanaye-yanayensu da kuma halayya da nau'o'in waqoqin baka na Hausa. Har ila yau, ya yi bayanin turke (jigo) dalla-dalla da nau'o'insa, tun daga ma'anarsa har zuwa muhallinsa da kuma matakan da akan bi wajen fitar da jigo da nau'o'insa (wato turke da warwararsa da bayanin turke a taqaice da kuma muhallinsa).

A cikin aikin Gusau (2009) ya zavo matanonin waqoqin makaxan baka na Hausa aqalla guda xari da arba'in da uku (143). An fara kawo waqoqi na Makaxan fada guda tamanin da tara (89) sannan aka kawo sauran hamsin da uku (53) na mawaqa game-gari.

Daga cikin waxannan waqoqi guda tamanin da tara (89) har da na da Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni inda aka kawo waqoqinsa guda takwas (8). Cikin waqoqin takwas (8) da aka zayyano akwai

waqar ‘Balaraben sarki’ da waqar ‘Uban makama uban gardaye’ da ta ‘Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa’ da waqar nan ta ‘Kai ab bahagon gulbi’ da waqar ‘Bawa na Jekadiya’. Akwai kuma waqar ‘Ginshimin Yari Magajin Magaji’ da kuma waqar ‘Dogo na Jekadiya’, sannan aka rufe da waqar nan tasa ta noma wato ‘Na yi hamdala nai shukura da godewa.

Sauran makaxa da mawaqa waxanda Gusau (2009) ya kawo waqoqinsu akwai Abubakar Akwara, Sabon Birni inda aka kawo waqoqinsa guda biyu (2). Sai kuma Makaxa Salihu Jankixi Sarkin Taushi, Gusau/ Sakkwato inda aka kawo waqoqinsa guda huxu (4).

Akwai kuma waqoqin Alhaji Aliyu Xandawo, Argungu/ Yawuri da na Makaxa Ibrahim Narambaxa Tubali, Isa waxanda suka qunshi ‘Amadun Bubakar gwarzon Yari’ da waqar ‘Mijin Nana Yalwa xan Sanda’ da waqar nan ta ‘Shiri bajimin Mamuda’ da dai sauransu. Duk da haka kuma, Gusau (2009) ya kawo waqoqin Makaxa Musa Xanqwairo, Maradun, guda goma sha biyar (15).

An kawo waqoqin Makaxa Sa’idu Faru, aqalla guda shida (6) da na Makaxa Sani Aliyu Xandawo Yawuri shi ma guda shida (6). Gusau (2009) bai tsaya nan ba, ya kawo waqoqin Alhaji Mamman Shata Katsina aqalla guda goma sha shida (16) da na Makaxa Alhaji

Xanmaraya Jos guda biyu (2). Da ta ‘Xan’adam mai wuyar gane hali’ da kuma ta ‘To Bisimilla Allah Ta’ala’. Har wa yau dai, littafin *Diwanin Waqoqin Baka* (2009) tattare yake da waqoqin Babangida Kakadawa, Gusau guda huxu (4) da na Makaxa Kassu Zurmi, guda uku (3) da waqoqin Makaxa Muhammadu Bawa Xan’anace Gandi, guda uku (3) da kuma na Makaxa Aliyu Gadanga inda aka kawo waqoqinsa aqalla guda biyar (5) da dai sauran waqoqin mashahuran makaxa da mawaqa da dama na qasar Hausa.

Makaxa Hana ya nuna wa mai bincike lambobin girmamawa da Makaxa Maidaji ya samu duk da ya bayyana cewa wasu daga cikin lambobin girmamawar ruwa ya vata su amma an samu biyu daga ciki. A ranar 9 ga watan Agusta shekarar 1986 Gwamnatin Jihar Sakkwato a lokacin jagorancin Gwamna Kanar Ahmad Muhammad Daku (1985-1987) ta ba shi babbar lambar yabo bisa qoqarinsa wajen wayar da kan al’umma dangane da manufofin gwamnati tare da havaka da kuma bunqasa harshe da adabi da al’adun Hausawa a harabar gidan Rediyon Rima, da ke jihar Sakkwato.

> Ga abin da aka bayyana tare da sa hannun gwamnan kamar haka: Certificate of Merit Award to Maidaji Sabon Birni in appreciation of his contribution towards public

enlightenment on government programmes and Cultural development in Sokoto State.

Daga bisani kuma a ranar 5 ga watan Janairu shekara ta 1996 aka sake karrama shi da wata lambar yabo a qarqashin jagorancin Gwamna Navy Captain Abdurrashid Raji (1996-1998) bisa qoqarinsa wajen bunqasa qudurorin gwamnati da tare da havaka ayyukan harshe da adabi da al'adun Hausawa a Gidan Rediyon Rima, da ke jihar Sakkwato.

Ita ma ga abin da ake cewa a cikin hatimin lambar yabon:

Certificate of Merit Award by Sokoto State Broadcasting Corporation to Maidaji Sabon Birni in recognition of services, outstanding Contribution and Commitment to the progress of the corporation.

"Da ma babu wata rayuwa da za ta wanzu a bangon duniya face ta xanxani azabar mutuwa" (Bunza, 2009: 30). Allah mai girma da xaukaka ya qara tabbatar mana da haka a cikin Alqur'ani mai tsarki:

Kowane rai mai xanxanar mutuwa ne. Kuma ana cika muku ijarorinku kawai ne a Ranar Qiyama. To, wanda aka nisantar daga barin wuta, kuma aka shigar da shi Aljanna, to, lalle ne ya tsira. Kuma rayuwar duniya ba ta zama ba face jin daxin ruxi (Alqur'ani mai girma, Sura ta 3:185).

Shi kansa Makaxa Maidaji Sabon Birni, a waqarsa ta *'Uban Jekadiya'* wadda ya yi wa Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Ummaru Na-Allah (1957-1966) yana cewa:

Jagora : Allahu duniya mui ta abin da za mu yi,
'Y/Amshi : Ba nan za mu tabbata ba.
Jagora : Ni ba abin da yay yi min zahi da duniya sai,
'Y/Amshi : Allah da yas shira mutuwa yag gama da shexa.
Jagora : In hairan kake,
'Y/Amshi : Ka iske hairan yana jiranka.
Jagora : In sheri kake,
'Y/Amshi : Ka iske sheri na jiranka.
Jagora : Lalle abin da ka haihwa,
'Y/Amshi : Du kana ishewa,
: Uban Jekadiya,
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin magatakarda.
(Makaxa Maidaji : Xahiru, 1990: 103)

Har wa yau, Makaxa Maidaji Sabon Birni, a waqarsa ta *'Na zo ganin bajinin Ali'* wadda ya yi wa Sarkin Tsibirin Gabas, Alhaji Ali Kambakarwa, Makaxa Maidaji Sabon Birni yana cewa:

Jagora : Gobirawa kui muna gahwara,
'Y/Amshi : Alhaji ban kwana ya kai,
: Ba mu san ta rai ba ga duniya,
: Na zo ganin bajinin Ali,
: Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya za ka lahiya.
(Maidaji: O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL 1/375 1/4)

Har wa yau dai, a waqar *'Allah za ni roqonka'* ta tsohon Gwamnan jihar Sakkwato, Alhaji Garba Nadama, Makaxa Maidaji Sabon Birni ya isar da ta'aziyyarsa kamar haka:

Jagora : Ko can duniya haka tag gada inji mai turu,
'Y/Amshi : Ka san duniya daxa ba mai hurce iyakatai,
: Allah za ni roqonka,
: In yi biyag gwamna mai girma.
(Maidaji: O.D.U Catalogue, 1985. Tape No. AL 0/52 1/6)

Iyalan Makaxa Maidaji sun bayyana wa mai bincike cewa a shekara ta 2000 bayan zaven mulkin farar hula na shekarar 1999, a lokacin da aka zavi gwamna Alhaji Attahiru Bafarawa na farko wanda ya yi mulki tsakanin shekara ta 1999 zuwa ta 2007, Makaxa Maidaji ya kamu da rashin lafiya. A lokacin da gwamna Attahiru Bafarawa zai kawo ziyarar farko qaramar Hukumar Sabon Birni aka aiko wa Makaxa Maidaji gayyatar tarbon gwamna. A lokacin, Makaxa Maidaji yana fama da cutar gizo-gizo wadda ta kama shi a qafa.

Yana cikin wannan cuta ne ya je garin Sabon Birni inda suka tarbi gwamna Alhaji Attahiru Bafarawa. A faxarsu bayan dawowarsu daga wannan tafiya ne ba da daxewa ba sai ciwo ya yi tsanani ga Makaxa Maidaji inda suka kai shi asibiti aka auna shi likita kuma ya

ce musu wannan cuta gizo-gizo ta koma cikin cikinsa ne inda ta kama mashi hanta.

Makaxa Maidaji ya rasu ranar asabar, cikin Watan Nuwamba, shekara ta 2000 lokacin kaka ana cikin girbin hatsi. Yawanci lokacin girbin gero ana yin sa a qasar Sakkwato yawanci a watan goma sha xaya na shekara wato watan Nuwamba ke nan.

Sannan hirar da wannan bincike ya yi da babban xan Makaxa Maidaji, Alhaji Adamu Baciri, ya jaddada cewa:

> A wannan shekara ta 2011, ta zama shekara goma sha-xaya (11) da qaurar mahaifinsu zuwa ga rabbil izzati. Da wannan hasashe ne bincike yake ganin Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni ya rasu ne a shekarar 2000 a cikin watan Nuwambar shekarar. Allah ya jiqansa da rahamarsa.

'Kar dai a yi tuya a manta da albasa' yana da muhimmanci qwarai a duba wasu ayyuka da aka yi kan waqoqin baka domin samun makamar inda kowane aiki ya fuskanta da kuma matsayinsa a fanni na ilimi. Wasu daga manazarta adabin Hausa sun aiwatar da rubuce-rubuce dangane da wasu xaixaikun makaxa da mawaqan baka.

Daga cikinsu akwai ayyuka na Dorson (1960) da Goody (1960) da Amos & Goldstein (1975) da Abdulqadir (1979) da Yusuf (1979)

da Umar (1985) da Gusau (2002) da Emilder (2003) da Daba (2006) da Bunza (2009) da sauransu.

Ayyukan rayuwar waxannan nagartattun makaxa da mawaqa, ta amfani da azancinsu da kuma gwanincewarsu ta hanyar da ta dace, babu shakka, za a sami abin tsinta daga fasaharsu da kuma balagarsu.

Domin sukan "faxakar ne a kan rayuwar al'umma a cikin harshe mai zaqi, mai karsashi, tare da alkinta manufa ko saqo ingantacce" (Abdulqadir, 1976: 1).

Waxannan nazarce-nazarce masu yawa da aka gabatar a kan waqoqin baka na Hausa an aiwatar da su ne domin neman shaidar karatu a matakai daban-daban, wasu kuma an wallafa su ne domin tallafa wa vangaren ilimi a matsayin bugaggun littattafai ko maqalu ko mujallu. Sauran ayyuka waxanda suke da dangantaka ta kamanci ko bambanci da wannan aikin sun haxa da:

2.2 Kundayen Bincike

Masu iya magana dai na cewa 'ba a hawa sama sai da tsani', kundayen binciken da aka gudanar a vangaren nazarin waqar baka na Hausa suna da yawa bisa fannoni mabambanta. Yawanci kamar

yadda aka bayyana, kundayen bincike ne na neman digiri tun daga na farko (B.A.), da na biyu (M.A.), har zuwa na uku (Ph. D).

Kowane manazarci akwai alqiblar da ya fuskanta dangane da aikin da ya gabatar. A cikin waxannan ayyuka an yi nazari da sharhin samuwa da bunqasar fitattun waqoqin baka ne bisa fannoni daban-daban. Idan an xauki aikin nan na King (1967) ya kawo cikakken bayani dangane da kaxe-kaxe a fadar Sarkin Katsina. Haka kuma, binciken ya fi mayar da hankali a kan sautin kixa da hawa da saukar murya a cikin xiyan waqoqin baka na Hausa ne. Yayin da King (1967) ya yi bayanin kaxe-kaxe a fadar Katsina, shi kuma Edward (1971) ya yi bayani kan waqoqin makaxan fada a Kano, inda ya duba siffofinsu da xabi'unsu da yanayin rayuwarsu, da ire-iren kayan kixansu, da harkokin da suke gudanarwa musamman gaisuwa da nau'o'inta.

A wajen aiwatar da binciken Edward (1971) ya tavo alaqar da ke tsakanin sarki da makaxinsa da irin yadda mawaqa suka rataya ga sarakunan da suke yi wa waqoqi. Babbar manufar da Edward (1971) ya gina nazarinsa a kanta ita ce, yin tsokaci kan waqoqin fada dangane da hawa da saukar murya da sautin kixa da kayan kaxe-kaxe da ake amfani da su, da tushensu da muhallan kaxa su, musamman a fadar Sarkin Kano. Domin haka ayyukan King (1967) da na Edward (1971),

za su qara haske ga wannan aikin musamman inda aka waiwayi nau'o'in waqoqin baka na Hausa kuma binciken zai mayar da hankali ta kallon fadar Gobir ta Sabon Birni.

'Bikin Magaji dai ba ya hana na Magajiya' domin manazarta irin su Furniss (1977) da Umar (1984) Xan'iya (1997) da Satatima (2009) kuwa sun gudanar da nazarin su ne ta kallon jigo da awon baka da salo da sarrafa harshe tare da fito da muhimmancin waqoqin baka ga al'ummar Hausawa.

Furniss (1977) ya gabatar da tasirin zamanci a kan waqoqin baka na Hausa inda ya ba da matuqar muhimmanci a kan jigo da salo da hikima a bakin mawaqa na Hausa, musamman na qasar Kano. Dangane da wannan bincike na Furniss (1977) wanda ke da cikakkiyar alaqa da wanda za a aiwatar, duk da wannan kundi ya kalli salo da kuma jigo a waqoqin Makaxa Maidaji, shi kuma ya kalli jigo da salo ne ta vangaren mawaqa na qasar Kano da kuma hikimominsu. Haka kuma manazarcin ya gudanar da rubutunsa ne a kan sigogin rubutattun waqoqin zamani, wannan kundi kuma ya faxo ne a vangaren waqoqin baka na Hausa da sigoginsu har ma da fasahar da ke cunkushe a cikin waqoqin Makaxa Maidaji Sabon Birni.

Yayin da Furniss (1977) ya aiwatar da aiki a kan tasirin zamananci a waqoqin baka, shi kuma Umar (1984) ya rataya aikinsa ne a kan alamtarwa (alamci) a waqoqin fada na Hausa. Ya yi hasashe ne kan alamtarwa a waqoqin fada na Hausa da kuma tsokaci dangane da yadda za a fito da yanayi ko alamomin halayyar zaman jama'a a waqoqin fada. Ya kuma duba yanayin tsarin zaman Hausawa da karkasuwarsu zuwa qungiyoyi.

Bugu da qari kuma, Umar (1984) ya mayar da hankalinsa a kan yadda ake sarrafa harshe da ma'ana, musamman dangane da alamomi guda biyu da suka fi shafar rayuwar zaman jama'a waxanda ya kira da 'ruwa da giwa' inda ya fito da amfaninsu da ayyukansu da yadda ake tadawuli da su a rayuwar Hausawa. Wannan bincike na Umar (1984), ya shafi wannan aikin ta fuskar tsokaci da sharhi a kan alamtarwa tare da taqaita misalai daga waqoqin Makaxa Maidaji Sabon Birni, inda shi kuwa, ya bayar da kandamin bayani ne game da alamtarwa tsagwaronta.

Shi kuma Satatima (2009) ya bayyana samuwa da bunqasar waqar baka na xarsashin zuciya. Satatima (2009) ya bayyana cewa waqoqin baka na xarsashin zuciya suna aukuwa ne a sanadiyyar aukuwar wani abu ga su makaxa da mawaqan wanda ke haddasa

samuwar ire-iren waqoqin. Waxannan waqoqi sun haxa da waqar Xan'ali ta Muhammadu Bawa Xan'anace da waqar dam na bakalori ta Musa Xanqwairo da waqar Kurkunu ta Sani Sabulu da waqar Zawara ta Sani Xanbaldo da waqar mu fatattaki 'ya'yan Baqi ta Ali Makaho da dai sauransu da dama. Saboda haka, Satatima (2009) ya kawo qwararan bayanai game da ginuwar waqoqin xarsashin zuciya da yanayinsu da kuma qananan turakun gina waqoqin. Satatima (2009) ya kawo waqoqin gargaxi da na nasiha da na juyayi da na fatan alheri da na ta'ziyya da na wayar da kai da na zambo da kuma na soyayya. Aikin Satatima (2009) tattare yake da zubin xiyan waqoqin na xarsashin zuciya da bayanin yawan layuka a xiyan waqoqin da kuma tsarin rerawa da takidi. Kuma aikin ya qunshi zavavvun waqoqi ne na xarsashin zuciya, inda aka yi sharhinsu.

Har ila yau, Xan'iya (1997) ta dubi adon harshe a dukkan vangarorin rubutaccen adabi. Xan'iya (1997) ta gabatar da adon harshe bisa ma'anarsa da kuma rabe-rabensa a Hausa tun daga qarni na 17 zuwa na 20. Daga bisani kuma ta danganta adon harshe a cikin rubutattun waqoqi da qagaggun labarai da kuma wasan kwaikwayo. Wannan bincike na Xan'iya (1997) zai qara haske a wannan kundi musamman wajen fito da ma'anar adon harshe da kuma rabe-rabensa.

Duk da cewa wannan aikin zai yi magana ne a kan adon harshen waqoqin makaxa Maidaji, ke nan, a nan gizo ke saqar. Domin ita ta ta'allaqa bincikenta ne ga adabin zamani ta fuskar rubutacciyar waqa da qagaggun Labarai da kuma wasan kwaikwayo, inda wannan bincike ya waiwaya ne zuwa gargajiyar adabi kuma vangaren waqar baka ta Hausa.

Wushishi (1998) ta gudanar da bincikenta wanda ta bayyana ginuwar adabin Hausa da kafuwar Hausawa da al'adunsu da tarihin samuwar adabin Hausa da adabin baka da kuma rubutaccen adabi. Aikin Wushishi (1998) ya qunshi bayanin sigogi da yanaye-yanayen waqa inda aka kawo waqoqin makaxan fada da na jama'a da na sana'a da na jarumtaka da makaxan sha'awa da na ban dariya da waqe-waqen yara maza da mata da na 'yan mata da na manyan mata da dai sauransu. Haka kuma ta yi bayanin zambo da azancin magana da karin magana da kuma dalilan da ke sa ana yin habaici da barkwanci da kirari da zaurance da sara da ba'a da baqar magana.

Su kuwa manazarta irin su Xangambo (1973) da Abdulqadir (1975) da Muhammad (1977) da Daba (1978) da Yahaya (1979) da Xahiru (1990) da Emilder (2003) duk sun duqufa wajen fayyace rayuwar makaxa da mawaqa da kuma fasahar waqa dangane da

al’ummar Hausawa. Misali Xangambo (1973) ya kawo bayani game da Makaxa Mamman Shata Katsina tun daga haihuwa har zuwa sana’ar Makaxa Mamman Shata ta farko ta tallar goro. Xangambo (1973) ya bayyana Makaxa Mamman Shata bai yi gadon kixa da waqa ba, domin ya fara waqa ne domin nishaxi. Sannan kuma Xangambo (1973) ya kawo bayani game da hikimomin da ke cikin waqoqin Makaxa Mamman Shata.

Yayin da Xangambo (1973) ya fito da dabarun Makaxa Mamman Shata Katsina wajen sarrafa harshe domin jawo hankalin mai sauraro wanda ya qunshi ambaton mutum da nasabar iyaye da mata da ‘ya’ya da abokai da sauransu shi kuwa Abdulqadir (1975) ya qara bayyana matsayi da kuma muhimmancin mawaqan baka a al’ummar Hausawa da Fulani tare da xaukar Alhaji (Dr.) Mamman Shata Katsina a matsayin jigon bincikensa.

Wannan nazari na Abdulqadir (1975) ya zo da kyawawanan bayanai game da tushen wanzuwar waqoqin baka a rayuwar al’ummar Hausawa da Fulani. Abdulqadir (1975) ya kawo bayanin wasu jigogin waqoqin baka da wuraren aukuwarsu tare da liqa su da rayuwa da tasirin waqoqin Mamman Shata ga al’ummar Hausawa. A cikin aikin, Abdulqadir (1975) ya ambato tarihin mawaqin tun daga haihuwarsa

har ya zuwa lokacin da ya fara waqa. Haka kuma an ambaci irin muhimmancin waqoqinsa a cikin al'ummar Hausawa, musamman wajen wayar da kan jama'a da kuma ba su nishaxi. Aikin, zai ba da haske a wannan aiki musamman a inda aka kalli asali da tasowar makaxan baka na Hausa da kuma a inda aka kalli asali da rayuwar Makaxa Sa'idu Maidaji da haihuwarsa da dai sauran fannonin tarihin rayuwarsa.

Sai Muhammad (1977) wanda ya dubi fasahar da Allah maxaukaki ya bai wa Alhaji Aqilu Aliyu wajen wallafa waqa. A wannan aiki an yi bincike mai zurfi a kan waqoqinsa da kuma abubuwan da waqoqin suka qunsa. Tare da karkata akalar aikin ta nazarin waqoqin Aqilu Aliyu da kuma irin fasahar da ke qunshe a cikinsu. Wannan aiki na Muhammad (1977) an gudanar da shi ne a kan nazari na rubutacciyar waqa, aikin wannan kundi yana magana ne a kan waqoqin baka. Amma duk da haka, ayyukan sun danganta zuwa ga mawaqa; wato Malam ya kalli fasihin rubutacciyar waqa ne, wannan aiki, ya kalli makaxin baka ne, wato, Makaxa Maidaji da fasaharsa da balagarsa da gwanincewarsa da kuma zalaqarsa.

Daga bisani kuma sai Daba (1978) ya qara gudanar da wani bincike a kan Alhaji Dr. Adamu Xanmaraya Jos da waqoqinsa.

Binciken Daba (1978) ya yi cikakken nazari ne a kan waqoqin Alhaji (Dr.) Xanmaraya Jos, inda ya dubi turakun waqoqinsa da zubi da tsari da kuma salon da ke qunshe a cikinsu, daga bisani kuma aka gudanar da sharhi game da waqoqin. Binciken yana tattare da ingantaccen nazari ta hanyar bayyana yadda Xanmaraya Jos yake taimako wajen faxakar da masu sauraronsa bisa aqidarsa ta inganta rayuwar al'umma musamman talakawa.

Har wa yau dai, Daba (1978) ya ci gaba da bayyana yadda waqoqin Xanmaraya ke qunshe da basira. Da irin yadda Xanmaraya Jos yake amfani da hikima tare da amfani da daidaitacciyar qafiya cikin zubi da tsarin waqoqinsa. Daga bisani, manazarcin ya raba waqoqin baka zuwa sassa goma, waxanda suka haxa da waqoqin yara da waqoqin zambo da waqoqin yabo da waqoqin ban-dariya da sauransu.

Waxannan ayyuka na Xangambo (1973) da Abdulqadir (1975) da Muhammad (1977) da Daba (1978) sun shafi wannan aikin da za a gudanar ta fuskar xaukar makaxi xaya tilo a bayyana waqoqinsa da tarihin rayuwarsa da bunqasarsa da kuma shaharar fasaharsa a fagen nazari.

Tsoho (1987) ya yi bayanin tarihin rayuwar Alhaju Aliyu Namangi da kuma tsarin karin waqarsa ta Kanzil Azimi da kuma bayyana tarkakken mataninta ta sigar sarrafa harshe. Tsoho (1987) ya yi tsokaci a kan amfani da nau'o'in adabin baka cikin waqar waxanda suka qunshi karin magana da da kirari. Haka kuma Tsoho (1987) ya kawo cikakken bayani dangane da ire-iren adon harshe da ke cikin waqar Kanzil Azimi waxanda suka qunshi tamka da kwalliya da sauransu.

Wannan aiki na Tsoho (1987) zai qara haske ga wannan kundi musamman a vangaren da za a yi bayani dangane da tarihin rayuwar Makaxa Maidaji. Da kuma vangaren da za a yi magana dangane da tsari da salo da kuma adon harshe. Ita kuwa Ramatu (2003) ta bayyana ma'anar kixa da asalinsa tare da bayyana muhimmancinsa a masarautar Zazzau.

Ramatu (2003) ta kawo bayanin kayan kixan Hausawa na gargajiya a Fadar Masarautar Zazzau kamar tambari da kakaki da taushi da kotso. Daga bisani Ramatu (2003) ta kawo cikakken bayani dangane kirarin Masarautar Zazzau, sannan kuma ta zayyano ire-iren ayyukan sarki da waziri da madaki da dagaci da wambai da salanke da

makama da magajin gari da sarkin fada da sauran masu riqe da muqaman sarauta a masarautar zazzau.

2.3 Bugaggun Littattafai

Masu iya magana dai suna cewa ‘na zaune bai ga gari ba’, domin kuwa baya ga kundayen nazari, masana da manazarta sun gudanar da rubuce-rubuce na littattafai a kan nazarin waqa, musamman waqar baka, daga cikinsu akwai Finnegan (1970) da Furniss (1996) da Yahya (1997 & 2001) da Gusau (2003 & 2008 & 2009) da Xangambo (2007).

Waxannan littattafai xaixai da xaixai sun qunshi tubalai na fannonin ilimi ne mabambanta, misali Finnegan (1970) ta kawo samuwa da bunqasar adabin baka a nahiyar Afirka baki xaya, tare da bayanin yadda mabambantan sassan yankin Afirka ke aiwatar da adabinsu waxanda suka haxa da na al’ummar Akan da na al’ummar Yarbawa da na Swahili da na Hausawa da na Fulani da na Mandingo da na Songhai da sauransu. Finnegan (1970) ta kawo nau’o’in adabin baka na al’ummun Afirka ta hanyar fexe su gunduwa-gunduwa, daga cikin wuraren da Finnegan (1970) ta kalla akwai waqoqin baka na alhini inda ta kawo misali daga al’ummar Akan, da waqoqin baka na

addini musamman na al'ummar Swahili da waqoqin baka na yaqi da waqoqin yara musamman a yammacin Sudan.

Daga bisani, Finnegan (1970) ta kawo gudunmuwar wasu daga cikin masana da manazarta adabi na al'ummar Afirka kamar su Kagame na qasar Ruwanda da yadda manazarta adabi na qasashen qetare ke kallon adabin baka na al'ummar Afirka baki xaya. Ta kuma kawo tatsuniya da karin magana da ka-ci-ci ka-ci-ci da dai sauransu da dama ta hanyar faxaxa tunani bincike zuwa ga adabin baka na al'ummar Afirka baki xaya. Wannan littafi zai qara ba da madogara a wannan aiki musamman inda za a kalli haliyya na nau'o'in waqoqin baka na Hausa. Domin kamin a bayyana na Hausawa yana da kyau a kalli sauran al'ummu musamman na Afirka ya suke kallon adabinsu kuma ya suke aiwatar da shi.

Kofoworola da Lateef (1987) sun bayyana asalin da samuwar waqoqin baka waxanda suke ganin sun samo asali ne daga waqoqin da ke yi cikin addinin bori. Sun kuma danganta makaxa da salonsu na kwaikwayon wasu xabi'u da kixan garaya wanda 'yan bori suke yi. Kofoworola da Lateef (1987) sun qara kawo bayani dangane matsayin kixa ga al'umma, inda suka yi kallon kayan kixan al'ummar Hausawa sun kawo bayani game da shantu da lalaje da kalangu da sauransu. A

wani qaulin kuwa, Gusau (2003) ya bayyana tarihin wanzuwar waqar baka ta Hausa ta hanyar kallon qasar Hausa da al'adunta, inda kuma ya qara da bayyana hasashe a kan asalin waqar baka ta Hausa wanda ya alkinta bisa turbar kirari na farauta da kirarin noma da kuma na yaqi. Gusau (2003) ya bayyana nau'o'in waqoqin baka na Hausa tare da kuma rattaba hanyar nazarin fexe waqar baka ta Hausa.

Waxannan ayyuka na Kofoworola da Lateef (1987) da na Gusau, (2003) sun bayar da haske matuqa gaya a inda aka yi magana a kan haliyya da nau'o'in waqoqin baka na Hausa. Da kuma inda aka yi bayani a kan jigo (turke) da nau'o'insa a waqoqin Makaxa Maidaji Sabon Birni da kuma awon baka a waqoqin Maidaji. Sannan kuma zai zama jagora wajen nazarin waqoqin Makaxa Maidaji wanda za a gudanar a wannan nazari.

Yayin da Gusau (2003) ya bayyana tarihin wanzuwar waqar baka ta Hausa ta hanyar kallon qasar Hausa da al'adunta, Yahya (1997) ya fi mayar da hankali ne a kan nazarin rubutacciyar waqa. Yahya (1997) ya yi tsokaci ne kusan a kan kowane nau'i na waqa, inda ya yi bayani a kan jigo da salo. Dalilin kawo wannan aiki na Yahya (1997) shi ne zai qara ma wannan aiki da aka gudanar haske

musamman a inda aka yi tsokaci kan jigo a waqoqin Makaxa Maidaji Sabon Birni.

Har wa yau dai Yahya (2001) ya qara bayyana muhimmancin salo a waqa ta la'akari da tubalan gina shi da nau'o'insa. Yahya (2001) ya duba yadda makaxa da mawaqa suke amfani da salo a cikin waqoqinsu a wajen isar da saqonninsu daban-daban, gwargwadon fahimtar kowane mawaqi inda ya kawo misalai daga mawaqa mabambanta. Da wannan aiki na Yahya (2001) aka asirce duk wani nau'in salo a waqoqin Makaxa Maidaji Sabon Birni bisa tsarin nazari.

Shi kuwa Furniss (1996) ya yi bayani a kan adabin Hausa dangane da tarihin ginuwarsa da sauran bayanai da suka shafi jigo da zubi da tsari. Haka kuma Furniss (1996) ya rattabo jadawali na manazarta a kan rubuce-rubuce cikin Hausa a fannin adabi da harshe da kuma al'adu. A wannan littafi an kawo bayani a kan wasan kwaikwayo tare da havakar rubutattun waqoqin Hausa.

Dangane da fannin adabi tsagwaronsa, akwai littattafai waxanda Richards (1926) da Roger (1981) da Hobsbaum (1983) da Xangambo (2008) da Chiegeonu (1999) da kuma Gusau (2003) suka wallafa.

Richards (1926) ya bayyana qa'idojin gudanar da tarke ne na adabi. Richards (1926) ya bayyana yadda ra'o'in a tarke suke a

cakuxe cikin ruxani, sannan kuma ya yi qoqarin fito da harshe dangane da tarke. A wannan littafi an fito da dangantakar da ke tsakanin fasihi da saqon da yake so ya isar dangane da fasaharsa da balagarsa da kuma zalaqarsa ta gina tunaninsa domin nishaxantarwa da tunatarwa da kuma gyara hali. Wato ya yi qoqarin fito da abin nan da masu iya magana ke cewa ‘gyara kayanka ba zai zama sauke mu raba ba’ tsakanin fasihi da kuma ingancin fasaharsa. A cikin littafi marubucin ya kuma kawo bayanin rauji da kuma yanayin kari.

Sai Hobsbaum (1983) wanda ya bayyana muhimmancin gudanar da tarke a adabi da kuma abubuwan da za a iya fahimta dangane da tarken waqa. Hobsbaum (1983) ya kawo ire-iren waqoqi na Turawa waxanda sukan gudanar cikin taqaitattun baituka, marubucin ya yi nazarinsu ta hanyar tarke da kuma bayyana maqunsarsu. Daga cikin waqoqin akwai “Journey of the Magi” wato mawaqin na bayyana tafiyar wasu mutane uku ne, masu hankali da suka kawo kyauta ga Annabi Isa tun yana yaro, E. S. Eliot ne ya rera ta. Sannan Hobsbaum (1983) ya yi tarken waqar George Herbert wadda ya kira da “The Pulley” wannan waqa tana magana a kan na’ura wadda take da wili xaure da igiya mai qarfi ko kuma a ce kaca

domin xaga abu mai nauyi sama ko a saukar da shi qasa, da dai sauran waqoqin makamanatansu a cikin littafin a taqaice.

Roger (1981) ya yi cikakken bayani dangane da yadda mawaqa kan kauce wa qayyadajjen tsari, abin nufi a nan kuwa shi ne, maimakon su kawo tsari na zahiri, sai su kawo wani zance wanda ba gaskiya a cikinsa inda za su yi qoqarin nuna wannan batu nasu gaskiya ne. Roger (1981) ya bayyana hanyoyin da akan bi wajen gano gaskiyar mawaqi a cikin waqoqinsa da kuma yadda za a fahimci falsafar waqa gaba xayanta.

Daga bisani kuma Roger (1981) ya kawo sigogin waqoqi waxanda suka qunshi tamka da kwalliya da sauran dabarun jawo hankali da makaxa da mawaqa suke amfani da su yayin rera waqoqinsu.

Saboda haka, idan muka yi wa aikin Richard (1926) da kuma na Hobsbaum (1983) da kuma na Roger (1981) kuxin goro dangane da gudummuwar da za su bayar a wannan aiki da ake qoqarin gabatarwa, sai a ce, littattafan za su zama madogara wajen fexe saqonnin da Makaxa Maidaji yake bayyanawa dangane da fasaharsa da balagarsa da kuma zalaqarsa bisa tsarin tarke na nazarin adabi.

Da yadda yake sassarqa tunaninsa domin nishaxantarwa da tunatarwa bisa ruhin zamantakewar rayuwa a cikin waqoqinsa musamman ga masu sauraron waqoqin nasa. Haka kuma, da waxannan littattafai na Richard (1926) da na Hobsbaum (1983) za a qara samun tubali wajen tarken waqoqin Makaxa Maidaji.

Chiegeonu (1999) ya kawo sharhin ma'anar adabi da haliyyar adabi da kuma dabarun aiwatar da ayyukan adabi. Littafin kuma ya yi cikakken bayani dangane da adon harshe da dai sauran ayyukan adabi da dama.

Wannan aiki na Chiegeonu (1999) zai qara ma aikin nan da za a gabatar haske musamman inda za a kalli adon harshe a waqoqin Makaxa Maidaji. Da kuma inda za a yi magana a kan hasashe da bigiren bincike, ta hanyar kallon adabi ta fuskar nazari dangane da fa'idarsa.

Xangambo (2008) ya yi bayani game da adabi da kuma rabe-raben adabin Hausawa dalla-dalla. Xangambo (2008) ya rarraba kayan kixan Hausawa na gargajiya zuwa kaso biyar (5). Kashin farko ya qunshi ganguna kamar su kalangu da dundufa da jami da kurya da talle da dai sauransu. Kashi na biyu ya qunshi kayan bushe-bushe kamar sarewa da qaho da siriqi da tivallaro da dai sauransu. Akwai

kuma kashin qwarya da akayau, sai kuma kashin isga da tsarkiya da ya qunshi goge da molo da garaya da kukuma da gurmi da dai sauransu da dama. Wannan aiki na Xangambo (2008) zai qara ma wannan aiki haske a yayin da ake magana dangane da abin kixa na Makaxa Maidaji Sabon Birni wanda yake amfani da taushi ko kuma turu a wajen waqarsa. Gusau (2008[b]) ya bayyana hanyoyi da dabarun da akan bi wajen nazarin adabin na al'ummar Hausawa.

Gusau (2008[b]) ya bayyana yadda wasu al'ummu musamman na Larabawa da na Turawa suka samar da adabinsu da kuma matakai na zanguna da adabin nasu ya shafo. Gusau (2008[b]) ya kawo makarantu ko mazhabobi ko kuma ra'ayoyin manazarta adabin Hausa mabambanta, ta yadda za a samu qarin haske domin jagoranci ga mai nazari.

Wannan aiki zai ba ni haske wajen kallon yadda manazarta adabin Hausa suke kallon nazarin waqar baka domin xora ta a kan mataki na wannan bincike nawa da zan gabatar. Abba da Zulyadaini (2000) sun yi qoqarin fito da hanyar da za a bi a yi nazarin waqar baka ta Hausa. Sun dubi waqar baka a qasar Hausa tare da kawo ra'ayoyin masana mabambanta. Abba da Zulyadaini (2000) sun ambaci rabe-raben makaxa da mawaqa dangane da muhallinsu. Sannan sai suka

kalli nau'o'in jigogin waqoqin baka na Hausa da suka danganci yabo da zambo da faxakarwa da habaici da ta'aziyya da sauran nau'o'i mabambanta.

Idan muka waiwayo littattafai dangane da tarihin makaxa da mawaqan baka na Hausa kuwa, za mu tarar akwai xaixaikun makaxa da mawaqan baka da aka yi wallafa a kansu, kaxan daga cikinsu akwai na Yusuf (1979) da Umar (1985) da Gusau (2002) da Sheme da wasu (2006) da Daba (2006) da Bunza (2009) da sauransu.

Har wa yau dai Gusau (2002) ya kawo tarihin rayuwar Makaxa Jankixi tun daga asalinsa da quruciyarsa zuwa girmansa da kuma bayanin waqa a bakin Jankixi. Gusau (2002) ya xora wasu daga cikin matanin waqoqin Jankixi a matakan nazarin waqoqin baka na Hausa daga bisani kuma aka kawo bayanin falsafar rayuwa a waqoqin Makaxa Salihu Jankixi.

Shi kuma Bunza (2009) ya tantance tarihin Narambaxa, da iyayen gidansa da waqoqin da ya yi musu. Bunza (2009) ya fayyace turakun waqoqin Makaxa Ibrahim Narambaxa ta hanyar yunqurin bin diddigin tarihi, da al'ada da harshe domin fayyacewa. Sannan ya rairayo ire-iren fasahohin Narambaxa da yadda suka kafa wata babbar mazhabar falsafa a zuqatan Hausawa. Saboda haka, Bunza (2009) ya

bayyana yadda Makaxa Narambaxa ke kallon sarki a waqoqinsa da yadda yake kallon fadar sarki tare da kuma salo a waqoqin Narambaxa.

‘Na zaune fa lalle bai ga gari ba’, domin kuwa Umar (1985) ya bayyana shahara da gogewar Dr. Adamu Xanmaraya Jos. Sannan suka bayyana yanayin waqoqinsa tare da kawo sharhi a kan wasu waqoqin Makaxa Xanmaraya Jos.

Daga cikin waqoqin akwai waqar ‘Karen Mato’ da Waqar ‘Lebura’ da ta ‘Duniya’ da kuma ta ‘Jawabin Aure’ da sauransu. Shi kuma Daba (2006) ya kawo cikakken bayani dangane da rayuwar Dr. Danmaraya Jos. Daba (2006) ya kawo bayanin samuwa da bunqasar waqar baka ta Hausa, ya kawo rabe-raben waqoqin baka da matsayinsu wajen tattalin arzikin Hausawa.

Har ila yau, Daba (2006) ya kawo cikakken bayani a kan turakun wasu daga cikin waqoqin Xanmaraya Jos ya kuma yi bayanin salonsu. Masu iya magana ke cewa ‘sai hali ya yi daidai a kan yi abota’ domin kuwa sai ga Sheme da Albasu da Qanqara da Malami (2006) sun haxu tamkar tsintsiya xaya inda suka xauraye tarihin rayuwar Makaxa Alhaji Dr. Mamman Shata Katsina. Sheme da wasu (2006) sun kawo bayanin Makaxa Mamman Shata a kammale wanda

ya soma tun daga haihuwarsa har zuwa mutuwarsa. Sun kawo jerin wasu daga cikin waqoqin Shata inda daga bisani suka fito da jigogi guda goma sha xaya (11) daga cikin waqoqin. A cikin littafin sun kawo waqar nan ta ‘Bakandamiyar Shata’ da kuma waqar nan ta ‘Ga mu nan zuwa’ ta ta’aziyya wadda aka yi wa Marigayi Alhaji Dr. Mamman Shata, Katsina. A wannan littafi sun alkinta hujjojinsu da tsari na hotuna.

Shi kuwa Yusuf (1979) ya kawo tarihin rayuwar Hamza Caji shi ma dai tun daga haihuwa har zuwa rasuwar Makaxa Hamza Caji. Yusuf (1979) ya bayyana shaharar Hamza Caji da yadda yake shirya waqoqinsa. Haka kuma Yusuf (1979) ya bayyana mutanen da Hamza Caji yake yi wa waqa da kuma makaxa waxanda Hamza Caji ya yi zamani da su. Har wa yau, an kawo cikakken bayani dangane da salon waqoqin Hamza Caji, har ta kai, Yusuf (1979) ya yi gwaji tsakanin basira da fasahar Makaxa Mamman Shata da balagar Hamza Caji da kuma zalaqarsa wajen rerawa da tsarawa, har ma ya shantake da kwatanta Hamza Caji da Hassan xan Sabit, mawaqin Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama.

Waxannan ayyuka na Yusuf (1979) da Umar (1985) da Gusau (2002) da Sheme da wasu (2006) da Daba (2006) da Bunza (2009) sun

bayar da qarin haske ainun a inda aka waiwayi waqa a bakin Makaxa Sa'idu Maidaji tun daga fara waqarsa da kuma ire-iren waqoqin Maidaji Sabon Birni. Sun kuma qara haskaka hanyar fexe waqoqin Makaxa Maidaji Sabon Birni musamman wajen bayyana asali da rayuwar Maidaji. Haka kuma sun qara haske a wannan bincike a vangaren waqa a bakin Makaxa Maidaji tun daga fara waqarsa da kuma ire-iren waqoqin Maidaji Sabon Birni.

Har wa yau dai waxannan littattafai sun bayar da damar watayawa wajen yin sharhi a kan jigo (turke) da nau'o'insa da salo da sarrafa harshe a waqoqin Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni.

Dangane da fassarar kalmomi kuma, an yi amfani da littattafai na qamus masu tafiya bisa nau'in fassarar harshen Hausa zuwa harshen Turanci da kuma harshen Turanci zuwa Hausa wajen samar da ingancin fassarar kalmomin da za a yi a karo da su a wannan bincike. Daga cikinsu akwai *Qamusun Hausa* wanda Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya da ke Jami'ar Bayero ta wallafa a shekarar 2006. Har wa yau dai, yayin gudanar da fassara daga harshen Hausa zuwa Turanci, da kuma fassara daga harshen Turanci zuwa na Hausa an yi amfani da qamus na Muhammad (1990) wato *Hausa Metalanguage*

domin samun daidaiton fassarar kalmomi tare da tabbatar da qa'idar nazari da kuma samun cikakkiyar madogara.

Akwai kuma qamus wanda Awde (1996) ya wallafa, *Hausa: Hausa-English, English-Hausa Dictionary*. An kuma yi amfani da *Qamus na Turanci da Hausa* na Skinner (1977).

2.4 Muqalu da Takardu

Kamar yadda tsarin nazari ya tanadar, akan gudanar da bincike na fannin adabi a kan abubuwa da dama a muqalu da mujallu da akan gudanar a wuraren tarurruka na qara wa juna ilimi. Baya ga waxanda akan samu daga kundayen bincike da kuma bugaggun littattafai.

A sakamakon ire-iren waxannan tarurruka an samar da fasahar adabi a ayyukan masana da manazarta birjik kamar na su Bello (1976) da Aminu (1978) da Sa'id (1975) da King (1980) da Muhammad (1980) da Powe (1981) da Amin (2004) da Tsoho (2010) waxanda suka tavo fannonin adabi, musamman waqoqin baka na Hausa. Za a kalle su domin mu ga inda suka fuskanta, da kuma bayyana irin gudunmuwar da za su bayar wajen havaka wannan aiki da za a gudanar.

Sa’id (1975) ya bayyana ma’ana da rabe-raben salon magana tare da kawo wadatattun misalai na zantuka waxanda suke qunshe da sassarqiya da ake shiryawa domin wasa da harshe tsakanin Hausawa. Har da kalaman da ake amfani da su a vatar da marar jin Hausa da shi. Sa’id (1975) ya qara da bayyana cewa mawaqa na amfani da salon magana cikin waqe-waqensu don su qara musu armashi.

Saboda haka wannan aiki na Sa’id (1975)ya qara haske a wannan bincike da aka gabatar musamman a vangaren da aka yi bayani game da salo a waqoqin Makaxa Sa’idu Maidaji. Sai kuma Aminu (1978) ya nuna cewa akwai maroqa da suke yin roqo ba tare da kayan kixa ba, waxanda ya kira da ‘Yangaram, sannan kuma akwai maroqa masu amfani da kayan kixa, waxanda yake ganin su ne makaxan baka na Hausa. Wato dai, Aminu (1978) ya yi bayani ne dangane da matsayin makaxan baka a qasar Hausa. Ya kawo misalan kayan kixa da suka haxa da algaita da kalangu da tambari da garaya da sauransu. Har wa yau, Aminu (1978) ya bayyana cewa mafi akasarin ‘ya’yan makaxan baka na Hausa ba sa tsayuwa haiqan wajen ci gaba da riqe gadonsu na waqa saboda shigowar karatun zamani na boko. Daga bisani kuma Aminu (1978) ya kawo xan taqaitaccen bayani dangane da wasu daga makaxan baka na Hausa waxanda suka

haxa da Makaxa Xanqwairo da Makaxa Dr. Mamman Shata Katsina da Makaxa Xan'anace da sauransu tare da misalan waqoqinsu. Aikin Aminu (1978) ya qara ma wannan aiki qaimi da madogarar bayyana cewa ba kowane makaxi ne yake xaukar kixa da mawaqa a mtsayin sana'a ko roqo ba, Makaxa Maidaji na xaya daga cikin waxannan makaxa da mawaqan Hausa.

Shi kuwa Powe (1981) ya yi nazarin kirari musamman na al'ummar Hausawa inda aka warware zare da abawa dangane da kirari a tsakanin al'ummar Hausawa ta hanyar bayyana nasabobinsa da suka qunshi duniya. Wannan aiki na Powe (1981) a kan kirari ya taimaka wajen bayyana kirari da ma yadda manazarta magabata suke kallon kirari a cikin wannan kundi.

King (1986) ya kalli hawa da saukar murya da takidi a zubi da tsarin waqoqin fada. King (1986), ya doshi salon zuba xiyan waqoqin fada dangane da takidi. Saboda haka, wannan aiki da za a gudanar zai qara ginuwa da hujjoji a kan tsarin xiya a waqoqin Makaxa Maidaji. Sannan da inda za a yi duba dangane da hawa da sauka da saukar-sauka da kuma ajewa da takidi da karvevveniya, duk za a sami qarin haske daga wannan maqala.

Yayin da King (1986) ya yi cikakken bayani dangane da salon tsarin xiyan waqoqin fada dangane da takidi da hawa da saukar murya, Tsoho (2001) ya yi cikakken tsokaci kan yabau a waqoqin iko wanda makaxa kan yi amfani da shi su waqe tare da kambama da kuma xaukaka sarkinsu a kan talakawa. Tsoho (2001) ya raba yabau zuwa gida biyu; da na take wanda akan yi wa masu asali daga aikatau da na kwalliya da na abokai da na sifa da kuma na tsarrarraki.

A kaso na biyu kuma ya qunshi na ‘yan’uwansa ko sa’o’insa da kuma na salsalarsa. Sannan kuma Tsoho (2010) ya qara fayyace sanqira a matsayin maroqin baki ko xanma’abba ko kuma wasu kan kira sanqira da karen maroqa.

Tsoho (2010) ya bayyana wasu daga ayyukan sanqira waxanda suka haxa da yin kirari ga makaxi kafin fara waqa da kuma da ba da qiryar wanda za a yi wa waqa, sannan kuma sanqira kan aiwatar da kirari yayin yin waqa da dai sauransu.

Ke nan, Tsoho (2010) ya bayyana matsayin sanqira a cikin yabo na waqoqin fada da kuma sauran mu’amalolin rayuwa kamar raxin suna da shelar sadaki. Waxannan ayyuka na Tsoho (2001 & 2010) sun

qara ma wannan aiki gishiri a vangaren da aka yi magana dangane da jigon yabo a waqoqin Makaxa Maidaji Sabon Birni.

Bello (1976) ya yi tsokaci a kan wasu sassa daga cikin jigogin waqoqin sarauta na yabo da zuga da zambo. Aikin Bello (1976) dai ya yi magana ne a kan waqoqin sarauta, kuma wannan kundi ya yi tambihi ne a kan makaxin sarauta guda xaya. Shi kuwa Muhammad (1980) ya bayyana irin zumuntar da ke akwai a tsakanin mawallafin waqoqin Hausa rubutattu da kuma makaxan baka na Hausa ta fuskar salon tsari. Muhammad (1980) ya kawo cikakken bayani ne dangane da karin waqa wanda yake xaya daga cikin vangarorin tsari.

Haka zalika, Amin (2004) ya gabatar da xoriyar tarke ne daga aikin da Powe (1981) ya gabatar. Inda ya bayyana yadda masana da manazarta adabi ke alkinta karin magana a duniya bisa tsarin nazari. Amin (2004) ya kawo cikakken bayanin yadda ya kamata ya zamanto ana fassara karin magana daga harshen asali zuwa harshen karva. Daga bisani, Amin (2011) ya bayyana cewa marigayi Makaxa Ibrahim Narambaxa xaya ne daga cikin fitattun mawaqan da aka tava yi a qasar Hausa. Amin (2011) ya qara da cewa mawallafin littafin *Narambaxa* ya qoqarta magance qishirwar da masu sha’awar waqoqin

wannan makaxin iko (Narambaxa) ke fama da ita wajen sanin haqiqanin tarihin sarakan da ya waqe, da bayanin garuruwansu da qasashensu, uwa-uba kuma ya ci qwallo wajen warware qullin gwarmai da ke tattare da tarihin Narambaxan da rasuwarsa, kamar kuma yadda ya tagaza wajen farfasa tsauraran xangaye da kalmomin da kan wahalar da masu sauraren Makaxa Narambaxa.

Yayin da Amin (2011) ya yi tsokaci dangane da Makaxa Narambaxa, shi kuwa Xangambo (1981) ya bayyana siddabarun salo a cikin ‘tabarqoqo’ wanda ya yi tahmisin Aliyu Xansidi Sarkin Zazzau. Xangambo (1981) ya yi cikakken sharhi dangane da salo, ma’anarsa da rabe-rabensa tare da kafa misalai daga waqar ‘tabarqoqo’. Sannan kuma Gusau (1985/1993) shi ma ya kawo cikakken bayani ne dangane da salo da ire-irensa da kuma sarrafa harshe a waqoqin baka na Hausa. Gusau (1985/1993) ya yi qoqarin fito da dabarun nuna gwaninta da makaxan baka suke amfani da su a cikin waqoqinsu. Ayyukan Xangambo (1981) da Gusau (1985/1993) sun qara haske ga wannan kundi musamman a vangaren salo da sarrafa harshe da aka kawo a cikin wannan aikin dangane da waqoqin Makaxa Maidaji Sabon Birni.

Har wa yau dai Gusau (1996) ya bayyana dabarar alkunya a waqoqin makaxan baka inda ya fito da yadda makaxan baka na Hausa

ke bayyana salon dabara a yayin rera waqoqinsu. Gusau (1996) ya yi cikakken bayanin dabarori na alkunya, sannan kuma an bayyana ma'anar alkunya da samuwar ita kanta kalmar alkunya. Daga bisani kuma Gusau (1996) ya kawo ire-iren alkunya a fagen nazarin waqar baka. Makaxan baka kan kwatanta tare da sakaya abu ta hanyar juyar da shi daga asalinsa ko ma'anarsa ta farko zuwa wata alama makusanciya. Gusau (1996) ya qara ba da madogara a yayin bayyana yadda dabarar alkunya ke kwaranya a waqoqin Makaxa Maidaji Sabon Birni musamman a vangaren kinaya da yadda yake aiwatar da kinaya a cikin waqoqinsa.

Shi kuma Adamu (2008) ya bayyana habaici a zamantakewar Hausawa. Adamu (2008) ya kawo habaici bisa ma'anarsa da asalinsa da yanayi da sigoginsa da rabe-rabensa da dalilan da ke sa a yi habaici da kuma misalansa a zamantakewar Hausawa. Aikin Adamu (2008) ya qara qaimi a vangaren habaici a waqoqin Makaxa Maidaji da kuma qalailaice waqoqin Maidaji ta fuskar kallon yanayi da sigogin habaici.

Abdulqadir (1981) ya bayyana bunqasar ayyukan adabin baka na Hausa ya ginu ne bisa hasashen ra'in Milman Parry da Albert B. Lord na daga ayyukan farko da suka aiwatar a shekara ta 1930. Daga nan ne masana da manzarta suka bazama wajen haqiqancewa a kan

yadda ya kamata a nazarci waqar baka. Abdulqadir (1981) ya kwatanta jigon waqar bakandamiya ta Makaxa Mamman Shata Katsina da shararriyar waqar nan na qasar Yuguslabiya wadda aka gabatar a kan auren Meho xan Smailanga. Abdulqadir (1981) ya yi qoqarin fito da nau'o'in jigo a cikin waxannan waqoqin waxanda suka haxa da yabo da faxakarwa. Har wa yau, Abdulqadir (1981) ya yi tsokaci dangane yadda manazarta ke kallon waqar baka a faxin duniya inda ya kalli nahiyar Rasha da Andalus da sauransu.

2.5 Naxewa

Wannan babi ya waiwayi ayyukan da suka gabata ne domin adonta tafiyar wannan kundi. Littattafai ne da maqalu da kuma kundayen bincike waxanda aka gabatar a fannoni mabambanta, aka nazarce su, tare da naqaltar fasahar da ke cikinsu aka xabbaqa su a cikin wannan bincike.

An gudanar da ayyuka da dama masu inganci a kan waqar baka ta Hausa da kuma nazarin waqoqin da su makaxan sukan rera. Domin haka, an yi waiwayen ayyukan da suka gabata tare da tabbatar da an daxe ana nazarin adabin Hausa tare da yi masa sharhi gwargwadon hali.

Babin ya bayyana cikakken tarihin rayuwar Makaxa Maidaji Sabon Birni wanda ya qunshi tun daga binciken da Gusau (1983 da 1988 da 2005 da kuma 2008) da na King (1986) da na Xahiru (1990) da kuma na Yakasai (1994) suka aiwatar. Nazarin rayuwar shahararre, fitacce, kuma gogaggen mawaqi irin Makaxa Maidaji Sabon Birni dangane da nasabarsa ba qaramin alfanu zai bayar ba, musamman ma ga masu sha'awar nazarin waqar baka da kuma masoya waqoqinsa.

Har zuwa wanda wannan bincike ya qara tabbatarwa da qwararan bayanai dangane da iyalansa da 'yan qungiyarsa da garuruwan da ya ziyarta da kuma iyayen gidansa. Sannan daga bisani wannan babi ya rairayo nazarce-nazarce da aka gabatar dangane da adabi da nau'o'insa da kuma sigoginsa.

BABI NA UKU: JIGO A WAQOQIN MAKAXA MAIDAJI SABON BIRNI

3.0 Gabatarwa

Shi wannan babi zai yi bayani ne a kan jigo da nau'o'insa a waqoqin baka na Hausa. Sannan zai fito da jigo ta hanyar qwayarsa da kuma tubalan da ake gina shi da su a waqoqin Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni.

3.1 Jigo da Ma'anarsa

Jigo a qa'idar masu nazarin waqa yana nufin maqasudin abin da waqa take xauke da shi (King, 1980: 29 da Xangambo, 2007:14).

Ashe ke nan, saqon da makaxi yakan zava ya gina waqarsa, cikin tsari bisa wasu zavavvun kalmomi inda za su doshi wata babbar manufa xaya, shi ake kira jigo.

Wasu manazarta suna amfani da kalmar turke ne a maimakon jigo suna kafa hujja da cewa su makaxan sukan kira gundarin saqon waqarsu ne da turke yayin da suke tsara waqoqinsu.

Ta haka ne manazartan suka amince su riqa amfani da wannan kalma ta turke a wajen nuna saqon da waqar baka take qunshe da shi,

maimakon aiki da kalmar jigo a matakin nazari na waqar baka ta Hausa (King, 1986: 6-8 da Gusau, 2003: 28; 2010:7) .

3.2 Ire-Iren Jigo

A waqoqin baka musamman na Hausa akan jejjefa wasu manyan manufofin da aka gina su a kansu. Makaxan sukan yi amfani da waxannan qananan zantuka ne su sarqa zaren tunaninsu a waqa don ta qara tsawo, sai dai lalle ne su dace da babbar manufar waqa.

Manazarta irin su Xangambo (1973) da Bello (1976) da Magaji (1980) da Ibrahim (1983) da Abubakar (1991) da Bunza (2009) suna ganin makaxan baka kan gina saqo a cikin waqa wadda al'ada ce tasu inda suke xarsa darusssan rayuwa daban-daban a cikin waqa ta amfani da amon kixa.

Yawanci, saqonnin da ake kawowa a cikin waqoqin baka sun haxa da asali da zuriyya ko nasaba da son addini da baiwa ko kyauta ko karimci da hali nagari da jaruntaka ko juriya da iya mulki ko iya dabara da yaqin neman zave da yabo da zambo da habaici da zuga da gargaxi da nasiha da faxakarwa da al'adu da tarihi da halayyar fada da bukukuwa da wasannin gargajiya da adabin baka da tsarin tattalin arziki da sauransu.

> Makaxan sarauta ko na fada suna yin waqoqi a kan jigogi daban-daban ne na gargajiya waxanda suka faro asali tun farkon fara kaxe-kaxe, misalin tsofaffin jigogi su ne na yabo da na zuga da na habaici da na zambo da na roqo da kuma na koxa kai. Waxansu jigogin kuma sababbi ne, waxanda suka fara saboda samuwar wani canji a cikin rayuwar Hausawa. Sababbin jigogi da suka wanzu a cikin Waqoqin Hausawa sabilin canji da ya auku a halin zaman Hausawa su ne na gargaxi da na wayar da kan jama'a da kuma na siyasa (Ibrahim, 1983: 9-10):

3.3 Nau'in Waqoqin Makaxa Maidaji

Waqoqin baka na Hausa na da nau'o'i mabambanta waxanda suka haxa da na fada da na noma da na siyasa da na yara maza ko mata da na sana'a da na jama'a har ma da waqoqin cikin tatsuniya da sauransu (Umar, 1984:32 da Yahya, 1984:6 da Gusau, 2003:16).

Wani abin ban ta'ajibi da mamaki dangane da Makaxa Maidaji, da wahala a sami wani makaxin fada tsayayye wanda karin waqarsa ba ya karewa. Mawuyacin abu ne a sami waqarsa ta zama ba ta xauke da saqo ayyananne.

Duk da cewa Makaxa Maidaji ya yi gadon kixa da waqa ne. Domin, mahaifin Maidaji, Muhammad Dango (Mainasara) ya yi

gadon kixa da waqa ne a hannun mahaifinsa Xantsara wato kakan Makaxa Maidaji. Duk da dai Mainasara kixan noma kawai ya yi, bai yi wa sarakuna kixa da waqa ba. Wato dai, gidansu sun gaji kixa tun daga kakannin kakanninsu. Ya qara tabbatar da haka a cikin waqar da ya yi wa sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Umaru, yana cewa:

Jagora : Ummaru na zagi ya gaji yaqi ga kakanai,
'Y/Amshi : Da shi da kakana babu zangon da ba su kwan ba.
Jagora : Kakanka ya ci Ganiyya,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana.
Jagora : Ya ci birnin ‘Yandoto,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana.
Jagora : Ya ci birnin Bardava,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana.
Jagora : Ya ci birnin Anganba,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana.
Jagora : Maza cikin tabki sun ka hwaxa suna voyo,
'Y/Amshi : Duniya na ji dashe-dashenta na Alqali,
: Mu yi zaman Xantsara da jadi da Jari kuma,
: Mu yi zaman Salihu,
: Shi da Xandada mai tabshi,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{147}$ $^{1}/_{4}$)

Ke nan, tun lokacin da Sarakunan Gobirawa suka taso daga Nijar suka zo suka kafa Sabon Birnin Gobir, kakanninsa suka biyo waxannan sarakuna a matsayin makaxan sarki. Kuma har zuwa yanzu zuriyarsu ce ke yi wa sarakunan Sabon Birnin Gobir kixa. Tun Zamanin da ake yaqe-yaqe tsakanin qasa da qasa zuriyarsu ce ke yi

wa sarakunan Gobirawan wancan lokacin kixa da waqa a lokacn yaqi. Ke nan, tun da Makaxa Maidaji Sabon Birni ya buxi ido har ya yi wayo ya ga gidansu ana kixa da waqa.

Hausawa na cewa ‘dakan xaka, shiqan xaka, tankaxen bakin gado’, wannan batu bai rasa nasabar cewa yayan Makaxa Maidaji, Malam Musa Nadada ya karvi kixa da waqa daga wurin mahaifinsu Muhammadu Dango (Mainasara) shi ne ya koya wa Makaxa Maidaji kixa da waqa. Makaxa Nadada Sabon Birni ya yi tashen waqa qwarai, mutum ne mai basira da hikima wajen shirya waqoqinsa. Ya yi waqoqi da dama duk da cewa malami ne shi domin kuwa har ya haddace Al-qur’ani mai tsarki, amma karatun bai hana shi kixa ba. Makaxa Nadada ya shahara ne a kixan noma da kixan fada. Sannan yana da yara masu yi masa amshin waqa waxanda cikinsu har da Makaxa Maidaji a matsayin Marafan Makaxa Nadada (Daudun Kixi).

Ke nan, kafin Makaxa Maidaji ya zama makaxin Masarautar Sabon Birni, yayansa Makaxa Musa Nadada ne makaxin garin. Wannan batu yana qara tabbatar da Makaxa Maidaji dai, ya koyi kixa da waqa na sosai ne a wajen yayansa Malam Musa Nadada. Kuma Makaxa Maidaji, ya fara da kixan kurkutu ne. Ganin zalaqarsa

dangane da waqa ne, ya haddasa Makaxa Nadada ya naxa masa muqami na '*Daudun Kixi'*.

> Kamar dai yadda ya gabata, ko da yake, Makaxa Maidaji Sabon Birni yana tare da yayansa ne wajen kixa, amma yakan yi gayauna ya tafi, ya dinga yi wa wasu mutane 'yan waqe-waqe a gona ko a kasuwa da sauran wurare (Gusau, 1983: 135).

"Da yawa mutane sukan so su ji yadda mawaqi yakan shirya waqarsa, wato, yakan rubuta ne sannan ya rera ta, ko kuwa, takan zo masa ne kawai ba tare da ya rubuta ba" (Yusuf, 1979: 6). Yawanci kowane makaxi da hanyoyi da yake bi wajen tsara waqa, Makaxa Maidaji Sabon Birni ma ba a bar shi a baya ba. Ya kan tsara waqoqinsa ta waxannan hanyoyi:

- Ya tsaya gida ya tsara waqarsa a tsanake;
- Yakan kuma tsara waqa ta nan take idan ta same shi.

Wato abin nufi a nan shi ne, idan muka xauki hanya ta farko za mu samu cewa Makaxa Maidaji Sabon Birni yakan haxu da 'yan amshinsa a gida lokacin da zai shirya waqa. Bayan sun haxu sai ya tsara musu yadda yake son waqar ta kasance. Su ma masu amshinsa

ba a bar su a baya ba, domin kuwa sukan qara gina waqar ta hanyar qiqiqiro abubuwan da za su faxa sai kuma a tsara su a waqe cikin murya da amon kixan da ya dace da karin waqar. Sukan tsaya tsayin daka wajen bambanta amon kixa da karin sabuwar waqar da za su gabatar da wadda suka riga suka aiwatar. Bayan sun hau da ita bisa murya da kixan da ya dace ne sai su yi ta nanatawa har sai ta zauna musu a kai, wato sun haddace ta tsaf. Kuma sukan tsaya sun xan yi gyare-gyare musamman ta fuskar canza kalmomin da ba su dace ba da waxanda suka dace. Domin a ko da yaushe, Makaxa Maidaji Sabon Birni mutum ne mai neman shawarar yaransa game da waqar da suke shirin gabatarwa.

Hanya ta biyu kuwa ita ce, idan aka umurce su da yin waqa nan take, kuma ba su qullo ta daga gida ba. To, Makaxa Maidaji Sabon Birni da yaransa sukan tsara waqa ta nan take, ba shiri, sai dai wani lokaci takan kasance gajeruwa. Daga bisani, wata waqar in sun koma gida sai a qara gina ta musamman idan mai waqar ya nuna yana bukatar hakan.

‘Wani hanzari ba gudu ba’ kamin Makaxa Maidaji ya tsara waqar da yake so ya aiwatar, akwai hanyoyi da yakan bi wajen samun bayanin wanda ko abin da yake so ya yi wa waqa. Hanyar da yake

idan zai yi masu sarauta waqa ta bambanta da hanyar da zai bi idan zai yi wa wani wanda bai shafi sarauta ba waqa. Waxannan hanyoyi sun haxa da:

- Makaxa Maidaji kan samu bayanai daga wajen waxanda zai shirya wa waqa da kansu. Sannan sau da yawa Makaxa Maidaji yakan aiki maroqinsa ya tambayo bayanin wanda ya yi masa kyauta a lokacin da yake yin waqa.

- Har wa yau kuma Makaxa Maidaji kan sami bayanin Sarki ko Hakimin da yake so ya yi wa waqa daga bakin talakan garin ko bafadensa. Yakan tambayi nasabar Sarkin; da iyayensa da kuma kakanninsa. Haka kuma ya kan sami tarihin wasu sarakunan waxanda ya yi wa waqa daga wurin ubangidansa, sarkin Gobir. Xahiru (1990) yana kan wannan ra'ayi, ya kafa da hujjarsa da cewa:

> Duk sarki yana da labarin wani sarki da ke maqwabtaka da shi da kuma na nesa da shi. Wannan ba zai rasa nasaba da jihadin Shehu Xanfodiyo wanda ya qara haxa kan sarakunan qasar Hausa wuri xaya. A wancan lokaci, dukkan sarakuna sukan taru a jihar Sakkwato domin karvar wani saqo. Wani dalili da zai qara qarfafa cewa kowane sarki yana da labarin xan'uwansa sarki, shi ne duk lokacin da za a naxa wani sarki a qasar Hausa, sarkin

da za a naxa kan gayyaci sarakuna na kusa da na nesa don taya shi murna (Xahiru, 1990: 10-11).

Wannan bincike ya tabbatar da Makaxa Maidaji mafi akasari ya kan tsara waqoqi ne idan an gayyace shi ko kuma wani ya nuna yana son a yi masa waqa. Wannan ya sa Makaxa Maidaji ya ziyarci garuruwa da dama waxanda suka haxa da:

a) Zariya da ke jihar Kaduna

b) Babban birnin Sakkwato

c) Tcibiri da ke cikin qasar Nijar

d) Maraxi can cikin qasar Nijar

e) Madawa da ke yankin qasar Nijar

f) Buza ita ma dai a cikin qasar Nijar

g) Daqwazo da ke cikin qasar Nijar

h) ‘Yankuzo da ke jihar Katsina

i) Gwaranyo da ke jihar Sakkwato

j) Gusau da ke jihar Zamfara da sauran garuruwa waxanda lokaci ba zai ba da damar a yi ta zayyanowa ba.

Wannan bincike ya gano cewa iyayen gidansa a masarautar Gobir guda uku ne. Ya bayyana hakan a hirarsa da Malam Alhassan a shekarar 11/2/1981 kamar haka:

B. S. Y. Alhassan: To kai kuma makaxin wane ne?

Makaxa Maidaji: To ni na fara tun daga Sarkin Gobir Ummaru xan Sarki Salihu. Tak kai ga Sarkin Gobir Ibrahim qanin Sarki Salihu. Hat tak kai ga Sarkin Gobir Muhammad qanen Sarki Salihu.

Da haka za a iya kafa hujja da cewa iyayen gidan Makaxa Sa'idu Maidaji a masarautar Gobir ta Sabon Birni su ne:

i) Sarkin Gobir Ummaru 1957 - 1966

ii) Sarkin Gobir Ibrahim 1970 – 1975

iii) Sarkin Gobir Muhammadu 1975 – 2003

Har wa yau kuma, wannan bincike ya gano wasu masarautu da ke karrama waqoqin Makaxa Maidaji da gayyatarsa daga lokaci zuwa lokaci da sanin ubangidansa sun haxa da:

i) Masarautar Sarkin Zazzau,
Alhaji Shehu Idris

ii) Masarautar Sarkin Katsinan Gusau,
Alhaji Muhammad Kabir Xanbaba

iii) Masarautar Sarkin Bazai na Jangeru,
Alhaji Muhammadu Jangeru

iv) Masarautar Sarkin Maraxi,
Alhaji Muhammadu Xangara

v) Masarautar Sarkin Buza,
Alhaji Muhammadu Abdullahi

Makaxa Maidaji bai koma ga mahaliccinsa ba sai da ya yi fice a tsakanin al'ummar Hausawa da ma al'ummu na qetare. An riqa

sanya faya-fayan waqoqin Makaxa Maidaji tun yana da rai a kusan dukkan gidajen radiyon da ake amfani da harshen Hausa. Hatta gwamnatin jihar Sakkwato da hukumomin gwamnatin jihar da hukumomi masu zaman kansu sun yi ta cin moriyar baiwar da Allah ya yi wa Makaxa Maidaji wajen isar da saqonni ko tallata hajarsu.

Kasancewar Makaxa Maidaji yana rera waqoqin masu burge jama'a wanda hakan ya haifar da tagomashin karvuwar waqoqinsa a tsakanin al'ummar Hausawa. An gayyace shi taruka da dama inda akan ba Makaxa Maidaji fage ya baje kolinsa wajen qara ma al'umma haske. Ta wannan siga, wannan bincike ya gano Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni yana da nau'in waqoqi kamar haka:

3.3. 1 Waqoqin Fada

Waqoqin Fada sun qunshi waqoqin da Makaxa Maidaji ya yi wa mutane waxanda suka jivinci gidan sarauta. Waxannan waqoqi na fada su ne manazarta irin su Xanjuma (1982[b]: 27) da Alhassan da wasu (1982:75) da Gusau (2008:137-147) da sauransu suke kira da "waqoqin sarakuna". Waqoqin fada sun qunshi waqoqi na sarakuna da

na hakimai da na dagatai da na masu unguwanni da na sauran mutane masu riqe da muqaman sarauta na Hausa.

A dunqule, makaxan fada na gayauna suna yi wa kowane xan jinin sarauta waqa ba tare da sun jingina a gare shi ba a matsayin ubangidansu. Gusau (2003) ya qara da cewa:

> Makaxan fada suna taka muhimmiyar rawa wajen gina rayuwar al'ummar Hausawa. Mutane ne masu kwarjini da ban sha'awa da riqe al'adun gargajiya kyawawa. Makaxan fada suna tsare mutuncin al'ummarsu da jawo musu kwarjini da xaukaka dangane da waqoqinsu da kuma rashin nuna tsoro a fagen daga (Gusau, 2003: 22).

Makaxa Sa'idu Maidaji ya rera waqoqi da dama na sarakuna kamar yadda ya bayyana a hirarsa da Alhassan, B. S. Y. a shekarar 1981, da hirar da ya yi da Gusau, S. M. a shekarar 1983 da lokacin da ya sake komawa a shekarar 1988 da kuma hirar Makaxa Maidaji da Alhaji I. Xiso na Rediyo Rima ta Jihar Sakkwato a shekarar 1991. Har wa yau, wannan bincike ya qara tabbatar da hakan a hirar da mai bincike ya yi da magajin Makaxa Maidaji Sabon Birni, wato Makaxa Hana a ranar 03/07/2011.

"Makaxan fada suna da wasu mashahuran lokuta waxanda suke rera waqoqinsu" (Gusau, 2008:137-160). Duba da wannan batu,

wannan bincike ya gano waqoqin Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni sun tasirantu da ra'ayin Gusau (2008) waxanda suka fito da lokuta mabambanta kamar haka:

3.3.1.1 Waqoqin Fada na Lokacin Yaqi

A lokacin yaqe-yaqe ana yi wa sarakuna kixa da waqa don zuga su da sa musu qaimi da xebe musu tsoro da kuma fargaba. Gusau (2008) yana cewa:

> Makaxi yakan yi shiga irin ta dakare, ya sanya sulke da kwalkwali ya riqe garkuwa, sannan ya rataya abin kixa a kafaxarsa. Amma in rana ta vatar masa, sai ya yi farat, ya fara kaxa abin kixansa, daga nan a qyale shi, a ce ashe mace ne. Misali Makaxa Ata Mai Kurya babban jarumi ne kuma makaxi, har ana yi masa kirari da cewa: "Ga kurya ga mashi". Sai kuma Idi Namanga Kura Gazau da Umaru Na-Maiyaqi da Giye xan Tagandu da sauransu (Gusau 2008:137-160).

Makaxa Maidaji Sabon Birni, ya rera waqoqi da ke bayyana sigar yaqi da gwagwarmayar da iyayen gidansa, sarakunan Gobir suka yi da abokan hamayya a wancan lokaci na yaqi. Duk da dai bai nuna an yi yaqi da shi kansa ba, amma ya nuna cewa an yi yaqi a zamanin kakansa wato Makaxa Xantsara. A waqar '*Umaru ginshimin Ali ci*

hwansa' ta Sarkin Gobir na Sabon Birni Alhaji Ummaru Na-Allah (1957-1966), Makaxa Maidaji cewa ya yi:

Jagora : Ummaru na zagi ya gaji yaqi ga Kakanai,
'Y/Amshi : Da shi da kakana babu zangon da ba su kwan ba.
Jagora : Kakanka ya ci Ganiyya,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana.
Jagora : Ya ci birnin 'Yandoto,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana.
Jagora : Ya ci birnin Bardava,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana.
Jagora : Ya ci birnin Anganba,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana.
Jagora : Maza cikin tabki sun ka hwaxa suna voyo,
'Y/Amshi : Duniya na ji dashe-dashenta na Alqali,
: Mu yi zaman Xantsara da jadi da Jari kuma,
: Mu yi zaman Salihu,
: Shi da Xandada mai tabshi,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{147}$ $^{1}/_{4}$)

Har wa yau dai a waqar '*Jikan Jari ginshiqi'* ta Sarkin Gobir na Sabon Birni Alhaji Umaru Shawai (1916-1945), Makaxa Maidaji Sabon Birni cewa ya yi:

Jagora : Salihu kai am mayaqi,
'Y/Amshi : Kai a Kannin da Hammadin.

Jagora : Ko hwamar Badar da anka yi,
'Y/Amshi : Su an na Annabi.

Jagora : Kakanninka sun ci birnin Kisira,
'Y/Amshi : Sun ci Qaura Kamusa can Badar,
: Jikan Jari ginshiqi,

: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$)

Haka nan kuma a waqar '*Jikan Kunda ai ina shirin zuwa gaisai'* ta Alhaji Shu'aibu Kunda, Makaxa Maidaji ya bayyana tsagwaron qarfin maganin tsari da kafin qasar Gobir wanda take da shi tun zamanin manyan sarakunan qasar Gobir ta Sabon Birni irin Ibrahim Babari (1737-1764 ko 1742-1770) da Umaru Jari (1904-1915) inda yake cewa:

Jagora : Shu'aibu zamanin yaqi,
'Y/Amshi : Na ga ba a taushi Gobir ba,
: An so a karya dahin Jari,
: Amma hwa ba dama.

Jagora : To, Gobirawa ko dauri,
'Y/Amshi : Ba mu gaji tsoro ba,
: Tun da kayan Babari,
: Na nan ga yaranai,
: Jikan Kunda ai ina kan zuwa gaisai,
: Tun da na san ba ka gaji qyamar mutane ba.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{3}$)

3.3.1.2 Waqoqin Fada na Yammaci

Makaxan fada, musamman na taushi da kotso sukan kai wa sarki gaisuwa duk kowane daren juma'a wato Alhamis da daddare. Wasu kuwa sukan kai kixan ne ranar Juma'a da safe. To, wannan gaisuwa ita ake kira 'yammaci'. Gusau (2008) ya qara da cewa:

> Kixan yammaci shi ne shaharrarren lokaci da sarki kan zauna a wani wuri kevavve cikin fadarsa ya dinga sauraron makaxin yana wasa shi da kuma yi wa abokan hamayyarsa zambo da habaici A irin wannan kixa na yammaci makaxa ke roqon sarakunansu abubuwan da suke buqata a fakaice. (Gusau, 2008:137).

A wannan fasali, Makaxa Maidaji Sabon Birni ba a bar shi a baya ba, a waqarsa ta '*Binu xan baraz zaki xan Bawa'* ta Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Umaru xan Salihu (1957-1966), cewa ya yi:

Jagora : Shin Ummaru ne ko Yakubu Daudu,
'Y/Amshi : Ko ko Kada ne yad dawo.

Jagora : To, ina masu son sarki,
'Y/Amshi : In anka shaqa mijina as sarki.
Jagora : Ga wani na jiran sarki,
'Y/Amshi : Daxa sai shi koma jiran Sarkin Karma.
: Na Malam gwanin daga na Allah,
: Jikan Hillani xan Musa na Malam.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{147}$ $^{1}/_{6}$)

Haka nan kuma a waqar Sarkin Gabas na Gwaranyo, Alhaji Umaru *'Namijin daga uban gardaye'* Maidaji ya bayyana cewa:

Jagora : Ran Juma'a naz zo Gwaranyo,
'Y/Amshi : Har daxi ya tsallake ni,
: 'Ya'yana sai ku yo mun murna,
: Na iske sarki.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{375}$ $^{1}/_{12}$)

A taqaice, lokaci na yammaci yana da muhimmanci qwarai ga makaxan Fada da kuma sarakunan domin a lokacin da sarki yake sauraron makaxinsa har ya rera wani xa da ya ba shi sha'awa ko dariya yakan yi magana don nuna farin cikinsa.

3.3.1.3 Waqoqin Fada na Lokacin Kewaya ko Rangadi

A qasar Hausa sarakuna sukan tafi kewaye ko rangadi tare da makaxansu suna yi musu waqa. Komai tsananin tafiya komai wahalarta, da makaxan ake zuwa. A zamanin tafiyar sukan ga abubuwa na aukuwa, basira kuma na qara zo musu, kansu na qara wayewa da al'amura. A tarihin qasar Hausa, yana cikin al'adar sarakuna a kowace shekara su zagaya qasashen da suke riqo don aza haraji da jangali ko don ganar wa idanunsu abubuwan da ke gudana.

Wata rana kuma sukan yi hawa su je wani wuri cikin qasar idan wani yamutsi ya auku don su sasanta rikicin. Ko kuma idan za su tarben babban baqo kamar Gwamna ko Shugaban Qasa, musamman bayan zuwan Turawan Mulki qasar Hausa. To, masarautar Gobir ta Sabon Birni ba a bar ta baya ba ga wannan al'ada. Hakan ya haifar da a waqoqin Makaxa Madaji yakan ambato ire-iren waxannan al'amura.

Misali, akwai waqar '*Toya matsahwa baqon dole'* wadda ya rera wa Sarkin Gobir Salihu (1945-1956) a lokacin da Sarki Salihu ya tarbi Gwamna. Makaxa Maidaji Sabon Birni cewa yake yi:

Jagora : Sarki za shi tarben gwamna,
'Y/Amshi : Ke mota dak kix xauki baba,
: Ki kai shi da lahiya don Allah,
: Toya matsahwa baqon dole,
: Jikan Sanda baban Yari.
Jagora : Taron shawara ne yaz zo,
'Y/Amshi : Mun yo rakkiya mun dawo,
: An yit tambaya ga sarki,
: Ban san inda zai kwana ba,
: Toya matsahwa baqon dole,
: Jikan Sanda baban Yari.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$ - AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{1}$)

Kamar yadda aka bayyana, sarakuna sukan tafi rangadi ko kewaye tare da mawaqansu, a waqar *'Bawa na Jekadiya'* ta Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003), Makaxa Maidaji Sabon Birni ya tabbatar da haka inda yake cewa:

Jagora : Zuwanmu Sakkwato kwananmu takwas,
: Gidan Dikkon Gande,
'Y/Amshi : Ana ta ba mu abinci,
: Mun qoshi, mun hole birjik kamad duma.
Jagora : Sakkwato mun ci abinci iri-iri,
'Y/Amshi : Kala-kala, ham munka sake hwata,
: Jikinmu yak koma jawur kamaj jini,
: Bawa na Jekadiya,
: Na Dango mai saje.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{142}$ $^{1}/_{4}$)

Haka nan kuma a waqar *'Baban Yari baban Makama'* ta Sarkin Gobir Salihu (1957-1966) Makaxa Maidaji Sabon Birni ya qara tabbatar da haka inda yake cewa:

Jagora : Ga Alhaji,
'Y/Amshi : Ya taho za mu tarbe,
: Da wace gaisuwa zan ishe mai.

Jagora : Ko waqar sarauta mukai mai,
'Y/Amshi : Koko dai salati mu kai mai.

Jagora : To, in kau salati mukai mai,
' Y/Amshi : To, sun ce, "'Yan'uwa babu zambo",
: Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$)

3.3.1.4 Waqoqin Fada na Lokacin Taro

Taron sarakuna ya samo asali ne tun zamanin masu jihadi da suke haxuwa don tattaunawa game da jihadi da shiri a kan qasashen da za a ci. Ba a bar zuwa taruka Sakkwato ba, sai bayan zuwan Turawan Mulkin Mallaka. "Da Turawan mulki suka shimfixa nau'in mulkinsu, suka zaunar da Gwamnan Jihar Arewa a Kaduna, sai sarakunan qasar Hausa suka koma suna halartar taruka a Kaduna" (Mani, 1970: 28 & 112-129 da Albasu, 1990: 21-30).

Har kuma aka kai wani zango da ake halartar taron daba don murna da zuwan wani babban baqo kamar taron daba

na zuwan xan Sarkin Ingila Prince Edward Wales a shekarar 1925. Daga nan kuma sarakuna suka ci gaba da zuwa taruka don shawara a majalisar sarakuna ta Kaduna tun daga 1960 (Chafe, 1990: 31-61).

A irin waxannan taruka, sarakuna sukan tafi tare da makaxansu. Kowane makaxi yakan so ubangidansa ya zarce sauran sarakuna, saboda haka makaxan suke takarar shirya wa sarakunansu waqoqi masu daxi da kwarzantawa. Dangane da wannan batu, Makaxa Maidaji ya bayyana hawan daba da Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Muhammadu Bawa (1975- 2003) ya yi a Sakkwato a waqar *'Kai ab bahagon gulbi'* a lokacin wani taro inda yake cewa*:*

Jagora : Ai ga taronmu na Sakkwato,
'Y/Amshi : Mun gama kaya ga hawan daba,
: An shirya dawakayye,
: Amma babu kaman namu.
Jagora : Doki ya hi dubu goma,
'Y/Amshi : Raqumi ya hi dubu goma,
: Duk an gamu an jera,
: Uban Shantali ya canye,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{7}$)

Ga wani misalin daga waqar '*Uban Makama uban Gardaye'* wadda ya yi wa Sarkin Gobir, Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003) inda Makaxa Maidaji ya zama 'xan magori wasa kanka da kanka'.

Domin kuwa a cikin xiya na wannan waqa ya kambama kansa da cewa:

Jagora : Taron Isa da anka yi niz zo,
'Y/Amshi : Ba da kamar makaxa niz zo ba.
Jagora : 'Yan yara sun ga shigata ta isa,
'Y/Amshi : Has sun ce wane xan sarki na,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{374}$ $^{1}/_{6}$)

A cikin waqar *'Jikan Jari ginshiqi'* ta Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Umaru Na-Allah xan Shawai (1916-1945), Makaxa Maidaji ya qara fito da kyakkyawar alaqar da ke tsakanin makaxi da sarki a lokacin tafiya ta zamowarsu xaya daga cikin tawagar sarki. Ga dai abin da yake cewa:

Jagora : Sarki za shi Sakkwato,
'Y/Amshi : Mu ko mun yi rakkiya.

Jagora : Baba ka zak ka lahiya,
'Y/Amshi : Dawowak ka lahiya,
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$)

3.3.1.5 Waqoqin Fada na Lokacin Naxin Sarauta

A lokacin naxin sarauta makaxan fada sukan shirya waqoqi na musamman. Akan ba makaxan fili su cashe sosai a yammacin ranar da

aka yi bikin wankan sarauta ko ba da sanda ga sabon sarki. Gusau (2008) ya qara da cewa:

> Tun a da can, su kansu sarakunan da makaxan fada suke yi wa waqoqi sukan ba wasu makaxansu sarautu na hakimci wato sarautar mai unguwa ko hakimi. Saboda su bayyana godiyarsu da kuma alfaharinsu ga waqoqin da wannan makaxi yake yi musu. Misali makaxa Sa'idu xan Dodo Mai Tabshi ya riqi muqamin mai unguwa a Sakkwato. Sarkin Busa na Sarkin Katsina shi ma yana da gari da ake kira Fardami wanda yake shugabanci. Domin haka, Buda Xantanoma yake ce wa Sarkin Kabin Argungu Muhammadu Sama (a lokacin yana Muza na garin Bayawa) ya ba shi sarautar kixa da riqon garin Hilinge (Gusau, 2008: 158-161).

Daga ire-iren waqoqi na lokacin naxin sarauta na Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni akwai ta Sarkin Gobir na Sabon Birni Alhaji Ibrahim (1970-1975), ta '*Uban zagi na Muhamman mai Sabon Birni'* wadda cikin wannan waqa akwai inda yake cewa:

Jagora : To, na taho al'adak kixin sabon Sarki,
'Y/Amshi : Had da ni makaxin na Garba yau na zama sabo.

Jagora : Na yi shekara biyu ban zo kixi ba gidan kowa,
'Y/Amshi : Anka ce Ibrahim na Dango as sarki,
: Marahwa kui mana tuqi mu ba tabshi kashi.

Jagora : Masu bixak kuxxi kui ta tahiyan neman kuxxi,

‘Y/Amshi : Masu aiki ku yi anniyya gyara gona,
: Ga zamanin Ibrahim ba a zaman banza,
: Uban Zagi na Muhamman mai Sabon Birni,
: Iro ya cika zakka yau ya zama sarki.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{147}$ $^{1}/_{11}$)

A waqar *‘Na zaka barka da arzukka’* ta Sarkin Madawa, Alhaji Muhammadu, Makaxa Maidaji Sabon Birni bayyana sanadiyyar tafiyarsa zuwa garin Madawa da ke cikin qasar Nijar domin murna naxin sabon sarki da aka gayyace shi. Ga abin da yake cewa:

Jagora : Ni Alhaji Maidaji xan mutanen,
‘Y/Amshi : Sabon Birni sabilin sarkin ga,
: Za ni in kwan huxu Madawa.

Jagora : Hwadawan Madawa,
‘Y/Amshi : Ina masoya sabon sarki,
: Ku yo mana kayan da za ni sa wa sabon sarki.
Jagora : Wanga gidan tawaye ne,
‘Y/Amshi : Gidan Jibo sarki yag gado,
: Hwaxa masu ba mai shiga gidan,
: Sai in bayan kai,
: Na zaka barka da arzukka,
: Sarkin Madawa Muhammadu,
: Ko yanzu duniya ta yo mai haske.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{376}$ $^{1}/_{7}$)

Akwai wani misali a waqar Magajin Gari, Alhaji Magaji Tangaxi Tsibiri ta *Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala’* Makaxa Maidaji ya qara fito da wani misali kamar haka:

Jagora : Ai dauri an Magajin gari na shinkinkimi,
‘Y/Amshi : Tun da an canza yanzu duniya tamu ta.

Jagora : Ai yara wanga Magajin gari irin namu ne,

‘Y/Amshi : Mu da qilli wancan mai abun rashin hankali,
: Na biyo jikan Sanda xan Kaso xan Bala,
: Jitau baraz zaki gagarau Magajin gari.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{1}$)

Duba da aikin Gusau (2008) a iya cewa gaba xaya waxannan su ne muhimman lokuta waxanda makaxan fada suka fi shirya waqoqinsu ga sarakuna da sauran mutane masu riqe da muqaman fada. Duk da dai akwai lokutan bukukuwan salla da bukin ’ya’yan sarakuna da sauran wasu lokuta mabambata.

3.3.2 Waqoqin Noma

Manazarta irin su Xahiru (1990) da Gusau (2002) da Bunza (2009) duk suna kan madogarar waqoqin noma sun qunshi waqoqin da makaxa kan ya yi wa mutane waxanda suka jivinci manoma. Idan muka waiwayi aikin Gusau (1983) za a ga ya kasa makaxan noma zuwa kashi uku:

> Kashi na farko, ya qunshi makaxan noma na sarauta, waxanda suka haxa abubuwa guda biyu; suna kixan noma, sannan kuma suna yin kixan sarauta. Daga cikin irin waxannan makaxa akwai Makaxa Salihu Jankixi da Makaxa Ibrahim Narambaxa da Makaxa Abu Xan Kurma Maru da Makaxa Xangiwa Zuru da sauransu. Kashi na biyu kuwa sun qunshi makaxan noma na jama’a, waxanda suka fi mayar da hankalinsu wajen yi wa jama’a

> waqa musamman na bajinta. Misalin irin waxannan makaxa sun haxa da Makaxa Illon Kalgo da Makaxa Audu Wazirin Xanduna. Kashi na uku, sun qunshi makaxan noma na jarumtaka, ta wani vangare suna yin kixan maza. Irin waxannan makaxa sun haxa da Makaxa Mamman Xan'anace da Makaxa Isa xan Makaho da Xan Balade Morai da sauransu (Gusau, 1983:52-64).

Makaxa Maidaji yana cikin kason farko na Gusau (1983), wato ke nan, ya qunshi abubuwa guda biyu; yana kixan noma, sannan kuma yana yin kixan sarauta. Makaxa Maidaji ya rera waqoqin noma da dama ga mutane daban-daban. Daga cikin waqoqin noma na Makaxa Maidaji akwai shahararriyar waqar nan ta *'Na yi hamdala nai shukura da godewa'*. A xiyan wannan waqa yana cewa:

Jagora : Maza ku kama noma noma abin yi ne,
'Y/Amshi : Don na ga ba a gumba in ba da tsaba ba.

Jagora : Shi wanda ba shi noma ya zam abin tausai,
'Y/Amshi : Yana bixar awo mata na harara tai,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau farilla ne.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{375}$ $^{1}/_{13}$)

Sannan akwai waqar *'Ya tara dame mai dama'* wadda Makaxa Maidaji Sabon Birni ya yi wa wani manomi da ake kira Alhaji Xan Bawa. Alhaji Xan Bawa babban attajiri ne da ke zaune a garin Tsauna

cikin Qaramar Hukumar Sabon Birni. A cikin wannan waqa Makaxa Maidaji yana cewa:

Jagora : Kullum dai na zaka yawona,
'Y/ Amshi : In na iske mijin 'yar Kuta,
: Sai ya ba ni dame in xauko.

Jagora : Xan Bawa inai ma horo,
'Y/ Amshi : Kai dai ka tsare horona.
Jagora : To, horon da nikai muku Anna,
'Y/Amshi : Kowa ya riqe kwasatai,
: Ya tara dame mai dama,
: Xan Bawa qanen mai gona.
(Maidaji : Gusau, S. M. 1983: 469-470)

Har wa yau dai, a cikin waqoqin noma na Makaxa Maidaji akwai waqar da ya rera wa wani qasurgumin manomi wanda yake zaune a qauyen da ke kusa da garin Rambaxawa.

Ana kiran wannan manomi da suna Alhaji Isyaka Abarshi wanda ya yi zamani da Makaxa Maidaji. Don har a lokacin gudanar da wannan bincike da na ziyarci garin Rambaxawa wannan manomi yana raye. Allah ya yi masa yalwar gona babba a nan gundumar Tara. A cikin waqar *'Abarshi xan mai damma xan Shibo'* ta wannan manomi Makaxa Maidaji yana cewa:

Jagora : Ina na Mani ga Anne xan Bawa,
'Y/Amshi : Mai katakka da aiki swahe duk.

Jagora : Duk Annen da ba ya da damman gero,
'Y/Amshi : Ba ni kixa mashi turayen dubu.

Jagora : Idan ka ishe xan Anne na noma,
‘Y/Amshi : Azzahwari ta kama yai gida
: Halama bai iya kishin zucci ba,
: Abarshi xan mai damma xan Shibo,
: Xan Shaku da niyya nig ganai.
(Maidaji : Gusau, S. M. 1983: 467-469)

Sannan akwai shahararriyar waqar nan ta noma wato ‘Yar Buhari *‘Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi’*. Wannan waqa an rera ta a lokacin Buhari wato wajejen 1984 shi ya sa ake kiran waqar ‘Yar Buhari. Wannan waqa ta samu karvuwa tsakanin al’umma sosai. Sannan a cikin wannan waqa Makaxa Maidaji ya fito da muhimman abubuwa da babu mai iya maganinsu. Yana cewa:

Jagora : Ka ga kayan gona iri-iri suna cikin qasanmu,
‘Y/Amshi : Don Allah ku qara shuka mana mu ga gujjiya.

Jagora : Sai an sa gero a shuka dawa da su gujjiya,
‘Y/Amshi : A sa masara kuma a shuka rogo a yi lawuru.

Jagora : Sai an sa gero a shuka dawa da su gujjiya,
‘Y/Amshi : A sa masara kuma a shuka rogo a yi lawuru.

Jagora : To, ashe Likita bai da maganin yunwa,
‘Y/Amshi : Wanga magani sai a bixo hura.
Jagora : Na ji malami bai da maganin yunwa,
‘Y/Amshi : Wanga magani sai a bixo hura.
Jagora : Had da ‘yan bori ba su maganin yunwa,
‘Y/Amshi : Wanga magani sai a bixo hura.
Jagora : Had da bokaye ba su maganin yunwa,
‘Y/Amshi : Wanga magani sai a bixo hura.
Jagora : Maganin yunwa kudaku da rogo da quli-quli,
‘Y/Amshi : In anka haxa su kuma a dawo ga hwaro-hwaro,

: Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.
(Maidaji : Hira da Rima Rediyo, Sakkwato)

Wasu daga cikin waqoqin noma na Makaxa Maidaji Sabon Birni sun haxa da waqar *'Ya hana aikin yini'* ta Alhaji Muhammadu Xanqoqari da waqar *'In zo kixi inda Sani na Ummu'* ta Alhaji Muhammadu Sani na Ummu da waqar nan ta *'Wuce maza xan kurma'* ta Alhaji Mamman Xankaltu da sauransu da dama. Binciken nan ya gano yawanci waxannan manoma na qasar Sabon Birni waxanda suke da kusancin unguwanni da na Makaxa Maidaji.

3.3.3 Waqoqin Jama'a

Waqoqin Jama'a a nan sun qunshi waqoqin da Makaxa Maidaji Sabon Birni ya yi wa mutane waxanda ba sa riqe da wani matsayi na sarauta. Daga cikinsu akwai waxanda ya yi wa attajirai, wato waqoqi waxanda ake yi wa masu hannu da shuni da na malamai da na ma'aikata, daxa masu aiki na qaramar hukuma ne ko na gwamnatin jiha ne ko ma na gwamnatin tarayya ne.

Makaxa Maidaji Sabon Birni ya rera waqoqi na musamman ga mashahuran mutane waxanda suka bayar da gudummuwarsu wajen inganta rayuwar al'umma ta fannoni daban-daban. Wannan bincike ya

gano akwai waqoqin da Maidaji ya yi wa manyan mutanen qasar nan irin su tsohon Shugaban Qasar Nijeriya, Alhaji Shehu Aliyu Shagari da tsohon Gwamnan Jihar Sakkwato, Alhaji Garba Nadama da Alhaji Hashimu Tsohon D.P.O. na ‘Yansanda a garin Gusau jihar Zamfara da sauransu da dama.

Daga ire-iren waqoqin Makaxa Maidaji na jama’a sun haxa da waqar ‘*Barka da shirin zamani’* wadda ya yi wa Alqalin Sabon Birni Malam, a waqar akwai inda yake cewa:

Jagora : Alqalin Sabon Birni,
‘Y/Amshi : Maganatai yanzu tana Ingila.

Jagora : Masu ruwan kihi nasu na,
‘Y/Amshi : Talakkawa sarki ad da su,
: Kai kau masu gari naka na.

Jagora : Cikin nassi magana ta fita,
: In ka ce a bari ka a yi,
‘Y/Amshi : In ka ce a yi kowa ya yi,
: Malam sai wada kal lissahwa,
: Barka da shirin zamani,
: Malam sannu da gyaran gari.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{378}$ $^{1}/_{4}$)

Sannan Makaxa Maidaji ya yi Waqar *‘A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo’* wadda ya yi wa Alhaji Aliyu na garin ‘Yankuzo, a cikin waqar yana cewa:

Jagora : Xan zaki hay ya qasura,
‘Y/Amshi : Hay ya yi jan wuya ya hiddo qwarai-qwarai.

Jagora : Da nit taho das Sabon Birni,
'Y/Amshi : Nib bi ta Tsahe nit tahi 'Yankuzo,
: In na yi dace ni ishe Ali sai,
: Na yi roqonai ya yi min gida.

Jagora : Ku zo ku ce na kama gida,
'Y/Amshi : Ali had da mata za shi yi min bana,
: A gai min da Alhaji Ali na 'Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{55}$ $^{1}/_{3}$)

Sannan kuma Makaxa Maidaji Sabon Birni ya yi waqar *'Ya wuce tantama'* wadda ya yi wa Alhaji Shu'aibu Salau xan Musa, a cikin waqar yana cewa:

Jagora : Sa'ad da munka tashi Sabon Birni,
'Y/Amshi : Ba mu da ukku xin tsohonai,
: In bayan sarautar Allah,
: Babu abun da yaz zama kullum.
Jagora : Kowas sha hura ba nono,
'Y/Amshi : Ban yi zaton akwai daxi ba.
Jagora : Kowas sha miya ba nama,
'Y/Amshi : Ban yi zaton akwai daxi ba,
: Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu'aibu zamaninai ya kai.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{143}$ $^{1}/_{2}$)

Makaxa Maidaji Sabon Birni ya yi waqar *'Na yi mamakin harka tai'* wadda ya yi wa tsohon shugaban qasar Nijeriya, Alhaji Aliyu Shehu Shagari, a cikin Waqar yana cewa:

Jagora : Shugaban qasa Allah kyauta mai,
'Y/Amshi : Zaman mutane na murnatai.
Jagora : Shugaba na can na aikinai,

‘Y/Amshi : Yana ta yin gaba bai hwasa ba,
: Yana ta yin aikin al’adu,
: Saboda koyon addini ne.

Jagora : ‘Yan makaranta kui ta karatu,
‘Y/Amshi : Ku zan ka yin aikin al’adu,
: Saboda koyon addini ne,
: Na yi mamakin harkatai,
: Shehu mai daraja Shagari.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{52}$ $^{1}/_{5}$)

Sannan kuma Makaxa Maidaji Sabon Birni ya yi waqar *‘Allah za ni roqonka’* wadda ya yi wa tsohon gwamnan Jihar Sakkwato, Alhaji Garba Nadama, a cikin waqar yana cewa:

Jagora : Allah za ni roqon ka,
: In yi biyag gwamna mai girma.
Jagora : Ko can duniya haka,
: Tag gada inji mai tulu,
‘Y/Amshi : Ka san duniya daxa,
: Ba mai hurce iyakatai.

Jagora : Babu abin da yai min ciwo,
: Allah ni ke kallo,
‘Y/Amshi : Ga ni ina kixin Gwamna,
: Ba ni da motad da za ni hawa,
: Allah za ni roqonka,
: In yi biyag gwamna mai girma.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{52}$ $^{1}/_{6}$)

Sai kuma cikin waqar nan ta *‘Na shira kaya za ni garai’* ta Alhaji Hashimu, Tsohon D.P.O na ‘Yansanda a garin Gusau cikin jihar Zamfara a wannan waqa akwai inda Makaxa Maidaji yake cewa:

Jagora : Hashimu uban tawaye,
'Y/Amshi : Hashimu dum mai biyak ka,

: Ya huta da tsiya sai ya sami kuxxi yai shagali.

Jagora : Maidaji cikin daji nike,
'Y/Amshi : Hashimu yi tattalin mai da ni gari,
: Tun da ba Bahillace nike ba,
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.

(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{51}$ $^{1}/_{3}$ – AL $^{0}/_{74}$ $^{1}/_{1}$)

3.3.4 Waqoqin Siyasa

A luggance kalmar siyasa na nufin ‘jin qayi’ ko ‘rangwame’ (Abraham, 1962: 819). A wani wuri kuma “an nuna yin hulxa da taron jama’a, ko tsayuwar mutane a kan wani ra’ayi, ko kuma yin rangwame a harkokin rayuwa shi ne siyasa” (CNHN, 1979: 112). A Larabci kalmar “siyasa na nufin gudanar da mulki ko tafiyar da mulkin jama’a da ba kowa haqqinsa” (Gusau, 1990:2). Za a iya kallon waqoqin siyasa musamman na waqoqin baka na Hausa ta fuska biyu:

- Siyasa ta Gaba Xaya
- Siyasa ta Jam’iyya

3.3.4.1 Waqoqin Siyasa ta Gaba Xaya

Makaxan baka sukan kalli siyasar da ke tsakanin gidajen da ke da gadon sarauta. Kuma sukan xauki vangare, musamman vangaren ubangidansu wanda suke yi wa waqa, ta hanyar bayyana kishin kai da burinsu na ya zama sarki. Sukan fito da kishinsu a cikin waqoqinsu, a

bayyane ta hanyar zuga ko yabo ko kuma a voye cikin zambo da habaici da kuma kinaya. Makaxan baka sukan tasirantu dumu-dumu wajen qoqarin fifita ubangidansu sama da abokin hamayya.

Wannan ya sa masana da manazarta suke kallon "Siyasa ta gaba xaya ita ce wadda ta qunshi kishin qasa ko kishin kai ko kuma ta addini" (Tijjani, 1979: 261-263; Aliyu, 1990: 64; Gusau, 2008: 381).

Idan ubangidansu ya zama sarki, sukan bayyana murnarsu da farin cikinsu, daga bisani kuma su haxa da gori da tsamgwama da gidan sarautar da ya sha kaye. Misali a waqar *'Uban Makama uban Gardaye'* wadda Makaxa Maidaji Sabon Birni ya yi wa Sarkin Gobir, Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003) ya fito mana da irin wannan batu, domin a cikin waqar yana cewa:

Jagora : Ina mazan suke?
'Y/Amshi : Sarkin Gobir ina mazan suke duk sun qare.
Jagora : 'Yan sarki kowa ya yi gona,
'Y/Amshi : Tun da Bawa na Habu ya kama,
: Ban san mai iya bankatai ba,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{144}$ $^{1}/_{1}$ – AL $^{1}/_{144}$ $^{1}/_{2}$)

Haka nan kuma a waqar *'Na zaka barka da azzukka'* wadda Makaxa Maidaji Sabon Birni ya yi wa Sarkin Madawa, Alhaji Muhammadu ya bayyana irin faxi tashin da aka shiga yayin neman

wannan sarauta. Daga bisani, Allah ya ba da nasara saboda haka yaqi ya faxi sai dai a bi sarki. Ga dai abin da yake cewa:

Jagora : Ko can na san gidan kadannu,
'Y/Amshi : Sai 'yan taru,
: Yaqi ya hwaxi 'yan hawa sun dawo ganga.

Jagora : Wanga gidan tawaye ne,
'Y/Amshi : Gidan Jibo sarki yag gado,
: Hwaxa masu ba mai shiga gidan,
: Sai in bayan kai,
: Na zaka barka da azzukka,
: Sarkin Madawa Muhammadu,
: Ko yanzu duniya ta yo mai haske.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{376}$ $^{1}/_{7}$)

Har wa yau, a waqar *'Bunu xan baraz zaki'* wadda Makaxa Maidaji Sabon Birni ya yi wa Sarkin Gobir, Alhaji Ummaru xan Salihu (1957-1966) ya qara da cewa:

Jagora : To, ina masu son sarki,
'Y/Amshi : In an ka duba suna hwamab banza.
Jagora : Ga wani na jiran sarki,
'Y/Amshi : Daxa sai ya koma jiran sarkin karma.
Jagora : Mu sai mai takobi da hamilo,
'Y/Amshi : Da taggo da wandon dirbanci,
: Na Malam gwanin daga,
: Na Allah jikan hillani xan Musa na Malam.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{147}$ $^{1}/_{6}$)

A taqaice Makaxa Maidaji, ya tasirantu da siyasar masarautarsa ta Sabon Birni. Ya samu cikakkiyar karvuwa tsakaninsa da sarakunan

Sabon Birni, tun daga Sarki Umaru Na-Allah (1957-1966) da Sarki Ibrahim (1966-1975) har zuwa Sarki Muhammad (1975-2003).

3.3.4.2 Siyasa ta Jam'iyya

Makaxa suna yin waqoqin ne domin samun qafa da yaxa hamayyar da ke tsakanin jam'iyyun don muzanta saura. Haka kuma suna yin waqoqin domin yaqin neman zave domin samun rinjaye da samun karvuwa da farin jini ga al'umma. Domin haka, waxannan jam'iyyu sun zamo suna da waqoqi da dama masu fitacciyar manufa wajen isar da saqo. A qasar Hausa, mawaqan baka sun taka muhimmiyar rawa wajen gina siyasa da samar da madogararta a yankin arewacin Nijeriya. An yi waqoqi birjik ga jam'iyyun NPC da NEPU da NPN da SDP da NRC da ANPP da PDP da dai sauransu. Wasu masana da manazarta suna ganin:

> Idan muka waiwayo siyasa ta jam'iyya kuma, ta faro ne daga zuwan Turawa inda 'yan qasa suka dage wajen tattara mutane masu ra'ayi da aqida iri xaya suka yi qoqarin kafa jam'iyyu domin qwato 'yancin qasa daga Turawan Mulkin Mallaka zuwa ga 'yan qasa. Manufar gudanar da waxannan waqoqi ita ce domin qoqarin wayar da kan jama'a a kan manufofin xan takara da jam'iyyarsa

don neman goyon bayan jama'a da amincewarsu (Tijjani, 1979: 263; Ubah, 1979: 296-297).

A iya cewa, waqoqin siyasa a yanzu sun zamo waqoqin da ke xauke da zance na hikima ta hanyar amfani da salo na kixan zamani wajen isar da jigonta wanda ka iya zama na faxakarwa ko na qasqantarwa ko kuma na qwarzantawa.

Makaxa Maidaji Sabon Birni ba a bar shi baya ba domin ya yi waqoqin siyasa da dama tun daga na jam'iyya har zuwa na mutane masu siyasa xin. Daga cikin waqoqin siyasar waxanda suka zo hannu a yayin gudanar da wannan bincike sun haxa da waqarsa ta '*Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi'* wadda ya yi wa jam'iyyar N. P. N. da waqar Alhaji Bakwai, N.P.N da ke garin Sabon Birni.

Idan aka kalli wannan waqa ta *'Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi'* wadda Makaxa Maidaji ya rera wa Jam'iyyar N.P.N a lokacin mulkin Alhaji Shehu Kangiwa a matsayin gwamnan Sakkwato da kuma lokacin mulkin Alhaji Shehu Aliyu Shagari na shugabancin qasar Nijeriya tsakanin shekara ta 1979-1981. Makaxa Maidaji ya xaukaka wannan jam'iyya sama da kowacce a cikin wannan waqa. A cikin waqar yana faxakar da mutane da su riqe jam'iyyar N.P.N

qwarai domin kada jama'a 'su saki reshe su kama ganye' wanda ka iya zame musu 'zaven tumun dare'. Ga dai abin da yake cewa:

Jagora : Ga masara ga gero to, kuma ga shinkahwa,
'Y/Amshi : Gwamnati ta shirya babu mai rigan mu da daxi.
Jagora : Gwamnati ta ba mu ruwa,
: To, har yanzu da saura,
: Tai mana lantarki don garinmu yai mana haske,
'Y/Amshi : Gwamnati ta shirya babu mai rigan mu da daxi.

Jagora : To, na ga jam'iyyar su wane sun shirya mana qarya,
'Y/Amshi : Tun da qarya ta shugabanmu ba shi da qarya.
Jagora : Sun ce sui mana gulbin hura su sa mana gulbi,
'Y/Amshi : Bayan nuhwar Allah babu mai hana mana noma.

Jagora : Bayan nuhwar Allah,
'Y/Amshi : Babu mai hana mana noma,
: Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi,
: Gwamnati N. P. N mai biyak ku ba shi da haushi.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{147}$ $^{1}/_{1}$)

Makaxa Maidaji Sabon Birni ya rera wa Alhaji Muhammadu Xanqoqari ta *'Sai mu taru mu yi roqon Allah'*. A wasu xiya na wannan waqa yana cewa:

Jagora : Alheri shi kai mu Sabon Birni,
'Y/Amshi : Tun da can aka shirawad duniya.

Jagora : In ka ji an yi magana ta zauna,
'Y/Amshi : Yanzu ba wata magana sai Legas.

Jagora : To, kowa shi hanqure, Babari,
'Y/Amshi : Da Gwamna sun yi magana ta zauna,
: Sai mu taru mu yi roqon Allah,
: Inda Alhaji Bakwai N.P.N.

(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{75}$ $^{1}/_{10}$)

3.4 Jigo a Waqoqin Makaxa Maidaji

Al'adar makaxan baka na fada ita ce yi wa sarakuna da kuma jinin sarauta ko wani wanda ya danganci sarauta waqa. Canjin zamani ne ya haddasa bazamar makaxan baka aiwatar da waqa ga malamai da attajirai da jami'an gwamnati har ma da 'yan siyasa da sauransu. Ta haka ne manazarta waqar baka ta Hausa suke nazarin jigo bisa alqibla daban-daban, wannan ne ya sa akan sami mabambantan jigogi a waqoqin da suke rerawa a yanzu.

Dangane da jigo a waqoqin Makaxa Maidaji Sabon Birni za a fahimci waqoqin nasa suna xauke da mabambantan jigogi kamar haka:

3.4.1 Jigon Yabo

Kalmar yabo babban jigo ne da makaxan baka suka fi yawaita yin waqa a kai. "Yabo kusan shi ne fitaccen jigo na waqoqin baka na Hausa domin mafi yawan waqoqin manufofinsu kan zamanto yabon waxanda ake yi wa su ne" (Gusau, 2008:376).

Wasu manazarta suna ganin “yabo ya qunshi ambaton kalmomin sambarka da nufin nuna amincewa da hali ko wani abin da mutum ya yi nagari” (Kunene, 1971:15).

Ko kuma a iya cewa “yabo wani lafazi ne da ake yi ga wani mutum domin a nuna halayensa da siffofinsa kyawawa da cewa abin so ne kuma abin qauna ne” (Sada, 1979:39). Duk da cewa Tsoho (2001) na ganin matsayin:

> Yabau a waqoqin fada na Hausa bai wuce na yabon ba wanda ake amfani da shi wajen tsima ubangida ya yi kyauta ta gani ta faxa. Tsoho (2001) ya bayyana kalmomi waxanda makaxa kan yi amfani da su wajen gina waxanda sukan zama tubali na ginin yabo suna zama ne a matsayin ‘yabau’ ne. Da zarar an cire kalmomin yabau zai zama kwatata babu wani tubali da zai nuna wannan furuci na yabo ne. Ken an, da yabau ne makaxan fada kan yi amfani don waqe da kambama tare da gwada xaukakar sarkinsu a kan talakawa (Tsoho, 2001:68-71).

Manazarta irin Kunene (1971: 47-52) da Bello (1976:24-29) da Sada (1979:40-41) da Ibrahim (1983:11-13) da Gambo (1990: 30-36) da Tsoho (2001:71-83) har ma da Gusau (2008:376) sun raja’a a kan cewa ana gina gundarin jigon yabo ne ta amfani da tubalai waxanda suka haxa da addini da asali ko nasaba ko zuri’a da kyauta ko karimci

ko baiwa da sifa da iya mulki (ga sarakuna) da jaruntakar yaqi da hali da xabi'a da kirari da roqo da habaici da zambo ga wani.

Makaxa Maidaji kan yaba aikin ubagidansa domin fito da abin a sarari domin al'umma su tabbatar. Ya kan zama 'kakaki abin magana' ga iyayen gidansa ko da kuwa zai tsawaita xan waqa ne.

Ta la'akari da waxannan abubuwa ne wannan bincike ya tsinto wasu wuraren da Makaxa Maidaji ya yi amfani da yabo a cikin waqoqisa. A waqar '*Sarki yai abin daka ya huta*' ta Alhaji Abdussalam Arzika, Makaxa Maidaji yana yaba kyawawan halayen wannan mashahurin manomi a qasar Sabon Birni kamar haka:

Jagora : Ina Arzika xan Imamu bawan Alllah,
: Bai ci amanar gida ba balle daji.
Jagora : Arzika jikan Salau magajin Sanda,
: Zaki mai kasam ma kainai nama.

Jagora : Arzika tun zamanin kana xan yaro,
: Hak kak kai kana cikin qarninka,
: To hay yau ba a ganai da matar wani ba.
Jagora : Hwaxa ma samarin ga masu son matanmu,
: Hwaxa musu Alhaji mai kixi ya gane,
'Y/Amshi : Sarki yai abin daka ya huta,
: Zaki xan Abubakar xan Buda.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{2}$)

Dubi abin da Makaxa Maidaji yake faxa na yabo ga Tsohon Shugaban qasar Nijeriya, Alhaji Shehu Aliyu Shagari a waqar nan ta '*Na yi mamakin harkatai'* kamar haka:

Jagora : Kaduna an gyare hanya,
'Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Zariya an gyare hanya,
'Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Huntuwa an gyare hanya,
'Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Tcahe an gyare hanya,
'Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Kwatarkwashi an gyare hanya,
'Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Hag Gusau an gyare hanya,
'Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Qaura an gyare hanya,
'Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Shinkahi an gyare hanya,
'Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Har Isa an gyare hanya,
'Y/Amshi : An yi godabe an sa mai kwalta.
Jagora : Sabon Birni mu bar garaje,
'Y/Amshi : Han mu kwalta na kawowa,
: Kowa ga hwanho qohwatai,
: Na yi mamakin harkatai,
: Shehu mai daraja Shagari.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{5}$)

A cikin Waqar *'Uban Na-Allah uban Madauci'* da Makaxa Maidaji ya rera wa Sarkin Zazzau, Alhaji Shehu Idris (1975-) qara fito da tasirin yabo a cikin waqoqinsa. Yana cewa:

Jagora : Alhaji Mani ba shi qin kowa,
: Komi kac ce yanai ma,
: Don bai tsare za'ida ba.

Jagora : Sarki da hanquri aka tsara taro,
'Y/Amshi : Ka diba duk kwararon qasag ga,
: Duk Shehu, Alhaji ya haxe su,

: Uban Na Allah uban Madauci,
: Shehu sannu da yau da gobe.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$)

Har wa yau dai cikin Waqar *'Ya wuce tantama'* Makaxa Maidaji ya qara fito da misalin yabo a cikin waqoqinsa. A wannan waqa ta Alhaji Shehu Kunda cewa ya yi:

Jagora : Allah yai maka hairan,
'Y/Amshi : Allah bai yi ka don ka sha haushi ba.
Jagora : Sa'ad da munka tashi Sabon Birni,
'Y/Amshi : Ba mu da ukku xin tsohonai,
: In bayan sarautar Allah,
: Babu abun da yaz zama kullum.

Jagora : Kowas sha hura ba nono,
'Y/Amshi : Ban yi zaton akwai daxi ba.
Jagora : Kowas sha miya ba nama,
'Y/Amshi : Ban yi zaton akwai daxi ba.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{143}$ $^{1}/_{2}$)

Can kuma cikin wannan waqa ta *'Ya wuce tantama'* Makaxa Maidaji ya ci gaba da kwarzanta tare da kambama Alhaji Shu'aibu Salau xan Musa a xiyan waqarsa cikin wannan tsari kamar haka:

Jagora : Ni da dai nas sauka Sabon Birni,
: To, na sauka ko han na kwan,
'Y/Amshi : Na ishe yara na wata waqa,
: To, ko yara kau ko 'yam mata,
: Sun ce wanda yas sai nama,
: Ya xara wanda yas sai kihi.
Jagora : To kuma wanda yas sai anta,
'Y/Amshi : Ya xara wanda yas sai hanji,

Jagora : To kuma wanda yas sai doya,
'Y/Amshi : Ya xara wanda yas sai gwaza,
Jagora : To kuma wanda yas sai doki,
'Y/Amshi : Ya xara wanda yas sai jakki,
: Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu'aibu zamaninai ya kai.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{143}$ $^{1}/_{2}$)

Har wa yau, a waqar *'A gai min da Alhaji Ali na 'Yankuzo'* ta Alhaji Abubakar, Makaxa Maidaji cewa ya yi:

Jagora : Gidan Mamman nit taho kixi sai na gai sai,
'Y/Amshi : Sai ga Audu xan Bala ga Musa nan,
: Komi nib bixa ga yau sai an yo min.

Jagora : Ga wani horo da zan hwaxa ma xan Shawai,
'Y/Amshi : Allah sa ka xauki horon in na yi.

Jagora : Ai kyawon xa shi xauki horon tsohonai,
'Y/Amshi : Ai ban ce ka xauki horon kowa ba,
: Ni ban ce ka xauki horon kowa ba.

Jagora : In ka ishe xan baqo bakin garkatai,
'Y/Amshi : Kai ka san akwai duhu bayan qumci,
: Dogo xan Abubakar na Malumfashi,
: Jikan Dabo xan Kilo gwamron giwa.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{4}$)

A taqaice, mafi akasarin waqoqin Makaxa Maidaji ya gina su a kan yabo ne. Wasu waqoqinsa na yabo sun haxa da waqar 'ya kwan cikin shiri ya tashi tsaye' da Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Abdulhamid (2003-) da waqar xan Sarkin Gangara, Alhaji Isa Baraz Zaki ta 'yai halin mazan jiya isa maqi garaje'. Akwai kuma waqar

Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Umaru Na-Allah ta ‘binu xan Baraz zaki’ da sauransu da dama. Makaxa Maidaji yakan gina waqoqinsa bisa tsari na nishaxantarwa da koxarwa da nusarwa da nasaba da gargaxi da wayar da kai da ta’aziyya da sauran manufofi.

3.4.2 Jigon Zuga

Zuga dabara ce ta xaukaka abu sama wadda ta qunshi wasu kalmomi da ake amfani da su a koxa mutum, a cicciva shi, a nuna fifikonsa kan wasu. “Zuga takan tsuma mutum ta sa masa kuzari da qwarin gwiwa” (Gusau, 2002[a]:29). A wajen zuga mutum “akan yi amfani da kalmomin wasawa ko kumburawa ko ban tsoro ko ciccivawa ko razanarwa ko fifitawa ko naqasawa da tauye zangon daraja da sauransu” (Bello, 1976:24-29).

“Zuga na sa wanda aka yi wa ita ya yi xaukar duman Magaji da nishi, wato ko bai iya abu ya ce sai ya yi” (Bunza, 2009:147-148). Wato dai “makaxi yakan zuga ubangidansa, har ya kai shi kan darajar da Allah bai kai shi ba” (Ibrahim, 1983: 9). Kenan, da zuga da kirari bori xaya suke yi wa tsafi, a kowane lokaci zuga ta cika ba za a rasa kirari a cikinta ba.

Haqiqa, Makaxa Maidaji gwani ne wajen shirya waqa qunshe da zuga. Ya rera waqoqi da dama xauke da zuga, musamman ma ganin ya yi waqoqin sarakuna masu ximbin yawa. Akwai waqar noma da ya kambama gonar manomin da cewa gabas da arewa, gandun nan ya kai mil xari sittin. Ga dai abin da Makaxa Maidaji ya rattabo a cikin waqar:

Jagora : Gandun Xangara yai gandu ko ga ‘yan dauri,
‘Y/Amshi : In don na yanzu ba gandu mai misalinai.
Jagora : Gandun Xangara ya yi gabas mil xari sittin,
: Na yi yamma na diba mil xari sittin,
: Gandun Xangara ya yi gusum mil xari sittin,
: Kuma nai arewa na diba mil xari sittin,
‘Y/Amshi : Abin da za a yi ciki ab ba mu gane ba.
Jagora : In za a sussukak damma sai a yo gayya,
: Makobiya dubu kowace ta yi buhu maitan,
‘Y/Amshi : Ai sai a yo kiran ‘yan boko ku lisafta,
: Na yi hamdala nai shukura da godewa,
: Tun da na sani noma yau farilla ne.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{175}$ $^{1}/_{13}$)

Sannan a waqar nan *ta’Ibrahim Xanmakoxa rainai yay haske’ da* Makaxa Maidaji ya rera wa Xangaran Sabon Birni, Alhaji Ibrahim, ya kawo zuga ne kamar haka:

Jagora : Bajinin Shi’itu,
: Abin da yas shira tun can hwarko,
‘Y/Amshi : Hay yau bai saba qulle-qullen banza ba.

Jagora : Ashe daka sai mata,
‘Y/Amshi : Kashin bisashe sai kura,
: Hawan doki sai Ba’auzine sai ‘yan sarki,
: Ga mu muna kallon mai kixi ana kallon kura,

: Su Alhaji Maidaji yau ana kallon-kallo.

Jagora : Yara mi an ma'anad da za ku yin kallon-kallon,
'Y/Amshi : Mu ba mu gane ba tun da ba mu zama birni,
: Ibrahim Xanmakoxa rainai yay haske,
: Na zaka in gai da Xangaran Sabon Birni.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{377}$ $^{1}/_{2}$)

A waqar da Makaxa Maidaji ya rera wa Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Umaru Na-Allah (1957-1966) ya kwarzanta sarki yayin wata shiga da sarkin ya yi a wani taro wanda sai da sarauniyar Ingila ta yi tambaya da cewa wannan sarkin wane gari ne? Tirqashi:

Jagora : Giwa ta hi gangarawa kuma tahi gewaye,
'Y/Amshi : Darzaze take ga rahi.

Jagora : Katakoren gidan Muhamman,
'Y/Amshi : Bajimin gidan Kada.

Jagora : Sarauniya da tas sabka tay yi girgiza,
'Y/Amshi : Sai tac ce ma Garba,
: Wannan sarkin wace jiha ne,
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin Magatakarda.
(Maidaji : Xahiru, G. (1990: 103-105)

Wasu waqoqin Makaxa Maidaji waxanda aka gina su a kan jigon zuga akwai waqar 'kai ab bahagon gulbi' ta Sarkin Gobir na Sabon Birni Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003) da waqar 'Gagari gaba na Salihu' ta Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Umaru Na-Allah xan Shawai (1966-1975) da waqar 'Balaraben Sarki' ta Sarkin

Zazzau Alhaji Shehu Idris (1975-) da waqar nan ta ‘ya wuce tantama’ ta Alhaji Shu’aibu Kunda. Akwai kuma waqar nan ta Innar Gobir ta Sabon Birni da Makaxa Maidaji ya rera wato ‘kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa’ ita ma tana xauke ne da zuga.

3.4.3 Jigon Faxakarwa

Jigon faxakarwa a waqoqin baka na Hausa yakan yi qoqari ne ya sanar da al’umma wasu abubuwa sababbi da suke aukuwa a rayuwar yau da gobe na zamantakewa.

Faxakarwa na nufin gargaxi wanda ya qunshi tunasarwa kan ‘yi’ ko ‘bari’ da yi wa mutum hannunka mai sanda cikin nusarwa da tsoratarwa, da amfani da sauran hanyoyin gyaran zama ko Kan Gyaran Rayuwa.

“Wannan na nufin faxakar da mutane a kan wani abu marar kyau da suke aikatawa da su daina ko su gyara ko a qarfafa riqo da wani aiki mai kyau” (Chamo, 2005:82). Wasu manazarta suna ganin fakakarwa na nufin “nuna halin xa’a wanda zai kasance tsayayyiyar hanya xauke da ma’aunin haliyyar xan’adam na zahiri da son rai, kuma ya kasance a kawar da aiwatar da wata halayya mara kyau da mai kyau” (Encyclopaedia Britannica, 1943-1973: 11).

Shi kuma ‘Yar’adua (2001) yana ganin manufar faxakarwa bai wuce “nusar da mutum a kan abubuwan da ya sani tun tuni, amma saboda sakaci ya kyale su ya manta da su” (‘Yar’adua, 2001: 126).

Shi kuwa a ra’ayin Bargery (1934) yana ganin faxakarwa ta danganci “tunasarwa tare da sa qaimi don a zaburar da mutum ya fahimci abu na haqiqa” (Bargery, 1934: 285). Don haka, faxakarwa ta qunshi yin tuni da hannunka-mai-sanda ga al’umma na gyara kayanka wanda ba zai zama sauke mu raba ba.

Mafi akasarin lokuta gwamnati kan umurci sarakuna su faxakar da talakawansu game da abubuwa masu aukuwa. Sau tari da yawa, waqoqin baka kan yi qoqarin fahimtar da jama’a shi waxannan abubuwa. Ta haka ne waqoqin baka ke taimakawa wajen yi wa jama’a sanarwa da wa’azi da gargaxi da jan kunne da kuma wayar da kai.

Duba da ayyukan Chamo (2005:82) da Gusau (2008:384) da (‘Yar’adua, 2001: 126) suna bisa ra’ayin cewa a adabin Hausa galibinsa tattare yake da tadodin faxakarwa da suka danganci kiwon lafiya da zaman tare tsakanin ‘ya’ya da iyaye da ma’aurata da kuma qasa baki xaya. Sannan ayyukan adabin Hausa maqil suke da sigogin faxakarwa na gyara hali da faxakarwa game da masu zalunci da

tarbiyya da shugabanci da sauran makamantansu a waqe ne, ko a wasan kwaikwayo kuma a cikin qagaggun labarai da tatsuniyoyi ne.

Makaxa Maidaji Sabon Birni mawaqi ne wanda ya ginu game da waqoqi xauke da tasirin faxakarwa. Makaxi ne wanda yake gina waqoqinsa cikin tsari na yabo da zuga sannan daga bisani ya cike waqarsa da faxakarwa domin isar da manufarsa. Wannan ya sa yawanci waqoqinsa sun ginu bisa saqo ayyananne.

Misali, Makaxa Maidaji yana nuna muhimmancin neman ilmi a rayuwar al'umma da tsayar da gaskiya a dukkan al'amura. Hausawa na cewa 'ilmi gishirin zaman duniya'. Ga abin da ya ce:

Jagora : In dai mutum yav vace,
: Maisai ga hanya mukai,
'Y/Amshi : In ko mutum ya qiya,
: Mu iza shi bayan gida.

Jagora : In noma mutum za shi yi,
'Y/Amshi : Kuma in hwatauci ya kai,
: Ya gama da ban-gaskiya.

Jagora : To, ashe zaman duniya,
'Y/Amshi : Kowa nashi aiki shikai,
: Abin da wani ba shi so,
: Wani na bixa tai qwarai,
: Harka da ilmi mukai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{147}$ $^{1}/_{2}$)

Sannan a cikin waqar da Makaxa Maidaji ya rera wa Sarkin Zazzau Alhaji Shehu Idris (1975-) yana faxakar da al'umma duk rai yana son zama da mai faranta masa, kuma yana gudun duk abin da zai vata shi. Yana horon al'umma da su sa qaimi wajen aikata ayyukan alheri tare da inganta zumunta da dai sauran kyawawan halaye. Sannan, ya ci gaba da faxakar da al'umma cewa duk wanda ya roqi kuma ya xaukaka ubangiji to, ba zai tave ba. Ga dai abin da ya ce:

Jagora : Akwai maza suna ga duniya duk ba a gane ba,
'Y/Amshi : Sai in bincika an tona za a ganewa.

Jagora : Ni Maidaji na yi tonon duniya ga nawa xan wayo,
'Y/Amshi : Wanda duk ka sa ma sharri ba ka mance shi.

Jagora : Ai cikin kashi biyu, Allah ba ya mance su,
: Wanda yay yi ma alheri,
'Y/Amshi : Wanda yay yi ma sharri ba ka mance shi.

Jagora : Duk wanda yay yi man alheri,
: Ina ta gai da shi,
'Y/Amshi : Wanda ba shi ban alheri, ba ni gai da shi,
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqon Allah ba ya tavewa.
(Maidaji : Gusau, S. M.1983: 612-615)

Sannan a waqar Sarkin Tsibirin Gabas, Alhaji Aliyu, Makaxa Maidaji ya rera wani xa da yake faxakar da al'umma da mutum ya sani duniya ba matabbaciya ce ba. Yana horon mutane da aikata ayyukan qwarai don inganta rayuwa. Ga abin da yake cewa:

Jagora : Gobirawa kui muna gahwara,
'Y/Amshi : Alhaji ban kwana yakai,
: Ba mu san ta rai ba ga duniya.

Jagora : Allah da yat tsira duniya,
'Y/Amshi : Ya yo ta don a yi shawara,
: Na zo ganin bajinin qani,
: Ali Sarkin gidanmu na can Gubur,
: Alhaji ya zaka lahiya.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{376}$ $^{1}/_{4}$)

Can kuma cikin waqar *'Jikan goye Kaso xan Kaso'* ta Sarkin Gidan Rumji, Alhaji Kaso Sanda, Makaxa Maidaji yana faxakar da al'umma su sani cewa komai daga Allah yake domin shi ne masanin gaibi. Ga dai abin da yake faxa cikin xiya na wannan waqa:

Jagora : Duw wada Allah ka yi ya gama,
'Y/Amshi : Shi Allah ba ya yin shawara,
: Komi yat tashi yinai yakai.

Jagora : Ko can haka nan duniya ta'iya,
'Y/Amshi : In wasu sun kwan suna lahiya,
: Wasu ko sun tashi ba lahiya.
Jagora : Ga wasu can sun aje jikkuna,
'Y/Amshi : Wasu kau sun tashi ba ko kwabo.
Jagora : Wasu sun yi dawaki suna riguna,
'Y/Amshi : Wasu kau sai xarma walki sukai,
: Jikan goye Kaso xan Kaso,
: Sarki xan Sanda mai duniya.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{1}$)

Makaxa Maidaji ya rera waqa ta musamman yana faxakar da mata da su yi aure tare da riqo da shi. Ya kwatanta matar da taqi sunnar Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, to, ta qi bin

umurnin ubangiji ne, za ta fuskanci fushin Allah. Sannan ya ci gaba da kwaxaitar da mata su zama masu haquri da zaman aure. Sannan ya danganta wadda ta rufa asiri ga sirrin mijinta, tana xaukar xabi'ar matan aljanna. Ga dai abin da yake cewa:

Jagora : Mata ku yi aure kuma,
'Y/Amshi : Ku zan ka addini shi ag gishirin zama.
Jagora : Cikin nassi aka aure,
'Y/Amshi : Kuma cikin nassi aka tagazag gida,
Jagora : Maccen da ka aure,
'Y/Amshi : Tai hikima ki wanka daga ciki,
Jagora : Maccen da ba ta aure,
'Y/Amshi : Fatsima na can na watsa mata qasa,
: Mata in ba ku ba gida,
: Wurin Allah ku ash shikashiki.
(Maidaji : Hirarsa Rima Rediyo)

Makaxa Maidaji yana nuna muhimmancin neman ilmi a rayuwar al'umma da tsayar da gaskiya a dukkan al'amura. Hausawa na cewa 'ilmi gishirin zaman duniya' sannan kuma suka ce 'in za ka faxi gaskiya, komi taka ja maka ka biya'. Ga abin da ya ce:

Jagora : In dai mutum yav vace,
: Maisai ga hanya mu kai,
'Y/Amshi : In ko mutum ya qiya,
: Mu iza shi bayan gida.

Jagora : In noma mutum za shi yi,
'Y/Amshi : Kuma in hwatauci ya kai,
: Ya gama da ban-gaskiya.

Jagora : To, ashe zaman duniya,
'Y/Amshi : Kowa na shi aiki shi kai,
: Abin da wani ba shi so,

: Wani na bixa tai qwarai,
: Harka da ilmi mu kai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya.

(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{147}$ $^{1}/_{2}$)

3.4.4 Jigon Siyasa

Idan ana magana dangane da waqoqin siyasa yana da kyau a kalli abubuwa guda biyu; *siyasa* da *waqa*. "Siyasa a gun Bahaushe na nufin sanin makama ta yadda za a fuskanci abu da kuma yadda za a gudanar da shi" (Yahaya, 1997: 20-30).

Siyasa ta qunshi jam'iyyu daban-daban, saboda haka, akwai waqoqi na tsofaffin jam'iyyu da dama tun kafin 1966, daga cikinsu akwai NEPU da NPC da NPN da NCNC da AG da dai sauransu. Tun daga wannan lokaci har zuwa yanzu ake samun waqoqin siyasa da jam'iyyu daban-daban da suka haxa da NRC da SDP da DPN da PDP da ANPP da ACN da CPC da sauransu. Misali waqoqin siyasa na baka sun haxa da waqar 'Samun 'yancin Nijeriya a 1960' ta Muhammadu Sarkin Taushin Katsina da waqar 'Sanata Isa Kachako' ta Alhaji Dr. Mamman Shata Katsina.

Kamar yadda wannan bincike ya bayyana a baya, daga cikin waqoqin siyasa waxanda Makaxa Maidaji ya rera xauke da jigon

siyasa akwai ta '*Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi'* wadda ya yi wa jam'iyyar N. P. N. Akwai kuma inda yake cewa:

Jagora : To, na ga jam'iyyar su wane sun shirya mana qarya,
'Y/Amshi : Tun da qarya ta shugabanmu ba shi da qarya.

Jagora : Sun ce sui mana gulbin hura su sa mana gulbi,
'Y/Amshi : Bayan nuhwar Allah babu mai hana mana noma,
: Gaskiya ta yi halinta an shirya mana komi,
: Gwamnati N. P. N mai biyak ku ba shi da haushi.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{147}$ $^{1}/_{1}$)

Wata waqar siyasa da wannan bincike ya gano ita ce waqar '*Sai mu taru mu yi roqon Allah'* wadda Makaxa Maidaji ya rera wa Alhaji Bakwai N. P. N. Ga wasu xiyan waqar kamar haka:

Jagora : Uban xan Jari kutunvun vauna,
'Y/Amshi : Babu mai iya tare ma hanya.

Jagora : Gobir babu sauran shairi,
'Y/Amshi : Tun da masu hitina sun qare
: Sai mu taru mu yi roqon Allah,
: Inda Alhaji Bakwai N.P.N.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{75}$ $^{1}/_{10}$)

Makaxa Maidaji mutum ne mai son bunqasar al'umma musamman qasar Hausa. A waqoqin nan nasa na siyasa ya nuna ingantattun ayyuka da mutane suke buqata. Sannan yana faxakar da mutane da su guji 'yan siyasar soki-burutsu, marasa cika alqawari.

Duk da cewa yayin gabatar da wannan bincike, waqoqin da Makaxa Maidaji ya rera waxanda jigonsu kacokan na siyasa ne guda biyu ne suka shigo hannu. Su ne kuma waxanda aka yi misali da su.

3.5 Tubalan Ginin Jigo a Waqoqin Maidaji

Tubalan ginin jigo sun qunshi qananan saqonni da akan samu a cikin waqa waxanda makaxa kan jejjefa su a wurare daban-daban. "Tubalan ginin jigo, qananan saqonni ne waxanda ake sassarqawa don a qara qulla zaren tunani na babban jigo a cikin waqa" (Gusau, 2002[a]: 28 da Xangambo, 2007:14). Ashe ke nan, tubalan ginin jigo sukan taka rawa ne ta xan taqaitaccen lokaci.

Tubalan ginin jigo suna qara qaimi wajen tsara xiyan waqa, za a iya samun waqa xaya ta qunshi tubalai da dama gwargwadon yadda makaxi ya tsara da kuma yadda yake tunanin zurfafa saqonsa.

Makaxa Maidaji yana daga cikin makaxa waxanda suke gina waqoqinsu ta amfani da tubalai. Mafi akasari, Makaxa Maidaji yana gina tunaninsa tare da qulla saqonni waxanda yake amfani da su wajen gina waqoqinsa. Kamar yadda wannan bincike ya gano, idan waqarsa jigonta na yabo ne da wahala a cikinta a rasa samu tubalai waxanda sukan danganci nasaba ko addini ko ta'aziyya ko

makamancin haka cikinta ba. Wasu daga cikin tubalan ginin jigo waxanda aka samu a cikin waqoqin Makaxa Maidaji sun haxa da:

3.5.1 Nasaba

Makaxa Maidaji ya rera waqoqi da dama waxanda ya ambaci nasabar sarakunan da ya rera wa waqoqi. Yana daga xabi'ar mawaqan baka na fada inda "sukan danganta basarake da asalinsa ta nuna masa fa cewa ya gaji gidansu" (Abba & Zulyadaini, 2000:47). Misali, a waqar Sarkin Zazzau, Alhaji Shehu Idris (1975-), Makaxa Maidaji ya kawo gidan sarautar Zazzau kamar haka:

Jagora : Aminu ya yi riqo jihag ga,
'Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqon su,
: Ya riqe al'amarin jiharsu.

Jagora : Muhammadu ya yi riqo jihag ga,
'Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqon su,
: Ya riqe al'amarin jiharsu.

Jagora : Yamusa ya yi riqo jihag ga,
'Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqon su,
: Ya riqe al'amarin jiharsu.

Jagora : Kuma Kabiru ya yi riqo jihag ga,
'Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqon su,
: Ya riqe al'amarin jiharsu.

Jagora : Yamusa ya yi riqo jihag ga,
'Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqon su,
: Ya riqe al'amarin jiharsu.

Jagora : Xahiru ya yi riqo jihag ga,

‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqon su,
: Ya riqe al’amarin jiharsu.
Jagora : Muhammadu ya yi riqo jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqon su,
: Ya riqe al’amarin jiharsu.

Jagora : Abdulkarimu ya yi riqo jihag ga,
‘Y/Amshi : To, yanzu Mani ke riqon su,
: Ya riqe al’amarin jiharsu,
: Uban Na-Allah uban Madauci,
: Shehu sannu da yau da gobe.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$)

Sannan a waqar da Makaxa Maidaji ya rera wa Sarkin Gobir Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003) ya kawo tarihin iyayen Sarki waxanda suka mulki qasar Gobir tun daga Alqalawa, zuwa garin Kadaye wato bayan rushewar Alqalawa, da komawar Gobirawa zuwa garin Gazau da kuma garin Tcibiri har zuwa mazaunin Sabon Birni (Augi, 1984:637-645). Ga dai abin da Makaxa Maidaji ya ce:

Jagora : Kai aj Jari da Shawai,
'Y/Amshi : Alhaji kai a Ibrahima,
: Kai ne mainasarar mashi,
: Ina wanda ka tambaba.

Jagora : Gohe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Duk mun ji su ga tarihi.

Jagora : Tambai ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.

Jagora : Balarabe ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.

Jagora : Ibrahim ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.

Jagora : Yakubu ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.

Jagora : Jadi ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.

Jagora : Shawai ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.

Jagora : Jari Kada ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.

Jagora : Salihu ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.

Jagora : Ummaru ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.

Jagora : Ibrahim ya buga tamburra,
'Y/Amshi : Dum mun ji su ga tarihi.

Jagora : 'Yan Gatawa da Yakubawa,
'Y/Amshi : Kowane an sa shi ga tarihi,
: Haba sarki riqe tarihin ga,
: Da kowa ka bixa jiddun.
Jagora : Gamkawa da Bacirawa,
'Y/Amshi : Kowane an sa shi ga tarihi,
: Haba Sarki riqe tarihin ga,
: Da kowa ka bixa jiddun,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{7}$)

A waxannan xiya da suka gabata Makaxa Maidaji ya faxi sarakunan da suka yi mulki a masarautar Gobir. Sunayen da aka ja wa layi su ne na kakannin sarki Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003). Sannan daga bisani, Makaxa Maidaji ya hori sarki da ya riqi tarihin nan na iyaye da kakanni domin shi ne ya san komi.

Waqoqin Makaxa Maidaji cike suke ire-iren tarihin sarakunan masarautun da ya yi wa waqa. Idan aka qara kallon wata waqa wadda ya rera wa Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003) ta *'Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo'* inda yake bayyana salsalar srautar Gobir kamar haka:

Jagora : Dagga Jari Kada tat taho ga sarki Shawai,
: Dag garai Salihu xan Durumbu yaz zama sarki,
: Dag garai Ummaru xan sarauniya yai sarki,
'Y/Amshi : Dag garai Ibrahim na Bawa yaz zama sarki,
: Mu leqa hwadar Inna Bawa shi ma ya kai.

Jagora : Gobirawa ku yi hankali ku bag ganganci,
'Y/Amshi : Inda nis saba ya hi inda nis sha daxi,
: Don wuyata ni ban kula da daxin wani ba.

Jagora : Shirya zamanka tun da ka zama sarki,
'Y/Amshi : Tun da kai sarki yau ba ka da haushin kowa,
: Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{144}$ $^{1}/_{4}$)

Makaxa Maidaji kan nuna godiyarsa ta amfani da nasaba domin yaba kyauta ko taimakon da ake yi masa. Yakan yi amfani da nasaba ta kusa da ta nesa, sannan da ta jini ko kuma ta alaqa. Misali a waqar *'Gagari gaba na Salihu'* ta Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Umaru Na-Allah (1957-1966) ya zayyano waxansu mutane da suke da nasaba da masarautar Gobir ta Sabon Birni kamar haka:

Jagora : Galadima ya yi taimako,
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo.
Jagora : A gai da Giye ya yi taimako,
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo.
Jagora : Sarkin Noma ya yi taimako,
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo.
Jagora : Sani Nalabo ya yi taimako,
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo.
Jagora : Magajin Tsamaye ya yi taimako,
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo.
Jagora : Durumbu da ya ba da taimako,
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo.
Jagora : Sarkin Rahi ya yi taimako,
'Y/Amshi : Saboda qanin Sahi xan Kilo,
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{143}$ $^{1}/_{4}$)

Tubalan nasaba suna da yawa a waqoqin Makaxa Maidaji, makaxi ne mai tunani mai hangen nesa kuma yana tsara zalaqar tunaninsa a lokacin da yake aiwatar da waqoqinsa.

3.5.2 Addini

Addinin Musulunci, addini ne da ke jagorancin kyautatuwar rayuwar xan'adam baki xaya. Yana qunshe da sharuxxa da hukunce-hukunce da ake buqatar kowa ya rarrabe su. "Wannan dama ce waqoqin baka suka samu, suke amfani da ita wajen ambaton ayyukan ibada don qaruwar jama'a" (Gambo, 1990: 71).

Kasancewar Bahaushe ba shi da wani addini da ya fi tinqaho da shi sama da Musulunci. Wannan ya sa mawaqan baka "sukan danganta basaraken da suke yi wa waqa da koyi da addini tare da dokokinsa domin aikinsa ya kyautata" (Abba & Zulyadaini, 2000: 46).

Makaxa Maidaji makaxi ne mai koyi da wannan batu, misali a waqar Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Umaru Na-Allah xan Shawai (1957-1966) yana cewa:

Jagora : Allahu duniya mui ta abin da za mu yi,
'Y/Amshi : Don ba nan za mu tabbata ba.

Jagora : Allah xai ka qin mutum ya ji zahi,
'Y/Amshi : Don mutum ya ce ba ya son ka me yake ma.

Jagora : Ni ba abin da yay yi min zahi da duniya,
'Y/Amshi : Sai Allah da yas shira mutuwa yag gama da shexa.

Jagora : In hairan kake,
'Y/Amshi : Ka iske hairan yana jiranka.
Jagora : In sheri kake,
'Y/Amshi : Ka iske sheri na jiranka.

Jagora : Lalle abin da ka haihwa,

'Y/Amshi : Du kana ishewa.

Jagora : In kai ta shawaran sheri,
'Y/Amshi : Su da xa uwayensu sun ji dai kumya,
: Tun da sun qi yarda,
: Uban Jekadiya,
: Sanda ubangijin Makama,
: Bajimin magatakarda.
(Maidaji : Gambo, 1990: 103-105)

Haka zalika, a waqar Sarkin Gobir na Sabon Birni Alhaji Umar Na-Allah, Makaxa Maidaji ya qara nuna tasirin addini a cikin waqar inda ya nusar da al'umma a kan muhimmanci aure da kuma sadar da zumunta. Makaxa Maidaji yana kwaxaitar da al'umma ga tsayawa haiqan ga aikata ayyuka kyawawa kamar zumunta da yawaita aure waxanda abubuwa ne guda biyu da ke xaukaka kowace irin al'umma. Tsayuwa ga aure tare da sada zumunta kan kare kowace irin al'umma daga tsananin musibar talauci. Sannan sukan tsabtace al'umma ga samun zuri'a tagari tsaftatacciya kuma sahihiya. Yana faxakarwar tare da jaddada cewa waxannan abubuwa da Allah, mai girma da xaukaka ke umartar bayi da su aikata kuma yana qaunar hakan. Ga dai abin da ya faxa kamar haka:

Jagora : Sarkin Makka ya aiko wasiqa,
'Y/Amshi : Ya aiko ma jikan ta Barga.
Jagora : Kuma Sardauna ya aiko wasiqa,
'Y/Amshi : Ya aiko ma jikan ta Barga,
Jagora : Sun ce galibin duniyag ga,

: A yi kono da salla da zakka,
'Y/Amshi : Ai ta abin da Allah ka qamna.

Jagora : A yi amre a zam son zumunta,
'Y/Amshi : A zam son zumunta,
: Ai ta abin da Allah ka qamna,
: Baban Yari baban Makama,
: Baba uban Lihidda na Sardauna.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{147}$ $^{1}/_{8}$)

Har wa yau, Makaxa Maidaji a matsayinsa na mai koyi da addinin Musulunci yakan yi addu'o'i ya faxakar da al'umma a cikin waqoqinsa da musulmai su yi koyi. Misali, a waqar *'Qi garaje uban Meli bai xauki wargi ba'* ta Malam Hassan Xansanda Makaxa Maidaji ya fito da tasirin mutuwa da kowane rai sai ya xanxana. Yana cikin faxar addini da an so mumini a ko da yaushe ya wayi gari ya tuna da ranar da zai koma wajen Ubangiji. Sannan yana faxakar da al'umma su sani waxanda suka tafi ba sun yi sauri ba ne, sannan wanda yake raye ba jinkiri ya yi ba shi ma lokaci ne. Ga dai abin da Makaxa Maidaji yake cewa cikin wannan waqa:

Jagora : Ka gani ba kukan uba nai ma Allah ba,
'Y/ Amshi : Ni ba kukan uwa nai ma Allah ba.
Jagora : Don mutuwa ba ni tsoran ta sha raina,
: Kwancin qabari shi xai ka ban tsoro,
: Kana kwance cikin duhu ba ka motsawa,
: In ka yi gabas bango ya tarbe ka,

: In ka yi yamma bango ya tarbe ka,
: Ba ka tashi tsaye sai itace su kwabre ka,
: Kuma kana so ka ga naka ba a ba ka hanya ba,
‘Y/ Amshi : Allah ka yo mana halin zuwa mui zaman kewa.

Jagora : Marafa na gane duniya zamanin yanzu,
: In zama yai daxi mutane ka vata shi,
: Tun da ban cuci mutun ba ko kay ya cuta min,
‘Y/ Amshi : In mutum ya cuce ni Allah shi saka min,
: Tun da na tsare Allah yana yo min komi,
: Qi garaje uban Meli bai xauki wargi ba,
: Dole in yaba Malam Hassan mai halin girma.
(Maidaji : Fasahar Baka, 2004)

Waqoqin Makaxa Maidaji suna xauke ne da koyarwa ta fifita Allah, yana tunatar da masu sauraronsa da su sani komi suka gani Allah ne ya shirya faruwar hakan. A cikin waxannan xiya yana cewa:

Jagora : Ashe Allah shi ka bajini,
'Y/Amshi : Kuma Allah shi ka xaukaka,
: To, Allah shi ka yin mazakkari,
: Ya shirya mai abubuwa.

Jagora : To Allah shi ad da duniya,
'Y/Amshi : Kuma Allah shi ad da lahira,
: Allah yay yo shirye-shiryen,
: Da za a shirawa na duniya.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{143}$ $^{1}/_{4}$)

Sannan kuma, waqoqin Makaxa Maidaji suna koyar da masu sauraron waqoqin tausayi da tauhidi da haquri da juriya da tawakkali ga Allah. Yana cikin koyarwa addinin Musulunci dogaro da Allah, da amincewa da qaddara. Makaxa Maidaji Sabon Birni ya daxa fito da

irin wannan batu a cikin waqar *'Ka buwayi maza'* ta Garkuwan Dutsi inda yake cewa:

Jagora : Don Allah Gobirawa,
'Y/Amshi : Sai ku yi niya,
: Ku zan ka yin wada sarki yac ce.
Jagora : Ashe wanda am musulmi,
'Y/Amshi : In abu ya samu ba ya savo,
: Amma na so a zan ajewa wajjen Allah,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$)

3.5.3 Ta'aziyya

Waqar ta'aziyya tana nufin nuna juyayi ko alhini game da rasuwar wani, sannan da tuna wasu abubuwan alheri da ya yi a lokacin da yake raye, daga nan kuma sai a yi kukan rashinsa. Ta'aziyya takan qunshi yi wa mutanen mamacin gaisuwa da taya su juyayi da ba su haquri, sannan da roqar wa mamacin gafara da sauransu (Abba da Zulyadaini 2000:35).

A waqar tsohon Gwamnan Jihar Sakkwato, Makaxa Maidaji ya yi ta'aziyyar Shehu Kangiwa kamar haka:

Jagora : Kullum hwata nikai,
'Y/Amshi : Allah ya ji qan Shehu Kangiwa.
Jagora : Allah yai addu'a,
'Y/Amshi : Allah ya ji qan Shehu Kangiwa.
Jagora : Annabi yai addu'a,
'Y/Amshi : Allah ya ji qan Shehu Kangiwa.

Jagora : Sarkin Musulmi yai addu'a,
'Y/Amshi : Allah ya ji qan Shehu Kangiwa.
Jagora : Waziri yai addu'a,
'Y/Amshi : Allah ya ji qan Shehu Kangiwa.
Jagora : Kuma Nana da tai addu'a,
'Y/Amshi : Allah ya jiqan Shehu Kangiwa.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{52}$ $^{1}/_{6}$)

Haka zalika a cikin waqar nan ta *'Jikan Jari ginshiqi'* Makaxa Maidaji ya isar da ta'aziyyarsa ta rasuwar ubangidansa Alhaji Umar Na-Allah xan Shawai (1966-1975) inda yake cewa:

Jagora : Ai kusu da yay yi sheka,
: 'Ya'yansa yay yi ma,
: Bilbili da yai gida,
: Don 'ya'yansa yay yi,
: Ummaru bai kau ba,
: Sai da yak kai ga halin na Innuwa.

Jagora : Ummaru Allah ji qan ka,
'Y/Amshi : Allah ya kam mai da gahwara,
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$)

3.5.4 Koxa Kai ko Wasa Kai

Koxa kai ko wasa kai shi ne "faxar kalmomin alfahari tare da nufin nuna shahara ko bunqasa ko qwarewa bisa wani abu da mutum yake yi" (Gambo, 1990:53). Makaxa na amfani da "koxa kai saboda su daxa kwarjininsu a wurin sarkin da suke yi wa waqa". "Akwai koxa kai na cika baki da na alfahari" (Abba & Zulyadaini, 2000: 61).

Wasu wuraren da Makaxa Maidaji ya yi amfani da sigar koxa kai akwai waqar *'Uban makama uban gardaye'* ta Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Muhammad Bawa (1975-2003) inda yake cewa:

Jagora : Taron Isa da anka yi niz zo,
'Y/Amshi : Ba da kamar makaxa niz zo ba.
Jagora : 'Yan yara sun ga shiga ta Isa,
'Y/Amshi : Has sun ce wani xan sarki na.

Jagora : Don sun gane ni,
'Y/Amshi : Da 'yan gangumma,
: Da sun ce wani ma sarki na.
Jagora : Wasu sun ce, ba dai sarki ne ba,
'Y/Amshi : Yalla dai makaxin sarki na.

Jagora : Bambanta ni uban Gardaye,
'Y/Amshi : Ya sake mana sabbin kaya,
: Saura yai mana sabon doki,
: In sake masa sabon launi,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{144}$ $^{1}/_{1}$ - AL $^{1}/_{144}$ $^{1}/_{2}$)

Sannan can cikin waqar *'Namijin daga uban gardaye'* ta Sarkin Gwaranyo Makaxa Maidaji yana cewa:

Jagora : Sauran kaya ina son ku riqe ni,
'Y/Amshi : Ina son ku riqe,
: Ku rungume ni,
: Ku riqe ni qwarai,
: Kamar nama ya kama kalwa.
Jagora : In nama yak kama kalwa,
'Y/Amshi : Mata ba sai kun hwaxa ba,
: Ku ruhe shi,
: Ku tsabtace shi,
: Hah hancin kowa ya kai mai,
: Namijin daga uban Gardaye,

: Sarkin Gwaranyo.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{375}$ $^{1}/_{12}$)

Haka zalika, a cikin waqar Alhaji Isa Baraz Zaki ta *'Yai halin mazan jiya Isa maqi garaje'* Makaxa Maidaji yana cewa:

Jagora : Ni dai ina biyax xan sarki,
'Y/Amshi : Shi ko yana gudu na
: Ku ce ya bar gudu,
: Ba hakan niy yi xammara ba.
Jagora : Matatai tana hwaxi,
'Y/Amshi : Wataqil wane mai kixin ga,
: Xanai shi na hwaxin,
: Baba shige cikin itace.
Jagora : Haba wane don gani na,
'Y/Amshi : Bari bar shiga itace,
: Akwai kububuwa,
: Mai zane tana kashe ka,
: Yai halin mazan jiya Isa maqi garaje,
: Tun da yai kira Alhaji bai kahwat tsayawa.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{378}$ $^{1}/_{9}$)

3.5.5 Habaici

Habaici wani nau'i ne na zancen hikima da ake amfani da shi a fakaice wato cikin voyayyiyar manufa don vata wa wani mutum rai ko ya sa masa qaimi da kuzari ko a yi masa faxakarwa. Habaici "jirwaye ne mai kamar wanka, Hausawa na cewa kowa ya yi zagi a kasuwa ya san da wanda yake" (Gusau, 1986:1 da Tanko, 1994:2).

Wannan ya nuna habaici "magana ce mai xaci da Bahaushe ke faxa a sakaye domin ya sanya xabi'ar gyara kayanka wanda ba ya zama sauke mu raba" (Garba, 1998:18).

Ke nan, habaici “wani nau’i ne na zancen hikima da ake amfani da shi a yi da mutum a fakaice” (Umar, 1983:23).

Yawanci habaici kan qunshi kwatanta wasu abubuwa ne da nufin nuna gazawa ko raini ko mayar da martani ga wanda aka yi wa. An fi yin habaici ga waxanda suka yi ruwa suka yi tsaki na kawo cikas ga wasu abubuwan rayuwa da ake nema ga waxanda suka qi ba da kai bori ya hau bayan an ci an suxe.

Saboda haka, habaici wata hanya ce da mawaqa suke amfani da ita domin su qasqantar da wani mutum ko kuma su muzanta shi su zage shi ko a caka masa magana a fakaice, sukan ci karensu ba babbaka’. Makaxa Maidaji ya yi amfani da sigar habaici a cikin waqoqinsa. Misali, a waqar Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Umaru Na-Allah (1957-1966) Maidaji cewa ya yi:

Jagora : Haba Gobirawa kun yi sake,
'Y/Amshi : Kun bar zakara ya shige akurki.
Jagora : Har ya cera ya hid da toro,
'Y/Amshi : To ku yi anniya tun da tsawa ta yi tsawo.

Jagora : Ku bar mishi akurki,
'Y/Amshi : Shure mutum ya kai,
: Tun da gawa ta yi tsawo.

Jagora : Haba Gobirawa ga tsarinku ya zama kada,
'Y/Amshi : Har ya aza qanquna sun miqe.
: Niqatau na Jekada bajimin magajin gari,
: Ummaru gam da ram bulgu wayayyen sarki.

(Maidaji : Xahiru, G. 1990: 105-107)

Haka kuma a waqar da Makaxa Maidaji ya rera wa Sarkin Gobir na Sabon Birni Alhaji Muhammadu ya qara fito da wani xa cikin tsarin habaici. A cikin xan waqar yana magana ne bisa qaulin cewa Sarki Muhammadu ya gade mulkin da kakanninsa da iyayensa suka yi, saboda haka Gobirawa ‘yan sarauta su yi hankali su bar yin wauta da gaugawa, su yi mubaya’a ga sarki tun da shi Allah ya zava. Ga dai abin da yake cewa:

Jagora : Gobirawa ku yi hankali ku bag ganganci,
‘Y/Amshi : Inda nis saba ya hi inda nis sha daxi,
: Don wuyata ni ban kula da daxin wani ba.

Jagora : Shirya zamanka tun da ka zama sarki,
‘Y/Amshi : Tun da kai sarki yau ba ka da haushin kowa.

Jagora : In kwana bai qare ba ba a saurin kuka,
‘Y/Amshi : Bawa ka san Allah ka gyara kayan kowa,
: Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{144}$ $^{1}/_{4}$)

Har wa yau dai a wata waqa da ya rera wa Sarkin Gobir na Sabon Birni Alhaji Umaru (1966-1975) Makaxa Maidaji yana cewa:

Jagora : Xan Inna xan sarauniya xan mai Runji,
‘Y/Amshi : Umaru xan Bawa ba a kai ma ‘yan kamanci.

Jagora : Alhaji ka rabu da dibin maza sunai ma bakanta,
‘Y/Amshi : Umaru ka san abin da Shawai yas shirya.

Jagora : In don xan hakimin ga mai mugun hali,
'Y/Amshi : Umaru na so a warware mai hakimci,
: Ashe kokuwar kare da kura ta qare,
: Gagara gasa na Alhaji Gardaye,
: Umaru gagon Bala uban Sarkin fada.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{4}$)

Har yanzu, a cikin waqar nan ta *'Gagari gaba na Salihu'* wadda Makaxa Maidaji ya rera wa Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Umaru Na-Allah (1957-1966) ya qara fito mana da misalin habaici a cikin wannan waqa inda yake cewa:

Jagora : Ga ni ina son vacin tcibilbila,
'Y/Amshi : Zaman zauri xai nika gudu,
: In zauri ya buwaya yanzu,
: Ko ga itace zama ta kai.

Jagora : To, na so in vaci hakimin sarki,
'Y/Amshi : Rowan nan da yat tcira,
: Baqar rowan nan da yat tcira,
: Da hwari shi ka sa mu tcira xumumuwa.

Jagora : Maza ku yi wasa da dariya,
'Y/Amshi : Ku zan ki gamawa da hwara'a,
: Mai rowa ko da yaushe,
: Kag gane shi da lauje cikin naxi.
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{143}$ $^{1}/_{4}$)

Kuma a cikin wata waqa Makaxa Maidaji yana cewa:

Jagora : Don Allah Gobirawa,
'Y/Amshi : Kowa ya kintsa kainai,
: Don ku sani,
: Akwai wani zarto yana tahowa.

Jagora : In don mutum yana iko,
‘Y/Amshi : Ba ya ba mu kyauta,
: Ka kama shawara,
: Gwara mu kwan gidan mutane.
Jagora : Alhaji don ganin gero,
‘Y/Amshi : Ba ni tsinka tambo,
: In don batun hwaxa,
: Ban ga batun ture-turenga,
: Yai halin mazan jiya Isa maqi garaje,
: Tun da yai kira Alhaji bai kahwat tsayawa.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{378}$ $^{1}/_{9}$)

A waqar Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Muhamadu Bawa (1975-2003) Makaxa Maidaji ya cashe wa waxansu mutane da suka tava masa ubangida inda ya mayar da raddi ga waxannan cikin harshe mai nauyi kamar haka:

Jagora : An ce wane shina hauka,
‘Y/Amshi : Ni ban san shi da hauka ba,
: Kuma ban san shi da hauka ba,
: Sai ya katse abin xarmi.

Jagora : Jiya can nij ji mutane na cewa wane hawa’i ne,
‘Y/Amshi : Ko mu mun ji mutane na cewa wane tavavve na.

Jagora : Shi wargi da hawa’i,
‘Y/Amshi : Ya xara wargi da bugun buta,
: In sun tashi rashin kunyan nan,
: In sun gamu dux xai na.

Jagora : Hawa’i da bugun buda,
: Ai na ce muku dux xai na,
‘Y/Amshi : Ai had da mashayin kamsul,
: Shi ma la’ananne na,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,

: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{7}$)

A waqar Alhaji Muhammad Xankaltu nan ma Makaxa Maidaji ya qara zancen habaici a cikin wannan waqa inda ya ce:

Jagora : Ban ja mutum ba ya bar ja na,
: Rabi da jefa min galma.
Jagora : Lalle su wane ai shagguna ku,
: Ka san uban shaggun nan,
: Ni uban mutum nika vacewa,
: Ba ya da halin ramawa,
'Y/ Amshi : Wuce maza xan kurma,
: A gai da Mamman xan Kaltu.
(Maidaji : Gusau, S. M. 1983: 476-478)

3.5.6 Kyauta da Karimci

Makaxan fada sukan nuna irin kyautar da sarki yake yi musu a cikin waqoqinsu. Makaxan sukan yi hakan ne, "don nuna wa jama'a kirkin da sarkinsu yake da shi" (Abba & Zulyadaini, 2000:51).'Yaba kyauta tukuici', Makaxa Maidaji makaxi ne mai son yaba kyauta. Yakan tsaya haiqan wajen tanada alakoro cikin karimci da jan rai ga wanda ya yi masa kyauta. A waqar da ya rera wa Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003) cewa ya yi:

Jagora : Ya ban buhuhuwa a yi man tuwo,
'Y/Amshi : Ya ban kuxi in sai miya,

: Amma kayan in mun canye su,
: Xan Inna dawowa mukai.

Jagora : Fam goma sha biyar Sarki yab bai,
'Y/Amshi : Yac ce mu sai kajin miya,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{374}$ $^{1}/_{7}$)

Har wa yau, a cikin waqa ta Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003) ya qara jaddada cewa:

Jagora : Zamanin Muhammadu xan Kilo,
'Y/Amshi : An ba mu naira zay yawa,
: An ba mu manyan riguna.

Jagora : In ka ganan da shadda tsanwa shar,
'Y/Amshi : Garko ka shirya man ita,
: In ka ganan da kwakwata,
: Magajin gari ka yi min ita,
: In ka gane ni da jikkak Kano,
: To, wadda Inna tay yi na.
Jagora : To, kuma in ka ganan da wandon Kano,
'Y/Amshi : To, wanda Inna tay yi na.
Jagora : A gaishe ki Inna,
'Y/Amshi : 'Yar Kilo xiyag Garba manyan duniya,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{374}$ $^{1}/_{7}$)

Sannan a Waqar da ya rera wa Innar Gobir ga abin da yake faxa game da Innar Gobir ta Sabon Birni:

Jagora : Inna hwarar uwa ta Dango ta gode Allah,
'Y/Amshi : Jikanyar Balarabe ta san ya kamata.
Jagora : Darzaza ta Bawa ko ba wuri ki hurce,
'Y/Amshi : Duk inda kib biya sai kowa ya wadata.

Jagora : To, na zaka in yi godiyar riga inda Inna,
'Y/Amshi : To, in za ki ba ni wata amma kak ki hwasa,
: Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{375}$ $^{1}/_{3}$)

Dubi abin da ya ce a wannan waqar da ya rera wa Sarkin Zazzau:

Jagora : Na gode maka Sarkin Gobir,
'Y/Amshi : Alhaji Makaxa ya gode,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.

Jagora : Ya gama mu da kaya,
'Y/Amshi : Kaya, ko yanzu ya gama mu da kayan iko,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.
Jagora : Ga wata riga Sarki yab ba ni,
'Y/Amshi : Ta zube qasa hat tai oba,
: Alhaji har bisaki ya share
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.
Jagora : Ga xan tasala da Sarki yab ba ni,
'Y/Amshi : Da ka naxa shi kamar xan xaki,
: Hay ya sa mani doron cilas,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.
Jagora : To, alkyabbag ga da Sarki yab ba ni,
'Y/Amshi : Ya qara mana hasken hwada,
Jagora : Ga hwan talatin Sarki yab ba ni,
'Y/Amshi : In yi jajibirin ras salla.
Jagora : Ai kuxin sun wuce kwasar nama,
'Y/Amshi : Rago za mu saye ko xan sa,
: Uban Makama uban Gardaye,
: Bawa sannu da kwanan yaqi.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{144}$ $^{1}/_{1}$ - AL $^{1}/_{144}$ $^{1}/_{2}$)

Wannan bincike ya tabbatar da Makaxa Maidaji bai yawaita zambo a cikin waqoqinsa ba. Domin, yana gina waqoqinsa ne a kan yabo ne da zuga da faxakarwa ko ilmantarwa da dai sauransu.

Shi kuwa zambo masana da manazarta suna kallonsa a matsayin:

> Hurumin da mawaqa ke amfani da shi yayin siffanta mutum da wasu siffofi munana waxanda za su wulaqanta shi ko su jawo masa rashin martaba a idon mutane, tare da kau da kai cewa wannan mutum yana da waxannan siffofi ko ba shi da su. Ta hanyar qarin gishiri don a daxa lalata hali ko xabi'ar wanda ake yi wa zambo (Wushishi, 1998: 113 da Gusau, 2008:380 da Bunza, 2009: 132).

Zambo "zagi ne na kai tsaye ta amfani da kalmomi hikima da ke bayyana a cikin waqa" (Garba, 1998:37 da Satatima, 1999:20). A wajen gina waqoqin zambo akan yi qoqari a dubi halayen mutum da siffofinsa, wato na gaskiya ko a qaga masa na qarya, a daxa vata shi ta ambata masa munanan kalmomi. Bunza (2009) yana ganin "idan sarauta ta faxi aka yi nema, aka bayar, aka sa ranar aski da naxi da abokan kokuwa da mutanen fada da 'ya'yan sarki sai dai su rufe kunnuwansu, ga sauraron zambo" (Bunza, 2009:132).

A hirar da Makaxa Maidaji suka yi da Malam B.S.Y. Alhassan tare da Malam A. V. King a shekarar 1982 a gidansa da ke garin

Rambaxawa ya habarta cewa bai cika yin zambo a waqoqi ba saboda abu ne da ya tabbatar ya sava qa'ida ta addini.

Amma, ya yi zambo na mayar da martani ga wasu waxanda suka addabi ubangidansa na wannan lokaci. Ga dai abin da ya ce a wannan hira:

B. S. Y. Alhassan: To, kamar xazu mun tavo maganar da kay yi cewa ga dalilan da ke sa a yi wa mutum zambo. Ko akwai waqarka wadda kay yi zambo daga hwarko har qarshe zambo na zalla kay yi?

Makaxa Maidaji: Ai babu.

B. S. Y. Alhassan: Ni ban ga kana son yi ma mutane zambo da yawa ba. Kuma na ga mutane suna sha'awar zambo ga waqa. Sai dai, in kay yanka kuma vatacce kake yi?

Makaxa Maidaji: Eh! Muna ji suna ta yi.

B. S. Y. Alhassan: Kuma na ga ko da maganar mawaqa za ka yi sai dai ka yi maganar alheri. Wato, kai ba ka yin zambo sai ta kama dole ke nan?

Makaxa Maidaji: Eh! To, sai bana mun ka xan yi wani xan kaxan. Saboda wani na yake wa sarki shegantaka.

A wannan waqa ta Sarkin Zazzau, Alhaji Shehu Idris (1975-) Makaxa Maidaji ya qara jaddada batunsa na bai cika son saka zambo a cikin waqoqinsa ba. Ga dai abin da yake cewa:

Jagora : Alhaji Shata ya hwaxa man,
'Y/Amshi : Ya ce Zariya ba a zambo,
: In makixi yas shirya zambo,
: Alhaji wawa na buge shi da gora,
: Yanzu ta hau wuyanai,
: Uban Na Allah uban Madauci,
: Shehu sannu da yau da gobe.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$)

3.7 Naxewa

Wannan babi, kamar yadda ya gabata, ya yi magana ne a kan saqonnin da waqoqin baka na Hausa suke qunsa.

A babin an kawo ma'anar kalmar jigo da yadda makaxi yake saqa tunaninsa a waqa ya fitar da jigo da nau'o'in jigon da ake samu a waqoqin baka na Hausa.

An yi bayani a kan jigon yabo da jigon zuga da jigon faxakarwa da jigon siyasa. Daga nan kuma aka yi nazari game da tubalai waxanda Makaxa Maidaji yake amfani wajen ginawa da tayar da jigogin waqoqinsa.

Har wa yau, wannan babi ya kawo nau'in waqoqin Makaxa Maidaji Sabon Birni da suka haxa da waqoqin noma da na fada da na siyasa da kuma na sauran jama'a masu riqe da muqaman sarauta.

BABI NA HUXU
TSARI DA SALO A WAQOQIN
MAKAXA MAIDAJI SABON BIRNI

4.0 Gabatarwa

Wannan babi zai bibiyi salo da tsari ne a waqoqin Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni domin fahimtar yadda yake jera tunaninsa. Haka kuma za a duba hanyoyin da Makaxa Maidaji Sabon Birni yake shirya waqoqinsa.

4.1 Me ake Nufi da Tsari a Waqoqin Baka?

Idan aka dubi ayyukan masana adabin baka irin su Parry (1935) da Muhammad (1978) da King (1981 & 1986) da Sadi (1989) da Yahaya (1997) da Abba & Zulyadaini (2000) da Schuh (2002) da Gusau (2002 & 2003 & 2008 & 2010) da Olatunji (2005) da Satatima (2008) da Bunza (2009) za a tarar sun nazarci hanyoyin tsari da ma'auni a waqoqin baka ta mabambantan fanni. Wasu daga manazarta sun bayyana tsari a waqar baka da cewa:

> Tsari a nazarin waqar baka shi ne fannin da ke fayyace xan waqa a matsayinsa na qunshiyar saqo ko manufa a cikin waqa da ke bayyana yadda mawaqi yake shirya tunaninsa wajen qulla kalmomi da jumloli su bayar da saqon da yake burin isarwa ga al'umma (Satatima, 2009: 127-128).

Tsari a waqar baka shi ne hanyar da mawaqi ya bi ya jera tunaninsa, tare da shirya shi domin ya isar da saqonsa ga mai sauraro. Dangane da tsari a waqar baka:

> Xiyan waqa tamkar rassa ne na itaciya wadda ake fara hawowa daga gindi kuma a sauka ta kansa. A kowane xa za a sami *hawa* da *sauka.* Ta hakan ne mai nazari zai kula da yadda makaxi yake qulla carbin tunaninsa da yadda yake saqa kalmomi da saqonni cikin jimloli na xiya (Gusau, 2003: 33-34).

Ke nan a iya cewa, tsari a waqar baka na bayyana fasalin da makaxa ke amfani da shi wajen bayyana dangantakar da ke tsakanin xa da manufa wajen isar da saqo ta amfani da salo mai gamsarwa wajen rera waqoqin.

4.2 Me da me Tsari ya Qunsa a Waqar Baka

Wasu daga cikin manazarta waqoqin baka na Hausa suna a kan ra'ayin an fara gabatar da wasu hanyoyi na nazarin adabin baka tun a wajejen 1935 lokacin da Milman Parry ya fito da hanya ta nazarin awon baka dangane da tsari da ma'auni a waqoqin baka.

Hanya ce wadda ta qunshi karin murya ta fuskar hawa da sauka da faxuwar murya da amsa-amon kari da tsarin layuka a xiya na waqoqin baka.

Har wa yau, Muhammad (1978: 79) ya yi magana a kan savi-zarce tare da kawo misalai daga xiyan waqoqin baka na Hausa. Muhammad (1978: 84) ya tabbatar da waqoqin baka na Hausa suna da amsa-amon kari wanda shi ne daidaituwar kari iri xaya a gavar qarshe ta layuka na xiya a waqar baka. Ke nan:

> Awon baka fage ne na nazarin waqar baka da ya shafi yadda makaxi yake shirya waqa a cikin zubin xiya da dabarun karin murya. A vangaren awon baka ne ake duba tsarin layuka da yawan xiyan waqa da tsarin rerawa da karin murya da amsa-amon kari da sauransu (Gusau, 2003:32).

Shi kuma King (1986: 1-2) ya yi qoqarin fito da hanyoyin tsarin xiya a waqoqin fada ta lura da yadda ma'ana take hawa da sauka da yadda ake yi mata takidi da saukar sauka da ajewa. King (1986: 6) ya yi nazarin tsarin rerawa ne ta fitar da tarbe da rakiya da karvevveniya da bayayyeniya a yayin rera xiya na waqoqin baka.

Ta hanyar dangantakar xiya a waqoqin baka, King (1986: 6-14) ya nuna akan gina xa a waqa ta baka bisa qaramin turke wato saqo

qarami, sannan a wajen rerawa za a iya maimaita shi sau da yawa a cikin waqa xaya. Kuma ya fitar da yadda za a fexe su ta hanya biyu wato waxanda ya kira da ma'ana (*component)* da kuma qirga (*structure)*.

Jigo (turke) ke nan yana iya zama babban saqo a waqa ko qaramin saqo a xa. Schuh (2002) ya fitar da wata hanya ta nazarin karin waqar baka ta bin tsarin 'gidan dara na kari' da kuma 'gurabun kari'. A bisa irin wannan nazari ne Schuh (2002) ya xora waqoqi uku da suka shafi aure na Dr. Adamu Xammaraya Jos ya fitar da karuruwansu. Waqoqin su ne, waqar 'Jawabin Aure' da waqar 'Auren Dole' da 'Gulma-Wuya' Schuh (2002: 154-161).

Akwai hirar da Malam A.V. King da Malam Magaji Tsho Yakawada suka yi da Makaxa Musa Xanqwairo Maradun da Abubakar Daudun Kixi (1984, AL $^{4}/_{13}$-$^{1}/_{5}$: ODU, ABUZ) da kuma hirar da aka yi da Makaxa Sa'idu Faru (1984, AL $^{4}/_{10}$- $^{4}/_{12}$: ODU, ABUZ). Sannan da hirar da Malam A. V. King da Malam B. S. Y. Alhassan suka yi da Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni, inda suka tabbatar da:

> Yawancin kalmomin fannu da ake amfani da su wajen nazarin tsarin waqar baka an samo su ne daga bakin

> makaxan kansu a muhallin da suke amfani da su wajen tsara waqoqinsu. Domin yayin rera waqoqin a tsakaninsu, sukan fito da hikimominsu ta amfani da kalmomi masu jan rai waxanda suke tamkar sara a tsakanin makaxa da mawaqan. Kalmomin fannun dai sun haxa da kalmar *turke* da *gindin waqa* da *amshi* ko *karvi* da *hauhawa* da *takidi* da sauransu (King, 1986: 6-8; Gusau, 2010: 17).

Ayyukan Gusau (1996; 2002; 2003; 2008; 2010) sun tabbatar da tafiyar aminci ne da ayyukan King (1984; 1989; 1986) wajen nazarin waqar baka ta Hausa. Misali, duk suna da ra'in xa yana iya qunsar saqo xaya ko ya qunshi saqonni biyu ko fiye da haka. Kuma Gusau (2010: 17) yana ganin ana rarrabe *xa* da *xa* a waqar baka ta maimaita rera gindin waqa (a wajen makaxi wanda = +qungiya +karvi +Layi) ko sautin kixa (a wajen makaxi wanda = –qungiya -karvi -layi).

Domin hawa da sauka suna tabbatar da saqo da makaxa sukan cusa ba kara zube yake ba. "Xiyan waqa tamkar rassa ne na itaciya wadda ake fara hawowa daga gindi kuma a sauka ta kansu" (Gusau, 2003: 34).

Daga waxannan bayanai na masana da manazarta waqoqin baka na Hausa, ke nan akwai hanyoyi guda biyu waxanda ake amfani da su wajen fitar da tsarin xa na waqar baka da suka haxa da:

4.2.1 Ma'ana

King (1986) ya ambaci ma'ana da 'component' ne. Ta hanyar fitar da ma'ana ne a xan waqa mai nazari zai fito da matakai waxanda makaxi yake bi ta kansu wajen tsara xa a waqarsa (Gusau, 2003: 33-38; 2010: 18). Waxannan matakai sun haxa da:

Hawa : Na nufin inda aka fara furta qaramin saqo (daga Jagora/ Kaxaita/ Wakili).

Hauhawa : Na nufin inda aka ci gaba da furta qaramin saqo (daga Jagora/ Kaxaita/ Wakili).

Sauka : Na nufin qarasa furta qaramin saqo da aka faro a *hawa* (daga 'Y/Amshi + layi, ko Kaxaita –Layi).

Ajewa : Wuri ne da ake numfasawa kan gavar qaramin saqo ('Yan Amshi/ Kaxaita).

Saukar Sauka : Wato kacokan wurin da aka iyar da qarasa qaramin saqo ('Yan Amshi/ Kaxaita).

4.2.2 Qirgar Ma'ana

A nan kuma King (1986) ya kira qirga da ‘Structure’ ne. A fage na qirga ana duba yawan qananan saqonni ne da aka zuba a xa, za a yi amfani da haruffan Abacada [a, b, c, d, e da sauransu] wajen qirga yawan qananan saqonni da aka zuba a xa na waqar baka. Sai kuma harafin [x] wajen nuna adadin layuka na gindin waqa (King, 1986: 8-13; Gusau, 2002: 45-47; 2003: 36-38).

4.3 Tsarin Xiya a Waqoqin Makaxa Maidaji

Tabbas ‘waiwaye adon tafiya ne’ domin idan an waiwaya an kalli sauran al’ummun duniya baki xaya, sun daxe suna tunanin yadda za su tsara hanyar nazarin adabinsu. Masana da manazarta da dama irinsu Levin (1962) da Burgess (1964) da Skinner (1970) da Finnegan (1970) da Gray (1975) da Muhammad (1978) da King (1981 & 1986) da Abba & Zulyadaini (2000) da Gusau (2002 & 2003) da sauransu sun tabbatar da hakan.

Kusan a iya cewa, kowace al’umma da lokacin da ta soma nazarin adabinta gwargwadon wayewarta da ci gabanta da saduwarta da wasu baqin al’adu.

Haqiqa, tsarin Makaxa Maidaji wajen rera waqoqi karvavve ne kuma mai armashi. Waqoqi ne da suke xauke da hanyoyi ko matakan

nazarin waqoqin baka na Hausa. Domin a waqoqinsa yakan fayyace xan waqa a matsayinsa na qunshiyar saqonsa ko manufarsa, tare da bayyana tunaninsa wajen qulla kalmomi da jumloli su bayar da saqon da yake burin isarwa ga al'umma. A xiyan waqoqinsa akwai masu sauqi da kuma masu tsauri. Wato xiya masu ma'ana xai-xaya da kuma xiya masu harshen damo wato masu ma'ana fiye da xaya a cure waje xaya.

Wannan bincike ya xora matanin waqoqin Makaxa Sa'idu Maidaji bisa mizanin manazarta adabin Hausa. Wannan bincike ya lura da tsarin xa a waqar baka ta Hausa ya ta'allaqa ne dangane da ma'ana da qirga. Sannan kuma xa a waqar baka ya kasu gida biyu. (King, 1986:1-54 da Gusau, 2002: 41-51; 2003:37; 2010:18) suna bayyana cewa:

4.3.1 Tsarin xa Mai Sauqi

Shi ne wanda zai qunshi qaramin saqo xaya. Waqoqin Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni cunkushe suke da misalai, yana gina waqoqinsa cikin tsarin rerawa mai armashi kuma karvavve. Waqoqi ne da ke tattare da zalaqar rerawa da gwanincewar harshe. Ga misalin

tsarin xa mai sauqi a waqar Arzika ta noma *'Sarki yai abin daka ya huta'* inda yake cewa:

Ma'ana	*Qirgar Ma'ana*	
Hawa	A^1	: Baba mijin Shibo mijin Maryama,
Sauka	A^2	: Giwa maganin itacen daji,
	X^1	: Sarki yai abin daka ya huta,
	X^2	: Zaki xan Abubakar xan Buda.

(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^1/_{147}$ $^1/_2$)

Har wa yau dai a waqar *'Gagari gaba na Salihu'* ta Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Ummaru xan Salihu (1957-1966), Makaxa Maidaji Sabon Birni ya qara fito da irin wannan batu:

Ma'ana	*Qirgar Ma'ana*	
Hawa	A^1	: Ga ni ina son vacin tcibilbila,
Sauka	A^2	: Zaman zauri xai nika gudu,
Ajewa	A^3	: In zauri ya buwaya yanzu,
Saukar sauka	A^4	: Ko ga itace zama takai,
	X^1	: Gagari gaba na Salihu,
	X^2	: Mai nasara xan Durumbu,
	X^3	: Xan Hayatu magajin gidan Kada.

(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^1/_{143}$ $^1/_4$)

A waqar *'Ya kwan yana aikin mota'* ta Sarkin Tashar Motar Sabon Birni, Alhaji Idi xan Argiji, Makaxa Maidaji ya bayyana cewa:

Ma'ana	*Qirgar Ma'ana*	
Hawa	A^1	: Ga ni ina shirin tahiya Zazzau,
	A^2	: Kuma ga ni ba 'yan kuxxi,
Hauhawa	A^3	: Ina nuhin tahiya Zazzau,

	A^4	: Kuma ga ni ba ‘yan kuxxi,
Sauka	A^5	: Ina dibin mota ni ko suna kallo na,
	A^6	: ‘Yan Kamishon suna dibin mota,
	A^7	: Ni ko suna kallo na,
Ajewa	A^8	: Don sun gane ni da taron,
	A^9	: Yara zay yawa bayana,
Saukar Sauka	A^{10}	: Har an yi jinga na tada,
	A^{11}	: Ba zan biyan kuxxi ba,
	X^1	: Ya kwan yana aikin mota,
	X^2	: Xan Argiji xan Shawai,
	X^3	: Sarkin tasha jikan Idi,
	X^4	: Jikan fulanin Vaure.

(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^0/_{54}$ $^1/_5$)

Ga kuma wani misalin xa mai sauqi daga waqar *‘Qi garaje uban Meli bai xauki wargi ba’* ta Malam Hassan xan Sanda inda Makaxa Maidaji Sabon Birni ya bayyana cewa:

Ma’ana	*Qirgar Ma’ana*	
Hawa	A^1	: Don mutuwa ba ni tsoron ta sha raina,
Hauhawa	A^2	: Kwancin qabari shi xai ka ban tsoro,
	A^3	: Kana kwance cikin duhu ba ka motsawa,
Sauka	A^4	: In ka yi gabas bango ya tarbe ka,
	A^5	: In ka yi yamma bango ya tarbe ka,
	A^6	: Ba ka tashi tsaye sai itace su kwabre ka,
Ajewa	A^7	: Kuma kana so ka ga naka ba a ba ka hanya ba,
Saukar Sauka	A^8	: Allah ka yo mana halin zuwa mui zaman kewa,
	X^1	: Qi garaje uban Meli bai xauki wargi ba,
	X^2	: Dole in yaba Malam Hassan mai halin girma.

(Maidaji : Gusau, S. M. Fasahar Baka, 2004.)

Sannan kuma a waqar *‘Kak ka yarda da raini uban Baraya’* ta Sarkin Zazzau, Alhaji Shehu Idris (1975-), Makaxa Maidaji Sabon Birni ya qara fito da irin wannan batu inda yake cewa:

Ma'ana	*Qirgar Ma'ana*	
Hawa	A^1	: Ai ga ni na zaka Zazzau mu gai da sarki,
Sauka	A^2	: Ban ga Habiba ba kuma ban ga Mariya ba,
Saukar Sauka	A^3	: Ai ko su Binta ba su da halin su daqile ni,
	X^1	: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
	X^2	: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.

(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{52}$ $^{1}/_{7}$)

A waqar *'Xan Sidi amshi sandar mulki qasatai'* ta Sarkin Buza, Alhaji Muhammadu, Makaxa Maidaji cewa ya yi:

Ma'ana	*Qirgar Ma'ana*	
Hawa	A^1	: Da na samu kurciya ko ko damisa ne,
	A^2	: Ko ko tattabara uwat tsuntsaye na samu,
	A^3	: Da na ba da saqo,
Hauhawa	A^4	: Saqon da ba ni ba za ta zo ta kwana ba,
Sauka	A^5	: In tac ce gari da nisa in ba da taguwa,
	A^6	: In tac ce gari da yunwa in ba da gari,
	A^7	: In tac ce gari da qishirwa in ba da salka,
	A^8	: In tac ce gari da xari in ba da bargo,
Ajewa	A^9	: In taz zo tac ce matan Falgore qasatai,
Saukar Sauka	A^{10}	: Ga darnin da yab bari ya koma katanga,
	X^1	: Xan Sidi amshi sandar mulki qasa tai,
	X^2	: Mai Buza xan Hassan mai taro hannu.
	(Maidaji : Hira da Rima Rediyo, Sakkwato)	

Ga kuma wani misalin xa mai sauqi daga waqar *'Ya wuce tantama'* ta Alhaji Shu'aibu inda Makaxa Maidaji ya bayyana cewa:

Ma'ana	*Qirgar Ma'ana*	
Hawa	A^1	: Ni da dai nas sauka Sabon Birni,
	A^2	: To na sauka ko han na kwan,
	A^3	: Na ishe yara na wata waqa,
Hauhawa	A^4	: To ko yara kau ko 'yan mata,
Sauka	A^5	: Sun ce wanda yas sai nama,
	A^6	: Ya xara wanda yas sai kihi,

	A^7	: To, wanda yas sai anta,
	A^8	: Ya xara wanda yas sai hanji,
	A^9	: To, kuma wanda yas sai doya,
	A^{10}	: Ya xara wanda yas sai gwaza,
Ajewa	A^{11}	: To, kuma wanda yas sai doki,
Saukar Sauka	A^{12}	: Ya xara wanda yas sai jakki,
	X^1	: Ya wuce tantama,
	X^2	: Shi Alhaji Shu'aibu zamani nai ya kai.

(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^1/_{143}$ $^1/_2$)

A waqar Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Ummaru xan Salihu (1957-1966), ta *'Na Malam gwani daga'* Maidaji ya bayyana:

Ma'ana	*Qirgar Ma'ana*	
Hawa	A^1	: Dur ran da na Yakuba yai sarki,
Sauka	A^2	: Da mu za a shan kalwa birni,
Ajewa	A^3	: Da mu za a shan kalwa,
Saukar Sauka	A^4	: Rannan da mu za a tarboso birni,
	X^1	: Na Malam gwani daga,
	X^2	: Na Allah jikan Hillani xan Musa na Malam.

(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^1/_{147}$ $^1/_6$)

4.3.2 Tsarin xa Mai Tsauri

Shi ne xa mai harshen damo wanda zai qunshi qananan saqonni biyu ko fiye da haka. Shaharar Makaxa Maidaji Sabon Birni a waqar baka ta Hausa da gwanincewarsa wajen saqa tunani don isar da saqo cikin rauji mai karsashi ya ba shi damar watayawa cikin nishaxi.

Za a iya samun misalin xa mai tsauri a waqar *'Malam Alo na baraz zaki'* ta Alhaji Ali Marafa inda Makaxa Maidaji yake cewa:

Ma'ana	*Qirgar Ma'ana*	
Hawa	A^1	: Kura ba ta gasa da xan zaki,
Ajewa	A^2	: Azamarsu ba ta zama xai ba,
Sauka	A^3	: Don azamar su wane 'yar gajera ta,
Saukar Sauka	A^4	: Har yanzu ba ta yi tsawo ba,
Hawa	B^1	: Ko can da shirin hwaxa Ali yat tasa,
Hauhawa	B^2	: Tun da ba a shira mai wuqa ba,
Sauka	B^3	: Yanzu akwai wuqa akwai mashi,
Saukar Sauka	B^4	: Don an shirya mai makami,
Hawa	C^1	: Ko can dokin qwarai shi ka kama gudu,
Hauhawa	C^2	: Shi daxe shina hamidanci,
Sauka	C^3	: Shi kuma dokin su wane sai bixar tsaba,
Saukar Sauka	C^4	: Tun ba a gwada mai ruwa ba,
	X^1	: Malam Alo na baraz zaki,
	X^2	: Jikan Kilo xan Marafa.

(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^0/_{53}$ $^1/_4$)

A waqar *'Sarkin gandu ubangijin gutsun gawo'* wadda aka rera wa Sarkin Gandu, Makaxa Maidaji yana cewa:

Ma'ana	*Qirgar Ma'ana*	
Hawa	A^1	: Bara na iske masassaqa suna xibar hwaru,
Hauhawa	A^2	: Su ko su ukku ne suna cajin hwaru,
Sauka	A^3	: Guda sai yac ce tsaya gabas ka yi saurare,
Ajewa	A^4	: Guda sai yac ce tsaya arewa ka yi saurare,
Saukar Sauka	A^5	: Guda sai yac ce tsaya gabas ka yi saurare,
Hawa	B^1	: Tun ba su gama gardama ba ko sai ga Tsintau,
Sauka	B^3	: Su duka sun shirya shawara don su vace mai,
Saukar Sauka	B^4	: Yac ce duk wanda yag gusa kau zai harbai,
	X^1	: Sarkin Gandu ubangijin gutsun gawo,
	X^2	: Iro mijin A'i gandu mai xakin Kande.

(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^1/_{143}$ $^1/_9$)

A waqar *'Kai ab bahagon gulbi'* ta Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Muhammadu Bawa (1975 - 2003) Makaxa Maidaji yana cewa:

Ma'ana	*Qirgar Ma'ana*	
Hawa	A^1	: To, sai an yi kadankarma,
Sauka	A^2	: A san babba a san yaro,
Ajewa	A^3	: Kuma sai an yi karambatta,
Saukar Sauka	A^4	: A san wane a san wane,
Hawa	B^1	: Ai ina da uba sulxanin Gobir,
Hauhawa	B^2	: Wanda ka hisshe ni,
Sauka	B^3	: Ni ba ni gudun hitinar Gobir,
Saukar Sauka	B^4	: Duw wada tat tashi,
Hawa	C^1	: Ai ga taronmu na Sakkwato,
Hauhawa	C^2	: Mun gama kaya ga hawan daba,
Sauka	C^3	: An shirya dawakayye,
Saukar Sauka	C^4	: Amma babu kaman namu,
Hawa	D^1	: Doki ya hi dubu goma,
Hauhawa	D^2	: Raqumi ya hi dubu goma,
Sauka	D^3	: Duk an gamu an jera,
Saukar Sauka	D^4	: Uban Shantali ya canye,
	X^1	: Kai ab bahagon gulbi,
	X^2	: Uban Shantali xan Mamman,
	X^3	: Xan Inna Kilo Sarki,
	X^4	: Uban Bunu da baraz zaki.

(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^0/_{50}$ $^1/_7$)

A waqar *'Na taho gai da babba gardaye'* wadda Makaxa Maidaji ya rera wa Alhaji Xansanda Gangara, akwai inda yake cewa:

Ma'ana	*Qirgar Ma'ana*	
Hawa	A^1	: Na ishe tsamiya ta yi kyaun kunne,
Sauka	A^2	: Ga makiyaya da ko gittocinsu,
Ajewa	A^3	: Ga tumakinsu mai takin oda,
Saukar Sauka	A^4	: Babu damar a sara sai dibi,
Hawa	B^1	: Ina manoman ga 'yan takin oda,
Sauka	B^2	: Wanda ya iske gawo ya sare,
Saukar Sauka	B^3	: Ya yi kashi ne da kainai ya tasa,
Hawa	C^1	: Ina makiyayan ga sun sukar mulki,

Sauka	C^2	: Wanda ya iske gawo ya sare
Saukar Sauka	C^3	: Ya yi kashi da kainai ya tasa,
Hawa	D^1	: Shin ina Lawwali shi da Zaqoli,
Ajewa	D^2	: Ku zo ku shaida wa babba gardaye,
Sauka	D^3	: Na taho in yi mai kukan yunwa,
Saukar Sauka	D^4	: Yau gidajenmu ba sauran tsaba,
	X^1	: Na taho gai da babba gardaye,
	X^2	: Babba xan Inna mai gandun daji.

(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^1/_{147}$ $^1/_7$)

Sannan a waqar *'Toya matsahwa baqon dole'* ta Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Salihu xan Umaru Shawai (1945-1956). Wannan tana xaya daga cikin waqoqin da Maidaji ya goya daga waqoqin yayansa Makaxa Nadada. Makaxa Nadada shi ne makaxin sarki Salihu, sai bayan rasuwar sarki Salihu ne, Makaxa Nadada ya koma harkar malanta, sannan ne Makaxa Maidaji ya zama mawaqin masarautar Sabon Birni. Makaxa Maidaji yana cewa cikin waqar:

Ma'ana	*Qirgar Ma'ana*	
Hawa	A^1	: An koma shiri na Ali na Gambai,
Hauhawa	A^2	: Motsin duniya ya tashi,
Sauka	A^3	: Sarki za shi tarben gwamna,
Ajewa	A^4	: Ke mota je ki xauki baba,
Saukar Sauka	A^5	: Ki kai shi da lahiya don Allah,
Hawa	B^1	: Taron shawara ne yaz zo,
	B^2	: Mun yo rakkiya mun dawo,
Sauka	B^3	: An yit tambaya ba sarki,
Saukar Sauka	B^4	: Ban san inda zai kwana ba,
Hawa	C^1	: Ni ban san inda zai kwana ba,
Hauhawa	C^2	: Ko birnin Kabbi ko Dutse,
Sauka	C^3	: Sarki bai tsaya dun nan ba,
Saukar Sauka	C^4	: Amma ya wuce sai Wurno,
Hawa	D^1	: In an kuma yin wani taro,

	D^2	: Ko ni mai kixi sai na zo,
Ajewa	D^3	: Amma ban zuwa huntuna,
Sauka	D^4	: Sai an kuma ban wata riga,
Saukar Sauka	D^5	: Sai an kuma ban wani doki,
	X^1	: Toya matsahwa baqon dole,
	X^2	: Jikan Sanda baban Yari.

(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{1}$)

Saboda haka, daga waxannan bayanai da suka gabata, ke nan, tsarin xa a waqar baka yana iya zama mai sauqi ko mai tsauri kamar yadda masana da manazarta waqoqin baka na Hausa musamman Muhammad (1978) da King (1981 & 1986) da Abba & Zulyadaini (2000) da Gusau (2002 & 2003 & 2008 & 2010) da Satatima (2008) suke kallon tsari na xan waqar baka bisa tafarkin nazari ya kasance.

4.4 Tsarin Rerawa a Waqoqin Makaxa Maidaji

Tsarin rerawa fitaccen abu ne a cikin zubin waqar baka. Wajibi ne a sadar da waqar baka ta hanyar karin murya cikin rauji. Makaxa Maidaji Sabon Birni na xaya daga cikin makaxa da mawaqan baka na Hausa masu rera waqa a cikin qungiya waxanda ake yi wa qulli da qari.

A wannan qungiya, Makaxa Maidaji shi ne shugabanta, wato jagora, sannan yana da ‘yan amshi. Yawanci yakan rera xa xaya ko

biyu ko fiye da haka gwargwadon yadda ya tsara a waqarsa sannan masu yi masa amshi su furta sauran saxaru.

Wani abin tambaya game da wannan batu, yaya manazarta da masana adabin Hausa suke kallon tsarin rerewa a waqar baka?

Shi dai Gusau (2002[a]: 42) yana da ra'ayin cewa tsarin rerawa wata hanya ce wadda ake furta muryoyin kalmomi cikin jimloli da aka shirya a yanayi na waqa domin a isar da wasu saqonni ga jama'a. Rerawa ke nan ta shafi furuci da fatar baki inda ake fitar da qwayoyin sauti ta amfani da harshen da ake magana da shi a rauji da ya shafi yanayin hawa da saukar murya ko faxuwarta mai ma'ana.

Har wa yau, Gusau (2003) ya qara da cewa rerawa "tsari ne inda makaxi yake amfani da karin murya cikin rauji mai ma'ana ya furta kalmomin da ya zuba a cikin waqoqinsa" (Gusau, 2003: 38).

Shi kuwa Satatima (2009) cewa ya yi rerawa "hanya ce wadda ake furta qwayoyin kalmomi cikin jumloli da tsara su saxara-saxara a cikin xiya tare da samar da rauji mai inganci da ake shiryawa da nufin isar da wani saqo" (Satatima, 2009: 132).

Dangane da fasalin da masana da manazarta adabin Hausa suke kallon waqar baka ta Hausa, ayyukan King (1981 & 1986) da na Gusau (2001; 2003; 2002; & 2010) sun fito da wasu dabaru waxanda

ake amfani da su wajen fito da tsarin rerawa a waqar baka ta Hausa. Waxannan dabaru sun haxa da:

4.4.1 Qulli

Qulli dai shi ne “fara furta qaramin saqo a xa daga bakin jagora ko da na qungiya ne ko kuma na kaxaita ne” (Gusau, 2010:19). Qulli “wuri ne inda ake fara furta qaramin saqo a xan waqa wanda yakan qunshi saxara xaya ko biyu ko ma fiye da haka” (Gusau, 1993/ 2003: 38).

Makaxan kaxaita idan suka fara qulla waqa, babu mai yi masu karvi, babu mai yi masu qari, sannan babu masu yi masu tarbe, su da kansu suke yi wa waqoqinsu takidi.

Makaxa Maidaji yawanci a wannan qaulin yana da wata alkintacciyar sifa dangane da yadda yake fara qulla waqarsa a qungiyarsa. Kamar yadda wannan bincike ya tabbatar, musamman idan aka kalli matanin waqoqinsa a rataye na xaya da ke cikin wannan kundi. Mafi akasari, Makaxa Maidaji, yakan fara qulla waqarsa ne da rera gindin waqa.

Kaxan ne daga cikin waqoqinsa sukan zamanto ya fara da qulla xa wanda ba shi ne gindin waqarsa ba. Mafi akasarin lokuta kuma,

yakan rera layin farko zuwa na biyu ne na xa a gindin waqa sannan masu yi masa amshi su qarasa sauran. Misali a waqar *'Na Ali xan Bajini'* ta Sarkin Gobir Alhaji Umaru Salihu (1957-1966), Makaxa Maidaji Ya fara qullin waqar ne da:

Qulli : Na Ali xan Bajini,
: Jikan Shekara ka gama lahiya,
: Shi Nadabo qanin Buzuwa,
: Sarki uban Shamaki xan Kasau.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{2}$)

Sannan a waqar *'Inna ta Gobir'* , Makaxa Maidaji ya fara qullin waqar ne da cewa:

Qulli : Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{375}$ $^{1}/_{3}$)

Haka nan a waqar *'Noma ta 'Yar Buhari'* , Makaxa Maidaji ya fara qullin waqar ne kamar haka:

Qulli : Manoma Allah ya taimaka mana a wajen hatsi,
: Cikin duniya ba abin da yak kai ga hwaro-hwaro.
(Maidaji : Hira da Rima Rediyo, Sakkwato)

Wasu daga cikin waqoqin Makaxa Maidaji waxanda ya fara qullawa ba ta hanyar rera gindin waqa ba sun haxa da waqar nan ta *'Balaraben sarki'* ta Sarkin Zazzau, Alhaji Shehu Idris (1975 -), Makaxa Maidaji ya fara qulla waqar ne kamar haka:

Qulli : Abdulkarimu ya dawo,

: Kullum ana buga mai tamburra,
: Balaraben sarki,
: Aikinka ya yi kyau Sarkin Zazzau.
(Maidaji : Gusau, S. M. 2009: 197-203)

Sannan a wata rerawa ta waqar *'Balaraben sarki'* ta Sarkin Zazzau, Alhaji Shehu Idris (1975 -), Makaxa Maidaji ya nuna fasaharsa da balagarsa ta juya saqonninsa cikin harshe mai zalaqa da karsashi. Wato, yawanci xiyan waqoqinsa ba su dogara da junansu ba. Yakan iya xauko xa na farko ya kai tsakiya ko qarshe. Ya fara qulla waqar ne kamar haka:

Qulli : Aikinka ya yi kyau sarkin Zazzau,
: Balaraben Sarki.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{374}$ $^{1}/_{2}$)

Har wa yau dai, a waqar *'Sarki yai abin daka ya huta'* ta noma, Makaxa Maidaji Sabon Birni ya fara ne da qulli kamar haka:

Qulli : Baba mijin Shibo mijin Maryama,
: Giwa maganin itacen daji,
: Sarki yai abin daka ya huta,
: Zaki xan Abubakar xan Buda.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{2}$)

Akwai wata waqar da ya yi wa Sarkin Zazzau, Alhaji Shehu Idris (1975 -), *'Uban Na Allah uban Madauci',* Makaxa Maidaji ya fara qulla waqar ne ta hanyar rera saxaru uku sannan masu yi masa amshi suka karva masa da rera gindin waqar:

Qulli : Alhaji Mani ba shi qin kowa,
: Komi kac ce yanai ma,
: Shehu bai iya za'ida ba,
: Uban Na Allah uban Madauci,
: Shehu sannu da yau da gobe.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$)

A waqar *'Ya tara dame mai dama'* ta Alhaji Xanbawa, Makaxa Maidaji Sabon Birni ya fara ne da qulli kamar haka:

Qulli : Xan Bawa magajin Jimro,
: Na Badiga jikan Mana,
: Kai munka sani gun qwazo,
: Ya tara dame mai dama,
: Xan Bawa qanen mai gona.
(Maidaji : Gusau, S. M. 1983: 469-470)

4.4.2 Qari

Qari na nufin qarasa furta qaramin saqo a xa ('Yan Amshi/ Kaxaita), wato wuri ne inda yakan qunshi tarbe ko rakiya da gindin waqa (Gusau, 2003: 38; 2010: 19). Ke nan, masu yi ma Makaxa Maidaji amshi yawanci sukan yi masa qari a waqoqinsa yayin da ya fara qulla waqarsa. Bari mu kalli waqar '*Na yi mamakin harkatai'* ta tsohon Shugaban Qasar Nijeriya, Alhaji Shehu Aliyu Shagari, Makaxa Maidaji da yaransa sun tsara waqar ne kamar haka:

Qulli : Shugaban qasa Allah kyauta mai,
Qari : Zaman mutane na murna tai,
Gindin waqa : *Na yi mamakin harkatai*,
: *Shehu mai daraja Shagari*.

(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{5}$)

Sannan a waqar '*Ka buwayi maza sai na zo'* ta Garkuwan Dutsi, Innar Gobir, Makaxa Maidaji ya kawo wannan xan waqar ne kamar haka:

Qulli : Kai nis sani qasas Sabon Birni,
Qari : Tun da kai ka wa 'ya'yana toshi,
Gindin waqa : *Ka buwayi maza sai na*,
: *Mu gai da Garkuwa na xan Gardaye*.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$)

Idan aka kalli waqar '*Uban Makama uban Gardaye'* ta Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003), Makaxa Maidaji ya kawo wannan xa ne kamar haka:

Qulli : Ina mazan suke?
Qari : Sarkin Gobir ina mazan suke duk sun qare,
Gindin Waqa : *Uban Makama uban Gardaye*,
: *Bawa sannu da kwanan yaqi.*
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{144}$ $^{1}/_{1}$)

4.4.3 Tarbe

Furuci ne da ake tarbo abin da aka furta a qulli ('Yan Amshi kawai). Wuri ne inda 'yan amshi suke qarasa ma'ana qarama wadda

jagora ya faro ta a vangarensa na qulli. Ana yin wannan dabara ta tarbe a waqoqi waxanda ake rerawa "ta hanyar jagora da 'yan amshinsa, amma ban da a waqoqi waxanda makaxi ba shi da 'yan karvi" (2003: 38; 2010: 19).

Idan aka kalli waqar '*Allah za ni roqonka'* ta tsohon Gwaman Jihar Sakkwato, Alhaji Garba Nadama (1981-1983), domin a fitar da wannan batu ta yadda Makaxa Maidaji da yaransa suka tsara waqar kamar haka:

Qulli : Ko can duniya haka,
: Tag gada inji mai tulu,
Qari : Ka san duniya daxa,
Tarbe : Ba mai hurce iyakatai,
Gindin Waqa : Allah za ni roqonka,
: In yi biyag gwamna mai girma.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{52}$ $^{1}/_{6}$)

Har wa yau, a waqar '*Dogo xan Abubakar na Malumfashi'* ta Alhaji Abubakar Malumfashi, Makaxa Maidaji cewa ya yi:

Qulli : Gidan Mamman nit taho kixi sai na gai sai,
Qari : Sai ga Audu xan Bala ga Musa nan,
Tarbe : Komi nib bixa ga yau sai an yo min,
Gindin Waqa : Dogo xan Abubakar na Malumfashi,
: Jikan Dabo xan Kilo Gwamron giwa.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{52}$ $^{1}/_{7}$)

A waqar '*Namijin daga uban Gardaye'* ta Sarkin Gabas na Gwaranyo, Alhaji Umaru, Makaxa Maidaji da yaransa sun kawo wannan xan waqa ne kamar haka:

Qulli : Ina qaunar mai kama maciji,
Qari : In dai bai shaqu da ni ba,
Tarbe : Bari in kwanan mutum sun qare,
: Shi za ya kausai,
Gindin Waqa : Namijin daga uban Gardaye,
: Sarkin Gwaranyo.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{375}$ $^{1}/_{12}$)

Sannan a waqar '*Harka da ilmi mukai'* ta Makaxa Maidaji Sabon Birni wadda ya yi don nuna muhimmancin ilmi a tsakanin al'umma cewa ya yi:

Qulli : In dai mutum yav vace,
: Maisai ga hanya mu kai,
Qari : In ko mutum ya qiya,
Tarbe : Mu iza shi bayan gida,
Gindin Waqa : Harka da ilmi mu kai,
: Allah ya gyara mana,
: Mu gama da ban-gaskiya.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{147}$ $^{1}/_{2}$)

4.4.4 Rakiya/ Karvevveniya

Rakiya ko kuma karvevveniya na nufin maimaita qari da 'yan amshi suka riga suka yi wa jagora. Wato wuri ne inda 'yan amshi suke maimaita qarin da suka yi wa jagora daga lokaci zuwa wani xan

lokaci. Domin ita ma karveveniya furucin qari ne da nufin yi wa jagora rakiya. Ke nan, tarbe da rakiya da karvevveniya duk ana yin su ne a waqoqin da ake “rerawa ta hanyar qulli da qari daga jagora da ‘yan amshi” (Gusau, 2003: 39; 2010: 19).

Domin fayyacewa, ga misali daga waqar ‘*Kai ab bahagon gulbi’* ta Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003), Makaxa Maidaji ya fito da wannan tsari:

Qulli : Kai aj Jari da Shawai,
Qari : Alhaji kai a Ibrahima,
: Kai ne Mainasarar mashi,
Tarbe : Ina wanda ka tambaba,
Qulli : Gohe ya buga tamburra,
Qari : Dum mun ji su ga tarihi.
Qulli : Gauxe ya buga tamburra,
Karvevveniya : Dum mun ji su ga tarihi.
Qulli : Tambai ya buga tamburra,
Karvevveniya : Dum mun ji su ga tarihi.
Qulli : Yakuba ya buga tamburra,
Karvevveniya : Dum mun ji su ga tarihi.
Qulli : Ibrahim ya buga tamburra,
Karvevveniya : Dum mun ji su ga tarihi.
Qulli : Balarabe ya buga tamburra,
Karvevveniya : Dum mun ji su ga tarihi.
Qulli : Jadi ya buga tamburra,
Karvevveniya : Dum mun ji su ga tarihi.
Qulli : Jari Kada ya buga tamburra,
Karvevveniya : Dum mun ji su ga tarihi.
Qulli : Shawai ya buga tamburra,
Karvevveniya : Dum mun ji su ga tarihi.
Qulli : Salihu ya buga tamburra,
Karvevveniya : Dum mun ji su ga tarihi.
Qulli : Ummaru ya buga tamburra,

Karvevveniya : Dum mun ji su ga tarihi,
Qulli : ‘Yan Gatawa da Yakubawa,
Qari : Kowane an sa shi ga tarihi,
: Haba sarki riqe tarihin ga,
Tarbe : Da kowa ka bixa jiddun,
Takidi + Qulli : Haba sarki riqe tarihin ga,
: Da kowa ka bixa jiddun,
Qari : Kai kag gane mahwarinai,
Tarbe : Kuma ka san wada yak qare.
Gindin Waqa : Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{7}$)

Sannan a waqar ‘*Uban Na Allah uban Madauci’* ta Sarkin Zazzau, Alhaji Shehu Idris (1975-), Makaxa Maidaji ya qara fito da tsarin karvevveniya da wannan sifa da (King, 1986) ya bayyana kamar haka:

Qulli : Sarki da hanquri aka tsara taro,
Qari : Ka diba duk kwararon qasag ga,
Tarbe : Duk Shehu, Alhaji ya haxe su.
Qulli : Kabiru ya yi riqo jihag ga,
Qari : To, yanzu Mani ke riqon su,
: Ya riqe al’amarin jiharsu.
Qulli : To, Jahwaru ya yi riqo jihag ga,
Karvevveniya : To, yanzu Mani ke riqon su,
: Ya riqe al’amarin jiharsu.
Qulli : Muhammadu ya yi riqo jihag ga,
Karvevveniya : To, yanzu Mani ke riqon su,
: Ya riqe al’amarin jiharsu.
Qulli : Yamusa ya yi riqo jihag ga,
Karvevveniya : To, yanzu Mani ke riqon su,
: Ya riqe al’amarin jiharsu.
Qulli : Muhammadu ya yi riqo jihag ga,
Karvevveniya : To, yanzu Mani ke riqon su,

: Ya riqe al'amarin jiharsu.
Qulli : Abdulkarimu ya yi riqo jihag ga,
Karvevveniya : To, yanzu Mani ke riqon su,
: Ya riqe al'amarin jiharsu,
Gindin Waqa : Uban Na Allah uban Madauci,
: Shehu sannu da yau da gobe.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$)

Har wa yau dai a waqar '*Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa'* ta Sarkin Zazzau, Alhaji Shehu Idris (1975-), Makaxa Maidaji Sabon Birni cewa ya yi:

Qulli : Aminu ya yi mulkin Zazzau,
Qari : *Bai ci amana ba*,
: Ya yi ya gama ya hurce ana marabatai.
Qulli : Kabiru ya yi mulkin duniya,
Karvevveniya : Bai ci amana ba,
: Ya yi ya gama ya hurce ana marabatai.
Qulli : Hamza ya yi mulkin duniya,
Karvevveniya : Bai ci amana ba,
: Ya yi ya gama ya hurce ana marabatai.
Qulli : Yamusa ya yi mulkin duniya,
Karvevveniya : Bai ci amana ba,
: Ya yi ya gama ya hurce ana marabatai.
Qulli : Abdullahi ya yi mulkin duniya,
Karvevveniya : Bai ci amana ba,
: Ya yi ya gama ya hurce ana marabatai.
Qulli : Malam Musa da yay yi mulkin duniya,
Karvevveniya : Bai ci amana ba,
: Ya yi ya gama ya hurce, ana maraba tai,
Qulli : Yamusa ya yi mulkin duniya,
Karvevveniya : Bai ci amana ba,
: Ya yi ya gama ya hurce, ana maraba tai,
Qulli : Kuma Audu ya yi mulkin duniya,
Karvevveniya : Bai ci amana ba,
: Ya yi ya gama ya hurce, ana maraba tai,

Gindin Waqa : Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqon Allah ba ya tavewa.
(Maidaji : Gusau, S. M. 1988: 612-615)

Sannan a waqar *'Iro na Bawa baqon dole'* wadda Makaxa Maidaji ya goya daga Makaxa Musa Nadada ta Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Salihu Shawai (1945-1956) ya kawo tsarin karvevveniya ta wannan fasali ne:

Qulli : Ai koma shiri Magajin Mani,
Qari : Kogin duniya ya tashi.
Takidi + Qulli : Haba koma shiri Magajin Mani,
Qari : Kogin duniya ya tashi.
Takidi + Qulli : Kai dai koma shiri Magajin Mani,
Qari : Kogin duniya ya tashi.
Qulli : Ko wacce akwai dole Gobir,
Qari : Jagoran hwaxa ya tashi.
Qulli : Jari da yai irin nashi ya yi,
Qari : Bai xau shawarak kowa ba.
Qulli : Almu da yai irin nashi ya yi,
Karvevveniya : Bai xau shawarak kowa ba.
Qulli : Gohe da yai irin nashi ya yi,
Karvevveniya : Bai xau shawarak kowa ba.
Qulli : Maso xan Danga da yai irin nashi ya yi,
Karvevveniya : Bai xau shawarak kowa ba.
Qulli : Ko Baciri da yai irin nashi ya yi,
Karvevveniya : Bai xau shawarak kowa ba.
Qulli : Sobe da yai irin nashi ya yi,
Karvevveniya : Bai xau shawarak kowa ba.
Qulli : Mayaqi da yai irin nashi ya yi,
Karvevveniya : Bai xau shawarak kowa ba.
Qulli : Jangwarzo da yai irin nashi ya yi,
Karvevveniya : Bai xau shawarak kowa ba.
Qulli : Xangwamci da yai irin nashi ya yi,
Karvevveniya : Bai xau shawarak kowa ba.

Qulli : Xan mai Jadi da yai irin nashi ya yi,
Karvevveniya : Bai xau shawarak kowa ba.
Qulli : Ko Jari Kada da yai irin nashi ya yi,
Karvevveniya : Bai xau shawarak kowa ba.
Qulli : Ko Ummaru da yai irin nashi ya yi,
Karvevveniya : Bai xau shawarak kowa ba.
Qulli : Kai ba ka jan wani sarki,
Karvevveniya : Tsoro ba ya jan wani kaxo.
Takidi + Qulli : Salihu ba ya jan wani sarki,
Karvevveniya : Tsoro ba ya jan wani kaxo.
Qulli : Kai ka xauki ragamar musulmi,
Qari : Wannan ba a hana ka na Malam,
Gindin Waqa : Iro na Bawa baqon dole,
: Jikan na Sanda baban Yari.

Ke nan idan aka kalli fasalin waqoqin Makaxa Sa'idu Maidaji, yakan yi amfani da tsarin karvevveniya cikin nishaxi da walwala. Yakan kuma nuna fasaharsa ta naqaltar kalmomi ta hanyar nuna godiya ko alhini ko kuma tarihi da sauran hanyoyin da suke ginshiqan rayuwa. Haka zalika, idan an waiwayi wasu daga cikin waqoqinsa, Makaxa Maidaji kan aiwatar da karvevveniya a taqaice domin faxakarwa. Misali a waqar '*Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo'* ta Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003), Makaxa Maidaji Sabon Birni ya yi amfani da irin wannan salo na karvevveniya kamar haka:

Qulli : Dikko na biyo in gaisai,
Qari : Hwan xari yab bayar,
Karvevveniya : Alhaji ya dai gode abin da yas shiryo mai.
Qulli : Uban Dawaki,
Qari : Riguna ya aiko min,
Karvevveniya : Alhaji ya dai gode abin da yas shirya mai.

Qulli : Garkuwa,
Qari : Na dai gode ya biya ni,
: Yai komi,
Karvevveniya : Alhaji ya dai gode abin da yas shiryo mai.
Qulli : Ai dole in gai da,
Qari : Waziri wanda al Lajinge,
Karvevveniya : Alhaji ya dai gode abin da yas shiryo mai.
Qulli : To kuma na gode ma,
Qari : Alhaji xan Adamawa,
Karvevveniya : Alhaji ya dai gode abin da yas shirya mai,
Gindin Waqa : Ga ni na zaka murna gare ka sarki gwarzo,
: Mu qara fata Allah shi yaxa Sabon Birni.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{144}$ $^{1}/_{4}$)

Akwai tsarin rerawa na bayayyeniya da wasu daga cikin makaxan baka suka tasirantu da shi. Bayayyeniya wuri ne inda ake "karva-karvar furuci tsakanin jagora da 'yan amshi inda 'yan amshi za su dinga maimaita rera abin da duk jagora ya furta ba tare da canza ko da kalma xaya ba" (Gusau, 2003:39).

Inda gizo ke saqa a nan kuwa shi ne, daga cikin waqoqin Makaxa Sa'idu Maidaji guda xari xaya cif (100) da ke a cikin wannan kundi a rataye biyu, ba a sami misalin wannan tsarin rerawa na bayayyeniya ba. Dalili kuwa shi ne:

> Tun asali, tsarin rerawa na bayayyeniya bai yi yawa a tsakanin makaxan baka na Hausa ba. Kaxan daga cikin makaxan baka da ke amfani da tsarin rerawa na bayayyeniya sun haxa da Sarkin Kotson Kano, Makaxa Alhaji Abdurrahman da Makaxa Xanmugai Daura da Makaxiya Uwaliya Mai Amada da Sarkin Makaxa

> Muhammad Lawal. A wani qaulin kuma waqoqin da ke tafiya da tsarin rerawa na bayayyeniya sun qunshi waqoqin da ake samu a yankin jihohin da ke gabashin Katsina musamman a wajen mata masu kixan fada da Kano da kuma Zariya waxanda ke da alaqa da kixan banga ko na jauje ko goge da kukuma da kuma a waqoqin bori da na 'yan mata (King, 1986: 4-5 & Gusau, 2003: 44).

A taqaice, ga misalin bayayyeniya kamar yadda King (1986) ya kawo daga waqar '*Abdurrahman Sarkin Daura'* wadda Muhammad Lawal Sarkin Makaxa ya rera kamar haka:

Qulli : Audu xan Malam Musa,
Bayayyeniya : Audu xan Malam Musa.
Qulli : Xan Tafida xan Malam Musa,
Bayayyeniya : Xan Tafida xan Malam Musa.
Qulli : Mai qafo magajin Malam Musa,
Bayayyeniya : Mai qafo magajin Malam Musa.
Qulli : Dodo Zaki,
: Kowane na tambabar gida
Qari : Dodo Zaki,
Karvevveniya : Wane bai san Audun ba,
: Dodo Zaki.
(King, 1986: 4)

Ga wani misalin bayayyeniya wanda Gusau (2003) ya kawo daga waqar Makaxiya Uwaliya wadda ta rera wa wani malami:

Qulli : Malam ya yi, Malam ya yi,
Qari : Malam ya yi, Malam ya yi.
Qulli : Malam ya yi, Malam ya yi,
Bayayyeniya : Malam ya yi, Malam ya yi.

Qulli : Wannan ba malami ba ne,
Karvevveniya : Ya ga wata.
Qulli : Sai hira yake mata,
Karvevveniya : Ya ga wata.
Qulli : Alqalaminsa ya kare,
Karvevveniya : Ya ga wata.
Qulli : Ya yi kishingixe kamar bafade,
Bayayyeniya : *Ya yi kishingixe kamar bafade.*
(Gusau, 2003: 44)

A taqaice, idan an yi waiwayi adon tafiya dangane da ayyukan Gusau (1984[a] da 1996 da 2001 da 2002 da 2003 da 2010) za a tarar da ya taqaita waxannan dabaru na tsarin rerawa a waqar baka waxanda ake ganin da wahala makaxa da mawaqan baka na Hausa su zarce wannan qa'ida ko da kuwa na kaxaita ne ko kuma na qungiya ne. Ga tsarin kamar haka:

i) Tsarin Rerawa ta + Jagora + 'Y/Amshi/ ('Y/Karvi) + Qulli + Tarbe (Qari) -/+ Karvevveniya (Rakiya) + Gindin Waqa -/+ Bayayyeniya + Kixa.

ii) Tsarin Rerawa ta + Jagora –'Y/Amshi - Qulli –Qari – Gindin Waqa + Kixa.

iii) Tsarin Rerawa ta + Jagora + 'Y/Amshi/ ('Y/Karvi) + Qulli + Qari + Karvevveniya + Gindin Waqa – Bayayyeniya + Kixa.

iv) Tsarin Rerawa ta + Jagora -'Y/Amshi - Qulli - Qari -Tarbe - Karvavveniya (Rakiya) + Gindin Waqa + Kixa.

(Gusau, 2002: 44; -2003: 40; Gusau, 2010: 19-21)

Haka zalika, daga wannan xan taqaitaccen jadawali yana da matuqar muhimmanci a fahimci dangane da rukunonin makaxa da mawaqan baka na Hausa, tsarin rerawa ya rarrabu kashi-kashi.

Kashi na farko ya qunshi, jagora wanda ‘yan amshinsa suke qari da tarbe da karvevveniya ko rakiya kamar Makaxa Maidaji da Makaxa Musa Xanqwairo da Makaxa Salihu Jankixi da Makaxa Ibrahim Narambaxa da sauransu. Kashi na biyu kuma ya qunshi jagora da ‘yan amshinsa masu yin karvi ta maimaita gindin waqa zalla kamar Makaxa Mamman Shata da Makaxa Muhammadu Gawo Filinge da Makaxa Audu Karen Gusau da makamantansu.

Kashi na uku kuwa ya qunshi jagora da ‘yan amshinsa suna maimaita duk abin da ya furta ne ba tare da yi masa qari ba, kuma ba sa rera gindin waqa domin waqoqinsu ba su da gindin waqa. Wato masu xauke da tasirin bayyayyeniya ke nan. Kashi na huxu kuwa ya haxa da jagora wanda babu mai yi masa amshi ko karvi, sannan babu mai yi musu qari, ba tarbe ba rakiya sannan kuma babu karvevveniya ballantana bayayyeniya amma suna amfani da sautin kixa. Ire-iren

waxannan mawaqa sun haxa da Makaxa Xanmaraya Jos da Makaxa Babangida Kakadawa da sauransu.

Dangane da tsarin rerawa a waqoqin Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni, yana amfani ne da tsarin rerawa na +Jagora + 'Y/Amshi + Qulli + Qari + Tarbe +/- Rakiya/ Karvavveniya + Gindin Waqa + Kixa.

Abin nufi a nan shi ne yana fara qulla waqarsa a matsayinsa na jagora, sannan 'yan amshi su karva suna yi masa qari. A wani xan waqar kuma, 'yan amshi za su iya yi masa tarbe, inda a wani qaulin suna haxawa da rakiya ko karveveniya a tsakaninsu da jagora, daga bisani sai su rufe rerawar da gindin waqa. A haxe kuma cikin waqar suna amfani ne da sauti na kixan gangar taushi.

Makaxa Maidaji a matsayinsa na jagoran qungiyarsa, shi ne yake da ikon juya rerawa daga wata zuwa ga wata waqa. Sannan idan aka ji Makaxa Maidaji yana ta rera gindin waqa, to, waqar ke nan ta qare zai juya zuwa ga wata. Duk da a wasu lokuta kuma, 'yan amshinsa ne suke xaukar wannan nauyi na maimaita gindin waqa sau biyu zuwa uku, daga nan kuma Makaxa Maidaji yakan xora waqar da yake tunanin ita zai rerawa.

Misali, za a qara kafa hujja da waqar Makaxa Maidaji ta *'Mainasara na Isa na Musa'* wadda ya rera wa Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Umaru Na Allah (1957-1966). Idan an nazarci waqar, Makaxa Maidaji ya fara qulla waqar ne kamar haka:

Qulli : Sarki ya kwana da hwarin ciki,
Qari : Hay yau bai kwan da muni ga rai ba,
Gindin Waqa : Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{147}$ $^{1}/_{8}$)

Sannan, can a cikin wannan waqa ta Sarkin Gobir na Sabon Birni, Umaru Na Allah (1957-1966), Makaxa Maidaji Sabon Birni ya kawo fasalin karvevveniya kamar haka:

Qulli : Kowane sarki shina na shi yayi,
Qari : Ga namu zamani ba iri nai.
Qulli : Baciri ya yi mulki qasat,
Qari : Shi ma bai zo ziyara gabas ba.
Qulli : Goba ya yi mulki qasat,
Karvevveniya : Shi ma bai zo ziyara gabas ba.
Qulli : Jacili ya yi mulki qasat,
Karvevveniya : Shi ma bai zo ziyara gabas ba.
Qulli : Mayaqi ya yi mulki qasat,
Karvevveniya : Shi ma bai zo ziyara gabas ba.
Qulli : Goba ya yi mulki qasat,
Karvevveniya : Shi ma bai zo ziyara gabas ba.
Qulli : Ali ya yi mulki qasat,
Karvevveniya : Shi ma bai zo ziyara gabas ba.
Qulli : Mainasara ya yi mulki qasat,
Karvevveniya : Shi ma bai zo ziyara gabas ba.
Qulli : Almu ya yi mulki qasat,
Karvevveniya : Shi ma bai zo ziyara gabas ba.
Qulli : Gulbi ya yi mulki qasat,
Karvevveniya : Shi ma bai zo ziyara gabas ba.

Qulli : Xanmagaji ya yi mulki qasat,
Karvevveniya : Shi ma bai zo ziyara gabas ba.
Qulli : Jadi ya yi mulki qasat,
Karvevveniya : Shi ma bai zo ziyara gabas ba.
Qulli : Jari ya yi mulki qasat,
Karvevveniya : Shi ma bai zo ziyara gabas ba.
Qulli : Shawai ya yi mulki qasat,
Karvevveniya : Shi ma bai zo ziyara gabas ba.
Qulli : Salihu ya yi mulki qasat,
Karvevveniya : Shi ma bai zo ziyara gabas ba.
Gindin Waqa : Mainasara na Isa na Musa,
: Alhaji mun yi murnaz zuwanka.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{147}$ $^{1}/_{8}$)

4.4.5 Takidi a Waqoqin Makaxa Maidaji

Tabbas, da na gaba akan gane zurfin ruwa, dalili kuwa shi ne, takidi a waqoqin baka na Hausa, manazarta irin su King (1986) da Gusau (2002; 2003) da Satatima (2009) sun fito da alkintacciyar sifa bisa tsarin rerawa na takidi a bakin makaxa da mawaqan baka na Hausa.

Takidi dai “tsari ne karvavve a zubin waqoqin baka na Hausa, ta hanyar takidi makaxi yake maimaita rera wani zubi na xa a waqa” (Gusau, 2003: 44). Duk da yake:

> Takidi ya sava wa dokar furuci ko rubutu na yau da kullum, makaxa sukan yi takidi a layukan farko ko na tsakiya ko na qarshe na xa a waqar baka. Wani lokaci

akan yi takidi a rabin saxara, kuma ana yi wa dukkan xa a waqar baka takidi (Gusau, 2002: 47).

Har wa yau, akwai nau'in takidi wanda 'yan amshi suke yi wa jagora rakiya wanda ake kira da 'Takidin Karvevveniya'. Ban da wannan kuma akwai takidi na 'Bayayyeniya' inda 'yan amshi suke rera duk abin da jagora ya furta a layi-layi na xiyan waqa. Makaxa Maidaji yana da wata alkintacciyar sifa wadda yake amfani da ita wajen rera waqoqinsa ta hanyar amfani da takidi. Makaxa Maidaji yana amfani da takidi a saxarun farko ko na tsakiya ko kuma a saxarar qarshe. Wani lokaci, Makaxa Maidaji yakan yi takidi a rabin saxara, kuma ya yi wa dukkan xa a waqarsa takidi. Duk da haka, Makaxa Maidaji kan yi amfani da nau'in takidi na karvevveniya wanda 'yan amshi suke yi wa jagora rakiya.

A waqar Makaxa Sa'idu Maidaji ta '*Harka da ilmi mukai'* wadda ya rera domin tunatarwa tare da faxakar da al'umma bisa muhimmancin ilmi cewa ya yi:

Qulli : Tun dak Kaduna har Zariya,
: Had da manyan Kano,
Qari : Komi mutum za shi yi,
: Ya gama da 'yan Sakkwato.
Takidi + Qulli : <u>Lalle dak Kaduna har Zariya</u>,
: <u>Had da manyan Kano</u>,
Karvevveniya + Qari : <u>Komi mutum za shi yi</u>,

: Ya gama da ‘yan Sakkwato,
Gindin Waqa : *Harka da ilmi mukai*,
: *Allah ya gyara mana*,
: *Mu gama da ban-gaskiya*.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{147}$ $^{1}/_{2}$)

Har wa yau a cikin waqar Sarkin Tashar motar garin Sabon Birni, Alhaji Idi xan Argiji ta *‘Ya kwan yana aikin mota’* Makaxa Maidaji ya rera wannan waqa ne ta amfani da tsarin rerawar takidi a saxarun tsakiya na xan waqa kamar haka:

Qulli : Ga ni ina shirin tahiya Zazzau,
: Kuma ga ni ba ‘yan kuxxi,
Takidi : Ina nuhin tahiya Zazzau,
: Kuma ga ni ba ‘yan kuxxi,
: Ina dibin mota ni ko suna kallo na,
: ‘Yan kamishon suna dibin mota,
: Ni ko suna kallo na,
: Don sun gane ni da taron,
: Yara zay yawa bayana,
: Har an yi jinga na tada,
: Ba zan biyan kuxxi ba,
Gindin Waqa + Qari : Ya kwan yana aikin mota,
: Xan Argiji xan Shawai,
: Sarkin tasha jikan Idi,
: Jikan fulanin Vaure.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{54}$ $^{1}/_{5}$)

A waqar ‘*Xangara jikan xan Lahiya”* wadda ya rera wa Sarkin Maraxi Xangara, Alhaji Bala xan Sani. Makaxa Maidaji ya kawo fasalin takidi ne a rabin saxara inda yake cewa:

Qulli : Xangara kai as sinadari,
Qari : Ko da xai abin kallo,

: Kallo nai akai,
Takidi + Qulli : Xangara kai am muzakkari,
Karvevveniya + Qari : Ko da xai abin kallo,
: Kallonai akai,
Gindin Waqa : Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{146}$ $^{1}/_{6}$)

A wasu daga cikin xiya na wannan waqa ta '*Xangara jikan xan Lahiya"* wadda ya rera wa Sarkin Maraxi Xangara, Alhaji Bala xan Sani. Makaxa Maidaji ya kawo fasalin takidi ne wanda makaxa da mawaqa suke aiwatarwa a farkon saxara inda yake cewa:

Qulli : Na Alhajiya Gwamma,
Qari : Wanga zamani,
: Ku am manyan duniya.
Takidi + Qulli : Qanin Hajiya Gwamma,
Karvevveniya + Qari : Wanga zamani,
: Ku am manyan duniya.
Gindin Waqa : Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{146}$ $^{1}/_{6}$)

Idan aka kalli waqar Makaxa Maidaji Sabon Birni ta *'Kak ka xau reni'* wadda ya rera wa Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Ibrahim (1970-1975). Makaxa Maidaji ya yi amfani da tsarin rerawa inda wani lokaci akan yi takidi a dukkan xa na waqa. Har wa yau, wannan nau'in takidi ne wanda 'yan amshi suke yi wa jagora rakiya wanda wasu daga cikin manazarta suke kira 'Takidin Karvevveniya'.

A wannan waqa, Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni ya fito da tsarin rerawa na takidi inda ya yi amfani da kalmomi a maimaice ambatar kalma a wurare da dama. Wannan na xaya daga cikin abin sha'awa da ke bayyana zalaqa tare da balagar makaxin baka dangane da iya wasa da harshe, sannan da saqa zance cikin hikima kamar haka:

Qulli : Mamman na gode,
Qari : Don albarkacin Durumbu magajin Shawai.
Taikidi + Qulli : Mamman na gode,
Qari : Allah dai ya qara imani yai komi.
Taikidi + Qulli : Dango na gode,
Karvevveniya + Qari : Allah dai ya qara imani yai komi.
Qulli : Dango xan Galadima,
Karvevveniya + Qari : Allah dai ya qara imani yai komi.
Qulli : Salihu Marahwa na gode,
Karvevveniya + Qari : Allah dai ya qara imani yai komi.
Taikidi + Qulli : Garba na gode,
Karvevveniya + Qari : Allah dai ya qara imani yai komi.
Taikidi + Qulli : Malam Garba na gode,
Karvevveniya + Qari : Allah dai ya qara imani yai komi.
Gindin Waqa : Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{147}$ $^{1}/_{4}$)

Haka zalika, a cikin wannan waqa ta *'Kak ka xau reni'* wadda ya rera wa Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Ibrahim (1970-1975) Makaxa Maidaji Sabon Birni ya ci gaba da rera waqar ta amfani da takidi kamar haka:

Qulli : Zamanin akwai manya,
Qari : Tsuntsu ko da yaushe ba ya gudun Xantsara.
Taikidi + Qulli : Zamanin akwai Jadi,

Qari : Jadi ko da yaushe ba ya gudun Xantsara,
Taikidi + Qulli : Zamanin akwai manya,
Qari : Ai Kakanku bai yi qyamar kakana ba,
Gindin Waqa : Kak ka xau reni,
: Xandango Durumbu xan Inna xan Shawai.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{147}$ $^{1}/_{4}$)

4.5 Matsayin Salo a Waqar Baka

Kalmar salo na xaya daga kalmomin fannu da masana suke amfani da su domin bayyana dabaru da ma'abota ayyukan adabi sukan yi amfani da su domin isar da saqo. Salo a waqa zavi ne na makaxi ya yi amfani da shi wajen qawata harshen da yake magana da shi ko kuma saqonnin da yake zubawa a cikin waqa. A dunqule:

> Ana aiwatar da saqonni a waqoqin baka cikin qarin gishiri ta amfani da kalmomi masu balaga, masu zaqi, masu jan hankali, waxanda suke da salo ingantacce. Ana tantance salo a waqar baka ta fito da halayen salon, mai sauqi ne ko mai tsauri, mai garxi ne, mai armashi ko maras karsashi ne, ko kuma ma mai gundurarwa ne (Yahya, 2001:1).

Gusau (2002:5) yana ganin ta dabarar salo, makaxi kan samu damar ya harzuqa ran mai sauraro da kalmomin da ya zuba waxanda

za su sosa zuciyar mai saurare, daga nan tunaninsa ya kaifafa, har ya shiga wani wadi na tunani tsakaninsa da mai waqa.

Ta haka ne wannan babi ya warware zare da abawa dangane da salo, tun daga ma'ana har zuwa matakai waxanda Makaxa Sa'idu Maidaji yake amfani da su a waqoqinsa dangane da salo.

4.6 Me ake Nufi da Salo

Kalmar salo tana da ma'anoni biyu, ta lugga da kuma ta manxiki. Daga cikin ma'anonin lugga akwai "hanyoyi na qirqira wani abu ko yanayin wani abu ko dabaru ko kuma fasali" (Abraham, 1962:772). Qamus kuma ya bayar da ma'anar salo ta lugga da cewa 'yayi' ko 'sauyi' ko 'launi' ko 'fice' ko 'hanya' ko 'siganta' (Awde,1996: 390 da CNHN, 2006:635).

A ma'anar kalmar salo ta fannu kuwa masana da yawa sun baje kolin tunaninsu ta hanyar bayyana madosarta inda suka tsayu a kan wata "dabara ce wadda ake kyautata harshen waqa da ita tare da qawata zaren tunani, ta yadda za a sarrafa shi cikin azanci ta zaven kalmomi ko sakaya furuci, a isar da saqo wanda ake ginawa ta hanyar kaifafa tunani da balaga mai armashi" (Xangambo, 1981:2 da Sa'id, 1981:35 da Yahya, 2002:220).

Abin da ake nufi da salo a waqar baka shi ne “hanyoyin da makaxi ya bi domin isar da saqonsa wanda ya qunshi zavi ko qarin daraja wanda ya rataya a wuyan mawaqi” (Abba & Zulyadaini, 2000:11). Za a iya nazartar salon waqoqi Makaxa Maidaji Sabon Birni ta wannan siga:

4.7 Adon Harshe A Waqoqin Makaxa Maidaji

Adon harshe wata dabara ce wadda ake amfani da ita wajen yi wa harshen waqa kwalliya a yayin isar da qananan saqonninta a cikin xiya. Adon harshe ya qunshi gwalagwalan kalmomi masu qawata zance da zuqatar mai sauraro tare da kambama wanda ake yi wa.

Toronkawa (2006:7) da Abbas (2008:140) da Gwarzo (2010:28) da sauransu suna ganin adon harshe “hikima ce da mawaqan baka suke yin amfani da ita domin qara wa waqarsu armashi”. Ke nan adon harshe:

> Dabara ce ta yi wa magana kwalliya don qara mata armashi da daxi wanda shi ne ma’auni na gwada hikimar zance da balaga da xan’adam yake da ita a harshensa da kuma sauran abubuwa da suke kewaye da shi. Hausawa na cewa idan kana da kyau ka qara da wanka (Xan’iya, 1997: 12).

Akwai hanyoyi da yawa waxanda ake bi ta kansu a yi wa waqa ado domin qara mata armashi da isar da saqonta cikin jan hankali, da suka haxa da kamantawa da siffantawa da alamtarwa da jinsintarwa da kinaya da qarangiya da sauransu. Ga bayanan waxannan dabaru na adonta harshe a waqar baka kamar haka:

4.7.1 Tamka

Tamka dabara ce wadda ake kwatanta abubuwa biyu dangane da wasu darajoji da za su iya zama na daidaito ko na fifiko ko na gazawa (kashi) ta amfani da wasu kalmomin na yin kamance, misali *kamar* da *tamkar* da *awa* da *kama* da *daidai* da *sai ka ce* da *xara* da *gaza* da *bai kai* da sauransu (Bargery, 1934:542 da Cuddon, 1979:629 da Umar, 1984:55-57).

A waqar da Makaxa Maidaji ya rera wa Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Umaru Shawai (1916-945), duk da dai asalin waqar ta yayansa ce, Alhaji Musa Nadada, amma daga bisani, Makaxa Maidaji ya hau halifancin sarautar waqa a masarautar Gobir daga hannun Makaxa Nadada sai ya goyi wannan waqa ya yi mata qare-qare. A cikin wannan waqa, akwai misalin tamka kamar haka:

Jagora : Ai Kusu da yay yi sheka,
: ‘Ya’yansa yay yi ma,
: Bilbili da yai gida,

: Don ‘ya’yansa yay yi,
: Ummaru bai kau ba,
: Sai da yak kai ga halin na Innuwa,
‘Y/Amshi : Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban Zagi xan Mamman na Baciri.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$)

Cikin waqar Makaxa Maidaji Sabon Birni ta Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003) ya kwatanta wannan sarki da kakanninsa irin su Muhammadu Babari da Muhammadu Maijindi da kuma Muhammadu Nadango waxanda tarihi ya nuna sun yi sarautar qasar Gobir ne tun qarnin bayyanar Sarkin Gobir na Sabon Birni, Bawa Jangwarzo. Ga abin da Maidaji yake cewa:

Jagora : Shiryayye na Dango,
‘Y/Amshi : Xan Inna fifita ni na Malam Salihu.
Jagora : Yau kai am Muhamman Babari,
: Kai am Muhamman Maijindi
‘Y/Amshi : Kai am Muhamman na Dango,
: Yadda duk ka hwaxa daidai kake,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai nikai.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{374}$ $^{1}/_{7}$)

A wata tafiya da Makaxa Maidaji ya yi tare da Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003) zuwa jihar Sakkwato, cewa ya yi:

Jagora : Zuwanmu Sakkwato kwananmu takwas,
: Gidan Dikkon Gande,

‘Y/Amshi : Ana ta ba mu abinci,
: Mun qoshi, mun hole birjik kamad duma,
Jagora : Sakkwato mun ci abinci iri-iri,
‘Y/Amshi : Kala-kala, ham munka sake hwata,
: Jikinmu yak koma jawur kamaj jini.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{142}$ $^{1}/_{4}$**)**

A waqar da Makaxa Maidaji ya rera wa Alhaji Muhammadu Xanqoqari ya kawo misalin tamka inda yake cewa:

Jagora : Wani ya yi gida ba dame,
‘Y/ Amshi : Ka ga kamar an yi ba a yi ba.
Jagora : Su wane sun yi dubun tanbaxa,
: Dubun da an yi kamar ba a yi ba,
: Dubun da babu hura ba tuwo,
‘Y/ Amshi :Ya hana aikin yini,
: Muhammadu xan qoqari.
(Maidaji : Gusau, S. M. 1983: 470-473)

Har wa yau dai, a lokacin da Makaxa Maidaji yake rera waqar Alhaji Hashimu D.P.O na garin Gusau, ya kawo misalin tamka ne da ke nuna fifiko ko kuma gazawa kamar haka:

Jagora : Maidaji cikin daji nike,
'Y/Amshi : Hashimu yi tattalin mai da ni gari,
: Tun da ba Bahillace nike ba,
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{74}$ $^{1}/_{1}$**)**

A waqar Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003), Makaxa Maidaji ya ci gaba da cewa:

Jagora : Kai aj Jari da Shawai,
'Y/Amshi : Alhaji kai a Ibrahima,

: Kai ne mai nasarar mashi,
: Ina wanda ka tambaba,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{7}$**)**

Har wa yau dai, a cikin waqar Sarkin Gobir na Sabon Birni, Makaxa Maidaji ya kwatanta sarkin ne da kakanninsa na asali, mafi akasari kowane mahaluqi yana jin daxin a zayyano asalinsa balle ma har a kwatanta shi da su. Ga abin da Makaxa Maidaji ya ce:

Jagora : Haba sarki yi tunani,
: Ka tuna tsohinka na addini,
: Na farko Abdullahi,
: Da Kaso Birnin Mai-Lalle,
: Da Dango mai Tansidi,
: Da Sardauna Sama'ila,
'Y/Amshi : Kowa ad da hwaxi Alqalawa *babu* kaman naka.
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan Inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{7}$**)**

4.7.2 Kwalliya

Kwatance na siffantawa, dabara ce wadda ake xaukar misali darajar wani abu a xora wa wani abu ba tare da amfani da wani tsakani ba (Scot, 1965:178 da Shipley, 1970:197 da Umar, 1984: 55). Akwai misalan kwalliya da yawa a waqoqin Makaxa Sa'idu Maidaji

Sabon Birni, a wata waqa da Makaxa Maidaji ya rera wa Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Umaru xan Salihu (1957-1966). Ya siffanta Sarki Salihu da giwa cikin zalaqar harshe tare da nuna karsashi da danqon soyayyar da ke tsakaninsa da sarki. Inda ya kwarzanta sarkin ta nuna farin cikinsa da samun sarautar da ya yi cikin dubban ‘yan’uwansa manema wannan gadon mulki kamar haka:

Jagora : Na Inna magajin sarauniya,
'Y/Amshi : Ruwan dare mai kama duniya,
: In dai kyauta ta Bawa,
: Ko da yaushe qira min wata yakai.
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{143}$ $^{1}/_{4}$)

Wannan xan waqa na nuni ga faxar nan ta Hausawa da ke cewa ‘ruwan dare game duniya’. Yayin da Makaxa Maidaji yake rera wa Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Ibrahim (1970-1975) ya kwatanta duniya da gishiri sai wanda ya xanxana zai gane. Ga dai abin da ya ce:

Jagora : Ashe duniya gishiri ta,
'Y/Amshi : Wane kay ya sake ta koma daudawa.
Jagora : Gaba da baya qarhin doki,
'Y/Amshi : In dai batu, batun Gobir na,
: Wada kuk ka hwaxi Ibrahim na ciki,
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{144}$ $^{1}/_{6}$)

Haka zalika a waqar Alhaji Muhammadu Xanqoqari, Makaxa Maidaji ya qawata zancensa tare da tunzura wanda yake yi wa waqa inda yake cewa:

Jagora : To, kowa shi hanqure, Babari,
'Y/Amshi : Da Gwamna sun yi magana ta zauna.
Jagora : Uban xan Jari kutunvun vauna,
'Y/Amshi : Babu mai iya tare ma hanya,
: Sai mu taru mu yi roqon Allah,
: Inda Alhaji Bakwai N.P.N.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{75}$ $^{1}/_{10}$)

Sannan a waqar Inna Gobir kuwa Makaxa Maidaji ya kawo salon qawatawar ne ta wannan siga:

Jagora : Hazo dushe rana,
'Y/Amsh : Goge mai kashe molo,
: Gogarma ta Iro,
: Gagara badau 'yak Kaso,
: Ta Muhamman Dosau 'yam mayaqi.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{145}$ $^{1}/_{5}$)

Awaqar da ya rera wa Sarkin Zazzau, Alhaji Shehu Idris (1975-) ya kwatanta alherin da yakan samu a wurin Mai Martaba Sarki a matsayin malkar damina wadda ke cike da ni'ima:

Jagora : Shehu na Xanmadami babban hadari,
'Y/Amshi : Mai ruwa sannu,
: Ran da yay yi malka ni'ima ba ta qarewa.
: Gaskiya da roqon Allah ba ka fasawa,
: Wanda duk yake roqon Allah ba ya tavewa.
(Maidaji : Gusau, S. M. 1988: 612-615)

A waqar Sarkin Katsina Gusau, Alhaji Muhammadu Kabir Xanbaba Makaxa Maidaji ya qara kawo wani misalin kwalliya inda ya bayyana cewa tun fil azal ya gargaxi masu son wannan sarauta cikin nuni na ishara da Mai Martaba Muhammad Xanbaba ne zai haye gadon sarauta. Ga abin da yake faxi:

Jagora : Kokowar kare da kura,
'Y/Amshi : Ai na hana ta tun bara da rani,
: Karen gida yac ce,
: Ni wanga gargaxi yai mani daxi,
: Ginshimin Yari Magajin Magaji,
: Barkakka da hwama,
: Ina tahowa mu gano,
: Mai riqon Gusau mai raba kaya.
(Maidaji : Gusau, S. M. 2009: 209-210)

Cikin waqar babban malamin Sarkin Garin Tara, Malam Hassan Xansanda, Makaxa Maidaji ya qawata zancensa game da wannan malami da cewa:

Jagora : Ga shi giwa na saraki ya dankwashe gaba,
: Na Umma ruwan wanke dartsa Uban Makau,
'Y/ Amshi : Ga Uban Sale ya mai da kora na xan mantai,
: Qi garaje uban Meli bai xauki wargi ba,
: Dole in yaba Malam Hassan mai halin girma.
(Maidaji : Fasahar Baka, 2004)

A lokacin da yake rera wa Sarkin Zazzau, Alhaji Shehu Idris (1975-) waqa kuwa, Makaxa Maidaji ya bayyana wani xa a cikin waqar kamar haka:

Jagora : Ni dai ina ganin balbela da ita da shanu,
'Y/Amshi : Ai ko da yaushe nan taka samun abin da tac ci,
: Kak ka yarda da raini uban Baraya,
: Shehu Alhaji Allah ya taimaka ma.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{52}$ $^{1}/_{7}$)

4.7.3 Alamtarwa

Alamtarwa wata hanya ce wadda ake bayyana wani abu ta ba shi wata alama da ta yi kama da shi ta fuskar siffa ko yanayi ko xabi'a ko hali ko asali ko jarumtaka ko qasaita da sauransu (Cuddon, 1976:671 da Umar, 1984: 46-49 da Xangambo, 2007:46). Alamtarwa, ke nan, dabara ce wadda take wakiltar wata manufa. Ga misali daga waqar Inna Gobir, inda ya ce:

Jagora : Hazo dushe rana,
'Y/Amsh : Goge mai kashe molo,
: Gogarma ta Iro,
: Gagara badau 'yak Kaso,
: Ta Muhamman Dosau 'yam mayaqi.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{52}$ $^{1}/_{7}$)

A cikin waqar nan da Makaxa Maidaji ya rera wa Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Umaru xan Salihu (1957-1966) ya qara kawo wani misalin kamar haka:

Jagora : Gwamron giwa uban lihidda,
: Bawa qanin Sahi bahago,
'Y/Amshi : Jari magajin na Abu,
: Ko da yaushe yana nan wurin jiya.
Jagora : Toron giwa ya katse haqo,

'Y/Amshi : Masu haqon sun yi birkixa,
: Ku kwashe haqon nan ku tashi,
: Tun da Bawa na Dango gani ya kai,
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{143}$ $^{1}/_{4}$)

A waqar tsohon Gwamnan Jihar Sakkwato, Makaxa Maidaji ya alamta duniya da cewa ba a tava zarce wa'adin da Allah maxaukaki ya zartar a kan komi. Shi ya sa sai ya ce:

Jagora : Ko can duniya haka,
: Tag gada inji mai turu,
'Y/Amshi : Ka san duniya daxa,
: Ba mai hurce iyakatai,
: Allah za ni roqon ka,
: In yi biyag gwamna mai girma.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{52}$ $^{1}/_{6}$)

A waqar Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Umar Shawai (1916-1945), Makaxa Maidaji ya alkinta in son samu ne duk mahaluqi yakan so ya zam yana da wanda zai gaje shi. Ya yi amfani da wannan dama ya isar da saqonsa kamar haka:

Jagora : Ai kusu da yay yi sheka,
: 'Ya'yansa yay yi ma,
: Bilbili da yai gida,
: Don 'ya'yansa yay yi,
: Ummaru bai kau ba,
: Sai da yak kai ga halin na Innuwa,
'Y/Amshi : Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$)

Sannan, Makaxa Maidaji ya qara kawo misalin alamtarwa a waqar Sarkin Maraxi Xangara, Alhaji Bala xan Sani inda ya kwarzanta shi da babu wani sama da shi in ba Allah maxaukaki ba. Da ma Hausawa na cewa 'babu sarki sai Allah', to, Makaxa Maidaji ya ce Sarkin Maraxi ag girgije, dubi abin da yake cewa:

Jagora : Tun da Allah as sarki,
'Y/Amshi : Yanzu ko Bala xan Sani ag girgije,
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mu kai.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{146}$ $^{1}/_{6}$**)**

A waqar Alhaji Abdullahi Uban Dawaki, Makaxa Maidaji ya qara kawo misalin alamtarwa kamar haka:

Jagora : Zaki mai sulke da bindiga mai masu,
'Y/Amshi : Kar ka so ka ji tsoro,
: Abin da ba ka gada ba,
: Ginshimin Zakari Baqadire,
: Qasaitacce uban Dawaki,
: Na Isaka gamda'aren mai daga.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{374}$ $^{1}/_{7}$**)**

4.7.4 Jinsintarwa

Jinsintarwa wata dabara ce ta xaukar wata daraja ko hali ko siffa ko aiki da sauransu na wani jinsi a xora wa wani jinsi. Ke nan "akan xauki wata halayya, bisa misali, da kawai jinsin mutum ko dabba ko tsuntsu ko wani abu aka sani da ita sai a ba wa wani jinsin

da ba a san shi da ita ba" (Yahya, 2002:226 da Gusau, 2003:59 da Xangambo, 2007:45).

Manazarta suna kan ra'ayin jinsintawa ta kasu zuwa mutuntarwa da dabbantarwa da abuntarwa. Daga bisani, Gusau (2003:590) ya bayyana bisa dukkan alamu ba kasafai ne makaxan baka suke sanya xiyan jinsintarwa a waqoqinsu da suke rerawa ba.

Za iya tsakuro misalin jinsirtarwa a waqar Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Umaru xan Salihu, inda Makaxa Maidaji ya fara buxe waqar ne ta sigar jinsintarwa inda ya xauki darajar xan zaki ya yi amfani da ita, inda ya ce:

Jagora : Binu xan baraz zaki Xanbawa,
'Y/Amshi : Jikan Kilo gwamron giwa,
: Na Malam gwanin daga,
: Na Allah jikan hillani xan Musa na Malam.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{147}$ $^{1}/_{6}$)

A cikin waqar nan ta D.P.O. na 'Yansanda da ke babban birnin Gasau cikin Jihar Zamfara Makaxa Maidaji cewa ya yi:

Jagora : Toron ku na Yawuri ya yi tsawo,
'Y/Amshi : Jibirila yas shirya maku shi,
: Tun da ba uban wani yay yi shi ba,
: Na shira kaya za ni garai,
: Na Alhaji D. P. O. na Gusau.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{74}$ $^{1}/_{1}$)

A cikin waqar Sarkin Gobir na Sabon Birni Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003) Makaxa Maidaji ya kawo misalin jinsintarwa da ya danganci abunta sauran ‘ya’yan sarki masu neman sarauta inda yake cewa:

Jagora : In ka ga xan hwarauta yai shiri,
‘Y/Amshi : Ga karhuna ga kambuna,
: In ba kare ya taho gidan,
: Qaryah hwarauta ta ya kai,
: Sarki Muhammadu xan Kilo,
: Koyaushe murna tai ni kai.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{374}$ $^{1}/_{7}$)

Sannan a waqar Alhaji Aliyu ‘Yankuzo, Makaxa Maidaji ya fito da misalin jinsintarwa kamar haka:

Jagora : Da ka ga sufar xan sarki,
‘Y/Amshi : Yara kun ga mai iya ta da gida,
: Ba matsalar ka tashi gidanku na ainihi
Jagora : Xan zaki hay ya qasura,
‘Y/Amshi : Hay ya yi jan wuya ya hiddo qwarai-qwarai,
: A gai min da Alhaji Ali na ‘Yankuzo,
: Duniya ta gyara wurin zama.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{52}$ $^{1}/_{4}$)

A waqar Alhaji Bakwai N. P. N., Makaxa Maidaji ya qara kawo misalin jinsintarwa kamar haka:

Jagora : Uban xan Jari Kutunvun vauna,
‘Y/Amshi : Babu mai iya tare ma hanya,
: Sai mu taru mu yi roqon Allah,
: Inda Alhaji bakwai N. P. N.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{75}$ $^{1}/_{10}$)

4.7.5 Kinaya

Kinaya dabara ce ta “sakaya zance da ake son isarwa ta juyar da shi daga ma’anarsa ta asali (farko) zuwa ga wata ma’ana ta biyu”. (Gusau, 1996:313-314; 2003:60). Har wa yau:

> Kinaya dabara ce ta amfani da kalma ko kalmomi domin tunanin da suke sa mutum ya yi game da ma’anoninsu, ya yi naso ga wani abu ko mutum da aka danganta kalma ko kalmomi da shi. Wato sanin da mutum yake da shi dangane da siffofin abin da kalmar da aka yi kinaya da ita zai wulla zuwa ga wani abu ko mutumin da aka yi wa kinayar. Wannan shi zai sa mai karatu ko mai sauraro ya fahimci siffar da mawaqi ke son a san ko a kalli wanda ya yi wa kinayar (da ita). Kinaya mafi sauqi ita ce wadda ake cewa abu kaza, kaza ne (Yahya, 1997: 46-47).

A waqar nan dai ta Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Umaru Shawai (1916-1945) Makaxa Maidaji ya kuma rattabo wani xa a cikin kinaya inda yake cewa:

Jagora : Wani <u>wawa</u> marar gaba,
‘Y/Amshi : Wai yaz zo a ba shi sarki sai D. O. ya hana,
Jagora : Wani <u>tsoho</u> mahaukaci,
‘Y/Amshi : Sai ya zo a ba shi sarki sai D. O. ya hana,
Jagora : Sai yac ce an qi ba ka,
‘Y/Amshi : <u>Xebi da qarhin Babarbara</u>,
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban Zagi xan Mamman na Baciri.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$)

Makaxa Maidaji ya rera wa Alhaji Mamman ‘Yankuzo waqa wadda a cikinta ya kawo xa cikin kinaya inda ya nuna mutum yana tafiya a hanya mai kyau ba zai taka kashi ba ko qaya, amma in ya shiga daji akwai alamun ya tako kashi ko qaya. To, Makaxa Maidaji yana bayyana cewa ya biyo hanya mai kyau ya zo wurin Alhaji Mamman domin a yi shagali, ga dai abin da ya ce:

Jagora : Shi <u>wanda ax xauke ga hanya</u>,
‘Y/Amshi : <u>Ba ya zuwa sarma da daji</u>,
Jagora : <u>Ai wanda ax xauke ga hanya</u>,
‘Y/Amshi : <u>Ba ya zuwa sarma da daji</u>,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{52}$ $^{1}/_{4}$**)**

Can kuma sai ya qara da:

Jagora : Ga Xangara ga Alhaji Mamman,
‘Y/Amshi : Ana <u>shirin shaviri gana</u>,
: Madogara Alhaji Mamman,
: Duniya Duniya ga ta gare ka.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{52}$ $^{1}/_{4}$**)**

Dubi yadda Makaxa Maidaji ya fito da wani misalin kinaya a wannan xa da ke mai kan uwa da wabi a cikin waqar Alhaji Mamman xan Abubakar Malumfashi. Ga abin da ya ce:

Jagora : Ga wani horo da zan hwaxa ma xan Shawai,
'Y/Amshi : Allah sa ka xauki horon in na yi.
Jagora : Ai kyawon xa shi xauki horon tsohonai,
'Y/Amshi : Ai ban ce ka xauki horon kowa ba.
Jagora : In ka ishe xan baqo bakin garkatai,
'Y/Amshi : Kai ka san akwai duhu bayan qumci,
: Dogo xan Abubakar na Malumfashi,
: Jikan Dabo xan Kilo Gwamron giwa.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{52}$ $^{1}/_{7}$)

4.8 Salon Sarrafa Harshe

Waqa dai, Abdulqadir (1975) yana ganin harshenta cikakke ne, duk da a wani lokaci yakan kauce wa wata qa'ida ta nahawu ya zama 'taqadarin harshe'. Gusau (2011) yana cewa:

> Harshe shi ne babban tubalin da ake amfani da shi wajen gina saqo, sannan a yi amfani da dabaru na nuna gwaminta a isar da saqon ga jama'a. Harshe yana ratsa dukkan sassan rayuwa kuma babban tubali ko ginshiqi ne a tsakanin rayuwar kowace al'umma. Harshe, a nan, ana nufin sarrafaffen zance cikin azanci da hikima da fasaha ta amfani da basira da kuma balagar zance tare da qirqira ta amfani da salon sarrafa mai qayatarwa, kacokan harshen waqa ke nan (Gusau, 2011: 3-4).

Har wa yau (Muhammad, 2006:1-11) yana ganin a tsarin rera waqoqi, akan yi amfani da ginshiqan turaku guda biyu; na xaya dai shi ne *harshe, na biyun kuma su ne rumbun kalmomi da jimloli*.

Rumbun kalmomi da jimloli ake tattaunawa yayin rera waqa. Rumbun kalmomi da jimloli ke ginin tubali qerarre a tayar da waqa dabaibaye da kalmomi masu xaga hankali tare da kaifafa zukata da tunani, wanda za a iya sauraro ko a haddace ko kuma a karanta a rubuce. Salon sarrafa harshe a waqoqin Makaxa Maidaji sun haxa da:

4.8.1 Qarangiya

Qarangiya dabara ce ta luguden haruffa ko kalmomi ko wasa da harshe cikin baqaqe da kalmomi a lokacin da ake qoqarin isar da wani saqo. Akan kira wannan gagara-gwari ko kakkarya harshe (Ibrahim, 1983: 79 da Xangambo, 1980: 294-298; 2007:49 da Gusau, 2003:61). Ga misali daga waqar da Makaxa Maidaji ya rera wa Garkuwar Dutsi, Innar Gobir:

Jagora : Gudurmusun dutsi,
'Y/Amshi : Mai xaukak ka shi ka ji ba 'yan kallo ba.
Jagora : Ina ruwan 'yan kallo,
'Y/Amshi : Kowa ya sa idanunai sai dibi,
: Ka buwayi maza sai na zo,
: Mu gai da Garkuwa xan Gardaye.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$)

Sannan a cikin waqar Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Ibrahim (1970-1975) Makaxa Maidaji cewa ya yi:

Jagora : Na biyo bisa hanya,
'Y/Amshi : Ko da xai ba ni wasan daji kakkarai.
Jagora : Kakkarai qaqqarqa,

'Y/Amshi : Kakkarai in ji zabin daji masu qwai,
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{146}$ $^{1}/_{2}$)

Har wa yau cikin waqar Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Umaru xan Salihu (1957-1966) Makaxa Maidaji ya qara da cewa:

Jagora : Ta-na-ta-hu ba cilu-cilu ba,
'Y/Amshi : Alhaji kai a Baranqwame,
: Tun da ina nan gare ka,
: Ba Uban da ka sa min baqi kawai,
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{143}$ $^{1}/_{4}$)

A waqar Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Umaru Shawai (1916-1945) Makaxa Maidaji duk da cewa Sakkwatanci ne ya yi amma ya maimaita kalmomi ta sigar wasa da harshe, ga dai abin da ya ce:

Jagora : Ran dakak kututturu,
'Y/Amshi : Ran nan anka kakkashikke Kannin da Hammadin.
Jagora : Ran hwamar kututturu,
'Y/Amshi : Ran nan anka kakkashikke Kannin da Hammadin,
Jagora : Ran da uwarsu tai jawabi,
'Y/Amshi : Ta ce ma Gobirawa haka kun ka kai ni,
: Ba Kammin babu Hammadin,
: Jikan Jari ginshiqi,
: Dibirtau uban zagi xan Mamman na Baciri.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{50}$ $^{1}/_{1}$)

4.8.2 Karin Magana

Kasancewar waqa aba ce wadda ta shafi hikima, ba za a yi mamaki idan an ji mawaqi ya yi amfani da hikimar karin magana a cikin waqa ba.

Karin magana wata “dunqulalliyar magana ce ta hikima xauke da ma’ana mai yawa wato dai, xabi’a ce da Hausawa ke voye manufa a cikin zance” (Abba & Zulyadaini, 2000:140).

Makaxa Maidaji Sabon Birni kan yi amfani da karin magana a waqoqinsa. A waqar Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Umaru xan Salihu (1957-1966) Makaxa Maidaji ya ya yi amfani da karin magana kamar haka:

Jagora : Na ga sabkon bubuquwa ta tsaya wanka,
'Y/Amshi : Ga mu mun tashi da swahe ham mun wuccikke ta,
Jagora : Ummaru na yi kwararenka an ce kana hwake,
'Y/Amshi : Munka zo mun ishe Sanda jikan Kilo ya hau,
: Sai mu zarce xan Inna an ce yana Kalgo,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{147}$ $^{1}/_{4}$)

A waqar Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Ibrahim (1970-1975) Makaxa Maidaji ya yi amfani da karin maganar da Hausawa ke cewa ‘haquri maganin zaman duniya’ ta wannan siga:

Jagora : Da arziki da wadata,
'Y/Amshi : Ai zaman duniya sai an sa hanquri,
: Da shiri yat tasa,
: Iro xan Shamaki sai na zaka in ganai.

(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{144}$ $^{1}/_{6}$)

Har wa yau, Makaxa Maidaji ya yi amfani da karin magana a waqar Alhaji Salau xan Musa a wani xa da yake cewa:

Jagora : Sa'ad da munka tashi Sabon Birni,
'Y/Amshi : Ba mu da ukku xin tsohonai,
: In bayan sarautar Allah,
: Babu abun da yaz zama kullum,
: Ya wuce tantama,
: Shi Alhaji Shu'aibu zamani nai ya kai.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{143}$ $^{1}/_{2}$)

Wata waqa wadda Makaxa Maidaji ya yi amfani da karin magana ita ce waqar Sarkin Madawa Alhaji Muhammadu inda ya ce:

Jagora : Wanga gidan tawaye ne,
'Y/Amshi : Gidan Jibo sarki yag gado,
: Hwaxa masu ba mai shiga gidan,
: Sai in bayan kai,
Jagora : Ashe sabilin kaza,
'Y/Amshi : Qadangare yag ga ruwan kasko,
: Ashe ko na san,
Jagora : Qadangare ya sha daxinai,
: Za ni in kwan huxu Madawa.
'Y/Amshi : Na zaka barka da arzukka,
: Sarkin Madawa Muhammadu,
: Ko yanzu duniya ta yo mai haske.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{376}$ $^{1}/_{7}$)

4.8.3 Savi-zarce

Savi-zarce dabara ce da ake gano "zaren mawaqi yayin da yakan faro batu daga wani xa, wanda ma'anar ba za ta cika ba sai an

jingina ta da xan da ke tafe" (Abba & Zulyadaini, 2000:108). Muhammad (1978:79-90) ya bayyana cewa a rubutacciyar waqa wadda ya kira da waqa I, akan sami gangara ne, amma a waqar baka wadda ya kira da waqa II akan sami savi-zarce ne. Shi kuwa Xangambo (2007:53) yana ganin savi-zarce shi ma dai "gangara ne a cikin waqa amma wadda take da zurfi".

Dangane da haka, wannan bincike ya tabbatar da waqoqin Makaxa Maidaji suna da sifofin savi-zarce a cikinsu. Misali a waqar Innar Gobir, Makaxa Maidaji ya kawo waxannan xiya ta amfani da savi-zarce kamar haka:

Jagora : Alhaji na yi anniya in zo gai da Inna,
'Y/Amshi : To, amma hwa ban zuwa sai na hwara xinki.

Jagora : To, Inna kya gane ni riga ta 'yar guda ta,
'Y/Amshi : Ita an nan cikin gida ita an nan ga daji.

Jagora : Mai riga guda ina addini gare shi,
'Y/Amshi : Ko ya so zuwa masallaci sai ya hwasa,
: Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{375}$ $^{1}/_{3}$)

Can kuma a cikin wannan waqa ya zayyana wasu xiya kamar haka:

Jagora : Abin da ag ga amarya shi taka kai ma ango,
'Y/Amshi : Abin da ag gare ni yau shi zan kai ma Inna.

Jagora : Kya san ban da raguna in ta zo mu yanka,

'Y/Amshi : Babu abin da ag garan sai turu da waqa,
: Kina da martabar Jangwarzo da Yunhwa,
: Giwa ta Bawa tausa gaba inda kis sa.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{375}$ $^{1}/_{3}$)

Sannan a wata waqa wadda Makaxa Maidaji ya rera wa Malam Hassan Xansanda ya kawo wasu xiya bisa sigar savi-zarce inda yake cewa:

Jagora : Ka gani ba kukan uba nai ma Allah ba,
'Y/ Amshi : Ni ba kukan uwa nai ma Allah ba.

Jagora : Don mutuwa ba ni tsoran ta sha raina,
: Kwancin qabari shi xai ka ban tsoro,
: Ka na kwance cikin duhu ba ka motsawa,
: In ka yi gabas bango ya tarbe ka,
: In ka yi yamma bango ya tarbe ka,
: Ba ka tashi tsaye sai itace shi kwabre ka,
: Kuma kana so ka ga naka ba a ba ka hanya ba,
'Y/ Amshi : Allah ka yo mana halin zuwa mui zaman kewa,
: Qi garaje uban Meli bai xauki wargi ba,
: Dole in yaba Malam Hassan mai halin girma.
(Maidaji : Fasahar Baka, 2004)

A waqar Alhaji Ali Marafa, Makaxa Maidaji ya yi qoqarin fito da manufarsa cikin sigar savi-zarce kamar haka:

Jagora : Kura ba ta gasa da xan Zaki,
'Y/Amshi : Azamarsu ba ta zama xai ba.

Jagora : Don azamar su wane 'yar gajera ta,
'Y/Amshi : Har yanzu ba ta yi tsawo ba,
: Malam Alo na baraz zaki,
: Jikan Kilo xan Marafa.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{0}/_{53}$ $^{1}/_{4}$)

Idan aka qara waiwayo waqar nan ta Sarkin Maraxi Xangara, Alhaji Bala xan Sani, Makaxa Maidaji ya yi amfani da savi-zarce wajen fito da manufar saqonsa da yake bukatar ya sanar wa mai sauraro ta hanyar kwarzanta wanda ya yi wa waqar kamar haka:

Jagora : Jikan Musa,
'Y/Amshi : Jikan saraki,
: Kun zama qusoshin duniya.

Jagora : In an bixi qusoshin duniya,
'Y/Amshi : Ina wani bayan kai Xangara?
: Xangara jikan xan lahiya,
: Bala xan Sani gaisai mukai.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{144}$ $^{1}/_{6}$)

4.8.4 Karin Harshen Waqa

A harshen Hausa akwai kare-karen harshe da suka haxa da "Sakkwatanci da Kananci da Zazzaganci da Dauranci da Gudduranci da Haxejiyanci da sauransu" (Abba & Zulyadaini, 2000:157). Gusau (2003) yana cewa:

> Amfani da karin harshe a waqa ya danganta da nahiyar da mawaqi ya fito, amma duk da haka karin harshen Sakkwatanci, shi ne fitaccen karin harshen waqar Hausa. Ta yiwu saboda Sakkwatanci na da ishasshiyar balaga da rumbun kalmomi masu vuvvuga da sauqin sarrafawa a karin waqa shi ya sa mawaqi na kowane nahiya yana

tsarma karin harshen Sakkwatanci yayin rera waqa ko ta baka ko rubutacciya (Gusau, 2003:64).

Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni yana gina xiyan waqoqinsa ne cikin harshen Sakkwatanci. Sakkwatanci karin harshe wanda mutanen yamma suke amfani da shi waxanda suka haxa da Zamfara da Kabi da Gobir. Kaxan daga cikin wuraren da Makaxa Maidaji Sabon Birni ya yi amfani da kalmomin dake buqatar qarin haske a cikin waqoqinsa sun haxa da:

1. Jagora : Shi wanda ax xauke ga hanya,
'Y/Amshi : Ba ya zuwa <u>sarma ga daji</u>.

Jagora : Ga Xangara ga Alhaji Mamman,
'Y/Amshi : Yau ana shirin <u>shavirigana</u>.
(Makaxa Maidaji : Waqar *Madogara Alhaji Mamman*)

Karin Harshe	**Daidaitacciyar Hausa**
sarma ga daji	yawon banza
shavirigana	shagali ko bidiri

2. Jagora : Ai ga ni na zaka Zazzau mu gaida sarki,
'Y/Amshi : Banga Habiba ba kuma banga Mariya ba,
: Ai ko su Binta ba su da halin su <u>daqile</u> ni.
(Makaxa Maidaji : Waqar *Kak ka yarda da reni*)

Karin Harshe	**Daidaitacciyar Hausa**
daqile	qwauro ko rowa

3. Jagora : Kakanka ya ci ganiyya,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana.
Jagora : Ya ci birnin 'Yandoto,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana.
Jagora : Ya ci birnin Bardava,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana.
Jagora : Ya ci birnin Anganba,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana.
(Makaxa Maidaji : Waqar *Kak ka yarda da reni*)

Karin Harshe	**Daidaitacciyar Hausa**
ganiyya	nasara ko galaba

4. Jagora : Alhaji Sabon Shibkau,
'Y/Amshi : Mijin Laddi manyan danqumai.
Jagora : Ashe zuma kake,
'Y/Amshi : Banga mai lashe dauxar hannuwa.
Jagora : In ko ka qiya,
'Y/Amshi : Magabci ya hi ka datsi a saurara maka.
(Makaxa Maidaji : Waqar *Hali nai girma*)

Karin Harshe	**Daidaitacciyar Hausa**
magabci	magauci ko maqiyi

5. Jagora : Alhaji Audu na Alhaji Dawai,
'Y/Amshi : Goga mai yi ma shanu hanya,
: Ya gade gidan gardaye,
: Saraki uban xan Malam.
(Makaxa Maidaji : Waqar *Ya gade gidan gardaye*)

Karin Harshe	**Daidaitacciyar Hausa**
goga	raqumi

6. Jagora : Uban Bunu uban baraz zaki,
'Y/Amshi : Kai qwazo ka gade Sarkin Gobir Shawai.
(Makaxa Maidaji : Waqar *Kak ka xau reni*)

Karin Harshe	**Daidaitacciyar Hausa**
bunu	babban xan sarki wanda ake sa ran ya zama sarki

7. Jagora : Tun dab bisa Azbin,
'Y/Amshi : Hab bisa Kano,
: Uban kowa ya san Xangara.
Jagora : Da Tawa da Tasawa,
'Y/Amshi : Had Damagaran,
: Kowa ya san Xangara.
(Makaxa Maidaji : Waqar *Xangara jikan xan lahiya*)

Karin Harshe	**Daidaitacciyar Hausa**
azbin	qasar Azbinawa a Nijar

8. J agora : Na ga ana son vacin tambari,
'Y/Amshi : Ana shakkag ganga,
: Maza suna son su yi wasa da kai,
: Halinka suke tsoro uban qasa.
(Makaxa Maidaji: Waqar *Bawa na Jekadiya*)

Karin Harshe	**Daidaitacciyar Hausa**
vaci	zagi

9. Jagora : To, hwaxa ma makiyaya su sha zuwa dajin Tsintau,
'Y/Amshi : In Tsintau ya ishe su ba ni zuwa ceto.
(Makaxa Maidaji : Waqar *Sarkin Gandu*)

Karin Harshe	**Daidaitacciyar Hausa**
daji	jeji

10. Jagora : Su wane sun dubun tanbaxa,
: Dubun da an yi kamar ba a yi ba,

: Dubun da babu hura ba tuwo.
(Makaxa Maidaji : Waqar *Sarkin Gandu*)

Karin Harshe	**Daidaitacciyar Hausa**
tambaxa	shiririta ko lalaci

Sauran ire-iren waxannan kalmomin karin harshe da Makaxa Maidaji Sabon Birni ya yi amfani da su a cikin waqoqinsa sun haxa da:

‘yan qirya	zuri’a ce a masarautar Tara
darzaje	a koro abu gaba xaya
darzaza	bin abu daki-daki ko kuma qut-da-qut
gagarau	buwayayye ko gangaran
gahwara	gafara
gamda’are	gwarzo
garka	qofar gida
geme	gemu
gogarma	sarki
gulbi	kogi
hawa’i	tavavve
hwan talatin	fam talatin
hwaru	fara
jikka dubu	dubu xari biyu

	ko zaure
lirwai	bin diddigi ko lissafi
masarta	makaxan gidan Sarki
muxa	yunwa ce daxaxxiya
muzakkari	mabuwayi
niqatau	mai niqe abu ya yi lugui-ligui don laushi
nuhwa	nufi
rabka tamburra	buga tambari
ragga	tsumma
rumhwa	rumfa
tabki	kogi ko fadama
tcibilbila	tsuntsu mai zama a masallaci
tcibiri	garin Gobirawa a qasar Nijar
tohwa	tofa
tozaye	tahiyar ruwa da iska
tsula	qaramin biri
turaye	taushi
wargi	wasa

4.9 Naxewa

Wannan babi ya yi magana ne dangane da adon harshe inda aka kawo hanyoyi waxanda ake bi ta kansu a yi wa waqa ado domin qara

mata armashi ta yadda za ta isar da saqonta cikin jan hankali.Dabarun da aka yi nazarinsu sun haxa da tamka da kwalliya da alamtarwa da jinsintarwa da kinaya da qarangiya. Babin kuma ya tavo vangaren salon sarrafa harshe inda aka yi bayani dangane da qarangiya da karin magana da savi-zarce da kuma karin harshe.

A vangare na biyu na babin kuma an kawo bayanai dangane da tsari a waqar baka. Babin ya tattauna tsari a waqoqin Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni da tsarin xa mai sauqi da kuma xa mai tsauri. Sannan aka yi bayani game da tsarin rerawa wanda ya qunshi qulli da qari da karvi ko amshi da karvevveniya ko rakiya a waqoqin Maidaji sabon Birni. A wannan babi an kawo bayanin Makaxa Maidaji, yana amfani ne da tsarin rerawa na +Jagora + 'Y/Amshi + Qulli + Qari + Tarbe +/- Rakiya/ Karvavveniya + Gindin Waqa + Kixa. An rufe babin ne ta bayyana takidi a tsarin waqoqin Makaxa Maidaji.

BABI NA BIYAR
KAMMALAWA

5.0 Gabatarwa

Wannan kundin bincike ne wanda aka gabatar dangane da ayyukan Makaxa Sa'idu Maidaji Rambaxawa, Sabon Birni kuma aka sanya masa suna "Nazarin Ayyukan Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni (1938-2000)".

An qudurci aniyar gudanar da bincike a kan wannan mashahurin makaxi wanda ya yi fice bisa zalaqarsa da zarra tsakanin takwarorinsa domin a fito da ainihin fasaharsa quru-quru tare da zaqulo yanayin gwanintarsa da hikimominsa da luggoginsa waxanda ya aiwatar yayin rera waqoqinsa. Saboda haka an yi wannan bincike ne da qudurin gano shin wane ne Sa'idu Maidaji Rambaxawa Sabon Birni? Ina ne asalinsa? Yaya kuma ya gudanar da rayuwarsa ta quruciya zuwa tsufa zuwa rasuwa?

- Yaushe ne Makaxa Maidaji ya soma waqa? Ko shi makaxi ne na gado ko na haye? Waxanne irin waqoqi ne Makaxa Maidaji yake rerawa? Su wa da wa ya yi wa waqoqi? Ko za a iya tantance adadin waqoqin da Makaxa Maidaji ya yi? Zuwa yau, waqoqin nawa aka samu na waqoqin Maidaji Sabon Birni?

- Bisa waxanne jigogi ne Makaxa Maidaji ya gina waqoqinsa a kansu? Yaya tsari na waqoqin Maidaji Sabon Birni yake? Waxanne matakai ne yake amfani da su wajen shirya waqoqinsa?

- Waxanne dabaru na adon harshe ne Makaxa Maidaji ya yi amfani da su wajen aiwatarwa da rera waqoqinsa? Yaya yake zaven kalmomi? Yaya yake shirya jimloli da rassansu a waqoqin nasa?

- Yaya dangantakarsa da yaransa take? Wane ne ya gaji Maidaji Sabon Birni bayan rasuwarsa?

- Shin ko Makaxa Maidaji Sabon Birni ya xauki waqar baka ne a matsayin sana'a ko kuma yana aiwatar da ita ne domin raya adabin Hausa?

- Shin mafi akasari, waxanne tasirori ne al'ummar Hausawa suke samu daga waqoqin Makaxa Maidaji Sabon Birni? Mene ne matsayin Makaxa Maidaji ta fuskar kaifin tunani da basira da zalaqa da sauran dabaru na aiwatar da harshe?

5.1 Abubuwan da Bincike ya Gano

Bayan da aka gama wannan nazari an gano abubuwa muhimmai da suka shafi hikimomin shiryawa da rera waqoqi na Makaxa Sa'idu

Maidaji Sabon Birni da inda ya yi wa sauran makaxa zarra kamar haka:

i) Wane ne Makaxa Maidaji

A wannan nazari an tantance tarihin rayuwar Makaxa Maidaji Sabon Birni wanda aka haifa a garin Tara, shekara ta 1938, Qaramar Hukumar Sabon Birni, jihar Sakkwato. Sunansa na yanka Sa'idu, sunan mahaifinsa kuwa Muhammadu Dango (Maigari), sannan sunan mahaifiyarsa Hauwa'u (Jimma). Binciken ya gano Makaxa Maidaji Sabon Birni qani ne ga Makaxa Musa Nadada Sabon Birni. Sannan kuma su shida ne a gidansu dukkansu maza ne.

Wannan bincike ya gano cikin nufar Allah, Makaxa Maidaji Sabon Birni, yana da matan aure guda uku. Waxannan mata, har ya rasu suna nan raye kuma yana tare da su. A waqoqinsa da dama yakan ambaci sunayen waxannan mata nasa musamman a waqoqin Innar Gobir inda yawanci yake nuna godiyarsa bisa abun alheri da ake yi wa iyalan nasa. Sunan matan kuwa su ne:

- Ta-Allah
- Mai Kuxi
- 'Yar Maigoro.

Wannan bincike ya qara gano cewa Allah ya wadata Makaxa Maidaji Sabon Birni da ‘ya’ya guda takwas maza huxu mata huxu waxanda har ya rasu suna raye. Sunayen ‘ya’yan kuwa su ne:

- Adamu Sa’idu Maidaji (Baciri)
- Sabi’u Sa’idu Maidaji
- Abdurrahman Sa’idu Maidaji
- Muhammadu Sa’idu Maidaji (Rani)
- Zulaihatu Sa’idu Maidaji (Zali)
- Salamatu Sa’idu Maidaji (Salmu)
- Hauwa’u Sa’idu Maidaji (Barno)
- Hadiza Sa’idu Maidaji (Taladi)

Binciken ya gano Makaxa Maidaji Sabon Birni ya yi yawon neman ilmin addinin Musulunci, amma bai yi zurfi a ilmin zamani ba, sannan kuma bai yi yawon bara ba. Har wa yau, binciken ya gano Makaxa Maidaji Sabon Birni ya ziyarci jihohin Nijeriya da qasashen waje da dama kafin rasuwarsa. Sannan binciken ya gano Allah ya yi masa rasuwa a shekara ta 2000. Domin haka, Alhaji Sa’idu Maidaji ya sami shekaru sittin da uku (63) a duniya.

ii) Lokacin da Makaxa Maidaji ya Fara Waqa

Binciken ya gano Makaxa Maidaji Sabon Birni tun yana qarami yake da himma da qwazo kan duk abin da ya sa gaba domin ya sami biyan bukata mai amfani. Domin haka, Makaxa Maidaji Sabon Birni yana xan shekara aqalla goma sha biyu (12) ya bar gidansu ya koma gidan yayansa Malam Musa Nadada da zaman barance. Sanadiyyar hakan ne ya riqa bin yayansa Makaxa Musa Nadada suna yawon kixa da waqa a gidajen sarakunan qasar Gobir. Ko da Makaxa Maidaji Sabon Birni ya cika shekara biyar (5) a qarqashin jagorancin yayansa, aka naxa Makaxa Maidaji Sabon Birni matsayin *Daudun Kixa* wato *Galadiman* Makaxa Nadada.

Haka zalika binciken ya tabbatar da fitar Makaxa Maidaji Sabon Birni waqa ta farko, ya tafi shi xaya ne, waqar da ya fara rerawa, ita ce wadda ya yi a lokacin da wani manomi ya yi gayyar noma a qauyensu. Bayan an yi wata gayyar sai ya tafi da wasu yara guda biyu suna yi masa kixa shi kuma yana waqarsa.

Binciken ya tabbatar da kafin Makaxa Maidaji Sabon Birni ya zama makaxin Masarautar Sabon Birni, yayansa Makaxa Musa Nadada ne makaxin garin. Wannan batu yana qara tabbatar da Makaxa Maidaji dai, ya koyi kixa da waqa na sosai ne a wajen

yayansa Malam Musa Nadada. Kuma Makaxa Maidaji, ya fara da kixan kurkutu ne.

iii) Makaxin Gado ko na Haye

Binciken ya gano Makaxa Maidaji Sabon Birni ya yi gadon kixa da waqa ne domin mahaifinsa Muhammad Dango (Mainasara) ya yi gadon kixa da waqa ne a hannun mahaifinsa Xantsara wato kakan Makaxa Maidaji Sabon Birni. Duk da dai mahaifin nasa Mainasara kixan noma kawai ya yi, bai yi wa sarakuna kixa da waqa ba. Wato dai, gidansu sun gaji kixa tun daga kakannin kakanninsu.

Binciken ya qara tabbatar da faxar Hausawa ‘dakan xaka, shiqan xaka, tankaxen bakin gado’, wannan batu bai rasa nasabar cewa yayan Makaxa Maidaji Sabon Birni, Makaxa Musa Nadada ya karvi kixa da waqa daga wurin mahaifinsu Muhammadu Dango (Mainasara) shi ne ya koya wa Makaxa Maidaji kixa da waqa. Makaxa Nadada Sabon Birni ya yi tashen waqa qwarai, mutum ne mai basira da hikima wajen shirya waqoqinsa duk da cewa malami ne shi domin kuwa har ya haddace Al-qur’ani mai tsarki, amma karatun bai hana shi kixa ba. Makaxa Nadada ya shahara ne a kixan noma da kixan fada. Makaxa Maidaji Sabon Birni yana cewa:

Jagora : Ummaru na zagi ya gaji yaqi ga kakanai,
'Y/Amshi : Da shi da kakana babu zangon da ba su kwan ba.
Jagora : Kakanka ya ci Ganiyya,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana.
Jagora : Ya ci birnin ‘Yandoto,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana.
Jagora : Ya ci birnin Bardava,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana.
Jagora : Ya ci birnin Anganba,
'Y/Amshi : Hak ko da kakana.
Jagora : Maza cikin tabki sun ka hwaxa suna voyo,
'Y/Amshi : Duniya na ji dashe-dashenta na Alqali,
: Mu yi zaman Xantsara da jadi da Jari kuma,
: Mu yi zaman Salihu,
: Shi da Xandada mai tabshi,
: Umaru ginshimin Ali ci hwansa,
: Xan baraz zaki uban zagi ba ya son wargi.
(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^{1}/_{147}$ $^{1}/_{4}$)

iv) Adadin Waqoqin Makaxa Maidaji

A wannan nazari an tattaro matanoni na waqoqin Makaxa Maidaji kimanin saba’in da takwas (78) waxanda aka yi misalai da su a aikin. Saboda haka, bisa qiyasi, a iya cewa aqalla Makaxa Maidaji yana da adadin waqoqi guda saba’in da takwas waxanda suka shigo hannu.

v) Nau’in Waqoqin Makaxa Maidaji

Wannan nazari ya qwanqwance zalaqar Makaxa Maidaji Sabon Birni game da nau'o'i na waqoqinsa waxanda suka haxa da waqoqin fada da waqoqin noma da waqoqin jama'a da kuma waqoqin siyasa.

vi) Jigogin Waqoqin Makaxa Maidaji

Nazarin ya lura da Makaxa Maidaji ya gina waqoqinsa ne bisa jigogi mabambanta. Amma ya fi yawaita gina waqoqi na jigon yabo. Daga cikin waqoqin da nazarin ya tattaro, kashi saba'in bisa xari ($^{70}/_{100}$) waqoqi ne na yabo. Jigogi na zuga da faxakarwa da siyasa su ne suka qunshi sauran kashi talatin bisa xari ($^{30}/_{100}$). Har wa yau kuma Makaxa Maidaji Sabon Birni ya yi amfani da wasu tubalai na gina jigo da suka haxa da ambaton addini da ta'aziyya da habaici da koxa kai da sauransu.

Sannan binciken ya gano hanyoyin da Makaxa Maidaji yake bi ta kansu ya gina saqonni, manya da qanana a waqoqinsa tare da rarrabe manyan jigogi na matanonin waqoqi nasa.

vii) Tsarin Waqoqin Makaxa Maidaji

A nazarin kuma an gano Makaxa Maidaji ya yi amfani da tsari na xiya masu sauqi da kuma tsari na xiya masu tsauri a layuka na

xiyan waqoqinsa. Ashe ke nan, tsarin xiya na Makaxa Maidaji, tsari ne mai harshen damo. An kawo misalai a wurare daban-daban kamar haka:

Ga misalin tsarin xa mai sauqi a waqar Arzika ta noma *'Sarki yai abin daka ya huta'* inda yake cewa:

Ma'ana	*Qirgar Ma'ana*	
Hawa	A^1	: Baba mijin Shibo mijin Maryama,
Sauka	A^2	: Giwa maganin itacen daji,
	X^1	: Sarki yai abin daka ya huta,
	X^2	: Zaki xan Abubakar xan Buda.

(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^1/_{147}$ $^1/_2$)

misalin xa mai tsauri a waqar *'Malam Alo na baraz zaki'* ta Alhaji Ali Marafa inda Makaxa Maidaji yake cewa:

Ma'ana	*Qirgar Ma'ana*	
Hawa	A^1	: Kura ba ta gasa da xan zaki,
Ajewa	A^2	: Azamarsu ba ta zama xai ba,
Sauka	A^3	: Don azamar su wane 'yar gajera ta,
Saukar Sauka	A^4	: Har yanzu ba ta yi tsawo ba,
Hawa	B^1	: Ko can da shirin hwaxa Ali yat tasa,
Hauhawa	B^2	: Tun da ba a shira mai wuqa ba,
Sauka	B^3	: Yanzu akwai wuqa akwai mashi,
Saukar Sauka	B^4	: Don an shirya mai makami,
Hawa	C^1	: Ko can dokin qwarai shi ka kama gudu,
Hauhawa	C^2	: Shi daxe shina hamidanci,
Sauka	C^3	: Shi kuma dokin su wane sai bixar tsaba,
Saukar Sauka	C^4	: Tun ba a gwada mai ruwa ba,
	X^1	: Malam Alo na baraz zaki,
	X^2	: Jikan Kilo xan Marafa.

(Maidaji : O.D.U Catalogue, 1985.Tape No. AL $^0/_{53}$ $^1/_4$)

Binciken ya qididdige yanayin tsari a waqoqin Makaxa Maidaji, musamman yadda yake qullawa da qari a layuka da xiya na waqoqinsa. Daga nan kuma aka tantance tsarin rerawa da tsarin xa da takidi da sauransu. An nuna shi makaxi ne wanda yake rera waqoqinsa tare da yara masu yi masa amshi da tarbe da kuma rakiya.

viii) Salon Waqoqin Makaxa Maidaji

A wannan nazari an fahimci salon da Makaxa Maidaji Sabon Birni ya yi amfani da shi a cikin waqoqinsa salo ne mai jan hankali, salo ne mai karsashi, salo ne wanda yake ingiza mai sauraro ci gaba dakon saukar saqo yayin rera waqoqinsa. Wato, makaxi ne wanda ya iya sarrafa harshe da amfani da murya mai zaqi wajen zavo kalmominsa masu kaifin ma'ana waxanda suke dacewa da saqonninsa a zubin waqa.

Sai kuma aka duba hanyoyin salo da sarrafa harshe waxanda Makaxa Maidaji ya yi amfani da su a matanoni na waqoqinsa. An bayyana Makaxa Maidaji ya tasirantu a waqoqinsa wajen zuba hanyoyi na sarrafa harshe kamar qarangiya da savi-zarce da kuma

kyautata yin zave na kalmomin fannu. Kuma an bayyana makaxi ne wanda yake amfani da yanayin karin harshe na Sakkwatanci.

Makaxi ne wanda yake tafiyar da karin muryarsa a waqa cikin kwanciyar hankali, ba tare da garaje ba kuma babu sassarfa. Wannan ne ya janyo al'umma ke sha'awar waqoqinsa tare da xokin zaqin muryarsa, sannan ga dacewa ta fuskar amo na taushi wanda ko malam ya ji ba zai ce ba daxi ba, sai dai ya ce ba kyau.

Binciken ya rarrabe matakai waxanda Makaxa Maidaji Sabon Birni yake sassarqa tunaninsa da dabaru na yi wa harshe kwalliya da kuma zaven kalmomi da aiwatar da jimloli. Makaxa Maidaji Sabon Birni kan keve wasu kalmomi na fannu waxanda yakan jejjefa su a cikin mabambantan waqoqinsa.

Har wa yau, nazarin ya gano a waqoqin Makaxa Maidaji akwai dabarun yi wa harshe kwalliya da aka yi amfani da su da yawa, tun ma ba ita kanta dabarar kwalliya da tamka da alamci da jinsintarwa da qarangiya da karin magana da savi-zarce da kuma kinaya ba.

ix) Zalaqar Harshen Makaxa Maidaji

Makaxa Maidaji Sabon Birni, makaxi ne wanda bai koma ga mahaliccinsa ba sai da ya yi fice a tsakanin al'ummar Hausawa da ma

al’ummu na qetare. Tun yana raye aka riqa sanya faya-fayan waqoqinsa a kusan dukkan gidajen radiyon da ake amfani da harshen Hausa. Hatta gwamnatin jihar Sakkwato da hukumomin gwamnatin jihar da hukumomi masu zaman kansu sun yi ta cin moriyar baiwar da Allah ya yi wa Makaxa Maidaji Sabon Birni wajen isar da saqonni ko tallata hajarsu.

Duk hakan ya faru ne sanadiyyar Makaxa Maidaji Sabon Birni yana rera waqoqi ne masu burge jama’a wanda hakan ya haifar masa da tagomashin karvuwar waqoqinsa a tsakanin al’umma baki xaya. An gayyace shi taruka da dama inda akan ba Makaxa Maidaji fage ya bajekolinsa wajen qara ma al’umma haske dangane da manhaja da manufar wannan taro.

Domin haka, Makaxa Sa’idu Maidaji Sabon Birni, makaxi ne wanda ya qara wa rumbun adabin Hausa yawa kuma ya adana tarihi tun ma ba na manyan masarautun qasashen Hausa ba.

x) Dabarar Isar da Buqata

xi) Dabarar Yaba Kyauta

Makaxa Maidaji Sabon Birni yana amfani da xabi'un yaba kyauta a cikin waqoqinsa

xii) Dabarar Fito da Tarihi

Makaxa Maidaji Sabon Birni yana amfani da dabarun sarrafa tarihi a cikin waqoqinsa da xabi'u na mutanen da yake yi wa waqoqi da sauran matakan rayuwa daban-daban waxanda yakan kyallaro a cikin waqoqinsa. Mutum ne wanda ya kalli mafi akasarin shikashikan rayuwar Hausawa, tun ma ba yanayin zamantakewar Hausawa ba.

xiii) Tasirin Addini

Binciken ya gano waqoqin Makaxa Maidaji Sabon birni sun tasirantu da addini qwarai da gaske. Har wa yau kuma an yi maganar waqoqinsa wajen amfani da ilmin addinin Musulunci da yadda Musuluncin yake kallon zamani tare kuma yadda yake cusa rayuwar da take dabaibaiye da shi a cikin tsari na waqoqinsa.

xiv) Matsayin Zambo a Wurin Makaxa Maidaji

Akwai wata lura kuma da aka yi a nazarin nan, Makaxa Maidaji Sabon Birni ba ya son yin zambo a zubin waqoqinsa kamar yadda wasu ‘yan’uwansa manyan makaxa suke yi.

A hirar da Makaxa Maidaji suka yi da Malam B.S.Y. Alhassan tare da Malam A. V. King a shekarar 1982 a gidansa da ke garin Rambaxawa ya habarta cewa bai cika yin zambo a waqoqi ba saboda abu ne da ya tabbatar ya sava qa’ida ta addini.

Amma, ya yi zambo na mayar da martani ga wasu waxanda suka addabi ubangidansa na wannan lokaci. Ga dai abin da ya ce a wannan hira:

B. S. Y. Alhassan: To, kamar xazu mun tavo maganar da kay yi cewa ga dalilan da ke sa a yi wa mutum zambo. Ko akwai waqarka wadda kay yi zambo daga hwarko har qarshe zambo na zalla kay yi?

Makaxa Maidaji: Ai babu.

B. S. Y. Alhassan: Ni ban ga kana son yi ma mutane zambo da yawa ba. Kuma na ga mutane suna sha’awar zambo ga waqa. Sai dai, in kay yanka kuma vatacce kake yi?

Makaxa Maidaji: Eh! Muna ji suna ta yi.

B. S. Y. Alhassan: Kuma na ga ko da maganar mawaqa za ka yi sai dai ka yi maganar alheri. Wato, kai ba ka yin zambo sai ta kama dole ke nan?

Makaxa Maidaji: Eh! To, sai bana mun ka xan yi wani xan kaxan. Saboda wani na yake wa sarki shegantaka.

Duk da a wasu lokutan kalmomin zambon sukan yi masa tutsutsu da banga-banga a zuciya. Dubi waqarsa ta Sarkin Gobir na Sabon Birni, Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003) ta *'Kai ab bahagon gulbi'* a ga abin da yake cewa da kansa a waqar:

Jagora : Ga ni ina son harkar zambo,
'Y/Amshi : Amma na zama mai geme,
: Kowa yaz zama mai geme,
: Ba dama shi yi shexanci.

Jagora : Cikin masu biyas sarki,
'Y/Amshi : Wasu sun hwara munahicci,
: Bari kowa ka munahicci,
: Hwaxa mai da akwai Allah,
: Kai ab bahagon gulbi,
: Uban Shantali xan Mamman,
: Xan'inna Kilo sarki,
: Uban Bunu da Baraz Zaki.

Idan an qara waiwayar waqarsa ta Sarkin Gobir na Sabon Birni, *Alhaji Ummaru xan Salihu (1957-1966),* ta *'Gagari gaba na Salihu'* Makaxa Maidaji ya qara fito da qudurinsa na qoqarin kawar da zambo

a cikin waqoqinsa duk da karakainar da zuciyarsa ta kan shiga. Ga abin da yake cewa:

Jagora : Ga ni ina son vacin tscibilbila,
'Y/Amshi : Zaman zauri xai nika gudu,
: In zauri ya buwaya yanzu,
: Ko ga itace zama ta kai.

Jagora : To, na so in vaci hakimin sarki,
'Y/Amshi : Rowan nan da yat tcira,
: Baqar rowan nan da yat tcira,
: Da hwari shi ka sa mu tsira xumumuwa,
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

Jagora : To, na yi karatu da ilimi,
'Y/Amshi : Har na sabka na yi shinhixa,
: Xiyana sun kama Sabbi,
: Yanzu diba takardu kaxai mukai,
: Gagari gaba na Salihu,
: Mai nasara xan Durumbu,
: Xan Hayatu Magajin gidan Kada.

xv) Dangantakar Makaxa Maidaji da ‘Yan Qungiyarsa

Har ila yau, wannan bincike ya gano akasarin yaran qungiyar Makaxa Maidaji jininsa ne, tun da dama gidansu tun asali, gidan waqa ne Makaxa Maidaji mutum ne mai kyakkyawar alaqa da yaran qungiyarsa, sun zauna, zama na ‘tsintsiya maxaurinki xaya’. Yana

zama tare da su cikin koyi na tarbiyya da girmamawa a tsakaninsu, duk da idan ka gan su yadda ka san abokai. Idan ba gaya wa mutum aka yi ba, ko kuma in ba ya sani ba, ba za a ce yaransa ne ba. Ko da yaushe, suna zaune wuri guda, abin dai gwanin ban sha'awa, duk da cewa wasu daga cikin yaran nasa yayyensa ne. Babu gardama a tsakaninsu. Wannan ya sa Makaxa Hana yake cewa shi kam yana da yaqinin cewa an haifi Makaxa Maidaji da waqa ne domin ya yi ta.

Makaxa Maidaji ya bayyana alaqarsa da 'yan qungiyarsa a hirarsa da Dr. Alhassan, B. S. Y. kamar haka:

B.S.Y. Alhassan: Na ji in kana waqa kana cewa 'ya'yana. Duka masu yi maka amshi xiyanka ne?

Makaxa Maidaji: Eh! Duka xiyana ne sai wannan babban wanmu ne, sai wannan tsohonmu dukkansu suna amshi. Shi wannan tsohon namu ko da nih hwara kixi tare da shi nih hwara. Waxanda nihwara da su kuma mutum biyu ko babu su. Biyu daga qannena sun kama makaranta.

B.S.Y. Alhassan: Yanzu wannan sana'a ko cikin masu yi maka amshi yanzu akwai wani wanda yake sha'awar ya karva gare ka da ganinka lokacin da kake ganin ya kamata ka huta. Kuma ya sunan shi?

Makaxa Maidaji: Eh! Akwai domin shi kan shi ya hwara nashi waqoqi. Sunan shi Hana.

Makaxa Maidaji yana cikin makaxa waxanda suke aiwatar da waqoqi a cikin qungiya wadda ta haxa da jagora da ‘yan amshi da kixa da sauran yara masu xaukar kayan kixa. Daga cikinsu akwai:

m) Alhaji Ibrahim (Tanko); qanen mahaifinsa ne; baransa ne kuma maroqinsa

n) Alhaji Maigari; yayansa ne

o) Alhaji Ibrahim Musa (Hana); babban xan Makaxa Nadada

p) Alhaji Adamu (Baciri); babban xan Makaxa Saidu Maidaji

q) Alhaji Adamu (Abara);

r) Alhaji Adamu (Xan Malam)

s) Alhaji Usman (Salau);

t) Alhaji Garba (Na-Maiqosai);

u) Alhaji Garba (Abbu)

v) Alhaji Ummaru (Dogo);

w) Alhaji Abdullahi (Xan Barno);

x) Alhaji Shu’aibu

xvi) Dangantakar Makaxa Maidaji da Sauran Makaxa

A nazarin an tabbatar da Alhaji Sa'idu Maidaji Sabon Birni, makaxi ne wanda ya zauna lafiya tare da 'yan'uwansa makaxa, manyansu da qananansu. Kuma shi ba makaxi ba ne wanda yake son takara ta yin waqa ba. Ba ya son jayayya da kowane irin makaxi. Domin haka, ba a sami wasu waqoqi da ya yi ko aka yi masa na waqeqeniya ba. Mutum ne kuma mai yawan zumunci, wanda ba ruwansa da hassada ko ganin qyashi.

xvii) Tasirin Waqoqin Makaxa Maidaji ga Sauran Al'umma

Wannan bincike ya gano Makaxa Maidaji Sabon Birni, makaxi ne wanda al'ummu na cikin gida da na wajen masarautarsa ta Sabon Birnin Gobir sun raja'a da nason waqoqinsa. Sukan gayyace shi a lokuta mabambata domin ya rera musu waqa a lokacin hidima. Kuma yakan yi waxannan tafiye-tafiye ne bisa umurnin ubangidansa Sarkin Gobir na Sabon Birni.

Masarautar Zazzau ta zame ma Makaxa Maidaji wurin da yakan baje kolinsa a dawa. Kamar yadda Makaxa Ibrahim Musa Hana wanda shi ne magajin Makaxa Maidaji a yanzu ya tabbatar ma

wannan bincike da cewa a lokacin da Maidaji Sabon Birni yake raye sukan sami gayyata daga fadar Zazzau sosai. Kuma ba yadda za a yi Makaxa Maidaji ya halarci taro ya zama Sarki da kansa bai fito ya saurari Makaxa Maidaji ba. In ma sarki ya lura da cewa lokaci zai qure masa bai ji gwaninsa ba, yakan dakatar da kowane makaxi ya umurci Makaxa Maidaji da hawa fage.

Haka abin yake a masarautar Buza ta qasar Nijar da Madawa da Maraxi da sauransu da dama. Ke nan, yawanci waqoqin da Makaxa Maidaji ya rera wa mutanensa bisa kyakkyawar alaqa ce tsakaninsu ya rera waxannan waqoqi.

Binciken ya gano baya ga waqoqin fada, Makaxa Maidaji Sabon Birni ya rera wa xaixaikun mutane waqoqi. ‘Yankasuwa ne ko jami’an gwamnati ne ko malami ne ko kuma alqalai ne duk dai ya waqe makamantansu.

Binciken ya gano Makaxa Maidaji Sabon Birni ya rera waqoqi na siyasa, na jam’iyyu da na xaixaikun mutane ‘yan siyasa. Kusan, wannan bincike ya tabbatar da Makaxa Maidaji a jam’iyyance yana goyon bayan jam’iyyar nan ta N. P. N. ne.

Binciken ya gano hatta da matsaloli irin na fari da yunwa da tavarvarewar tattalin arziki da kuma yanayin zumunta da martabar

mata da sauransu duk ya dube su a cikin waqoqinsa. Ta wannan ne, ya aiwatar da jigogi daban-daban a waqoqinsa waxanda suka dubi dangogin rayuwa mabambanta.

Haka kuma nazarin ya fahimci waqoqin Makaxa Maidaji suna a matsayin makaranta wadda take koya wa al'umma hanyoyin zamantakewar rayuwa kyawawa. Sannan waqoqi ne waxanda suke yin tunasarwa da wayarwa, kuma addinin Musulunci ya yi matuqar tasiri a cikin waqoqin, musamman nuna yadda za a yi zaman duniya ta yadda za a sami rayuwar lahira managarciya. Ta haka ne waqoqin suke yin nuni game da qiyama da mutuwa da kwanciyar qabari da hisabi da gudun famfalaqi da sauransu.

xviii) Matsayin Kixa da Waqa a Wajen Makaxa Maidaji

Wannan bincike na qarfafa Alhaji Sa'idu Maidaji, makaxi ne wanda ke gudanar da kixansa domin sha'awa bai xauke shi a matsayin sana'a ba. Yana amfani da abin kixa na taushi ne ko turu kamar yadda suke kiran abin kixan na su tare da yara masu yi masa amshi da kaxa turayen taushi. Nazarin ya fahimci Makaxa Maidaji ba ya yin waqa

tare da xanma'abba. Binciken ya tabbatar da Makaxa Maidaji Sabon Birni manomi ne.

xix) Iyayen Gidan Makaxa Maidaji

Wannan bincike ya gano cewa iyayen gidansa a masarautar Gobir guda uku ne. Ya bayyana hakan a hirarsa da Malam Alhassan a shekarar 11/2/1981 kamar haka:

B. S. Y. Alhassan: To kai kuma makaxin wane ne?

Makaxa Maidaji: To ni na fara tun daga Sarkin Gobir Ummaru xan Sarki Salihu. Tak kai ga Sarkin Gobir Ibrahim qanin Sarki Salihu. Hat tak kai ga Sarkin Gobir Muhammad qanen Sarki Salihu.

Da haka za a iya kafa hujja da cewa iyayen gidan Makaxa Sa'idu Maidaji a masarautar Gobir ta Sabon Birni su ne:

- Sarkin Gobir Ummaru 1957 – 1966
- Sarkin Gobir Ibrahim 1970 – 1975
- Sarkin Gobir Muhammadu 1975 – 2003

Har wa yau kuma, wannan bincike ya gano wasu masarautu da ke karrama waqoqin Makaxa Maidaji da gayyatarsa daga lokaci zuwa lokaci da sanin ubangidansa sun haxa da:

- Masarautar Sarkin Zazzau,

Alhaji Shehu Idris

- Masarautar Sarkin Katsinan Gusau,
  Alhaji Muhammad Kabir Xanbaba

- Masarautar Sarkin Bazai na Jangeru,
  Alhaji Muhammadu Jangeru

- Masarautar Sarkin Maraxi,
  Alhaji Muhammadu Xangara

- Masarautar Sarkin Buza,
  Alhaji Muhammadu Abdullahi

xx) Waxanda Makaxa Maidaji ya yi wa Waqa

Binciken ya gano Makaxa Maidaji Sabon Birni makaxi ne wanda yake da farin jini a filin waqa, domin kuwa Allah ya xaukaka shi daga cikin makaxa da mawaqan baka na Hausa da ake da su. Shaharar Makaxa Maidaji Sabon Birni da zalaqar muryarsa ya sa mutane da dama suna qaunar waqoqinsa. Wannan ya haifar da manyan mutane da dama sukan gayyace shi domin ya je ya rera musu waqa. Daga cikin mutanen da ya yi wa waqa sun haxa da:

1. Sarkin Gobir na Sabon Birni,
   Alhaji Balarabe xan Muhammadu Natawwa (1902-1904)

2. Sarkin Gobir na Sabon Birni,
   Alhaji Muhammadu Jadi (1915-1916)

3. Sarkin Gobir na Sabon Birni,

Alhaji Ummaru Shawai (1916-1945)

4. Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Salihu (1945-1956)

5. Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Umar Na Allah (1957-1966)

6. Sarkin Gobir na Sabon Birni,
Alhaji Ibrahim xan Ummaru Shawai (1970-1975)

7. Sarkin Gobir Sabon Birni,
Alhaji Muhammadu Bawa (1975-2003)

8. Sarkin Buza ta Qasar Nijar, Alhaji Abdussalam

9. Sarkin Katsinan Gusau,
Alhaji Muhammad Kabir Xanbaba (1984-)

10. Sarkin Zazzau,
Alhaji Shehu Idris (1975-)

11. Tsohon Shugaban Qasar Nijeriya,
Alhaji Aliyu Shehu Shagari (1979-1983)

12. Tsohon Gwamnan Jihar Sakkwato,
Alhaji Garba Nadama (1981-1983)

13. Innar Gobir ta Sabon Birni
Hajiya Bahillata

14. Innar Gobir ta Sabon Birni
Hajiya Ta-Allah

15. Innar Gobir ta Sabon Birni
Hajiya Dela Atumbula

16. Sarkin Tara,
Alhaji Abdullahi Saraki Tara

17. Marafan Sabon Birni
Alhaji Ali Ibrahim Musa Dodo Xanmarafa

18. Sarkin Bazai na Jangeru,
Alhaji Muhammadu Jangeru

19. Xan Sarkin Hillani,
Alhaji Muhammadu Dikko Xanmaliki Lamixo

20. Sarkin Madawa,
Alhaji Muhammadu Baqo

21. Sarkin Gabas na Gwaranyo,
Alhaji Ummaru Sambo

22. Sarkin Maraxi,
Alhaji Bala Xansani Xangara

23. Sarkin Tsibirin Gabas,
Alhaji Ali Agada

24. Xangaran Sabon Birni,
Alhaji Ibrahim Makoxa Xangara

25. Alqalin Sabon Birni, Alhaji Malam Ahmad

26. Garkuwan Dutsi,
Hakimin Sabon Birni Alhaji Sulaiman

27. Malamin Masarautar Tara
Malam Hassan Xansanda

28. Uban Dawaki, Alhaji Bala

29. Magajin Gari,

Alhaji Magaji Tangaxi Tsibiri

30. Sarkin Tashar Motar Sabon Birni,
Alhaji Idi xan Argiji xan Fulanin Vaure

31. Sarkin Gandu, Alhaji Suntau

32. Alhaji Sani na Ummu

33. Alhaji Muhammadu Xanqoqari

34. Alhaji Mamman Xanqarbu

35. Alhaji Xanbawa

36. Alhaji Isyaka Abarshi

37. Alhaji Idi Falalen Karo

38. Alhaji Xansanda Gangara

39. Alhaji Abdulmumini Arzika

40. Alhaji Hashimu D. P. O. na Gusau

41. Alhaji Shu'aibu Salau xan Musa

42. Alhaji Ali 'Yankuzo

43. Alhaji Mamman Kubau

44. Alhaji Mamman xan Abubakar Malumfashi

45. Alhaji Shu'aibu Kunda

5.2 Wanda ya Gadi Makaxa Maidaji

Alhaji Ibrahim Musa Nadada (Hana) babban xa ga Makaxa Musa Nadada, *Daudun Kixa* ko kuma *Galadiman Kixa* na Makaxa Sa'idu Maidaji Sabon Birni shi ne wanda ya gaji kixa a hannun Makaxa Maidaji Sabon Birni a halin yanzu.

5.3 Naxewa

Kamar yadda bayanai suka gabata a wannan aiki, an yi bitar ayyukan da wasu mawallafa suka gabatar masu dangantaka da fagen wannan nazari. Baya ga haka kuma, nazarin ya duba jigogi manya da qanana, waxanda Makaxa Maidaji ya cuccusa a cikin tsarin waqoqinsa. Sai dai kafin nan sai da aka yi bayani bakandame game da shi kansa jigo da yadda akan gina shi a waqoqin baka na Hausa.

- Binciken kuma ya tabbatar da Makaxa Maidaji makaxi ne wanda ya xauki noma a matsayin sana'arsa. Shahararren manomi ne kuma ayyukan gona ne duka magabatansa suka aiwatar. Ta haka ne ma ya sa aka haifi Sa'idu Maidaji a cikin gona har ake yi masa laqabi da 'Maidaji' kamar dai yadda aka yi bayani a cikin wannan aiki.

A wannan nazari, har wa yau, an fahimci, aqalla Makaxa Maidaji ya yi wa mutane arba’in da biyar (45) waqoqi, kama daga iyayen gidansa sarakunan Gobir da sarakunan wasu garuruwa da sukan gayyace shi da attajirai da alqalai da sauran mutane masu riqe da sarautun gargajiya.

Bisa jimla, wannan nazari ya tabbatar da Makaxa Maidaji, makaxi ne mai fasaha, mai azanci, mai zalaqa, mai zurfin tunani da kaifafa harshe, gwani kuma a fage na zaven kalmomi na waqa. Makaxi ne wanda ya sassaqa tunani da saqonni ingantattu a waqoqinsa masu tsima jiki.

A lokacin da nake kammala wannan nazari, ina fatan wannan aiki ya zama mai amfani ga dukkan masu nazarin harshe da adabi da al’adun Hausawa tare kuma da sauran masu sha’awa da qoqarin havaka harshen Hausa.

MANAZARTA

Abalogu, U. N. da Ashiwaju, G. da Amadi-Tshiwala, M. R. (eds). (1981). Emaconprint Limited, Lagos, Nigeria.

Abba, M. & Zulyyadaini, B. (2000). *Nazari kan Waqar Baka ta Hausa*. Gaskiya Corporation Limited, Zaria, Nigeria.

Abbas, U. A. (2008). "Sassarquwar Adabi Cikin Adabi: Nazarin Adon Harshe a Waqoqin Finafinan Hausa". Kundin Digiri na Uku. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Abraham, R. C. (1977). *Dictionary of Hausa Language*. Hodder & Stoughton, London.

Ado, U. (1994). "Nason Adabin Baka Cikin Rubutaccen Wasan Kwaikwayo". Kundin Digiri na Biyu. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Abdu, S. (2003). *Poet of the People Republic*. Benchmark Publishers Limited, Kano, Nigeria.

Abdulqadir, X. (1975). "The Role of an Oral Singer in Hausa/Fulani Society: A Case Study of Mamman Shata". Kundin Digiri na Uku. Indiana University, Bloomington, U.S.A.

Abdulqadir, X. (1976). 'The Role of a Hausa Poet' a Cikin *Harsunan Nijeriya VI*. Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Abdulqadir, X. (1981). 'Oral Composition: A Historical Appraisal' a Cikin *Oral Poetry in Nigeria.* Emaconprint Limited, Lagos, Nigeria.

Abdulqadir, H. D. (2002). "Nazarin a kan Jigon Faxakarwa na Adabin Baka". Kundin Digiri na Biyu. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Abubakar, H. S. (1991). "Shehu Ajilo Xanguzuri: Rayuwarsa da Ayyukansa". Kundin Digirin Farko. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Abubakar, S. (1982). “Birnin Shehu: The City of Shehu: A Social and Economic History”. Kundin Digiri na Uku. Ahmadu Bello University, Zaria, Nigeria.

Adamu, M. (1978). *The Hausa Factor in West African History*. Ahmadu Bello University Press & Ibadan: Oxford University Press.

Adamu, M. (1989). *Kammalallen Tarihin Afirka, Juzu’i na 2*. Usmanu Xanfodiyo University Press, Sokoto, Nigeria.

Adamu, M. T. (1997). *Asalin Hausawa da Harshensu*. Xan Sarkin Kura Publishers Limited, Kano, Nigeria.

Ajayi, J. F. A. & Crowder, M. (1971). *History of West Africa*. Longman Group Limited, London.

Albasu, S. (1990). ‘From Caliph to Sultan: The Changing Role and Functions of the “Caliph” of Sokoto After British Conquest’ a Cikin *State and Society in the Sokoto Caliphate.* Gaskiya Corporation Limited, Zaria, Nigeria.

Alqali, M. (1989). “Cuxexeniyar Adabi: Tasirin Adabin Baka akan Rubutattun Waqoqin Hausa Dangane da Habaici da Zambo da Kirari da Karin Magana”. Kundin Digiri na Biyu. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Alqur’ani Mai Girma. Riyadh: Darussalam Global Leader in Islamic Books.

Amin, M. L. (2004). ‘Re-Interpreting Hausa Proverbs on Duniya’ a Cikin *HARSHE 2: Journal of African Languages.* Sashen Harsunan Nijeriya da na Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya, Nijeriya.

Amin, M. L. (2010). ‘Bitar Littafin *Narambaxa*’ a Cikin *HARSHE 4: Journal of African Languages.* Sashen Harsunan Nijeriya da na Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya, Nijeriya.

Aminu, M. (1978). ‘Muhimmancin Maroqan Baka a Qasar Hausa’ a Cikin *Nahawu da Adabin Hausa*. Yahaya, I. Y. & Rufa’i, A. (ed). Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Augi, A. R. (1984). "The Gobir Factor in the Social and Political History of the Rima Basin". Kundin Digiri na Uku. Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria, Nigeria.

Awde, N. (1996). *Hausa: Hausa-English, English-Hausa Dictionary*. Hippocrene Books Limited, U.S.A.

Baldick, C. (2004). *Dictionary of Literary Terms*. Oxford University Press, London.

Bango, A. & King, A. V. (1986). 'An Intoduction to the Life and Works of Abubakar Akwara'. Paper Presented at the Department of Nigerian and African Languages. Ahmadu Bello University, Zaria, Nigeria.

Barabash, Y. (1977). *Aesthetics and Poetics*. Progress Publishers, Moscow, Russia.

Bargery, G. P. (1934/1951). *A Hausa-English Dictionary and English-Hausa Vocabulary*. London: Oxford University Press.

Barry, P (1995). *Beginning Theory: An Introduction to Literary and Cultural Theory*. Manchester University Press, Manchester, England.

Barth, H. (1965). *Travels and Discoveries in North and Central Africa*. Vol. I & Vol. II. London.

Bello, G. (1976). 'Yabo, Zuga da Zambo a Waqoqin Sarauta' a Cikin *Harsunan Nijeriya VI*. Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Berger, A. A. (1992). *Popular Culture Genres: Theories and Text.* London: Sage Publishers.

Birniwa, H. A. (2005). 'Tsintar Dame a Kala: Matsayin Karin Magana a Cikin Waqoqin Siyasa'. *Xunxaye Journal of Hausa Studies*. Department of Nigerian Languages. Usman Xanfodiyo University, Sokoto, Nijeriya.

Black, M. (1962). *Models and Metaphors*. Cornel University Press, Cornel.

Bunza, A. M. (2009). *Narambaxa*. Ibrash Islamic Publications Centre Limited, Lagos, Nigeria.

Burgess, J. W. (1964). *English Literature*. Longmans, Green and Company Limited, London.

Burton, S. H. (1954). *The Criticisms of Poetry*. Longman, London.

Chafe, K. S. (1990). 'The Transformation of Socio-Political Policies of the Leaders of the Sokoto Caliphate: A Preliminary Study of the Impcat of the Socio-Economic Progrmme and Policies on Political Integration' a Cikin *State and Society in the Sokoto Caliphate.* Gaskiya Corporation Limited, Zaria, Nigeria.

Chiegeonu, N. (1990). *Introduction to Study of Literaure and Criticism*. Odumatt Press and Publishers, Oyo, Nigeria.

Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya. (2006). *Qamusun Hausa*. Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Chamo, I. Y. (2005). "Saqo a Finafinan Hausa: Nazari a Kan Jigo da Rabe-Rabensa". Kundin Digiri na Biyu. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Cuddon, J. A. (1979). *Dictionary of Literary Terms*. Andre Doustsch, London.

Daba, H. A. (1978). "Hausa Oral Poetry: A Case Study of Adamu Xanmaraya Jos". Kundin Digiri na Biyu. Jami'ar Khartoum, Sudan.

Daba, H. A. (2006). *Xanmaraya Jos in Folkloric Perspective.* Benchmar Publishers Limited, Kano, Nigeria.

Dorson, R. A. (1960). 'Oral Styles of American Folk Narations'. *Styles in Language.*

Dunfawa, A. A. (2003). *Ma'aunin Waqa. Garkuwa Publishers, Sokoto, Nigeria.*

Xan'iya, D. (1997). "Adon Harshe Cikin Rubutaccen Adabin Hausa". Kundin Digiri na Biyu. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Xangambo, A. (1973). "Shata da Waqoqinsa". Kundin Digirin Farko. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Xangambo, A. (1981). 'Rikixar Azanci: Siddabarun Salo da Harshe Cikin Tabarqoqo Tahamisin Aliyu Xansidi'. *Studies in Hausa Language, Literature and Culture*. (ed. Yahaya, I. Y. da Wasu). Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Xangambo, A. (1982). “Jigon Ban-dariya a Adabin Hausa”. Departmental Seminar. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Xangambo, A. (2007). *Xaurayar Gadon Fexe Waqa*. Amana Publishers Limited, Kaduna, Nigeria.

Xangambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa*. Amana Publishers Limited, Kaduna, Nigeria.

Xanjuma, M. S. (1982). Rabe-Raben Waqoqin Hausa da Tasirinsu ga Rayuwa a Qasar Hausa”. Kundin Digiri na Biyu. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Edward, B. F. (1971). “ Hausa Court Music in Kano”. Kundin Digiri na Uku. Jami’ar Columbia.

Encyclopaedia Britannica, 1943-1973.

Finnegan, R. (1970). *Oral Literature in Africa.* Oxford University Press, London.

Furniss, G. (1977). “Some Aspects of Hausa Modern Poetry: Themes, Style and Values with Special Reference to the ‘Hikima’ Poetry Circle in Kano”. Kundin Digiri na uku. SOAS, London.

Furniss, G. (1996). *Poetry, Prose and Popular Culture in Hausa*. Edinburgh University Press Limited, Edinburgh, Germany.

Furniss, G. Malami, B.; William, B. (2004). *Bibliography of Hausa Popular Fiction 1987-2002.* Koln: Germany.

Gagan, R. (1991). (ed). *Dictionary of Literary Terms*. New Delhi Amol Publication, India.

Gambo, D. (1990). “Maidaji Sabon Birni da Waqoqinsa”. Kundin Digirin Farko. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Garba, M. (1998). “Azancin Magana a Waqoqin Makaxan Baka”. Kundin Digiri na Biyu. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Gray, B. (1975). *The Phenomenon of Literature.* Mouton & Co. N.V. Publishers, The Hague, Netherlands.

Gray, M. (1994). *Dictionary of Literary Terms*. Longman Group, London.

Greenberg, J. H. (1963). *The Languages of Africa*. The Huque, London.

Gumel, M. A. (1992). "Tarbiyya da Dangoginta a Waqoqin Baka na Hausa". Kundin Digiri na Biyu. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da na Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya, Nijeriya.

Gusau, S. M. (1983). "Waqoqin Noma na Baka: Yanaye-Yanayensu da Jigoginsu, Musamman a Sakkwato". Kundin Digiri na Biyu. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Gusau, S. M. (1984[a]). 'Nazarin Zavavvun Waqoqin Baka na Hausa'. Cyclo Styled Edition. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Gusau, S. M. (1984[b]). "Adabin Hausa na Gargajiya: Ma'anarsa da Yanaye-Yanayensa". Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Gusau, S. M. (1985/1993). 'Salo da Sarrafa Harshe a Waqoqin Baka na Hausa' a Cikin *Nazari a kan Harshe da Adabi da Al'adu na Hausa*. Rufa'i, A. Yahaya, I. Y., Bichi, A. Y. (editoci). Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano Nijeriya.

Gusau, S. M. (1988). "Waqoqin Makaxan Fada: Sigoginsu da Yanaye-Yanyensu". Kundin Digiri na Uku. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Gusau, S. M. (1991). 'Tsokaci kan Tushen Kalmar Adabi' a Cikin *Mujallar Bagaruwa.* No. 1, Vol. 1. Kano: Qungiyar Hausa. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Gusau, S. M. (1996[a]). *Makaxa da Mawaqan Hausa*. Benchmark Publishers Limited, Kano, Nigeria.

Gusau, S. M. (1996[b]). 'Dabarar Alkunya a Waqoqin Makaxan Fada' a Cikin *Mujallar Afirka ta Yamma kan Nazarin Harshe da Adabi da Sharhi.* Vol. I No. 1. (ed. Zafar Khan). Tsangayar Fasaha da Addinin Musulunci, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Gusau, S. M. (1999). 'Muhimman Garuruwan Qasar Hausa: Waiwaye kan Tarihin Kafuwarsu a Taqaice' a Cikin *Mujallar Afirka ta Yamma kan Nazarin Harshe da Adabi da Sharhi.* Vol. I No. 2.

Tsangayar Fasaha da Addinin Musulunci, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Gusau, S. M. (2001). 'Waqar Gogarman Tudu ta Ibrahim Narambaxa a Mazubin Nazari' a Cikin *Algaita Journal of Current Research in Hausa Studies*. (ed. Yusuf, M. A.). Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Gusau, S. M. (2002[a]). *Salihu Jankixi Sarkin Taushi*. Baraka Press and Publishers Limited, Kaduna, Nigeria.

Gusau, S. M. (2002[b]). 'Saqo a Waqoqin Baka: Tsokaci kan Turke da Rabe-Rabensa'. a Cikin *Nazari a kan Harshe da Adabi da Al'adun Hausawa. (*ed. Bichi, A. Y. da Wasu). Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano Nijeriya.

Gusau, S. M. (2003 [a]). "Waqar Sa Sanusi Sarkin Yaqi a Mazubin Nazari" *FAIS Journal of Humanities*. Abba, I. A. (ed). Tsangayar Fahasa da Addinin Musulunci, Jami'ar Bayero, Kano Nijeriya.

Gusau, S. M. (2003[b]). *Jagoran Nazarin Waqar Baka*. Benchmark Publishers Limited, kano, Nigeria.

Gusau, S. M. (2008[a]). *Waqoqin Baka a Qasar Hausa: Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu*. Benchmark Publishers Limited, Kano, Nigeria.

Gusau S. M. (2008[b]). *Dabarun Nazarin Adabin Hausa*. Benchmark Publishers Limited, Kano, Nigeria.

Gusau, S. M. (2009). *Diwanin Waqoqin Baka: Zavavvun Matanoni na Waqoqi na Hausa*. Century Research and Publishing Limited, Kano, Nigeria.

Gusau, S. M. (2011). *Adabin Hausa a Sauqaqe.* Century Research and Publishing Limited, Kano, Nigeria.

Gusau, S. M. & Funtua, A. I. (2011). *Waqoqin Baka na Hausa.* Century Research and Publishing Limited, Kano, Nigeria.

Gwarzo, S. S. (2010). "Salo da Sarrafa Harshe a Littafin Abin Mamaki na Misbahu Muhammad Abubakar". Kundin Diflomar Gaba da Digirin Farko a Fannin Hausa. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Halliru, A. (1983). "Aliyu Xandawo da Waqoqinsa". Kundin Digirin Farko. Jami'ar Usmanu Xanfodiyo, Sakkwato, Nijeriya.

Hukumar Binciken Tarihi da Kyautata Al'adu ta Jihar Katsina. (2003). *Waqokin Alhaji Mamman Shata* (Diwani na Xaya) The Government Printer, Katsina, Nigeria.

Ibrahim, M. S. (1977). *Adabin Hausa.* Mahaxar Ilmi, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya, Nijeriya.

Ibrahim, M. S. (1981). "Adabin Gargajiya na Hausa Kafin da Kuma Bayan Musulunci" a cikin *Nazari a kan Harshe da Adabi da Al'adu.* Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Ibrahim, M. S. (1983). *Kowa ya Sha Kixa*. Longman Nigeria Limited, Zaria, Nigeria.

Junju, M. H. (1985). 'Asalin Hausawa da Harshensu' a cikin *Nazari a kan Harshe da Adabi da Al'adun Hausawa*. Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Kafin Hausa, A. U. (1979). "Classification of Maroqa in a Hausa Society". Department of African language and Culture, Ahmadu Bello University, Zaria, Nigeria.

Kani, A. M. & Gandi, K. A. (1990). *State and Society in the Sokoto Caliphate.* Gaskiya Corporation Limited, Zaria, Nigeria.

King, A. V. (1967). "Music at the Court of Katsina". Kundin Digiri na uku. London.

King, A. V. (1986). "Statement, Restatement and Extension: Stanzaic Structure in Hausa Court Songs". Department of African Language and Culture, Ahmadu Bello University, Zaria.

King, A. V. (1981). 'Form and Functions in Hausa Professional Songs'. *Oral Poetry in Nigeria.* Nigeria Magazine, Lagos, Nigeria.

Kofoworola, Z. & Lateef, Y. (1987). Hausa Performing Arts and Music. Nigeria Magazine, Lagos, Nigeria.

Kunene, D. P. (1971). *Heroic Poetry of the Bosotho*. Clarendon Press, Oxford, London.

Magaji, A. (1980). "Kassu Zurmi da Waqoqinsa". Kundin Digirin Farko. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Magaji, A. (1983). “Gudummuwar Waqoqin Baka na Hausa Dangane da Keve Tarihi”. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Mani, A. (1970). *Zuwan Turawa Nijeriya ta Arewa.* Gaskiya Corporation, Zaria, Nigeria.

Muhammad, X. (ed). (1990). *Hausa Meta-language.* University Press Limited, Ibadan Nigeria.

Muhammad, X. (1973). ‘A Vocabulary of Literary Terms in Hausa’a a Cikin *Harsunan Nijeriya III.* Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nigeria.

Muhammad, X. (1977). “Individual Talents in the Hausa Poetic Tradition: A Case Study of Aqilu Aliyu and his Arts”. Kundin Digiri na Uku. SOAS University, London.

Muhammad, X. (1978). ‘Waqa Bahaushiya’ a Cikin *Studies in Hausa Language and Literature* I. Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Muhammad, X. (1981). ‘Bakandamiya: Towards a Characterization of the Poetic Masterpiece in Hausa’ a Cikin *Oral Poetry in Nigeria.* Emaconprint Limited, Lagos, Nigeria.

Muhammad, Y. M. (2003). *Adabin Hausa*. NAERLS Printing Press, Zaria, Nigeria.

Ndudim, C. (1999). *Introduction to Study of Literaure and Criticism*. Odumatt Press and Publishers, Oyo, Nigeria.

Newman, P. da Wasu (Tsarawa), (1977). *Sabon Qamus na Hausa Zuwa Turanci*. Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya. University Press Limited, Ibadan, Nigeria.

Northern Nigeria Publication Company. (1971). *Hausawa da Maqwabtansu*.

Nyuidze, Emilder II. (2003). *Songs of Xanmaraya Jos: Theory and Style.* Volume One. Jos: Greenword Publishing Company.

O.D.U. (1985). Oral Documentation Unit Catalogue of Recordings, Department of Nigerian and African Languages, Ahmadu Bello University, Zaria, Nigeria.

Okpewho, I. (ed). (1990). *The Oral Performance in Africa.* Spectrum Books Limited, Ibadan, Nigeria.

Olatunde, O. O. (2005). *Features of Yoruba Oral Poetry*. University Press PLC, Ibadan, Nigeria.

Parry, M. (1932). 'Studies in the Epic Technique of Oral Verse-Making'. *HSCP*.

Peck, J. and Coyle, M. (2002). *Literary Terms and Criticisms*. Hampshire, Palgrave Macmillan.

Ramatu, (2003). "Makaxan Sarauta da Muhimmancinsu a fadar Zazzau". Kundin Digiri na Biyu. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Richards, I. A. (1961). *Principles of Literary Criticism*. Routledge and Kegan Paul Limited, London.

Roger, C. (1981). *Figures of Reality.* Croomhelm Limited, London.

Sabon Birni. "District Notebook". (DNB/ 44). Ref. 93/15/44).

Sada, S. Y. (1979). "The Social and Prosodic Features of Oral Poetry as Examplified by Hausa Court Poetry". Kundin Digiri na Biyu. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Sadi, S. A. (1989). "Tsokaci a kan Hanyoyin Nazarin Adabin Baka na Hausa". Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Sankalawa, L. B. (1994). "Nazarin Rayuwar Makaxa Sani Sabulu Kanoma da Falsafar Waqoqinsa". Kundin Digirin Farko. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Satatima, I. G. (1999). "Tarsashin Adabin Baka a Cikin Rubutattun Waqoqin Hausa". Kundin Digiri na Biyu Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Satatima, I. G. (2009). "Waqoqin Baka na Xarsashin Zuciya: Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu". Kundin Digiri na Uku. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Sheme, I. Qanqara, A. I., Albasu, Y. T., Malami, A. (2006). *Shata Ikon Allah.* Informat Publishers, Kaduna, Nigeria.

Skinner, N. (1971). 'Realism and Fantasy in Hausa Literature'. *Review of National Literatures Vol. 2 No 2.*

Skinner, N. (1980). *An Anthology of Hausa Literature in Translation.* Northern Nigeria Publishing Company, Zaria, Nigeria.

Toronkawa, M. U. (2006). "Adon Harshe a Waqoqin Sarauta Uku na Makaxa Rabo Ango Yabo". Kundin Diflomar Gaba da Digirin Farko a Fannin Hausa. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Tsoho, M. Y. (1987). "Tarkakken Matanin Waqar Kanzil Azimi ta Aliyu Namangi". Kundin Binciken Digiri na Biyu. Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya, Nijeriya.

Tsoho, M. Y. (2001). 'Tubalan Ginin waqoqin Yabo: Tsokaci kan Yabau a Waqoqin Iko' a Cikin *FAIS Jurnal of Humanities*. Vol, 1, Number 4. Tsangayar Fasaha da Addinin Musulunci, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Tsoho, M. Y. (2010). 'Sanqira: Gudummuwarsa a Gina Waqoqin Yabo' a Cikin *HARSHE 4: Journal of African Languages'*. Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya, Nijeriya.

Umar, M. B. (1984). "Symbolism in Oral Poetry: A Study of Symbolical Indices of Social Status in Hausa Court Songs". Kundin Digiri na Biyu. Department African Languages and Cultures, Ahmadu Bello University, Zaria, Nigeria.

Umar, M. B. (1985). *Xanmaraya Jos da Waqoqinsa*. University Press Limited, Ibadan, Nigeria.

Waya, T. (1990). "Habaici, Zambo da Karin Magana: Matsayinsu da Tasirinsu". Kundin Digirin Farko. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Westly, D. (1986). "Oral Traditions And The Beginning Of Hausa Fiction" Kundin Digirin na Uku. Sashen Nazarin Harsuna da Adabin Afirka. Jami'ar Wisconsin, Madison, U.S.A.

Wushishi, B. J. (1998). "Adabin Baka: Sigoginsa da Hikimominsa". Kundin Digiri na Biyu. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Wurma, A. G. (1990). "Tasirin Hausawa a Tarihin Afirka ta Yamma". Kundin Digiri na Biyu. Sashen Harsunan Nijeriya da na Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, zariya, Nijeriya.

Yahaya, D. H. (1991). “Alhaji Musa Xanqwairo: Makaxin Fada ko na Jama’a”. Kundin Digirin Farko. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Yahaya, I. Y. (1973). “Tarihin Adabin Hausa: Ma’anar Adabi”. Maqala Wadda ya Gabatar. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero, Kano, Nijeriya.

Yahaya, I. Y. (1979). “Oral Arts and Socialization Process: A Socio-Folklore Perspective of Initiation From Childhood to Adult Hausa Community Life”. Kundin Digiri na uku. A.B.U/B.U.K.

Yahaya, I. Y. (1988). *Hausa a Rubuce: Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa*. Northern Nigeria Publishing Company, Zaria, Nigeria.

Yahya, A. B. (1984). “Matsayin Waqoqin Baka a Cikin Adabin Hausa”. Sashen Hausa, Jami’ar Usmanu Xanfodiyo, Sakkwato, Nijeriya.

Yahya, A. B. (1988). “Qawancen Jigo Tsakanin Waqoqin Baka da Rubutattu”. Takarda Wadda ya Gabatar. Jami’ar Usmanu Xanfodiyo, Sakkwato, Nijeriya.

Yahya, A. B. (1997). *Jigon Nazarin Waqa*. Fisbas Media Services, Kaduna, Nigeria.

Yahya, A. B. (2001). *Salo Asirin Waqa*. Fisbas Media Services, Kaduna, Nigeria.

Yusuf, H. (1979). *Hamza Caji da Waqoqinsa*. Hudahuda Publishers, Kano, Nigeria.

‘Yar’adua, T. M. (2001). ‘Wasan Kwaikwayo: Sigoginsa da Jigoginsa’ a Cikin *Algaita Journal of Current Research.* Maiden Issue. Sashen Koyar Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero, Kano, Nigeria.

Zarruq, R. M. (1985). “Wasu Matsaloli a Karin Sautin Hausa da Hanyoyin Koyar da shi”. Kundin Digiri na Biyu. Sashen Harsunan Nijeriya da na Afirka, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya, Nijeriya.

Zarruq, R. M. da Wasu. (1987). *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa.* University Press Limited, Ibadan, Nigeria.

Zaruma: A Cultural Magazine of Sokoto State. (1978). Sidi Umaru Printing Press, Sokoto, Nigeria.

Zaruma: A Cultural Magazine of Sokoto State. (1982). Sidi Umaru Printing Press, Sokoto, Nigeria.